مختصر منهاج السنة النبوية

# TAFARKIN SUNNAH

## TATTAUNAWA TA RUWAN SANYI TSAKANIN IBNU TAIMIYYAH DA 'YAN SHI'AR ZAMANINSA

**Wanda Ya Taqaita Shi A Larabce**

**SHEIKH ABDALLAH AL-GUNAIMAN**

**FASSARA DA YAXAWA**

**CIBIYAR AHLUL-BAITI DA SAHABBAI TA NAJERIYA**

**97, Titin Ahmadu Bello, Sokoto, Najeriya**

**www.ahlulbaity.com**

**Kwamitin Fassara**

**Dr. Muhammad Mansur Ibrahim**
Na Cibiyar Yaxa Addinin Musulinci Ta Jami'ar Usmanu Xan Fodiyo, Sakkwato kuma Darektan Cibiyar Ahlulbaiti da Sahabbai

**Shugaba**

**Dr. Ibrahim Bello** Na Kolejin Ilimi Ta Shehu Shagari Da Ke Sokoto.
Ya Rasu A Lokacin Da Yake Cikin Aikin. Allah Ya Jiqan Sa.

**Memba**

**Mal. Aminu Ibrahim Maru** Na Hukumar Jaridu Ta Jihar Sokoto
Digiri a sashen Hausa

**Memba**

**Mal. Usmanu Sarkin Vurmin Jabo** Na Kolejin Sarkin Musulmi Abubakar Ta Sokoto.
Digiri a ilimin addinin musulunci

**Memba**

**Aliyu Rufa'i Gusau**
Na Ma'aikatar Lamurran Addini Ta JIhar Zamfara
Yana da babbar takardar shaidar qwarewa a fannin ilimin addini daga jami'ar Afirika ta duniya da ke Sudan, da diploma a kolejin fasaha da kimiyya ta Sokoto. Ya kusa kammala digirinsa a fannin Hausa.

**Sakatare**

**Kwamitin Bita**

**Sokoto Bureau Of Translation,**
Federal Housing Estate, Runjin Sambo, Sokoto.

**Tare Da:**

**Dr. Muhammad Mansur Ibrahim**
Darektan Cibiyar Ahlulbaiti da Sahabbai

**Da Aliyu Rufa'i Gusau**
Na Ma'aikatar Lamurran Addini Ta Jihar Zamfara

*Babban kifi, babbar gora*

*Bigi sai Bigi, babba sai manya*

*Minhaju Gari, babban kundi*

*Ilimi a ciki gayya-gayya*

*Tattaunawa ta ruwan sanyi*

*A cikinta da ba kama-karya*

*Xan Taimiyyah a bayaninsa*

*Ya yi ta yana sa-in-sanya*

*Hujjojin Shi'ah ya rorrosa*

*A cikinsu gaba xaya ba qwaya*

*Da ya bayyana Shubhohi ne duk*

*Kuma ba su gira ko an shanya*

*Center a yaba ma ta tilas ne*

*Da ta fassara aikin tas sanya*

*A daka, a dafa, a saka kwanna*

*Kowa ya ci yara har manya*

*Aliyu Rufa'i Gusau*

**QUMSHIYA**

**Gabatarwar Cibiyar Ahlul-Baiti Da Sahabbai............................................. 1**

**Rayuwar Ibnu Taimiyyah.......................................................................... 10**

Wane Ne Ibnu Taimiyyah?........................................................................ 10

Asalinsa.................................................................................................... 10

Tashinsa Da Iliminsa................................................................................. 11

Mujaddadi Ibnu Taimiyyah ........................................................................ 11

Jarabawar Da Ibnu Taimiyyah Ya Gamu Da Ita.......................................... 12

Rasuwarsa................................................................................................. 13

Littafan Da Aka Duba Don Ba Da Tarihinsa............................................... 13

**Gabatarwar Sheikh Gunaiman Wanda Ya Taqaita Littafin.......................... 16**

**0.1 Gabatarwar Ibnu Taimiyyah................................................................. 18**

**Zango Na Xaya: 'Yan Shi'ah Da Aqidunsu................................................ 22**

1.0 Malamai Ku Bayyana Gaskiya............................................................... 22

1.1 Zumuntar Shi'ah Da Yahudawa Da Nasara............................................ 24

1.1.2 Jadawalin Zumuntar Shi'anci Da Yahudanci....................................... 26

1.2 Mafarin Sunan 'Yan Shi'ah "Rafilah"..................................................... 28

1.3 Wautar 'Yan Shi'ah.............................................................................. 29

1.4 Shaidar Malamai A Kan 'Yan Shi'ah...................................................... 36

1.5 Wai Imamah Ita Ce Tushen Addini........................................................ 41

1.6 Wane Shugabanci Ne Ya Fi?................................................................. 43

1.7 Tsakanin Shi'anci Da Sufanci................................................................. 49

1.8 Zancen Khadir Da Ilyasu:...................................................................... 49

1.9 Mu Koma Kan Maganar *Imamah:*............................................................ 49

1.10 Asalin Addini A Wurin 'Yan-Sha-Biyu.................................................. 50

1.11 Takin Saqar 'Yan Shi'ah........................................................................ 51

1.12 Daga Gani Sai Kai Ya Kumbura?!........................................................ 52

1.13 Shugabanci Ba Ya Cikin Rukunan Addini............................................ 53

1.14 Ina Nassin Yake?..................................................................................... 56

1.15 Zaven Siddiqu Nassi Ne Ko Shawara?................................................. 56

1.16 Halifofi Shiryayyu..................................................................................... 59

**2.0 Zango Na Biyu: Dalilan Wajabcin Imamiyyah!............................................................................................ 64**

2.1 Wannan Da Wannan Suna Da Banbanci................................................. 85

2.2 Wai Imamansu Ba Su Kuskure!............................................................... 87

2.3 Adadin Imamai........................................................................................... 92

2.4 Wace Mubaya'a Ce Ingantatta?................................................................ 92

2.5 Mazhaba Da Qiyasi.................................................................................... 92

2.6 Wai 'Yan Shi'ah Ne Kawai Za Su Shiga Aljanna!................................... 95

2.7 Maganar Wofi: Wai Su Kaxai Ke Da Tabbacin Suna Kan Gaskiya!....... 101

2.7 Wai Sun Karvo Mazhabarsu Daga Ma'asumai........................................ 106

2.7.1 Imami Na Farko: Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu:* ............................. 106

2.7.2 Hasan Da Husaini:..................................................................................... 108

2.7.3 Zainul Abidina Da Baqir Da Sadiq:........................................................ 110

2.7.4 Musa Xan Ja'afar:...................................................................................... 112

2.7.5 Ali Ar-Ridha:.............................................................................................. 113

2.7.6 Muhammadu Al-Jawad:............................................................................ 114

2.7.7 Ali Al-Hadi:................................................................................................ 116

2.7.8 Hasan Xan Muhammad Al-Askari:......................................................... 117

2.7.9 Muhammad Xan Hassan (Mahadi-Na-Voye):........................................ 118

2.7.10 Hadisin Mahadi:...................................................................................... 119

2.8 Wai Imamai Sha Biyu Sun Fi Kowa!:........................................................ 120
2.9 Malaman Sunnah Sun Fi Qarfin Zargi:..................................................... 123
2.9.1 Malaman Sunnah Ba Su Ta'assubanci:.................................................. 124
2.9.2 Addu'a Ga Halifofi Cikin Huxuba:........................................................ 126
2.9.3 Shafar Qafa Wajen Arwalla:.................................................................. 127
2.9.4 Mutu'ar Hajji Da Ta Aure:...................................................................... 128
2.9.5 Ba A Cin Gadon Annabawa:.................................................................. 129
2.9.6 Fatima Ta Nemi Gonar Fadak:............................................................... 131
2.9.7 Wai Don Me Aka Ce Da Abubakar "Siddiqu"?:.................................... 136
2.9.8 Abubakar Halifan Manzo:...................................................................... 137
2.9.9 Wai Don Me Aka Ce Da Umar "Faruqu"?:............................................ 140
2.9.10 A'isha Uwar Muminai:.......................................................................... 142
2.9.11 Ina Laifin Nana A'isha?:....................................................................... 143
2.9.12 Suna Jin Haushin A Kira Ta "Uwar Muminai":..................................... 150
2.9.13 Sukar 'Yan Shi'ah Ga Mu'awiyah:........................................................ 152
2.9.14 'Yan Shi'ah Sun Tsani Mu'awiyah:...................................................... 155
2.9.16 Khalidu Xan Walidu "Takobin Allah":................................................. 161
2.9.17 'Yan Shi'ah Suna Kariyar Murtaddai:.................................................. 163
2.9.18 Wai Iblisu Ma Ya Fi Mu'awiyah.. Inji Shi!:......................................... 167
2.9.19 Yazidu Ya Zama Sarki, Husaini Ya Samu Shahada:............................. 170
2.9.20 Yazidu Bai Cancanci La'anta Ba:........................................................ 175
2.10 Garin Neman Qiba An Samo Rama:....................................................... 180
2.11 Na Gaba Ya Yi Gaba:................................................................................ 183
2.12 Hadisin Mayafi Ba Hujja Ba Ne:............................................................. 186
2.13 Tilas Mai Hawan Ruwa Ya Yi Babban Masaki:....................................... 188

2.14 Ayar: ﴿ ۞ أَجَعَلۡتُمۡ سِقَايَةَ ٱلۡحَآجِّ وَعِمَارَةَ ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِ ﴾التوبة: ١٩: ...................... 188

2.15 Hadisin Wasiyya Qagagge Ne: ............................................................. 189

2.16 Bai Isa Kayan Gabas Ba:......................................................................... 190

2.17 Siddiqai Basu Qidayuwa: ..................................................................... 191

2.18 Ba Aliyu Ne Farau Ba: ......................................................................... 192

2.19 Fixar Hadisin Amru Xan Maimun: ..................................................... 193

2.20 Mafi Yawan Hadisansu Na Qarya Ne: ................................................. 196

2.21 Yamutsa Hazon Hadisin Ranar Shura: ................................................. 200

2.22 Wata Sabuwar Tatsuniya Tasu: ........................................................... 208

2.23 Bajini Xan Bajini Xan'uwan Bajini: .................................................... 209

2.24 Son Ali Da Sauran Sahabbai Duk Wajibi Ne:....................................... 210

2.25 Son Aliyu Bai Isa Shinge: ..................................................................... 210

2.26 Hadisan Gizo Da Qoqi: ........................................................................ 212

2.27 Sun Mayar Da Sahabbai Dalga: ............................................................ 213

2.28 Tawali'u Ne Ba Rashin Cancanta Ba: .................................................. 215

2.29 Abu Ne Daga Allah: .............................................................................. 216

2.30 Halifa Abubakar Bai Damu Ba: ............................................................ 217

2.31 Tsananin Tsoron Allah Ne: ................................................................... 218

2.32 Ja Da Baya Ba Tsoro Ba: ...................................................................... 218

2.33 Wani Jihadin Ne Ya Tsayar Da Siddiqu: .............................................. 219

2.34 Ba Rashin Yarda Ba Ne: ........................................................................ 220

2.35 Siddiqu Ba Jahili Ba Ne: ...................................................................... 223

2.36 Aliyu Mai Wuta Aljihu: ......................................................................... 223

2.37 Barewa Ba Ta Gudu Xanta Ya Yi Rarrafe: .......................................... 224

2.38 Mafi Yawan Mutanen Kufa Jahilai Ne: ................................................ 226

2.39 Girma Ya Kai !: .......................................................................... 227

2.40 Ba Dai A Madina Ba: ............................................................... 228

2.41 Akwai Abin Da Siddiqu Ya Gani: .......................................................... 229

2.42 Gadon Fatima Da Laqabin “Halifa”: ........................................................ 233

2.43 Ya Kuma Dira A Kan Umar: .................................................................. 234

2.44 Sayyidina Umar: Mai Gani Da Hasken Allah: ...................................... 237

2.45 Halifa Umar Ba Azzalumi Ba Ne: ............................................................ 241

2.46 Gargaxi Ne Ba Haddi Ba: ........................................................................ 244

2.47 Allah Ne Kawai Ba Ya Mantuwa Ba Ya Kure: ...................................... 244

2.48 Halifa Umar Ba Jahili Ba Ne: ................................................................. 245

2. 49 Wannan Shi Ne Halin Bayin Allah Na Gari: ........................................ 247

2. 50 Halifa Umar Bai Jahilci Haddin Shan Giya Ba: .................................. 248

2.51 Ba Ta San Zina Haramun Ce  Ba.: ........................................................ 249

2.52 Annabi Sulaimana Ne Ba Halifa Umar Ba: .......................................... 250

2.53 Ra’ayin Shiryayyaun Halifofi Ne: .......................................................... 251

2.54 Ijtihadi Ne Wannan: ................................................................................. 252

2.55 Ra’ayin Sahabbai Hujja Ne: .................................................................... 253

2.56 Shawara Ba Laifi Ba Ce.: ........................................................................ 254

2.57 Xan Shi’ar Ya Dira A Kan Usman: ....................................................... 266

2.58 Mu Zuba Zuwa: ......................................................................................... 273

2.59 Maganar Shaharastani Ba Hujja Ce Ba.: ................................................ 291

2.60 ‘Yan Shi’ah Na Taimakon Kafirai A Kan Musulmi: ............................ 308

**3.0 Zango Na Uku: Dalilai Na Hankali: ........................................................ 315**

3.1 Wai Allah Ne Ya Naxa Ali!: ...................................................................... 336

3.2 Wane Nassi Ne Ke Iya Samuwa?: ............................................................ 339

3.3 Wai Ali Kaxai Ke Iya Kare Shari’a: ........................................................ 340

3.4 Wai Dole Ne A Samu Shugaba Ma’asumi!: ............................................ 343

3.5 Wai Ali Ya Fi Sauran Sahabbai – Inji Shi!: .............................................. 345

**4.0 Zango Na Huxu: Hujjojinsu Na Alqur’ani: ............................................. 348**

4.1 Ayar المائدة: ٥٥ ﴿إِنَّمَا وَلِيُّكُمُ اللَّهُ وَرَسُولُهُ وَالَّذِينَ آمَنُوا الَّذِينَ يُقِيمُونَ الصَّلَاةَ﴾: .......................... 348

4.2 Ayar المائدة: ٦٧ ﴿بَلِّغْ مَا أُنْزِلَ إِلَيْكَ مِنْ رَبِّكَ﴾: .................................................. 358

4.3 Ayar Cikar Addini: ....................................................................................... 362

4.4 Ayar النجم: ١ – ٢ ﴿وَالنَّجْمِ إِذَا هَوَىٰ (١) مَا ضَلَّ صَاحِبُكُمْ وَمَا غَوَىٰ (٢)﴾: ......................... 364

4.5 Ayar Tsarkake Ahlul-Baiti: .................................................................... 367

4.6 Ayar ﴿فِي بُيُوتٍ أَذِنَ اللَّهُ أَنْ تُرْفَعَ وَيُذْكَرَ فِيهَا اسْمُهُ﴾ : ............................................. 372

4.7 Ayar Mawaddah: ........................................................................................ 373

4.8 Ayar البقرة: ٢٠٧ ﴿وَمِنَ النَّاسِ مَنْ يَشْرِي نَفْسَهُ ابْتِغَاءَ مَرْضَاتِ اللَّهِ﴾: ............... 376

4.9 Ayar Mubahala: ........................................................................................... 379

4.10 Ayar البقرة: ٣٧ ﴿فَتَلَقَّىٰ آدَمُ مِنْ رَبِّهِ كَلِمَاتٍ فَتَابَ عَلَيْهِ إِنَّهُ هُوَ التَّوَّابُ الرَّحِيمُ (٣٧)﴾: .............. 382

4.11 Ayar البقرة: ١٢٤ ﴿إِنِّي جَاعِلُكَ لِلنَّاسِ إِمَامًا﴾: .................................................. 383

4.12 Ayar مريم: ٩٦ ﴿إِنَّ الَّذِينَ آمَنُوا وَعَمِلُوا الصَّالِحَاتِ سَيَجْعَلُ لَهُمُ الرَّحْمَٰنُ وُدًّا (٩٦)﴾: ..... 384

4.13 Ayar الرعد: ٧ ﴿إِنَّمَا أَنْتَ مُنْذِرٌ وَلِكُلِّ قَوْمٍ هَادٍ (٧)﴾: ........................................ 385

4.14 Ayar الصافات: ٢٤ ﴿وَقِفُوهُمْ إِنَّهُمْ مَسْئُولُونَ (٢٤)﴾: .................................................. 387

4.15 Ayar محمد: ٣٠ ﴿وَلَتَعْرِفَنَّهُمْ فِي لَحْنِ الْقَوْلِ﴾: .................................................. 388

4.16 Ayar الواقعة: ١٠ – ١١ ﴿وَالسَّابِقُونَ السَّابِقُونَ (١٠) أُولَٰئِكَ الْمُقَرَّبُونَ (١١)﴾: ...................... 389

4.17 Ayar ٢٠ التوبة: ﴿ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ بِأَمْوَٰلِهِمْ ﴾: .................... 390

4.18 Ayar Ganawa: ........................................................................................ 391

4.19 Ayar ٤٥ الزخرف: ﴿ وَسْـَٔلْ مَنْ أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ مِن رُّسُلِنَآ ﴾: ................................ 393

4.20 Ayar ١٢ الحاقة: ﴿ لِنَجْعَلَهَا لَكُمْ تَذْكِرَةً وَتَعِيَهَآ أُذُنٌ وَٰعِيَةٌ ﴿١٢﴾ ﴾: .............................. 394

4.21 Surar ١ الإنسان: ﴿ هَلْ أَتَىٰ عَلَى ٱلْإِنسَٰنِ حِينٌ مِّنَ ٱلدَّهْرِ لَمْ يَكُن شَيْـًٔا مَّذْكُورًا ﴿١﴾ ﴾: .............. 395

4.22 Ayar ٣٣ الزمر: ﴿ وَٱلَّذِى جَآءَ بِٱلصِّدْقِ وَصَدَّقَ بِهِۦٓ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُتَّقُونَ ﴿٣٣﴾ ﴾: .......... 399

4.23 Ayar ٦٢ الأنفال: ﴿ وَإِن يُرِيدُوٓاْ أَن يَخْدَعُوكَ فَإِنَّ حَسْبَكَ ٱللَّهُ ﴾: ............................ 400

4.24 Ayar ٦٤ الأنفال: ﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِىُّ حَسْبُكَ ٱللَّهُ وَمَنِ ٱتَّبَعَكَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٦٤﴾ ﴾: ............ 402

4.25 Ayar ٥٤ المائدة: ﴿ يُحِبُّهُمْ وَيُحِبُّونَهُۥٓ ﴾: ...................................................... 403

4.26 Ayar ١٩ الحديد: ﴿ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلصِّدِّيقُونَ ﴾: .................................................. 406

4.27 Ayar ٢٧٤ البقرة: ﴿ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمْوَٰلَهُم بِٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ سِرًّا وَعَلَانِيَةً ﴾: .......... 408

4.28 Ayoyin ﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ﴾: ...................................................... 410

4.29 Ayar ٥٦ الأحزاب: ﴿ صَلُّواْ عَلَيْهِ وَسَلِّمُواْ تَسْلِيمًا ﴿٥٦﴾ ﴾: ................................... 411

4.30 Ayar ١٩ – ٢٠ الرحمن: ﴿ مَرَجَ ٱلْبَحْرَيْنِ يَلْتَقِيَانِ ﴿١٩﴾ بَيْنَهُمَا بَرْزَخٌ لَّا يَبْغِيَانِ ﴿٢٠﴾ ﴾: ............... 413

4.31 Ayar ٤٣ الرعد: ﴿ وَمَنْ عِندَهُۥ عِلْمُ ٱلْكِتَٰبِ ﴿٤٣﴾ ﴾: .............................................. 414

4.32 Ayar ٨ التحريم: ﴿ يَوْمَ لَا يُخْزِى ٱللَّهُ ٱلنَّبِىَّ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَعَهُۥ ﴾: ............................ 416

4.33 Ayar ٧ البينة: ﴿ أُوْلَٰٓئِكَ هُمْ خَيْرُ ٱلْبَرِيَّةِ ﴿٧﴾ ﴾: ............................................ 417

4.34 Ayar ٥٤ الفرقان: ﴿ فَجَعَلَهُۥ نَسَبًا وَصِهْرًا ﴾: ...................................................... 419

4.35 Ayar ١١٩ التوبة: ﴿ وَكُونُواْ مَعَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿١١٩﴾ ﴾: ........................................... 420

4.36 Ayar ﴿وَٱرۡكَعُواْ مَعَ ٱلرَّٰكِعِينَ ٤٣﴾ البقرة: ٤٣: ................................................... 422

4.37 Ayar ﴿وَٱجۡعَل لِّي وَزِيرٗا مِّنۡ أَهۡلِي ٢٩﴾ طه: ٢٩: .................................................... 423

4.38 Ayar ﴿عَلَىٰ سُرُرٖ مُّتَقَٰبِلِينَ ٤٧﴾ الحجر: ٤٧: ................................................ 424

4.39 Ayar ﴿وَإِذۡ أَخَذَ ٱللَّهُ مِيثَٰقَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ﴾ آل عمران: ٨١: ............................................ 428

4.40 Ayar ﴿فَإِنَّ ٱللَّهَ هُوَ مَوۡلَىٰهُ﴾ التحريم: ٤: .......................................................... 430

**5.0 Zango Na Biyar: Hujjojin Shi'ah Daga Cikin Hadissai: ........................... 432**

5.1 Hadisin Liyafar Kiran Jama'a: ................................................................ 432

5.2 Hadisin Ghadir Ba Hujja Ne Ba: ............................................................. 435

5.3 Hadisin Matsayin Ali: .................................................................................. 438

5.4 Wakilcin Ali A Madina: ............................................................................. 441

5.5 Hadisin Wasicci: ......................................................................................... 444

5.6 Hadisin Qulla Zumunci: ............................................................................. 444

5.7 Hadisin Yaqin Haibara: .............................................................................. 446

5.8 Hadisin Tsuntsu:: ......................................................................................... 449

5.9 Hadisin Gaisuwar Sarauta Ga Ali: ............................................................ 450

5.10 Hadisin Amanoni Biyu: ............................................................................ 452

5.11 Wasu Hadisan Qarya: ................................................................................ 453

5.12 Hadisin Kafirta Wanda Ya Sava Ma Ali: ................................................ 455

5.13 Matsayin Hadissan Shi'ah: ....................................................................... 457

6.0 Zango Na Shida: Daga Cikin Dalilan Shi'ah, Xabi'u Goma Sha Biyu Na Ali 458

6.1 Zuhudunsa: ........................................................................................................ 458

6.2 Yawan Ibadarsa: ........................................................................... 465

6.3 Fifikonsa A Fagen Ilimi: ........................................................................ 469

6.4 Kaifin Basirarsa: ........................................................................... 471

6.4.1 Malam Zurqe Bai Ko San Hadisi Ba: ................................................ 472

6.4.2 Wai Ali Ne Ya Qaga Ilimin Nahawu!: ............................................... 473

6.4.3 Fiqihun Ali: ........................................................................... 473

6.5 Jaruntakar Ali Ba Dalili Ce A Nan Ba: ................................................. 473

6.5.1 Ba Don Ali Ne Kawai Aka Ci Badar Ba!: ............................................ 477

6.5.2 Kuma Wai A Hannunsa Ne Aka Ci Nasara A Uhudu: .......................... 477

6.5.3 Ali A Yaqin Taron Dangi (Ahzab): .................................................... 480

6.5.4 Gudunmawar Ali A Yaqin Banun-Nadhir: .......................................... 482

6.5.5 Malam Zurqe Ya Sake Fesa Ta: ........................................................ 483

6.5.6 Gudunmawar Ali A Yaqin Banul-Musxalaq: ....................................... 484

6.5.7 Ali A Ranar Haibara: ........................................................................ 484

6.5.8 Ali A Yaqin Hunainu: ........................................................................ 485

6.6 Kuma Wai, Ali Ya San Gaibi: ............................................................... 486

6.7 Ana Karva Addu’ar Ali: ........................................................................ 488

6.8 Wata Hujjar Banza : ........................................................................... 489

6.9 Wai Ali Ya Yi Yaqi Da Aljannu! : ............................................................ 490

6.10 Rana Ta Sake Hudowa Saboda Ali!: ...................................................... 491

6.11 Wata Kuma Mu’ujizar Sayyidina Ali!: .................................................. 492

6.12 Ali Bai Buqatar Irin Wannan Al’amara: ................................................ 493

**7.0 Zango Na Bakwai: Dalilan Shugabancin Sauran Imamai Cikon Sha Biyu: 495**

7.1 Samun Nassi A Kansa: ................................................................................ 495

7.2 Samuwar Ma'asumai A Kowane Zamani: ............................................... 498

7.3 Darajojin Imamai Goma Sha Biyu: .......................................................... 499

**8.0 Zango Na Takwas: Ayubban Sauran Halifofi, InJi Shi: ........................... 500**

8.1 Wai Abubakar Ba Shi Da Lafiya: ............................................................ 501

8.2 Wai Mubaya'ar Abubakar Ba Ta Yi Ba: .................................................. 504

8.3 Wai Halifofi Uku Jahilai Ne!: .................................................................. 505

8.4 Kuma Wai Halifofi Sun Yi Abin Kunya!: ................................................. 505

8.5 Wai Halifofi Uku Sun Bauta Ma Gumaka: ................................................ 506

8.6 Wai Abubakar Ya Nemi Yin Murabus: ...................................................... 507

8.7 Kuma Wai Abubakar Ya Yi Nadama!: ...................................................... 507

8.8 Wai Abubakar Ya Faxa Gidan Fatima Ba Sallama!: .................................... 508

8.9 Wai Halifofi Sun Fice Daga Rundunar Usamatu!: ....................................... 509

8.10 Wai Abubakar Bai Tava Jagoranci A Zamanin Manzon Allah Ba!: ........... 510

8.11 Wai Manzon Allah Ya Tuve Abubakar Daga Amirul Hajji!: ...................... 510

8.12 Kuma Wai Umar Bai Iya Hukunci Ba!: ..................................................... 512

8.13 Wai Umar Ya Qago Sallar Asham: ............................................................ 513

8.14 Wai Musulmi Sun Haxu A Kan Kashe Halifa Usman!: .............................. 514

**9.0 Zango Na Tara: Rashin Cancantar Abubakar Ga Halifanci A Wurinsu:......... 516**

9.1 Rashin Samun Ijma'i A Kansa: ..................................................................... 516

9.2 'Yan Shi'ah Ba Su Yarda Da Ijma'i Ba :......................................................... 519

9.3 Wai Kuma Al'umma Ba Ta Haxu Kan Abubakar Ba!: .................................. 520

9.4 Wata Suka Ga Ijma'i: ...................................................................................... 521

9.5 Kuma Wai Zaven Abubakar Ya Sava Ma Nassi: ............................................ 522

9.6 Suka Ga Hadisin Koyi Da Abubakar Da Umar: ........................................ 522

9.7 Wai Hijirarsa Tare Da Annabi Ba Daraja Ba Ce! : .................................... 524

9.8 Gaba Ta Koma Baya: .................................................................................... 531

9.9 Babu Shakka Abubakar Ya Damu: ............................................................. 534

9.10 Abubakar Ne Dai Ayar Ke Nufi: .............................................................. 537

9.11 Shi Wannan Ayar Ke Nufi: ........................................................................ 538

9.12 Abubakar Da Manzon Allah A Ranar Badar: ........................................... 542

9.13 Abubakar Ya Yi Hidimar Manzo Da Dukiyarsa: ...................................... 544

9.14 Abubakar Xin Ne Dai Liman: ..................................................................... 547

9.15 Darajojin Abubakar A Cikin Hadissai: ...................................................... 549

## GABATARWAR CIBIYAR AHLUL-BAITI DA SAHABBAI

Godiya ta tabbata ga Allah wanda aikin alheri ba ya kammala sai da taimakonsa. Muna godiya a gare shi bisa taimakon da ya yi mana na kammala wannan aiki mai tarin albarka.

Babbar manufar da aka kafa wannan cibiya a kanta ita ce, bayyana gaskiyar Allah game da kyakkyawar dangantakar da ta wanzu a tsakanin *Ahlul-Baiti,* iyalan gidan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da kuma Sahabbai, wato almajiransa. Babu shakka sanin wannan kyakkyawar dangantaka na qara mana sanin qoqarin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wajen shiryar da al'ummarsa, da nasarorin da ya samu a cikin aikin da Allah ya xora ma sa na yin tarbiyyar jama'arsa. Kamar yadda Allah ya ce:

﴿لَقَدْ مَنَّ ٱللَّهُ عَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ إِذْ بَعَثَ فِيهِمْ رَسُولًا مِّنْ أَنفُسِهِمْ يَتْلُوا۟ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتِهِۦ وَيُزَكِّيهِمْ وَيُعَلِّمُهُمُ ٱلْكِتَٰبَ وَٱلْحِكْمَةَ وَإِن كَانُوا۟ مِن قَبْلُ لَفِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿١٦٤﴾﴾ آل عمران: ١٦٤

*Haqiqa Allah ya yi baiwa a kan muminai a lokacin da ya tayar da manzo a cikinsu, daga kawunansu, yana karanta ma su ayoyin Allah, yana tsarkake su, yana ilmantar da su littafin (Alqur'ani) da Hikima (Sunnah), kodayake sun kasance a cikin bayyanannen vata gabanin haka. Ali Imran: 164.*

Tsarkake su da Allah ya xora wa Manzo yi, shi ne tarbiyyarsu. Don haka duk wata suka ga tarbiyyar tasu to, suka ce ga Manzon Allah xin kansa. Kuma ma dai Alqur'ani ya ba mu tabbacin wanzuwar so da qauna da rahama a tsakaninsu. Kamar in da Allah yake cewa:

﴿مُّحَمَّدٌ رَّسُولُ ٱللَّهِ ۚ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ أَشِدَّآءُ عَلَى ٱلْكُفَّارِ رُحَمَآءُ بَيْنَهُمْ﴾ الفتح: ٢٩

*Muhammadu Manzon Allah ne. Kuma waxanda ke tare da shi masu tsanani ne a kan kafirai, masu jinqayi a tsakanin junansu. Al-Fathi: 29*

Da kuma in da yake cewa:

﴿هُوَ ٱلَّذِىٓ أَيَّدَكَ بِنَصْرِهِۦ وَبِٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٦٢﴾ وَأَلَّفَ بَيْنَ قُلُوبِهِمْ﴾ الأنفال: ٦٢ – ٦٣

*(Allah) shi ne wanda ya qarfafe ka da taimakonsa da kuma muminai. Kuma ya haxa zukatansu. Al-Anfal: 62-63.*

Wannan cibiya ta samu littafin nan na Shehun musulunci Ibnu Taimiyyah daidai da wannan manufa, domin ya bayyana gaskiyar wannan al'amari ta hanyar hujjoji bayyanannu masu qwari.

**Wannan Littafi**

Babu shakka Ibnu Taimiyyah ya yi bajimin qoqari a cikin wannan littafi, kamar yadda ya saba yi a sauran littafansa waxanda suke matsayin taurari a samaniyar ilimin addini. Muna kyautata zaton cewa, babu mai hankali da basira da zai karanta wannan littafi face ya amfana da shi ta fuskar gano bakin zaren duk abubuwan da ake taqaddama a kansu kan matsayin Sunnah da Shi'ah a addini. Malamin ya sanya haquri da juriya kamar yadda ya sa ilimi da basira a cikin mayar da martanin abubuwan da 'yan Shi'ah suke faxa a kan Sahabbai. Ya yi shi ta hanyar tattaunawa yana mai mayar da martani a tsanake kan littafin da jagoran 'yan Shi'ar zamaninsa Ibnul Muxahhir ya wallafa mai suna *Minhajul Karamati Fi Isbatil Imamati.* Malamin ya bi littafin daki-daki yana tattaunawa a kan dalilan da aka kawo.

Da yawan mutane sukan yi zaton cewa, 'yan Shi'ah na riqe da hujjoji ko aqalla shubhohi masu qarfi, waxanda ke da wahalar tunkuxewa in ba ga malamai ba. Amma wanda ya karanta wannan littafi take zai gano lamarin ba haka yake ba. Domin kuwa mawallafin ya tabbatar a aikace cewa, ba su da wata hujja ko guda qwaqqwara. Bil hasili ma, duk a cikin qungiyoyin da ke jingina kansu ga musulunci babu marasa hujja irinsu. Domin su ne waxanda duk hujjar da suka kafa, da an dube ta da kyau ana iya amfani da ita wajen hujjace su. Ya kuma ba da haske game da dabarun da suka cancanta mai tattaunawa da su ya bi don lurar da su gaskiya. Kamar in da ya ke cewa:

> *To, a wajen jayayya, idan musulmi ya tattauna da Kirista ba zai iya faxin wani abu game da Isa Alaihis Salamu ba face gaskiya. Amma in kana son ka fito da jahilcin Kirista da rashin hujjarsa, to, sai ka qaddara jayayyar a tsakanin sa da Bayahude, ka koma gefe ka saurare shi. Idan har Kirista ba zai iya kare Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama ba, to, duk zargin da ya yi masa zai tarar Bayahude yana yi wa Annabi Isah Alaihis Salamu irinsa. Kuma duk hujjar da zai kawo don ya kare Annabi Isah Alaihis Salamu wannan hujjar ta fi kare Annabi Muhammadu Sallallahu Alaihi Wasallama daga shi nasa zargin. Saboda haka, in zargin da Bayahude yake yi wa Annabi Isah Alaihis Salamu qarya ne, to, zargin Kirista ga Annabi Muhammadu Sallallahu Alaihi Wasallama ya fi zama qarya.*
>
> *To, wannan shi ne abin da ke tsakanin Ahlus-Sunnah da 'yan-sha-biyu ga lamarin Abubakar da Ali. Xan Shi'ar ba zai iya tabbatar da imanin Ali ba, da cewa shi xan aljanna ne, ballantana ya tabbatar da shugabancinsa sai fa in ya tabbatar da haka ga Abubakar da Umaru da Usmanu.*

*Don in ba haka ba duk lokacin da ya so ya tabbatar da wata daraja ga Ali, to, dalilai ba sa taimaka masa, kamar yadda in Kirista ya so ya tabbatar da annabcin Isa Alaihis Salamu ba zai iya ba sai in ya yarda da annabcin Muhammadu Sallallahu Alaihi Wasallama, domin dalilai ba za su taimake shi ba.*

*Bisa ga haka, idan ka tattauna da wani daga cikin 'yan-sha-biyu, to, qaddara masa tattaunawar tsakanin sa da Harijawa masu kafirta Ali da Nasibawa masu fasiqantar da shi. Harijawa sun tafi a kan cewa, Ali azzalumi ne, mai neman duniya, wanda ya nemi halifanci da qarfi, ya yaqi mutane a kansa. A garin haka kuwa ya kashe dubun dubatar musulmi, abin da ya hana cin nasarar mulkinsa. Ya kuma kasa samun abin da yake so na kevanta da mulki, sai magoya bayansa suka dare masa, suka yaqe shi har daga qarshe suka kashe shi.*

*To, ka ga wannan magana in qarya ce, to, ba shakka maganar xan Shi'ar a game da Abubakar da Umar ta fi ta zama qarya. In kuma har maganar xan Shi'ar a game da Abubakar da Umar daidai ne, kuma magana ce ta gaskiya, to, lalle ko maganar Harijawa a kan Ali ta fi cancantar zama gaskiya.*[1]

Wannan littafi ya karva sunansa bisa gaskiya, domin mawallafin ya shimfixa qa'idodi masu tarin yawa a cikinsa, masu kuma amfani, waxanda ke bayyana tafarkin Ahlus-Sunnah a cikin sha'anin ilimi da aqida. Dubi waxannan haskakan maganganu nasa a matsayin misalai:

*Ita dai magana duk wanda zai yi ta, wajibi ne ya yi ta akan ilimi da adalci, musamman in ta shafi mutuncin wani mutum musulmi kowane iri ne. Ba daidai ba ne a yi ta a kan jahilci da zalunci, kamar yadda 'yan bidi'a ke yi a ko'ina. Dubi yadda 'yan-sha-biyu ke bijirowa da mutane masu kusanci da juna ta fuskar girma da xaukaka, da zamansu waliyyan Allah, amma sai su raba su; wasu su ce ma'asumai ne da ko rafkanwa xayansu ba ya yi. Sauran kuma su ce masu fajirai ne ko fasiqai ko kafirai. Kai tsaye kana iya gane jahilcinsu da taqin saqar maganarsu. Kamar Bayahude ne ko Kirista, duk sadda xayansu ya buqaci tabbatar da annabcin Musa ko Isah Alahimas Salam, tare da yin suka ga annabcin Muhammadu Sallallahu Alaihi Wasallama, ba zai iya ba, don nan take jahilcinsa da taqin saqar maganarsa zasu fito fili.*
*Da yawa cikin mabiyan Ali da na Usman na da ra'ayin cewa, Ali na da hannu cikin wannan juyin mulki da ya kai ga kashe Usman. Waxannan sun ce Ali na da hannu don ba su son Usman. Suna son su ce ko Ali ma ba ya sonsa. Waxancan su kuma sun ce Ali na da*

[1] Shafi na 80

*hannu don ba su son Alin. Suna son su shafa masa kashin kaji. Amma mafi yawan musulmi sun san qarya vangaroran biyu ke yi.*[1]

*Kasancewar Malam Sa'alabi na cikin malaman da ke amsa sunan Sunnah kawai bai isa hujja akan karva duk maganarsa ko da kuwa tana zancen darajar halifa Abubakar ne, sai fa in an tabbatar da ingancinta. Kamar dai xan Shi'ar yana son ne ya ce, ga wani malami nan daga cikinku na kafa muku hujja da shi, don ya faxi abin da ya zo daidai da ra'ayina. To, ai Ahlus-Sunnah gaskiya suke bi ba malamai ba. To, ta ya ya ruwayar fataken dare, mai maqoshin kolo a ruwaya, wanda ke yaki-halas yaki-haram; da sahihi da la'ifi duk hajarsa ce take zama hujja a kanmu?*[2]

*Kasancewar ana samun qarya da gaskiya da yawa a cikin riwayoyi, ya sa dole a koma ga ma'abuta ilimin hadisi, a matsayinsu na rariya uwar tata a fagen, don a rarrabe tsakanin garin taba da na gero. Kamar yadda ake komawa ga malaman Nahawu don banbancewa a tsakanin Nahawun larabawa da na Ajamawa. Da kuma yadda ake komawa ga malaman Lugga, don tantance abin da yake mallakar luggar da wanda ba mallakarta ba. Da kuma yadda ake tuntuvar malaman waqa da na Xibbu akan abin da ya shafe su. Kowane "Allazi" daga cikin ilimi, da nashi "Amanu" da aka san shi da shi. Wani ko "kafaru" ake samu gare shi. To, malaman Hadisi su ne mafiya girman daraja a kan sauran malamai. Su ne kuma mafiya gaskiya da xaukakar matsayi, da kishin addini.*[3]

*Gaba xayan qungiyoyin musulunci sun yarda da cewa, duk wanda ya yi imani da Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama wajibi ne ya yi wa hakan rakiya da tsare dokoki. Idan kuwa ba haka ba, gobe lahira kashinsa ya bushe Annabi na ji na gani. Akwai daga cikin Shi'ah 'yan sha biyu da ke cewa, da zaran mutum ya so sayyidina Ali Raliyallahu Anhu a zuci to, yana iya aikata duk abin da ya ga dama don ya fi qarfin zunubi. A kan haka kenan, babu wata buqata ta samun wani shugaba ma'asumi a yau, don samun wata falala, domin son da suke ma Ali Raliyallahu Anhu a cewarsu, ya ishe su shinge.*[4]

A cikin lumana, Ibnu Taimiyyah ya warware duk shubhohin da malaman Shi'ah ke kafa hujja da su. Babu zagi babu cin mutunci. Duba waxannan maganganun nasa alal misali:

*Da Annabi Sallallahu Alaihi Wasallam ya yi nufin naxa Ali Raliyallahu Anhu a matsayin Yarima mai jiran gado, waxannan*

1 Shafi na 145
2 Shafi na 371
3 Shafi na 358
4 Shafi na 51

*Sahabbai uku ba zasu musa masa ba. Da kuma qaddarar Allah za ta sa su yi masa musu, da sauran Sahabbai sun shawo kansu. Don gaba xayansu ba su saba da savawa ko bari a sava wa umurnin Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama ba. Ba ka ganin aqalla kashi xaya cikin uku na musulmi sun tallafa ma Ali a wajen yaqar da ya yi ma Mu'awiyah alhalin ba shi da wani nassi da ya sa shi yin haka? Ya kake zato da Ali na da nassi na zama halifa tun farko, amma waxancan suka amshe masa? Nawa ne daga cikin Sahabbai za su mara masa baya a wannan hali?*[1]

*Idan 'yan Shi'ah suka ce, Ali Raliyallahu Anhu bai tava sujada ga gunki ba, saboda ya karvi musulunci tun bai balaga ba. Kuma haka bayan ya musuluntar ma bai yi ba, tunda musulmi ne. Sai mu ce ma su, ai babu wani abin alfahari a cikin wannan. Tunda kowane musulmi haka yake. Da ma shari'a ba ta hau kan yaro ba, balle. Idan kuwa suka ce: A'a, ba muna magana ne a kan bayan musuluntarsa ba, muna yi ne kan kafin haka. To, sai mu ce masu: Wannan kuma sanin gaibu sai Allah. Mu dai ba mu san wannan magana ba. Kuma shi xan Shi'ar da ke faxar wannan magana ba ya daga cikin mutanen da ake shiga xaka da zancensu.*[2]

*Mun yafe wa xan Shi'ar qaryar ijma'i da ya yi. Muna so ya tabbatar mana da maganar ta hanya xaya ingantancciya. Domin wadda Sa'alabi ya ambata mai rauni ce. A cikinta akwai mazajen da ba a yarda da su ba. Balle daxa wanda xan magazili ya riwaito, wanda shi rauninsa ya vaci matuqa. Hadissan da ya tattara a cikin littafinsa, ko kurtu a makarantar ilimin hadisi ya san cewa qaryayyaki ne kawai aka kitsa. To, isnadin nan guda xaya rak ingantacce da muke nema gare shi muna son ya qunshe wannan magana da waccan.*[3]

Shi dai Ibnu Taimiyyah bai tsayar da martaninsa kawai ga wannan xan taliki da yake tattaunawa da shi ba. A'a, ya fuskanci addinin Shi'ar ne ga baki xayansa ya kai masa hari da makaman hujjoji. Saurari abin da yake cewa:

*Duk da yake shi wannan xan Shi'ar sawun varawo ne ya taka; ko da aka haife shi shehunansa sun riga sun yamutsa hazo a fagen tarihin musulunci. Shi kuma da ya zo sai kawai ya hau ba tare da ya tankaxe ya rairaye ba, balle ya kai ga tsagwaron gaskiyar da ma'abuta ilimi manya da qanana suka sani a yanke.*[4]

Mawallafin ya kasance a cikin hattara sosai game da qarairayin da aka jingina ga Ali don a bajintar da shi. A irin waxannan wurare in babu cikakkiyar hattara sai a

[1] Shafi na 508-509
[2] Shafi na 383
[3] Shafi na 350
[4] Shafi na 510

shiga rigar mutuncin Alin, wanda kuma ba shi ne manufa ba. Yi nazarin in da yake cewa:

> *Amma cewar da xan Shi'ar yayi Ali Raliyallahu Anhu bai tava bugun wani abu da takobinsa ba face ya gama da shi. Ba mu da masaniya akan ingancin wannan* magana *ko rashin ingancinta. Babu wata riwaya ingantatta a hannunmu da za mu iya rosa wannan da ita. Amma da za'a sami wani mutum shi kuma ya ce Khalidu ne da Zubairu da Bara'u xan Malik da Abu Dujanata da Abu Xalhata da makamantansu waxanda ba su tava bugun wani abu da takobinsu ba face sun gama da shi, ka ga an yi kunnen doki kenan. Musamman da yake kasancewar irin su Khalidu xin, da shi Bara'u mafi shahara da wannan irin jaruntaka kamar yadda masana tarihi za su iya faxa. Don kuwa har an riwaito cewa, Annabi Sallallahu Alaihi Wasallama ya ce: "Khalidu wani takobi ne daga cikin takubban Allah, wanda Allah ya zare a kan mushrikai".*
>
> *Babu wanda zai ji wani qaiqayi ko ya yi wani kokwanto, idan aka ce, wanda Manzon Allah ya siffanta da kasancewa takobin Allah, ba ya saran abu face ya gama da shi. Aka kuma taras da cewa Khalidun nan ya kashe kafirai ba adadi a fagen fama. Kuma har ya koma ga Allah bai tava gudu daga wurin yaqi ba. Wannan* magana *ta fi qanshin gaskiya, da an jingina ta gare shi.*[1]

Ka ga a nan ya yi qoqarin fidda kansa ga abin da babu da tabbaci a cikinsa. A wurare da dama zaka iske ya yi irin wannan. Kamar in da mawallafin wancan littafin ya ce, wai Abubakar ya nemi a yi ma sa murabus, kuma wai, wannan ya nuna daman can shi bai cancanta ba. Sai Ibnu Taimiyyah ya ce:

> *Kamata ya yi marubucin ya bayyana ingancin wannan magana. Idan kuwa ba zai iya ba, to ya sani ba duk abin da aka riwaito ne gaskiya ba. Kuma saqar duk da aka kitsa a kan zance da bai inganta ba, ita ma hakan.*
>
> *Abu na biyu: Idan ta tabbata cewa, Abubakar Raliyallahu Anhu ya faxi wannan magana, babu mai ikon ce masa don me? Domin kuwa babu wani dalili da zai hana a yi masa murabus xin matuqar ya nemi hakan don wani dalili na qashin kansa. Mu dai ba mu da wata masaniya a kan ya nemi murabus ko bai nema ba, balle mu ga wurin vata lokaci a kan wannan batu.*[2]

Mawallafin ya wofintar da jimillar hajar ta 'yan-sha-biyu, mafi yawan lokuta a cikin ruwan sanyi. Amma ya kan xan tsananta harshe a wani wurin. Kamar in da yake cewa:

> *A kan haka ne jahilcinsu da zaluncinsu suka gagari yawun alqalami siffantawa. Domin sun kasance suna godogo da*

[1] Shafi na 475
[2] Shafi na 506

*riwayoyin qarya da ruxaxxun lafuzza da mummunan qiyasi, suna kuma ji da iqrarin cewa riwayoyi ne na gaskiya, kai mutawatirai ma. Kuma lafuzzan can nasu nassosa ne qwarara, ga su sarai. Kuma duk hujjar da suka bari ta hankali, hujja ce gar.*[1]

Haka dai mawallafin ya ci gaba da fexe gaskiyar Allah qarara dangane da lamarinsu:

*Wannan feshin qarya ba wani abu ne ba a wurin waxannan mutane, domin kuwa jini da tsokarsu da qarya suka tofo. Hakan ta sa kodayaushe suke qoqarin musanta abin da duniya ta gama tabbatar da kasancewarsa gaskiya, tare da qoqarin tabbatar da abin da duniya da lahira an yarda da kasancewarsa toka.*[2]

Ya dai kai matsaya ta qarshe a kansu ne in da ya ce:

*Babu wata qungiya ta 'yan bidi'a da za a ce gara 'yan-sha-biyu da su.*[3]

Wani lokacin kuma ya kan shaci fushi don kishin kariyar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ko iyalansa da Sahabbansa daga cin mutuncin da 'yan-sha-biyun suka yi ma su. Mafi nauyin maganar da ya furta a cikin wannan littafi ita ce maganar da ya yi a kan wautar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da 'yan Shi'ah ke yi cewa wai, ya yi gudun hijira tare da Abubakar *Raliyallahu Anhu* don bai san shi maqiyinsa ne ba:

*Ka ga dole ne duk wanda zai riqa a matsayin aboki a cikin irin wannan tafiya ya kasance soyayyarsa da shi ta shafe ta kowa. Hakan kuwa ta tabbata, don ya nuna masa irin baqin cikin da yake ciki a kan halin da ya shiga. Amma kuma sai duk hakan ta zama busar iska; ya kasance yana qiyayya da shi a zuci? Bayan kuma shi ya sakankance har ga Allah cewa, shi masoyinsa ne?*

*Ko shakka babu, babu wanda zai yi wannan zavin tumun dare sai mafi wauta da jahilcin mutane. Allah kuwa ya qasqanta duk wanda ya jingina irin wannan wauta da jahilci ga Manzonsa, kuma mafi cikar halittarsa ga hankali da ilimi da gogewa.*[4]

## Aikinmu a Cikin Wannan Littafi

Littafin da muka dogara da shi a wannan aiki shi ne taqaitaccen *Minhajus Sunnah* na larabci, wanda Sheikh Abdallah Al-Gunaiman, wani malami mai koyar da Tauhidi a masallacin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi. Wanda kuma aka buga shi a maxaba'ar Darus Siddiq da ke *San'a'a* ta qasar Yaman, a shekarar 1426H/2005M. Malamin ya bi sawun Imamuz Zahabi ne wajen taqaita littafin na Ibnu Taimiyyah akan abin da ya shafi aqidar Shi'ah ita kaxai.

A haqiqanin gaskiya ba fassara ce kaxai aikin da muka yi wa wannan littafi ba. Domin kuwa mun duba zubin littafin da tsarin tafiyarsa da kanun bayanansa duk mun yi gyara mai ma'ana a cikinsu. A wasu lokutan mukan buqaci koma ma asalin

---

[1] Shafi na 374
[2] Shafi na 527
[3] Shafi na 51
[4] Shafi na 528

littafin na Ibnu Taimiyyah mai sifili takwas don tantance tushen maganar da yadda aka faxe ta, ko don cike wani givi da aka bari.

Game da fassara xin ita kanta, mun bi tsarin da muka saba da shi a wannan cibiya na lizimtar bayar da ma'anar magana kamar yadda mai ita ya faxe ta ba tare da qari ko ragi ba. Mukan kuma yi qoqarin kusantar da ma'anar ga mai karatun Hausa, ta hanyar lulluve ta da nau'oin adon magana da irin namu salo na Hausawa a maimakon lizimtar kalimomin da marubucin ya yi amfani kawai da su da larabci. A duk lokacin da mawallafin ya bayyana qwarewarsa a harshen larabci sai mu kuma mu bayyana tamu qwarewa a harshenmu na Hausa; sai mu haxiye maganar tasa, mu fito da ita da namu salo kamar daxai ba fassara ce muke yi ba. Wannan ita malamai suka sani da suna Fassara mai 'yanci. Bari mu xan ba da 'yan misalai ga masu karatu waxanda suka san harsunan biyu don gane muhimmancin bin wannan tsari da muka yi.

Ibnu Taimiyyah ya ce:

وإذا قام الدليل القطعي على ثبوت إمامتهم، لم يكن علينا أن نجيب عن الشبه المفصلة، كما أن علينا أن نجيب عما يعارضه من الشبه السوفسطائية. وليس لأحد أن يدفع ما علم يقينا بالظن.

Ga yadda muka fassara shi:

> *Da zarar kuwa irin wannan dalili yankakke ya tabbata, a kan dacewar halifofin da shugabancin, kamar yadda ya tabbata a wurinmu, to, babu buqatar sai mun ci dugadugan sauran qyaleqyalin da suka yi wa qaryar. Tsayawa bayar da amsa a kan waxannan wofintattun Shubuhohi, bayan an rosa ginshiqansu, vata lokaci ne. Babu wani mutum da ke iya rosa masaniyar da aka sakankance da ita, alhali makamin da ke hannunsa sungumin ragga ne kawai.*[1]

Sai kuma in da ya ce:

الجواب من وجوه: أحدها: قد تقدم بيان بطلان كل ما دل على أنه إمام معصوم قبل الثلاثة. الثاني: أن النصوص إنما دلت على خلافة الثلاثة قبله. الثالث: أن يقال: الإجماع المعلوم حجة قطعية لا سمعية، لا سيما مع النصوص الكثيرة الموافقة له، فلو قدر ورود خبر يخالف الإجماع كان باطلا: إما لكون الرسول لم يقله، وإما لكونه لا دلالة فيه. الرابع: أنه يمتنع تعارض النص المعلوم والإجماع المعلوم، فإن كليهما حجة قطعية، والقطعيات لا يجوز تعارضها لوجوب وجود مدلولاتها، فلو تعارضت لزم الجمع بين النقيضين. وقد دل الإجماع المعلوم والنص المعلوم على خلافة الصديق رضي الله عنه وبطلان غيرهما، ونص الرافضة مما نحن نعلم كذبه بالاضطرار، وعلى كذبه أدلة كثيرة.

Ga yadda muka fassara maganar:

[1] Shafi na 500

*Mun riga mun warware duk wata magana da ke cewa, dole ne Ali ya zama halifa kafin halifofi uku da suka gabace shi. Domin kuwa gaba xayan nassosan da suka tuzgo akan shugabanci na tabbatar da halifancinsu ne kafin shi. Kuma amon ijma'i akan haka ya game duniya. Hujja ne kuma yankakka, ba naji-naji ba. Musamman kuma da aka sami nassosa da dama suka mara masa baya. Da wani labari zai tuzgo ya tunni wannan ijma'i, to, sai a tuhumce shi don ya tabbata zakka. Lalle ne kuma a qarshe a taras cewa, labarin qanzon kurege ne.*
*A qa'ida, ba ta yiwuwa ingantaccen nassi ya ci karo da lafiyayyen ijma'i. domin kuwa ko wanne daga cikinsu hujja ce yankakka. Su kuwa yankakkun hujjoji, amanar da ke tsattsage da cikannansu ta dalilai da ke tabbatar da ingancinsu ba ta bari su yi kabra da juna. Da wata 'yar hayaniya za ta faru tsakaninsu sai dai a sasanta su amma ba dai rabuwa ba.*[1]

Ga kuma wata magana tasa in da yake mayar da martani a kan wata falala da suka ce ta cancantar da Ali zama halifan farko. Ita ce wai, tauraro ya sauko qasa saboda shi. Ga abin da ya ce da larabci:

لم ينقض قط كوكب إلى الأرض بمكة ولا بالمدينة، ولا غيرهما. ولما بعث رسول الله صلى الله عليه وسلم كثر الرمي بالشهب، ومع هذا فلم يتزل كوكب إلى الأرض. وهذا ليس من الخوارق التي تعرف في العالم، بل هو من الخوارق التي لا يعرف مثلها في العالم، ولا يروي مثل هذا إلا من هو من أوقح الناس، وأجرئهم على الكذب، وأقلهم حياء ودينا. ولا يروج إلا على من هو من أجهل الناس وأحمقهم وأقلهم معرفة وعلما.

Ga yadda muka fassara ta:

*Babu inda tarihi ya nuna tauraro ya tava faxowa qasa a Makka ko Madina, ko wasu garuruwa kusa da su. Eh, gaskiya ne, lokacin da aka aiko Annabi Sallallahu Alaihi Wasallama ana yawaita jifa da taurari. Amma duk da haka ba a samu cewa, tauraro ya tava saukowa qasa ba. Da hakan ta zama wani abu na keta hankali, kuma sananne a duniya. Hasali ma kai! Wani abu ne da bai tava faruwa a faxin duniya ba, balle ya zama abin kakabi. Kuma babu ma wanda irin wannan labari zai riqa fitowa bakinsa sai mafi wauta daga cikin mutane, wanda kuma ya ce wa musailamu cas, saboda cikar rashin kunya da wasa da addini. Kamar kuma yadda babu wanda zai saurare shi, balle har ya yarda da shi, sai mafi jahilci da wauta daga cikin mutane, wanda wayewarsa da ilimin addini ba ta cika cikin cokali ba.*[2]

---

[1] Shafi na 521
[2] Shafi na 365

Muna fatar samar da wannan littafi a cikin harshen Hausa ya kasance babbar gudunmawa ga yunqurin da ake yi na yaxa Sunnah da warware rikittan da aka tayar a cikin tarihin magabata.

## RAYUWAR IBNU TAIMIYYAH[1]

### Wane ne Ibnu Taimiyyah?

Sunansa Ahmad xan Abdulhalimu xan Abdussalami xan Abdullahi xan Haliru xan Muhammadu xan Haliru xan Aliyu xan Abdullahi. Ya shahara da sunan *Ibnu Taimiyyah* saboda kakarsa da ake kira Taimiyyah. Ana kuma ce ma sa "Majduddini". Sannan ana ce ma sa "Numairi" saboda shi xan qabilar Banu Numairi ne. Ana ce ma sa kuma "Harrani" saboda Harrana ne garin da aka haife shi. Sannan ana ce ma sa "Dimashqi" saboda a garin Dimashqa ne ya girma, ya yi karatu.

### Asalinsa

Ibnu Taimiyyah xan asalin qasar Turkiyyah ne. Don an haife shi a garin Harrana wadda take arewa maso gabascin qasar ta Turkiyyah. An haife shi ne a ranar litinin 10 ga watan Rabi'ul Awwal 661H. Amma bayan shekaru shida sai iyayensa suka yi hijira daga qasar zuwa qasar Siriya in da suka sauka a babban birnin Dimashqa, hedikwatar Sham. Dalilin hijirar tasu kuwa shi ne kauce ma fitinar 'yan Tattar waxanda suka auka ma garuruwan musulmi suka yawaita varna da zubar da jinainan bayin Allah ba li ba la.

Game da mahaifansa kuwa, shi xan gidan malanta ne. Domin ya sami kansa a tsakanin iyaye da kakanni da 'yan'uwa ma'abuta karatu. A lokacin da zasu yi hijira kuwa babu abin da ya wahalar da su kamar littafai da ke tare da su masu xinbin yawa, ga su kuma suna gudun maqiya. Ba domin kiyayewar Allah ba ma ba zasu tsira da rayukansu zuwa Sham ba.

Isarsu qasar Sham ke da wuya mahaifin Ibnu Taimiyyah Shihabuddini ya fara koyarwa da wa'azi a babban masallacin Jum'ah na Dimashqa wanda ake kira *Al-Jami'ul A'azam* masallaci mafi girma. Daman shi fitaccen malamin furu'a ne a mazahabar Hambaliyyah. Nan take aka shugabantar da shi ga babbar makarantar hadisin nan da aka sani *Darul Hadis As-Sukkariyyah*, aka kuma ba shi gida a cikin makarantar in da nan ne xansa Ibnu Taimiyyah ya girma.

Kafin haka, kakan Ibnu Taimiyyah Majduddini sanannen malami ne da ya yi wallafe-wallafe a fannin hadisi da Usulul Fiqhi. Shi ne mawallafin littafin nan na *Muntaqal Akhbar* wanda Imamus Shaukani ya yi wa sharhi a cikin *Naulul Auxar.*

Haka ma baffansa Fakhruddini, malami ne fitacce da ya wallafa babban littafin Tafsirin Alqur'ani. Shi ne kuma wanda ya gaji Ibnul Jauzi a kujerarsa ta karantarwa da babban mimbarinsa na Bagadaza. Kuma Ibnu Taimiyyah ya yi karatu a wurinsa.

---

[1] Wannan tarihin mun rubuta shi a gurguje, kuma a taqaice ranar da za a kai littafin wurin xab'i. In Allah ya so za mu wallafa cikakken tarihin malamin a wani littafi mai zaman kansa in da za mu faxaxa magana akan aqidarsa da gudunmawarsa a wajen kyautatar da fahimtar musulmi ga Alqur'ani da hadisi. Shugaban Kwamitin Fassara.

**Tashinsa da Iliminsa**

Ibnu Taimiyyah ya tashi a gidan ilimi kamar yadda muka gani. Ya kammala hardar Alqur'ani a cikin quruciya. Sannan ya kula da sanin ilimoman Fiqihu da Hadisi da Tafsiri da Arabiyyah. Ya soma karantarwa da fatawa da rubuta littafai da tattaunawa da malamai *Munazara* tun bai wuce shekaru ashirin ba. Koda ya cika shekaru talatin an fara yi masa laqabin *Mujtahidi* kuma "Mai raya Sunnah".

Yana da matuqar wuya a iya sifaita baiwar da Allah ya yi wa Ibnu Taimiyyah ta fuskar ilimi. Masu ba da labarinsa na ganin kasawarsu wajen bayyana irin hikimomin da ke tattare da shi ta wannan haujin. An lisafta malaman da ya gurfana a gabansu don xaukar karatu aka tarar sun zarce malamai xari biyu. Akwai kuma littafan da ya karanta su sau da yawa a wurare daban-daban kamar *Musnad* na Imamu Ahmad.

Game da nasa littafai shi kuma, Ibnu Taimiyyah ya wallafa sama da littafai hamsin a fannona daban-daban na addini, banda qananan wallafe-wallafensa da aka tara cikin *Majmu'ul Fatawa* mai sifili talatin da bakwai. Ya ishi mai karatu misali abin al'ajabi cewa, duk da yake Ibnu Taimiyyah bai wallafa Tafsirin Alqur'ani ba, amma malamai daga bisani sun wallafa shi daga cikin littafansa. Ma'ana an tattara wuraren da ya yi sharhi akan ayoyin Alqur'ani daga cikin littafansa a tsakankanin maganganunsa da kafa hujjojinsa, sai ga shi an samu kusan kammalallen Tafsiri mai Mujalladi huxu.

**Mujaddadi Ibnu Taimiyyah**

Muna iya cewa, Allah gwanin sarki ya tashi Ibnu Taimiyyah ne a wani lokaci da buqatar irinsa ta yawaita. Don kuwa a wancan lokaci al'umma tana fama da matsaloli da rikitta da tashin hankula na ciki da na waje. Daga cikin gida musulmi na fama da rabuwar kai, da yawaitar qungiyoyi da yaxuwar bidi'ah da raunin ilimin furu'a. Ga kuma lalacin da ya yaxu a cikin jama'a da zaluncin sarakuna da kwaxayin malamai. Tsibbace-tsibbace da bokanci da duba sun zama gama-gari a cikin al'umma. Daga waje kuma 'yan mishan sun kai ma musulmi farmaki, 'yan Shi'ah masu kiran kansu *Faximawa* sun haxa kai da su. Sannan ga Tattar sun shelanta mummunan faxa da musulunci da musulmi a duk in da suke a wancan lokaci.

Shaihun musulunci ya fuskanci duka waxannan matsaloli da nufin magance su. Ya kuma samu taimakon Allah matuqa a wajen cimma wannan gurin nasa. Ga shi kuma Allah ya ba shi makamai da ya wuyata a samu wanda ya yi tarayya da shi a dukansu. Mutum ne da aka sifaita shi da kaifin basira da qarfin qwaqwalwa, har wasu ma na ganin bai tava sanin abu ya manta da shi ba. Yana da qarfin tuna ayoyin Alqur'ani da nassosan hadissai da maganganun malamai na kowane fanni. Don haka ya kasance mai kaifin hujja wadda take yanke wuyan abokin gaba nan take. Ga shi kuma jarumi da ba ya tsoron ko-ta-kwana. Don haka ba ya da ja da baya ga abin da ya sa gaba. Sannan yana da kwarjini a idon jama'a da kyawawan xabi'u da suka daxa soyar da shi ga mutane. Ga shi mutum mai kishin gaskiya da qoqarin yaxa ta. Haxa da halinsa na gudun duniya da rashin kula da jin daxinta. Irin wannan malami Allah ya xora shi a kan kyakkyawar hanya irin ta Annabawa wane irin canji kake tsammanin al'umma ba za ta ci moriyarsa ba ta hanyarsa?

Xan Taimiyyah nan take ya rurrusa aqidun da suka zame ma musulunci tsutsar goro ta hanyar rubuce-rubucensa da wa'azozansa da karantarwarsa. Ya kece raini a

wajen wargaza aqidun Yahudawa da na ‘Yan mishan. Ya yi faxa da qungiyoyi mabiyan son zuciya irin mulhidai da zindiqai da ‘yan Shi’ah da waxanda suka wuce wuri a Sufanci. Ya yi kira ga koma ma littafin Allah da Sunnar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba tare da ta’assubanci ga wani mutum ko qungiya ko mazhaba ba.

Sa’annan ya kira sarakuna da talakawa zuwa ga yaqar kafirai waxanda suka keta hurumin musulmi, musamman dai Tattar. Ya kuma fita ya yi yaqi a matsayin xaya daga cikin sojoji.

Tare da haka kuma Ibnu Taimiyyah ya kafa wata makaranta da Allah ya yawaita almajiranta tun daga wancan zamani har zuwa yau, kuma tana ci gaba da bunqasa har a naxe qasa. Wannan makaranta tasa tana mutunta magabatan Sahabbai da Tabi’ai da waxanda suka biyo bayansu, da shugabannin mazhabobi, tana kuma la’akari da ra’ayoyansu da fatawoyinsu baki xaya. Tana kuma rinjayar da nassi ingantacce idan ya zo daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a kan maganar kowa kome darajarsa. Wannan makaranta dai tana da xaruruwan littafai da dubaiban malamai a cikinta. Dukkaninsu suna jingina kansu ga Sunnah da biyar magabata ba ga shi Ibnu Taimiyyah xin ba.

**Jarabawar Da Ibnu Taimiyyah ya Gamu da Ita**

Yana da wuya Allah ya xaukaka wani bawansa ba tare da ya gamu da wasu jarabawoyi ba a rayuwarsa. Wannan ita ce sunnar Allah ga Annabawa da malamai mutanen kirki.

Shehun musulunci ya gamu da jarabawoyi da dama a sakamakon jihadinsa na makami da na alqalami waxanda suka dagula ma sa jin daxin rayuwa. Zamu faxi wasu daga cikinsu a taqaice kamar yadda suka zo a tarihinsa daga littattafai da dama.

A shekarar 696H ya gamu da qyashin abokan tafiya, malamai, waxanda suka xauki littafinsa *Al-Fatwal Hamawiyyah* suka kai qorarsa da shi a wurin mahukunta. Sun bi duk hanyoyin da suke iyawa wajen murxa maganarsa da ba ta irin ma’anar da suke so su jingina ma sa. A wannan lokaci sarki Saifuddin Jagan ya goyi bayan Ibnu Taimiyyah, ya kuma husata da waxanda suka kafa adawa da shi. Don haka wannan jarrabawa ba ta daxe ba ta kuranye.

A shekarar 705H lokacin da farin jinin Ibnu Taimiyyah ya gama bayyana, bayan an ga rawar da ya taka a yaqin da aka yi da Tattar, har kuma ya samu kusanci da hukuma abin da ya ba shi damar sa a kawar da wasu varnace-varnace. Nan take sai qurjin hasada ya sake vallewa a zukatan wasu malamai daga cikin sufaye. Sai wani malami da ake kira Nasrul Mambiji da wani malami bamalike ana ce ma sa Ibnu Makhluf suka tafi hedikwatar sarauta da ke qasar Masar suka kai qarar Ibnu Taimiyyah suna tuhumar sa da gurvata aqidun jama’a. Suka kafa hujja da littafinsa na *Al-Aqidatul Wasixiyyah.* A nan ma sarki ya ba da umurni aka zaunar da shi tare da manyan malamai in da aka karance littafin nasa, daga qarshe kuma aka barrantar da shi daga sava ma magabata. Sai ma a wannan karon ya samu takardar yabo daga Sarkin Musulmi.

Wata xaya bayan faruwar wannan, sai waxannan malaman suka sa sarki ya rubuta ma sa wata takarda ana neman sa da zuwa Misra don ya bayyana a gaban sarki. A wannan karon da tuhumar yana neman sarauta! An dai zaunar da shi a gaban Ibnu Makhluf don ya yanke ma sa hukunci, abin da xan Taimiyyan ya qi yarda da shi,

kasancewar shi ne abokin husumar da ya kai qararsa. Shehul Islami sai da ya share wata goma sha biyu cur a gidan kaso kafin a nemi ya fita, in da shi kuma ya qi fita ya ce, sai an bayyana ma sa laifinsa. Daga qarshe ya fita daga kurkukun bayan ya cika wata goma sha biyar da sati biyu bisa ga nacewar wani basaraken garinsu.

Wata bakwai bayan fitowarsa sai aka sake mayar da shi a cikin watan Shawwal na 707H saboda ya ci gaba da zama a Masar mutane na amfana da shi. A wannan karon sai ya kasance mutane suna tururuwa a gidan kaso don gaishe shi da yin fatawa a wurinsa, abin da ya daxa cinna wutar gaba a tsakaninsa da waxanda ke biyar sa da baqar yadiya.

Bayan fitowarsa ma, xan Taimiyyah bai fasa abin da yake yi na karantarwa da fallasa miyagun aqidu ba. Wannan ya sa aka xauke shi daga Alqahira zuwa Iskandariyyah da nufin ya haxu da 'yan dabar garin su kashe shi. Ana haka ne sai aka samu canjin gwamnati lokacin da sarki Muhammad xan Qalawun ya sake koma ma kujerar sarauta sai ya mayar da Shehul Islami zuwa hedikwatar ta Masar. Daga nan kuma suka fita a shekarar 712H da nufin yaqar kafiran Tattar, sai Allah ya mayar da maqiyan garuruwansu ba tare da an yi yaqi ba. Don haka, sai Ibnu Taimiyyah ya koma gida Sham, in da ya haxu da tarbo wanda ba a tava ganin irinsa ba, bayan ya yi shekara bakwai da sati bakwai a qasar Masar tun wancan kiran da aka yi ma sa.

Ko bayan komawarsa gida Shehul Islami ya ci gaba da samun matsaloli da malamai masu qaramin sani da taurin kai. Kamar yadda suka yi cah a kansa wai don ya ce, in mutum ya yi rantsuwar saki kaffara kawai zai yi, aurensa na nan. Haka ma don cewar da ya yi saki uku na komawa xaya idan an yi su zama guda. Waxannan malamai ba su samu sukuni ba sai da suka sa aka hana shi fatawa a shekarar 719H.

A shekara ta 720H aka sake iza qeyar babban malamin zuwa gidan kaso in da ya share wata biyar da kwana goma sha takwas.

A shekara ta 726H wasu alqalai sun tsoma bakinsu a cikin rikicin Ibnu Taimiyyah da maqiyansa, in da aka wallafa wata fatawa ta qarya aka jingina ta gare shi, wai ya haramta ziyarar qabarin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da na sauran Annabawa. Alhalin shi kuwa ya rarrabe tsakanin ziyararsu ne ita kaxai da kuma haxa ta da yin tafiyayya. Ya labarta savanin magabata a kanta, sannan ya nuna karkata ga hanawa idan ya kasance an yi tafiyayya saboda ita. Ya kuma bayyana hujjojinsa na ingantattun hadissai. Wannan rikicin ma dai sai da ya sake mayar da wannan bawan Allah a gidan maza, in da ya samu damar da ya yawaita wallafe-wallafe gami da bautar Allah Ta'ala.

A shekara ta 728H aka fitar da duk littafan da ke tare da shi da alqalumma da tawadar da aka samu a wurinsa, saboda wani malami da ake kira Ikhna'i ya kai qarar sa, don ya yi ma sa raddi, kuma wai ya jahiltar da shi. A nan ya zama dole Ibnu Taimiyyah ya haqura ya duqufa ga zikiri da sallah da karatun Alqur'ani da yake waxannan suna a kansa tun zamanin quruciya.

**Rasuwarsa**

Allah ya karvi ransa a gidan maza na birnin Dimashqa yana da shekaru 67 waxanda suke cike da karantarwa da haquri da jihadi. Ya rasu kafin wayuwar garin litinin 20 ga watan Zul Qi'ida 728H.

Bai yi aure ba ballantana ya bar zuri'a. Bai kuma tava furta kalima xaya da take nuna rashin sha'awarsa ga auren ba. To, ko me ya hana shi cin moriyar wannan Sunnah? Sanin gaibu sai Allah.

**Littafan da Aka Duba Don ba da Tarihinsa**

*Al'Uqudud Durriyyati Min Manaqibi Shaihil Islami Ibni Taimiyyati* na Muhammad xan Ahmad xan Abdulhadi, tahaqiqin Muhammad Hamid Al-Faqi, bugun Darul Katib Al-Arabi.

*Al'A'alamul Aliyyati* na Bazzar, tahaqiqin Zuhair Shawish, bugun Al-Maktabul Islami, Beirut, Lebanon.

*A'ayanul Asri* na Ibnu Aibak As-Safadi, tahaqiqin Ali Abu Zaidah da wasu, bugun Darul Fikri, Beirut, Lebanon.

*Ad-Durar Al-Kaminatu Fi A'ayanil Mi'ati As-Saminti,* na Hafiz Ibnu Hajar Al-Asqalani, tahaqiqin Sayyid Jad Alhaq, bugun Jami'ar Ummul Qura, makka, Saudi Arabia.

*Buhus An-Nadwatil Alamiyyati An Shaihil Islami Ibni Taimiyyati,* tahaqiqin Muqtada Hasan, bugun Dar As-Sami'i.

*Da'awatu Shaikhil Islami Ibni Taimiyyata Wa Asaruha Fil Harakatil Islamiyyatil Mu'asirati,* na Salahuddin Maqbul, bugun Majma'ul Buhusil Ilmiyyati, New Delhi, India 1412H/1992M.

*Dhailu Xabaqatil Hanabilati,* na Hafiz Ibnu Rajab Al-Hambali, tahaqiqin Muhammad Hamid Al-Faqi, bugun Darul Ma'arifati, Beirut, Lebanon.

*Shajaratuz- Zahab Fi Akhbari Man Zahab,* na Ibnul Imadi Al-Hambali, bugun Darul Fikri, Beirut, Lebanon.

*Shaikhul Islami Wa Juhuduhu Fi Ilmil Hadis,* na Firiwa'i, bugun Darul Asimati.
*Husulul Ma'amul Min Kalami Shaikhil Islami Ibni Taimiyyata Fi Ilmil Usul,* na Abdurrahman xan Abdullahi Al-Amir, bugun Darul Waxan, Riyadh, Saudi Arabia, 1423H/2002M.

*Ibnu Taimiyyah: Hayatuhu Wa Asruhu,* na Imam Muhammad Abu Zuhrata, bugun darul Fikril Arabi, Alqahira, masar. 1898H/1974M.

## Godiya

Wannan aiki ya xauki tsawon shekaru da dama, amma a wannan shekara da muke cikinta ta Hijirar 1429 ya daxa kankama sosai. Kuma a tsakkiyar aikin ne Allah ya karvi xaya daga cikin masu himma a aikin, shi ne Dr. Ibrahim Bello wanda ya ba da lokacinsa da kuzarinsa sosai don ganin nasarar aikin, sai dai ajali ya riske shi tun bai ko gama kabbarar harama a cikin aikin ba. Muna roqon Allah ya isar da ladarsa ta wannan aikin don ta zamo haske a cikin qabarinsa, ya kuma tara mu da shi a Darus-Salami.

Ya zama tilas a kan wannan cibiya bayan godiya ga Allah, ta yi kevantacciyar godiya ga kwamitin da ya yi aikin na fassara, musamman sakatarensa Alhaji Aliyu Rufa'i wanda himmarsa a aikin ta zarce ta kowa. Ya kuma ba da gudunmawa mai tarin yawa a wajen fassarar ita kanta, sannan ya taimaka ainun a wajen bitar da ta share sama da watanni uku. Haka kuma qwarewarsa a sanin qa'idojin rubutun Hausa ta taimaka mana matuqa. Ba mu da wata sakayya a gare shi sai addu'a; Allah ya sa aikin ya zamo sanadin tsira. Sai kuma Mal. Aminu Ibrahim Maru da Sheikh Usman Sarkin Vurmin Jabo waxanda da su ne aka aza harsashin aikin tun da farko. Muna roqon Allah ya yi musu sakayya kyakkyawa.

Sai cibiyar fassara da take Runjin Sambo a qarqashin jagorancin Dr. Tahir Muhammad Argungu. Su ma muna godiya a kan nasu qoqari.

Gudunmawar masu saka aikin a cikin na'ura mai qwaqwalwa ita ma ba abar mantawa ce ba. Waxannan sun haxa da Al-Irshad Computers na Mal. Aminu Mustafa Digar Agyare da Aliyu Kambaza Business Centre da ke kan titin Amir Yahaya duk a nan Sokoto.

A can kuma qasar Masar in da aka buga littafin Alhaji Uba Ahmad Ibrahim, wakilin gidan rediyon doce-belle ne ya yi tsaye don ganin aikin ya tafi daidai bisa haruffan Hausa, da kuma daidaita ayoyin Alqur'ani bisa haruffan xab'i na birnin Madina. Allah ya saka ma su ga baki xaya da mafificin alherinsa.

Wannan gabatarwa ba za ta kammala ba sai mun miqa godiya ga jagororin wannan Cibiya da waxanda ke taimaka ma ta ta fuskoki daban-daban. Allah ya ba kowa ladar qoqarinsa, ya kuma xora mu bisa shiriya a cikin zantukanmu da ayyukanmu.

Daga qarshe ina miqa godiya tare da yabawa ga uwargidana Mamar Mu'azzam a kan bitar da ta yi wa littafin daga bisani, da gyare-gyaren da ta yi masu ma'ana.[1]

Allah ya daxa tsira da aminci ga shugabanmu Muhammadu da iyalansa da Sahabbansa baki xaya. Alhamdu Lillah.

Baban Ramlatu,
Muhammad Mansur Ibrahim
Sokoto.
24 ga Rajab 1429H (26-07-2008M)

---

[1] Haryanzu dai ga shi za mu miqa wannan littafi zuwa maxaba'a amma da sauran wani vangare da ya rage wanda ba a gyara tuva-tuvan na'ura ba a cikinsa. Mai karatu zai samu gargada idan ya zo wurin. Muna ba da haquri, sai wani bugu na gaba idan Maisama ya nufa. Masu Fassara.

## GABATARWAR SHEIKH GUNAIMAN

### Wanda Ya Taqaita Littafin

Yabo da godiya Sun tabbata ga Allah Mai girma, mai rinjayar da gaskiya a kan qarya, wanda ya ce:

﴿ بَلۡ نَقۡذِفُ بِٱلۡحَقِّ عَلَى ٱلۡبَٰطِلِ فَيَدۡمَغُهُۥ فَإِذَا هُوَ زَاهِقٞۚ وَلَكُمُ ٱلۡوَيۡلُ مِمَّا تَصِفُونَ ﴿١٨﴾ ﴾ الأنبياء: ١٨

*A'a, muna jefa gaskiya a kan qarya, sai (qarya) ta koma halakakka. Kuma bone ya tabbata a gare ku saboda abin da kuke Siffantawa*[1].

﴿ وَقُلۡ جَآءَ ٱلۡحَقُّ وَزَهَقَ ٱلۡبَٰطِلُۚ إِنَّ ٱلۡبَٰطِلَ كَانَ زَهُوقٗا ﴿٨١﴾ ﴾ الإسراء: ٨١

*Kuma ka ce: "Gaskiya ta zo, kuma qarya ta lalace. Haqiqa, qarya ta kasance lalatacciya.*[2]

﴿ قُلۡ جَآءَ ٱلۡحَقُّ وَمَا يُبۡدِئُ ٱلۡبَٰطِلُ وَمَا يُعِيدُ ﴿٤٩﴾ ﴾ سبأ: ٤٩

*Ka ce, "Gaskiya ta zo, kuma qarya, ba ta iya fara (kome). Kuma ba ta iya mayarwa*[3]

Ina gode masa, godiya mai albarka. Ina shedawa babu abin bauta da cancanta sai Allah shi kaxai ba ya da abokin tarayya. Kuma Annabi Muhammadu bawansa ne, Manzonsa. Ya aiko shi da shirIya da addini na gaskiya don ya rinjayar da shi a kan sauran addinai. Ko maqiya sun qi ko sun so.

Bayan haka, babu shakka, wannan littafi *Minhajus Sunnah* na daga cikin manyan Littafan da shahararren malamin nan Ahmadu xan Abdulhalimi xan Abdussalami, wanda aka fi sani da "Ibnu Taimiyyah" ya wallafa, wanda a cikinsa ya xaura sirdin fafata yaqi da qarya, ya tarwatsa gungun maqaryata da karnukan farautarsu, ya kuma taimaki gaskiya. Wannan shi ya qarfafa buqatar da ke akwai musamman ga matasa musulmi, da su tunkari wannan littafi don cin moriyar abin da ya qunsa.

Wannan bukata ta fi qarfafa a wannan lokaci, inda annobar Shi'ah ta barbazu, ta kai caffa a wasu garuruwan musulmi. A wasu wuraren ma, ta yaga ta ciza, ta saki dafinta. Ta yaudari waxanda suka jahilci lamarinta, ta hanyar shigar burtu. Babu Shakka wannan littafe waraka ne ga wanda ya kamu da rashin lafiyar Shi'ah.

Wani abin al'ajabi shi ne, inda za ka taras da cewa, dukan qungiyoyin bidi'ah, vacewarsu ba ta yi zurfin ta mabiya Shi'ah ba, waxanda ke tinqaho da ci gaban sarkin baka. Kullum suna qara kutsawa cikin duhun dajin vata, amma suna ganin sun fi kowa shiriya, bayan suna yaqar masoyan Allah da Manzonsa.

[1] Suratul Anbiya',18
[2] Suratul Isra'i, 91
[3] Suratu Saba a 49

Littafansu sun cika har sun batse da zage-zage da la'antar manya-manyan bayin Allah; ba su kunyar kafirta manyan Sahabbai irinsu Abubakar da Umar da Usmanu Allah ya yarda da su ballantana qananansu. Sun kuma yi haka ne kawai saboda Sahabban nan sun bice wutar tsafi, suka rugurguza gumakan Farisa.

Duk wanda ya buxe shafukan littafan 'yan Shi'ah, zai ga yadda suka cika su fal da riwayoyin kafirta Sahabbai *Raliyallahu Anhum.* Su a wajensu yin haka ya zama tamkar ibada, har ma suna raya cewa wanda bai shiga sahunsu ba, ya zama abincin wuta. A cikin Littafinsu *Al Wafi* sun ce, wai, Allah ba zai karvi aikin wanda ba mabiyi Shi'ah ba, kome kyawon sa. Haka kuma a wani Littafi *Alkafi* mai muhimanci ainun a wurinsu, sun bayyana baqar adawarsu ga musulunci, da ma wanda ya zo da musuluncin gaba xaya.

A wautar mabiya Shi'ah, sun ce, Allah ya saukar da Alqur'ani ne domin ya bayyana abubuwa guda biyu kawai. Na farko shi ne, nuna matsayin Ali *Raliyallahu Anhu* ta hanyar bayyana darajarsa da ta iyalansa. Na biyu kuma shi ne, aibanta Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da fallasa su. Wannan shi ne ya kai su ga tuhumar cewa, mafi yawan sassan Alqur'ani mai girma sun halaka ta hannun Sahhabai Allah ya yarda da su.

Dukan tunaninsu da harkokin addininsu sun dogara kacokan a kan qarya, wadda suke zuqa ma limamansu. Sun cika shafa wa Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kashin kaji, ta inda har sun jingina su ga munafunci. Sai dai mu, muna sane cewa, sara da sassaqa ba su hana gamji toho. Allah wadaran 'yan Shi'ah, ya cika su da tsoro, ya kunyata su, gami da 'yan kanzaginsu.

Kodayake asalin wannan littafi ya qunshi bayanai iri-iri na martani ga masu aqidar Shi'ah da masu kore qaddara da masu falsafa, na zavar wa kaina kevantuwa ga abin da ya shafi Shi'ah kawai, saboda irin kariyar da ke tattare a wannan vangare ga abin da ya shafi tsarin shugabanci, da alfarmar Sahabbai da kuma mutuncin uwayen muminai (Matan Annabi, *Sallallahu Alaihi Wasallama*).

Ban shigar da kalma ko xaya ba ta qashin kaina a cikin wannan aiki, dalili da cewa, mawallafin littafin (Ibnu Taimiyyah) bai bar wata kafa ta yin haka ba. Ya riga ya xinke shi da hujjoji masu qarfi. Allah ya saka masa da alheri, ya sa mu yi tarayya da shi a cikin ladar wannan gagarumin qoqari nasa, Amin.

Allah shi ne mafificin wanda ake roqo. Tsira da amincin Allah su tabbata ga fiyayyen halitta Muhammadu xan Abdullahi da iyalan gidansa da Sahabbansa.

## 0.1 GABATARWAR IBNU TAIMIYYAH

Shehul- Islami Ibnu Taimiyyah ya ce:

Yabo da godiya su tabbata ga Allah Mai girma da xaukaka. Wanda Ya ce:

﴿ كَانَ ٱلنَّاسُ أُمَّةً وَٰحِدَةً فَبَعَثَ ٱللَّهُ ٱلنَّبِيِّـۧنَ مُبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ وَأَنزَلَ مَعَهُمُ ٱلْكِتَٰبَ
بِٱلْحَقِّ لِيَحْكُمَ بَيْنَ ٱلنَّاسِ فِيمَا ٱخْتَلَفُوا۟ فِيهِ ۚ وَمَا ٱخْتَلَفَ فِيهِ إِلَّا ٱلَّذِينَ أُوتُوهُ مِنۢ بَعْدِ مَا
جَآءَتْهُمُ ٱلْبَيِّنَٰتُ بَغْيًۢا بَيْنَهُمْ ۖ فَهَدَى ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لِمَا ٱخْتَلَفُوا۟ فِيهِ مِنَ ٱلْحَقِّ بِإِذْنِهِۦ ۗ
وَٱللَّهُ يَهْدِى مَن يَشَآءُ إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ﴿٢١٣﴾ ﴾ البقرة: ٢١٣

*Mutane sun kasance qungiya xaya (a kan gaskiya. Daga bisani sai suka yi savani, wasu suka bi gaskiya, wasu suka bi vata) sai Allah Ya aiki Annabawa suna masu bayar da bishara kuma masu gargaxi. Kuma ya saukar da Littafi da gaskiya tare da su. Domin (Littafin) ya yi hukunci a tsakanin mutane, a cikin abin da suka sava wa juna a ciki; kuma babu waxanda ya sava a cikinsa, face waxanda aka bai wa shi daga bayan hujjoji bayyanannu sun je musu, domin zalunci a tsakanin su. Sai Allah ya shiryar da waxanda suka yi imani ga abin da suka sava a cikinsa na gaskiya da izininsa. Kuma Allah yana shiryar da wanda yake so, zuwa ga hanya madaidaciya*[1].

Na shaida babu abin bauta da cancanta sai Allah shi kaxai, ba ya da abokin tarayya, kamar yadda ya shedi kansa da cewa;

﴿ شَهِدَ ٱللَّهُ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ وَأُو۟لُوا۟ ٱلْعِلْمِ قَآئِمًۢا بِٱلْقِسْطِ ۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلْعَزِيزُ
ٱلْحَكِيمُ ﴿١٨﴾ ﴾ آل عمران: ١٨

*Allah ya sheda cewa, haqiqa, babu abin bautawa da cancanta face shi. Su ma mala'ikku da ma'abuta ilimi sun shedi haka. Yana tsaye da adalci. Babu abin bautawa face shi, mabuwayi, mai hikima.*[2]

Kuma na shaida Annabi Muhammadu bawansa ne, Manzonsa. Cikamakon Annabawa, wanda Allah ya sifanta shi da cewa;

﴿ لَقَدْ جَآءَكُمْ رَسُولٌ مِّنْ أَنفُسِكُمْ عَزِيزٌ عَلَيْهِ مَا عَنِتُّمْ حَرِيصٌ
عَلَيْكُم بِٱلْمُؤْمِنِينَ رَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴿١٢٨﴾ ﴾ التوبة: ١٢٨

---

[1] Suratul Baqara: 213

[2] Suratul Ali- Imarana 18

*Haqiqa Manzo daga cikinku ya je muku. Ba ya son duk abin da ke wahalar da ku. Mai kwaxayi ne ga (shiriyar) ku Mai tausayi ne, mai jinqai ga muminai"*[1]

Tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama.*

Bayan haka;

Wasu 'yan'uwa Ahlus-Sunnah Sun isko ni da littafin *Minhajul karamati fi Ma'arifatil Imamati* na wani malamin Shi'ah, inda ya ke tallar hajarsa ta Shi'anci, tun ma ba a fadar sarakuna ba.

Littafin ya samu karvuwa ga mafi yawan waxanda ba su fahimci addini ba. Kuma ya samu taimakon qungiyar Shi'ah ta *Baxiniyyah*, mavarnata. Waxanda suka samo tushe daga malaman falsafar Yahudanci, ta Sabi'awa, waxanda ba su ganin kan kowa da gashi. Sun fanxare ma tafarkin Annabawa, sun juya ma musulunci baya, suka mayar da addini zavi son ka. Ba haka ba ma, lamarin addini a wajensu yana da matsayi irin na jam'iyyar siyasa, wadda a ke da zavin shiga da fita a kowane lokaci. Ita kuwa annabta a idanunsu, wata hanyar holewa ce kawai da kyautata zaman duniya.

Wane mutum! Ire-iren waxannan marubuta fa da daxewa sun watsu a sassa na duniya, inda jahilci ya barbazu sakamakon qamfar malamai masana shari'a, masu tumbuke shukar vata da aka dasa cikin al'umma. Mabiya Shi'ah sun qware wajen lavewa ga sabara su harbi barewa, musamman wajen aqidar qaryata Manzanci a fa kaice. Bugu da qari kuma sun halaka mutane masu ximbin yawa ta hanyar yaudara.

Qungiyoyin Shi'ah da na Jahamiyya su ne manya –manyan qofofin shigowar nau'ukan varna da damfara, musamman waxanda aka shigar cikinsunayen Allah da Siffofinsa da Littafansa. Kamar yadda aka samo tabbacin hakan daga limaman qungiyoyin *Karramiyyah* da *Baxiniyyah* da sauran tarkacen zindiqai.

Shi wanda ya kawo min littafin, ya shaida mini cewa, suna amfani ne da littafin wajen yaxa gurvatacciyar aqida, musamman a gidajen masu mulki da masarautu. Za a iya tabbatar da haka, lura da cewa marubucinsa ya rubuta shi ne musamman ya aika shi ga sarki *Khudabandah.* A nan ne waxanda suka isko ni da littafin suka nemi in yi fashin baqi game da varnar da ke cikinsa. Saboda a ceto bayin Allah a kuma fallasa maqaryata. Sai na amsa musu da cewa, ai wannan littafi hujja ne a wajen masu shi, kodayake a cikin asiri sun jahilci cewa, babu komi cikin sa, sai shirme da maganganu marasa kan gado.

Abin da ya kyautu mu fayyace a nan shi ne, a gane cewa, su dalilai sun rarrabu ne zuwa gida biyu. Akwai dalilai na tsintsar Ilimi kuma akwai na kaifin hankali. Abin kaico shi ne, su mabiya Shi'ah, idan ka lura da ra'ayinsu da kyau za ka san cewa, sun vace vari. Domin sun rasa ilimi da hankali gaba xaya. Sun yi zo-zo zo da waxanda Allah Ya sifanta da cewarsa

[1] Suratul Taubati, 128

Kuma suka ce: “Da mun zamo muna saurare ko muna da hankali da ba mu kasance a cikin ‘yan sa’ira ba.[1]

Rubuce- rubucensu sun cika sun batse da qissoshi da labaran cin qanzon kurege, ga su kuma da wauta kamar xiyan fari. Sun goge wajen mayar da fari baqi a sashen riwaito hadisi, ba ruwan su da tacewa tsakanin maruwaici maqaryaci da wanda ba shi ba. Ba su dogara da komi ba face zato da an-yi-an-ce. Ga su da biyar ra’ayoyin malamansu a makance. Kuma suna jin cewa, wannan hanya da suke a kai itace a’ala, musamman a fagen kafa dalili. Wannan irin hali shi ya kai su har suka fantsama, suka faxa cikin jerin gwanon *Mu’utazilawa* da masu kore qaddara. Kamar yadda a wani lokacin kuma sai a tsince su a tashoshin *Mujassimah* da *Jabariyyah*. Wani abin al’ajabi da mamaki a nan shi ne, duk da irin zurfin vacewar waxannan qungiyoyi da aka zayyano, ‘yan Shi’ah sun zarce su nesa ba kusa ba a fagen rashin fahimtar lamurra. Wanda hakan ya sa malamai suka haxu a kan cewa, qungiyarsu ta fi kowace qungiya dolanci da jahilci. Sun tafka varnar da Allah ne kawai ya san iyakacinta a cikin al’umma.

Qungiyoyin *Isma’iliyyah* da *Nusairiyyah* da *Baxiniyyah* da Yahudawa da Kirista, manya- manyan arna da zindiqai, duk ta qofar Shi’anci suka samu hanyar barbaza varna a cikin musulunci bayan sun rinjayi wasu garuruwan musulmi, ta hanyar zubar da jini da kwashe dukiyoyinsu. Hasali ma duk qasar musulmin da masifar yaqi ta faxa ma, za ka taras da cewa, hakan ya faru ne bayan qullin qawancen makirci tsakanin kafirai da mabiya Shi’ah. Misalin faruwar irin wannan ba ya lissafuwa a duniya.

Dalilin wannan qazamin qawance nasu, ba ya rasa nasaba da cewa tun asalatan, Shi’ah ta fito ne daga cikin tsatson zindiqai da munafukai, da suka bayyana a zamanin Sarkin Musulmi Aliyu xan Abu Xalib *Raliyallahu Anhu.* Babbar aniyarsu ita ce faxa da Musulunci. Wannan shi ya sa Aliyu *Raliyallahu Anhu* ya hanzarta xaukar qwaqqwaran matakin wargaza gungunsu, ta hanyar lallasa musu nau’ukan azaba iri- iri, bayan da ya fahimci cewa, tsawa da gargaxi ba su bishe su. Ya yi amfani da bulala, ya koma yana qona su da wuta. Da lamarinsu ya vaci sai ya zaro takobinsa ya tunkare su cikin hanzari a fusace. Daga nan suka ce, qafa me na ci ban ba ki ba. Suka kama gudu ba waiwaye.

Dalilin da ya sa Sarkin Musulmi Aliyu xan Abu Xalib Allah ya yarda da shi ya xaukar wa mabiya Shi’ah wannan mataki shi ne, saboda faifayewar su a wajen yabonsa, inda suka fifita shi sama da darajar halifa Abubakar *Raliyallahu Anhu* da Sarkin Musulmi Umar xan Haxxabi *Raliyallahu Anhu* wanda shi a wajensa bai tava fifita kansa a kan waxannan Sahabbai ba. Abin da ma ya tabbata daga wajensa shi ne, an ji shi da bakinsa yana cewa: “Abubakar ne ya fi kowa girman daraja a cikin wannan al’umma, sannan Umar, in ban da Manzonta”. Imamul Buhari a cikin ingantaccen littafinsa ya riwaito cewa,

[1] Suratul Mulk

muhammadu xan Hanafiyya xan Ali *Raliyallahu Anhu* ya tambayi babansa cewa, wane ne mafifici daga cikin Sahabbai? Sai wancan jawabi ya zama amsa ga wannan tambaya.

Wannan shi ne dalilin da ya sa malaman farko ba su yi savani ba a kan fifikon Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* a kan sauran al'umma. Wajen da suka yi muhawara kawai shi ne, tsakanin Aliyu da Usmanu yardar Allah ta tabbata a gare su, wane ne ba wane ne ba? Abin mamaki wai, kare da tallar tsire, tarihi ya nuna cewa, malaman Shi'ah na farko-farko, kai! har ma da na baya- bayansu an ji su suna fifita Abubakar *Raliyallahu Anhu* a kan sauran Sahabbai. Abdul Jabbar Al hamadani ya cirato daga littafin *Tathbitun Nubuwah* cewa; Abul qasim Al balakhi a cikin raddin da ya yi wa xan Rawandi ya ce, wani ya tambayi Shariku xan Abdullahi cewa; wa ya fi matsayi a tsakanin Abubakar da Ali? Sai ya kada baki da hanzari ya ce, Abubakar mana. Sai mai tambayar a cikin mamaki ya ce; "Kai da kanka ke faxin haka?" "To, ina amfanin kusancin ka ga Ali?". "Ai duk wanda bai yarda da cewa wannan magana haka take ba, to ba shi ba Ali". in ji Malam Shariku. Ya ci gaba da cewa, na rantse da Allah, watarana na ga Aliyu *Raliyallahu Anhu* da idanuna ya hau kan mimbari yana huxuba, ya na cewa, ku saurara, ku sani cewa mafi alheri daga cikin wannan al'umma bayan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne Abubakar sannan Umar yardar Allah ta tabbata a gare su. Kana ganin cewa zai kyautu a yi biris da wannan magana tasa? Na rantse da Allah, Aliyu *Raliyallahu Anhu* ko alama ba maqaryaci ba ne.

## Zango Na Xaya
## ‘Yan Shi’ah da Aqidunsu
## 1.0 Malamai ku Bayyana Gaskiya

Duk lokacin da mabiya suka fara la’antar magabata, bayyanar da ilimi ya zama tilas. A lokacin da aka isko ni da wannan littafi wanda malamin Shi’ah ya rubuta aka kuma neme ni da mayar masa da martani, da yake, ba a ce ma maci dambu ya sha ruwa, sai na feqe alqalami kuma na jawo tawwada na shiga rubutu, ina mai fatattakar varna da vatan da suke neman bazawa, domin kange muminai daga faxawa cikin tarkonsu. Rashin yin hakan kuma, yana sa ‘yan barandar, karkatattu su zaci ko kasawa aka yi. Shi ya sa na himmatu ga rubuta abin da ya sawwaqa don cika alqawarin nan da Allah ya riqa ga malamai, domin tabbatar da adalci da ba da shaida domin Allah. Kamar yadda Allah Maxaukakin Sarki ya ce;

﴿ ۞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُونُواْ قَوَّٰمِينَ بِٱلۡقِسۡطِ شُهَدَآءَ لِلَّهِ وَلَوۡ عَلَىٰٓ أَنفُسِكُمۡ أَوِ
ٱلۡوَٰلِدَيۡنِ وَٱلۡأَقۡرَبِينَۚ إِن يَكُنۡ غَنِيًّا أَوۡ فَقِيرٗا فَٱللَّهُ أَوۡلَىٰ بِهِمَاۖ فَلَا تَتَّبِعُواْ ٱلۡهَوَىٰٓ أَن تَعۡدِلُواْۚ
وَإِن تَلۡوُۥٓاْ أَوۡ تُعۡرِضُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٗا ١٣٥ ﴾ النساء: ١٣٥

*Ya ku waxanda suka yi imani! Ku kasance masu tsayuwa da adalci, masu shaida saboda Allah, kuma ko da a kan kawunanku ne, ko mahaifa da mafi kusantar zumunta, ko (wanda ake yi wa shaida ko ake shaida a kansa) ya kasance mawadaci ko matalauci. To Allah ne mafi cancanta da al’amarinsu. Saboda haka kada ku bibiyi son zuciya, har ku karkata. Kuma idan kuka karkatar da magana, ko kuwa kuka kau da kai, to lalle ne, Allah ya kasance Masani ga Abin da kuke aikatawa*[1]

A cikin wannan aya an yi amfani da kalmar *Layyu* wadda ke nufin canzar da shaida da kuma kalmar *I’rad*; voye shaida da rashin bayyanar da ita, wanda dukan yin haka laifi ne da bijire ma gaskiya, wanda zai jefa mutane ga ramin halaka.

Babu shakka Allah ya yi umurni da abi gaskiya, a fayyace lamurra kamar yadda suke. Ya kuma yi hani daga yin qarya da kwana- kwana ko munaqisa ga abin da ya zama tilas ne a fitar da shi fili. Hadisi ya zo a cikin Buhari da Muslimu cewa; Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce “Masu cinikayya suna da zavi matuqar suna tare. Idan suka yi gaskiya sai a sanya albarka cikin cinikinsu. Idan kuwa suka yi qarya suka voye aibi sai a shafe albarkar cikinsu”.[2]

Wane mutum! Wannan fa game da ciniki kenan, ballantana ga voye Ilimi musamman irin lokacin da bidiar la’antar magabatan wannan al’umma ta

---

[1] Suratul Nisa’I 135

[2] Buhari Kitabul Buyai (3/56) Muslim Kitabul Buyu, (3/1164)

bayyana. Ai ko alama, ba zai kyautu ba aji shiru kamar an aiki bawa garinsu. Bayani ya zo cikin wani hadisi cewa; “Duk sadda ‘yan bayan wannan al’umma suka la’anci magabatansu, dole ne masu ilimi su yi magana. Wanda ya voye ilimi a wannan lokaci, dai dai ya ke da wanda ya voye abin da Allah ya saukar wa Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama”.*[1] Abin kulawa a nan shi ne, su fa jama’ar farko na wannan al’umma, su suka yi tsayuwar gwamin jaki a kan ganin cewa wannan addini ya samu kafuwa da yaxuwa a duniya baki xayanta. Don haka, duk wata suka da aka yi gare su ta na komawa ne kai tsaye ga addinin musulunci. Wannan kuwa shi ne ummul-haba’isin bijire ma abin da Allah ya aiko Manzonni da Annabawa da shi. Dama kuma shi ne matuqar gurin ‘yan Shi’ah; watsa gubar aqidar Shi’ancinsu a sassan duniya. Dabarun da suke yi kuwa domin su cimma nasara ga wannan baqar anniya tasu shi ne, sukan rava ne su zagayo ta bayan manyan kangararrun mutane maqiya addinin Allah. Sai su kai farmaki ga wuraren da suka fahimci cewa, musulmi suna da rauni, sai su baje kolinsu a wannan nahiya. Kaico! Abin tausayi da juyayi, shi ne irin yadda ‘yan Shi’ah ke ribantar wasu ta hanyar amfani da shubuhohi na jahilci da biyar son rai waxanda su ne manyan sinadarai ga kowane irin vata. Allah ya kiyashe mu. Allah Ta’ala Ya ce:

﴿ وَٱلنَّجۡمِ إِذَا هَوَىٰ ١ مَا ضَلَّ صَاحِبُكُمۡ وَمَا غَوَىٰ ٢ وَمَا يَنطِقُ عَنِ ٱلۡهَوَىٰٓ ٣ إِنۡ هُوَ إِلَّا
وَحۡيٞ يُوحَىٰ ٤ ﴾ النجم: ١ - ٤

*Ina rantsuwa da tauraron, a lokacin da ya faku. Ma’abucinku bai vata ba. Kuma bai qetare haddi ba. Kuma ba ya yi*n maga*na daga son zuciyarsa. (maganarsa) ba ta zamo ba face wahayi ne da ake aikowa”.*[2]

A nan ka ga sai Allah ya yabi Manzonsa yabo na musamman, ta hanyar tsarkake shi daga vata da halaka. Vata kuwa a nan, tana nufin jahilci. A yayin da halaka ke nufin biyar son zuciya. Kamar yadda Allah Mabuwayi ya ce:

﴿ وَحَمَلَهَا ٱلۡإِنسَٰنُۖ إِنَّهُۥ كَانَ ظَلُومٗا جَهُولٗا ٧٢ ﴾ الأحزاب: ٧٢

*Kuma mutum ya xauke (amana). Lalle shi (mutum) ya kasance mai yawan zalunci, mai yawan jahilci”.*[3]

Wannan aya ta fayyace sarai cewa, azzalumi halakakke ne, a inda shi kuma jahili vatacce ne, in ba wanda Allah ya yi wa gyaxar dogo ta hanyar tuba ba.

Na’am Wannan ba shakka shi ne halin ‘yan bidi’a waxanda suka nisanta kansu daga littafin Allah da sunnar Manzonsa tsira da amincin Allah su tabbata gare shi. Ba su biyar komi in ba zato ba da abin da rayukansu ke so.[4]

---

[1] Ibn Majh, (1/96-97)
[2] Suratul Najm. 1-4
[3] Suratul Ahzab 72
[4] Suratull Najmi 23

Qungiyoyin vata a wajensu ne jahilci da zalunci suka yanke cibiya, tun ma ba mafiya lalaci daga cikinsu ba, ina nufin 'yan Shi'ah. Abin da ya kai su ga wannan matsayi kuwa shi ne, kai wa matuqa da suka yi wajen bayyana mummunar qiyayya ga manyan masoya Allah watau Sahabbai, muhajiruna da Ansaru. Allah ya yarda da su da duk waxanda suka bibiyi hanyarsu da kyautatawa.

Wani abin lura a nan shi ne, abu ne sananne cewa, 'yan Shi'ah suna da qwaqqwarar hulxa da taimakekeniya a tsakanin su da kafirai da munafukai daga cikin Yahudawa da Kiristoci da Majusawa maqiya musulunci, da sauran fanxararrun qungiyoyi irinsu *Nusairiyyah* da *Isma'iliyyah*. Kuma kowa ya san cewa, sai hali ya zo daidai ake qulla abota. Ma'aunin gano wannan matsayi nasu kuwa abu ne mai sauqi. Za ka taras da su a duk lokacin da wani savani ya abku tsakanin Muminai da Kafirai suna gaugawar kai xauqi da agaji na musamman ga abokan faxan musulmi, kamar dai yadda aka sha ganin hakan a fayafayin tarihin duniya.

Sun tallafa wa maqiya musulunci na qasar Turkiyya a kan musulmin qasashen Khurasana da Iraqi da Jazira da kuma qasar Sham. Sun kai gagarumin taimako ga Kiristoci, aka yaqi Musulmi a qasar Sham da Masar da sauran qasashe, kuma hakan ta sha faruwa a lokuta daban- daban. Ai ko ka san ba zai yiwu musulmi su manta da irin wannan ta'asar ba. Da yawa-yawan ta'addancinsu ya abku ne a qarni na huxu da na bakwai, lokacin da kafiran Turkawa suka kutsa cikin garuruwan musulmi suka kashe adadi mai ximbin yawa, waxanda Allah ne kaxai masanin iyakar su. To, a wannan lokaci 'yan Shi'ah sun taka rawa wadda babu waiwaye cikinta inda aka tursasa musulmi aka ci zarafinsu ainun, duk saboda gudummuwar shugabannin sharri na mabiya Shi'ah. wannan shi ne dalilin da ya sa ake yi musu suna da karnukan farautar Yahudawa.[1]

### 1.1 Zumuntar Shi'ah da Yahudawa da Nasara

*Minhajul Karamah Fi Ma'arifatul Imamah*, shi ne sunan littafin da nake baka labari a fasalin da ya gabata, wanda marubucin Shi'ah ya Wallafa. Ni dai a ganina da an ba littafin sunan *Minhajun Nadamah* da ya fi dacewa. Yadda abin yake shi ne, kamar mutum ne mai datti, qazami, Bamaguje mabiyi shexan, amma ya rinqa lissafa kansa daga cikin tsarkakan bayin Allah. Ai ka ga wannan abu ne mai nisa. Babu shakka zuciyar da ke cike da qyamar manyan-manyan waliyan Allah ita ce zuciya mafi muni da qazancewa a cikin halittun da ke bayan qasa. Bayan Annabawan Allah kuwa babu mahalukin da darajarsa ta yi ko kusa da ta Sahabbai. Wannan shi ne dalilin da ya sa Allah ya hana a ba kowa ganima a bayansu sai masu cewa;

[1] Faxace faxacen da ke faruwa a yankunan gabas ta tsakkiya tsakanin musulmi da maqiyansu da abin da ke faruwa a yau a qasar Afganistan da Iraqi hujjoji ne masu qarfi cewa 'yan Shi'ah na taimakon maqiya musulunci akan musumi. Masu fassara.

﴿ رَبَّنَا ٱغْفِرْ لَنَا وَلِإِخْوَٰنِنَا ٱلَّذِينَ سَبَقُونَا بِٱلْإِيمَٰنِ وَلَا تَجْعَلْ فِى قُلُوبِنَا غِلًّا لِّلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ رَبَّنَآ إِنَّكَ رَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴾ الحشر: ١٠

*Ya Ubangijinmi! Ka yi gafara a gare mu, da kuma ga 'yan'uwanmu waxanda suka riga mu yin imani. Kada ka sanya wani qulli a cikin zukatanmu ga waxanda suka yi imani, Ya Ubangijinmu! Haqiqa, kai ne Mai tausayi, mai jin qai.*

Duba sarai malam ka gani, Shi'anci da Yahudanci sun yi kunnen doki wajen biyar son rai. In kuwa gefen faifayewa ne da kuma kantar jahilci, tsakaninsu da kiristoci ba a san gwani ba. Wannan ita ce haqiqanin shaidar da mutane suka bayar a kansu.

Malaman garin Kufa su suka fi kowa sani da tantance halayyar mabiya Shi'ah, saboda can ne tushenta. Bari mu ji wani malami daga cikinsu abin da yake cewa: "Duk a faxin duniya ba wanda ya fi Shi'ah sakarci. Kamar mujiya suke a duniyar tsuntsaye ko kuma jakkai a sashen dabbobi. Wallahi sun sha neman in fesa qarya a kan sayyidina Aliyu *Raliyallahu Anhu* wai don in qara bayyana darajarsa. Inda na yi haka ko to, da shirye suke su cika gidana da zinari da azurfa. Amma kash! Ni ba irin mai yin haka ne ba"[1]. In ji malam Sha'abi.

Haka ne. Wani malami ma mai suna Baban Hafsa wanda aka fi sani da Ibnu Shahin[2] a cikin littafinsa mai suna *Alluxfu Fis- Sunnati* ruwitowa ya yi daga Imamus Sha'abi cewa: "Kashedinku da qungiyoyin bidi'a, musamman mabiya Shi'ah, waxanda suka shiga musulunci da qafar hagu; ba su shige shi saboda Allah ba, sai don huce haushi ga Musulmi. Wannan Shi ne babban dalilin da ya harzuqa sayyidina Ali har ya sa aka hura wuta aka rura ta sosai, ya ce a kama su xaya bayan xaya a rinqa jefawa a cikinta. Daga nan ya yunqura ya kai ma wasunsu xauki da hargagi, suka firgita. Suka cika wandunansu da iska, gudun fanfalaqi ya same su ba ji ba gani. Amma gwanin tsalle da nuna qwarewa cikin gudu a wannan rana Abdullahi xan Saba'i, ya tsira da rayuwarsa inda ya samu mafaka a Sabat ta qasar Iran, ya ko ci gaba da fesa gubarsa a can. Haka shi ma Abdullahi xan Yasaru da ya samu tserewa bai ci burki ba sai garin Khazar.

Su dai Mabiya Shi'ah, rashin lafiyarsu guda ce da ta Yahudawa. Bari mu hawar da su kan teburin misali ka ga yadda abin ya ke:

[1] Suratul Hashari 15

[2] Sunansa, Umar bn Ahmad bn usman Al bagadadi Ya rasu Shekara 385, Taskiratul huffaz 3/183

### 1.1.2 **Jadawalin Zumuntar Shi'anci Da Yahudanci**

| **Yahudawa Sun Ce** | **'Yan Shi'ah Sun Ce** |
|---|---|
| Babu maganar Jihadi sai ranar da Dujjal ya bayyana, kuma Allah ya aiko shi da takobi daga sama. | Babu maganar Jihadi sai ranar da Mahadinsu ya bayyana, kuma sai sun ji anyi shela daga sama. |
| Ba wanda ya cancanci shugabanci sai zauri'ar Annabi Dawuda *Alaihis Salamu.* | Ba wanda ya cancanci shugabanci sai Ali *Raliyallahu Anhu* da zuriyarsa. |
| Suna jinkirin sallar magariba sai bayan fitowar taurari. | Suna jinkirin sallar magariba sai bayan fitowar taurari[1] |
| Suna bauxe ma alqibla wurin yin sallah. | Suna bauxe ma alqibla wurin yin sallah |
| Suna rufe idanunsu wurin ibada. | Suna rufe idanu wurin sallah |
| Idda ba dole ba ce ga mata a wurin su. | Idda ba dole ba ce ga mata a wurin su. |
| Sun karkatar da ma'anar littafin *At- Taurah.* | Sun karkatar da ma'anar littafin *Alqur'ani.* |
| An wajabta salloli 50 a kansu kowane wuni. | Su ma sun ce, salloli 50 aka wajabta masu kowace rana. |
| Suna birkice sallama ga musulmi su ce, *Assamu* madadin *Assalamu* suna roqon mutuwa ga musulmi. | Su ma dai haka xin suke yi. |
| Sun haramta ma kansu wasu nau'oin kifaye guda biyu; Tarwaxa ba Buku. | Su ma 'yan Shi'ah sun ce, duk kifaye sun yi magana da Ali in ban da waxannan biyu. Don haka ba su cin su. |
| Ba su yin shafa a kan safa. | Su ma 'yan Shi'ah haka. |
| Sun halalta ma kan su cin dukiyar kowa in ba wasu-wasu ba. Kamar | 'Yan Shi'ah ma suna ganin cewa, dukiyar kowa halas ce gare su in dai |

[1] Anan sun yi biris da hadisin da ya tuzgo daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa; "Al'ummata ba za su gushe ba akan fixira matuqar basu jingirin sallar magariba. Abu Dawuda ya ruwaito shi a cikinsunan 1/169 da ibn Majah 1/225, cikin musnadi 4/147-5/422.

| | |
|---|---|
| yadda Allah ya labarta mana cikin Alqur’ani. | ba xan Shi’ah ba ne. |
| Wajen yin sujada suna yin dungure. Wato, suna aza gefen goshi. | Su ma ‘yan Shi’ah suna yin irin wannan sujada. |
| Ba su zuwa sujada kai tsaye sai sun fara wani irin sunkuyar da kai. | Su ma ‘yan Shi’ah haka suke yi. |
| Suna qiyayya da mala’ika Jibrilu *Alaihis Salamu.* | A wajensu mala’ika Jibrilu ya yi kure wajen kawo ma Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* manzanci maimakon Ali. Don haka su ma suna adawa da shi. |

Aqidun Shi’ah ba da na Yahudawa kawai suka yi kama ba. Wasu aqidun nasu kama suke yi da na Kiristoci. Dubi auren ‘yan mishan, mine ne ba jin daxi kawai ba, tun da ko sadaki ba sa bayarwa? A gefe xaya kalli auren mutu’ar Shi’ah, ai ka ga biri ya yi kama da mutum ko?

Idan ka kalli wata fuska sai ka ga gara ma Yahudawa da Kirista a kan ‘yan Shi’ah. Domin kuwa duk Bayahuden da ka tambaya wane ne ya fi daraja a cikin mutane? Zai ce maka: “Sahabban Annabi Musa *Alaihis Salamu*”. Tambayi Kirista irin wannan tambaya, shi kuma zai ce maka: “Sahabban Annabi Isa *Alaihis Salamu*”. A yayin da idan ka tambayi xan Shi’ah, su wane ne suka fi kowa qasqanci a bayan qasa? Sai ya ce maka: “Sahabban Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama.*

A lokacin da Allah mai girma da xaukaka ya ba da umurni a nema wa magabatan musulmi gafara, a lokacin su ‘yan Shi’ah ke cika bakinsu da zagi na fitar arziki da cin zarafi gare su, ba kunya ba tsoron Allah. Don mi ba za a zare takobi a nufe su ba, daga nan har ranar da Allah zai naxe qasa? Allah ya tarwatsa gungunsu ya watse haxin kansu. Kamar yadda Allah ya ce:

﴿كُلَّمَآ أَوۡقَدُواْ نَارٗا لِّلۡحَرۡبِ أَطۡفَأَهَا ٱللَّهُۚ﴾ المائدة: ٦٤

*Kuma kodayaushe suka hura wata wutar yaqi, sai Allah ya bice ta”*[1].

Waxannan jawabai da aka jiyo haka su ke. Domin kuwa dimun sun yi kama da duk abin da ya sifanta su da shi.

Sun yi fatar gurvata musulunci kamar Yadda Bulus xan Yusha’u wani basarake daga cikin Yahudawa ya rikirkita addinin Kiristanci. Duk da sallah

[1] Suratul Ma’ida: 64

suka yi ba ta zuwa ko ina don ba a amsarta. Bayani ya gabata cewa, Aliyu *Raliyallahu Anhu* sai da ya tarwatsa gungunsu har ma ya kai ga azabtar da su da wuta, lokacin da su Abdullahi xan Saba'i da Abubakar Al-Kurus suka yi gudun da muka faxa a xazu. Su ne kuma dai waxanda suka faifaye har suka Allantar da Aliyu wanda har ta kai yake cewa, a waqe:

*Yayin da har lamarin wajensu ya kumbura*
*Sai nayyi gwami nak kirawo Qambara*
*Yad dinga jejjefa su xai-xai-xai ciki*
*Domin musulmi dagga nan su yi hattara*

## 1.2 Mafarin Sunan 'Yan Shi'ah "Rafilah"

Sanannen suna ne ga 'yan Shi'ah da aka kira su da shi "Rafilah". Asalin sunan kuwa shi ne, saboda a farkon lamarinsu sun kasance masu biyyaya ga imaminsu Zaidu xan Aliyu xan Husaini, amma daga baya sai suka wancakalar da shi suka yi watsi da lamarinsa. Wannan kuwa ya faru ne a lokacin mulkin Hisham wajejan shekara ta 121 bayan hijira. Kalmar *Raflu* mai ma'anar wancakalarwa ita ce ta bi su har aka san su da suna 'yan Shi'ah.

Farkon al'amarin Shi'ah ta rabu ne zuwa gida biyu: *Rafilah* da kuma Zaidiyyawa, a lokacin yunqurin juyin mulkin da suka ingiza Zaidu xan Aliyu xan Husaini ya yi, a qarshe kuma suka dare masa.

Tarihin wannan suna na *Rafilah* ya samo asali ne bayan da suka tambayi Zaidu xin matsayin sayyidina Abubakar da Umar a wurinsa. Shi kuma sai ya faxi kyakkyawar magana game da su. Daga nan sai suka bijire masa suka ba shi baya don su nuna masa rashin jin daxinsu game da yabon da ya yi wa manyan Sahabban. A nan ne sai ya ce; *Rafaltumu ni?* Kun watsar da ni? Sai sunan kuwa na Rafila ya bi su har lahira. Su kuwa sauran waxanda suka zauna tare da shi sai mutane suka ba su sunan Zaidiyyawa saboda jivintar lamarinsa da suka yi. Har kwanan gobe kuwa Zaidiyyawa na makokin kashe shi a daidai itaciyar da aka tsire shi, sun ma mayar da wurin wajen yin bauta safe da marece.

Da haka suka kafu a matsayin qungiya mai aqidodi daban-daban da suka haxa da; rabke salloli a yi su lokaci guda har koyaushe ba tare da lalura ba. Ba su yin sallah sai a lokuta guda uku,[1] wannan kuwa duk saboda kamanta kansu da Yahudawa.

A cewarsu, sakin aure ba ta yadda zai tabbata sai an kafa shaidu. Kuma duk wanda ba xaya daga cikinsu ba najasa ne. Ba su cin yankan kowa sai nasu. Sun ce duk da ruwan da musulmi ya yi amfani da su, ya zama najasa. Idan kuma ya ci abinci a cikin wani kwano ko akushi dole ne sai an wanke kafin xan Shi'ah ya ci a cikinsa. Duk sun xauko waxannan xabi'oi da aqidoji daga Yahudawa, musamman Samirawa, qungiyar Yahudawa mafi muni. Kuma a kan wannan dalili ne da yawan mutane ke kiran mabiya Shi'ah da sunan

[1] Suna rabke sallar Azahur da La'asar, Magariba da isha, Sai kuma Sallar Asuba. Masu fassara.

Samirawa. Manufa a nan ita ce, kamar yadda Samirawa suka bar addinin Yahudanci haka Shi'ah suka bar addinin musulunci.

Sun qware ga munafucci, wato Taqiyya kenan. Ga kuma sharri kamar Yahudawan asali.

### 1.3 Wautar 'Yan Shi'ah

Akwai Labarun wauta da soki burutsu tattare da Shi'ah. Kaxan daga cikinsu su ne; Akwai wata rijiya wadda Zaidu bn Aliyu xan Husaini ya gina, shi ne aka samu wani sashe na mabiya suka haramta ma kansu shan ruwan rijiyar don qiyayya ga Zaidu, sun mance da cewa Annanbi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da kansa tare da Sahhabbansa Allah ya yarda da su, sun kasance suna shan ruwan rijiyoyin da kafirai suka gina ballantana rijiyar da wani musulmi ya gina. Kuma akwai wasu daga cikinsu da ba su cin taura, wai don kawai a qasar Sham ake samun ta inda magoya bayan sayyidina Mu'awiyah suka fi yawa. Alhali kuwa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da kansa yana cin abincin da aka shigo da shi daga qasashen qetare. Ko da kuwa qasashen kafirai ne. Kamar yadda yake sanya tufafin da asalinsu kafirai ne suka xunka su.

Haka kuma 'yan Shi'a sukan canfa lamba goma, suna matuqar qyamar ta, ta yadda ko gida za su gina ba za su yarda yawan xakunansa ya zamo goma ba. To, ko a masallatansu ma, ba su yin ginshiqai guda goma. Dalili kuwa, shi ne tsananin qyamar da suke yi wa Sahabbai guda goma da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi masu bushara da aljanna.

Dubi hadisin da ya zo cikin Sahihu Muslim riwayar Jabir Allah ya yarda da shi, cewa watarana wani hadimin Haxibu xan Abu Balta'ata ya ce; "Ya Manzon Allah! na rantse da Allah sai Haxibu ya shiga wuta". Sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce masa, ka sha qarya. Saboda Haxibu ya halarci yaqin Badar da Hudaibiyya.[1]

To, me ya yi zafi wanda ya sa mabiya Shi'ah suke adawa da waxannan manyan bayin Allah, in ba kaxan daga cikinsu ba? Yanzu Mu ma jingine zancen Sahabbai a gefe, bari mu ba da wani misali, mu qaddara cewa yanzu haka akwai wasu gogaggun qafirai guda goma a duniyarmu ta yau, me zai zama dalilin camfa adadin yawansu har a ce ana qyamar amfani da shi idan ba tsagwaron jahilci ba? Ai Allah ya ambaci cewa:

﴿ وَكَانَ فِي ٱلۡمَدِينَةِ تِسۡعَةُ رَهۡطٖ يُفۡسِدُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا يُصۡلِحُونَ ٤٨ ﴾

النمل: ٤٨

*Kuma waxansu jam'a (Su) tara sun kasance a cikin birnin, suna yin varna kuma ba su kyautatawa.*[2]

Shi kenan sai ya zama dole a camfa lamba tara (9), a qaurace ma yin amfani da duk wani abu da ke da dangantaka da ita, hujja da cewa tarihi ya

---

[1] Sahihu Muslim (4/1942)

[2] Suratul Namli, 48

labarta samuwar wasu ‘yan daba guda tara masu varna a cikin birni a wani lokaci da ya gabata? Idan kuwa har wannan ba aikin hankali ne ba, to ya za a yi qaurace wa lamba goma (10) ya zama aikin hankali? Ai ita lamba goma xin ma, Allah ya faxe ta a wurare da yawa a cikin Alqur’ani Mai girma kuma ta fuska kyakkyawa. Kamar in da Allah ya ce;

﴿ فَمَن لَّمْ يَجِدْ فَصِيَامُ ثَلَاثَةِ أَيَّامٍ فِي الْحَجِّ وَسَبْعَةٍ إِذَا رَجَعْتُمْ ۗ تِلْكَ عَشَرَةٌ كَامِلَةٌ ﴾

البقرة: ١٩٦

*Sa’an nan wanda bai samu ba, sai azumin yini uku a cikin hajji da bakwai idan kun koma, sun zama goma kenan cikakku*[1].

Wannan game da hukunce-hukuncen hajji kenan. Game da lamarin Annabi Musa *Alaihis Salamu* kuwa, sai Allah ya ce;

﴿ ۞ وَوَاعَدْنَا مُوسَىٰ ثَلَاثِينَ لَيْلَةً وَأَتْمَمْنَاهَا بِعَشْرٍ فَتَمَّ مِيقَاتُ رَبِّهِ أَرْبَعِينَ لَيْلَةً ﴾

الأعراف: ١٤٢

*Kuma muka yi wa’adi ga Musa da darare talatin, kuma muka cika su da wasu goma, sai miqatin Ubangijinsa ya cika dare arba’in.*[2]

Kai! Ba ma fa sai an tafi da nisa ba, duba farkon *Walfajri* ka ga abin da Allah ya ce:

﴿ وَالْفَجْرِ ① وَلَيَالٍ عَشْرٍ ② ﴾ الفجر: ١ - ٢

*Ina rantsuwa da alfijir da darare goma (na farkon watan Muharram).*

A cikin Sahihul Buhari, Hadisi ya tabbatar da cewa: “Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kasance yana I’itikafi cikin kwanaki goma na qarshen Ramalana har ranar da ya bar duniya”.[3]

Game da daren Lailatul qadari kuwa, ga abin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Ku Lalube ta cikin ranaku goma na qarshen Ramalana”.[4]

Ga kuma wani hadisin da ya ce: “Babu kwanakin da aikin alheri ya fi soyuwa a wurin Allah cikinsu fiye da kwanaki goma (yana nufin na farkon watan Muharram)”.[5]

Waxannan bayanai da Makamantansu suna da yawan da sun fi qarfin qididdiga.

Wani halin kwan-gaba-kwan-baya da bankaurar mabiya Shi’ah shi ne, lale marhabin da suke yi da lamba tara (9) saboda ximauta da makanta har sun

---

[1] Suratul Baqar, 196
[2] Suratul A’araf, 142
[3] Suratul fajr 1-2
[4] Buhari 3/47-48, Muslim 2/830-831
3- Buhari Kitab As saum, babi na 72 muslim 2/283
[5] Bukuhari 2/20 Tirmizi 2/129

mance da cewa cikin waxancan Sahabbai goma da ba su son a ce an yi wa bushara da aljanna, guda tara ne suke qyama. Ga shi kuma lamba tara (9) ta zo ne a matsayin zargi, da bayanin adadin 'yan daba kamar yadda ya gabata. To, ya kenan?

Kada a manta cewa, sun qaurace ma sunan Abubakar da Umar da Usmanu kuma ba su qaunar duk wani mai sha'awar su, saboda tsananin qiyayya da masu su na asali. Alhali kuwa ko da a ce waxannan mutane sun zama 'yan gaba-gaba ga ayyukan kafirci a duniya, ba wai gaba-gaba a wajen taimakon Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba, wannan ba ya zama dalilin qaurace ma sunayensu. Ai a cikin Sahabbai akwai mai suna Walidu wanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi ma addu'a cewa: "Ya Allah ka kuvutar da Walidu".[1] Ko ka manta da Walidu xan Mugirata na daga cikin manya manyan masu adawa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, wanda har shaguve Alqur'ani ya yi game da shi a *Suratul Muddassir*?

Akwai mai suna Amiru a cikin Sahabbai kamar yadda akwai mai irin wannan suna cikin mushrikai. Haka ma Khalidu da Hishamu da Uqbatu, kai! Har da sunan Aliyu akwai masu irin sa a cikin kafirai, kamar Aliyu xan Umayyata xan Khalafu, kafiri, gamji sai sara.

Tambaya a nan ita ce, wa ya tava cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya umurci Sahabbai da su qaurace ma waxannan sunaye, wai saboda dangantakarsu da wani kafiri? Idan kuwa babu ita ce amsar, to, ina dalilin qyama da qaurace ma sunayen manyan Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*?

A cewarsu wai, Sahabban munafukai ne. Shi ne dalilin da ya sa suke qyamar su. Assha! Magana ta yi muni. Amma kada ku manta da matsayin Aliyu Allah ya yarda da shi a wajenku. Ba kun ce shi ma'asumi ba ne wanda ba ya kure gaba xaya? To, ai ba a ga ya nuna qyamarsa ga xaya daga cikin waxannan manyan waliyai ba. Hasali ma, ya girmama su. Kai! Har ma shi da kansa ya sanya wa wasu daga cikin 'ya'yansa sunayensu.

Gaskiyar lamari dai, musulunci bai hana amfani da sunan duk da bai sava ma Shari'a ba, ko da ko an ambaci wani kafiri da shi. Kuma kangare ma wannan tafarki ba komi ba ne face fito na fito da shari'ar Musulunci. Sunayen Aliyu da Ja'afaru da Hasan da Husaini da suke yawan sa wa, ai ba tabbaci ne cewa duk masu waxannan suna masoya ne ga waxanda ke da sunayen na asali ba.

A wata Sabuwa kuma suna da wata xabi'ar ta wauta, inda suke sammako da maraici a gindin wani dutse mai kogo da ke garin Samarrah. Su kan yi tamatela suna jiran bayyanar Mahadinsu wanda suke da aqidar yana cikin dutsen. Kuma sun tanadar masa ingarman doki taka-hau don da ya

[1] Buhari 6,48-49

bayyana ya garzaya da su zuwa aljannar duniya. Sun girke wani mutum a daidai wurin mai qatuwar murya yana qwalla kira a kai-a kai yana cewa fito maza fito maza Ya Maulana! Sannan wani babban abin da ke xaure kai shi ne yadda suke zagaye wannan bagire xauke da makamai tsoron wai kada a hargage su. Sannan sai su ayyana mutum guda wanda jiddadun za a same shi a tsaye a wannan wuri riqe da makami duk da Sallah babu ruwansa da ita don kada hankalinsa ya xauku har Mahadi ya vullo ba da saninsa ba.

A lokacin da duk suka yi ma wannan wuri nisa kuwa, sai su rinqa fuskantar dabra da wajen suna qwala ihu da kiraye-kiraye cikin gaugawa, wanda babu buqatar yin hakan da a ce gaskiya ne wannan mahadin yana raye. Kuma har Allah ya umurce shi da fitowa. To, ka ga daman ai Allah *Subhanahu WaTa'ala* ya ce:

﴿ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمْ لَهُ ٱلْمُلْكُ ۚ وَٱلَّذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِهِۦ مَا يَمْلِكُونَ مِن قِطْمِيرٍ ﴿١٣﴾ ﴾ فاطر: ١٣

> *Wannan Shi ne Allah, Ubangijinku gare shi Mulki yake, kuma waxannan da kuke kira waninsa ba su mallakar ko fatar gurtsun dabino. Idan kun kira su ba za su ji kiranku ba, kuma ko sun jiya, ba za su karva muku. Kuma a Ranar qiyama za su kafirce wa shirkinku, kuma babu Mai ba ka labari kamar wanda ya sani.*[1]

Wannan ya nuna gara ma 'yan bautar gumaka, waxanda duk da rashin ji da ganinsa amma ga shi gabansu suna kallo, savanin masu zaman jiran gawon shanu.

Idan wani xan Shi'ah ya bugi qirjin cewa shi, babu mai xauke shi daga ra'ayinsa na yarda da samuwar Mahadin nasu, to, ai maganarsa ba ta da banbanci da ta 'yan bautar gumaka da suke cewa, babu mai raba su da ra'ayinsu na cewa tabbas gumukansu za su cece su wurin Allah. Kuma ha kanshi ne dalilin da ya sa suka dage kai da fata suna bauta masu. Da waxannan da waxancan duk ja buge man, saboda jirgin halaka guda ya xauko su, zai kuma sauka da su tashar wahala.

Abin la'akari a nan shi ne, duk da wanda ya riqi mala'iku da Annabawa matsayin ababen bauta bai fita daga zargi da fushin Allah ba, balle wanda ya ciccivi wani mahalukin da ba ma ko xuriyarsa. Duba min gaba ka gani wai makaho ya so tsegumi.

Bugu da qari, har karvar umurni da hani suke yi daga wurin wannan hadarin kaka da Allah bai halitta ba ta hannun malumansu. Alhalin ko Allah Maxaukakin Sarki yana cewa:

[1] Suratul faxir 13-14

﴿ ٱتَّخَذُوٓاْ أَحۡبَارَهُمۡ وَرُهۡبَٰنَهُمۡ أَرۡبَابٗا مِّن دُونِ ٱللَّهِ وَٱلۡمَسِيحَ ٱبۡنَ مَرۡيَمَ وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُوٓاْ إِلَٰهٗا وَٰحِدٗاۖ لَّآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۚ سُبۡحَٰنَهُۥ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ٣١ ﴾ التوبة: ٣١

*Sun riqi Malamansu (Yahudawa) da Ruhubanawansu (Nasara) ababen bauta, baicin Allah, Kuma sun riqi Masihu xan Maryama (haka). Alhalin ba a umurce su ba face su bauta Ubangiji guda. Babu abin bauta wa face shi. Tsarkinsa ya tabbata daga abin da suke yin Shirka da shi.*[1]

Kuma hadisi ya zo a cikin Tirmizi da waninsa, daga Adiyyu xan Hatimu Allah ya yarda da shi ya ce: “Ya Manzon Allah! Ba fa bauta musu su ke yi ba”. Sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Ba suna halalta musu haram ba, kuma suna haramta masu halal, su yi xa’a gare su? To, bautar da suke yi masu kenan”.

A nan idan ka dubi lamarin ‘yan Shi’ah za ka taras da su suna jingina hukunce-hukuncen halattawa da haramtawa ga Imaminsu da suka kira Mahadi, wanda bayani ya gabata cewa, sam babu samuwarsa kuma ko da abin da suka jingina ma Imamin ya ci karo da Alqur’ani da sunna da ijma’in malamai su ba ruwansu. Wautarsu ba ta tsaya a nan ba, ta kai su ga liqa ta ga Imamin nasu duk wata matsala da suka qirqira maras tushe. Qarshe kuma su ce, tafi maganar kowa.

Za a same su suna hanzari wajen misalta waxanda suke qiyayya da su da dabbobi. Wani lokacin ma sukan xauki matakin gana wa dabbar azaba, wai don xebe ta kaicin maqiyansu. Misali, sukan kamo akuya sai su xaure ta, su rinqa tsigar gashinta qarfi da yaji, wai sun ci zarafin Aisha. Kaico!

Wani lokaci kuma sukan samo salka su tsatstsageta da kakide (dasqararren mai). Daga nan sai su zaro wuqa su tsaga cikin salkar, sai kakiden ya bultso sai su rinqa riganganto wajen shan man, suna yi suna Santi, suna cewa, wai jinin Umar *Raliyallahu Anhu* ne suke sha. Ba wannan kaxai ba, sukan bushi iska a wani karon, su kamo jakuna biyu, su raxa wa xaya sunan Abubakar, xayan kuma sunan Umar, su ce, me za su yi in ba lallasa musu azabar duniya ba?

Wannan ya sa watarana da wani sarki ya lura da irin wannan xanyen aiki nasu ya sa aka ciyo kwalarsu, aka tungume su aka xaure ya rinqa gwada masu nau’ukan azaba, a cikin izgili, yana cewa Abubakar da Umar ne ya ke son sai ya ga baya gare su.

Wasu ‘yan Shi’ah kuwa karnuka suke kamowa su basu sunayen halifofin can guda biyu da muka ambata. Suna kiran su suna zagi da tsinuwa suna xebe musu albarka. Wani daga cikinsu kuwa ko karensa ba ya son a

---

[1] Suratul Tauba 31

jingina ma sunayen waxannan bayin Allah. Wanda ko duk ya kuskura ya yi haka, to, faxa ya gama qulluwa a tsakankinsu, ya rinqa kururuwa da kumfar baki kenan, wai don mi ake ambatar karensa da sunan 'yan wuta?!.

Akwai wani gogaggen kafiri wanda ya kashe Sarkin Musulmi Umaru xan Haxxabi har lahira, ana ce masa, Abu Lu'uluata, Bamajuse. Su kuwa wasu 'yan Shi'ah shi suke matuqar girmamawa saboda a ganinsu ya yi namijin qwazo da ya kamata a so shi, a kuma jinjina masa saboda shi.

Harwayau, daga cikinsu akwai masu zuwa maqarbarta su zavi wasu qaburburan da ko kakanninsu ba su san waxanda ke kwance a cikinsu ba. Amma duk da haka, sai su zagaye su, su gina dogayen hasumiyoyi a kansu, kuma su rinqa kai musu ziyara lokaci-lokaci. Kai! Wani lokaci ma har da shirya bukukuwa a wurin, da sunan wai qaburburan Ahlul-baiti ne suke girmamawa. Wataqila ma qaburburan wasu manyan maqiya musulunci ne, amma da yake sun ximauce, sun makance gane ha kan zai wuyata gare su.

Bari a ba da wani gajeren bayani domin masu hankali. Idan aka yi la'akari da waccan aika-aikar mabiya Shi'ah ta azabtar da wasu dabbobi da sunan waxannan Sahabbai sai a ga iyakar wauta sun yi ta. Xauki misalin abin da yake qunshe a cikin kundin tarihin duniya, in da aka zayyana sunayen wasu qeqasassun kafirai irin su Fir'auna da Abu Lahabi da Abu jahali wawa, yanzu yana yiwuwa saboda son musuluncinmu da qyamar matsayinsu, sai mu kamo wasu dabbobi bayin Allah mu ayyana ma kowace dabba sunan xaya daga cikinsu, sannan mu rinqa koxa masu azaba?

A tsarin Shari'ar musulunci, duk da gawar kafiri ba a yarda da tozarta ta ba bayan an kashe shi. Saboda muradin musulunci shi ne ya dakatar da cutar kafirin, kuma ta hanyar kashe shi wannan buqatar ta biya. A kan yi masa haka ne kawai in ya kasance shi ya fara yi wa wani musulmi haka.

An samu ingantaccen hadisi cikin Sahihu Muslim daga Buraidah Allah ya yarda da shi ya ce: "A duk lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* zai tura rundunar yaqi yakan umurci shugaban rundunar da cewa, ya ji tsoron Allah a karan kansa da kuma jama'arsa. Daga nan kuma ya qara da cewa, ku yi yaqi saboda Allah, ku yaqi wanda duk ya kafirce ma Allah, kada ku ci gululi, kuma kada kuyi yaudara. Sannan ku kuma nisanci *Musla'* wato, wulaqanta gawa. Kada kuma ku kashe qananan yara.[1]

A Wani bayani mai kama da wannan, yazo a cikin littafan *Sunan* cewa, Manzon Allah *sallahu alaihi wasallam* ya kasance yana horon mutane da yin sadaqa, kuma yana tsawatar su game da yin *Musula*.

A nan, ya bayyana a fili cewa yin *Musula* ga kafirai bayan mutuwarsu, wulaqanci ne ga halittar Allah. Kuma Shari'a ba ta goyi bayan aiwatar da haka ba, tattare da kasancewarsa kafiri. Kenan su waxancan manyan Sahabbai Allah ya yarda da su, waxanda 'yan-sha-biyu ke aibatawa tare da nuna qiyayya gare su, ko da a ce tun farko su ba musulmi ba ne, to, wannan ba zai zama lasisin

[1] Muslim, 3/11356

wulaqantar da gawarsu ba ta hanyar duka ko tsage sashen jiki ko tsigar gashin gawar, balle maganar azabtar da wata dabba da sunansu. Wannan bai ko taso ba tattare da cewa azabtarwar ba za ta kai ga jikin Sahabban ba.

Daga cikin shiriritarsu, suna shirya bukukuwan baqin ciki da koke-koken tuna rasuwar malamansu, da wasu mutane. Tabbas wannan na nuna cewa sun jahilci haramcin kukan mutuwa da bukukuwan makokin a addinin musulunci. Kamar yadda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Wanda ya mari fuska, ya keci wuyan riga, ya yi hargowar jahiliyya, to ba shi tare da mu". [1]A wani hadisin kuwa cewa ya yi "Na barrantar da kaina daga mace mai aske kanta da mai hargowa a lokacin faruwar wata musiba, da kuma mace mai kece tufafinta" [2]. A wani wurin kuma ya ce: "Ana azabtar da mamaci saboda kukan da ake fasa masa." [3]

Za ka ga 'yan Shi'ah sun fi kowa aikata ayyukan jahiliyyah, kamar marin fuska, da keta tufafi, da iface-iface. Duka wai don tuna wata tsohuwar musiba. Kuma baka tava jin sun yi wa wani daga cikin bayin Allah da aka yi wa kisan zalunci daga cikin Annabawa da Waliyyai ko qyasham ba. Abin da yake nuna maka cewa, ko Husainin ma dai a lava ga sabara ne a harbi barewa. In ba haka ba, me ya sa ko mahaifin nasa ba sa yi masa kuka? Ashe ba kisan sharri ne shi ma aka yi masa ba? Ba sai mun tambaye su ba game da Usmanu xan Affana wanda aka yi wa kisan gila yana a matsayin halifan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a kuma cikin birnin Manzo yana rungume da Alqur'ani ba. Ba za mu tambaye su don me ba su yi masa kuka ba, domin mun riga mun san matsayinsu a kansa. Amma dai duk mai hankali ya gani a tarihi irin musibar da ta cimma musulmi a sakamakon kisan Usman, ba a tava ganin aukuwar irin ta ba ko a lokacin da aka kashe Husaini. Amma waxannan musibun sun wuce. To, mine ne na tashintashina?

Abin da 'yan Shi'ah ke yi xin nan kuwa babban dalili ne a kan wautarsu. Domin babu wani mai kiran kansa musulmi da ke yin irin wannan xabi'a in ba su ba. Wautarsu ba a nan ta tsaya ba. Yanzu haka dai wasu daga cikinsu ba su qona wata itaciya da ake kiya *Xarfa'u* wai don sun ji an ce jinin Husaini ya zuba ga reta! To, in banda wauta wa ya ce ba a qona itace idan wani jini ya zuba a kansa? Kuma ma shin wannan iccen shi ne yake har yanzu a cikin dazuzzuka? Irin waxannan abubuwa na wauta a cikinsu suna da yawa. Kuma tun farkon vullar Shi'ah a zamanin Tabi'ai ake hikaito irin waxannan labaran game da su, ga su ko har yau ba su bari ba.

Don mu yi masu adalci, dole ne a nan mu faxi cewa, ba dukkan ayyukan wauta da 'yan Shi'ah ke yi suka kevanta da 'yan-sha-biyu ba. A'a, wasunsu an fi sanin su ne a wajen sauran qungiyoyin Shi'ah, musamman dai Gulatu. Haka kuma wasu abubuwan da jahilan 'yan Shi'ah ke qudurtawa, malamansu ba su

[1] Buhari, (2/82). Muslim, (1/100)
[2] Muslim, (2/644). Buahri (2/80.) . a nan idan shi mamacin ne ya bada wasiccin fasa masa kunka kenan kamar yadda ake yi a zamanin jahiliya ko kuma yaqi karantar da iyalinsa. Masu fassara.
[3]

fatawa da su, kamar haramta cin naman raqumi, da kuma cewa sharaxi ne sai mace ta yarda da saki kafin ya tabbata.

### 1.4 Shaidar Malamai a Kan 'Yan Shi'ah

A baya an ambaci wani littafi mai suna *Minhajul-Karamati.* Amma a haqiqanin gaskiya kamata ya yi sunan nasa ya kasance *Minhajun- Nadamati.* Domin kuwa nadama littafin ya qunsa ba karama ba. A cikin rubutun, marubucin ya bi sawun malamansa ne a duniyar Shi'ah irin su Mufid da alamjiransa kamar Xusi da ire-irensa.

Irin waxannan rubuce-rubuce na 'yan-sha-biyu ba abin da ke cikinsu sai qarya, irin wadda ke nuna su a fili, a matsayin manyan-manyan jahilai a sararin Subhana. Taqama kawai suke yi da harkar ilimi da nazari, amma abin ba haka yake ba. A haqiqa, idan kana neman mutane marasa kan gado, ga kuma qarfin hali a fagen qin ba nazari haqqinsa, to, da zarar ka yi kicivis da xayansu, to, haqarka ta cimma ruwa. Duk abin da suka dogara a kansa za ka taras ruvavve ne, da ya kamata a saka kwandon shara.

Malamansu naji da faxi, ba su da hanya qwaqqwara ta karvar riwaya sai ga azurakan mutane irin su: Abu Mikhnaf Luxu xan Yahya da su Kalbi, waxanda ma'abuta ilimi suka bada shedar cewa, shahararrun maqaryata ne su. Masana sirrin riwayoyin hadisi kuma, sun ba da shaidar cewa, 'yan shi'a na daga cikin manyan maqaryata a duniya.

Malam Razi Baban Hatim ya riwaito daga Malik wanda aka tambaya game da matsayin 'yan Shi'ah sai ya ce: "Ba a shiga batun su, kashedinka da karvar maganarsu, don gwanayen qarya ne su". Baban Hatim kuma ya riwaito daga Imamus Shafi'i cewa: "Ban tava ganin maqaryatan mutane irin 'yan Shi'ah ba". Shi kuwa mashahurin malamin nan Yazidu xan Haruna cewa ya yi: "Ana iya karvar riwayar kowane xan bidi'a idan ba ya tallar ta, amma banda 'yan Shi'ah, saboda maqaryata ne".

Haka shi ma Malam Shariku, alqalin Kufa, wanda ya zauna da su, ya kuma san su sarai, kai, yana ma cikin almajiran sayyidina Ali ga shaidar da ya bayar a kansu: "Ana iya karvar ilimi a wajen kowa banda 'yan Shi'ah. Saboda sun iya qera hadisan qarya, kuma sun xauki yin ha kan wata hanya ta shiga Aljanna".

Haka kuma Malam Sulaimanu xan Mahrana wanda aka fi sani da A'amash yana cewa: "Qarya a wajen 'yan Shi'ah ba bakin komai take ba. Babu mamaki ka ji su suna yaxa cewa sun kama wani malami na Allah da wata, saboda tsabar qazafi".

Waxannan bayanai babu za'ida a cikinsu. Duba su a cikin *Al –Ibanatul–Kubra* na Ibnu Baxxata. Shi ma Abul–Qasim Al-Xabari ya riwaito cewa Imamus-Shafi'i ya ce: "Ban ga waxanda suka zarce 'yan Shi'ah iya qarya ba a duk cikin qungiyoyin bidi'a baki xaya".

Saqon da ake son a iyar a nan shi ne, malamai na duniya kaf sun fayyace cewa, 'yan Shi'a su ne limaman maqaryata. Kuma har tinqaho suke yi

da wannan matsayi. Suna cewa, mu addininmu duk taqiyyah ne. suna nufin halalta wa kansu fesa qarya a duk sadda suka ga dama. Wannan kuwa ba wani abin mamaki ba ne ga wanda ya san asalinsu.

Tattare da haka kuma sai ka ga suna zungurar magabatan wannan al'umma da cewa wai, gaba xaya sun yi ridda; sun bar lemar Musulunci.

Da 'yan Shi'ah suna da ganewa sun fi kowa cancantar waxannan sifoffin da suke jingina wa zavavvin bayin Allah. Saboda a duk lokacin da mutum ya tashi neman waxanda suke ridda da munafucci da zarar ya ci karo da gungun 'yan Shi'ah haqarsa ta cimma ruwa. Idan kuma a na son gano gaskiyar wannan zance, mutum ya yi nazari, game da rassan Shi'ah irinsu *Galiyyah*, da *Nusairiyyah* da *Isma'iliyah*. Duk wanda ya leqa ciki da wajensu, zai ga abin mamaki, kuma cikinsa zai xuri ruwa, ya juyo a firgice saboda gigita da tsoro game da zurfin tavarvarewar lamarinsu.

A sashen hukunce-hukuncen shari'ah ‘yan Shi'ah suna dogara ne kacokan ga riwayoyi waxanda aka ce an naqalto su ne daga *Ahlulbaiti* duk da yake mafi yawan riwayoyin na qarya ne. Su kuwa ba su iya tantancewa tsakanin ingantaccen Hadisi daga mai rauni ba. Idan ma an saki kari cewa, Hadisan da ake riwaito masu ingantattu ne, to, ba su kai ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba. Amma sai suka gina wasu harsasai guda uku na shirme don su tabbatar da dacewar su karvi waxannan riwayoyin. Waxannan harsasan sun haxa da; cewa, kowanne daga cikin *Ahlulbaiti* ma'asumi ne; yana kafaxa-da-kafaxa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.* Na biyu kuma wai, duk abin da zai faxi tsararre ne. Na uku kuma duk abin da *Ahlulbaiti* suka yi ijma'i a kansa ya zama hujja. Kuma faxar xayansu ba ta kasancewa sai in sun yi ijma'i akan abu.

Waxannan abubuwa su ne tubalan da suka gina karvar riwayoyinsu a kai. Idan aka lura da kyau, su, ba su xauki Alqur'ani mai girma da muhimmanci ba, balle ya zama tushen da suke dogara a kansa. Haka ma Hadisi, to, balle kuma ijma'i ko qiyasi.

Maganar hankali da qiyasi a wurin ‘yan Shi'ah yana ta'allaqa ne ga rubuce-rubucen Mu'utazilawa waxanda a wani gefen sun xara 'yan Shi'ah hankali. Abin da ke nuna maka haka, shi ne, mu'utazilawa basu tava yin suka ga halifancin Abubakar da Umar da Usmanu Allah ya yarda da su ba. Magabatansu suna fifita Abubakar da Umar a kan sauran Sahabbai. Su kuwa 'yan bayansu sun kame baki ba su ce komai ba. Amma an samu kaxan da suka fifita Aliyu *Raliyallahu Anhu* a kan sauran Sahabbai *Raliyallahu Anhu* a nan ne ra'ayinsu ya zo xaya ba banbanci da na Zaidiyyah tare da cewa ba su yi ja-in-ja ga halifancin waxanda suka gabaci Aliyu xin ba. Harwayau wani sashe na Mu'tazilawa sun yi qawance da Zaidiyyah a gefen maganar Adalci da Imamah da fifita Ali a kan Usman.

## 1.5 Wai Imamah Ita Ce Tushen Addini!

'Yan-sha-biyu sun tafi a kan cewa, idan ana magana game da tushe da asalin addini, to, shugabanci na gaba ga komai. Mai littafin da muke magana a kansa ya ce, muhimmancin littafin nasa yana da girma saboda yana qunshe da bayanin manyan mas'aloli waxanda suka shafi hukunce-hukuncen addini da kuma sha'anin shugabanci, wanda ta hanyarsa ake kai wa ga daraja maxaukakiya don kasancewar sa xaya daga rukunan Imanin da ake samun shiga Aljanna da tsira daga dukan fushin Allah. A kan haka ne ma a cewarsa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Wanda duk mutuwa ta riske shi ba a qarqashin wani shugaba ba, to, ya yi mutuwar jahiliyyah".

Marubucin ya nemi kusanci da rubuta littafin nasa ne zuwa ga wanda ya kira shi *Sarkin Sarakuna* Ulijayo Khudabandah, bayan ya yi masa yabo wanda ya wuce iyaka. Sannan ya sa masa suna "*Minhajul Karamati Fi Ma'arifatil Imamati*". Ya kuma yi masa tsarin fasali-fasali kamar haka:

- Fasali na Xaya: Bayanin Mazhabobi game da wannan mas'ala.
- Fasali na Biyu: Wajibi ne abi ra'ayin Shi'ah 'yan-sha-biyuh ga wannan mas'ala.
- Fasali na Uku: Dalilai masu tabbatar da shugabancin Aliyu *Raliyallahu Anhu* bayan rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.
- Fasali na Huxu: Bayani a kan Imamai goma sha biyu.
- Fasali na biyar: Kakkausan suka game da shugabancin Abubakar da Umar da Usman *Raliyallahu Anhum.*

Tun a karon farko maganarsa cewa, shugabanci shi ne tushe, kuma shi ne mafi girman mas'ala cikin lamurran addini a wajen Musulmi, wannan zancen banza ne. Kuma yarda da hakan kafirci ne. Domin yin Imani da Allah da Manzonsa na gaba ga sha'anin shugabanci. Wannan shi ne abin da Malaman Shi'a da kansu suka yi ijma'i a kansa balantana Malaman Sunnah. Wannan kuma abu ne da ya zama tilas kowa ya sani. Babban Misali shi ne Kalmar Shahada wadda ita ce babbar qofar shiga musulunci. Kuma a kanta ne aka yi xauki ba daxin duk da ya gudana a tsakanin musulmi da waxanda ba musulmi ba.

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "An umurce ni da in yaqi mutane har sai sun sheda babu wanda ya cancanci bauta sai Allah. Su kuma shaida cewa, ni Manzon Allah ne. Su kuma tsayar da sallah, su ba da zakkah. Idan suka yi haka, sun kare jinainansu da dukiyoyinsu sai da dalili.

Haka kuma Allah Maxaukakin Sarki ya ce:

﴿ فَإِذَا انسَلَخَ الْأَشْهُرُ الْحُرُمُ فَاقْتُلُوا الْمُشْرِكِينَ حَيْثُ وَجَدتُّمُوهُمْ وَخُذُوهُمْ وَاحْصُرُوهُمْ
وَاقْعُدُوا لَهُمْ كُلَّ مَرْصَدٍ ۚ فَإِن تَابُوا وَأَقَامُوا الصَّلَاةَ وَآتَوُا الزَّكَاةَ فَخَلُّوا سَبِيلَهُمْ ۚ إِنَّ
اللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿٥﴾ ﴾ التوبة: ٥

*Kuma idan watanni masu alfarma suka shige to, ku yaqi Mushrikai inda duk kuka same su, kuma ku kama su ku*

*zaune musu dukkan madakata. To, idan sun tuba, kuma suka tsayar da Sallah, kuma suka bayar da zakka, to, ku sakar musu da hanyarsu. Haqiqa, Allah mai gafara ne, mai jinqai. Suratut Taubah: 5*

Kuma a lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya naxa Aliyu *Raliyallahu Anhu* a matsayin kwamanda zuwa Haibara, farkon abin da ya umurce shi da shi, shi ne ya fara kiran mutane zuwa ga Imani da Allah da Manzonsa. Ka ga a nan bai ce masa ya kira su ga imani da shugabanci ba. Sa'annan a duk lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya samu rinjaye a kan wasu kafirai, farkon abin da yake shimfixa masu shi ne Imani da Allah da Manzonsa.Wannan ita ce hanyar kiyaye alfarmar jini da dukiya. Wannan ya zo daidai da faxar Allah Maxaukakin Sarki:

﴿ فَإِن تَابُواْ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُاْ ٱلزَّكَوٰةَ فَإِخْوَٰنُكُمْ فِي ٱلدِّينِۗ وَنُفَصِّلُ ٱلْأَيَٰتِ لِقَوْمٍ يَعْلَمُونَ ﴿١١﴾ ﴾ التوبة: ١١

*Sa'anan idan sun tuba kuma suka tsayar da Sallah, kuma suka bayar da zakka, to 'yan'uwanku ne a cikin addini. Suratut Taubah: 11*

Dubi yadda Allah a nan ya ambace su a matsayin 'yan'uwa a addini dalili da tubar da suka yi. Kuma a duk lokacin da wasu suka rungumi musulunci a hannun Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama,* ba tare da wata-wata ba yakan karve su a cikin farin ciki hannu biyu-biyu ba tare da an tsaya bincike, ko nuna masu wani matsayi ba game da lamarin shugabanci. Bugu da qari, babu ko samatar samun wani Hadisi ko bayani wanda ke nuna buqatar yin hakan ga duk wanda ya karvi musulunci.

A zahiri wannan ya nuna babu hanyar da za a zagayo cikin Musulunci har a iya nuna cewa mas'alar shugabanci ita ce mafi zama a'ala a gefen girma da muhimmanci. Idan kuwa a lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yake raye lamarin shugabancin bai zama wani rukuni da saninsa yake wajibi ba, wane ne ya isa daga baya ya lizimtar da shi a matsayin rukunin addini?

Wata tambaya muhimmiya a nan ita ce, ashe akwai wasu mutane mafiya xaukaka da daraja fiye da jama'ar da suka rayu da Imaninsu tare da mafificin halitta *Sallallahu Alaihi Wasallama*? Domin kuwa ya aka yi su ba su xauki wannan mas'ala da girma ba? Ba su fahimta ba ne, sai ku a yanzu kuka samu fahimta?

Abin da ya kyautu a gane a nan shi ne, ko da an xauka cewa sha'anin shugabanci da matsayinsa zai yiwu ya canza salo daga zamani zuwa wani, to, xaukar sa a matsayin mafificin abu katovara ce ta kai tsaye. Domin kuwa babu lokacin da ya kamata shugabanci ya yi qima da alkadari kamar zamaninsa *Sallallahu Alaihi Wasallama*. idan ko har ba a bashi wannan matsayi ba a zamaninsa, to, ya ko za a yi ya samu wannan matsayi daga baya?

Amma abin da yake tabbas shi ne, ita mas'alar Imani da Allah da Manzonsa, a kowane zamani ko yanayi ita ce mafi muhimmanci a musulunci. Don haka, duk wanda ya iya shata wani lokaci da cewa shugabanci a cikinsa ya shiga gaban komi har Imani da Allah, to ya shigar da kansa a cikin sarqaqiya.

To, idan ma haka ne, cewa shugabanci shi ne tushe mafi girma a musulunci, ya aka yi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* har ya bar duniya bai bayyana haka ba, kamar yadda ya bayyana matsayin Imani da Allah da ranar Lahira da Sallah da Azumi da Zakka da Ayyukan Hajji?! Kuma dukan waxannan abubuwa babu wani nassi wanda ya kusanci kwatanta su da matsayin shugabanci.

Idan kuma 'yan Shi'ah suka dage a kan cewa lalle sha'anin shugabanci shi ne mafi muhimmanci har a zamanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* wai saboda ganin cewa shi Annabin ne da kansa yake shugaba kuma Manzo a lokaci guda, sai mu ce, to, saurari waxannan bayanan:

**Bayani Na Xaya:**

Ko da wannan ya inganta, to, ba zai yiwu a ce, shugabanci ne a gaban sahun sauran lamurran addini ba, sai dai ko a ce, a wasu lokuta yana da qarfin matsayi. To, kuma a lokacin da ya fi kowane daraja ba ta zama mafi muhimmanci ba, to, yaushe za ta zama?

**Bayani Na Biyu:**

Har abada imani da Allah da gasgata manzanni ya fi maganar shugabanci qarfi. Wannan ita ce aqidar musulmi.

**Bayani Na Uku:**

In da haka ne, da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi gaggawar sanar da al'ummarsa kamar yadda ya bayyana masu sauran addini.

### 1.6 Wane Shugabanci ne ya fi?

Shi wannan xan Shi'ar da ya tafi a kan cewar shugabanci shi ne lamari mafi muhimmanci ga addini muna bin sa bashin bayani. Shin yana nufin cewa shugabancin Imamansu goma sha biyu ne? Ko kuwa kowanne daga cikinsu shugabancinsa a zamaninsa? Ko dai yana nufin yarda da mas'alar baki xayanta? Ko kuma yana nufin wata ma'ana ce ta daban?

Idan yana nufin shugabancin sha biyu ne da suke cewa, to, ai a zamanin Sahabbai da Tabi'ai ba a san shi ba. Kuma ma su kansu 'yan Shi'ar cewa suka yi ba a sanin kowane Imami sai na gaba da shi ya ayyana shi. To, ya imani da abin da yake haka ke zama wajibi ballantana mafi girman wajibai?

In kuma yana nufin imani ne da kowane Imami a lokacin bayyanarsa, to, kenan tun daga shekara ta 260H har zuwa yau kuma har abada imani da voyayyen Mahadin da ba a tava gani ko aka ji xuriyarsa ba, ya fi imani da Allah da Manzonsa?

In ko ya ce, a’a, shi fa yana maganar yarda da shugabanci ne a dunqule. Sai mu ce, wane irin dunqulallen abu ne wannan da ya zarce imani da Allah da Manzonsa, kuma ya fi sallah da azumi da zakkah da hajji? Ku dai sake tunani!

In ko kuna da wata ma’ana da kuke nufi, to, ku bayyana muna ita!

Bayan wannan ana iya tsokaci ga wani vangare mai qarfi ainun wajen ruguza wancan tunani, tsokacin shi ne, kasancewar ba a wajabta ma mutane biyayya ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba saboda kawai yana a matsayin shugaba, amma an wajabta haka ne saboda matsayinsa na Manzon Allah zuwa ga mutanen duniya baki xaya. Wannan shi ne matsayin da har qasa ta naxe ba zai canza ba. Kuma shi ne babban dalilin da ya sa xa'a zuwa gare shi a cikin kowane zamani ta zama tilas ga waxanda suka rayu tare da shi da waxanda suka zo bayan rayuwarsa.

Bayanai da dama ne za su iya qarfafa abin da ya gabata. Domin akwai yanayin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* zai yi umurni ko ya zartar da hukunci ga wani mutum guda ko wasu mutane, amma duk da haka sai hukuncin ya zarce ya shafi kowa da kowa. Kamar dai a lokacin da ya gargaxi wasu daga cikin Sahabbansa Allah ya yarda da su inda ya ce musu: “Kada ku rigaye ni yin ruku'i da Sujada”. Ka ga wannan hukuncin bai tsaya a kan waxancan jama'a kawai ba. A madadin haka, hukuncin ya shafi duk wani masallaci da ke koyi da liman a halin yin Sallah.

Haka kuma a wani lokaci wani ya yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* tambaya game da aikin Hajji cewa, na gabatar da yin aski kafin yin jifa a cikin rashin sani. Sai ya amsa masa da cewa: “Jifarka ta yi daidai”. To, shi ma wannan hukunci irin wancan ne; bai tsaya a kan mai tambayar kawai ba, a'a. Duk wanda ya sami kansa cikin irin wannan hali babu laifi a kansa.

Ga kuma qarin wani misali wanda a lokacin da jinin Haila ya riski uwar muminai Aisha *Raliyallahu Anhu* alhali tana cikin harama da Umrah, sai ya ce mata: “Ki ci gaba da sauran ayyukanki na Hajji, xawafi ne kawai ba zaki yi ba”. Ire-iren waxannan misalai su ke nuna banbancin da ke tsakanin biyayyar da ake yi wa Annabawa, da irin wadda ake ma Sarakuna da shugabannin siyasa a kowane zamani.

A gefen halifofin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuwa, musamman waxanda suka biyo bayan wafatinsa, ba su banbanta ba daga wakillansa na zamanin rayuwarsa, a inda za ka tarar cewa, da zarar wani wakili ya ba da umurni, xa'a a gare shi ta zama wajibi. Dalili kuwa shi ne, umurnin nasa tamkar na Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne. Allah Maxaukakin Sarki ya ce:

﴿ وَمَا مُحَمَّدٌ إِلَّا رَسُولٌ قَدْ خَلَتْ مِن قَبْلِهِ ٱلرُّسُلُ ۚ أَفَإِيْن مَّاتَ أَوْ قُتِلَ ٱنقَلَبْتُمْ عَلَىٰٓ أَعْقَٰبِكُمْ ۚ وَمَن يَنقَلِبْ عَلَىٰ عَقِبَيْهِ فَلَن يَضُرَّ ٱللَّهَ شَيْـًٔا ۗ وَسَيَجْزِى ٱللَّهُ ٱلشَّٰكِرِينَ ﴿١٤٤﴾ ﴾ آل عمران: ١٤٤

*Kuma Muhammadu bai zama ba face Manzo, Lalle ne Manzanni sun shuxe a gabaninsa. Ashe idan ya mutu ko*

*kuwa aka kashe shi, za ku juya a kan dugaduganku? To, wanda ya juya a kan dugadugansa, ba zai cuci Allah da kome ba. Kuma Allah zai saka wa masu godiya.*

Wannan ayar ta fayyace cewa, mutuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba za ta dakatar da matsayinsa na Manzo ba. Amma yanzu da zarar wani basarake ko shugaba ya wuntsile ya mutu, sai a xauki muqaminsa a naxa wa wani domin shi an rufe nasa faifan, ya gama nasa ya yi kenan.

Haqiqa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya isar da Mazanci, ya kiyaye amana tare da shimfixa adalci, ya baza nasiha cikin al'umma, ya taimaki addinin Allah da gaske, kuma ya kafu ga bautar Allah. Haka lamarinsa ya kasance har ya koma ga Mahaliccinsa. Wannan Shi ya sa xa'a gare shi ta zama dole, yana raye ko bayan wafatinsa. Domin bayan rasuwarsa addinin Musulunci bai buqaci wani ragi ko qari ba, kuma wannan shi ne musabbabin zaburar Sahabbai Allah ya yarda da su wajen tattara Al-qur'ani mai girma a waje xaya.

Amma kuma duk da haka, wani na iya shan iska ya ce, ai shi Annabin da kansa ya zama shugaba ne kawai a halin da yake raye, domin kuwa bayan rasuwarsa shugabanci ya koma ne a wuyan wani wanda ba shi ba. Mu kuma sai mu ce masa, kana so ne ka ce bayan rasuwarsa akwai mutumin da ake yi wa biyayya kamar yadda ake yi masa? Idan wannan ita ce manufarka, ai kuwa kowa ya sheda cewa wannan maganar wofi ce. Idan kuma yana so ne ya ce, yana nufin bayan wucewarsa an samu wakilinsa wajen zartas da lamurran da suka shafi umurni da haninsa, sai a ce da shi wannan ba baquwar magana ba ce, saboda ko a lokacin da yake raye ba baqon abu ba ne cewa, yana wakilta wani musamman lokacin da zai yi wata tafiya.

In aka ce, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba ya umartar wani bayan rasuwarsa, amma lokacin rayuwarsa yana yin haka. Sai mu ce, umurnin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da ya bayar a lokacin rayuwarsa yana wajaba a yi masa xa'a ga wanda ya ji shi kai tsaye, da wanda maganar ta kai gare shi daga baya. Daman ko ai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: *"Wanda duk ya halarci maganata ya isar da ita ga wanda bai halarta ba. sau da yawa wanda aka isar wa da saqo yakan fi wanda ya isar kiyaye saqon".*

In an ce lokacin da yake raye yana hukunci a kan hukunce-hukunce na musamman, misalinsa shi ne; ba wani mutum kyauta, da zartar da haddi a kan wani mutum, da aika wasu sanannun mayaqa zuwa wani wuri. Sai a ce haka yake. Yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* xa'a wajibi ne ga abubuwan da ke kama da haka har ranar qiyama, savanin shugabanni. kodayake mai yiwuwa kafa dalili a kan abin da ya yi kama da wannan, zai iya wuyata. Kamar yadda ilimin abu na voyuwa ga wanda bai halarci abin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya faxa ba.

Wanda ya halarci abu shi ya fi sanin abin da Manzo ya faxa, kuma ya fi wanda bai halarta ba fahimta, kodayake ana iya samun waxansu da aka isar da

saqon gare su, su fi waxanda suka ji maganarsa kiyaye umurnisa. Wannan fifikon tsakanin mutane yana da nasaba da sanin umurni ko hanin da Manzo ya yi ne kawai. Amma ba shi da wata alaqa da fifikon wajabcin yi wa Manzo xa'a.

Babu banbanci tsakanin wajabcin yi wa shugabanni xa'a a rayuwar Manzo, da yi masu ita bayan rasuwarsa. Wajabcin yi masa xa'ar ya game duk bayi bai xaya. Kodayake ana samun banbanci wajen hanyar isar da saqon, jinsa da fahimtar sa, wasu na samun saqon manzo game da wani lamari, wasu kuma su sami wani saqon nasa wanda wasu ba su samu ba. Saboda haka mutanen farko na fahimtar wani lamari nasa wanda mutane na biyu Ba su fahimta ba. Duk wanda ya yi umurni da abin da Manzo ya yi umurni da shi, to, ya wajaba a yi masa xa'a don biyayya ga Allah da Manzonsa, ba don xa'a ga wanda ya yi umurnin ba.

Idan mutane nada shugaba mai qarfi wanda ke umurni da abin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi umurni da shi, kuma yake hukunci da irin hukuncinsa, to, lamurransu za su daidaita. Saboda haka ba ya halalta a sa wani shugaba ba shi ba. Ba ya yiwuwa a samu wani mutum kamar sa bayan wucewar sa, ana dai samun wanda ya yi kusa da shi, wanda ya fi cancanta ya zama mai maye wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, saboda ya fi kusanci ga yin umurni da abin da Manzo yake umurni da shi da kuma hani ga abin da Manzo ya yi hani da shi.

Sanannen abu ne cewa, ba a cika yin xa'a ba ga umurninsa a mafi yawan lokuta sai in ya kasance mai cikakken qarfi da ikon da zai tilasta ma jama'a yin xa'a. Don haka dole ne ya kasance ya samu waxanda suka saxaukar da rayukansu don tabbatar da an yi masa xa'a. Addini dai dukansa xa'a ne ga Allah da Manzonsa. Duk wanda ya yi wa Manzon Allah xa'a to ya yi wa Allah xa'a.

Addinin Musulunci ko bayan rasuwar Manzo, yana nan a matsayinsa na xa'a ga Allah da Manzonsa. Xa'a ga shugabanni a cikin abin da Shari'ah ta ce ayi musu xa'a, shi ma xa'a ne ga Allah da Manzonsa.

Wannan ne ya sa tushen addini shi ne gasgata cewa, babu wanda ya cancanci bauta in ba Allah ba, da kuma cewa Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* Manzon Allah ne.

Idan Shi'a 'yan-sha-biyu sun ce: Hankali ya nuna wajabcin shugabanci, amma bai nuna Manzanci ba. Saboda haka shugabanci ya fi muhimmanci ta wannan fuskar. Sai a ce masu: to, ai ba gaba xayan malamai ne suka yarda da cewa, hankali na wajabta wani abu ba. To, in ma mun yarda da waxanda suka ce hankali na wajabta haka, sai mu ce abin da hankali ke wajabtawa na al'amarin shugabanci, kaxan ne cikin al'amurra na hankali. Don ko ai hankali ya yarda da kaxaita Allah da bauta, kamar yadda ya yarda da faxin gaskiya, adalci da makamantansu.

Haka kuma, duk wanda ta tabbata wurinsa cewa Muhammadu Manzon Allah ne, kuma ta tabbata cewa yi masa xa'a wajibi ne a kansa, ya kuma yi iyakar qoqarinsa wurin yin masa xa'a gwargwadon iko, Tabbas wannan zai shiga aljanna bai da buqata zuwa ga matsalar shugabanci. Duk ko wanda ya ce

mai irin wannan ingantattar aqida ba zai shiga Aljanna ba, to, yana ban hannun makaho da nassoshin Al-qur'ani. Don ko sanannen abu a musulunci shi ne cewa, Allah ya wajabtar da Aljanna ga wanda ya yi imani da Allah da Manzo kuma ya yi musu xa'a.

Allah Maxaukakin Sarki ya ce:

﴿ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ فَأُوْلَٰٓئِكَ مَعَ ٱلَّذِينَ أَنۡعَمَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِم مِّنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ وَٱلصِّدِّيقِينَ وَٱلشُّهَدَآءِ وَٱلصَّٰلِحِينَۚ وَحَسُنَ أُوْلَٰٓئِكَ رَفِيقٗا ﴿٦٩﴾ ﴾ النساء: ٦٩

*Duk wanda ya yi wa Allah xa'a da Manzonsa waxannan suna tare da waxanda Allah ya yi ma ni'ima na daga cikin Manzanni da Shahidai da Salihai. Waxannan abokan arziki. Suratun-Nisa'i: 13*

Shi dai Mahadin naku, mutane ba su da hanyar sanin sa, kuma ba hanyar sanin abin da yake umurni da shi da abin da yake hani da shi, da labaran da yake bayarwa. Idan mutum ba zai sami tsira ba sai ya yi wa irin wannan Mahadin naku xa'a, duk da yake ba a iya sanin me yake umurni kuma me yake hani, kenan babu wanda zai kai ga hanyar tsira.

In sun ce abin ba haka yake ba, domin idan Mahadin ya bayyana zai ba da umurnin a yi abin da 'yan Shi'ar sha biyu suke a kai. Sai a ce: to babu buqatar kasancewarsa kenan. Domin abin da 'yan Shi'ah ke a kai sananne ne ko da shi Mahadin ko babu shi. Daga nan za a san cewa, babu buqata ga samuwarsa. Kuma xa'a ga Allah ba ta rataya a kansa ba, balle samun tsira. Anan ne muke cewa, ba shi halasta iqirarin shugabancin irin wannan mutum, ballantana a ce wajibi ne a yarda da shi a matsayin haka. Wannan abu ne da yake bayyane ga wanda ya yi tunani amma 'yan Shi'ah sun fi kowa jahilci don ba su tunani.

A kan haka, babu dalilin da zai sa 'yan Shi'ah su rataya tsirar halittar Allah a kan wannan aqida ta Mahadi. Musamman da yake yau da gobe ta tabbatar da kasancewar ta tatsuniya.

Idan kuwa har suka nace a kan haka, to, lalle ne xayan abubuwa biyu zai tabbata. Wato maganarsu ta zama qarya muraran bisa hujjojin da muka gabatar. Ko kuma kamar suna cewa ne Allah Maxaukakin Sarki ya haramta wa bayinsa samun rahamarsa, qarshe kuma zai tattara su ya zuba wuta. Idan kuwa har haka ta tabbata to, su ne farkon waxanda suka tave, waxanda kuma za a azabtar, don ba su da wata masaniya da komai daga Mahadin nasu balle su nemi tsira. Iyakar abin da suka sani 'yan riwayoyi ne daga malamansu da ba su taka kara sun karya ba dangane da shi.

In ko har wani xan Shi'a ya ce mana ya riwaito wani abu daga wurin wannan Mahadin to, tabbas shi maqaryaci ne.

Na ga wasu Malaman Shi'ah kamar Ibnul-Udi Al-hilli yana cewa: "Idan 'yan Shi'ah suka yi savani game da wani abu a kan ra'ayi biyu, to, duk ra'ayin da ba a san mai shi ba shi ne gaskiya, don kuwa Mahadinmu yana a cikin sa".

Wannan ita ce magaryar tuqewa ta jahilci da vata. Domin ko me zai hana in har akwai Mahadin ya zan yana cikin masu xaya ra'ayin, amma ba a faxe shi ba don ba a gan shi ba balle aji ra'ayinsa?

Asalin da 'yan-sha-biyu suka gina addininsu a kai shi ne, abin da ba a sani ba da abin da babu shi. Suna zaton cewa, wannan shugaban nasu akwai shi kuma ba ya kuskure, alhali kuwa ba a san inda yake ba, kuma babu shi, da kuma shi samamme ne wanda ba ya kuskure, su ma sun yarda cewa, ba a iya sanin umurninsa da haninsa, tun da ba a ganin shi.

A kan haka babu yadda 'yan-sha-biyu za su yi su tabbatar mana da wanzuwar wannan Mahadi balle shugabancinsa. Dalili kuwa shi ne shugaba, wato Imami, na karva wannan suna ne, a lokacin da ake iya saduwa da shi, ya kuma yi umurni a bi, ko dole. Idan kuwa haka ta faskara, to, duk wata hanya da za a bi don tabbatar da wanzuwar sa waqa ce kawai da baqar wahala. Kuma gaba xayan malaman Shi'ah ba su musun haka. Domin sun tafi tare da malaman da suka yarda da cewa, hankali na iya sanin abu mai kyau da mummuna.

In waxannan Shi'a 'yan-sha-biyu suka ce, imaninmu da wannan ma'asumi da ake jira kamar imanin da 'yan xariqa ke yi ne, game da Ilyasu, da Khadir, da Gausi da Quxubi da mutanen gaibi, waxanda ba a tabbatar da samuwarsa ba balle a san abin da suke umurni da hani. Duk wanda ya yarda da mutanen da aka ambata xin nan ba zai qi yarda da samuwar Mahadinmu ba.

To, bari mu ba ku amsa ta fuskoki kamar haka:

**Fuska Ta Farko**: Ai sani ne baku yi ba, imami da xayan waxannan mutane da aka ambata, ba wajibi ne a kan xaya daga cikin Malaman Musulunci, da qungiyoyin Sunnah ba. Duk wanda ko aka samu daga cikinsu yana jin cewa, imanin da mutanen wajibi ne, ko har ma yake wajabta hakan a kan mabiyansa, to, shi da 'yan Shi'ah uwarsu xaya ubansu xaya. Musamman da zai rataya hakancan da kammaluwar imanin xayan su da Allah.

**Fuska Ta Biyu:** Duk malaman musulmi da shugabaninsu sun haxa a kan cewa, sanin wajibban addini da mustahabbansa ba su rataya akan gasganta samuwar mutanen da aka ambata ba. Duk kuwa wanda ya zaci haka daga cikin 'yan xariqa da wasunsu to, tabbas jahili ne kuma vatacce. Ka ga a nan sun banbanta da 'yan Shi'ah da ke ganin cewa, ba addini ga wanda bai gasgata samuwar Mahadinsu ba.

Sannan kuma lafuzzan da su 'yan xariqu ke amfani da su irin, Gausi da Quxubi da Autadu da Abdalu da sauransu, ba wanda ya riwaito su daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ko Sahabbansa da isnadi tsaftatacce. Gara ma dai kalmar *Abdalu* da aka samu wasu magabata sun yi amfani da ita, duk da yake hadisin da aka riwaito akan ta mai rauni ne. Mun yi magana mai warkarwa game da wannan a wani littafe ba wannan ba.

## 1.7 Tsakanin Shi'anci da Sufanci

**Fuska Ta Uku:** Wannan matsayi na Shi'ah 'yan-sha-biyu ya yi daidai da na sufaye, waxanda ke da aqidar cewa manyan waliyyansu, wato Gausi ko Quxubi su ke shiryar da mutane a duniya. Haka kuma a cewarsu, babu wani alheri da zai sami wani mutum sai da sani da kuma izininsu. Kai! Hasali ma sun san zahirin mutane da baxininsu, na farko da na qarshe. Irin wannan aqida kuwa, duk musulmin duniya na qwarai sun haxu a kan cewa, vata ce. Domin kuwa ba ta da banbanci da aqidar Kiristoci a wannan babin. Saboda kamar suna cewa ne akwai wani mai tarayya da Allah a cikin ayyukan da ya kevanta da su.

Kamar yadda wasunsu ke cewa game da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da wasu shaihunansu, wai ilimin xaya daga cikinsu da ikonsa daidai su ke da na Allah Ta'ala.

Cikinsu akwai wanda ke danganta wa xayan mutanen nan abin da ke iya yiwuwa ga Annabawa da muminai mutanen kirki kamar faruwar wata karama ko kasancewar xayansu idan ya yi addu'a ana karva, da kashefi, wato a sanar da wani bawan Allah wani abin da ya faku ga sauran mutane. Waxanda ke jingina samuwar waxannan karamomi ga mutane rayayyu kuma sanannu ai sun fi kusa da gaskiya bisa ga masu danganta su ga wanda Allah bai halicce shi ba.

## 1.8 Zancen Khadir Da Ilyasu

**Fuska Ta Huxu:** Gaskiyar magana ita ce, abin da Malamai masu zurfin bincike suke a kansa, cewa Ilyasu da Khadir sun mutu kamar yadda kowane mahaluki yake mutuwa. Kuma babu wanda Allah ya sanya a tsakanin sa da bayinsa ko ya wakilta shi wajen halittawa ko azurtawa ko shiryarwa ko bada nasara da makamantan su. Ko da Manzanni aikinsu bai wuce na isar da saqo ba.

## 1.9 Mu Koma Kan Maganar *Imamah*

Game da maganar *Imamah* dai, wato shugabancin sha biyun da 'yan Shi'a suka naxa, ba mu gan shi a Alqur'ani ba. Alhalin kuwa Alqur'anin cike ya ke da bayanin duk abin da musulmi ke da buqatar sanin sa, kamar sanin sunayen Allah da tauhidinsa da siffofinsa, da ayoyinsa da Mala'ikunsa da littaffansa da Manzanninsa da ranar Alqiyama. Ga kuma sauran bayanai da suka haxa da labarai masu qarfafa imani, da umurni da hani. To, duk waxannan abubuwan 'yan Shi'ah sun ce ba su kai muhimmancin shugabancin sha biyu ba. To, ina yake a Alqur'ani?

Haka kuma Allah Ta'ala ya rataya samun tsira akan abubuwa ga shi ko shugabancin irin na Shi'ah baya cikinsu. Allah Ta'ala na cewa:

﴿وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ فَأُوْلَٰٓئِكَ مَعَ ٱلَّذِينَ أَنۡعَمَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِم مِّنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ وَٱلصِّدِّيقِينَ
وَٱلشُّهَدَآءِ وَٱلصَّٰلِحِينَۚ وَحَسُنَ أُوْلَٰٓئِكَ رَفِيقٗا ٦٩﴾ النساء: ٦٩

*Duk wanda ya yi wa Allah da Manzonsa xa'a to waxannan na tare da Annabawa da Siddiqai da Salihai, to tarayya da waxannan ya kyautatu. Suratun-Nisa: 69*

Kuma Allah ya ce:

﴿وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ يُدۡخِلۡهُ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ
خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ وَذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ١٣﴾ النساء: ١٣

*Kuma duk wanda ya yi wa Allah da Manzonsa xa'a Allah zai shigar da shi aljannar da qoramu ke gudana a qarqashin ta, suna madawwama a ciki. Wancan shi ne babban rabo. Suratun Nisa'i:13.*

Kuma Allah na cewa:

﴿وَمَن يَعۡصِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَيَتَعَدَّ حُدُودَهُۥ يُدۡخِلۡهُ نَارًا خَٰلِدٗا فِيهَا وَلَهُۥ
عَذَابٞ مُّهِينٞ ١٤﴾ النساء: ١٤

*Kuma duk wanda ya sava wa Allah da Manzonsa, kuma ya qetare iyakokinsa, Allah zai shigar da shi wuta, ya na mai dawwama a cikin ta. Kuma ya na da azaba mai qasqantarwa. Suratun Nisa'i: 14.*

In ko wani ya ce: Ai shugabanci irin na Shi'ah shi ma yana cikin xa'a ga Allah da Manzonsa. Sai mu ce masa: Ya za a yi shugabanci ya zarce Sallah da Zakka da Azumi da Hajji da sauran ta fuskar muhimmanci, sannan Allah ya faxe su ya wofintar da shi?

In an ce: Ba shi yiwuwa mu yi xa'a ga Manzo in ba mu yi xa'a ga shugaba ba saboda shi ya san shari'ah. Sai mu ce: wannan ita ce aqidar 'yan-sha-biyu. Amma ba su da hujja ko 'yar qarama ce akanta. Domin sannannen abu ne cewa Alqur'ani bai yi nuni da wannan ba kamar yadda ya bayyana sauran assullan addini. Ya gabata cewa, wannan shugaban da su ke rayawa, ba wanda ya amfana da wannan shugabancinsa, kuma dama abubuwan da Manzanni suka zo da su ba a buqatar shugabannin Shi'ah don saninsu.

### 1.10 Asalin Addini a Wurin 'yan-sha-biyu

Asullan addini a wajen su huxu ne: Tauhidi, adalci, Annabci da shugabanci. Kuma Shugabanci shi ne na qarshe. A cikin Tauhidi ne sukan shigar da aqidarsu ta kore siffofin Allah da ya sa ma kansa da kuma cewa, Alqur'ani halittar Allah ne, ba maganarsa ba. Haka kuma a nan ne suke cewa, ba a ganin Allah a Lahira.

A cikin rukuninsu na biyu, wato adalci sukan shigar da qaryata qaddara, da kuma cewa Allah ba zai iya shiryar da wanda ya so ba ko ya vatar da wanda ya so. Ba lalle ne kuma abin da ya so ya faru ba, ko abin da bai so ba ya qi faruwa.

Abin da muka sani game da 'yan Shi'ah shi ne, ba su cewa, Allah na da iko akan komai, ba su kuma cewa abin da Allah ya so ne ke kasancewa. Amma dai Tauhidi da Adalci da Annabci duk suna gaba ga shugabanci. To yaushe ne suka dawo suka sanya shugabanci ya zama mafi xaukaka da muhimmanci akan komai?

Sannan kuma, sun nuna cewa shugabanci wajibi ne don kasancewar sa mai sadarwa zuwa ga wajibbai. To yaya hanyar da ke kai mutum riskuwar maqasudi ke zama mafi xaukaka da muhimmaci a kan abin da ke maqasudin?

## 1.11 Takin Saqar 'Yan Shi'ah

Farkon tuqa da warwarar da Shi'ah 'yan-sha-biyu suka yi a wannan babi, shi ne irin yadda suka xauki mas'alar shugabanci, a matsayin abu mafi xaukaka da girma a addinin musulunci. Qarshe kuma sai suka dawo suka tsira wata wofintattar aqida game da shi. Wato qudurce samuwar wani shugaba a baxini, kuma ma'asumi, wanda kuma luxufi ne gare su a cikin al'amurransu na addini da duniya. Alhali kuwa babu shi ba alamarsa. Haka kuwa na tabbatar da kasancewar su mafi zama nesa daga wannan luxufi tattare da kasancewar sa babban gurinsu.

A maimakon haka, sai suka wayi gari suna xa'a ga kafirai da azzalumai don neman biyan buqatunsu, tunda waccan hanyar ta toshe. A qarshe kuma suka tave; ba su ga tsuntsu ba su ga tarko.

A dunqule Allah Ta'ala ya rataya samun maslahohin lahira da na duniya a kan shugabanni, duk xai ne shin mun ce shugabanci ne abu mafi muhimmanci ko a'a. Su dai Shi'ah 'yan-sha-biyu sun fi kowa nisa daga samar da wannan maslahar, da kuma alherin da suka ce ana nema, kamar yadda su ke rayuwa.

Abu na biyu kuma shi ne, cewar da suka yi shi wannan ma'asumi a matsayinsa na shugaba, kasancewarsa samamme zata taimaka wa mabiyansa akan aikata abubuwan alheri na wajibi da nisantar munana daidai da yadda yake umurnin su. Ka ga bisa wannan iqirari, kamata ya yi a taras da 'yan-sha-biyu sun fi kowa riqe addini hannu bi-biyu, tunda Mahadin can nasu na nan raye. Amma sai al'amarin ya kasance ba haka ba; aka wayi gari suka zama kurar baya.

Bayan wannan kuma suka ce, ba kowa ba ne wannan ma'asumi illa Ali. Shi ne kawai ya karva wannan suna daga cikin Sahabbai. Saboda haka shi ya fi kowa cancanta da ya jivinci al'amurran musulmi bayan wucewar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kai tsaye. Kuma ma wai, kan malamai ya

haxu a kan haka. Suka kuma qara da cewa shi Alin, ya zavi Alhasan ya gade shi, shi kuma ya zavi Alhusaini. Bisa wannan tsari har aka kai ga wannan Mahadi da ake dako.

Ka ga duk wanda ya ji wannan magana sai ya zaci cewa ‘yan-sha-biyu na da cikakkar masaniya da al’amarin Mahadin nasu. Wato ko dai ya kasance sun tava sa shi a ido, ko wani wanda ya sa shi. Ko ko a’a, suna da wani kundi da ke qunshe da maganganunsa na horo da hani, ko wani abu mai kama da haka. Amma abin mamaki da na tambayi wani daga cikinsu a kan haka, sai ya karva man da cewa ba su da ko xaya daga cikin waxannan abubuwa. Ka ga a haka sun tabbata ashararu; waxanda basu jin kunyar yin amai su lashe.

Bayan wannan kuma, duk wanda ya kalli abin da idon basira zai fahimci irin kantar jahilcin da ke damun waxannan mutane. Domin kuwa a zahiri, aqidar dakon bayyanar wasu dokoki da hukunce-hukunce a hannun Mahadin nasu na nuna cewa abin da ke hannunsu na dokoki, waxanda suka samu ga malamansu ba gaskiya ba ne. Idan kuwa har suna jin gaskiya ne, to, tabbas babu wata fa’ida a cikin bayyanar Mahadin, ko da hakan za ta yiwu.

Ka ga a haka ma, har gara masu aqidar cewa Khadir na nan raye da su, domin ko akwai masu raya ganin sa har ma su riwaito wasu nasihohi daga wurin shi duk da yake ingancin hakan abu ne mai wuya. Amma duk da haka gara su da ‘yan-sha-biyu. Kai! Ba waxannan kawai ba, babu wata qungiya ta ‘yan bidi’a da za a ce gara ‘yan-sha-biyu da ita.

## 1.12 Daga Gani Sai Kai ya Kumbura?!

A bayyane take cewa, a aqidar wannan xan sha biyu, yin zamani xaya da wannan Mahadi nasu da suke jira, ko da kuwa bai bayyana ba ta ishi wanda ya yi imani da shi dalili na samun tsira. Wato a ma daina haqilo akan rashin bayyanarsa.

To, ka ga wannan magana ko kare ba ya ci ba. Domin kuwa, masaniya da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, ko yin zamani xaya da shi, ko yarda da an yi shi ba tare da amincewa da abin da ya zo da shi balle ya aikata ba, ba ya sa mutum ya samu rahamar Allah. Ka kuwa san ko waye Annabi, kuma ko waye wannan Mahadi da suke waqa.

Gaba xayan qungiyoyin musulunci sun yarda da cewa, duk wanda ya yi imani da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* wajibi ne ya yi wa hakan rakiya da tsare dokoki. Idan kuwa ba haka ba, gobe lahira kashinsa ya bushe Annabi na ji na gani.

Akwai daga cikin Shi’ah ‘yan-sha-biyu da ke cewa, da zaran mutum ya so sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* a zuci to, yana iya aikata duk abin da ya ga dama don ya fi qarfin zunubi. A kan haka kenan, babu wata buqata ta samun wani shugaba ma’asumi a yau, don samun wata falala, domin son da suke ma Ali *Raliyallahu Anhu* a cewarsu, ya ishe su shinge.

## 1.13 Shugabanci ba ya Cikin Rukunan Addini

Xan Shi'ar ya ce, duk wanda bai yi imani da kasancewar mas'alar shugabanci rukuni daga cikin rukunan addini ba, to, babu shi babu tabbata cikin aljanna; ko ya shige ta ana koro shi.

Martaninmu a kan wannan magana shi ne, Allah Maxaukakin Sarki ya zayyana siffofin muminai a cikin Alqur'ani, amma bai faxi maganar shugabanci a cikinsu ba. Haka kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai ambace shi ba a cikin bayanan imani da rukunansa waxanda ya naqalto daga bakin Jibrilu *Alaihis Salamu* a cikin sanannen hadisin nan da Nawawi ya kawo a cikin *Arba'una.* Hadisin kuwa hujja ce karvavviya ga dukkan musulmi na qwarai.

Idan kuwa har 'yan-sha-biyu suka qi yarda da wannan hadisi a matsayin hujjarmu, tattare da su ma suna kafa mana hujja da hadisan da basu kama qafar wannan ba, muna kuma qin karva. To, ga waxancan ayoyi da muka yi masu nuni da su a farko, su nuna mana inda Allah ya umarci muminai da yin imani da wani abu wai shi *Imamah* balle abu ya zama fitina. Allah Ta'ala na cewa:

﴿ إِنَّمَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِرَ ٱللَّهُ وَجِلَتۡ قُلُوبُهُمۡ وَإِذَا تُلِيَتۡ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتُهُۥ زَادَتۡهُمۡ
إِيمَٰنٗا وَعَلَىٰ رَبِّهِمۡ يَتَوَكَّلُونَ ٢ ٱلَّذِينَ يُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَمِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ يُنفِقُونَ ٣
أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ حَقّٗاۚ لَّهُمۡ دَرَجَٰتٌ عِندَ رَبِّهِمۡ وَمَغۡفِرَةٞ وَرِزۡقٞ كَرِيمٞ ٤ ﴾
الأنفال: ٢ - ٤

*Muminai kawai su ne waxanda in a kira sunan Allah zuciyarsu na girgiza in aka karanta masu ayoyin Allah imaninsu na qaruwa kuma suna dogaro akan Allah). Waxanda ke tsaida Sallah kuma suna ciyarwa daga abin da mu ka arzitta su da shi, waxannan su ne muminai na haqiqa, suna da xaukaka qwarai wurin Allah da gafara da arziki mai yawa) Al-anfal 2-4.*

Allah ya sheda cewa masu sifofin da ya ambata suna da imani amma bai ambaci shugabanci ba. Kuma Allah Ta'ala yana cewa:

﴿ إِنَّمَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ ثُمَّ لَمۡ يَرۡتَابُواْ وَجَٰهَدُواْ بِأَمۡوَٰلِهِمۡ وَأَنفُسِهِمۡ
فِي سَبِيلِ ٱللَّهِۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلصَّٰدِقُونَ ١٥ ﴾ الحجرات: ١٥

*Waxanda dai suka yi imani su ne waxanda na yi imani da Allah da Manzonsa sannan ba su yi qwanqwanto ba suka kuma yi jihadi da kuxaxensu da rayukansu a tafarken Allah to waxannan su ne masu gaskiya) Al-hujurat 15.*

Sai Allah ya sa (masu waxannan sifofi) cikin masu ingantancen imani ba tare da ambaton shugabanci ba.

Bayan waxannan ayoyi kuma, tarihi ya tabbatar da cewa, babu lokacin da wani ya zo karvar musulunci daga wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* aka samu ya lissafa masa *Imamah* daga cikin rukunan imani. Ka kuwa san ba ta yuwa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya voye wa al'ummarsa wani abu na addini. Tunda kuwa har bai yi haka ba, ka ga ashe qarya ce kawai 'yan-sha-biyu ke yi.

To, kuma koda 'yan-sha-biyu za su yarda da rashin makama a nan, su ce, a'a, ai mas'alar Imamah na qunshe ne a cikin nassosa; ba qarara take ba, ta yadda sai an duba sannu a gan ta. Har yau dai basu tsira ba. Domin kuwa ko da haka ne, to, matsayin matsalar bai wuce kasancewa wani reshe na addini amma ba asali ba.

Wata tuqa da warwara kuma, da yin ban hannun makaho da gaskiya, a cikin lamarin 'yan-sha-biyu shi ne, cewar da wannan wakili nasu ya yi wai, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce, duk wanda ya mutu bai san imamin zamaninsa ba, to, ya yi mutuwa irin ta jahiliyyah.

To, kafin mu je ko ina dai, wannan hadisi ba gaskiya ba ne. don ko su 'yan-sha-biyun ba su iya yin bayanin yadda suka samo shi balle ingancinsa.

Tabbas, akwai ingantaccen hadisi mai kama da wannan, wanda Muslimu ya riwaito daga Nafi'u. sai dai hujja ne a kansu. Bari ka ji yadda abin ya ke:

Nafi'u ya ce, Abdullahi xan Umar ya zo wurin Abdullahi xan Muxi'u lokacin da aka samu taqaddama tsakanin mutanen Madina da sarki mai ci a wancan lokacin, wato, Yazidu xan Mu'awiyah har suka yi niyyar yi masa tawaye da barazanar cire mubaya'arsa daga wuyansa. A nan ne Ibnu Umar ya zo wurin Abdullahi xan Muxi'u wanda shi ne jagoran wannan fitinar, sai xan Muxi'u ya ce, ku ba shi matashi, sai shi kuma Ibnu Umar ya karva da cewa, Ni ban zo da nufin zama ba, na dai zo ne in sheda maka abin da na ji da kunnuwana daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* sa'ad da yake cewa: *Duk wanda ya cire hannu daga xa'a ran gamon sa da Allah ba shi da hujja. Kuma wanda duk ya mutu ba tare da ya yi wa shugaban musulmi mubaya'a ba, to, ya mutu mutuwa irin ta jahiliyyah.*

Wannan ya nuna rashin halalcin fita daga xa'ar shugaba musulmi wanda ya tabbata. Haka kuma wanda ya qi bin shugaba na musulunci shi ne zai yi mutuwar jahiliyyah. Kowa ya sani kuwa cewa, 'yan-sha-biyu sun fi kowa sava ma shugabannin musulunci.

Da 'yan-sha-biyu sun san tsiyar da suke yi, da ko wancan gurvataccen hadisin nasu ba su kafa hujja da shi ba. Domin kuwa shi ma turmuza hancinsu yake yi. Saboda xabi'u irin na jahiliyyah sun haxa har da yaqi a kan 'yan gidanci. Babu ko wanda ya kai su wannan xabi'ar. To, kuma ko a hakan Alqur'ani da Sunnah ba su kafirta mai irin wannan xabi'a ba balle wanda bai kai shi ba. Dubi waxannan hadisai:

Ya zo a ciki Sahihi Muslim ta hanyar Abu Hurairata ya ce Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: *Duk wanda ya fita daga xa'a, kuma ya bar jama'ar musulmi sannan ya mutu, to, ya mutu mutuwa irin ta jahiliyyah.*

Ya kuma zo a cikin Buhari da Muslimu ta hanyar Abdullahi xan Abbas *Raliyallahu Anhu*. Daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: *Duk wanda ya ga shugabansa na da wani abin da ya ke qi to, ya yi haquri duk da haka. Lalle wanda ya fito yaqi da Sarkin Musulmi kwatankwacin taqa xaya, kuma ya mutu, to, ya mutu ne irin mutuwar jahiliyyah.*

Ka ga qarara waxannan xabi'u da suka tabbata ga 'yan-sha-biyun Shi'ah sun bayyana su xin ne suke mutuwar jahiliyyah ma damar suka gamu da Allah ba su tuba ba.

Haka kuma idan aka yi la'akari da kasancewar babu wanda ya san Mahadin can na 'yan-sha-biyu daga cikinsu balle wani umurni ko hani nasa tun da ya faku ne tun yana xan shekara biyu ko uku lokacin da ya shiga rijiyar *Samarra*. Yau kuwa a cewar su shekaru kusan xari huxu kenan.[1] Ka ga kenan ashe su ne waxanda basu san imaminsu ba. Wato, da za a qaddara kasancewar wancan hadisi ingantacce, to, su ne waxanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ke yi wa bushara da mutuwa irin ta jahiliyyah.

Amma kuma a kula "Sanin shugaban zamani" ba ya nufin sanin shanu ko alama, ana nufin dai sani irin wanda zai ba mabiyan sa cikakkar damar yi masa xa'a da kasancewa tsintsiya maxaurinki xaya. Wato, irin abin da mutanen jahiliyyah suka rasa kafin aiko manzo.

Harwayau dai a kan maganar shugabanci. Siffofin da suka tabbata ga Mahadin 'yan-sha-biyu, na rashin bayyana ga jama'a balle a yi masa xa'a, sun tabbatar da cewa shi ba shugaba ba ne a ma'aunin shari'ar musulunci. Dalili kuwa shi ne, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi umurni ne kawai da yin xa'a ga shugabannin da ke tare da jama'arsu. Ko su ma a kan abin da bai sava wa Allah ba. Bayan haka kuma ya hore su da haxin kai. Ka ga a cikin wannan magana akwai abin da ke tabbatar da cewa, shugaba a musulunci ba ma'asumi ba ne. don haka aka ce kada a yi masa xa'a idan ya kauce hanya.

Kai! Ko tunanin da 'yan-sha-biyu ke da shi na cewa, wai saboda kasancewar shugabanci abu mafi daraja a addini ne aka ga Sahabbai rana a kansa bayan rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, ba gaskiya ba ne. ba a gan su a rana ba, sun dai qara wa juna sani ne kawai akan mas'alar, kamar yadda suka yi a kan wasu mas'aloli da suka fi ta muhimmanci. Idan dai har 'yan-sha-biyu na neman lokacin da aka ga Sahabbai rana, to, shi ne lokacin halifancin Ali *Raliyallahu Anhu*.

---

[1] Allah Sarki! Yanzu dai an qara wasu shekaru xari huxu bayan maganar nan ta Ibnu Taimiyyah, da wasu xari huxu kuma a bayan su, amma dai labarin bai canza ba. 'Yan Shi'ah na nan suna ta jiran gawon shanu don bayyanar wanda Allah bai ko halicce shi ba sai cikin qwaqwalensu. Daga Masu Fassara.

Abin da ya faru lokacin naxa Abubakar *Raliyallahu Anhu* a *Saqifa*, da halifofi biyu na bayansa, sunansa shawarwari in har ana son gaskiya. Kuma ba a tashi taron ba sai da kowa ya fahimci juna a cikinsu.

## 1.14 Ina Nassin Yake?

Qare waccan magana kuma ke da wuya sai xan sha biyun ya jeranto sunayen Imaman nan da suke cewa su goma sha biyu. Kuma ya qara da cewa, wai, Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai bar duniya ba sai da ya bayyana su a matsayin waxanda za su gade shi. Kuma wai har da cewa, duk Ahlus-Sunnah sun yarda da haka. To, ina ma nassin ya ke ballantana wani daga cikin Ahlus-Sunnah ya karvi wannan magana, to, balle kuma a ce duka?!

## 1.15 Zaven Siddiqu Nassi ne ko Shawara?

A wurin xan sha biyu, halifancin Abubakar naxin mutane ne ba na Allah ba. Tunda wai, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai bar wasiccin ya gade shi ba. Kuma wai, wannan shi ne abin da Ahlus-Sunnah suke a kai.

To, abin da za mu ce a nan shi ne, lalle a cikin Ahlus-Sunnah akwai masu ra'ayin cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai yi wasicci da wani ya hau kujerarsa ba. Amma kuma tattare da haka, sanannen abu ne cewa, akwai wata jama'a daga cikinsu, da ke da ra'ayin cewa, halifancin Abubakar abu ne da aka yi bisa ga umurnin Allah da Manzonsa, wato nassi. Akwai maganganu masu yawa a kan haka a mazhabar Ahmad da wasu mazhabobi.

Alqali Abu Ya'ala da wasu malamai, sun ambaci riwayoyi biyu daga Imamu Ahmad a kan wannan lamari:

Riwaya ta farko na cewa, halifancin Abubakar ya tabbata ne nassance; ta hanyar wasu hadisai. Kuma a kan wannan fahimta ne wasu malaman hadisi da *Mu'utazilawa* da *Ash'ariyyawa* suke. Shi ma Abu Ya'ala ita ce fahimtarsa. A yayin da riwaya ta biyu kuma ke cewa, a'a, halifancin nasa ya dai tabbata ne ta hanyar ijtihadi. Wannan kuwa shi ne abin da Hasanul Basri da wasu malaman hadisi su ke.

Akwai hadisai da dama da ke tabbatar da waxannan riwayoyi kamar hadissan da malam xan Hamidu ya kafa hujja da su, daga cikinsu har da hadisin da Buhari ya riwaito daga Jubairu xan Mux'imu cewa: "Wata macce ta zo wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai ya umurce ta da zuwa ta dawo. Sai ita kuma ta tambaye shi da cewa, idan ban taras da kai ba fa? Sai ya karva mata da cewa: "Sai ki nemi Abubakar". Sai kuma hadisin rubuta wasiyyar da Annabi ya yi quduri a lokacin jinyarsa.

Hadisi na biyu shi ne wanda Huzaifa xan Yamani ya riwaito cewa: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Ku yi koyi da biyun nan da ke zuwa bayana; Abubakar da Umar".

Hadisi na uku daga Abu Hurairata Allah ya qara masa yarda ya ce: Na ji Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “A lokacin da nake barci sai na ga wata guga a kan rijiya, sai na xibi ruwa daga cikin abin da Allah *Subhanahu WaTa’ala* ya sawwaqe mini. Sannan xan Abu Quhafata (Abubakar) ya xauki gugar ya xebo sau xaya ko biyu. Akwai rauni a cikin xibarsa, Allah ya gafarta masa rauninsa. Sannan guga ta koma hannun Umar xan Haxxabi, ban ga wani gwani mai xiba irin tasa ba. Har sai da mutane suka qoshi da ruwan suka zauna a wurin”. Buhari ya riwaito shi.

Hadisi na uku daga Abdurrahman xan Abu Bakarata daga babansa ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* watarana ya ce: “Wane ne daga cikinku ya yi mafarki?” Sai na ce: “Na yi mafarkin na ga kamar sikeli na reto daga sama. Sai aka auna ka da Abubakar sai ka rinjaye shi . Sannan aka auna Abubakar da Umar sai Abubakar ya rinjaye shi. Sannan sai aka auna Umar da Usman sai Umar ya rinjaye shi. Daga nan sai aka xauke sikelin”. Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Mafarkinka na nuni ga halifanci irin na annabta da za a yi. Bayan sa kuwa Allah zai ba da mulki ga wanda ya so”.

Hadisi na Huxu: Daga Jabir Al-Ansari ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Wani mutumin kirki a yau ya yi mafarkin an rataya Abubakar gare ni. An kuma rataya Umar ga Abubakar. Shi kuma Umar sai aka rataya masa Usman”. Jabir *Raliyallahu Anhu* ya ce: “Mutumin kirkin nan da ya yi mafarkin ba wani ba ne face Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.* Ratayar kuma abin da take nufi shi ne gadon junansu da za su yi xaya bayan xaya”. Abu Dawuda ya riwaito shi.

Hadisi na Biyar: Daga Nana Aisha *Raliyallahu Anha* cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya shiga wurin ta ranar da ya fara rashin lafiya. Ya ce: “Ki kira mani babanki da xan’uwanki, in rubuta wa Abubakar saqo”. Sannan kuma dai sai ya ce: “Ai Allah da Musulmi za su qi karvar kowa sai Abubakar”. A wani lafazi na hadisin “Saboda haka, kada kowa ya sa ransa”.

In ka haxa waxannan hadissai da dukkan riwayoyi ingantattu da suka nuna gabatar da Abubakar ya ba da Sallah, zaka aminta cewa, tabbatattar magana dai ita ce, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi nuni ga mutane cewa, Abubakar ne mai maye gurbinsa. Ya kuma yi musu ishara zuwa ga haka da abubuwa masu yawa da suka haxa da maganganunsa da ayyukansa. Kuma ya so ya rubuta wannan don ya zama wasiccin da za a zartas bayansa amma Allah bai nufa ba saboda wata hikimar da Maxaukakin Sarki yake nufi ta karantar da mu yin shawara a tsakaninmu ga al’amurranmu.

Malam Ibnu Hazam ya kafa hujja a kan ingancin halifancin Abubakar da cewa, muhajirai da Allah ya kira su masu gaskiya su ne suka ba shi wannan suna. Allah *Subhanahu WaTa’ala* ya ce game da su:

﴿ لِلْفُقَرَآءِ ٱلْمُهَـٰجِرِينَ ٱلَّذِينَ أُخْرِجُوا۟ مِن دِيَـٰرِهِمْ وَأَمْوَٰلِهِمْ يَبْتَغُونَ فَضْلًا مِّنَ ٱللَّهِ
وَرِضْوَٰنًا وَيَنصُرُونَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓ ۚ أُو۟لَـٰٓئِكَ هُمُ ٱلصَّـٰدِقُونَ ﴿٨﴾ ﴾ الحشر: ٨

*(Arzikin qasa) na matalautan muhajirai ne waxanda aka fitar da su daga gidajensu da kuxaxensu suna neman falalar Allah da Manzonsa. To, waxannan su ne masu gaskiya) Al-Hasr 8.*

Ibnu Hazam, daga cikin masu ra'ayin cewa, halifancin Abubakar ya tabbata ne da nassi daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kare wannan ra'ayin nasu da hujjoji masu qarfi. Kuma ya ce, ba shi yiwuwa Sahabbai su haxu a kan ce masa Halifa in babu wani nassi a kan haka. Daga cikin hadissan da ya kafa hujja da su har da, hadisin matar da ta ce ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* idan ban same ka ba ya zan yi? Sai ya ce, ki je wurin Abubakar. Da kuma hadisin A'ishah *Raliyallahu Anha* wanda *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce mata: "Na so in aika ma babanki da xan'uwanki su zo don in bar masu saqo a rubuce don kada mutane su yi savani, wani ya ce, ni ne na fi cancanta, ko wani mai guri ya yi guri. Amma kuma Allah da Manzonsa da muminai duk Abubakar suka zava".

Ibnu Hazam harwayau, ya mayar da martani a kan sauran hujjojin da malaman da ke xaya vangaren suka yi amfani da su. Kamar maganar da sayyidina Umar *Raliyallahu Anhu* ya yi cewa; "In na zavi halifa a bayana to, wanda ya fi ni ma ya yi haka". Yana nufin Abubakar. "In kuma ban sa wani ba, to, kuma wanda ya fi ni ya tafi bai sa kowa ba". Yana nufin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Sai kuma hadisin nana Aisha Allah ya qara mata yarda cewa, an tambaye ta, shin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* zai sa wani ya maye gurbinsa wane ne zai sa?

Waxannan hadisai duk da yake suna nuna cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai ayyana wani tsayayyen shugaba a bayansa ba, amma malam Ibnu Hazam ya ce, ba shi yiwuwa su keta ijma'in da Sahabbai suka yi. Domin ba su yi qarfin da za su iya yin haka ba duk da ingancinsu.

Idan har an qaddara gaskiya ne cewa, Manzo ya faxi wanda zai gade shi, to, ko a haka ma 'yan-sha-biyu ba su da hujja. Domin Rawandiyawa daga cikinsu na ganin cewa, Abbas ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bar nassi a kan zai gaje shi, ba Ali ba. Alqali Abu Ya'ala ya qara haske a kan wannan maganar, inda ya faxi cewa, wasu 'yan Rawandiyyah na ganin bayan Abbas 'ya'ya da jikokinsa ne za su ci gaba da halifanci har ranar tashin qiyama. Kuma wai, in ji Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kuma sannan nassin da ya faxi haka wai ba a fayyace yake ba. Waxannan ra'ayoyan biyu sun yi hannun riga da ra'ayoya biyu na 'yan-sha-biyu da kuma Jarudiyawa daga cikin Shi'ah. Su dai Jarudiyawa, savanin 'yan-sha-biyu, ganin suke yi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya faxi shugabancin Ali amma ba qarara ba. Ya dai bayyana sifofin da ba a same su ga kowa ba sai Ali.

Abin nufi dai a nan, shi ne cewa, kowane daga cikin waxannan bayin Allah guda uku; Abubakar da Abbas da Ali an samu masu raya cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bar nassi a kansu. Kuma cewa, ya bar nassi a kan Abubakar shi ne ya xara sauran ra'ayoyan qarfi ta fuskar hujja da

kuma karvuwa a wurin malamai, duk da yake a mafi rinjayen zance babu nassin ga ko xaya.

Alamu masu yawa sun nuna cewa, Abubakar ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya zava, kuma Sahabbai sun fahimci haka. Don haka ne ma Umar *Raliyallahu Anhu* ya ce, a cikin huxubar da ya yi gaban Muhajiruna da Ansaru: "Babu wanda mutane ke so daga cikinmu kamar Abubakar" Buhari da Muslim. Bisa wannan dalili ne gaba xayansu suka yi wa Abubakar bai'a, in ban da Sa'adu xan Ubadata, a sakamakon sha'awar da yake da ita ga matsayin. Amma kuma daga baya ya yi mubaya'ar.

Muhajiruna sun yi wa Abubakar wannan mubaya'a ne a kan sanin da suka yi na cewa, Allah da Manzonsa shi suka fifita. Ka ga a haka ta tabbata cewa, halifancin nasa ya tabbata ne ta hanyoyi ingantattu.

## 1.16 Halifofi Shiryayyu

Xan sha biyu ya ce, wai, Umar *Raliyallahu Anhu* ne kawai da wasu mutane guda huxu suka tabbatar da naxin Abubakar *Raliyallahu Anhu* a matsayin halifa. Kuma wai, wannan magana haka take har wurin Ahlus-Sunnah don daga gare su ne ya riwaito ta.

To, muna sanar da shi cewa, babu wani Ahlus-Sunnah da ke da wannan fahimta. Duk da yake ba mu musun cewa, akwai wasu daga cikin zaqaquran magana, wato *Ahlul-Kalam*, da ke ganin cewa, a duk lokacin da aka samu mutum huxu sun goya ma mutum xaya baya to, yana iya zama halifa. Wasu kuma suka ce, mutum biyu dai. Wasu ma suka ce, kai ko xaya ya samu bukata ta biya.

Amma ra'ayin Ahlus-Sunnah a kan wannan magana shi ne, shugabanci na qulluwa ne idan masu qarfin iko da faxa a ji waxanda xa'arsu ga shugaba ke sa a kai ga maqasudi, suka yi wa mutum mubaya'ah.

Xan sha biyun ya ci gaba da cewa; Usmanu xan Affan ya zama halifa ne da umurnin da Umar ya bayar ga mutane shida yana xaya daga cikinsu, sai wasunsu suka zave shi.

To, harwayau dai, ba zaven da waxannan qwarorin jama'a suka yi wa Usmanu ne ya ba shi damar zama halifa ba. Ko alama, mubaya'ar dai da gaba xayan musulmi a wannan lokaci suka yi masa ce ta ba shi wannan dama. Kuma tarihi ya tabbatar da cewa, babu mutum xaya da bai yi masa wannan mubaya'a ba.

Imamu Ahmadu xan Hambali ma cewa ya yi, ba a tava irin mubaya'ar da aka yi wa Usman ba ta fuskar samun haxin kan kowa da kowa da rashin samun jayayya. Mubaya'ar kuwa ta tabbata ne a lokacin da sauran 'yan kwamitinsu su biyu; Abdurrahman xan Aufu da Ali suka yi masa mubaya'a a masallaci, sauran jama'a suka rufa masu baya.

Kafin haka kuwa, Abdurrahman xan Aufu ya xauki tsawon kwana uku ba tare da ya ko samu isasshen bacci ba, don shagaltuwa da neman shawarar jama'a da xaukar ra'ayin Sahabbai. Kai, har ma sai da ya nemi jin ta bakin matan aure da qananan yara kafin ya cimma waccan matsaya da suka xora mutane a kan ta, shi da Ali.

A qarshe kuma suka tabbatar wa jama'a cewa, sun xora Usmanu a kan wannan matsayi ba don tsoro ko kwaxayin wani abu ba. Bisa wannan dalili da yawa daga magabata irin su malam Ayyub As-Sukhtiyani suka tafi a kan cewa, duk wanda ya fifita Ali *Raliyallahu Anhu* a kan Usmanu bai raga wa Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba. Domin su a nasu fiqihu Usmanu na gaba gare shi, ittifaqan.

Daga nan kuma sai xan sha biyun ya ce: "Shi ko halifancin Ali *Raliyallahu Anhu* ya tabbata ne sakamakon mubaya'ar da gaba xayan jama'a suka yi masa, savanin halifofi uku da suka gabace shi.

Wannan magana ko alama ba gaskiya ba ce. Tarihin musulunci ya tabbatar da cewa, yadda kan musulmi ya haxu a kan yi wa Sahabban can uku mubaya'a ya fi yadda ya haxu a kan yi wa Ali ita, nesa ba kusa ba. Wannan ta fuskar yawan jama'a kenan. To, ko ta fuskar girma da xaukaka, waxanda suka haxu a kan bai'ar tasu sun yi wa waxanda suka haxu a tasa fintinqau. Don kuwa a wancan zamanin akwai manya-manyan Sahabbai waxanda ba a samu irin su ba a lokacin mubaya'ar Ali don sun rasu ko ba su nan. Ga kuma waxanda suka murje idanu daga cikin mutanen kirki suka qi yi wa Ali mubaya'a saboda wasu shubhohi da suka gitta masu. Abin da bai faru ba a lokacin da aka naxa halifofi uku na farko. Domin naxin na Ali ya zo a wani lokaci na hatsaniya da tashin hankali da kuma girgizar zukata a kan kisan gilar da aka yi wa halifan da ya gabace shi. Har ma ana raxe-raxin cewa, ko cikin waxanda suka yi mubaya'ar, wasu tilasta su aka yi da kaifin takobi.

To, amma in ban da Sa'adu da muka faxa, wa aka tava jin xuriyar ya yi gunguni game da zaven Abubakar, balle qin yin mubaya'a? Shi ma kuma ya zo ya yi daga baya, bai bixi wata fitina ko tada zaune tsaye ba. Musamman da yake an tunatar da shi faxar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa, wannan halifanci abu ne na Quraishawa, kuma duk mutanensa sun miqa wuya babu wata jayayya. Kamar yadda wasu suka ce Ali ya yi jinkirin mubaya'a shi ma ga Abubakar sai daga bisani sannan ya yi.

Xan sha biyun yana iya cewa, Ahlus-Sunnah ma sun yarda da cewa, mutane ne suka yi ma halifofi uku mubaya'a ba nassi ne ya tabbatar da ita ba. Sai mu ce, babu shakka Ahlus-Sunnah sun yarda da zancen da Manzo Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi a kan halifofi shiryayyu, da kuma cewa, lokacinsu zai miqa har shekaru talatin. Don haka, Ali yana a cikinsu. Al'umma kuwa ta haxu a kan shugabancin Sahabban nan uku, kuma sun samu cimma maqasudin shugabanci, don sun yaqi kafirai, sun ci qasashe da dama. Amma a lokacin halifancin Ali ko kafiri xaya ba a yaqa ba, balle a ci wani gari. Abin da ya faru dai kawai shi ne yaqi a tsakanin musulmi.

Bisa ga haka, muna fahimtar cewa, nassoshin da ‘yan-sha-biyu ke raya cewa akwai game da Ali, da waxanda Rawandiyyawa ke cewa akwai a kan Abbas duk ba su da tushe, kuma ba su sa wanin su ya zamo halifa ba. Shi dai Ali ya zamo halifa da zaven da aka yi masa bayan wafatin sayyidina Usman.

Xan sha biyun ya ci gaba da cewa, wai, Ahlus-Sunnah sun yi savani bayan mutuwar Ali, kuma rabu biyu; sashensu suka naxa Al-Hassan a yayin da xaya sashen suka zavi Mu'awiyah.

Amsa ita ce: Ahlus-Sunnah ba su yi jayayya cikin wannan ba. Abin da dai ya faru shi ne, mutanen Iraqi sun yi wa Hassan mubaya'a a matsayin magadin babansa. Mutanen Sham kuwa daman tare suke da Mu'awiyah, kuma bayan mutuwar Ali sai suka shelanta shi a matsayin Sarkin Musulmi.

Xan sha biyun ya ci gaba da cewa: Sannan aka sa shugabancin cikin gidan Banu Umayyata, bayansu kuma sai suka mayar da ita gidan Banul Abbas.

Amsarmu ita ce: Ahlus-Sunnah ba su ce, xayan gidajen nan biyu shi ya cancanci shugabanci ba. Kuma su, ba su ce dole a yi masu xa'a ba ga duk abin da suka yi umurni da shi.

Abin da Ahlus-Sunnah ke yi shi ne, suna faxin abin da ya gudana. Kuma suna umurni da abin da ya wajaba, suna kafa shedu da abin da ya auku, suna umurni da abin da Allah da Manzonsa suka yi umurni da shi. Suna cewa, waxannan su ne suka yi shugabanci, kuma sun kasance suna da qarfi da iko, suna kuma iya samar da maqasudin shugabanci, kamar zartar da haddi, da raba kuxaxe, da zaven alqalai, da naxa hakimai da gwamnoni, da xaukar mayaqa tare da aika su wuraren jihadi, da tsayar da Hajji da Sallolin Idi da na Juma'a, da sauran abubuwan da suka wajaba a kan shugaba.

Ahlus-Sunnah kuma harwayau, suna cewa, ba ya halasta a yi wa xayan waxannan da na'ibansu xa'a a cikin savon Allah. Amma ana bin su wajen aikata abubuwan da suke xa'a ne ga Allah *Subhanahu WaTa’ala*. Sai a fita yaqar kafirai tare da su, a yi sallar juma'a da ta Idi a bayansu ko na wakilansu, a yi hajji a qarqashin jagorancinsu, a taimaka masu a wurin umurni da kyakkyawa da hani daga mummuna, da makamantansu.

Abin da aka sani ne cewar mutane ba su gyaruwa sai da shugabanni. Kuma samun sarakuna tsayayyu ko da azzalumai ne ya fi alheri a kan barin mutane kara-zube. Kamar yadda ake cewa, shekaru sittin da shugaba azzalumi ya fi dare xaya ba tare da shugaba ba.[1]

An riwaito daga Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce: “Ba makawa ya kasance mutane na da shugabanni, masu tsoron Allah ne ko Fajirai” Aka ce masa: “Mun san hikimar da ke cikin samun shugaba mai tsoron Allah. To, wanda bai tsoronsa fa?” Sai ya karva masu da cewa: “Ana tsare lafiyar hanya da shi, a tsayar da haddodin Allah, a yaqi magabta tare shi, a kuma raba ganima da shi”. Ali xan Ma'abadu ya ambaci wannan a littafin *Axxa'atu Wal-Ma'asiyatu*.

[1] Iraqi a yau ta ishe mu misali. Daga Masu Fassara.

To, duk wanda ya yi shugabanci kowane iri ne, shugabancinsa ya fi alfanu ga musulmi a kan shugabancin wanda babu shi, kamar Mahadin can na ‘yan Shi’ah. Wanda har yanzu suna nan suna ta jiran sa, ba kuwa zai bayyana ba har a naxe qasa. Babu wata maslaha da yardarsu da shugabancin nasa ta haifar ga lamurran duniya ko na addini illa kafewa a kan miyagun aqidu, da haifar da fitina tsakanin musulmi, da vata lokaci.

Mutane ba su iya zama lokaci ko xan kaxan ba tare da shugaba ba. Kai lamurransu ma vaci suke yi. To, yaya za su gyaru in ba su da shugaba sai wanda ba a sani ba, ba a kuma san abin da yake faxa ba, bai iya aikata kome dangane da shugabanci, kai dai wannan da babu shi fa!?

Amma iyayensa ba su kasance suna da qarfi da iko ba na zama shugabanni. Malamai daga cikinsu suna da shugabanci na ilimi kamar fannin hadisi da fatawa da makamantansu, amma ba su da shugabanci irin na siyasa. Saboda haka suka kasa shugabanci ko da ko sun fi cancanta ko ba su fi ba.

Duk dai yadda abin ya ke, za a tarar cewa, ba a ba su ikon shugabanci ba, kuma ba a shugabantar da su ba. Kuma bai yiwuwa a kai ga maqasudin shugabanci da su tunda ba su da qarfi da iko. Ko da mumini ya yi musu xa’a to ba za a kai ga maslahohin da ake samu idan aka yi wa shugabanni xa’a kamar jihadin maqiya da ba masu haqqi haqqinsu da tsaida haddoda.

To, in wani ya ce: Lalle wasu daga cikin waxannan limaman na Shi’ah na da qarfi da ikon da ke iya samar da maqasudin shugabanci, to sai mu ce wannan dai girman kai ne da qin gaskiya.

Da lamarin ya kasance haka da ba a sami wanda ya yi jayayya da su har ya karve mulki ya hana wa kowa ba. In kuma ya ce: Su ne shugabanni don su ya wajabta su yi shugabanci, kuma mutane sun sava ma Allah saboda qin shugabantar da su.

To, wannan daidai yake da wani ya ce: Wane ya kamata ya zama alqali amma ba a yi masa ba, amma an zalunce shi an hana masa alqalanci. Na san wataqila su ce, wannan ba zata hana su karva sunansu na shugabanni, waxanda Allah ya zava ba. Kuma waxancan mutane da suka qi shugabantar da su, tabbas azzalumai ne. sun kuma savi Allah a haka.

A nan sai mu gaya masu cewa, koda ya zama wajibi a shugabantar da su, ba za a yi laifi wa Allah idan ba a yi haka ba, sai idan hakan ta kasance da gangan. Wannan shi ne musulunci. Ai Umar xan Abdulaziz ya so ya shugabantar da Qasim xan Muhammad jikan Abubakar Siddiq saboda yarda da cancantarsa, amma masu qarfi daga cikin banu Umayyata suka taka masa burki. Kun ga wannan ba laifinsa ba ne.

Duk wanda bai yi zalunci ba, kuma bai taimaka ga yin sa ba, ba laifin da ke hawa kansa. Sanannen abu ne cewa, masu tsoron Allah ba su taimakon shugabanni sai ga abubuwan alheri da tsoron Allah. Ba su taimakawa ga savo da qetare iyaka.

Abin da Ahlus-Sunnah suka yi imani da shi a wannan babi shi ne: Ya kamata a shugabantar da wanda ya fi cancanta in ya yiwu. Wasu daga cikinsu

ma na jin yin haka wajibi ne. Wasu kuma suka ce mustahabbi ne dai. Sannan duk wanda ya bar wanda ya fi cancanta kuma yana da iko to shi azzalumi ne. Amma wanda ya kasa shugabantar da mafifici ga shi ko yana son haka, to yana da uzuri a wurin Allah da mutane. A qarshe kuma za su yi xa'a ga wanda Allah ya ba shugabanci domin babu abun da ke faruwa sai da iko da yardarsa. Yana kuma canza abin da duk ya so, a lokacin da ya so. Wannan idan mun qaddara ingancin wancan nassi da 'yan Shi'ah ke da'awa kenan.

Balle ma bai inganta ba, ko alama. Babu abin da ma mafarkin ha kan zai kawo illa ruxani. Domin kuwa duk mai imani da hankali, ba ya musun cewa, Allah Ta'ala ya san gobe. Ka ga a haka ba zai umurci bayinsa da shugabantar da wanda ba zai iya tabbatar da maqasudin shugabanci ba. Duk ma wanda ke da irin wannan hasashe da hangen nesa daga cikin mutane, a kan wasu mutane biyu da ke qarqashinsa, lalle zai yi umurni ne kawai da shugabantar da wanda buqata ke iya biya da shi. Wannan shi ne irin abin da ya faru a kan halifofi uku na farko da na huxu. Al'amarin kuwa hukunci ne na Allah. Duk ko wanda ya qi yarda da shi, to, da shi yake jayayya.

Iyakar abin da Ahlus-Sunnah ke son tabbatarwa a nan, wanda kuma shi ne aqidarsu, shi ne: Duk shugaban da Allah Ta'ala ya yi wa baiwar cikakken qarfi, da ikon tabbatarwa da aiwatar da manufofin shugabanci, to, shi ne karvavve kuma yardadde a wurin Allah da mutanen kirki. Kamar dai yadda duk wanda ke shiga gaba a bishi sallah shi ne liman ko an qi, ko an so. Wannan kuwa koda akwai wanda ya fi shi cancanta da shugabancin ko limancin. A haka kuma, yi masu xa'a, da taimaka masu cikin duk abin da ba savon Allah ba, wajibi ne a wannan mahanga ta Ahlus-Sunnah. Domin Buhari da Muslimu sun riwaito cewa, Ibnu Abbas *Raliyallahu Anhu* ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Duk wanda ya ga abin da yake qi ga shugabansa, to, ya yi haquri. Haqiqa ba wanda zai fita daga xa'ar shugabansa ko da nisan taqa guda ne sannan ya mutu bisa wannan halin, face ya mutu irin mutuwar jahiliyyah.

## ZANGO NA BIYU

### 2.0 Dalilan Wajabcin bin Imamiyyah!

A fasalin littafinsa na biyu, xan Shi'ar ya ce: Wajibi ne a bi Mazhabar Imamiyyah.

Wato, yana cewa, tunda Sahabbai sun yi savani bayan rasuwar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*, to, wajibi ne a kan musulmi su yi biyayya ga mazhabar Shi'ah 'yar sha biyu. Saboda wai a cewarsa, jagororin wannan mazhaba ba su kuskure. Duk abin da ya fito daga bakinsu, shi ne mafi inganci da zama gaskiya. Saboda haka mabiyan wannan mazhaba ne kawai za su sami tsira gobe qiyama.

Ya qara da cewa, babban abin da ke tabbatar da kasancewar wannan mazahaba mafi cancanta daga cikin mazhabobi shi ne, savanin can da wai, Sahabbai suka yi bayan Manzo. A qarshe wasu daga cikinsu suka mara wa wani baya saboda kwaxayin abin duniya, ya zama halifa. Kamar yadda Umar xan Sa'ad sarkin Tehran ya zavi kashe Husaini don ya tsira da mulki. Amma kuma duk da haka, wasu suka jajirce suka goyi bayan gaskiya; suka mara wa wanda ya fi cancanta baya, suka bar duniya da qyaleqyalinta.

Saboda haka, inji shi, wajibi ne a kan kowane musulmi, ya yi wa kansa qiyamullaili, ya bi mazhabar mutanen kirki, wato Imamiyyah, ya fita batun azzalumai. Musamman ma wai, ga shi Allah Ta'ala ya ce:

﴿أَلَا لَعْنَةُ ٱللَّهِ عَلَى ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٨﴾﴾ هود: ١٨

*Ku saurara! La'anar Allah ta tabbata akan azzalumai. Suratu Hud 18.*

Kafin mu ce wani abu a nan, muna son a fahimta cewa, a cikin wannan magana, xan Shi'ar ya kasa Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* gida huxu bayan wafatinsa. a) Wanda ya nemi halifanci, alhali bai cancanta ba, wato Abubakar. b) Wanda ya nemi halifanci bisa qa'ida, saboda haqqinsa ne, wato Ali c) Waxanda suka goyi bayan halifofi uku na kafin Ali, don kwaxayin abin duniya. d) Waxanda suka goyi bayan su don rashin basira.

Ka ga kenan, a kaikaice xan Shi'ar na cewa ne, gaba xayan Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* sun halaka bayan rasuwarsa, in banda Ali. Saboda sun sani sun take sani.

Duk wanda ya dubi wannan iqirari nasa da idon basira, to, zai fahimci cewa, yana fifita Yahudawa ne da Nasara a kan sahabban Annabi. Tabbas abin da yake nufi kenan. Domin tarihi ya tabbatar da cewa, an samu shiryayyun mutane masu tsayawa a kan gaskiya daga cikin Yahudawa da Nasara kamar yadda Allah ya ce:

﴿وَمِمَّنْ خَلَقْنَآ أُمَّةٌ يَهْدُونَ بِٱلْحَقِّ وَبِهِۦ يَعْدِلُونَ ﴿١٨١﴾﴾ الأعراف: ١٨١

*Daga cikin mutanen da muka halitta akwai wata al'umma masu shiryarwa da gaskiya, sannan kuma da ita suke adalci. Al-A'araf 181.*

To, idan kuwa har aka rasa shiryayyun mutane daga cikin Sahabbai, tattare da kasancewar zamaninsu mafi girman qarni, ka ga ba za a same su ba a kowane qarni. Wannan ita ce manufarsa.

Allah Sarki! Allah ya kiyashe mu da mugun masoyi. Ka ga wannan sukar lamiri da xan Shi'ah ya yi wa Sahabbai ta haxa har da Ali *Raliyallahu Anhu*. Domin kuwa duk abin da ya gudana bayan wucewar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*, har zuwa lokacin da shi ya zama halifa ai da hannunsa a ciki. Illa dai sun yi abubuwa ne shi da takwarorin nasa, Sahabbai, bisa ijtihadi da nufin kare alfarmar Shari'ah. Amma xan Shi'ar sai ya ce, wai sun yi hakan can ne, a sakamakon kasancewar su maqiya Allah da Manzo, kuma makwaxaita abin duniya. Wal iyazu billahi.

Ka ga wannan iqirari ko shakka babu, qaryata Allah *Subhanahu WaTa'ala* ne da ya ce:

﴿وَالسَّابِقُونَ الْأَوَّلُونَ مِنَ الْمُهَاجِرِينَ وَالْأَنصَارِ وَالَّذِينَ اتَّبَعُوهُم بِإِحْسَانٍ رَّضِيَ
اللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُوا عَنْهُ وَأَعَدَّ لَهُمْ جَنَّاتٍ تَجْرِي تَحْتَهَا الْأَنْهَارُ خَالِدِينَ فِيهَا أَبَدًا ۚ
ذَٰلِكَ الْفَوْزُ الْعَظِيمُ ﴿١٠٠﴾﴾ التوبة: ١٠٠

*Kuma magabatan farko na Muhajirai da Ansarai da waxanda suka bi su da kyautatawa, Allah ya yarda da su kuma sun yarda da shi, kuma ya yi musu tattalin gidajen aljanna, qoramu suna gudana a qarqashinsu, suna madawwama a cikinsu har abada. Wancan ne rabo mai girma.*

*Suratut Taubah: 100*

Da kuma inda Ya ce:

﴿مُّحَمَّدٌ رَّسُولُ اللَّهِ ۚ وَالَّذِينَ مَعَهُ أَشِدَّاءُ عَلَى الْكُفَّارِ رُحَمَاءُ بَيْنَهُمْ ۖ تَرَاهُمْ رُكَّعًا سُجَّدًا
يَبْتَغُونَ فَضْلًا مِّنَ اللَّهِ وَرِضْوَانًا ۖ سِيمَاهُمْ فِي وُجُوهِهِم مِّنْ أَثَرِ السُّجُودِ ۚ ذَٰلِكَ مَثَلُهُمْ فِي
التَّوْرَاةِ ۚ وَمَثَلُهُمْ فِي الْإِنجِيلِ كَزَرْعٍ أَخْرَجَ شَطْأَهُ فَآزَرَهُ فَاسْتَغْلَظَ فَاسْتَوَىٰ عَلَىٰ سُوقِهِ
يُعْجِبُ الزُّرَّاعَ لِيَغِيظَ بِهِمُ الْكُفَّارَ ۗ وَعَدَ اللَّهُ الَّذِينَ آمَنُوا وَعَمِلُوا الصَّالِحَاتِ مِنْهُم مَّغْفِرَةً
وَأَجْرًا عَظِيمًا ﴿٢٩﴾﴾ الفتح:٢٩

*Muhammadu manzon Allah ne. Kuma waxannan da ke tare da shi masu tsanani ne a kan kafirai, masu rahama ne a tsakaninsu, ka na ganinsu suna masu ruku'i masu sujada, suna neman falala daga Ubangijinsu, da yardarsa. Alamarsu tana a cikin fuskokinsu, daga Kufan sujuda. Wannan ita ce siffarsu*

*a cikin Attaura. Kuma siffarsu a cikin Linjila ita ce, kamar tsiron shuka wanda ya fitar da reshensa, sa'an nan ya qarfafa shi, ya yi kauri, sa'an nan ya daidaita a kan qafafunsa, yana bayar da sha'awa ga masu shukar, domin (Allah) ya fusatar da kafirai game da su. Kuma Allah ya yi alqawali ga waxanda suka yi imani kuma suka aikata ayyukan qwarai daga cikinsu da gafara da lada mai girma.*

*Suratul Fathi, Aya ta 29.*

Allah Ta'ala ya ce:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ بِأَمۡوَٰلِهِمۡ وَأَنفُسِهِمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلَّذِينَ
ءَاوَواْ وَّنَصَرُوٓاْ أُوْلَٰٓئِكَ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلِيَآءُ بَعۡضٖۚ ﴾ الأنفال: ٧٢

*Haqiqa, waxanda suka yi imani suka kuma yi hijira da jihadi da dukiyarsu da rayukansu a tafarkin Allah da waxanda suka karvi baquncin (su) suka kuma taimaka, waxannan sashensu majivinta lamurran sashe ne. Suratul-Anfal: 72*

Har zuwa inda Allah ya ce:

﴿ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلَّذِينَ ءَاوَواْ وَّنَصَرُوٓاْ أُوْلَٰٓئِكَ
هُمُ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ حَقّٗاۚ لَّهُم مَّغۡفِرَةٞ وَرِزۡقٞ كَرِيمٞ ﴿٧٤﴾ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنۢ بَعۡدُ وَهَاجَرُواْ
وَجَٰهَدُواْ مَعَكُمۡ فَأُوْلَٰٓئِكَ مِنكُمۡۚ وَأُوْلُواْ ٱلۡأَرۡحَامِ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلَىٰ بِبَعۡضٖ فِي كِتَٰبِ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ
بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمُۢ ﴿٧٥﴾ ﴾ الأنفال: ٧٤ ـ ٧٥

*Kuma waxanda suka yi imani kuma suka yi hijira, kuma suka yi jihadi a cikin hanyar Allah, kuma da waxanda suka bayar da masauki, kuma suka yi taimako, waxannan su ne muminai na gaskiya, suna da gafara da wani abinci na karimci. Kuma waxanda suka yi imani daga baya, kuma suka yi hijira kuma suka yi jihadi tare da ku, to, waxannan suna tare da ku, kuma ma'abuta zumunta, sashensu majivintan sashe ne a cikin littafin Allah. Lalle Allah ne Masani ga dukkan komi.*

*Anfal: 74-75*

Da kuma in da Maxaukakin Sarki ya ce:

﴿ لَا يَسۡتَوِي مِنكُم مَّنۡ أَنفَقَ مِن قَبۡلِ ٱلۡفَتۡحِ وَقَٰتَلَۚ أُوْلَٰٓئِكَ أَعۡظَمُ دَرَجَةٗ مِّنَ ٱلَّذِينَ أَنفَقُواْ
مِنۢ بَعۡدُ وَقَٰتَلُواْۚ وَكُلّٗا وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلۡحُسۡنَىٰۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ خَبِيرٞ ﴿١٠﴾ ﴾ الحديد: ١٠

*Wanda ya ciyar daga cikin ku ya yi jihadi kafin addini ya yi qarfi ba su zama xaya da waxanda suka ciyar*

*suka kuma yi jihadi bayan haka. Waxancan sun fi xaukaka. Kuma dukansu Allah ya yi masu alqawarin aljanna. Kuma Allah masani ne ga abin da kuke aikatawa. Al-hadid 10*

Da kuma inda Allah Ta'ala ya ce:

﴿ لِلْفُقَرَاءِ الْمُهَاجِرِينَ الَّذِينَ أُخْرِجُوا مِن دِيَارِهِمْ وَأَمْوَالِهِمْ يَبْتَغُونَ فَضْلًا مِّنَ اللَّهِ
وَرِضْوَانًا وَيَنصُرُونَ اللَّهَ وَرَسُولَهُ ۚ أُولَٰئِكَ هُمُ الصَّادِقُونَ ﴿٨﴾ وَالَّذِينَ تَبَوَّءُوا الدَّارَ وَالْإِيمَانَ
مِن قَبْلِهِمْ يُحِبُّونَ مَنْ هَاجَرَ إِلَيْهِمْ وَلَا يَجِدُونَ فِي صُدُورِهِمْ حَاجَةً مِّمَّا أُوتُوا
وَيُؤْثِرُونَ عَلَىٰ أَنفُسِهِمْ وَلَوْ كَانَ بِهِمْ خَصَاصَةٌ ۚ وَمَن يُوقَ شُحَّ نَفْسِهِ فَأُولَٰئِكَ هُمُ
الْمُفْلِحُونَ ﴿٩﴾ وَالَّذِينَ جَاءُوا مِن بَعْدِهِمْ يَقُولُونَ رَبَّنَا اغْفِرْ لَنَا
وَلِإِخْوَانِنَا الَّذِينَ سَبَقُونَا بِالْإِيمَانِ وَلَا تَجْعَلْ فِي قُلُوبِنَا غِلًّا لِّلَّذِينَ آمَنُوا رَبَّنَا إِنَّكَ
رَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴿١٠﴾ ﴾ الحشر: ٨ - ١٠

*(Arzikin qasa) na matalautan muhajirai ne, waxanda aka fitar da su daga gidajensu, aka raba su da dukiyarsu, suna neman falalar Allah da yarda, kuma suna taimakon Allah da Manzonsa. To, waxannan su ne masu gaskiya.*

*Waxanda da suka yi tanadin gidaje da imani gabaninsu suna son waxanda suka yi hijira zuwa wurin su, ba su jin wata buqata a cikin zukatansu game da abin da aka ba su. Kuma suna fifita wasu ('yan'uwan su) akan kawunansu. Kuma wanda duk ya kange ransa daga tsananin rowarta to, waxannan su ne masu ribanta.*

*Kuma waxanda suka zo daga bayansu, suna cewa, "Ya Ubangijinmu! ka yi gafara a gare mu da kuma ga 'yan'uwanmu waxanda suka riga mu yin imani. Kada ka sanya wani qulli a cikin zukatanmu ga waxanda suka yi imani. Ya Ubangijinmu! Lalle kai ne mai tausayi, mai jinqai. Suratul Hashri: 10*

Ka ga bisa ga abin da waxannan ayoyi suka qunsa, wajibi ne a kan kowane musulmi ya qaunaci Muhajiruna da Ansaru. Duk abin da ya faru tsakanin su kuma, na rayuwa da hidima ga addinin Allah, ya fahimce shi a matsayin ijtihadi to wata qaddara da ta riga fata. Savanin abin da 'yan Shi'ah ke yi na zagi da cin mutuncin su, tare da xaukar su ba bakin komi ba.

Ibnu Baxxata da waxansu malamai sun riwaito hadisi daga Sa'adu xan abu Waqqas ya ce: Darajojin mutane uku ne. Biyu sun wuce saura xaya. Mafi kyan abin da za ku iya kasancewa shi ne, ku shiga cikin matakin qarshe. Sannan sai ya karanta:

> *(Arzikin qasa) na matalautan muhajirai ne, waxanda aka fitar da su daga gidajensu, aka raba su da dukiyarsu, suna neman falalar Allah da yarda, kuma suna taimakon Allah da Manzonsa. To, waxannan sune masu gaskiya.*

Ya ce: Waxannan Muhajirai kenan, kuma sun wuce. Sannan ya karanta:

> *Da waxanda suka yi tanadin gidaje da imani gabaninsu suna son waxanda suka yi hijira zuwa wurin su, ba su jin wata buqata a cikin zukatansu game da abin da aka ba su. Kuma suna fifita wasu ('yan'uwansu) akan kawunansu. Kuma wanda duk ya kange ransa daga tsananin rowarta to, waxannan sune masu ribanta.*

Sannan ya ce: Waxannan sune Ansaru. Kuma su ma sun wuce. Sannan ya karanta:

> *Kuma waxanda suka zo daga bayansu, suna cewa: "Ya Ubangijinmu! ka yi gafara a gare mu da kuma ga 'yan'uwanmu waxanda suka riga mu yin imani. Kada ka sanya wani qulli a cikin zukatanmu ga waxanda suka yi imani. Ya Ubangijinmu! Lalle kai ne mai tausayi, mai jinqai. Suratul Hashri: 8-10*

Ya ce: Waxancan biyu sun wuce, *wannan* daraja ita ta rage, to ku kyautata ga abin da ku ka kasacewa, ko da kuna samun wannan darajar da ta saura; ku kasance kuna nema masu gafarar Allah.

Ibnu baxxa xin kuma ya riwaito daga Maliku xan Anas cewa: "Wanda duk ya zagi magabata ba za a ba shi ganimar mayaqa ba, domin ba shi da alhaki a cikinta. Saboda waccan ayar da ta gabata".

Malamai da dama sun ta fi a kan haka game da fassarar ayar kamar Baban Ubaidu xan Sallamu da sauran su.

Kamar yadda Ibnu Abbas *Raliyallahu Anhu* ya ce: "Allah Ta'ala ya yi umurnin a nema ma Sahabbai gafara, alhali ya san yaqi zai auku a tsakaninsu".

Ita kuma Nana Aisha cewa ta yi: "An umrce su, su nema ma Sahabbai gafara amma sai suna zagin su". Tana nuni zuwa ga 'yan Shi'ah.

A cikin Buhari da Muslim, Abi Sa'id Al-khudri ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Kada ku zagi Sahabbaina. Domin kuwa da xayanku zai ciyar da zinarin da ya kai girman dutsen Uhudu, ba zai kai mudun da xayansu ya ciyar ba ko ma rabinsa". Kuma Muslim ya riwaito irinsa daga Abu Hurairata *Raliyallahu Anhu*.

Harwayau a cikin Sahihu Muslim daga Jabir xan Abdullahi ya ce: An ce ma Nana Aisha: Akwai mutanen da ke zagin Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* har ma da Abubakar da Umar, sai ta ce: "Me kuke mamaki a cikin wannan? Ayyukansu ne suka yanke, Allah yana son kada ladarsu ta yanke, sai ya samar masu ita ta hanyar masu zagin su".

Ibnu Baxxata ya riwaito da ingantaccen isnadi daga Abdullahi xan Abbas *Raliyallahu Anhu* ya ce: "Kada ku zagi Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Don Allah Ta'ala ya umurce mu da roqa masu gafara alhalin kuwa ya san yaqi zai auku tsakanin su".

An kuma riwaito daga Abdullahi xan Umar na cewa: Kada ku zaki Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Domin zaman da xayansu ya yi awa xaya a tare da shi *Sallallahu Alaihi Wasallama*, yana taimakon sa ya fi aikin xayanku na shekara arbain. A riwayar waki'u sai ya ce: "Ya fi ibadar xayan ku har qarshen ransa.

Allah Ta'ala ya ce:

﴿ ۞ لَّقَدْ رَضِيَ ٱللَّهُ عَنِ ٱلْمُؤْمِنِينَ إِذْ يُبَايِعُونَكَ تَحْتَ ٱلشَّجَرَةِ فَعَلِمَ مَا فِي قُلُوبِهِمْ فَأَنزَلَ
ٱلسَّكِينَةَ عَلَيْهِمْ وَأَثَٰبَهُمْ فَتْحًا قَرِيبًا ﴿١٨﴾ وَمَغَانِمَ كَثِيرَةً يَأْخُذُونَهَا ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا
حَكِيمًا ﴿١٩﴾ ﴾ الفتح: ١٨ - ١٩

*Haqiqa Allah ya yarda da muminai a lokacin da suke yi maka mubaya'a a qarqashin itaciya. Kuma saboda ya san abin da ke cikin zukatansu sai ya saukar da natsuwa a kan su, kuma ya ba su nasara makusanciya. Da ganimomi masu yawa waxanda za su samu. Kuma Allah ya kasance Mabuwayi ne, mai Hikima.*

﴿ وَعَدَكُمُ ٱللَّهُ مَغَانِمَ كَثِيرَةً تَأْخُذُونَهَا فَعَجَّلَ لَكُمْ هَٰذِهِۦ وَكَفَّ أَيْدِيَ ٱلنَّاسِ عَنكُمْ
وَلِتَكُونَ ءَايَةً لِّلْمُؤْمِنِينَ وَيَهْدِيَكُمْ صِرَٰطًا مُّسْتَقِيمًا ﴿٢٠﴾ وَأُخْرَىٰ لَمْ تَقْدِرُوا۟ عَلَيْهَا قَدْ
أَحَاطَ ٱللَّهُ بِهَا ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرًا ﴿٢١﴾ ﴾ الفتح: ٢٠ - ٢١

*Allah ya yi maka alqawarin ganimomi masu yawa waxanda za ku samu, sai ya gaggauta maku wannan, ya kuma hana mutane kai wa gare ku, don wannan ya zama abin lura ga muminai, ya kuma shiryar da ku ga hanya miqaqqiya. Da wasu (ganimomin) da ba ku da iko a kansu (yanzu), Allah ya kewaye da sanin su. Kuma Allah ya kasance mai iko ne akan kome. Suratul-fathi: 20-21*

To, ga shi dai qarara Allah ya ba da labarin cewa, ya yarda da Sahabban Manzonsa, kuma ya ce, ya san abin da ke cikin zukatansu, wanda a sakamakonsa ne ya ba su nasara makusanciya.

Waxannan da Allah ya yarda da su sun qunshi duk waxanda suka yi mubaya'a a qarqashin bishiya ranar Hudaibiyyah. Kuma daga kansu aka ja

layin magabata. Su ne waxanda Alqur'ani ya kira su magaba ta wurare da dama. Sauran Sahabbai kuwa suna girmama su akan gabacinsu. Su ne kuma suka naxa sayyidina Abubakar, sauran jama'a suka amince musu.

Yawan waxanda suka samu wannan sheda dai ya kai dubu xaya da dari huxu. Kuma su ne *Sabiquna* a cikin Alqur'ani.

Amma wasu malamai na ganin cewa, magabatan farko su ne waxanda suka yi sallah zuwa Alqibla biyu, ma'ana waxanda suka musulunta kafin sauya Alqibla daga Baitul-Maqdis zuwa Ka'aba. Amma wannan ra'ayin yana da rauni akan na farko domin waccan Alqibla ba ta da fifiko a kan wannan. Ba kuma su ne suka canja Alqibla don raxin kansu ba balle ya zama dalilin wani girma gare su. Ga shi kuma babu wani dalili na Shari'ah da ke nuna fifikon yin sallah ga Alqibla biyu, kamar yadda dalilai ke nuna fifikon waxanda suka ciyar, kuma suka yi jihadi kafin qarfin musulunci da yarjejeniyar Hudaibiyyah, da kuma fifikon yin mubaya'ar da suka yi a qarqashin itaciya.

Masana kuwa sun sani cewa, daga cikin magabatan na farko tilas akwai Abubakar da umar da Usmanu da Ali da Xalhatu da Zubairu. Kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi mubaya'a da hannunsa a maimakon Usman. Saboda shi ya aike shi wurin mushrikai a garin Makka, sai aka yi mubaya'ar ba ya nan. Kuma a dalilin Usmanun ne aka yi mubaya'ar, jin cewa an kashe shi.

Ya tabbata a cikin Sahihu Muslim daga Jabir xan Abdullahi *Raliyallahu Anhu* cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Babu wanda zai shiga wuta cikin waxanda suka yi mubaya'a a qarqashin itaciyar". Allah Ta'ala ya ce;

﴿ لَّقَد تَّابَ ٱللَّهُ عَلَى ٱلنَّبِيِّ وَٱلْمُهَٰجِرِينَ وَٱلْأَنصَارِ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُ فِي سَاعَةِ
ٱلْعُسْرَةِ مِنۢ بَعْدِ مَا كَادَ يَزِيغُ قُلُوبُ فَرِيقٍ مِّنْهُمْ ثُمَّ تَابَ عَلَيْهِمْ إِنَّهُۥ بِهِمْ
رَءُوفٌ رَّحِيمٌ ﴿١١٧﴾ ﴾ التوبة: ١١٧

*Haqiqa Allah ya gafarta wa Annabi da Muhajirai da Ansarai waxanda suka bi shi cikin lokacin tsanani, bayan zukatan wasu daga cikinsu sun kusa karkata. Sannan Allah ya yi gafara a kansu. Haqiqa Shi, mai yawan tausayi ne da rahama a kan su. Suratut Tauba: 117*

Allah ya haxa tsakanin Manzo da su wurin yafewa. Allah Ta'ala ya ce:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَهَاجَرُوا۟ وَجَٰهَدُوا۟ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلَّذِينَ ءَاوَوا۟
وَّنَصَرُوٓا۟ أُو۟لَٰٓئِكَ بَعْضُهُمْ أَوْلِيَآءُ بَعْضٍ ﴾ الأنفال: ٧٢

*Haqiqa waxanda suka yi imani, kuma suka yi hijira ga jihadi da dukiyarsu da rayukansa a cikin tafarkin Allah da waxanda suka karvi baqunci (Muhajirai) kuma suka taimaka, to, waxannan sashensu majivinta sashe ne.. Suratull Anfal: 72*

Zuwa inda Allah ya ce:

﴿ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنۢ بَعۡدُ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ مَعَكُمۡ فَأُوْلَٰٓئِكَ مِنكُمۡۚ ﴾ الأنفال: ٧٥

*Waxanda da suka yi imani suka kuma yi hijira da jihadi, to, waxannan suna cikinku. Suratul Anfal: 75*

Sai Allah ya tabbatar da jivintar lamarin juna tsakaninsu. Kuma ya ce ma muminai:

﴿ ۞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّخِذُواْ ٱلۡيَهُودَ وَٱلنَّصَٰرَىٰٓ أَوۡلِيَآءَۘ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلِيَآءُ بَعۡضٖۚ وَمَن يَتَوَلَّهُم مِّنكُمۡ فَإِنَّهُۥ مِنۡهُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٥١ ﴾ المائدة: ٥١

*Ya ku waxanda suka ba da gaskiya! kada ku riqi Yahudawa da Nasara masoya. Sashensu masu jivintan sashe ne. Kuma duk wanda ya jivinci lamarinsu daga cikin ku, to, haqiqa shi, yana daga cikinsu. Tabbas Allah ba ya shiryar da mutane azzalumai. Suratul-Ma'ida: 51*

Zuwa inda Allah ya ce:

﴿ إِنَّمَا وَلِيُّكُمُ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱلَّذِينَ يُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَهُمۡ رَٰكِعُونَ ٥٥ وَمَن يَتَوَلَّ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ فَإِنَّ حِزۡبَ ٱللَّهِ هُمُ ٱلۡغَٰلِبُونَ ٥٦ ﴾ المائدة: ٥٥ - ٥٦

*Abin sani kawai, majivincinku Allah ne da Manzonsa, da waxanda suka yi imani, waxanda suke tsayar da sallah, kuma suna bayar da zakka, alhalin su masu ruku'i ne. Kuma duk wanda ya jivinci Allah da Manzonsa da waxanda suka yi imani, to, haqiqa rundunar Allah su ne masu galaba. Suratul Ma'ida: 55-56*

Kuma Allah Ta'ala ya ce:

﴿ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتُ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلِيَآءُ بَعۡضٖ ﴾ التوبة: ٧١

*Muminai maza da muminai mata sashensu masu jivintar sashe ne. Suratut Tauba: 71*

To, ka ga Allah ya tabbatar da soyayya a tsakaninsu, kuma ya umurci muminai da son su da jivintar su. 'yan-sha-biyu kuwa sun barranta daga gare su; zagin su su ke. Jivinta kuwa ita ce soyayya, adawa ita ce kishiyar soyayya. Su kuwa adawa suke yi da su, suna qin su.

Wasu maqaryata sun qago wani hadisi cewa, wannan ayar ta sauka ne saboda Ali, a lokacin da ya yi sadaka da zobensa yana a cikin sallah. Masana hadisi sun haxu a kan cewa wannan hadisi qarya ne.

Don ka gane qaryar wannan hadisi yi nazarin waxannan abubuwa da za mu faxa:

1) Ayar ta zo ne da sigar jam'i ba mutum guda ba.

2) Kuma “alhali” da aka faxa a cikin ayar ba yana nufin yin sadaka lokacin sallar ba, ballantana ya zamo dalili. Da ya zama dalili kuwa, to, da sauran sha biyun ba su cancanci shugabancin ba, tunda ba su yi hakan ba.
3) Ba a yaba ma mutum sai in ya aikata wajibi ko mustahabbi. Yin zakka a cikin sallah kuwa ba wajibi ba ne, ba mustahabbi ba. Ba ya ma cikin abubuwan da ke nuna natsuwa a cikin sallah.
4) In da bayar da zakka a cikin sallah abu ne mai kyau, to, da ba za a samu banbancin wanda ya bayar yana ruku’i da wanda ya bayar yana tsaye ko zaune ba. Wataqila ma hakan ya fi yiwuwa.
5) Zakka ba ta wajaba a kan Ali a lokacin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba.[1]
6) Bayar da zobe ba shi ne ya fi ba a wajen zakka. Mafi yawan malamai ma sun tafi a kan cewa, fitar da zobe ga zakka ba ya inganta.
7) Wannan hadisin ya nuna an bayar da zakka ga mai bara. Abin yabo shi ne a fitar da zakka tun da farin, kuma da gaggawa idan lokacinta ya yi. Ba sai ya jira almajiri ya roqa ba.
8) Hawan ayar da gangararta na magana ne akan jivintar musulmi da barin jivintar kafirai.

Nan gaba za mu yi cikakken bayani a kan wannan ayar in Allah ya so.

Su dai ‘yan Shi’ah yana da wuya su kafa hujja da wata aya face ta zama hujja a kan su. Kamar yadda suka kafa hujja da wannan aya cewa wilayana nufin shugabanci, sai ga shi an gano abin da take nufi soyayya da jivinta, kuma su, ba su so kuma ba su jivintar waxanda ayar ta ce a so kuma a jivinta.

‘Yan Shi’ah, cikinsu har da *Isma’iliyyah* da na *Nusairiyyah* suna bayyana jivintar kafirai kamar Yahudawa da Nasara da Munafikai. Suna Qin Muhajiruna da Ansaru da waxanda suka biyo bayansu da kyautatawa har ranar qiyama. Wannan sanannen abu ne ga wanda ya nazarce su.

Kuma Allah Ta’ala yana cewa:

﴿ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ حَسْبُكَ ٱللَّهُ وَمَنِ ٱتَّبَعَكَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٦٤﴾ ﴾ الأنفال: ٦٤

*Ya kai Annabi Allah ya ishe ka da waxanda suka bi ka daga cikin muminai. Suratul Anfal: 64.*

Abin nufi shi ne Allah ya isheka kuma ya ishi waxanda suka bi ka daga cikin muminai, Sahabbai su ne mafifitan waxanda suka bi Manzo daga cikin muminai kuma sune na farko.

Kuma Allah Ta’ala yana cewa:

﴿إِذَا جَآءَ نَصْرُ ٱللَّهِ وَٱلْفَتْحُ ﴿١﴾ وَرَأَيْتَ ٱلنَّاسَ يَدْخُلُونَ فِى دِينِ ٱللَّهِ أَفْوَاجًا ﴿٢﴾ فَسَبِّحْ بِحَمْدِ رَبِّكَ وَٱسْتَغْفِرْهُ إِنَّهُۥ كَانَ تَوَّابًۢا ﴿٣﴾ ﴾ النصر: ١ - ٣

[1] Don bai mallaki abin da zai fitar ma da zakka a lokacin ba. Masu Fassara.

*Idan nasarar Allah ta zo da buxi. Har ka ga mutane na ta shiga addinin Allah jama'a-jama'a. To, ka yi tasbihi da godiyar Allah. Haqiqa shi mai yawan karvar tuba ne. Suratun-nas: 1-3.*

Waxanda Manzo ya ga sun shiga addinin Allah jama'a jama'a su ne waxanda suka kasanse a zamaninsa, Sahabbai kenan.

Allah Ta'ala kuma ya ce;

﴿وَإِن يُرِيدُوٓاْ أَن يَخۡدَعُوكَ فَإِنَّ حَسۡبَكَ ٱللَّهُۚ هُوَ ٱلَّذِيٓ أَيَّدَكَ بِنَصۡرِهِۦ وَبِٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٦٢
وَأَلَّفَ بَيۡنَ قُلُوبِهِمۡ﴾ الأنفال: ٦٢ - ٦٣

*Idan har (Kafirai) sun yi nufin su yaudare ka , to, Allah Ya ishe ka. Shi ne ya qarfafa ka da nasararSa da kuma muminai. Kuma ya daidaita tsakanin zukatansu. Suratul-Anfal: 62-63.*

Abin da kowa ya sani ne cewa, Allah ya qarfafa Manzonsa ne da Sahabbai a lokacin rayuwarsa.

Allah Ta'ala kuma ya ce:

﴿وَٱلَّذِي جَآءَ بِٱلصِّدۡقِ وَصَدَّقَ بِهِۦٓ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُتَّقُونَ ٣٣ لَهُم مَّا يَشَآءُونَ
عِندَ رَبِّهِمۡۚ ذَٰلِكَ جَزَآءُ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٣٤ لِيُكَفِّرَ ٱللَّهُ عَنۡهُمۡ أَسۡوَأَ ٱلَّذِي عَمِلُواْ وَيَجۡزِيَهُمۡ
أَجۡرَهُم بِأَحۡسَنِ ٱلَّذِي كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٣٥﴾ الزمر: ٣٣ - ٣٥

*Wanda ya zo da gaskiya, kuma (da wanda) ya gasganta shi, waxannan ne masu tsoron Allah. Suna da abin da suke so wurin Ubangijinsu. Wannan shi ne sakamakon masu kyautatawa. Domin (Allah) Ya yafe masu mafi munin ayyukansu, kuma ya saka masu da mafi kyawon abin da suka kasance suna aikatawa. Suratuz-Zumar: 33-35.*

Wannan nau'i da Allah ya faxi na mutane masu faxin gaskiya da waxanda ke gasgatawa, su savanin masu qirqiro qarya ne ko su qaryata gaskiya a lokacin da ta zo masu kamar yadda za mu fayyace wannan a nan gaba in Allah ya so.

Sahabbai da suka kasance suna shedar cewa, babu wanda ya cancanci bauta sai Allah, kuma suka shedi annabtar Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama*, duka gasgata Alqur'ani, su ne suka fi kowa shiga cikin ayar da ke maganar masu gaskiya da gasgatawa. Babu kuwa wasu jama'a da ke da'awar musulunci da suka fi 'yan Shi'ah yi wa Allah qarya da kuma qaryata gaskiya. Babu kuma wanda ya fi su wuce makaxi da rawa a wajen so da qi kamar su.

Cikinsu ne aka samu waxanda ke xaukaka mutum har su kai shi matsayin Allah. Da waxanda ke jingina annabta ga wanda ba Annabi ba. Ga su da qaryar ma'asumanci ga waxanda ba Annabawa ba. Da ire-iren waxannan abubuwa na miyagun aqidodin da ba a samun su ga sauran qungiyoyi. Malamai

sun haxu a kan cewa, ba wata qungiyar da qarya ta zame ma ruwan–dare kamar Shi'ah.

Kuma Allah Ta'ala ya ce:

﴿ قُلِ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ وَسَلَٰمٌ عَلَىٰ عِبَادِهِ ٱلَّذِينَ ٱصْطَفَىٰٓ ۗ ءَآللَّهُ خَيْرٌ أَمَّا يُشْرِكُونَ ﴿٥٩﴾ ﴾ النمل: ٥٩

*Ka ce: Godiya ta tabbata ga Allah, kuma aminci ya tabbata ga zavavvun bayinsa. Shin Allah Shi ya fi, ko abin da kuke shirka da shi. Suratun-namli: 59.*

Wasu magabata sun ce: Ayar na nufin Sahabban Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama.* Ba shakka kuwa su ne mafifita daga cikin waxanda aka zava a cikin wannan Al'umma, waxanda Allah ya ce game da su:

﴿ ثُمَّ أَوْرَثْنَا ٱلْكِتَٰبَ ٱلَّذِينَ ٱصْطَفَيْنَا مِنْ عِبَادِنَا ۖ فَمِنْهُمْ ظَالِمٌ لِّنَفْسِهِۦ وَمِنْهُم مُّقْتَصِدٌ وَمِنْهُمْ سَابِقٌۢ بِٱلْخَيْرَٰتِ بِإِذْنِ ٱللَّهِ ۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلْفَضْلُ ٱلْكَبِيرُ ﴿٣٢﴾ جَنَّٰتُ عَدْنٍ يَدْخُلُونَهَا يُحَلَّوْنَ فِيهَا مِنْ أَسَاوِرَ مِن ذَهَبٍ وَلُؤْلُؤًا ۖ وَلِبَاسُهُمْ فِيهَا حَرِيرٌ ﴿٣٣﴾ وَقَالُوا۟ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ٱلَّذِىٓ أَذْهَبَ عَنَّا ٱلْحَزَنَ ۖ إِنَّ رَبَّنَا لَغَفُورٌ شَكُورٌ ﴿٣٤﴾ ٱلَّذِىٓ أَحَلَّنَا دَارَ ٱلْمُقَامَةِ مِن فَضْلِهِۦ لَا يَمَسُّنَا فِيهَا نَصَبٌ وَلَا يَمَسُّنَا فِيهَا لُغُوبٌ ﴿٣٥﴾ ﴾ فاطر: ٣٢ - ٣٥

*Sannan muka gadar da littafe ga waxanda muka zava daga cikin bayinMu. Daga cikinsu akwai mai zaluntar kansa, kuma daga cikinsu akwai mai tsa kaitawa, kuma daga cikinsu akwai mai gaggautawa zuwa ayyukan alheri da izinin Allah. To, wannan ita ce babbar falala. (Akwai) Aljanna ta tabbata wadda suna shigar ta, ana qawata su a ciki da mundaye na zinari da lu'u'lu'i, kuma alhariri ne abin sawarsu. Suka ce godiya ta tabbata ga Allah wanda ya kuranye muna baqin ciki. Haqiqa Ubangijinmu mai yawan gafara ne da godiya.Wanda ya saukarda mu a gidan zama (mai daxi) daga cikin falalarSa. Ba wata wahala da za ta shafe mu a ciki, ba kuma gajiya. Suratu-Faxir: 32-35*

Al'ummar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ita ce aka zava a bayan shuxewar Yahudawa da Nasara waxanda su ne al'ummomi biyu da aka yi gabanin ita wannan al'umma.

Hadisi mutawatiri ya zo da cewa: Mafifitan shi ne qarnuka shi ne qarnin da nake cikin sa. Sannan masu biyar su, sannan waxanda suka zo bayan su. Ka ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Sahabbansa sune zavavvu kenan daga cikin bayin Allah.

Allah Ta'ala kuma ya ce :

﴿ مُّحَمَّدٌ رَّسُولُ ٱللَّهِ ۚ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ أَشِدَّآءُ عَلَى ٱلْكُفَّارِ رُحَمَآءُ بَيْنَهُمْ ﴾ الفتح: ٢٩

*Muhammadu Manzon Allah ne. Waxanda ke tare da shi kuma masu tsanani ne akan kafirai, masu rahama a tsakaninsu. Suratul-Fathi: 29.*

Allah Ta'ala ya kuma ce :

﴿ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنكُمۡ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَيَسۡتَخۡلِفَنَّهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ كَمَا ٱسۡتَخۡلَفَ
ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ وَلَيُمَكِّنَنَّ لَهُمۡ دِينَهُمُ ٱلَّذِي ٱرۡتَضَىٰ لَهُمۡ وَلَيُبَدِّلَنَّهُم مِّنۢ بَعۡدِ خَوۡفِهِمۡ أَمۡنٗاۚ
يَعۡبُدُونَنِي لَا يُشۡرِكُونَ بِي شَيۡـٔٗاۚ وَمَن كَفَرَ بَعۡدَ ذَٰلِكَ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡفَٰسِقُونَ ٥٥ ﴾
النور: ٥٥

*Allah ya yi ma waxanda suka yi imani da ayyuka na gari daga cikin ku alqawarin ba su shugabanci a bayan qasa, kamar yadda ya ba waxanda suka gabace ku. Kuma zai tabbatar masu da addininsu wanda (Allah) Ya yardar masu. Kuma zai musanya halin tsoron da suke a kai zuwa halin aminci. Suna bauta maNi, ba su yi maNi tarayya da kowa. To, wanda duk ya kafirta bayan haka, to, waxancan su ne fasiqai. Suratun-Nur: 55.*

To, ga shi dai Allah ya yi alqawari ga waxanda suka yi imani da ayyuka na gari zai basu shugabanci a bayan qasa kamar yadda ya yi masu alqawarin gafara da lada mai yawa cikin waxancan ayoyin. Allah kuwa ba ya sava alqawari.

To, kuma Allah ya riga ya shugabantar da su kamar yadda ya shugabantar da waxanda suka gabace su xin, ya samar masu da aminci bisa alqawarinsa daidai-wa-daida. Abin da ya rage shi ne cikon alqawarin nasa na yi masu gafara da basu lada mai girma. Kuma tabbas, Allah zai qarasa cika alqawarinsa.

Waxannan ayoyi ana kafa hujja da su ta fuska biyu: 1) Cewa, waxanda aka ba shugabancin muminai ne kuma sun yi ayyuka na gari. 2) Kuma an gafarta masu, za a basu sakamako da lada mai girma don sun yi imani kuma sun yi ayyuka na gari. Waxannan su ne alqawurran da Allah ya yi a Suratun-Nur da kuma Suratul-Fathi.

Sanannen abu ne cewa waxannan sifofin da Allah ya ambata sun dace da na Sahabbai a zamanin halifancin Abubakar da umar da Usmanu saboda dai a wannan lokacin ne aka samu cikakken shugabancin da ya tabbatar da addini, da kuma aminci bayan tsoro. Aka sami galaba a kan mafi girman qasashen kafirci: Farisa da Roma. Aka buxe qasar Sham da Iraqi da Masar da Khurasana da yammacin Afirka.

A lokacin da aka kashe Usmanu sai aka samu fitina. Ba a sake buxe wani gari ko xaya ba na kafirai. Kai a lokacin ma kafirai suka yi kwaxayin kama qasashen musulmi, cikinsu har da Sham da Khurasana. Musulmi suka koma barazana ga junansu.

Wannan ya nuna imanin Abubakar da umar da Usmanu da waxanda ke tare da su a lokacin da aka tabbatar da su a bayan qasa, a ka ba su shugabanci. Suka kuma sami aminci. Waxanda ke tare da halifofin uku kuma suka riski lokacin fitina, ayar harwayau tana nuni ga imaninsu. Kamar su: Ali da Xalhatu da Abu Musal-Ash'ari da Mua'wiyah da Amru xan Asi. Domin suna cikin musulmin da Allah ya ba shugabanci, ya tabbatar masu da addini, kuma ya ba su aminci tun da farko.

Amma waxanda farkon lamarinsu ya fara ne a lokacin fitina da rarrabuwar kan musulmi kamar 'yan Shi'ah da Harijawa masu saurin ficewa daga cikin musulunci, to, waxannan ba su shiga cikin ayar ba, ba su kuma cikin waxanda aka siffanta da imani da ayyuka na gari.

Kuma su waxannan ba a shugabantar da su ba, ba a kuma tabbatar da su ba, ba su kuma sami aminci bayan tsoro ba kamar yadda Sahabbai suka kasance. Haqiqanin lamarinsu shi ne, ba su gushe ba suna cikin tsoro da fargaba da rashin tabbas a rayuwa.

Wani zai iya tambaya: Me ya sa a ayar Suratul Fathi Allah ya ce: Ya yi alqawari ga waxanda suka yi imani da ayyuka na gari daga cikin ku.. Bai ce ya yi musu alqawari dukansu ba?

Haka ma kuma a ayar Suratul Ma'ida cewa Allah ya yi: Ya yi ma waxanda suka yi imani daga cikinku kuma suka yi ayyuka na gari alqawari..

Wannan a Larabce shi ake kira bayanin jinsi. An zo da shi don a nuna duk siffofin can nasu ba su ne dalilin gafarar su kaxai ba. Imaninsu dai ne da ayyukan qwarai su ne dalilin samun gafarar da suka yi. A haka kenan ana iya samun waxanda za su yi koyi da su, su ma su samu gafara da lada mai girma.

Kamar yadda Allah Ta'ala ya ce:

﴿ فَٱجۡتَنِبُواْ ٱلرِّجۡسَ مِنَ ٱلۡأَوۡثَٰنِ ﴾ الحج: ٣٠

*Ku nisanci qazanta daga cikin gumaka. Suratul-Hajji: 30.*

Wannan bai nufin cewa, akwai gumaka da ba su da qazanta. A'a yana nufin jinsin gumaka jinsi ne mai qazanta. Wannan yana da misalai da yawa a Alqur'ani da tsantsar harshen Larabawa

Haka ma wani zai iya cewa: Ai munafukai a zahiri suna cikin musulmi.

Sai a ce: Eh. Amma ba su siffantu da waxannan siffofin ba. Yaushe ne munafukai suka zamo masu rahama ga musulmi da tsanani akan kafirai, ko suka nace akan yawan ruku'i da sujada don neman yardar Allah? Kai, asali ma ayar tana maganar waxanda ke tare da Manzon Allah ne, su ko munafukai ba su tare da shi, ba su kuma cikin muminai. Kamar yadda Allah Ta'ala ya ce:

﴿ فَعَسَى ٱللَّهُ أَن يَأۡتِيَ بِٱلۡفَتۡحِ أَوۡ أَمۡرٖ مِّنۡ عِندِهِۦ فَيُصۡبِحُواْ عَلَىٰ مَآ أَسَرُّواْ فِيٓ أَنفُسِهِمۡ نَٰدِمِينَ

٥٢ وَيَقُولُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَهَٰٓؤُلَآءِ ٱلَّذِينَ أَقۡسَمُواْ بِٱللَّهِ جَهۡدَ أَيۡمَٰنِهِمۡ إِنَّهُمۡ لَمَعَكُمۡۚ حَبِطَتۡ

أَعۡمَٰلُهُمۡ فَأَصۡبَحُواْ خَٰسِرِينَ ٥٣ ﴾ المائدة: ٥٢ - ٥٣

*Zai yiwu Allah ya zo da wani buxi ko wani al'amari daga wurinSa, sai (munafikai) su wayi gari suna masu nadama a kan abin da suka voye cikin zukatansu. Kuma waxanda suka yi imani na cewa, shin waxancan ne suka yi mafi girman rantsuwa cewa, lalle suna tare da ku? Ayyukansu sun lalace, sai suka wayi gari suna masu hasara. Suratul-Ma'ida: 52*

Kamar kuma cewar da Allah Ta'ala ya yi:

﴿ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَقُولُ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ فَإِذَآ أُوذِىَ فِى ٱللَّهِ جَعَلَ فِتْنَةَ ٱلنَّاسِ كَعَذَابِ ٱللَّهِ وَلَئِن
جَآءَ نَصْرٌ مِّن رَّبِّكَ لَيَقُولُنَّ إِنَّا كُنَّا مَعَكُمْ أَوَلَيْسَ ٱللَّهُ بِأَعْلَمَ بِمَا فِى صُدُورِ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿١٠﴾
وَلَيَعْلَمَنَّ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَلَيَعْلَمَنَّ ٱلْمُنَٰفِقِينَ ﴿١١﴾ ﴾ العنكبوت: ١٠ - ١١

*Daga cikin mutane akwai masu cewa, mun yi imani da Allah. Amma idan aka cutar da su a tafarkin Allah sai su mayar da fitinar mutane kamar azabar Allah. To, kuma wallahi inda wata nasara ta zo daga Allah haqiqa za su ce, lalle mun kasance tare da ku. To, shin Allah bai san abin da ke cikin zukatan dukan talikai ba? Wallahi Allah ya san waxanda su ka yi imani. Kuma wallahi ya san munafukai. Suratul Ankabut: 10-11*

Ka ga waxannan ayoyin sun bayyana maka cewa, su munafukai ba su cikin muminai, ba su kuma cikin ma'abuta littafi.

Babu dai inda zaka sami munafunci ya yi katutu kamar cikin Shi'ah 'yan-sha-biyu. Sun fi koya raya musulunci a zahiri, amma suna amfani da wannan suna cutar musulunci da musulmi.

Kuma munafukai a wancan lokaci da yawansu sun tuba, sun gyara zamansu, sun shiga sahun muminai, bayan da Allah ya fallasa su, ya bayyana siffofinsu, ya kuma yi razani a kansu in ba su daina ba. Duba abin da Allah Ta'ala ya ce masu:

﴿ لَّئِن لَّمْ يَنتَهِ ٱلْمُنَٰفِقُونَ وَٱلَّذِينَ فِى قُلُوبِهِم مَّرَضٌ وَٱلْمُرْجِفُونَ فِى ٱلْمَدِينَةِ لَنُغْرِيَنَّكَ
بِهِمْ ثُمَّ لَا يُجَاوِرُونَكَ فِيهَآ إِلَّا قَلِيلًا ﴿٦٠﴾ مَّلْعُونِينَ أَيْنَمَا ثُقِفُوٓا۟ أُخِذُوا۟ وَقُتِّلُوا۟ تَقْتِيلًا
﴿٦١﴾ ﴾ الأحزاب: ٦٠ - ٦١

*Wallahi in munafukai da waxanda ke da cuta a cikin zukatansu da masu yin varna a Madina ba su daina ba, za mu baka iko a kansu. Sannan ba za su sake yin maqwabtaka da kai a cikin ta ba, sai kaxan. (Su) la'anannu ne, a duk wurin da aka same su za a kama su a karkashe su kashewa. Suratul-Ahzab: 60-61*

Idan muka duba wannan razani da Maxaukakin Sarki ya yi a kansu, muka kuma ga bai ba Manzonsa dama akan kama su da karkashe su ba, bai

kore su daga Madina ba, mun san cewa, sun tuba, sun daina munafucci kenan. Ko banza dalilin munafucci ya riga ya kau, don addini ya xaukaka, babu sauran wanda za a goya ma baya sai gaskiya.

A lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya je Hudaibiyyah duk waxanda ke tare da shi sun yi masa mubaya'a qarqashin itaciya sai *Jaddu xan Qaisu.* Shi ne ya je ya vuya a bayan wani jan raqumi. Haka ya zo cikin hadisi cewa, dukkansu za su shiga aljanna sai na wancan na wajen jan raqumi.

A taqaice dai, munafikai sun kasance qasqantattu, waxanda ake da rinjaye a kansu, musamman ma a qarshen rayuwar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da kuma lokacin yaqin Tabuka. Don Allah Ta'ala ya ce:

﴿ يَقُولُونَ لَئِن رَّجَعْنَآ إِلَى ٱلْمَدِينَةِ لَيُخْرِجَنَّ ٱلْأَعَزُّ مِنْهَا ٱلْأَذَلَّ ۚ وَلِلَّهِ ٱلْعِزَّةُ وَلِرَسُولِهِۦ
وَلِلْمُؤْمِنِينَ وَلَٰكِنَّ ٱلْمُنَٰفِقِينَ لَا يَعْلَمُونَ ٨ ﴾ المنافقون: ٨

*Suna cewa: "Wallahi idan mun koma Madina masu xaukaka za su fitar da qasqantattu daga cikinta". Xaukaka kuwa ta tabbata ga Allah da Manzonsa da muminai, amma munafukai ba su sani ba. Suratul-Munafiqun: 8.*

Sai Allah Ta'ala ya ba da labarin cewa, xaukaka ta muminai ce ba ta munafikai ba. Daga nan muka san cewa, xaukaka da qarfi na tare da muminai ne, kuma muka gano qasqanci da wulakancin da munafukai su ke cikin sa. Saboda haka ba zai yiwu Sahabbai su zamo munafukai ba.

Sanannen abu ne cewa, shiryayyun halifofi da manyan Sahabbai na cikin mafi xaukakar mutane a wancan lokaci. Ka ga kenan ba zai yiwu su zamo munafukai ba. Qasqanci da wulaqancin da munafukai ke ciki shi ya yi daidai da halin 'yan-sha-biyu waxanda, babu wata qungiya mai jingina kanta ga musulunci wadda zindiqanci da munafunci suka kai yawan na Shi'ah a cikin ta.

Kai ma tilas ne ka tarar da xayan alamomin munafunci cikinsu. Domin tushen munafunci shi ne qarya. Su kuma sun gina addininsu ne a kanta, da sunan *Taqiyyah.* Taqiyyah ko tana nufin mutum ya furta savanin abin da ke cikin zuciyarsa. Shi'ah 'yan-sha-biyu sun mayar da wannan xaya daga cikin asullan addininsu, har ma suna rawaito wannan daga shugabanin Ahlul-Baiti waxanda Allah ya barrantar da su daga wannan. Kamar yadda suka hikaito wannan daga Ja'afar As-Sadiq cewa wai, ya ce: "Taqiyya addinina ce, kuma addinin iyayena". Allah Ta'ala kuwa ya tsarkake Ahlul-Baiti da sauran muminai daga wannan. Ahlul-Baiti kam sun fi kowa gaskiya da imani. Taqawa ita ce addininsu ba Taqiyya ba.

Abu ne mai yiwuwa 'yan Shi'ah su kafa hujja a kan wannan aqida tasu da cewa, ai Allah Ta'ala ya ce:

﴿ لَّا يَتَّخِذِ ٱلْمُؤْمِنُونَ ٱلْكَـٰفِرِينَ أَوْلِيَآءَ مِن دُونِ ٱلْمُؤْمِنِينَ ۖ وَمَن يَفْعَلْ ذَٰلِكَ فَلَيْسَ مِنَ
ٱللَّهِ فِى شَىْءٍ إِلَّآ أَن تَتَّقُوا۟ مِنْهُمْ تُقَىٰةً ﴾ آل عمران: ٢٨

*Kada muminai su xauki kafirai majivinta lamurransu koma bayan muminai. Kuma wanda ya aikata haka shi ba kome ne ba a wurin Allah, sai fa in kun ji tsoron su don ku kiyayi cutarsu. Suratu Ali-Imran: 28*

Amsar da za mu ba su a nan ita ce, ai idan aka dubi wannan aya da kyau, tare da la'akari da dalilin saukarta, da sauran hukunce-hukuncen shari'ah, to, za a fahimci cewa, ba tana halasta wa muminai yin qarya da munafucci ba. Ko alama. Ta dai ba su damar kariyar kansu ne daga kafirai a lokacin da wani al'amari ya kai mashafar turare. Ya halasta ga musulmi bisa wannan qa'ida ya furta kalmar kafirci alhalin zuciyarsa na tsattsage da imani. Amma da sharaxin an tilasta shi a kan haka. Savanin abin da ya faru tsakanin Sahabbai da Ahlul-Baiti. Tarihi ya tabbatar da cewa, babu wanda ya yi wa Abubakar mubaya'a a kan tilas. To, ballantana a tilasta wani akan yabonsa. Ka ga kuwa sayyidina Ali da 'yan gidan annabta da dama sun bayyanar da yabon halifa Abubakar da sauran Sahabbai, sun kuma yawaita du'ai gare su. Wa zai tilasta masu yin haka?

Ko a zamanin Banu Umayyah da Banul Abbas akwai 'yan adawa da dama waxanda basu kama qafar Aliyu ba ta fuskar imani da tsoron Allah. Suna tsanar shugabannin lokacinsu saboda nasu dalilai, kuma ba su fitowa su yabe su don jin tsoronsu, amma sun rayu a cikin cikakken 'yanci da walwala, ba a xauki kowane mataki a kansu ba. To, balle zamanin halifofi shiryayyu.

Daga nan za mu san cewa abin da Shi'ah 'yan-sha-biyu ke faxa cewa su faxi abin da ba ya cikan zukatansu ba tare da wata tilastawa da aka yi masu ba, yana xaya daga cikin hanyoyin qarya da munafunci. Ga dai ko fursunonin yaqi, kafirai, ba wanda ya tava hana su bayyana addininsu a qasashen musulmin da suka kamo su. Haka su ma Harijawa, duk da aqidarsu ta kafirta sayyidina Usman da sayyidina Ali da sauran musulmi, ba su tava voye aqidarsu ko wani sarki ya tilasta su yin haka ba.

To, ya za a zaci Ali da sauran Ahlul-Baiti sun fi fursunonin yaqi raunin zuciya da imani, kuma Harijawa da xaixaikun Ahlus-Sunnah duk sun fi su qarfin hali da dauriyar bayyana abin da ke cikin zukatansu? Mu mun sani ta hanyar ilimi mutawatiri cewa, babu wanda ya tilasta wa Ali da 'ya'yansa ambaton darajojin halifofi da nema masu rahamar Allah. A'a, sun dai kasance suna faxain wannan ba tare da an tilasta su ba, kuma xayansu na yin wannan yabon a gaban makusantansa, kamar yadda wannan ya tabbata ta hanyar ilimi mutawatiri.

A taqaice dai, duk maganar da ke cikin Alqur'ani wadda ta shafi muminai da masu taqawa da masu kyautatawa da yabonsu, su- Sahabbai- ne farkon waxanda ke shiga ciki daga cikin wannan al'umma. Kamar yadda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: *Mafifitan qarnuka shi ne*

*qarnin da aka aiko ni cikinsa, sannan waxanda ke bi masu, sannan waxanda ke bi masu.*

Wani abu kuma da ke bayyana maka qaryar wannan xan Shi'ar shi ne, abin da ya riwaito game da halayyar Sahabbai bayan rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa wai, wasu sun nema ma kansu shugabanci ba tare da suna da alhaki cikinsa ba, kuma mafi yawan mutane suka yi masu mubaya'a don son abin duniya.

Wannan maganar tasa da Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya ke babu shakka. Domin shi ne mafi yawan mutane suka yi ma mubaya'a. kuma sanannen abu ne cewa, Abubakar bai nema ma kansa shugabanci ba, ko ta wace hanya. Abin da ma ya ce shi ne, na yardar maku da xayan mutanen nan biyu: Umar ko Abu Ubaida, duk wanda kuke so. A nan ne Umar ya ce: Wallahi da in shugabanci mutanen da Abubakar ke cikinsu na fi son in miqa wuyana a sare shi in dai wannan ba zai kusantar da ni ga savon Allah ba". Wannan lafazinsa ne a cikin Sahihul Buhari da Sahihu Muslim. An kuma riwaito yana cewa: "Ku xauke mani wannan nauyi! Ku xauke mani wannan nauyi! Amma musulmi sun zave shi kuma sun yi masa mubaya'a don sun san cewa shi ne mafifici a cikinsu. Kamar yadda Umar ya ce musu ranar Saqifa a gaban Muhajiruna da Ansaru: "Kai ne shugabanmu, kuma wanda ya fi soyuwa ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* daga cikin mu. Wannan ma yana cikin Sahihul Buhari da Muslim.

To, mu qaddara ma halifa Abubakar ya nemi wannan shugabanci, aka kuma ba shi, to, ko a haka, qarya ce tabbatatta a ce ya ba su abin duniya, kuma a kansa ne suka yi masa bai'a.

Dalilinmu a kan haka kuwa shi ne, koda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kwanta dama Abubakar *Raliyallahu Anhu* duk ya qarar da dukiyarsa wurin taimakon addini. Kuma babu baitulmali a qarqashinsa balle a ce. Qari a kan haka, kuma sahabban da suka yi masa bai'a har da Ali *Raliyallahu Anhu* mutane ne da ba a yi masu gudun duniya kamar su ba.

A siyasar sayyidina Abubakar gwamnati tana raba kuxi ne daidai ga mutane. Ba a fifita kowa a kan wani. Wannan kuma ita ce siyasar Ali *Raliyallahu Anhu* a lokacinsa. Don haka, da ma sun yi wa Aliyu mubaya'a da abin da zai yi shi ne daidai abin da Abubakar ya yi. Kuma arzikin da za su samu shi xin ne. to, ya za a ce sun zave shi don abin duniya?

A siyasar Umar akan raba dukiyar gwamnati ne ga mutane daidai kusancinsu da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da kuma qoqarin da suka gabatar wajen kafa addini. Lokacin da Umar ya ba da shawarar yin haka ga Abubakar sai ya ce masa: Zan sayi imaninsu ne daga gare su?

To, wace dukiya ce mafi yawan musulmi suka samu don sun yi wa Abubakar mubaya'a? Tunda yake yana daidaitawa wurin ba da kyauta a tsakanin musulmin farko da waxanda suka shiga musulunci daga baya? Abubakar ya kasance yana cewa, sun shiga musulunci ne saboda Allah, kuma

shi zai saka masu. Amma kuxin masarufi to, abin amfani ne kowa na da buqata da shi.

Ga shi kuwa Mahajiruna da Ansaru da waxanda suka kyautata bin sawunsu irin su Umar da Abu Ubaidata da Usaidu xan Hudairu da sauransu, duk Abubakar bai banbanta su ba da waxanda aka xiyauta da waxanda suka musulunta cikin mutanen Makka bayan an bude ta, kai har ma waxanda suka musulunta bayan rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Shin ko waxannan sun sami wani abin duniya saboda shugabancin Abubakar?

Anan yana da kyau mu bayyana wata qa'ida wadda zata taimaka a fagen jayayya da Shi'ah 'yan-sha-biyu waxanda suke zargin magabatan Sahabbai, musamman halifofi guda uku. Wannan qa'idar ita ce:

Savanin da ke tsakanin Ahlus-Sunnah da Shi'ah 'yan-sha-biyu yana da matuqar kama da savanin da ke tsakanin musulmi da Kirista. Mu musulmi, mun yi imani da cewa Isa *Alaihis Salamu* bawan Allah ne, kuma Manzonsa. Ba mu wuce wuri game da shi kamar yadda Kirista ke yi. Ba mu kuma yi masa jafa'i kamar yadda Yahudawa ke yi.

Kirista na raya cewa, Isa *Alaihis Salamu* abin bauta ne. Sun fifita shi a kan Annabawa: Muhammadu da Ibrahimu da Musa da sauran su. Kai ma har ma suna fifita Sahabban Isa *Alaihis Salamu* a kan waxannan Manzanni. Haka Shi'ah 'yan-sha-biyu ke son fifita waxanda suka yi yaqi a zamanin fitina tare da sayyidina Ali kamar su Muhammadu xan Abubakar da Ashtar An-Nakha'i a kan manyan Sahabban Annabi irin Abubakar da Umar da Usmanu da dukkan Muhajiruna da Ansaru.

To, a wajen jayayya, idan musulmi ya tattauna da Kirista ba zai iya faxin wani abu game da Isa *Alaihis Salamu* ba face gaskiya. Amma in kana son ka fito da jahilcin Kirista da rashin hujjarsa, to, sai ka qaddara jayayyar a tsakanin sa da Bayahude, ka koma gefe ka saurare shi. Idan har Kirista ba zai iya kare Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba, to, duk zargin da ya yi masa zai tarar Bayahude yana yi wa Annabi Isah *Alaihis Salamu* irin sa. Kuma duk hujjar da zai kawo don ya kare Annabi Isah *Alaihis Salamu wannan* hujjar ta fi kare Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* daga shi nasa zargin. Saboda haka, in zargin da Bayahude yake yi wa Annabi Isah *Alaihis Salamu* qarya ne, to, zargin Kirista ga Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fi zama qarya.

Wannan ya tava faruwa a tsakanin malaman Kiristoci da wani malami musulmi shi ne, Alqali Abubakar At-Tabarani. A lokacin da musulmi suka aika masa da gayyata don ya zo fadar wani sarki na Kirista a Qusxanxiniya (Istanbul). Malaman na Kirista sun san girmansa, kuma suna jin tsoron cewa, ba zai yi sujada ga sarkinsu ba idan ya shiga wurinsa. Don haka sai suka shigar da shi ta wata gajeruwar qofa don ya shiga a sunkuye. Nan take sai malamin ya fahimci manufarsu. Sai ya juya ya shiga qofar da baya, ya sanya kuturinsa kamar shi ne mai gaida sarkin. Abin da ya faru anan sai ya zama akasin abin da suke nufi.

Zaunawar malamin ke da wuya sai wani daga cikin fada-fadansu ya tambaye shi: “Mene ne ya faru game da matar mai gidanku”? Yana nuni da habaici ga qazafin da munafukai suka yi wa Nana Aishah, kuma harwayau da yawan ‘yan Shi’ah suna ci gaba da yi mata wannan qazafin.

Amsar da malam Abubakar ya ba fadan Kirista a nan ita ce, ya ce masa: “Ai su biyu ne maqiyan Allah suka yi wa zargi da Zina; Maryam da Aishah. Amma Maryam ta haifi xa ba tare da tana da miji ba. Ita kuma Aishah ba ta haifi xa ba kodayake tana da miji”.

Ka ga a nan ya xaure su. Don haka, sai suka yi tsit kamar ruwa ya ci su. Abin nufinsa shi ne, barrantar Nana Aisha game da wannan qazafin ya fi qarfi qwarai, a kan barrantar Maryam, duk da yake ita ma wankakkiya ce. Don shubuha ta fi qarfi a game da lamarinta, to, in duk da haka ya tabbata cewa masu sukar Maryam qarya ce suke yi, to, tabbatar qaryarsu a game da sukar da aka yi wa Aisha *Raliyallahu Anha* ta fi qarfi.

Makamancin wannan ne, Allah Ta’ala ya yi wa mushrikai in da yake cewa:

﴿ يَسْـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلشَّهْرِ ٱلْحَرَامِ قِتَالٍ فِيهِ ۖ قُلْ قِتَالٌ فِيهِ كَبِيرٌ ۖ ﴾ البقرة: ٢١٧

*Suna tambayar ka game da yaqi a cikin watan da aka haramta, ka ce yaqi a cikin babban laifi ne. Suratul Baqarati: 217*

Sannan ya ce:

﴿ وَصَدٌّ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ وَكُفْرٌۢ بِهِۦ وَٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ وَإِخْرَاجُ أَهْلِهِۦ مِنْهُ أَكْبَرُ عِندَ ٱللَّهِ ۚ وَٱلْفِتْنَةُ أَكْبَرُ مِنَ ٱلْقَتْلِ ۗ ﴾ البقرة: ٢١٧

*Amma kange mutane daga hanyar Allah da kafirce ma Allah da (hana mutane isa) masallaci mai Alfarma da fitar da mazaunansa daga ciki, (wannan) ya fi girman laifi a wurin Allah. Kuma fitinar da mutane (don su bar addini) ya fi kisa girman laifi. Suratul Baqarati: 217*

Wannan ayar ta sauka ne a lokacin da mushrikai suka aibanta musulmin da suka kashe Ibnul Hadrami, cikin xaya daga cikin watanni masu alfarma, sai Allah ya ce, wannan laifin da waxannan musulmi suka yi yana da girma, amma abin da mushrikai suke a kai na kafirci da kange mutane daga addini da fitar da musulmi daga garinsu, waxannan laifuffukan sun fi girma a wurin Allah. Kuma keta alfarmar Makka ya fi zama laifi a kan keta alfarmar wata.

A nan duk qungiyoyin biyu sun aikata laifi. Amma kuma mai babban laifi ya take nasa, ya rinqa hargowa a kan mai laifi qarami. Don haka, sai aka ce, su kare laifinsu tukuna kafin su yi maganar na wasu. Idan har sun kasa kare kansu daga wancan laifi, to, don me za su damu da masu laifin da bai kai nasu ba.

Wannan shi ne halin da ke tsakanin musulmi da Yahudawa da Nasara, kuma shi ne halin da ke tsakanin Ahlus-Sunnah da sauran ‘yan bidi’a, musamman ma ‘yan Shi’ar sha biyu.

To, wannan shi ne abin da ke tsakanin Ahlus-Sunnah da ‘yan-sha-biyu ga lamarin Abubakar da Ali. Xan Shi’ar ba zai iya tabbatar da imanin Ali ba, da cewa shi xan aljanna ne, ballantana ya tabbatar da shugabancinsa sai fa in ya tabbatar da haka ga Abubakar da Umaru da Usmanu.

Don in ba haka ba duk lokacin da ya so ya tabbatar da wata daraja ga Ali, to, dalilai ba sa taimaka masa, kamar yadda in Kirista ya so ya tabbatar da annabcin Isa *Alaihis Salamu* ba zai iya ba sai in ya yarda da annabcin Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama,* domin dalilai ba za su taimake shi ba.

Bisa ga haka, idan ka tattauna da wani daga cikin ‘yan-sha-biyu, to, qaddara masa tattaunawar tsakanin sa da Harijawa masu kafirta Ali da Nasibawa masu fasiqantar da shi. Harijawa sun tafi a kan cewa, Ali azzalumi ne, mai neman duniya, wanda ya nemi halifanci da qarfi, ya yaqi mutane a kansa. A garin haka kuwa ya kashe dubun dubatar musulmi, abin da ya hana cin nasarar mulkinsa. Ya kuma kasa samun abin da yake so na kevanta da mulki, sai magoya bayansa suka dare masa, suka yaqe shi har daga qarshe suka kashe shi.

To, ka ga wannan magana in ta kasance qarya ce, to, ba shakka maganar xan Shi’ar a game da Abubakar da umar ta fi ta zama qarya. In kuma har maganar xan Shi’ar a game da Abubakar da Umar daidai ne, kuma magana ce ta gaskiya, to, lalle ko maganar Harijawa a kan Ali ta fi cancantar zama gaskiya.

Kowa ya sani cewa, shugaban da mutane suka zava a cikin yardarsu da amincewarsu ba tare da tilastawa da qarfin takobi ko sanda ba, kuma bai ba kowa kuxi ba cikin waxanda suka zave shi. Sannan duk suka haxu a kan shugabancinsa. Kuma bai shugabantar da ‘yan’uwansa ko ‘ya’yansa ba, bai kuma bar wa magadansa dukiya ba daga cikin dukiyar musulmi. Ya kasance shi yana da kuxi kuma ya qarar da su a hanyar Allah. Sannan bai nemi a maida masa kuxin ba. Ya kuma yi wasicci da cewa, abin da ya bari na dukiya a mayar da shi baitulmali tare da cewa, bai mallaki komai ba sai wani tsohon tufa da doki da baqar kuyanga.

Har ya kai ga lokacin da aka xauko wannan dukiyar tasa za a saka a baitulmali Abdurrahman xan Aufu ya ce wa Umar, qwace zaka yi wa iyalan Abubakar? Sai Umar ya ce: Abubakar ne ya sauke wa kansa wannan kaya, ni kuma ba zan xora wa kaina shi ba. A nan ne Abdurrahman ya ce: “Ya Allah! Ka jiqan Abubakar. Haqiqa Abubakar ka wahalar da shugabanni bayan ka”.

Ga shi kuma har ya qare mulkinsa bai kashe musulmi ko xaya ba, bai sa musulmi ya yaqi musulmi ba. A maimakon haka, ya xaura yaqi da murtaddai da kafirai har Allah ya bashi nasarar cin manyan garuruwa da isar da saqon musulunci cikinsu. Da ya ga manzon mutuwarsa kuma sai ya tsayar wa da

musulmi halifa qaqqarfa, amintacce, mai xinbin hikima da tarin ayyuka, wanda ya tsara aikin gwamnati, ya ci garuruwa da birane, ya shimfixe qasa da adalcinsa.

To, wannan bawan Allah idan har mai sukar sa na da gaskiya, to, gaskiyar wanda yake sukar Ali ta tabbata. In ko har Ali wankakke ne daga tuhuma, to, wankuwar Abubakar ta zama dahir.

Idan kuma har murtaddai na da uzuri akan rashin yi wa Abubakar mubaya'a, to, uzurin su Mu'awiyah na rashin yi wa Ali mubaya'a ya fi qarfi. Domin su cewa suka yi, ba za mu yi mubaya'a ba sai ga wanda zai yi muna adalci, ya kare mu daga wanda ke son zaluntar mu, ya karva mana haqqinmu daga wanda ya zalunce mu. In ko har bai yi haka ba, to, shi azzalumi ne ko ajizi. Kuma bai wajaba mu yi mubaya'a ga azzalumi ko ajizi ba.

To, in har maganar su Mu'awiyah vatatta ce, to, vacin maganar mai cewa Abubakar da Umar azzalumai ne, masu neman duniya da shugabanci ya fi girma.

Duk mai hankali yana iyar fahimtar wannan magana cikin sauqi. Ya ya ma za a iya kwantanta shubuhar da Abu Musal-Ash'ari ya yi na cewa, a saukar da Ali daga shugabanci, Mu'awiyah kuma daga gwamna, a mayar da lamari ga musulmi su sake zave. Ina wannan shubha ta kai wadda Abdullahi xan Saba'i da 'yan'uwansa 'yan Shi'ah suka kawo cewa, Ali Imami ne ma'asumi, ko waxanda suka ce shi abin bauta ne ko an yi kuskuren annabta don shi ne ya cancance ta?

Ya za ka kwatanta shubhar masu ganin Mu'awiyah ya zama shugaba da shubuhar masu cewa Ali abin bauta ne ko kuma Annabi ne? Na farkon basu zama kafirai don irin wannan magana. To, amma na biyun fa?

A taqaice dai, 'yan Shi'ar sha biyu ba su iya tabbatar da imanin Ali da adalcinsa matuqar sun tsaya a kan aqidarsu ta 'yan-sha-biyu. Domin za mu lulluve su da zarge-zargen Harijawa da Nasibawa su rikirkita su.

Su dai Harijawa sun ce, ba su yarda cewa Ali mumini ne ba. Sai suka ce shi kafiri ne, azzalumi. Kamar dai yadda su 'yan-sha-biyu ke faxa game da Abubakar da Umar. Kuma duk dalilin da 'yan Shi'ah za su kawo a kan zargin Abubakar da Umar to, Harijawa za su kawo wanda ya fi shi qarfi. Idan kuma su, 'yan Shi'ah sun kafa hujja da hadissan da aka riwaito mutawatirai cewa, Ali ya musulunta, ya kuma yi hijira da jihadi, to, ai an riwaito irin su da ma waxanda suka fi su qarfi a game da musuluncin Abubakar da Umar da Usman. Kai, da ma Mu'awiyah da Yazid da sarakunan Banu Umayya da na Banul Abbas.

In suka ce, ai an san Ali na sallah da azumi da jihadi, to, su ma halifofi ukun ai haka ne. In suka raya cewa su waxancan munafikai ne, to, su ma Harijawa sun ce, Ali *Raliyallahu Anhu* munafiki ne. Suka ce, ya kasance yana hasadar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* don yana xan qanin babansa, kuma wai, daman yana da qudurin vata addininsa, bai samu damar haka ba a zamanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da zamanin

halifofi ukun. Amma da ya samu dama wai, sai ya haxa kai aka kashe halifa na uku, don ya samu kujerarsa. Sannan ya hura wutar fitina, yana mai karkashe Sahabban Manzo da al'ummarsa don qin Manzo da yake yi da adawa da shi. Suka ce, shi munafiki ne a voye, wanda yake bayyana savanin abin da ke zuciyarsa, saboda addininsa shi ne taqiya. Kuma a baxini tare yake da ku 'yan Shi'ah masu cin zarafin magabatan al'umma da masu ce masa shi Allah ne ko Manzo. Suka ce, don haka ne qungiyar Shi'ah *Baxiniyyah* suka zamo mabiyansa. Kuma su ne suka san sirrinsa, suke cirato shi daga wurinsa.

Ka ga duk yadda xan Shi'ah zai kare Ali da wata hujja, to, hujjar ta isa ta kare halifofi uku har da qari. Kuma idan maganar Harijawa qarya ce, to, qaryar maganar 'yan Shi'ah a kan halifofi ta fi fitowa fili, kuma ta fi karvuwa a wurin jahillai. Amma ba wanda zai warware wannan rikicin sai Ahlus-Sunnah.

Idan kuma suka ce, za su tabbatar da imanin Ali *Raliyallahu Anhu* da adalcinsa ta hanyar wani nassi na Alqur'ani da za su ce ya kevance shi, sai a ce masu: Ayoyin Alqur'ani a game suke. Babu kuma wata ayar da za su iya raya cewa, ta kevance shi face ana iya raya cewa ita wannan ayar ta kevanci Abubakar da Umar. Kuma idan aka yi hujja sai hujjar wanda ya jingina ayar ga Abubakar da Umar ta fi karvuwa.

Idan kuma sun ce, darajojin Ali sun tabbata ne ta hanyar ciratowa da riwaya, sai a ce musu riwayoyin da suka bayyana darajojin waxancan halifofin sun fi yawa da qarfin inganci. In suka ce, mutawatiri ne, a ce masu wa ya yi tawaturin, tun da kun ce, Sahabbai duk sun kafirta sai kaxan daga cikinsu? Ga shi ko babu 'yan Shi'ah a cikin Sahabbai waxanda yawansu ya kai na waxanda ke riwayar mutawatiri. Ba ta yadda za ku iya tabbatar da wannan ta hanya yankakkiya sai in kun bi hanyar Ahlus-Sunnah, kamar yadda kiristoci ba su iya tabbatar da annabcin Isa *Alaihis Salamu* in ba su bi hanyar musulmi ba.

Wannan ba shi da banbanci da wanda ke son tabbatar da cewa Ibnu Abbas faqihi ne ba tare da ya yarda cewa Ali shi ma faqihi ne ba. Ko ya faxi haka game da Ibnu Umar ba tare da ya yarda da haka ga babansa Umar ba. Ko ya ce, malam Alqamatu da malam Aswadu (almajiran Ibnu Mas'ud) masana ne, amma ba tare da ya tabbatar da sanin Ibnu Mas'ud ba. Da ire-iren wannan.

Rashin gano wannan ne ya sa 'yan-sha-biyu suka fi kowa jahilci da vata, kamar yadda Kirista suke mafi jahilcin mutane. Haka Shi'ah 'yan-sha-biyu suka fi kowa sharri da cuta kamar yadda Yahudawa suka fi kowa sharri da cuta. 'Yan Shi'ah sun haxa tsakanin vatan Kirista da sharrin Yahudawa.

### 2.1 Wannan da wannan Suna Da Banbanci

Xan Shi'ar ya ba da misali da qissar Umaru xan Sa'ad wanda ya nemi kuxi da mulki ya aikata abin da bai dace ba. To, wannan na nufin duk magabatan farko su ma sun kasance haka? To, ga babansa nan Sa'adu xan Abu Waqqas, yana cikin waxanda suka fi kowa gudun duniya game da mulki da shugabanci. A lokacin da fitina ta auku sai ya qaurace wa mutane ya yi zaman sa a gidansa da yake Al-Aqiq, sai da xan nan nasa ya same shi, yana nuna

ganin laifinsa a kan ya bar mutane suna jayayya a kan mulki ya qauracewarsa. Sai Sa'adu ya ba shi amsa da hadisin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Allah Ta'ala na son bawa mai taqawa, mai voye kansa, kuma mai wadatar zuci"

Kar mu manta, Sa'adu xin nan fa a lokacin shi kaxai ya rage cikin 'yan kwamitin naxin sarauta sai Ali. kuma jarumi ne da ya buxa qasar Iraqi, ya karya Kisran Farisa da rundunarsa. Kuma shi ne wanda ya yi saura daga cikin *Asharatul Mubassharuna Bil Jannah.*

To, idan ya kasance bai dacewa a kwatanta Umaru xan Sa'ad da babansa, ya za a kwatanta shi da Abubakar da Umar?

'Yan Shi'ah suna darajanta xan Abubakar suna fifita shi a kan babansa Abubakar Siddiq, ba don kome ba sai don ya musguna wa sayyidina Usman, kuma yana cikin muqarraban Ali, kuma Alin na aure da uwarsa. A kan haka, 'yan Shi'ah suke son sa, suna zagin ubansa, suna la'antar sa. To, ya za su yi da *Nasibawa* idan suka yi haka game Umaru xan Sa'ad, suka yabe shi a kan sa hannunsa wajen kisan Husaini, suka zagi babansa don bai goyi bayan Mu'awiyah ba a lokacin fitina? Akwai banbanci a tsakanin wannan jahilcin da wancan?

A gaskiya, gara ma Nasibawa, idan suka yi haka, da 'yan Shi'ah. Domin Abubakar ya fi Sa'adu daraja, Usman kuma ya fi nisa ga cancantar kisa a kan Husaini. Tattare da cewa, kowannensu an zalunce shi, kuma duk sun yi shahada. Amma banbancinsu shi ne, Usman yana halifa aka kashe shi, kuma ya qi yaqar waxanda suka zo kisansa, bayan sun neme shi da ya yi murabus bai yi ba. Ga shi kuma cikin magabatan musulmin farko. Shi kuma Husaini ba sarki ba ne, ba gwamna ba. Amma ya nemi sarauta abin ya faskara, kuma da ya lura abin ba zai yiwu ba ya nemi a bar shi ya koma aka qiya. Da aka nemi ya miqa kansa a je da shi wurin sarki ya qi, a kan haka aka yaqe shi har aka kashe shi.

Haqurin da Usman ya yi babu shakka ya fi girma. Don haka shahadarsa tana gaba da ta Husaini. Wannan shi ya sa fitinar da ta cimma al'umma a kan kisan Usman ta fi girma.

A taqaice dai, duk wanda 'yan Shi'ah suke yabo, to, za ka tarar a cikin waxanda Harijawa ke yabo akwai waxanda suka yi masu fintinkau wajen girman daraja. Haka kuma duk wanda 'yan Shi'ah suke zagi, to, a cikinsu akwai wanda sharrinsa ya zarce na wanda suke zagin.

Su kuwa Ahlus-Sunnah sun tsaya tsaka ne, ta hanyar jivintar dukkan musulmi, waxanda suka haxa da Sahabbai da Tabi'ai da na bayan su. A lokaci xaya kuma sun yarda da matsayi da darajar da Ahlul-Baiti suke da su. Savanin abin da su Mukhtar suka aikata.

Magabatan wannan al'umma gaba xaya sun yarda da cewa, Abubakar da Umar da Usman na da fifikon daraja a kan Ali *Raliyallahu Anhu*. Magoya bayansa ma daga cikinsu basu musun haka.

Ya tabbata daga Ali *Raliyallahu Anhu* xin kansa ta hanya mutawatira cewa, ya ce: *Mafifitan wannan al'umma bayan Manzonta su ne: Abubakar da*

*Umar.* Amma wasu daga cikin mabiyansa suna ganin cewa, Ali ya fi Usmanu. Amma dai akasarin malamai suna ganin rashin dacewar wannan ra'ayi, saboda ya ci karo da ijma'in Sahabbai. Har ma Ayyub – daga cikin malaman Tabi'ai – yana cewa: "Duk wanda ya fifita Ali a kan Usman bai raga ma Sahabbai ba".

### 2.2 Wai Imamansu Ba Su Kuskure!

Xan-sha-biyu ya ce: "Dukkan musulmi in banda Imamiyyah da Isma'iliyyah sun ce Annabawa da imaman 'yan Shi'ah suna iya yin kuskure. Sai suka ce yana yiwuwa a aiko wanda ke iya yin qarya da mantuwa da kuskure da sata. To, wace amincewa ta yi saura da mutane za su yi ga maganganunsu, ko yaya akai su yi masu xa'a? kuma yaya bin su ke zama wajibi ga jama'a alhali kuwa mai yiwuwa ne abin da suke umurni da shi kuskure ne? Kuma ba su taqaita imamai ga wani adadi ba, su dai duk wanda ya yi wa Baquraishe mubaya'a to wannan mubaya'ar ta yi daidai a wurinsu. Kuma wajibi ne duk musulmi su yi masa xa'a in dai wani abin qi bai bayyana gare shi ba, ko da ya kai matuqa ga kafirci da fasicci da munafunci a voye."

**Martani:**

Cewa mafi yawan musulmi na ganin Annabawa ba a kiyaye su daga kuskure ba, kuma wai, yana yiwuwa su yi qarya da sata, duk wannan ba haka yake ba. Duk musulmi sun haxu a kan cewa Allah ya kiyaye Annabawa daga yin kuskure ga abin da ya shafi isar da saqonsa. Ba shi yiwuwa wani kuskure ya dawwama a cikin shariah. Duk abin da suka isar da shi na umurnin Allah ko haninsa, to, wajibi ne a yi musu xa'a cikinsa. Abin da suka ba da labari kuma wajibi ne a gasgata su. Bin umurninsu da nisantar haninsu wajibi ne. Waxannan abubuwa duk qungiyoyin musulmi sun haxu a kansu, sai fa Harijawa waxanda ke halatta samun kuskure a cikin umurni ko hanin da Annabawa suka yi. To, waxannan vatattu ne. Ahlus-Sunnah sun haxu a kan haka.

Ya gabata cewa in wasu mutane daga cikin musulmi suka faxi maganar da take kuskure ce, wannan ba a xaukar sa a matsayin suka ga dukan musulmi. In da kuwa ana haka, to, da kuskuren Shi'ah 'yan-sha-biyu ya zama aibi a kan musulmi, ga shi kuwa ba a san wata qungiya da ta fi Shi'ah 'yan-sha-biyu kuskure da qarya ba, wannan ba ya cutar da musulmi da komai, haka ma idan sauran qungiyoyi idan sun yi nasu kuskure.

Mafi yawan mutane ko kuma da-yawansu ba su yarda cewa Annabawa na iya aikata kaba'ira ba. Amma mafi yawan malaman na ganin suna iya faxawa cikin wani cikin aikata wani qaramin laifi, daga baya sai a faxakar da su, su tuba, kuma sai Allah ya qara xaukaka darajarsu fiye da wadda suka kasance a kai.

A taqaice dai babu musulmin da ya ce wajibi ne ayi wa Manzo xa'a in ana tsammanin cewa abin da ya yi umurni da shi kuskure ne. Abin da dai suka haxu a kansa shi ne, yin xa'a na rataya ne ga abin da yake sawaba ne.

Malamai suna da ra’ayi biyu sanannu game da yiwuwar cewa in manzanni suka yi ijtihadi za su iya yin kuskure ko a’a. Dukan malamai sun haxu akan cewa in sun yi kuskure ga ijtihadi Allah zai gyara masu kuskuren, kuma ana yi masu xa’a ne ga abin da Allah Ta’ala ya bar su a kai, ba wanda Allah Ta’ala ya canza kuma yayi hani gare shi ba.

Amma cewa imaman Shi’ah ba su yin kuskure to, lalle babu musulmin da ya ce haka in ba ‘Yan-sha-biyu da Ismailiyyawa ba. Wane vata ne ya kai ga maganar da babu musulmin da ya aminta da ita sai masu ilhadi da munafukai?

Shin yana yiwuwa a sami waxanda suka fi vata akan masu qin Muhajiruna da Ansaru na farko sannan kuma su yi soyayya da kafirai da munafukai ga shi kuwa Allah Ta’ala ya ce:

﴿ ۞ أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ تَوَلَّوْا۟ قَوْمًا غَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيْهِم مَّا هُم مِّنكُمْ وَلَا مِنْهُمْ وَيَحْلِفُونَ عَلَى ٱلْكَذِبِ وَهُمْ
يَعْلَمُونَ ﴿١٤﴾ أَعَدَّ ٱللَّهُ لَهُمْ عَذَابًا شَدِيدًا ۖ إِنَّهُمْ سَآءَ مَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ﴿١٥﴾ ٱتَّخَذُوٓا۟ أَيْمَٰنَهُمْ جُنَّةً فَصَدُّوا۟
عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ فَلَهُمْ عَذَابٌ مُّهِينٌ ﴿١٦﴾ لَّن تُغْنِىَ عَنْهُمْ أَمْوَٰلُهُمْ وَلَآ أَوْلَٰدُهُم مِّنَ ٱللَّهِ شَيْـًٔا ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ
أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِ ۖ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ﴿١٧﴾ يَوْمَ يَبْعَثُهُمُ ٱللَّهُ جَمِيعًا فَيَحْلِفُونَ لَهُۥ كَمَا يَحْلِفُونَ لَكُمْ ۖ وَيَحْسَبُونَ أَنَّهُمْ
عَلَىٰ شَىْءٍ ۚ أَلَآ إِنَّهُمْ هُمُ ٱلْكَٰذِبُونَ ﴿١٨﴾ ٱسْتَحْوَذَ عَلَيْهِمُ ٱلشَّيْطَٰنُ فَأَنسَىٰهُمْ ذِكْرَ ٱللَّهِ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ حِزْبُ
ٱلشَّيْطَٰنِ ۚ أَلَآ إِنَّ حِزْبَ ٱلشَّيْطَٰنِ هُمُ ٱلْخَٰسِرُونَ ﴿١٩﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ يُحَآدُّونَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓ أُو۟لَٰٓئِكَ فِى ٱلْأَذَلِّينَ
﴿٢٠﴾ كَتَبَ ٱللَّهُ لَأَغْلِبَنَّ أَنَا۠ وَرُسُلِىٓ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ قَوِىٌّ عَزِيزٌ ﴿٢١﴾ لَّا تَجِدُ قَوْمًا يُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ
وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ يُوَآدُّونَ مَنْ حَآدَّ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَوْ كَانُوٓا۟ ءَابَآءَهُمْ أَوْ أَبْنَآءَهُمْ أَوْ
إِخْوَٰنَهُمْ أَوْ عَشِيرَتَهُمْ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ كَتَبَ فِى قُلُوبِهِمُ ٱلْإِيمَٰنَ وَأَيَّدَهُم بِرُوحٍ مِّنْهُ ۖ
وَيُدْخِلُهُمْ جَنَّٰتٍ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا ۚ رَضِىَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُوا۟ عَنْهُ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ
حِزْبُ ٱللَّهِ ۚ أَلَآ إِنَّ حِزْبَ ٱللَّهِ هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ ﴿٢٢﴾ ﴾ المجادلة: ١٤ - ٢٢

*Shin ba ka ga mutanen da ke jivintar waxanda da Allah ya yi fushi da su ba. Su dai ba cikinku suke ba, ba kuma cikinsu suke ba, kuma suna rantsuwar qarya cikin sani. Allah ya tanadar masu azaba mai tsanani, haqiqa abin da suke yi ya munana. Sun riqi rantsuwarsu a matsayin garkuwa, sai suka kange (mutane) daga hanyar Allah. To, suna da azaba mai qasqantarwa. Dukiyarsu ba zata wadatar da su ba, haka ma ‘ya’yansu ba za su wadatar da su da wani abu ba, waxannan sune ma’abuta wuta, kuma masu dawwama ne a cikinta. Ranar da Allah zai tada su, dukan su, sai su yi masa rantsuwa kamar yadda suke yi maku suna tsammanin cewa suna bisa wata hujja, a’a lalle su ne maqaryata. Shaixan ya samu galaba a kansu, sai ya hana su tuna Allah. Waxannan su ne qungiyar shaixan. To, a sani cewa qungiyar shaixan ita*

*ce ke yin hasara. Waxanda ke fito-na-fito da Allah da Manzonsa waxannan na cikin qasqantattu. Allah ya rubuta cewa: "Wallahi Ni da manzannina ne za mu yi galaba", haqiqa Allah mai qarfi ne, mabuwayi. Ba za ka tarar da mutanen da suka yi imani da Allah da ranar lahira suna son wanda ya sava wa Allah da Manzonsa ba, koda sun kasance iyayensu ne ko 'ya'yansu, ko 'yan'uwansu. To, waxannan an rubuta imani cikin zukatansu, kuma zai sa su aljannar da qoramu ke gudana a cikinta, suna madawwama cikinta. Allah ya yarda da su, su ma sun yarda da shi. Waxannan su ne rundunar Allah, to kuma rundunar Allah sune masu ribanta. Al-Mujadalah: 14-22.*

Waxannan ayoyin an saukar da su ne akan munafukai, qungiyar 'yan-sha-biyu kuwa ta fi duk sauran qungiyoyi yawan munafukai, har za ka tarar cewa ba wani xan Shi'ar face yana da xaya daga cikin alamomin munafunci. Kamar yadda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Abu huxu duk wanda ya sifaitu da su to, munafuki ne tsintsa, wanda yake da sifa xaya daga cikinsu kuwa, to, ya na da sifar munafunci har sai ya bar ta: 1) Idan ya yi magana sai ya yi qarya, 2) In aka amince ma sa sai ya yi yaudara, 3) In ya yi alqawari sai ya sava, 4) In kuma ya yi husuma sai ya yi fajirci. Buhari da Muslim sun riwaito shi cikin sahihansu.

Allah Ta'ala ya ce

﴿ تَرَىٰ كَثِيرًا مِّنْهُمْ يَتَوَلَّوْنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ۚ لَبِئْسَ مَا قَدَّمَتْ لَهُمْ أَنفُسُهُمْ أَن سَخِطَ ٱللَّهُ عَلَيْهِمْ وَفِى ٱلْعَذَابِ هُمْ خَـٰلِدُونَ ﴿٨٠﴾ وَلَوْ كَانُوا۟ يُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلنَّبِىِّ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيْهِ مَا ٱتَّخَذُوهُمْ أَوْلِيَآءَ وَلَـٰكِنَّ كَثِيرًا مِّنْهُمْ فَـٰسِقُونَ ﴿٨١﴾ ﴾ المائدة: ٨٠ - ٨١

*Za ka ga dayawa daga cikinsu na jivintar kafirai. Abin da zuciyarsu ta umurce su da shi ya munana, don ya kai su ga fushin Allah kuma su masu dawwama ne a cikin wuta. Da sun kasance sun yi imani da Allah da Annabi da abin da aka saukar ma sa da ba su riqe su majivinta ba. Amma dai dayawansu fasiqai ne. Al-Ma'ida: 80-81.*

Allah Ta'ala kuma ya ce:

﴿ لُعِنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِنۢ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ عَلَىٰ لِسَانِ دَاوُۥدَ وَعِيسَى ٱبْنِ مَرْيَمَ ۚ ذَٰلِكَ بِمَا عَصَوا۟ وَّكَانُوا۟ يَعْتَدُونَ ﴿٧٨﴾ كَانُوا۟ لَا يَتَنَاهَوْنَ عَن مُّنكَرٍ فَعَلُوهُ ۚ لَبِئْسَ مَا كَانُوا۟ يَفْعَلُونَ ﴿٧٩﴾ ﴾ المائدة: ٧٨ - ٧٩

*An la'anci waxannan da suka kafirta daga cikin Bani Isra'ila a bisa harshen Dawuda da Isah xan Maryam. Wannan ya kasance ne don savon da suka aikata, kuma sun kasance suna*

*wuce wuri. Sun kasance ba su hanin junansu daga munkarin da suke aikatawa. Wallahi abin da suke aikatawa ya munana. [Al-Ma'ida 78-79].*

Su 'yan Shi'ar sha biyu galibinsu ba su hani da munkarin da suke aikatawa, kai za ka tarar cewa an fi aikata munkari kamar zalunci da aikata alfasha da makamantansu a garuruwansu kuma su suna jivintar kafiran da Allah ya yi fushi da su, ba su kasance tare da musulmi ba, ba kuma tare suke da kafirai ba, kamar yadda Allah Ta'ala ya ce:

﴿ ۞ أَلَمْ تَرَ إِلَى ٱلَّذِينَ تَوَلَّوْا۟ قَوْمًا غَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيْهِم مَّا هُم مِّنكُمْ وَلَا مِنْهُمْ ﴾ المجادلة: ١٤

*Shin ba ka ga waxanda suka jivinci mutanen da Allah ya yi fushi da su ba, ba su cikinku kuma ba su cikinsu? Al-Mujadala 14.*

Saboda haka ne 'yan-sha-biyu suke jinsi na daban a wurin musulmi. Wannan ne ya sa da musulmi suka yaqe su a wani tsaunin da suka fake cikinsa a wani sashe na Sham, inda suke zubar da jinin musulmi suna qwatar dukiyarsu, suka yi masu fashi da makami, suna masu halatta haka. Suna kuma cewa aikin addini ne suke yi, sai wasu turkawa suka yaqe su, sai 'yan Shi'ah suka rinqa cewa su musulmi ne, turkawan na cewa ku dai wani jinsi ne daban da musulmi. Don banbantarsu daga musulmi.

Ga shi kuma Allah ya ce *(Suna rantsuwa akan qarya suna kuma sane da hakan)[Al-mujadala 14]* wannan ita ce halayyar 'yan-sha-biyu. Haka ma inda Allah Ta'ala ya ce:

﴿ ٱتَّخَذُوٓا۟ أَيْمَٰنَهُمْ جُنَّةً فَصَدُّوا۟ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ فَلَهُمْ عَذَابٌ مُّهِينٌ ﴿١٦﴾ ﴾ المجادلة: ١٦

*Sun riqi rantsuwarsu abin kariya, sai suka kange mutane daga tafarkin Allah.* Har zuwa inda yake cewa: *(Ba za ka tarar da mutane masu imani da Allah da ranar alqiyama suna son wanda ya sava wa Allah da Manzonsa ba). Al-mujadala: 22.*

Da yawansu na son kafirai har cikin zukatansu fiye da son musulmi, don haka lokacin da wasu kafirran turkawa suka fita daga gabas suna yaqar musulmai da zubar da jininsu a qasar Khurasana da Iraqi a Sham da Jazira da sauran garuruwan musulmi, Shi'ah 'yan-sha-biyu sune masu taimaka masu wurin yaqar musulmi. Wazirin Bagadaza da aka fi sani da Ibnul Alqami shi da makamantansa sun fi kowa taimaka wa kafirran turkawan a kan musulmi. Haka ma Shi'ah 'yan-sha-biyu na Halab a qasar Sham da sauran 'yan Shi'ah, sun fi kowa taimaka wa kafirran wurin yaqar musulmi. Haka ma kafirran da musulmi suka yaka a qasar Sham 'yan-sha-biyu sun fi kowa taimaka masu, haka ma in Yahudawa sun sami daula a Iraqi da waninsa to, 'yan Shi'ah ne za su taimaka ma su, su kowane lokaci suna jivintar kafirrai suna kuma taimakon su wurin yaqar musulmi.

Sannan wannan xin da ya raya cewa Imamai ba su kuskure bai kafa hujja ba a kan haka sai abin da ya gabata na cewa Allah ba zai bar duniya ba,

ba tare da Imamai ma'asumai ba don abin da ke cikin haka na maslaha da luxufi sanannen abu ne. Cewa wannan Imamin na qarshe wanda ke fake kuma ana jiran sa babu maslahar da ya haifar ko luxufi. In ya kasance matacce kamar yadda mafi yawan musulmi ke gani ko in yana raye kamar yadda Shi'ah 'yan-sha-biyu ke cewa, haka ma kakanninsa ba wata maslahar da aka samar daga gare su ko luxufi, kamar yadda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kasance a Madina bayan hijira. Ya kasance shugaban muminai wanda ya wajaba a yi masa xa'a, kuma wannan ya zama sanadin tsirarsu, kuma bayansa ba a samu wani cikin imaman naku da ya riqa ragamar mulki ba sai Ali *Raliyallahu Anhu* a lokacin halifancinsa.

Abin da duk musulmi suka sani ne cewa maslaha da luxufin da muminai suka samu lokacin halifofi uku na farko sun fi waxanda aka samu lokacin Ali, kasancewar lokacinsa lokaci ne na tashin hankali da fitina da rarrabuwar kan musulmi. To, idan babu wanda aka samu daga cikin waxanda Shi'ah 'yan-sha-biyu ke cewa imamai ne ma'asumai sai Ali *Raliyallahu Anhu* kuma shi kaxai ne ya yi shugabanci bayan masu qarfi a cikin musulmi sun yi masa mubaya'a ga shi kuma maslahar addini da ta duniya da mumina suka samu bata kai wadda suka samu lokacin halifofi ukun na farko ba, mun sani a yanke cewa maslaha da luxufin da suka raya cewa ana samu don imaman da basu kuskure ya zama qarya, ba makawa.

Wannan irin shiriyar da ake rayawa ce ga wasu mutanen da ke fake a tsaunukan lebanon da sauran tsaunukan kamar na Qasiyun ta Damaskas, da *Magaratud Dami* da tsaunin *Al-Fatah* a Masar, da tsaunuka da koguna makamantan su. Waxannan wurare ne na zaman aljannu, kuma akwai shaixanai a cikinsu, suna bayyana wasu lokuta ga wasu mutane, suna voyuwa daga mutane mafi yawan lokuta, sai jahilai su yi tsammanin cewa mutane ne, alhalin aljannu ne. kamar yadda Allah Ta'ala ya ce

﴿وَأَنَّهُۥ كَانَ رِجَالٌ مِّنَ ٱلْإِنسِ يَعُوذُونَ بِرِجَالٍ مِّنَ ٱلْجِنِّ فَزَادُوهُمْ رَهَقًا ۝٦﴾ الجن: ٦

*Kuma haqiqa wasu mazajen mutane sun kasance suna neman tsari daga wasu mazajen aljannu. Sai wannan ya qara ma su (aljanun) girman kai. Al-Jin: 6.*

Waxannan 'yan Shi'ah sun yi imani da su kuma sun yi imani da vatattun shehunan qungiyoyi bin waxannan aljannun, amma sharrin Shi'ah 'yan-sha-biyu ya xara sharrin shehunan da ke raya cewa akwai mazan da ke voye, lalle sharrin da ke faruwa daga yan Shi'ah 'yan-sha-biyu ya fi tsanani, don suna kira ne zuwa ga wani shugaban da ba ya yin kuskure a cewarsu, ba su da shugabanni masu qarfi waxanda ke iya taimakon su sai dai kafiri ko fasiqi ko munafuki ko jahili, shugabanninsu ba sa fita daga cikin waxannan da aka ambata.

Qungiyar Shi'ah *Isma'iliyyah* ta fi *Imamiyyah* sharri. Su xin ma kira suke zuwa ga wani imamin da ba ya kuskure, kai dai su kira suke zuwa ga

sarki mai yawan kafirci da zalunci, wannan abu ne sananne ga duk wanda ya san halin da suke a kai.

Ga shi kuwa lalle Allah Ta'ala ya ce

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَ وَأُوْلِي ٱلۡأَمۡرِ مِنكُمۡۖ فَإِن تَنَٰزَعۡتُمۡ فِي شَيۡءٖ فَرُدُّوهُ إِلَى ٱللَّهِ وَٱلرَّسُولِ إِن كُنتُمۡ تُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِۚ ذَٰلِكَ خَيۡرٞ وَأَحۡسَنُ تَأۡوِيلًا ٥٩ ﴾ النساء: ٥٩

*Ya ku waxanda suka ba da yaskiya ku yi xa'a ga Allah da manzonsa da shugabanninku. To, in kun yi savani cikin wani abu, to ku maida shi zuwa ga Allah da Manzonsa wannan ne ya fi zama alheri, kuma shi ya fi kyakkyawan qarshe. An-Nisa'i 59.*

Sai Allah Ta'ala ya yi umurnin cewa a mayar da abin da aka yi savani cikin sa zuwa ga Allah da Manzonsa. Ka ga da akwai wani wanda ba ya kuskure wanda Allah Ta'ala ya yarda da shi bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da ya yi umurnin cewa a mai da lamari zuwa wurinsa. Ta haka ne Alqur'ani ya yi nuni da cewa babu wani wanda ba ya yin kuskure face Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.*

## 2.3 Adadin Imamai

Amma cewar da xan Shi'ar ya yi ba a qayyade yawan imamai ba. Wannan gaskiya ne, don abin da Allah ya ce shi ne:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَ وَأُوْلِي ٱلۡأَمۡرِ مِنكُمۡۖ فَإِن تَنَٰزَعۡتُمۡ فِي شَيۡءٖ فَرُدُّوهُ إِلَى ٱللَّهِ وَٱلرَّسُولِ إِن كُنتُمۡ تُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِۚ ذَٰلِكَ خَيۡرٞ وَأَحۡسَنُ تَأۡوِيلًا ٥٩ ﴾ النساء: ٥٩

*Ya ku waxanda suka ba da gaskiya! ku yi ma Allah xa'a ku kuma yi ma Manzo da shugabaninku. An-Nisa: 59.*

Allah Bai qayyade adadinsu da wani yawa na musamman ba.

Haka Annabi ya faxa a cikin hadissai masu yawa waxanda aka riwaito, bai qayyade yawansu ba. Ya zo cikin Buhari da Muslim ta hanyar Abu Zarri *Raliyallahu Anhu* cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: *Haqiqa babban masoyina ya yi mani wasicci da in ji magana in kuma yi xa'a ko da (shugaban) ya kasance bawa ne daga Habasha mai yankakkun gavvai.*

## 2.4 Wace Mubaya'a ce Ingantatta?

Amma cewar da ya yi game da waxanda ba Imamiyyah da Isma'iliyyah ba wai, duk wanda ya yi wa Baquraishe mubaya'a to, shugabancinsa ya qullu, kuma yi masa xa'a ya zama wajibi akan dukan mutane idan halinsa voyayye ne koda kuwa ya fi kowa fasicci da kafirci da munafunci. To wannan koda ya ke wasu malaman tauhidi sun faxe shi, to ba shi ne mazhabar Ahlus-Sunnah ba. Umar xan Haxxabi dai ya ce: *Duk wanda ya yi wa wani mutum mubaya'a ba*

*tare da shawartar musulmi ba to, kada a yi masa mubaya'a shi da wanda ya yi masa mubaya'a….}* Buhari ya riwaito shi.

Ahlus-Sunnah kuma ba su wajabtar da xa'ar shugaba ga duk abin da ya yi umurni da shi, sai dai ga abin da shariah ta yarda da shi. Ba su yarda a yi masa xa'a ga savon Allah Ta'ala koda ya kasance shugaba adili, in ya umurce su da xa'ar Allah sai su yi masa xa'a, kamar ya umurce su da tsai da sallah da ba da zakka da faxan gaskiya da adalci, da aikin hajji da jihadi soboda Allah, su dai ga haqiqanin lamarin Allah ne suka yi wa xa'a. Ba haramun ba ne in sun yi wa Allah Ta'ala xa'a wajabcin xa'a ga Allah ba ya faxuwa don kawai fasiqi ya yi umurni da xa'ar, kumar in fasiqi ya faxi gaskiya ba ya wajaba a qaryata shi, kuma wajabcin bin gaskiya ba ya faxuwa don kawai fasiqi ne ya faxe ta. Ahlus-Sunnah kuma ba su yi wa shugabanni xa'ar da ba ta da qaidi, suna dai yi masu xa'a ne qarqashin xa'ar Allah Ta'ala.

Kamar yadda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce *Xa'a dai tana kasancewa ne ga abin da shariah ta yarda da shi.* Kuma ya ce: *Ba a yi wa kowa xa'a in ya yi umurni da savon* Allah Ta'ala. Ya kuma ce: *Ba ayi wa mutum xa'a cikin abin da ya kasance savon mahalicci ne.* Ya kuma ce: *Wanda duk ya umurce ku da savon Allah to, kada ku yi masa xa'a.*

Maganar Shi'ah 'yan-sha-biyu masu raya biyar Ali *Raliyallahu Anhu* cewa wajibi ne ayi wa wani ba Manzon Allah ba *Sallallahu Alaihi Wasallama* xa'a ga duk abin da ya yi umurni da shi, ya fi muni da Shi'ar aka dangantawa ga Usmanu *Raliyallahu Anhu* mutanen Sham masu cewa wajibi ne ayi wa shugaba xa'a ga komai don dai su suna xa'a ne ga mai mulkin da ke raye amman 'yan-sha-biyu wanda suke yi wa xa'a ya vace, kuma babu shi.

Sannan kuma waxancan bu su ce shugabanninsu ba su yin kuskure ba kamar yadda 'yan Shi'ah suka ce. Su kam cewa suke yi, Allah zai karvi ayyukansu na gari kuma ya gafarta masu kurakuransu. Wannan ko ya fi sauqi a kan wanda ke cewa shugabanninsa ba su yin kuskure faufau.

Daga nan ya bayyana cewa waxannan da ake dangantawa ga qin Ali *Raliyallahu Anhu* Shi'ar Usmanu koda yake sun fita daga wani sashen adalci da kuma gaskiya sai dai fitar da Shi'ah 'yan-sha-biyu suka yi daga gaskiya da da adaki ta fi tsanani da muni. To yaya ma za'a kamanta 'yan Shi'ah da Ahlus-Sunnah waxanda ke bin Alqur'ani da Sunnah, suna yi ma shugaba xa'a ga abin da yake umurni da shi na xa'ar Allah, su bar abin da duk suka yi umurni da shi in ya kasance savon Allah?.

### 2.5 Mazhaba da Qiyasi

Xan Shi'ar bayan haka kuma sai ya tuhumci Ahlus-Sunnah da cewa wai, sun rungumi qiyasi, sun sanya fahimtar malamansu a cikin addini. Da haka, inji shi wai, sai suka shigar da bidi'oi a cikin addini, kuma wai, a sandiyyar haka aka samu mazhabobi guda huxu waxanda babu su a zamanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ko zamanin Sahabbai. Ya ce kuma

wai, Sahabbai sun ja kunnen al'umma a kan yin hattara da qiyasi don hanyar shexan ce, amma sai malaman Sunnah suka yi biris, inji shi.

**Martani:**

Ba gaskiya ba ne cewa gaba xayan Ahlus-Sunnah sun yarda da qiyasi. Domin kuwa wasu malaman bagadaza da 'yan Zahiriyyah irin su Dawuda da Ibnu Hazam da wasu sufaye daga cikin Ahlus-Sunnah duk ba su yarda da qiyasi ba. Kamar dai yadda su ma 'yan shi'ah bakinsu bai haxu a kan sa ba. Kuma hasali ma, riqo da qiyasi ai ya fi fatawowin Askari. Domin malaman da suka yarda da qiyasi irin su Malik da Laisu da Auza'i sun fi su ilimi da sanin makamar addini, balle daxa Malam-na-Voye da ko ganinsa ba a yi ba.

Kuma Ahlus-Sunnah, mabiyan waxannan mazhabobi guda huxu suna kan tudu ne, a yayin da masu dakon MAlam-na-Voye suke kware. A qashin gaskiya babu wata ingantattar magana da za ta fiton bakin 'yan-sha-biyu face akwai wadda ta yi daidai da ita ko wadda ta fi ta a wurin Ahlus-Sunnah. Banbancin kuwa da ke tsakanin Sunnah da bidi'ah kamar wanda ke tsakanin imani da kafirci ne. Ga shi kuma Allah Ta'ala na cewa: *Ba za su zo ma ka da wani misali ba face mun zo ma ka da gaskiya da bayani mafi kyau. Al-Furqan:33.*

Babu kuma waxanda suka cika addinin Allah da qarya da varnace-varnace kamar 'yan Shi'ah. Ta hanyar yi wa ayoyin Allah fassarar son zuciya. Nan gaba za mu kawo samfurin wannan fassara tasu tare da mayar da martani akai in Allah ya so.

Dangane kuma da cewar da ya yi, wai, Ahlus-Sunnah sun yi biris da kiraye-kirayen Sahabbai. Abin da ban mamaki. Yaushe ne 'yan Shi'ah suka fara ganin Sahabbai da gashi a ka balle har su nuna damuwa wai an yi biris da maganarsu? Ashe ba su ne suke qaryata Sahabbai ba, suna ce ma su azzalumai?! To, Sahabbai dai ba su yi wannan kiran ba. Da kuwa sun yi shi to, da babu shakka Ahlus-Sunnah ne farkon waxanda za su saurare su daga cikin qungiyoyin musulmi, don su ne suka yarda da musuluncinsu da adalcinsu da shugabancinsu.

Abin da kuma ya faru a tarihin musulunci na samuwar mazhabobi, Allah ne ya hukunta shi. Ba haxin bakin malamai ne ba. Ba ma zama xaya ko wuri xaya aka yi su ba. Kuma tattare da hakan babu wani xaya daga cikin shugabannin mazhabobin da ya tava umurnin wani ya yi ma sa xa'a ya bar abin da littafin Allah da Sunnar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* suka qunsa. Kuma duk da samuwar waxannan mazhabobi, malaman Sunnah ba su yi kwance da sirdi ba. Kullum tsaye su ke kamar haure ga qara wa juna sani da yi wa kai hisabi dangane da hukunce-hukuncen da mazhabobin suka qunsa.

Idan kuma xan Shi'ar na son ya ce ne, Sahabbai sun bar ma al'umma gadon fatawoyi da tarin ilimi, waxanda da malamai sun yi riqo da su babu buqatar su samar da mazhabobi, amma suka yi biris da su, to, wannan ba gaskiya ba ne. Littafan malaman waxannan mazhabobi shaqe su ke da fatawoyi da fahimtar Sahabbai. Kuma ba lalle ne a kira mazhabobin da sunan Sahabbai

ba. Banbance-banbancen da ake samu tsakanin mazhabobin na fatawoyi ma duk ya samo asali ne daga Sahabban.

Sannan yana da kyau a sani cewa, babu wani malami daga cikin Ahlus-Sunnah da ke jin cewa duk abin da shugabannin mazhabobin suka haxu a kansa hujja ne koda ya ci karo da wani ingantaccen nassi. A'a, aqidarsu ita ce, da zarar maganarsu ko ta xayansu ta sava wa nassi to, nassi shi ne abin biya. Haka kuma duk lokacin da aka samu wani savani to, komawa ga littafin Allah da Sunnar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne mafita.

Haka kuma cewar da xan Shi'ar ya yi wai, Sahabbai sun yi kashedi ga musulmi daga bin qiyasi magana ce maras asali. Domin kuwa ta tabbata cewa, su kansu Sahabbai sun yi amfani da iliminsu da gogewarsu ta rayuwar musulunci suka yi qiyasin wasu hukunce-hukunce. Qiyasin da dai suka yi allawaddai da shi, shi ne irin na waxanda suka qiyasta halal a kan haram kamar waxanda suka kamanta Riba da halaltaccen ciniki da qiyasta mushe a kan yankakkiyar dabba. Ko irin qiyasin Shexan. To, in har ka ga wani nassi na Sahabbai mai nuna hattara da qiyasi, ka ji irin wanda suke nufi.

### 2.6 Wai 'Yan Shi'ah ne Kawai za su Shiga Aljanna!

Xan Shi'ar ya ce: Dalili na biyu mai nuna wajabcin bin mazhabar Imamiyyah, shi ne: Abin da shehunmu jagora mafi girma, Khawwajah, mai taimakon addini da gaskiya, muhammadu xan Al-Hassan ax-Xusi Allah ya tsarkake ruhinsa ya ce, bayan na tambaye shi game da mazhabobi sai ya ce: Mun yi bincike game da su kuma da cewar Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama:* "Al'ummata za ta rarrabu zuwa qungiyoyi saba'in da uku, daga cikinsu akwai qungiya guda mai tsira sauran kuma suna wata". ga shi kuma ya bayyana a cikin wani hadisi ingantacce qungiyar da ke tsira da kuma qungiyoyin da za su halaka shi ne cewarsa: Iyalaina kamar jirgin Annabi Nuhu *Alaihis Salamu* ne, wanda ya shige shi zai tsira, wanda bai shiga ba kuma ya halaka. Sai muka tarar da cewa qungiyar da za ta tsira ita ce ta Imamiyyah, don sun sava wa dukan mazhabobi, dukan mazhabobi kuma sun haxu a cikin asullan aqidojinsu.

**Martani:**

Da farko shi wannan xan Shi'ar ai ya kafirta wannan malamin nasa da yake fankamawa bai sani ba. Don malamin nasa na cikin masu cewa, duniya ba ta da farko. Shi kuma ya kafirta duk wanda ya ce haka a cikin littafinnan nasa da muke tattaunawa da shi.

Wannan malamin nasa kuma yana da kyau a sani shi ne wannan da ya yi qaurin suna wajen taimakon arna 'yan Shi'ah Baxiniyah Al-Isma'iliyyah a Alamauta. Sannan lokacin da Turkawa mushrikai su ka zo qasar musulmi, har suka iso bagadaza cibiyar halifanci, wannan mutum ne ya kasance malamin duban da ya ba mushrikai su Hulaku sa'a don su kashe halifan musulmi, da malamai da masu riqo da addini. Kuma ya ce kada a kashe masu sana'o'in

hannu da 'yan kasuwan da xan Shi'ar ke samun amfani na duniya daga wurinsu. Kuma ya yi rubda ciki da dukiyoyin waqafi na musulmi, yana bayarwa daga cikinta ga mushrikai, malamai da shehunnansa na qungiyar Bakhshiyyah masu siddabaru da makamantansu. Sannan kuma lokacin da ya yi wani gini a wurin da ake kira Maragah ya gina shi kamar ginin mabiyan addinin Sabi'awa mushrikai, ya fi quntata wa mutanen da addininsu ya fi kusa da addinin Allah, waxanda suka fi rabo wurinsa kuwa sune waxanda suka fi nisa daga addinin Allah kamar su Sabi'awa da masu kore sifofin Allah Ta'ala da sauran mushrikai, kodayake sana'arsu ta kasance duban taurari da tsibbu da makamantan wannan.

Abu ne da yake sananne game da wannan da ya kira shehinsa – shi da mabiyansa, shi ne suna wulaqanta abubuwan da musulunci ya farlanta, suna qin barin abin da musulunci ya yi hani da shi, kuma ba su kiyaye salloli, ba su barin aikata savo kamar Zina da shan giya da miyagun abubuwa kamar waxannan, har ya kai ga cewa an san abin da suka aikatawa na munkari cikin watan azumi na dangin ashsha da shan giya, wannan malamin nasa bai kasance yana da wani tasiri ba sai tare da 'yan'uwansa mushrikai waxanda addininsu ya fi na Yahudawa da Narasa zama qumsa cuta.

Don hakan ne duk lokacin da musulunci ya qarfafa cikin turkawan Mugul, sai lamarin waxannan 'yan Shi'ar ya yi rauni don tsananin qiyayyar da suke yi wa musulunci da musulmi. Don haka Sarki Nuruz mujahidi kuma Shahid ya nisantar da su. Shi ne kuma wanda ya kira Sarkin Mugul Gazan zuwa ga musulunci, ya yi masa alqawarin zai taimake shi in ya musulunta. Shi ne kuma ya kashe mushrikan da ba su musulunta ba cikin Bakhshiyyah mushrikai masu sihiri, ya rusa wuraren bautar gumakansu, ya karya gumakan, ya kuma halaka masu kula da su, sannan ya lizimta ma Yahudawa da Nasara biyan jiziya soboda bayyanar musulunci a cikin turkawa Magul da mabiyansu.

A taqaice dai lamarin Tusi da mabiyansa mashahuri ne wurin musulmi, kuma ya fi qarfin a sifanta shi. Duk da haka an ce a qarshen rayuwarsa ya kasance yana tsare salloli biyar, kuma yana yawan karanta tafsirin Al-bagawi da fiqihu da makamantan haka. In dai har ya tuba ne daga ilhadi, to, Allah na karvar tuban bayinsa kuma yana gafarta zunubai. Allah Ta'ala na cewa:

﴿ ۞ قُلْ يَٰعِبَادِىَ ٱلَّذِينَ أَسْرَفُوا۟ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمْ لَا تَقْنَطُوا۟ مِن رَّحْمَةِ ٱللَّهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَغْفِرُ ٱلذُّنُوبَ جَمِيعًا ۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ﴿٥٣﴾ ﴾ الزمر: ٥٣

*Ka gaya wa bayina waxanda suka wuce wuri cikin zaluntar kawunansu cewa, kada su yanke qauna daga rahamar Allah. Haqiqa Allah na gafarta dukan zunubbai. Haqiqa shi, mai gafar ne, mai jinqai. Az-Zumar: 53.*

Amma dai abin da xan Shia'ar ya riwaito daga shi Tusi in ya kasance kafin tuba ne, to, ba a karvar maganarsa. In kuma bayan tuba ne, to, bai tuba daga bin mazhabar Shi'ah 'yan-sha-biyu ba kenan. Ya dai tuba ne daga ilhadi kawai. To, bisa qaddarawa ta biyun ma ba za a karvi maganarsa ba. Abin da

ya fi bayyana shi ne cewa xan Shi'ar nan ya kasance yana huxuwa da shi da makamatan sa lokacin da yake yi ma mushrikan Al-magul duba, a wannan lokacin an san ilhadi ne halinsa.

To, wanda ya kasance yana sukar mutane kamar Abubakar da Umar da Usmanu da Muhajirai da Ansarai na farko, kuma yake sukar irin su Maliki da Shafi'i da Abu Hanifa da Ahmad xan Hambali da mabiyansu, yana aibata su saboda kurakuran da ba nasu ba kamar cewa wasu na ganin halaccin wani nau'i na dara, ko waqe. Wanda yake haka, ya zai kafa hujja maganar irin waxansu da ba su ko yi imani da Allah da ranar qarshe ba, balle su haramta abin da Allah ya haramta da wanda Manzo ya haramta, kuma ba su bin addinin gaskiya. Waxanda kuma suke halatta haramtattun abubuwan da duk musulmi sun haxu a kan haramcinsu, kamar zina da shan giya da rana a cikin watan azumi. Waxanda suka tozarta sallah, suke bin son rayukansu, suka keta hurumin shariah, suka wofinta abubuwan da addini ya haramta, suka bi hanyar kafirai.

Wannan dai shi ne halin da Shi'ah 'yan-sha-biyu suke a kai. Kodayaushe suna qiyayya da waliyyan Allah salihai magabata na farko daga cikin Muhajiruna da Ansaru, da waxanda suka yi masu kyakyawan bi, suna jivintar kafirai da munafukai.

Abin mamaki shi ne wannan makirarren xan Shi'ar maqaryaci da yake ambaton Abubakar da Umar da Usmanu da sauran magabatan farko da Tabi'una da kuma sauran shugabannin musulmi da malamai da masu riqo da addini, yake ambaton su da munanan siffofi na qarya ba su ji ba, ba su gani ba, sannan ya zo wurin wanda ya shahara wurin musulmi da kasancewa mai sava wa Allah da Manzonsa, yana cewa wai: "Malaminmu mafi xaukaka" har da cewa: "Allah ya tsarkake ruhinsa". Tare da cewa shi kansa ya sheda da kafircinsa da masu kama da shi, tare da la'anar da ya ke yi ma mafifitan muminai na farko da na qarshe.

Waxannan 'yan Shi'ar na shiga cikin ma'anar cewar da Allah Ta'ala ya yi:

﴿ أَلَمْ تَرَ إِلَى الَّذِينَ أُوتُوا نَصِيبًا مِّنَ الْكِتَابِ يُؤْمِنُونَ بِالْجِبْتِ وَالطَّاغُوتِ وَيَقُولُونَ لِلَّذِينَ كَفَرُوا هَٰؤُلَاءِ أَهْدَىٰ مِنَ الَّذِينَ آمَنُوا سَبِيلًا ﴿٥١﴾ أُولَٰئِكَ الَّذِينَ لَعَنَهُمُ اللَّهُ وَمَن يَلْعَنِ اللَّهُ فَلَن تَجِدَ لَهُ نَصِيرًا ﴿٥٢﴾ ﴾ النساء: ٥١ - ٥٢

*Shin ba ka ga waxannan da aka ba su wani rabo na (ilmin) littafi ba, amma suna gasgata gunki da Xagutu, kuma suna ce ma waxanda suka kafirta: "Waxancan (mushrikai) sun fi muminai kasancewa bisa hanyar shiriya. Waxannan su ne Allah ya la'anta. Wanda duk Allah ya la'anta kuwa ba za ka sami mai taimakon sa ba. An-Nisa: 51-52.*

Su ma 'yan-sha-biyu an ba su wani sashe na littafe, don sun yarda da wani sashe na littafin da Allah ya saukar, kuma suna da wani yanki na imani da sihiri da Xagutu wanda shi ne duk abin da ake bauta ba Allah ba. Saboda suna imani da falsafa da ta qunshi wannan, suna ganin cewa addu'a da ibada ana yi wa matattu, suna yin masallatai akan qaburbura, suna xaukar cewa, tafiya zuwa wurinsu kamar hajji ne.

Wannan hadisi da xan-sha-biyun ke godogo da shi, fassararsa ta zo ta fuskoki biyu: Fuska ta farko, an tambayi Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* game da qungiyar da zata tsira, sai ya ce "wanda suke akan irin abin da nake yau a kansa; ni da Sahabbaina". A wata riwayar ya ce: "Su ne jama'a". Dukan waxannan maganganu biyu sun ci karo da ra'ayin 'yan-sha-biyu, kuma suna nuna cewa, ba su ne qungiyar da za ta tsira ba, don sun fita daga cikin jama'ar musulmi, suna kafirta shugabannin musulunci suna kiransu Fasiqai, irin su Abubakar da Umar da Usmanu. Ba zancen su Mu'aawiyah da sauran Bani Umayyah ake yi ba. Suna kuma kafirtar da malaman Sunnah da masu ibada daga cikinsu kamar su Maliki da Sauri da Auza'i da Laisu xan Sa'adu da Abu Hanifa da Shafi'i da Ahmad xan Hanbali da Ishaqa, da Abu Ubaidi da Ibrahimu xan Adhama da Fudailu xan Iyal da Abu Sulaimanad-Darani da Ma'aruf Al-Karkhi da makamantansu.

'Yan-sha-biyu kuma sun fi kowa jahiltar tarihin Sahabbai balle koyi da su, sawa'un lokacin rayuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ko bayansa. Ga su kuma da qin hadisi da malamansa. To, in har siffar qungiyar da za ta tsira ita ce bin abin da Sahabbai suke a kai lokacin Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* to, wannan taken Ahlus-Sunnati wal jama'a ne. Su ne qungiyar da za ta tsira. Don Sunnah ita ce abin da Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kasance a kansa shi da Sahabbansa, da abin da ya umurce su da shi, ko ya tabbatar da su a kanshi, ko ya aikata shi da kansa. Jama'a kuma su ne waxanda suka haxu, ba su rarrabe addininsu ba zuwa qungiyoyi. To, waxanda suka rarraba addininsu suka koma qungiyoyi ba su cikin Jama'a, Allah ya barrantad da Annabinsa dagare su. Wannan ya sa aka san cewa, Ahlus-Sunnati wal Jama'ah ne ke da wannan siffar ta masu tsira, ba siffar 'yan-sha-biyu ba ce.

Suna iya cewa, tunda hadisin ya ce: "Abin da nake a kansa ni da Sahabbaina a yau" to, duk wanda ya fita daga wannan hanyar ba ya a kan hanyar qungiyar da za ta tsira. Kuma Sahabbai sun yi ridda bayansa, don haka ba su cikin qungiyar da ke tsira.

Sai a ce masu, haka yake. Mutanen da suka fi kowa shahara a ridda su ne masu jayayya da Abubakar da mabiyansa kamar Musailamu sarkin qarya da mabiyansa da ire-irensu. To, 'yan-sha-biyu na son su, suna kariyarsu, suna ganin laifi Abubakar ya yaqe su wai, ba a kan gaskiya ba. Sannan waxanda suka fi kowa ridda bayansu su ne waxanda Ali *Raliyallahu Anhu* ya qona su a lokacin da suke cewa shi Allah ne abin bauta. Su ne sabi'awa mabiyan Abdullahi xan Saba'i waxanda suka fara bayyana zagin Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma*.

Haka kuma farkon wanda ya fara da'awar annabta a cikin musulunci shi ne Mukhtar xan Baban Ubaidu, xan Shi'ah ne. Daga nan ake sanin cewa waxanda suka fi kowa ridda suna cikin 'yan Shi'ah. Don haka ba a san wata ridda da ta wuce wuri kamar ta qungiyar 'yar Shi'ah *Nusairiyyah*, da ta 'yan Shi'ah Isma'iliyya Baxiniyyah da makamantansu ba. Wanda ya fi kowa shahara wurin yaqar waxanda suka yi ridda dai shi ne Abubakar *Raliyallahu Anhu.* Kuma masu ridda daxai sun fi yawa cikin qungiyoyin da ke husuma da Abubakar. Ka ga dai ridda na nan biye da 'yan-sha-biyu kenan.

Wannan bayyane yake ga duk wanda ya bar musulunci da musulmi. Ba mai shakkar cewa jinsin masu ridda sun fi yawa cikin waxanda ke da dangantaka da 'yan Shi'ah kuma riddarsu tafi kowace muni da tsanani a kafirci.

Sai cewarsa wai: 'Yan Shi'ah sun banbanta da kowace mazhaba, sannan duk sauran mazhabobi sun haxu a kan wasu asulla na aqida. Idan yana nufin cewa 'yan Shi'ah sun savawa duk mazhabobi ga abin da suka kevanta da shi, wannan haka yake, ba ga 'yan Shi'ah kaxai ba, ga duk sauran qungiyoyi. Ba ka ganin Harijawa sun banbanta da kowa ga abin da suka kevanta da shi kamar kafirta mai savo, da kafirta Ali *Raliyallahu Anhu*, da cewa ba a yi wa Manzo xa'a ga abin da Manzo bai ce Allah Ta'ala ne ya yi umurni da shi ba, da cewa yana yiwuwa Manzon Allah ya yi zalunci wurin rabon abubuwa da kuma cikin hukuncinsa, da kuma qin bin hadisi mutawatiri in ya sava wa zahirin Alqur'ani, kamar cewa hannu varawo ana yanke shi ne daga kafaxa.. da dai ire-iren waxannan.

Amma in sun ce su 'yan Shi'ah sun kevantu da dukan maganganansu, to, ba haka ba ne, don aqidunsu xaya ce da ta Mu'utazilawa. Kuma manyan 'yan Shi'ah na farko masu sifaita Allah da jiki ne. Sannan sun yi muwafaqa da Mu'utazilawa a sha'anin yarda da qaddara. Manyansu na farko sun kasance suna tabbatar da qudura ga bawa, kuma na farkonsu masu tsananin inkari ne ga qudurar Allah fiye da inkarin da suke yi ma siffofin Allah, da cewar da suke yi masu zumubi ba su fita daga wuta.

A taqaice dai 'yan Shi'ah na da maganganun da suka kevanta da su, kuma akwai waxanda suke tare da wasu a cikinsu, kamar yadda Mu'utazilawa da Harijawa da makamantansu su ke.

Amma Ahlul-hadith kuma Ahlus-Sunnah wal Jama'a sun kevantu da bin Alqur'ani da Sunnar da ta tabbata daga Manzonsu *Sallallahu Alaihi Wasallama* ga asuli da reshe, da kuma abin da Sahabban Manzo suka kasance a kansa. Wannan Savanin Mu'utazilawa da Harijawa da Shi'ah 'yan-sha-biyu da waxanda suka yi muwafaqa da su a cikin wasu maganganunsu. Basu bin hadissan da amintattun malamai suka riwaito daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* waxanda malaman hadisi sun san ingancin su.

Kuma ai sava wa mazhabobin da suka yi ya fi nuna vacin maganganunsu fiye da nuna cewa maganganun qwarai ne. Kasancewar kuwa maganganun qungiya sun banbanta da na sauran qungiyoyi ba shi ke nuna

cewa maganganun daidai suke ba, kamar yadda haxuwarsu ga wata magana ba shi ke nuna cewa kuskure ce ba.

To in an ce: Annabi ya ce al'ummarsa za ta rarrabu zuwa kashi saba'in da uku, kuma xaya ce kawai ke tsira. Saboda haka dole ne xayar ta banbanta da saba'in da biyun da suka rage. Sai mu ce haka ne. Haka ma hadisin ke nuna cewa saba'in da biyun na banbanta da junansu kamar yadda suka banbanta da xayar mai tsira. Hadisin bai nuna cewa sauran qungiyoyin za su haxu a kan asullan aqidodi ba. Kai zahirin hadissin na nuna cewa saba'in da ukun dukansu sun banbanta da juna. A nan za a san cewa, gefen banbanci shi ne abin zargi ba gefen da suka haxu a kansa ba, don Allah Ta'ala ya yi umurni da jama'a da kuma jituwa tsakanin musulmi, ya kuma zargi rarrabuwa da savani. Allah Ta'ala ya ce:

﴿ وَٱعۡتَصِمُواْ بِحَبۡلِ ٱللَّهِ جَمِيعٗا وَلَا تَفَرَّقُواْۚ ﴾ آل عمران: ١٠٣

*Ku yi riqo da igiyar Allah gaba xaya, kuma kada ku rarraba. Ali-Imran: 103.*

Ya kuma ce:

﴿ وَلَا تَكُونُواْ كَٱلَّذِينَ تَفَرَّقُواْ وَٱخۡتَلَفُواْ مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلۡبَيِّنَٰتُۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ ١٠٥ يَوۡمَ تَبۡيَضُّ وُجُوهٞ وَتَسۡوَدُّ وُجُوهٞۚ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ٱسۡوَدَّتۡ وُجُوهُهُمۡ أَكَفَرۡتُم بَعۡدَ إِيمَٰنِكُمۡ فَذُوقُواْ ٱلۡعَذَابَ بِمَا كُنتُمۡ تَكۡفُرُونَ ١٠٦ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ ٱبۡيَضَّتۡ وُجُوهُهُمۡ فَفِي رَحۡمَةِ ٱللَّهِۖ هُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ١٠٧ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱللَّهِ نَتۡلُوهَا عَلَيۡكَ بِٱلۡحَقِّۗ وَمَا ٱللَّهُ يُرِيدُ ظُلۡمٗا لِّلۡعَٰلَمِينَ ١٠٨ ﴾ آل عمران: ١٠٥ - ١٠٨

*Kada ku kasance kamar waxanda suka rarrabu suka yi savani bayan bayani ya zo masu, to, waxannan suna da babbar azaba. Ranar da wasu fuskoki za su yi fari, wasu kuma su yi baqi. Amma waxanda fuskokinsu suka yi fari sai a ce masu: "Shin kun kafirta ne bayan imanininku? To, ku xanxana azaba saboda abin da ku ka kasance kuna aikatawa. Ali-Imran: 105-106.*

Xan Abbas da waninsa sun ce, fuskokin Ahlus-Sunnah za su yi fari, fuskokin 'yan bidi'a da masu savani su yi baqi. Allah Ta'ala ya ce

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ فَرَّقُواْ دِينَهُمۡ وَكَانُواْ شِيَعٗا لَّسۡتَ مِنۡهُمۡ فِي شَيۡءٍۚ إِنَّمَآ أَمۡرُهُمۡ إِلَى ٱللَّهِ ثُمَّ يُنَبِّئُهُم بِمَا كَانُواْ يَفۡعَلُونَ ١٥٩ ﴾ الأنعام: ١٥٩

*Lalle waxanda suka rarraba addininsu; suka zama qungiyoyi ba ka cikinsu ga komai. Al-Anam: 109.*

Ya kuma ce:

﴿ وَمَا ٱخۡتَلَفَ فِيهِ إِلَّا ٱلَّذِينَ أُوتُوهُ مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَتۡهُمُ ٱلۡبَيِّنَٰتُ بَغۡيَۢا بَيۡنَهُمۡۖ ﴾ البقرة: ٢١٣

*Ba waxanda suka yi savani a cikinsa face waxanda aka ba su shi bayan bayani ya zo masu, (suka yi haka) don zalunci tsakaninsu. [Al-baqara 213]*

Ya kuma ce:

﴿ وَمَا تَفَرَّقَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ إِلَّا مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَتۡهُمُ ٱلۡبَيِّنَةُ ٤ ﴾ البينة: ٤

*Waxanda aka ba su littafi ba su rarraba ba sai bayan bayani ya zo masu. Al-Bayyinah: 4.*

Idan lamarin ya kasance haka, to, qungiyar da tafi kowaci savawa jama'a da kuma savani tsakanin ita kanta, tafi sauran qungiyoyi cancantar zargi, wadda ta fi qarancin rarrabuwa da kusantar jama'a ta fi cancantar kasancewa a kan gaskiya. In dai Imamiyyah sun fi cancantar sava wa sauran qungiyoyin al'umma to, sun fi kowa nisa daga gaskiya, musamman ma kasancewar sun fi duk qungiyoyin al'umma savani tsakanin kansu, har aka ce qungiyarsu ta kasu zuwa saba'in da biyu. Wannan abin da muka faxa shi ne wanda aka riwaito daga Tusi da mabiyansa. Al-Hasan xan Musa An-Nubakhti ya rubuta littafi game da qididdigar qungiyoyin Shi'ah, ga shi kuma shi ma xan Shi'ar ne.

Amma Ahlus-Sunnah sun fi kowa qarancin savani a cikin asullan addininsu, sun fi kowace qungiya kusantar juna kasancewa tsakiya a wuraren savani, don ba su faifayewa ba su kuma kasawa. Ka ga ko ai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Mafi alherin lamurra shi ne matsakaicinsu". Don haka Ahlus-Sunnah su ne mafifitan dukan qungiyoyi. Don su ne matsakaita a kowane fanni.Ko a mas'alar Sahabbai, Ahlus-Sunnah ba su wuce wurin da masu guluwi ke yi, ba su kuma cin zarafi. Xauki misali Ali *Raliyallahu Anhu* 'yan-sha-biyu sun faifaye game da shi, a yayin da Harijawa suka ci zalunsa; suna kafirta shi, suna ce masa azzalumi, mai yunwar jinin musulmi, can ga bakinsu. Ahlus-Sunnah suka shiga tsakani, suka faxi gaskiya.

Ni a iya sanina, 'yan-sha-biyu ba su tava haxuwa a kan wata mas'ala ba koda qwaya xaya. Ita kanta wannan maganar da xan Shi'ar ya ambata xaya ce daga cikin maganganun 'yan Shi'ar sha biyu ba duka ba. Daga cikinsu akwai masu sava ma wannan a tauhidi. Kuma mafi yawan 'yan Shi'ah sun sava ma Imamiyyah ('yan-sha-biyu) game da lamarin Imamai goma sha biyu. Zaidiyyah da Isma'iliyyah suna tsananin gaba da wannan aqidar ta imamai goma sha biyu.

### 2.7 Maganar Wofi: Wai su Kaxai ke da Tabbacin Suna Kan Gaskiya!

Xan Shi'ar ya ce: Fuska ta uku, ita ce: Imamiyyah sun tabbatar cewa su da imamansu za su tsira, kuma cewa wanda ba su ba zai halaka. Ahlus-Sunnah ko ba su da tabbacin tsira ga kansu balle ga waninsu. Don haka bin 'yan Shi'ah shi yafi cancanta ga mai hankali. Ka ga in da mutane biyu sun fita daga cikin Bagadaza suna son tafiya Kufa sai suka ga hanyoyi biyu kowanensu ya zavi

xaya, sai wani mutum na uku ya zo shi ma zai je Kufa. Da ya tambayi na farkon, ka san hanyar da ka zava na kai ka Kufa? Kuma ita amintacciya ce ko a'a? Sai ya ce: Ni ban san komai ba game da wannan. Da ya tambayi na biyun sai ya ce masa, ni na tabbata tana kai ni Kufa, kuma amintacciya ce, kuma na san cewa hanyar da wannan ya bi ba zata kai shi Kufa ba, kuma ba amintacciya ba ce. To, in wannan mutum na uku ya bi hanyar mutumin farko lalle ya tabbata wawa a wurin masu hankali. Amma in ya bi na biyu to, ya nuna sanin-ya-kamata.

**Martani:**

In dai har wajibi ne a yi wa shagabannin da Shi'ah ke rayawa xa'a don a tsira, to, bin shugabannin Bani Umayyah da yi masu xa'a shi ma wajibi ne. Kuma in haka ne, masu bin su ido-rufe suna bisa gaskiya duk da zagin da suke yi wa Ali *Raliyallahu Anhu* da yaqan 'yan Shi'ar da suke tare da shi da suka yi. Kar ka manta su ma suna ganin cewa, yi wa shugabanni xa'a wajibi ne a komai, kuma wai, Allah Ta'ala ba zai kama shugaba da kowane irin zunubi ba, kuma wai mabiya ba su da laifi ga duk abin da suka yi wa shugaba xa'a a cikinsa. Kai, waxannan sun fi cancantar ace suna da hujja fiye da 'yan Shi'ah, don su suna xa'a ne ga shugabannin da Allah ya tsayar, ya kuma qarfafa mulkinsu.

Sanannen abu ne cewa maslaha da luxufin da aka samar wa bayin Allah ta hanyar sarakunan Bani Umayyah sun fi waxanda aka samu saboda shugaban 'yan Shi'ar da babu shi, babu alamarsa, kasasshe; wanda bai iya bayyana don tsoro. Don haka ne maslahar duniya da ta lahirar da mabiya Bani Umayyah suka samu ta fi wadda mabiyan Na-Voye suka samu. Don duk tsawon jiran da suke ma sa ba ya umurnin su da kyakkyawa balle ya hane su daga aikata mumuna, bai taimakon su don samun wata maslaha ta addininsu ko ta duniyarsu. Savanin mabiyan Bani Umayyah da suka amfana qwarai ga lamurran addininsu da na duniyarsu ta hanyar shugabannin nasu da suke yi ma xa'a.

Daga wannan ya bayyana cewa, idan hujjar da masu biyar Ali *Raliyallahu Anhu* ke kafawa daidai ta ke, to, mabiyan Usmanu su xin ma hujjarsu tana a kan hanya. Tasu ma ta fi cancantar kasancewa gaskiya. In ko hijjarsu vatatta ce, to ta 'yan Shi'ah ta fi vaci. Don da su da saura Ahlus-Sunnah duk sun haxu a kan cewa, xa'ar imaman Shi'ah kuskure ne kawai da vata.

Maganar 'yan-sha-biyu dai an gina ta a kan turaku biyu waxanda gara da gumxa suka zaizaye. Na farko, cewa suna da imami ma'asumi. Na biyu, cewa yana umurni da wani abu. To, ka ga ai imaman da suke raya cewa ma'asumai ne; ba sa kuskure sun mutu tun tuni, shi ko wanda suke jira ya vace tun fiye da shakaru xari huxu da hamsin. Wasu malaman tarihi ma sun ce ba a tava samun sa ba. To, wa suke yi wa xa'a? Sai fa malaman Shi'ah ko litaffan

da suka rubuta waxanda suke cewa sun karvo daga imamai da ba su kuskure. To, kuma ai suna kuskure, sannan ba su da tabbacin cewa za su tsira.

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* dai shi ne ke isar da saqo daga Allah Ta'ala game da abin ya yi umurni da shi kuma da wanda ya yi hani daga gare shi, ba wata halittar da ake yi wa xa'a kai tsaye sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.* To, in an mayar da imami ko shaihi bayan fakuwarsa ko mutuwarsa abin kira, kuma ana neman ya biya wasu buqatu, kenan mamacin ya yi kama da Allah Ta'ala, wanda kuwa yin haka fita ne daga tushen musulunci shi ne Tauhidi.

Duba mafi yawan 'yan xariqu, suna dogaro ne a kan wasu hikayoyin da aka riwaito daga shehinsu, waxanda da yawa daga cikinsu qarya ce aka yi masa, wasu kuma kuskure ne shehin ya yi, sai su bar riwaya ta gaskiya daga Annabi ma'asumi zuwa ga riwayar da ba a gasgatawa kuma daga wanda ba ma'asumi ba. To, idan waxannan 'yan xariqun sun yi kuskure ne anan, to, 'yan-sha-biyu sun fi su kuskure don sun fi zura qarya a cikin abubuwan da suke riwaitowa daga imamansu, kuma sun fi tsananin wuce iyaka ga raya cewa imamansu ma'asumai ne.

Misalin da ya bayar na masu tafiya Kufa shirme ne kawai. Wa ya sani ko wanda ya ce ya sani qarya yake yi? Wataqila ma dibara ce yake yi don ya samu abokin tafiya in sun yi nisa ya yi masa fashi! Shi dai na farkon ya bar ka da nazarinka, bai yi ma ka qarya ba don ka so shi. Ashe aikin hankali ba shi ne ka bi wannan kawai don ya cika baki ba, sai dai ka yi naka nazari har ka gano lafiyayyar hanya.

Kuma wai, yana nufin duk wanda ke bisa aqidarsu ya sakankance zai shiga aljanna koda kuwa ya bar farillai, ya aikata haramun? To, wannan kam ko 'yan-sha-biyun ba su ce haka ba. Kuma duk wani mai hankali ma ba zai faxi haka ba.

Wai, a ganinsu sun samu tabbacin tsira ne saboda son Ali *Raliyallahu Anhu* a matsayinsa na aikin lada da suka ce, savo ba ya cutar da mai shi. Saboda haka kenan barin salloli da aikata alfasha koda zuriyar Ali ne *Raliyallahu Anhu* ba zasu cutar ba, kai, koda mutum ya zubar da jinin Bani Hashim, dangin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* matuqar dai yana son Ali *Raliyallahu Anhu*. Wa zai gasgata wannan wofintattar magana? In kuma sun dawo sun ce, so na gaskiya na sa mutum ya bi masoyinsa, sai lamari ya koma ga cewa dole ne kenan a aikata wajibbai kuma a bar abubuwan da Allah Ta'ala ya haramta.

In kuma suna nufin cewa, duk wanda ke da aqida ingantacciya ya kuma aikata wajibai ya nisanci abubuwan da aka haramta zai shiga aljanna, to, wannan ita ce aqidar Ahlus-Sunnah, don su suna yanke cewa wanda ya ji tsoron Allah Ta'ala zai shiga aljanna kamar yadda Al-Alqur'ani ya ba da tabbaci. Amma Ahlus-Sunnah ba su yanke hukuncin shiga aljanna akan wani mutum na musamman don ba su da tabbacin cewa yana cikin masu tsoron Allah Ta'ala. Amma in an san cewa, ya mutu akan taqawa to, ana sanin cewa

ya na cikin 'yan aljanna. Don haka ne suke cewa, waxanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce 'yan aljanna ne to, batu ya qare. Amma wanda mutane da yawa suka yaba da cewa mai rikon addini ne to, ba dukan Ahlus-Sunnah ke yarda da yin yanke a kan zamansa xan aljanna ba, sai dai kyautata zato.

Daga nan ne ya bayyana cewa, 'yan-sha-biyu ba su da wani yaqinin da ake yabawa wanda suka kevanta da shi koma bayan Ahlus-Sunnah.

In sun ce suna da yaqini a kan wanda suka ga yana lizimtar aikata wajibai sannan yana nisantar muharramai cewa shi xan aljanna ne, ba tare da imami ma'asumi ya faxa masu abin da ke cikin zuciyarsa ba. Sai a ce masu wannan matsalar ba ta rataya da shugabanci ba. In ma an qaddara cewa akwai ingantacciyar hanya mai kai ga wannan to, ta Ahlus-Sunnah ce, kuma sun qwarewa shiga hanyar. In ko babu wata ingantacciyar hanya zuwa ga wannan, to, wannan magana da ba a gina a kan ilimi ba, babu wata falala a cikinta, haka ma cikin rashinta. A taqaice dai babu wani ingantaccen ilimin da za su raya face Ahlus-Sunnah sun fi su cancantarsa, amma abin da suka raya na jahilci to, wannan naqasu ne, kuma Ahlus-Sunnah sun fi kowa nisa daga gare shi.

Kuma ma a qashin gaskiya yaqinin da Ahlus-Sunnah ke da shi na samun tsirar shugabanninsu ya fi na Shi'ah 'yan-sha-biyu. Don shugabanninsu bayan Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* sune magabata na farko daga cikin Muhajiruna da Ansaru, sun kuwa sani yanke cewa, za su sami tsira. Suna sheda cewa Sahabban nan goma za su shiga aljanna, kuma Allah ya ce wa Sahabban Badar: "Ku yi abin da kuke so, lalle na gafarta maku". Kai har ma suna cewa: "Babu wanda zai shiga wuta cikin waxanda suka yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* mubaya'a a qarqashin itaciyar nan". Kamar yadda ya tabbata a cikin ingantaccen hadisi daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Waxannan sun fi mutum dubu da xari huxu, kuma shugabanni ne na Ahlus-Sunnah. Suna sheda cewa babu wanda zai shiga wuta cikinsu, kuma shahada ce da aka gina ta a kan ilimi, kamar yadda Alqur'ani da Sunna suka nuna.

Ahlus-Sunnah na yin sheda ko dai gamammiya ko kuma ga wasu sanannu, amma duk suna gina wannan akan ilimi. Amma 'yan-sha-biyu su suna sheda a kan abin da ba su sani ba, ko su yi Shedar-Zur wadda sun san qarya ce, kamar yadda imamus-Shafi'i ya ce: "Ban ga mutanen da ke shedar qarya kamar Shi'ah 'yan-sha-biyu ba".

Kuma duk imamin da aka shaida cewa zai tsira ko dai ya kasance wanda ake yi wa gamammiyar xa'a ne, ko kuma wanda ake yi wa xa'a in ya yi umurni da abin da yake xa'a ne ga Allah Ta'ala da Manzonsa, da kuma abin da yake faxa daga ijtihadinsa in ya san babu abin da ya fi wannan. In imami shi ne na farkon to, Ahlus-Sunnah ba su da wani shugaban da ke haka bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Su suna faxa ne kamar yadda Mujahid da Hakim da Malik da sauransu suka faxa cewa: "Duk mutum ana karva kuma ana barin maganarsa face Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama"*. Su

suna sheda cewa shugabansu shi ne mafificin halitta. Kuma suna sheda cewa duk wanda ya yi koyi da shi, ya bi umurninsa, ya hanu daga haninsa zai shiga aljanna. Kuma shaidar su Ahlus-Sunnah ta fi ta Shi'ah 'yan-sha-biyu kamala har bisa wadda su ke yi wa shugabanninsu Askari i da ii da makamantansu cewa wanda ya yi masu xa'a zai shiga aljanna.

Allah Ta'ala dai ya yi alqawarin ni'ima ga wanda ya yi masa xa'a kuma ya yi wa Manzonsa xa'a, kuma ya yi alqawarin tavarwa ga wanda bai aikata haka ba. To, an rataya ni'ima a kan xa'a ga Allah Ta'ala da Manzonsa. Kamar yadda Allah ya ce:

﴿ وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ فَأُوْلَٰٓئِكَ مَعَ ٱلَّذِينَ أَنۡعَمَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِم مِّنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ وَٱلصِّدِّيقِينَ وَٱلشُّهَدَآءِ وَٱلصَّٰلِحِينَۚ وَحَسُنَ أُوْلَٰٓئِكَ رَفِيقٗا ﴿٦٩﴾ ﴾ النساء: ٦٩

*Kuma wanda duk ya yi wa Allah da Manzonsa biyayya to, waxannan suna tare da waxanda Allah ya yi wa ni'ima daga cikin Annabawa da siddiqai da shahidai da salihai kuma maqwabtaka da waxannan ta kyautata An-Nisa: 69.*

Da makamantansa.

Idan ya kasance haka, to, Allah Ta'ala na cewa:

﴿ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ مَا ٱسۡتَطَعۡتُمۡ ﴾ التغابن: ١٦

*ku ji tsoron Allah gwargwadon ikonku At-Tagabun: 16.*

Duk wanda ya yi iyakar qoqarinsa wurin yin xa'a ga Allah da Manzonsa to, zai kasance cikin 'yan aljanna.

Saboda haka cewar 'yan-sha-biyu wai, ba mai shiga aljanna sai in shi xan-sha-biyu ne ba ya da banbanci da maganar Yahudawa da Nasara:

﴿ وَقَالُواْ لَن يَدۡخُلَ ٱلۡجَنَّةَ إِلَّا مَن كَانَ هُودًا أَوۡ نَصَٰرَىٰۗ تِلۡكَ أَمَانِيُّهُمۡۗ قُلۡ هَاتُواْ بُرۡهَٰنَكُمۡ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ﴿١١١﴾ بَلَىٰۚ مَنۡ أَسۡلَمَ وَجۡهَهُۥ لِلَّهِ وَهُوَ مُحۡسِنٞ فَلَهُۥٓ أَجۡرُهُۥ عِندَ رَبِّهِۦ وَلَا خَوۡفٌ عَلَيۡهِمۡ وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ ﴿١١٢﴾ ﴾ البقرة: ١١١ - ١١٢

*Kuma sun ce ba wanda zai shiga aljanna face in ya kasance Bayahude ne ko Banasare. Wannan gurinsu ne. Ka ce, su kawo hujjarsu in sun kasance masu gaskiya. Ba haka ba ne, duk dai wanda ya miqa wuyansa ga Allah (ya musulunta) kuma ya kasance mai kyautatawa, to, yana da ladarsa wurin ubangijinsa. Kuma ba tsoro gare shi, ba baqin ciki. Al-Baqarah: 111-112.*

Sanannen abu ne cewa, wanda 'yan-sha-biyu ke jira ba shi wajaba a kan kuwa ya yi masa xa'a, don ba a san wata maganar da aka naqalta daga wurinsa ba. Don haka, wanda ya yi wa Manzo xa'a zai shiga aljanna ko da bai yi imani da wannan imamin ba. Wanda ya yi imani da wannan imamin kuma ba zai shiga aljanna ba in bai yi wa Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* xa'a ba. Don haka xa'ar Manzo ita ce abin dogara akai wurin samun tsira ba zama xan-sha-

biyu ba. Ko a nan ta bayyana cewa, Ahlus-Sunnah sun tabbatar da cewa za su samu tsira da kuma tsira ga duk wanda yake bisa tafarkin na Sunnah.

### 2.7 Wai Sun Karvo Mazhabarsu Daga Ma'asumai

Xan Shi'ar ya ce: Fuska ta huxu, ita ce, 'yan Shi'ah Imamiyyah sun karvo mazhabarsu ne daga imamai ma'asumai waxanda aka sani da falala da ilimi da gudun duniya da tsentseni, masu shagalta kowane lokaci da ibada da addu'a da karatun Alqur'ani, da dawwama a kan wannan tun yarantansu har mutuwarsu. Daga cikinsu akwai masu koya wa mutane ilimi, kuma a kansu ne suratul-Insan ta sauka. Da ayar tsarkin Ahlul-Baiti da wajabcin son su, da ayar la'ani da sauransu. Ali *Raliyallahu Anhu* ya kasance yana yin raka'a dubu kowane yini da dare kuma yana karanta Alqur'ani duk da jarabar yaqi da ya yi fama da ita.

### 2.7.1 Imami na Farko:
### Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu*

Xan Shi'ar ya ce: Imami na farko shi ne Ali *Raliyallahu Anhu* wanda shi ne mafificin bayi bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Allah Ta'ala ya kira ran Manzo wurin da ya ce:

﴿وَأَنفُسَنَا وَأَنفُسَكُمْ﴾ آل عمران: ٦١

*Da kawunammu da kawunanku. Al-Imran: 61*

Manzo ya qulla 'yan'uwantaka da shi, kuma ya aurar masa da xiyarsa. Falalarsa ba a voye take ba, mu'ujizozi da yawa sun bayyana a hannunsa har wasu mutane suka ce shi ma abin bautawa ne, ya kashe su. Wasu kuma suka bi maganarsu kamar *Gulatu* da *Nusairiyyah*.

**Martani:**

Ba mu yarda cewa, 'yan-sha-biyu sun karvo mazhabarsu daga Ahlul-Baiti ba, ba su ba ba sauran 'yan Shi'a ba. Su da suka sava wa Ali *Raliyallahu Anhu* da Ahlul-Baiti a cikin duk asullansu da saka sava wa Ahlus-Sunnah a cikinsu! Abin da ya tabbata daga Ali *Raliyallahu Anhu* da Ahlul-Baiti shi ne tabbatar wa Allah Ta'ala da siffofin da ya tabbatar wa kansa da imani da qaddara da tabbatar da halifancin halifofi uku na farko, da tabbatar da falalarsu, kuma duk a nan 'yan-sha-biyu sun sava ma su. An samu riwayoyi da yawa game da wannan cikin littaffan malamai ta yadda waxannan riwayoyin na sa mutum ya kai ga samun ilimi na yaqini cewa Ali da Ahlul-Baiti ba su tare da 'yan-sha-biyu.

'Yan-sha-biyu kuma harwayau sun sava a tsakanin junansu game da abubuwan da suka shafi sifofin Allah Ta'ala da imani da qaddara, da sauran abubuwan da suka shafi asullan addininsu. To wace magana ce suka karvo daga imamansun da ba su kuskure? Har ma abin da ya shafi imamancin suna da Savani da yawa cikin sa.

Kai har ma game da Mahadin su ke jira suna da savani. Daga cikinsu akwai masu cewa Ja'afar xan Muhammad ne. Wasu kuma sun ce a'a xansa ne Musa xan Ja'afar. Akwai kuma waxanda suka ce Muhammad xan Abdullahi xan Hasan shi ne Mahadin. A yayin da wasu suka ce Muhammad xan Hanafiyya ne. Wasu kuma sun ce Ali xan Hassan xan Husain ya yi wasici ne ga xansa Abu Ja'afar, wasu kuma na cewa ga xansa Abdullahi. Haka dai a kowane imami sai da suka yi savani.

Wasu abubuwan da ya faxa sharholiya ce kawai, irin cewar da ya yi, a kansu ne aka saukar da Suratul Insan. Domin wannan surar a Makka ta sauka tun kafin auren Ali da Nana Fatima. Ita ma ayar tsarkake Ahlu-Baiti da tafi da qazanta daga gunsu, tattare kasancewarta tana magana ne a kan matan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, ba labari take bayarwa ba, umurni ne kamar irin umurni da aka yi wa musulmi baki xaya da yin alwala kuma Allah ya yi irin wannan maganar a Suratul Ma'ida ya ce: *Allah ba ya nufin ya quntata ma ku, amma yana son ne ya tsarkake ku. Al-Ma'ida:6.*

Sai cewar da ya yi wai, Ali na sallah raka'a dubu kowace rana. Wannan ya nuna bai ma san mene ne falala ba. Domin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai tava wuce raka'a goma sha uku a dare xaya ba kamar yadda ya zo a cikin Buhari da Muslim. A cikin Buhari da Muslim kuma, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Mafificin tsayuwar dare shi ne na Annabi Dawuda *Alaihis Salamu;* ya kan yi baccin rabin dare, sannan ya yi tsayin sulusi, sannan ya sake baccin sudusi".

Haka shi ma cewar da ya yi, wai, Ali shi ne mafificin talikai bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, cika baki ne kawai, ba hujja.

Hadisin da ya kawo cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya qulla 'yan'uwantaka tsakaninsa da Ali shi ma irin wancan ne. Don Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya qulla tsakaninsa da kowa ba, bai kuma yi tsakanin Muhajirai wasu-wasu ba, ko tsakanin Ansarai wasu-wasu. Abin da ya tabbata a sahihan hadissai shi ne, ya yi wannan haxin zumunci ne tsakanin Muhajirai da Ansarai, kamar yadda ya yi a tsakanin Sa'adu xan Rabi'u da Abdurrahman xan Aufu, da kuma tsakanin Salmanul-Farisi da Abud-Darda'i.

Sai cewa, Allah ya sanya Ali shi ne ainin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* in da ya ce: *Da kawunanmu da kawunanku. Ali Imran: 61.* Wannan in da Allah ya ce ne: *In da ma lokacin da kuka ji shi (qazafin) muminai maza da mata sun zaci alheri ga kawunansu (yana nufin ga 'yar uwarsu kuma uwarsu A'ishah). An-Nur:12.* Ka ga duk muminai 'yan'uwan juna ne sashensu majinvinta sashe.

Aurar ma sa da Fatima kuma daraja ce kamar aurar ma Usman da Ummu Kulsumi da Ruqayyatu. Don haka ma ake ce ma Usman *Dhun-Nuraini* mai haske biyu. Haka auren 'yar Abubakar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi daraja ne ga Abubakar. Haka auren xiyar Umar shi ma daraja ne ga Umar xin. Saboda haka duk halifofinsa huxu Allah ya ba su wannan falalar ta surukuta da shi *Sallallahu Alaihi Wasallama.*

Sai cewar da ya yi Ali na da mu'ujizoji masu yawa. Wataqila yana nufin karamomi. Wannan ko ba wani kayan gabas ne ba ga Ali, don ya fi daraja a kan mafi yawan waxanda suka samu karamomin, cikinsu har da jahilai. Kuma don wasu sun xaukaka shi har sun ce ma sa Allah, wannan bai zama daraja. Ai duk mu'ujizar da ta bayyana gare shi in har akwai to, ta Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ta fi ta, amma babu mai hankalin da ya tava ce ma sa Allah. Shikenan don wasu sun ce Annabi Isah Allah ne sai a fifita shi a kan Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama*? Ina banbancin shirmen masu ce ma sa Allah da na Harijawa masu kafirta shi? In ka ce saboda xaukakarsa ne da zamansa na Allah waxancan suka ce shi ne Allah, wani zai ce, saboda yawan zunubansa da miyagun ayyukansa Harijawa suka kafirta shi. In ka ce saboda rashin hankalin Harijawa ne suka kafirta shi, to, su ma waxancan 'yan Shi'ar saboda rashin hankalinsu ne suka Allantar da shi. Kuma tare da haka Harijawa sun fi 'yan Shi'ah hankali da riqon addini sau ba iyaka, sun fi su kafa hujja mai xan sauraruwa.

A wurin Ali kansa gara Harijawa da Gulatun 'yan Shi'ah masu Allantar da shi.

### 2.7.2 Hasan da Husaini

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: 'Yayansa biyu su ne jikokin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama,* kuma su ne shugabannin matasan aljanna. Imamai biyu ne bisa ga nassin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Su ne suka fi kowa ilimi da zuhudu a zamaninsu. Sun yi jihadi a tafarkin Allah yadda ya kamata har aka kashe su. Hasan ya sa rigar gashin dabbobi a qarqashin tufafinsa masu tsada ba tare da mutane sun san da haka ba. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* watarana ya xora Husaini akan cinyarsa ta dama ya xora xansa Ibrahimu akan cinyarsa ta hagu, sai Jibrilu *Alaihis Salamu* ya sauko ya ce ma sa: "Allah ya ce ba zai haxa ma ka su ba, don haka ka zavi xayansu". Sai Manzo ya ce, in Husain ya mutu zan yi kuka, Ali ma ya yi, sannan Fatima ta yi, amma in Ibrahim ya mutu to, ni kaxai zan yi kuka, sai ya zavi mutuwar Ibrahim ya kuwa mutu bayan kwanan uku. Wannan ne ya sa, inji xan Shi'ar duk lokacin da Husaini ya zo wurinsa sai ya ce maraba da wanda na fansa da xana Ibrahim.

**Martani:**

Tabbataccen abu shi ne Hasan shugaba ne da Allah zai kimtsa shirin musulmi da shi a lokacin tashin hankali da rikici a tsakaninsu. Haka *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya faxa. Kuma ta tabbata cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* kan xora Hasan a xaya cinyarsa, Usamatu xan Zaidu a xaya, ya ce: "Ya Allah! Haqiqa ina son su, kai ma ka so su, ka so wanda yake son su".

Wannan kuwa na nuna abin da Hasan ya yi na sauka daga muqami da rashin ci gaba da tilasta waxanda ba sa son shugabancinsa shi ne abin da Allah da Manzo ya fi so. Yin hakan ba aibi ne ba, ba kuma keta alfarmar gaskiya ne

ba kamar yadda ‘yan-sha-biyu ke gani. Wannan shi ya sa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya so su shi da Usamatu. Ka ga ai ko Usamatu yana cikin masu qyamar fitina da yaqi a lokacin tashin hankali, shi ya sa bai shiga cikin rundunar Ali ko ta Mu’awiyah ba. Shi kuma Hasan a kullum yana ba mahaifinsa shawarar barin yaqi. Savanin abin da ‘yan-sha-biyu ke cewa, Hasan ya tozarta musulmi da ya nemi a zauna lafiya. In da a ce, akwai wani shugaba da ya wajaba kowa ya bi shi don yana ma’asumi kuma duk wanda ya hau ba shi ba mulkinsa vatacce ne, ai da wannan sulhin da Hasan ya yi ya zama varna kamar yadda suke cewa. To, da haka ne ko za a yabi Hasan a kan wannan gyara? Sai dai ko a ce an yi masa uzuri don rauni ko kasawa. Hasan kuma ya fi Husaini damar yin yaqi, amma ya bar shi. Allah na xaukaka darajar muminai ko a aljannan wani ya fi wani. Tattare da kasancewar yardar Allah ta tabbata a gare su baki xaya.

Sannan idan har Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ya nassanta zamansu imamai, to, ba wani amfani ga nassanta su da Alin ya yi. Mu dai mun san Hasan da Husaini abar qaunar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne a duniya, kuma ya saka su a cikin bargo ya yi masu addu’a. Suna da darajoji masu yawa, da matsayi babba a wurin musulmi. Amma cewa, sun fi kowa ilimi ko gudun duniya wannan cika baki ne kawai, ba dalili.

Sai cewar da ya yi wai, sun yi jihadi har suka bar duniya. Abin da duniya ta sani shi ne, Hasan ya kira Mu’awiyah da kansa ya damqa masa ragamar shugabancin musulmi duk da kasancewar rundunar Iraqi duka tana tare da shi. A tarihinsa bai tava zavin yaqar musulmi ba. A lokacin mutuwarsa kuma wasu sun ce an saka masa guba ne a abinci. Ta haka ya samu xaukakar yin shahada kenan. Amma dai bai mutu yana riqe da makami ba, sam. Shi kuma Husaini ya fita da nufin yaqi, amma a zatonsa zai samu goyon bayan ‘yan Shi’ar Iraqi. Da ya lura da cin amanarsu dai ya canza niyya, ya buqaci a bar shi ya koma gida, ko ya je jihadin kafirai ko ya tafi da kansa wurin sarki Yazidu. Rashin samun damar yin ko xaya daga cikin abin a ya nema shi ya sa ya yi yaqi kuma har aka kashe shi akan zalunci, ya yi shahada.

Shi kuma Hasan da xan Shi’ar ya ce wai, yana sanya tufan gashin dabbobi a qarqashin tufan auduga, wannan ba wata daraja a cikinsa, don kamar shigen cewa, Ali na raka’a dubu a kullum ne. Kawai abin da za mu ce shi ne, da yin haka addini ne da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya sunnanta haka, ko dai ta hanyar ya aikata, ko ya nuna ma wani ya aikata, ko wani ya yi haka Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tabbatar da abin da ya yi xin. Tunda kuwa aka ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba haka yake yi ba, ba kuma haka Sahabbai suke yi ba, mun san ba wata falala a cikin haka. Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da kansa ya kan sanya rigar auduga musamman a cikin tafiye-tafiyensa.

Daga qarshen hadisin da ya kawo cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya xora Husaini da Ibrahim a kan cinansa, kuma Jibrilu *Alaihis Salamu* ya zo ya ba shi zavi a tsakaninsu, tatsuniya ce kawai da ba ta da asali

sai a cikin qwaqwalen jahilai. Kuma ai a ga Hasan nan an bari tare da Husaini. To, sai me?

### 2.7.3 Zainul Abidina da Baqir da Sadiq

Shi kuma Ali xan Husaini Zainul abidina ya kasance yana azumi da rana, ya yi sallah da dare, ya kuma karanta Alqur'ani. Yana yin sallar raka'oi dubu ga yini da darensa kowace rana. Yana kuma addu'a bayan rakao'i biyu da addu'oi nasa da waxanda aka riwaito daga iyayensa, sannan ya jerfar da takarda yana mai cewa, yaya ma zan iya yin ibada irin ta kakana Ali. Kamar yana damuwa. Ya kasance yana yawaita kuka har hawaye suka yi masa tsaga a fuska, yayi sajada har aka kira shi mai tambon sallah. Kuma Manzo ya kira shi *Sayyidul Abidina,* shugaban masu ibada.

Akwai lokacin da Hishamu xan Abdulmalik ya je aikin hajji ya yi qoqarin sunbuntar Hajarul-Aswad bai samu damar yin haka ba saboda gwamatso, amma lokacin da Ali xan Husaini ya zo yin haka sai dukan mutane suka ba shi wuri ya sumbaci dutsen shi kaxai. Sai Hishamu xan Abdulmalik ya ce, wane ne wannan? Sai Farazdaq ya yi waqoqin nan nasa da aka sani game da shi. Sai Zainul Abidina ya aika ma Farazdaq dinari dubu zuwa, shi ko ya qi karva, ya ce, abin da ya sa na yi wannan waqar don fusata saboda Allah da Manzonsa. Ba zan karvi kuxi a kansa ba. Sai ya ce mu Ahlul-Baiti abin da ya fita daga wurinmu ba ya komawa. Sai Farazdaq ya karvi kuxin.

Akwai wasu mutane a Madina, abincinsu na zo masu da dare ba su san daga inda yake zuwa ba, sai da Zainul Abidina ya mutu sai suka gane cewa abincin daga wurinsa yake zuwa.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Xansa Muhammad Al-Baqir ya fi kowa zuhudi da ibada. Sujada duk ta kware fuskarsa. Ya fi kowa ilimi a zamaninsa. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kira shi *Baqir, m*ai ramin sujada. Jabiru xan Abdullahi ya zo wurinsa a lokacin Baqir xin yana qarami a makarantar Allo, sai ya ce masa: "Kakanka Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na gaishe ka". Sai aka ce wa Jabir yaya aka yi haka? Sai ya ce: Na kasance wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* Husaini na bisa qafarsa yana wasa, sai Manzo ya ce, za a haifa ma sa xan da ake kira Ali, ranar tashin qiyama wani mai kira zai kira yana cewa, shugaban masu ibada ya tashi, sai Alin ya tashi, sannan a haifa ma sa xan da ake kira Muhammad Al-Baqir, zai fexe ilimi fexewa. In ka haxu da shi ka isar ma sa da gaisuwata. Abu Hanifa ya riwaito shi da waninsa.

Xan Shi'ar ya ce: Sai kuma xansa As-Sadiq wanda ya fi duk mutanen zamaninsa ilimi da ibada. Malamman tarihi sun riwaito cewa, shagaltarsa da ilimi ta hana masa neman shugabanci. Umar xan Abul Miqdami ya ce: Na kasance in na dubi Ja'afar xan Muhammad As-Sadiq sai in san cewa yana daga cikin zuriyar Annabawa. Shi ne ya yaxa fiqihun 'yan-sha-biyu da ilimi na haqiqa da aqidodi na yaqini. Bai kasance yana ba da labarin abu ba face ya auku. Don haka na ake kiran sa As-Sadiq Al-Amin.

Abdullahi xan Husaini ya tara mabiyan Ali don yin mubaya'a ga 'ya'yansa biyu, sai Sadiq ya ce ma sa, wannan lamarin ba zai auku ba, sai ya yi fushi a kan haka. Sai ya ce, mai shuxin hular can ne zai zama sarki, yana nuna Mansur. Da Mansur ya ji haka, ya san cewa lamarin zai auku, kuma sarauta za ta kai wurinsa. Amma lokacin da ya samu matsala har ya gudu sai ya rinqa cewa, ina zancen mai gaskiyar nan nasu? A qarshe dai shi ya sami mulkin.

**Martani:**

Shi dai Zainul Abidina yana daga cikin manyan Tabi'ai a fagen ilimi da riqon addini. Malaman Sunna sun yi ma sa sheda a zamaninsa.

Malam Yahaya xan Sa'idu ya ce: "Zainul Abidina ne mafi darajar bahashimen da na tarar a Madina". Shi kuma Muhammadu xan Sa'adu cewa ya yi: "Zainul Abidina ya kasance amintacce, yardajje, mai yawan hadisai, na qwarai; masu gajeruwar hanya". Yahaya xan Sa'idu kuma ya ce, na ji Zainul Abidina na cewa: "Ya ku mutane! Ku so mu irin son musulunci. Wannan son da kuke yi mana ya kusa zama abin kunya a kanmu".

Sai cewa yana raka'a dubu kullum. Mun riga mun faxi cewa, wannan ba zai yiwu ba sai in an yi sallolin ba yadda shari'ah ta nema ba. Kuma tun can asali shari'a ba ta yi umurni da yin haka ba. Haka kuma ba wani hadisi mai asalai a kan cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ya sa ma sa wannan laqabi na *Sayyidul Abidina.*

Shi ma xansa Abu Ja'afar Al-Baqir yana daga cikin masu ilimi da riqon addini. An ce ana kiransa *Baqir* ne don ya tona ilimi, ba don sujada ta ci goshinsa ba kamar yadda xan Shi'ar ya ce. Amma shi ma ba gaskiya ba ne a ce ya fi kowa ilimi a zamaninsa. Ga irin su Zuhuri a zamaninsa wanda malamai sun san ya fi shi ilimi. Hadisin cewa, Annabi ya kira *Baqir* shi ma ba ya da asali, qarya ne. Haka cewa, wai, Jabir *Raliyallahu Anhu* ya isar ma sa da gaisuwar Annabi.

Ja'afarus-Sadiq ma haka. Yana cikin malamai masu daraja. Amru xan Abul Miqdami ya ce: Duk na kalli Ja'afar xan Muhammadu nikan gano cewa, yana cikin zuri'ar annabta. Amma cewa, ya kama ibada ya bar sha'anin mulki ya ci karo da aqidarku ta 'yan-sha-biyu. Domin a wurinku dole ne ya jagoranci jama'a tun da Allah ne ya xora ma sa, inji ku. In da ya tsaya ya yi wannan wajibin ai da ya fi ma sa yawan nafilfili ko?

Sai cewa, shi ya yaxa ilimin Imamiyyah da aqidunsu. Yana son ya ce ya qago wani ilimi ne da babu shi kafin lokacinsa? Ko kuma waxanda suka gabace shi ne ba su yi bayanan da ya kamata ba? Ai duk mai hankali ya san cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya gama bayyana ma al'ummarsa duk wata aqida da ya wajaba su qudurta, ya karantar da su cikakken addininsu. Sahabbai kuma sun yi iya qoqarinsu wajen ganin sun xauko wannan sun isar da shi ga sauran musulmi. Maganar xan Shi'ar dai in ba ta zama suka ga Ja'afarus-Sadiq ba, to, suka yake nufi ga magabatansa. Kuma Ja'afarus-Sadiq ya zama shi ne alqiblar maqaryatan wannan al'umma, kowa ya kwaso sharar

maganganunsa sai ya jingina a gare shi. Allah zai yi hukunci da adalci a tsakaninsa da maqaryata.

### 2.7.4 Musa xan Ja'afar

Xan Shi'ar ya ce: Sai kuma xansa Musa Al-Kazim. Ana kiransa bawan Allah Nagari, ya fi kowa bautar Allah a zamaninsa. Yana azumi da rana kuma ya tsayar da sallah da dare. An kira shi Kazim don in wani abu ya zo masa daga wani sai ya aika masa kuxi. Ibnul jauzi xaya daga cikin Hambalawa ya ce: An riwaito daga Shaqiq Al-Balakhi ya ce, na fita zuwa hajji a shekarar 149H, sai na sauka a Qadisiyyah, sai ga wani saurayi kyakkyawa, wankan tarwaxa, yana sanye da tufa mai gashi, ya rataya gwado, yana kuma sanye da takalma, ya zaune shi kaxai. Sai na ce a raina, wannan saurayin Sufi ne, yana son ya zama nauyi akan mutane, wallahi zan tafi wurinsa in tsawace shi. Sai na kusanta gare shi. Lokacin da ya ga na nufo shi sai ya ce, ya Shaqiq: *Ka nisanci mafi yawan zato don sashen zato zunubi ne. Al-Hujurat 12.*

Sai na ce cikin raina wannan bawa ne salihi ya furta abin da ke cikin raina, zan tafi wurinsa in ce ya yafe ma ni, sai ya vace daga idanuna. A lokacin da muka sauka *Waqisa* sai ga shi yana sallah, gavovinsa na kakkarwa, idonsa na zubar da hawaye, sai na ce: Zan je in ce ya yi mani uzuri, sai ya taqaita sallah ya ce, ya Shaqiq: *Lalle ni mai yawan gafartawa ne ga wanda ya tuba, ya yi imani, ya kuma aiki na gari, sannan ya shiriya. Xaha:82.* Sai na ce wannan yana cikin *Abdalu* zavavvun matanen da Allah kiyaye duniya da su, ya yi magana game da sirrina sau biyu kenan. Lokacin da muka sauka wurin da ake kira *Zibalah*, sai ga shi tsaye bakin wata rijiya, da wani abu a hannunsa don xibar ruwa, sai abin ya faxa cikin rijiya. Sai ya xaga kansa sama ya ce:

Kai ne Ubangijina idan na yi qishi
Kai ne kuma abincina idan na ji yunwa
Ya shugbana! Ba ni da wata guga in ba wannan ba.

Sai Shaqiq ya ce: Wallahi na ga rijiya ta taso, ya xauki gugarsa, cike da ruwa, ya yi alwala, ya yi sallah raka'a huxu, sannan ya tafi wurin wani tulin rairayi, sai ya rinqa xibar rairayin yana sa wa cikin guga yana sha, sai na ce ka ciyar da ni cikin sauran abin da Allah Ta'ala ya ciyar da kai, ko abin da Allah Ta'ala ya ni'imta ka da shi, sai ya ce: Ya kai Shaqiq! Ni'imomin Allah Ta'ala bayyanannu da voyayyu ba su gushe ba a kanmu, ka kyautata zato ga Allah Ta'ala. Sai ya bani gugar, sai na tarar cewa wani abin sha ne da aka haxa da sukari, ban tava shan abu mai daxi da qanshi ba irinsa. Na sha na yi dis. Na yi kwana da kwananaki bayan haka ba na sha'awar wani abin ci ko abin sha. Ban sake ganin sa ba sai a Makka, sai na gan shi a wani wuri cikin masallaci da tsakiyar dare yana sallah da natsuwa, yana nishi da kuka, bai gushe a cikin wannan halin ba har safiya ta waye, da asuba ta yi sai ya zauna wurin sallarsa yana tasbihi, sannan ya tashi don ya yi sallar farilla, sai ya yi xawafi shuxi bakwai sannan ya fita. Sai na bi shi, na kuma tarar cewa yana da mabiya da kuxi da bayi, savanin yadda na gan shi a hanya, sai mutane suka kewaye shi

suna yi masa sallama suna neman albarkarsa. Sai na ce masu: Wane ne wannan? Suka ce: Musa ne xan Ja'afar. Sai na ce, na yi mamakin irin waxannan abubuwa ga wani ba irin wannan sharifin ba. Wannan bahambale ne ya riwaito shi.

Kuma a hannunsa ne Bishir Al-Hafi ya tuba, don akwai ranar da ya wuce ta gidansa a Bagadaza sai ya ji ana ta yin ma-sha'a, da waqoqi da raye-raye a gidan nasa. Sai ga wata kuyanga ta fito da shara, sai ta jefar da ita a juji. Sai ya ce mata, ke yarinya, maigidan nan bawa ne ko xa? Sai ta ce da shi, xa ne. Sai ya ce, kin yi gaskiya, don da bawa ne da ya ji tsoron Ubangijinsa. Da kuyangar ta shiga gida sai ta tarar mai gidan yana shan giya, ya ce: me ya tsayar da ke? Sai ta ba shi labari. Sai ya fita ba takalma har ya isa wurin shugabanmu Ja'afar ya tuba a hannunsa.

**Martani:**

Iyakar abin da aka sani a kan Musa shi ne, an haife shi a garin Madina, a bayan shekara ta 120. daga nan kuma Sarkin Musulmi Mahadi ya kira shi zuwa Bagadaza. Ya kuma sake dawo da shi Madina bayan haka. A nan ne ya ci gaba da rayuwa har zamanin Sarki Rashid. A zamanin Sarki Haruna Rashid da ya je Umrah, ya bi ta Madina, ya kuma ya xauki Musal Kazim karo na biyu zuwa hedikwatar mulki; Bagadaza, ya kuma tsare shi a can har ajalinsa ya riske shi yana a tsare.

Musal-Kazim mutum ne da ya shahara a fagen qoqarin ibada. Waxanda ke bayansa babu wani ilimi na addini da duniya ta qaru da shi daga wurin su, domin kuwa kafin ka yarda mutum na iya ba ka riga sai ka duba ta wuyansa. Labarin da aka yaxa kuwa cewa Bishir Al-Hafi ya tuba ne a hannunsa na daga cikin qarairayi na masu qarin gishiri. Domin kuwa bai samu sukunin da zai iya haxuwa ma da Bishir ba zuwansa Bagadaza, kuma a girke yake wuri xaya.

### 2.7.5 Ali Ar-Ridha

Xan Shi'ar ya ce: Shi kuwa Ali Ar Ridha shahararren malami ne. kuma ya fi kowa Zuhudu a zamaninsa. Malaman Sunnah da dama ne suka yi karatu a wurinsa. Sarki Ma'amun ya naxa shi saboda iliminsa. Ya tava yi wa xan'uwansa Zaidu gargaxi yana tunatar da shi cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tabbatar wa zuri'ar Fatima cewa, Allah ya yi mata alqawarin wuta ba zata ci zuri'arta ba don kamun kan da ita Fatimar ta yi. Ya ce masa: To, me zaka ce ma Manzon Allah idan ka zubar da jinin musulmi, ka qwaci dukiyarsu babu dalili, ka razanar da hanyoyinsu saboda jahilan Kufa sun ruxe ka? A wata riwaya kuma an ce: Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* me ya sa ka sa wa Fatima wannan suna? Sai ya ce: Don Allah ya cire ta ita da zuri'arta daga masu shiga wuta. Ali ar-Ridha ya ci gaba da ce masa: Kasancewar ta kare mutuncinta ba zai hana ka shiga wuta ba in har ka yi zalunci. Wallahi zuri'arta ba su samu wancan

matsayin ba sai don xa'ar Allah. Idan kuwa ka kuskura ka nemi abin da suka samu ta hanyar sava ma Allah, to, kamar kana so ne ka fifita kanka a kansu.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Kuma Sarki Ma'amun ya rubuta sunan Ali ar-Radha akan kuxi, ya aika zuwa garuruwa cewa, a yi masa mubaya'a. ya kuma daina sa baqaqen kaya, ya sanya kore a madadin haka.

Kuma wai, inji xan Shi'ar, a cikin wata qasida da Abu Nawwas ya yi yana yabon sa, ya faxi cewa: Ba za a iya qare yabon ka ba tun da Jibrilu ne da kansa ke hidimar kakanka.

**Martani:**

Ba shakka zuri'ar sayyidina Husaini basu tava gamuwa da musibar da ta fi jinginar da 'yan Shi'ah ke yi gare su ba. yabon da suke masu gara ma zargi da shi. In ba don Ahlus-Sunnah sun san waxannan bayin Allah ba, da an qware su a dalilin maganganun 'yan Shi'ah da za su iya sa a munana zato ga waxannan talikai.

Duk abin da xan Shi'ar nan ya faxi a kan Ali Ar-Ridha ba na kamawa a ciki. Ka ga dai cewar da ya yi, ya fi kowa ilimi da gudun duniya a zamaninsa. Maganar fanko ce wayam; babu hujja ko misqala zarratin akan ta. Duk wanda yake son wani in bai sa tsoron Allah da adalci ba zai iya faxin irin wannan a kansa. Cika baki kuwa ai kowa ma zai iya shi. In ba haka ba, wa zai haxa Ridha ta fuskar ilimi da Shafi'i, da Ishaqa xan Rahawaihi, da Ahmadu xan Hambali da Ashabu xan Abdul Azizi ire-irensu? Ko ina ya yi gudun duniyar irin su Abu Sulaiman Ad-Darani da Ma'aruf Al-Karkhi da ire-irensu?

Kuma cewa, malaman Sunnah da yawa sun yi karatu wurinsa. To, kamar su wa? Ba wani malamin da aka san ya yi karatu wurinsa. Amma in an ce yana da xalibai waxanda ba sanannu ba, wannan abu ne mai yiwuwa, tunda masu neman ilimi duk inda suka samu abin tsinta ba su yin sakaci da shi. Amma a ce ga wani malami da aka sani ya yi xalibta wurinsa ba gaskiya ba ne.

Sai maganar da suke yaxawa cewa, ma'aruf Al-Karkhi ya yi hidima a wurinsa. Kuma ma wai, a hannunsa ya musulunta. Duk irin waxannan kalamai ne da ba su da tushe. Kamar hadisin Fatima da ya kawo da cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi mata alqawarin kare ta da zuri'arta daga wuta don ta tsare mutuncinta. Wannan ba abu ne da aka sani a addini ba, cewa, zuri'ar wani zata haramta ga wuta don shi ya kama kansa. Ballantana kuma irin lafazinsu na ce ma Jibrilu (AS) mai hidimar Manzon Allah. Wannan duk da yake yana nuna kamar sun darajanta Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, amma akwai cin haqqin Mala'iku da rashin sanin girmansu a cikin wannan magana. Amma su 'yan Shi'ah koyaushe irin waxannan waqoqin daxinsu suke ji, har da kafa hujja da su a addini. Wannan ko ba xabi'ar masu basira ga addini ba ce.

### 2.7.6 Muhammadu Al-Jawad

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Imami na gaba shi ne: Muhammadu Al-Jawad, wanda ya bi tafarkin mahaifinsa ta fuskar ilimi da taqawa da baiwa. Kuma a lokacin da mahaifinsa ya rasu, sai Sarki Ma'amun ya nutsa ga qaunarsa saboda iliminsa da addininsa, da kammalar hankalinsa cikin qarancin shekarunsa. A kan haka ne kuma ya so ya aura masa da 'yarsa Ummul Fadhli kamar yadda ya aura wa mahaifinsa da 'yarsa Ummu Habib. Anan ne kuma, inji xan Shi'ar, Abbasiyyawa suka tsananta masa, suka ji tsoron sarautar ta fice daga hannunsu, ta hanyar shi ya yi wa Jawad mubaya'a kamar yadda ya yi wa babansa. Don haka dattawansu suka haxu suka kira shi zuwa ga oda. Suka ce masa, wai, wannan xan qaramin yaro ne da ba shi da karatu. Sai Sarkin ya ce: Na fi ku saninsa. Amma in kuna so ku gwada shi. Sai suka aminta da haka. Anan ne kuma wai, suka ba Alqali Yahaya xan Aksamu kuxi mai yawan gaske don ya qure shi.

Xan Shi'ar ya ci gaba da ba da labari: Wai, sai aka sanya rana da wuri da lokaci. Mutane suka haxu. Sarki ya sa aka kira shi, aka kuma kira Abbasiyyawa. Daga nan sai Alqali ya fara tambayar sa game da hukuncin mai harama in ya yi farauta. Nan take sai Jawad ya ce masa: A ina ya kashe shi; a harami ko a wajensa? Ya san hukuncin yin haka ko bai sani ba? Ya kashe dabbar ne don buqatarsa gare ta ko don ya kare kansa? Qaramar dabba ce ko babba? Cikin dangin tsuntsaye take ko cikin wani dangi na daban?

Sai kawai aka ga Alqali ya rikice, in ji mai xan Shi'ar mai ba da labari. Ya shige gashi har kowa ma ya gane haka a wurin. Sai Sarki Ma'amun ya ce da jama'arsa: Kun fahimci abin da nike gaya muku, wanda kuma kuke musunsa? Sannan sai ya juya kan Imamu Jawad, ya ce masa: Ka shirya neman auren? Imamu ya ce: Na'am. Nan take kuwa ya nemi xiyar Sarki aka ba shi ita a kansadaki Dirhami xari biyar, daidai sadakin kakarsa Fatim. Ya kuma biya naqadan, ta zama matarsa.

**Martani:**

Muhammad Al-Jawad, babu shakka, yana cikin fitattun Hashimawa, masu kwarjini ga idon jama'a. Ga shi kuma karimin mutum. Wannan laqabin nasa ma yana nuni ne ga karimci da sakin hannunsa. Bai yi tsawon rai ba, don a lokacin wafatinsa bai wuce shekaru ashirin da biyar ba (95H-120H). Kuma Sarki Ma'amun ya aurar masa da 'yarsa. Yana kuma aika masa Dirhami miliyan xaya kowace shekara. Sannan Sarki Mu'utasim ya gayyace shi zuwa Bagadaza inda ya zauna can har ya cika.

To, ka ji gaskiyar labari. Amma irin wannan saqaqqen labari na xan Shi'ar ko alama babu qanshin gaskiya a cikinsa. Wannan labarin warin qarya ma yake yi. Don masana sun san Alqali Yahaya ya fi qarfin ya yi tambaya don neman qurewa wai, a kan hukuncin farauta! Kai tafi ma labarin haka yake. To, sai me? Sai ya zan imami don ya jera ma Alqali waxannan tambayoyi? Magana da mai hankali da basira take da daxi. Amma su 'yan Shi'ah kullum irin waxannan labarai su ne hajarsu da suke baje koli. Allah ya sawwaqa.

### 2.7.7 Ali Al-Hadi

Xan Shi'ar ya ce: Imamu na gaba shi ne, Ali xan Muhammad wanda ake ma laqabi da *Askari.* Mutawakkil ya tura shi daga Madina zuwa Bagadaza, daga nan kuma zuwa garin *Surra Man Ra'a*. A can ne ya sauka wani wuri da ake kira Askar, sai aka yi masa wannan suna. Ya ce: Mutawakkil dai ya gargaxo shi ne daga Madina don shi sarkin mai qin Ali ne. Sai ya lura da mutane sun karkata zuwa gare shi ainun, sai ya ji tsoron sa. Ya yi umurni a zo da shi. Mutanen Madina kuwa duk suka fashe da kuka, saboda alherinsa a wurinsu da yawan ibadarsa. Aka dai bincika gidansa ba a samu komai ba sai Alqur'ani da littafan karatu da na addu'oi. Wannan ya sa sai wannan imami ya yi daraja a wurinsa, har ya rinqa yi masa hidima da kansa.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: A lokacin da Yahaya xan Hubairata ya zo da Al-Hadi a Bagadaza sai ya soma da gidan gwamna Ishaqu xan Ibrahim Ax-Xa'i yana mai ce masa: Ka ga wannan jikan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne, kuma ka san halin Sarki. In har ka ba shi shawarar kashe shi, to, da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* zaka kyas ranar Alqiyama. Da suka shiga wurin Sarki kuma, aka ba shi labarin Zuhudunsa da tsentseninsa sai ya mutunta shi. Ana haka kuwa sai watarana sarki Mutawakkil ya yi rashin lafiya. Ya kuwa yi alwashin idan Allah ya ba shi lafiya zai yi sadaka da kuxi mai yawa, amma bai ayyana yawan ba. don haka da ya warke sai ya nemi malamai a Bagadaza babu wanda ya san amsar da zai ba shi. Sai da aka nemi Al-Hadi sannan ya ba shi da cewa, zai yi sadaka da Dirhami 83 domin su ne yawan yaqoqan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma ga shi Allah ya kira da yawa inda ya ce: *Haqiqa Allah ya taimake ku a cikin wurare masu yawa 9:25*. Ya ce: Domin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fita yaqi 27 da kansa, ya tura an yi yaqi ba da shi ba har sau 56.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Mas'udi ya ce, An ba sarki Mutawakkil labarin Al-Hadi na voye makamai, waxanda 'yan Shi'arsa daga garin Qum ke kawo masa. Don haka nan gaba zai yi yunqurin juyin mulki. Wai, sai ya sa wasu turkawa suka shiga gidansa da dare amma ba su samu kome ba. suka tarar da shi ya kulle kansa a wani wuri yana ta karatun Alqur'ani, akan rairayi da tsakuwa, sai aka tungumo shi a haka zuwa wurin sarki, shi kuma a lokacin yana shan giya daa kofinta a hannunsa. Wai, sai sarki ya girmama shi, ya zaunar da shi kusa da shi har ya taya masa shan giyar. Sai Al-Hadi ya ce masa: Yi haquri. Ni ban tava shan ta ba, bale in saba da ita. A nan ne fa, inji xan Shi'ar, Al-Hadi ya yi masa gargaxi mai ratsa zukata, ya karanta masa ayoyin Alqur'ani. Mutawakkil kuwa ya yi ta rusa kuka har sai da ya jiqe gemunsa.

**Martani:**

Wannan magana, ita da ta xazu duk 'yan gida guda ne. Sunan gwamnan ma a yadda ya faxe shi ba haka yake ba, tunda shi bai san tarihi ba.

Sunan gwamnan Bagadaza na wancan lokacin shi ne Ishaq xan Ibrahim Al-Khuza'i. Ba ya da alaqa da qabilar Xayyi' balle a ce masa Xa'i. Kuma fa sanannen mutum ne, xan babban gida; duk masana tarihi sun san shi. Ga ma xan cikinsa ya yi gwamnan Bagadaza a zamanin Mutawakkil xin da bayansa! Kuma xan baffansa ne; Abdullahi xan Xahiru ya yi gwamna a Khurasan. Sannan shi ne wanda ya yi wa Imamu Ahmad sallah lokacin da ya cika. Ya yi gwamna ne tun zamanin Mu'utasim da Wasiq, da wani xan lokaci a zamanin Mutawakkil. Saboda haka wannan gida na Khuza'ata sanannu ne, ba abin da ya haxa su da Xayyi', balle a kira xayansu Xa'i kamar yadda shi xan Shi'ar ya yi.

Sai kuma zancen fatawar da ya ce an yi, wacce ke kware al'aurar jahilcinsa. Wane masani ne zai yarda da wannan fassara da fatawa da ya jingina ma Al-Hadi? Duk ma yaqoqan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba su kai adadin da ya faxi ba. Ba kuma dukan yaqoqan aya ke magana ba; waxanda aka yi kafin Hunainu take magana. A su xin ma, wuraren da aka ci nasara; ba irin Uhudu ba misali. Kuma don ayar ta ce waxannan yaqoqa na da yawa ba ya nuna duk wanda ya yi rantsuwa a kan wani abu mai yawa wannan adadin ne fatawarsa ba. Kana tsammanin a nan kaxai ne Maxaukakin Sarki ya faxi "Mai yawa"? Duba sauran ayoyin Alqur'ani mana gasu nan tari, a cikinsu har da masu nuni ga xari bakwai, da masu nuni ga dubu xari biyu, a kowacce an ce suna da yawa.

Saboda haka, yawan abu, ba ya nufin wani kevantaccen adadi bale an yi hikima da ba da irin wannan fatawa. Wannan fa da a ce maganar tana da wani tushe da za a iya gaskata ta kenan. To, ina kuma ga shi an tabbatar da cewa, sun fesa ta?!

### 2.7.8 Hasan xan Muhammad Al-Askari[1]

Xan Shi'ar ya ce: Imami na sha xaya shi ne: Al-Hasan xan Muhammad Al-Askari, xan wannan da ya gabata. Kuma ya kasance malami, mai gudun duniya, mai yawan kirki da ibada. Shi ne mafifici duk a zamaninsa. Da yawa malaman Sunnah ke ruwaya daga wurinsa.

**Martani:**

Maganarsa a nan ba ta banbanta da sauran maganganun da ya saba yi na cika baki ba, da faxin abin da ba shi aka sani ba. Duk dai malamai sanannu a zamanin wannan taliki an san su, an san riwayoyinsu. Kuma ba mu san xaya daga cikinsu da ya karvo kalima xaya ba daga wurin wannan Askari. Duba fitattun littafan Sunnah guda shida: Buhari da Muslim da Abu Dawuda da Tirmidhi da Nasa'i da Ibnu Majah duk sun rayu a kusan lokacinsa, amma ba wanda ya ce ya ji ko qala daga wannan mutum. Kai qarewa ma, ka duba littafin da Ibnu Asakir ya wallafa wanda ya jera sunayen malaman da aka yi ruwaya

[1] Wannan fasalin ya faxi a cikin taqaitawar Sheikh Gunaiman. Saboda muhimmancinsa muka xauko shi daga asalin littafin *Minhajus-Sunnati*, bugun Darul Hadith, Alqahira, 1425H/2004M (4/39-40).

wurinsu. Ko samatar wannan mutum babu. To, ya za a saurari wannan cika baki wai, Da yawa malaman Sunnah ke ruwaya daga wurinsa?

Haka ita ma cewar da ya yi wai, shi ne mafifici duk a zamaninsa. Mun saba da jin irin wannan tun ba yau ba.[1]

### 2.7.9 Muhammad Xan Hassan (Mahadi-na-Voye)

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Bayan Askari kuma sai xansa; shugabanmu Muhammadu Al-Mahadi amincin Allah ya tabbata a gare shi. Ibnul Jauzi ya riwaito daga Ibnu Umar cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Wani mutum zai bayyana a qarshen zamani wanda sunansa ya yi daidai da nawa, haka ma alkunyarsa. Zai cika qasa da adalci kamar yadda aka cika ta da zalunci. Wancan shi ne Mahadi".

**Martani:**

Abin da malamai suka kawo irin su Xabari da Abdulbaqi da ire-irensu masana tarihi da ilmin dangantaka shi ne cewa, Askari bai tava haifuwa ba. Su kuma 'yan Shi'ah sun ce ya bar cikinsa, amma xan nasa ya vuya tun yana qarami. Wasu daga cikinsu su ce, shekarunsa biyu, wasu uku, wasu ma har biyar. To, irin wannan yaro in har akwai shi, a shari'ar Allah da Manzo ai wajibi ne a sa shi qarqashin kulawar wata macce; uwa ko kaka ko inna, don ta kula da shi ta yi renonsa. Dukiyarsa da ya gada kuma a matsayinsa na maraya dole ne a ba da ita ga maza daga cikin dangin ubansa don su kula da ita. In har babu sai a bar ta a hannun sarki ya kula masa har sai ya girma ya isa aure. Kamar yadda Maxaukakin Sarki ya ce:

﴿وَابْتَلُوا الْيَتَامَىٰ حَتَّىٰ إِذَا بَلَغُوا النِّكَاحَ فَإِنْ آنَسْتُم مِّنْهُمْ رُشْدًا فَادْفَعُوا إِلَيْهِمْ أَمْوَالَهُمْ ۖ وَلَا
تَأْكُلُوهَا إِسْرَافًا وَبِدَارًا أَن يَكْبَرُوا ۚ وَمَن كَانَ غَنِيًّا فَلْيَسْتَعْفِفْ ۖ وَمَن كَانَ فَقِيرًا فَلْيَأْكُلْ
بِالْمَعْرُوفِ ۚ فَإِذَا دَفَعْتُمْ إِلَيْهِمْ أَمْوَالَهُمْ فَأَشْهِدُوا عَلَيْهِمْ ۚ وَكَفَىٰ بِاللَّهِ حَسِيبًا ﴿٦﴾﴾ النساء: ٦

*Kuma ku jarraba marayu, har lokacin da suka isa aure. To, idan kun lura da shiriya daga gare su, to, ku miqa masu dukiyoyinsu. Kada ku ci ta da varna da yin gaggawa gudun su girma (su karvi abarsu) 4:6.*

To, wanda ko kula da kansa ba a xora masa ba da nassin Alqur'ani, ba a kuma yarda a hannunta masa dukiyarsa ba, ina maganar a ce shugaba ne ga musulmi, kuma har wai mutum ba ya zama musulmi sai ya ba da gaskiya da shi?!

---

1 Ire-iren wannan bawan Allah da 'yan Shi'ah ke xaukakawa, waxanda duniyar malamai ba ta ko san da su ba suna da yawa. Shi dai Askari ko a littafan Shi'ah duk da yawan qaryarsu yana da matuqar wuya ka ji sun ce sun samo wani ilimi daga wurinsa. Duba *Biharul Anwar* na Majlisi ga misali wanda, ya cika sifili xari da sha biyar, amma da qyar ka samu riwayar Asakari a ciki. Galibin riwayoyinsa daga Ja'afarus-Sadiq ne, wanda suka fi kowa sha'awar su zuqa ma qarya.

Kuma wannan xan taliki, in har ma Allah ya halicce xin, to, bai amfanin su da komai a duniya ko a addini. Bai tava karantar da kowa bihin ba, ba a kuma tava qarar da hairinsa ba. Ba xaya daga cikin manufofin shugabanci da aka samu ta wurinsa. In da ma akwai shin, to, sharrin da samuwarsa ta haifar ya isa. Don kuwa masu ba da gaskiya da shi ba su more masa ba, masu qaryata shi kuma za su xanxani kuxarsu. To, ina amfanin wannan shugaba?! Wace maslaha zata sa Allah ya halicci wanda yake haka, sai ka ce ba gwanin Sarki ba?!! Tsarki ya tabbatar ma Allah daga yin irin wannan.

Suna iya cewa, ya vuya ne saboda zaluncin mutane. To, amma ai ko a zamanin iyayensa ana zalunci. Me su, basu vuya ba? Kuma ga mabiyansa nan cike da sassan qasa. Me ya hana shi bayyana koda sau xaya a wurinsu, ko kuma ya aiko masu wani xan aike da zai karantar da su wani abu na addini? Kuma ai za iya fakewa wurin wasu magoya bayansa masu qarfi irin na Sham..

In ko har bai iya faxa ma kowa kome saboda tsoronsa, to, ina amfanin kasantuwarsa? Ka ga ai ko Annabawan da aka aiko da mutane basu gaskata su ba, sun dai bayyana ga mutane sun isar da saqo, sun tsayar da hujja akan mutane. Su ko 'yan-sha-biyu ba abin da abin jiran nasu ya tsinana masu sai wahala da damuwa, da qiyayya da mutane, da addu'ar da Allah bai karva. Fiye da shekaru 450 suna abu guda, basu je ko ina ba!

Kai, ya ma sava ma hankali da al'adar da aka sani ga wannan al'umma. Don tun farkonta ba a tava sanin wani ya wuce shekaru 120 ba, balle 450. Imamul Buhari ya riwaito daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yana cewa: "Kun ga daren nan na yau? Duk wanda ke bayan qasa daga yau, ba zai rayu fiye da shekara xari ba".

Idan ya kasance a wancan zamanin ba a wuce shekaru xari, to, ga al'ada daga baya abin ma ragewa zai yi. Domin wannan ita ce sunnar Allah a cikin halitta; shekarunsu suna yi suna ragewa. Nuhu *Alaihis Salamu* shekaru 950 ya yi yana kiran jama'arsa. Adamu *Alaihis Salamu* shi ma sai da ya shekara dubu kamar yadda ya inganta a cikinsunan na tirmidhi. Amma tsawon rayuwa yana ta ragewa kodayaushe. Ya kuma inganta a cikin hadisi cewa: "Tsawon rayuwar al'ummata yana reto a tsakanin shukaru sittin zuwa saba'in. Kaxan ne za su wuce haka".

Sukan kafa hujja da cewa, wai ai Haliru ma yana nan raye. To, wannan hujja gara ma yin shiru da kafa ta. Domin ko wane ne ya yarda cewa har yanzu Haliru na a duniya?! Malamai na gaskiya tun tabbatar da mutuwarsa. Kai, in ma mun sallama; yana raye, to, ai shi ba cikin wannan al'umma yake ba. Shi ya sa ake samun maqaryata daga cikin aljannu da mutane koyaushe suna cewa, su ne Haliru. Waxanda ke ganin su kuma sai su gaskata hakan.

Shi ma Muhammadu xan Hassan; Mahadin 'yan biyu, mutane da dama sun yi da'awar su ne shi. Kuma wannan qarya ba ta banbanta da waccan ga masu basira da hankali.

### 2.7.10 Hadisin Mahadi

Cewar da xan Shi'ar ya yi wai, Ibnul Jauzi ya riwaito daga Ibnu Umar cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Wani mutum zai bayyana a qarshen zamani wanda sunansa ya yi daidai da nawa, haka ma alkunyarsa. Zai cika qasa da adalci kamar yadda aka cika ta da zalunci. Wancan shi ne Mahadi".

**Martani:**

Tun farko dai baku yarda da hadissan Ahlus-Sunnah ba. To, don me za ku kafa hujja da shi? In kun ce, ai don mu kafa maku hujja da hadisan malamanku ne. Sai mu ce, to, ku bari mu kawo maganganunsu.

Sannan kuma wannan hadisi ba ya da wani qarfin da za a kafa hujja da shi. Duk da haka kuma xan Shi'ar ya canza lafazin hadisin, domin in aka karanta shi a yadda ya ke, mu ne za mu kafa maku hujja da shi. Hadisin cewa ya yi: "Sunansa ya yi daidai da nawa. Na mahaifinsa kuma ya yi daidai da na mahaifina". To, shi wannan Mahadin naku ai ba xan Abdullahi ne ba. Ya kuma zo a wani hadisin cewa, daga zuri'ar Hassan yake. Naku kuma jikan Husaini ne.

A wannan wuri dai xan Shi'ar ya yi halinsu da aka san su da shi na maguxi da algussu don voye gaskiya. Ka ga cewar da ya yi Ibnul Jauzi ya riwaito. Ba fa Ibnul Jauzin da duniya ta sani ne; malamin Sunnah ba. Wani Ibnul Jauzi ne xan La'ilaha'ula'i. Sunansa na ainihi Yusufu xan Quzzu. Shi ne wanda ya wallafa wani littafin tarihi mai suna *Mir'atuz Zamani*, da kuma wani littafi akan Imamai goma sha biyu mai suna *I'ilamul Khawasi*. Shi wannan mutum kamar hawainiya ya ke; yana rikixewa ne duk inda ya je. Ya yi rubutu akan darajojin *Khulafa'ur Rashiduna*, ya kuma yi akan zaginsu. Shi xan maula ne kawai da sunan malamai. Wannan shi ne xan Shi'ar ya ke kafa hujja da shi.

### 2.8 Wai Imamai Sha Biyu Sun fi Kowa!

Xan Shi'ar ya qara sharhi bayan kawo waxancan Imamai yana cewa: Waxannan su ne Imamai masu girman daraja, ma'asumai, waxanda matsayinsu a wurin Allah ba ya misaltuwa, don sun kai qolin ga kamala. Sun tsaya inda Allah ya tsayar da su a lokacin da wasu suka shagalta da sha'anin mulki da sharholiya da shaye-shaye. Wanda hakan ta sa suka yi varna da danginsu kamar yadda kowa ya sani. Mu; 'yan Shi'ah ba abin da muke sai Allah ya isa. Inji shi.

Sannan sai ya yi kwaikwayon wani mawaqi xan'uwansa; xan Shi'ah da ke kira ga a jefar da mazhabobin Sunnah gaba xaya don taqaitar madogararsu, a koma ga masu karvo hukunce-hukunce kai tsaye daga Allah ta hannun kakansu!

**Martani:**

Da kuka ce su ma'asumai ne ai baku ba da kowace irin hujja ba sai cika baki da cewa, ai dole ne Allah ya samar da shugaba ma'asumi; wanda ba ya

kuskure ko tuntuven harshe, don hakan ta samar da maslaha da luxufi ga jama'a. Wannan hujjar kuwa yanar gizo ta fi ta qarfi. Shi ya sa kun kasa nuna ma kowa ma'asumin sai Malam-na-Voye wanda bai tava amfaninku ba; ku da kuka yarda da shi, ballantana sauran musulmi da suka xauke shi a matsayin Malam Babu.

Cewa kuma matsayinsu a wurin Allah ba ya misaltuwa don sun kai qolin ga kamala. Wannan shi ma cika baki ne kawai. In wani ma yana so sai ya yi irin wannan cika bakin ga wasu da suka fi su ilimi da daraja daga cikin magabata. Kuma baku da abin da za ku ce masa. Duk wani masanin tarihi yana sane da cewa, Imamanku na goma da na sha xaya (Askari babba da qarami) ba su kai darajar wasu magabatan ba ma na lokacinsu.

Ko kiran su shugabanni da kuka yi. Muna buqatar ku bayyana mana irin shugabancinsu. Suna da qarfi ne na mulki da iko akan jama'a ta yadda ake jin tsoron su? Ko kuwa shugabanni dai ne ta fuskar ilimi da karantar da jama'a? Idan kun ce suna da qarfi to, mun san kuna yaudarar kanku ne. Kuma kun sani in banda Ali daga cikinsu babu wanda ya samu wannan qarfi. Shi xin ma kuma bai same shi yadda ake so ba, tun da kusan rabin al'umma basu tare da shi, ko abin da ya fi haka ko ya kasa. Kai da yawa ma sun yaqe shi. Daga cikin waxanda ke tare da shi kuma wasu suka kauce masa lokacin da zai yaqi waxancan don rashin amincewarsu da yin yaqin. A cikin waxanda suka kauce ma yaqin kuwa akwai da dama da sun fi waxanda suka yi yaqin na kowane vangare.

Idan kuma kun ce, su shugabanni ne ta fuskar ilimi da karantar da jama'a, don haka ya wajaba al'umma ta goyi bayansu. Sai mu ce, ba haka ba ne. Kasancewar mutum ya isa ya yi shugabanci ko limanci ko alqalanci ko jagorancin yaqi ba ta wajabta zamansa haka xin. Sallah kuwa a bayan liman ake yin ta, ba bayan wanda kawai ya cancanci limanci ba. Haka ma alqali mai iko ne ke yanke hukunci. Kuma kwamandan mayaqa shi ke jagoranci ba duk zarumin da yake iyawa ba.

Harwayau muna neman qarin bayani. Kuna nufin waxannan bayin Allah kowanensu ya kamata ya zama shugaba a lokacinsa, shi kaxai? Ko ko a'a, yana cikin waxanda suka cancanta a cikin Quraishawa irin sa?

Zancen da xan Shi'ar ya yi cewa, sun tsaya inda Allah ya tsayar da su a lokacin da wasu suka shagalta da sha'anin mulki da sharholiya da shaye-shaye, ba zancen adalci ba ne. Domin ba wani Ahlus-Sunnah da ya ce ayi koyi da masu sharholiya da varna; sara kai ne ko ba sara kai ba. Amma kasancewar Ahlus-Sunnah suna neman taimako da sara kai a kan abin da suke da amfani a cikinsa, suna kuma taimaka masu a cikin abin da shari'a ta yarda da shi. In har wannan laifi ne, to, 'yan Shi'ah sun fi su yin wannan laifi. Domin su kowa ya san a wurin kafirai suke neman taimako da agaji. Shi kansa wannan malamin da muke taqaddama da shi shaida ne a kan haka, don kafiran *Mugul* da ire-irensu da dama sara kansa ne ta wannan fuskar. Kuma wannan shi ne tarihin 'yan Shi'ah tun daxai.

Muna qara nanata cewa, su waxannan imaman da 'yan Shi'ah ke bi, waxanda suka ce ma'asumai ne, ba su da iko ko xaya na zartar da hukunci. Ba a yin sallar jum'ah, kai ko ma salawatul hamsi bayan xayansu don ba liman ne ba. Ba a neman warware jayayyar fili ko gado ko wata husuma tsakanin 'yan'uwa a wurinsu. Ba su shugabantar jihadi ko hajji, balle su tsayar da haddi ga masu laifi. Mutum kuma ba ya neman haqqinsa kowane iri na zama xan qasa daga wurinsu. Ba su hana 'yan fashi ko varayi wanzuwa. Basu raba ma jama'a dukiyar baitul-mali. Iyakacinsu yin fatawa kamar yadda sauran malamai ire-irensu suka kasance suna yi. To, duk wanda yake neman wani abu irin wannan kuma ya tasar ma wanda ba shi da iko ai sunansa wawa. Wanda ya nemi abu daga mai shi, mai iko a kanshi, shi ne mai hankali.

Sannan malamin ya yi tsaga da faxi a cikin tuhumar da ya yi ma sarakuna. Domin kuwa kowa ya san a cikinsu akwai na kirki irin su Umaru xan Abdulazizi da sarki Mahadi. Da yawan waxanda ake tuhuma da savo a cikinsu kuma ba a bayyane suke yi ba. Wasunsu suna da zunubbai, amma akwai yiwuwar sun tuba, ko sun samu ladar da zata kankare zunubin nasu, ko Allah ya jarabce su da wani abin da ke kankare laifinsu. Abin da ya kamata a sani shi ne, su sarakuna ayyukansu na lada manya ne, haka ma zunubansu. Ba daidai suke da xaixaikun musulmi ba. Ina ko zaka haxa talaka mai qoqarin ibada gwargwadon qarfinsa da wanda ke tsayar da dokokin Allah akan al'umma, ya hana savo, ya qarfafi ayyukan alheri da yawa, ya yaqi kafirai, ya sadar da haqqoqan mutane da dama zuwa gare su, ya kwatanta adalci, ya hana da yawa daga cikin zalunci?!

Mu, bamu tava cewa sarakuna basu savo ko aikata zunubi ba. Kamar yadda sauran gama-garin musulmi duk suke, haka su ma sarakuna. Amma wa ya ce in mutum na zunubi an gama zaman lafiya da shi, kuma ba a taimakon sa a inda yake akwai maslaha da alheri a ciki?

'Yan Shi'a na iya cewa, imamansu na da wani voyayyen ilimi da babu shi a wurin kowa! To, ina amfani voyayyen ilimi da ba a bayyana shi? Me ya raba shi da taskar kuxi da aka tsuke ta ba a ba kowa? Ya za a kira mutane ga bin wanda bai iya karantar da su kome irin Malam Babu na 'yan Shi'ah?

In ko har suka ce, a'a, suna bayyana ma kevantattun mutane ne da suke da kusanci da su, to, mun san qarya suke yi. Dubi Ja'afar As-Sadiq, wanda malamai irin su Malik da Sufyanu xan Uyainata da Shu'ubatu da Sufyanus-Sauri da Ibnu Juraiju da Yahaya xan Sa'idu da ire-irensu daga cikin mashahuran malamai suka yi karatu wurinsa. Wa zai yarda cewa, As-Sadiq ya voye ma waxannan taurari wani karatun da ya bayyana ma jahillai, da al'umma ba ta ko san da zamansu ba?! Babu shakka waxannan malamai da muka ambata da ire-irensu sun fi qaunar Allah da Manzo da kishin tsare addini da isar da shi ga al'umma da son masu son Allah da qiyayya da masu qin sa fiye da shaihunan Shi'ah. Wannan ko shi ne halin 'yan Shi'ah a kowane zamani. Mutum ya duba lokacinsa. Ga wannan xan Shi'ah da muke magana a kansa. Suna ganin shi ne mafificinsu a wannan zamani. Amma in ya furta wata

magana ko kare ba ya ci ba. Sai ya nace a kan maganar da duk mai hankali ya san qarya ce. To, in ya sani ya ya yima Allah da Manzonsa qarya? In kuma bai sani ba ai iya qurewar jahilci kenan.

## 2.9 Malaman Sunnah Sun fi Qarfin Zargi

A qoqarinsa na xaukaka alqadarin mazhabarsa, xan Shi'ar ya zargi Ahlus-Sunnah yana mai cewa: Babu wani mutum xaya daga cikin Ahlus-Sunnah in dai ya san inda kansa ke ciwo, kuma ya kalli mazhabobi da idon basira, sai ya zavin mazhabar 'yan-sha-biyu ya bar saura. Amma ta kan yiwu ya voye, ya bayyana akasin haka don neman abin duniya. Tun da an gina masu makarantu da cibiyoyi don su ci gaba da yin farfaganda ga sarakunan Banul Abbas, su sanya qaunarsu cikin zukatan mutane.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Sau da yawa ni kan ga cikinsu wanda yake ibada ta hanyar Shi'anci irin na Imamiyyah ('yan-sha-biyu), amma ba ya bayyana shi don kwaxayin abin duniya. Na ma tava ganin wani shugaba a mazhabar Hambali yana iqirarin shi xan sha biyu ne. Sai na ce masa: "To, don me kake karantar da Hambaliyyah?" Sai ya ce, "Don wurinku ba masqi!" Kuma babban malamin Shafi'awa a wannan zamani da zai mutu wasicci ya yi da wasu muminai (yana nufin 'yan Shi'ah) su yi masa wanka. Ya kuma nemi a rufe shi a maqabartar Kazim ta 'yan Shi'ah. Har ma kuma ya kafa shedu a kan zai mutu bisa mazhabar Shi'ah!

**Martani:**

Ko shakka babu wanda yake furta wannan magana bai fita daga xayan biyu; ko dai bai san su waye Ahlus-Sunnah ba, ko kuma maqaryaci ne na gidi. Yaushe ne aka kafa makarantu da cibiyoyi? Sunnah ta riga su kafuwa da nisa. A Bagadaza ne aka fara gina makarantu a cikin qarni na biyar. Kamar makarantar *Nizzamiyyah* an kafa ta a kusan shekarar 460H. Kuma akan mazhaba xaya kacal manhajarta ta ke. A lokacin ma duk mazhabobin Sunnah sun gama yaxuwa a gabascin duniya da yammacinta. Kuma babu wanda yake da makaranta a cikinsu. Malikawa kuma da ke yamma ai basu ko ambaton sarakunan Banul Abbas, balle su yi kira ga a so su.

Kai, a haqiqanin gaskiya ma Sunnah ta fi qarfi kafin kafa daular Abbasiyyah. Domin a zamanin Abbasiyyar ne 'yan Shi'ah da wasu 'yan bidi'a irin su suka fara miqe qafafu. Kuma ba wani Ahlus-Sunnah da ya ce halifanci kayan gidan Abbas ne kamar yadda 'yan Shi'ah kuka ce gadon gidan Ali ne. A wurin malaman Sunnah duk Baquraishe in yana da cancanta ana iya ba shi, Alawi ne ko Abbasi ko Umawi ko ma ba su ba. Zargin magabata shugabannin mazhabobin Sunnah da fadanci ko zargi ne maras tushe. Su malamai ne 'yan "Sunnah sak"! Amma suna ganin halifofi huxu na farko da gashi, ga shi ko babu xan gidan Abbas a cikinsu.

Duk mai hankali ya san ba a samun xan sha biyu cikin malaman Sunnah. Domin sun fi kowa ganin wautarsu da jahilcinsu da vatan kansu. Kai

sun fi kowa nisa daga shiriya. Dole ne a qyamace su, don sun haxa duk sharrin da ke cikin sauran qungiyoyin bidi'ah, kamar *Jahamiyyah* da *Qadariyyah*. Waxannan kuwa kowace ta samu rabonta na zargi da suka daga bakunan magabatan al'umma.

Wallahi, duk da yawan nazarce-nazarcena ga maganganun malamai na Sunnah da na Shi'ah ban tava ganin wanda ake zargi da zama xan Shi'ah Imamiyyah daga cikin mutanen kirki ba, balle ko a ce yana qudurta ta a voye. Amma ka ga Zaidiyyah, an tuhumci Hasan xan Salihu xan Hayyu da yin ta. Ga shi ko malami ne na kirki, mai gudun duniya. Amma babu wanda ya ce ya soki Abubakar ko Umar balle ko a ce bai yarda da halifancinsu ba. Daman su Zaidiyyah ba su wannan. Kuma ko 'yan Shi'ah na farko babu wanda aka zarga cikinsu da ganin fifikon Ali a kan Abubakar da Umar. Suna dai son sa. Kuma cikinsu akwai masu fifita shi a kan Usman. Kuma ko cikin jama'ar Ali xin, waxanda suka taya shi yaqi ba kowa ne ke ganin ya fi Usman ba.

Game da maganarsa kuwa, wai ya ga malaman Sunnah fitattu waxanda a voye 'yan Shi'ah ne. Sai mu ce masa: Ku ne duniya ta san kuna wannan xabi'a; ku shiga cikin musulmi ku voye aqidarku, kuna ganin wannan wani abin neman kusanci zuwa ga Allah. Kuma a cikin musulmi a kansamu munafuki. To, ina abin mamaki don an samu munafikin xan Shi'ah ya saqe jiki cikin almajiran wata mazhaba ta Sunnah? Wanda ya kafa hujja da irin waxannan munafukai akan vacin aqidar Sunnah shi ne jahili.

### 2.9.1 Malaman Sunnah ba su Ta'assubanci

Xan Shi'ar ya ce: Su dai 'yan-sha-biyu ba su da ra'ayin riqau ga abin da ba gaskiya ba. Savanin Ahlus-Sunnah. Misali a nan shi ne Imamul Ghazali da Mawardi daga cikin malaman Shafi'iyyah sun tafi a kan cewa, daidaita qaburbura shi ya yi daidai da shari'ah. Amma saboda 'yan-sha-biyu sun mayar da shi al'ada mun bar shi. Za mu rinqa xaga qaburburanmu zuwa sama. Kuma wai, Zamakhshari daga cikin malaman Hanafiyyah ya fassara faxar Allah Ta'ala da ya ce: *(Allah) Shi ne wanda yake yin salati akan ku da Mala'ikunsa Ahzab :43*. Zamakhsharin ya ce: Ya halalta bisa ga wannan aya ayi salati ga xaixaikun musulmi. Amma saboda 'yan-sha-biyu suna yi wa imamansu salati sai muka hana.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Mai littafin *Al-Hidaya* daga cikin Hanafiyyawa ya ce, sanya zobe a hannun dama shi ne Sunnah. Amma tunda 'yan-sha-biyu na yin sa to, mun mayar da shi hagu. Ire-iren wannan na da yawa, inji shi. Ya kuma ci gaba da cewa: "Duba wanda ke canza shari'ah, ya musaya hukuncin da Annabi ya sanya don kawai yana adawa da wasu mutane. To, ina dalilin bin wannan da xaukar maganarsa?"

**Martani:**

Duk waxannan maganganu da xan Shi'ar ya yi sun fi dacewa da a mayar masa da su. Domin Allah ya tsarkake malaman Sunnah daga irin wannan.

A haqiqanin gaskiya, bamu tava sanin wata qungiya mai ra'ayin riqau ga qarya kamar 'yan-sha-biyu ba. Su ne waxanda aka san suna shedar zur idan shari'ah za ta hau kan xan Shi'ah irin su. Wane ta'assubanci ma ya wuce qarya? Su ne fa suka ce, wai, 'ya macce na gadon duk dukiyar ubanta, don su kori Abbas daga magadan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, su bar Fatima ita kaxai! Kuma a cikinsu akwai masu haramta cin naman raqumi, wai, don Nana A'ishah ta hau kansa a ranar yaqin basasa. Suka sava ma Alqur'ani da Sunnah da ijma'in Ahlul-Baiti da malaman Sunnah don bin son ransu. Abin da kowa ya sani ne cewa, koda wancan raqumin da Nana A'ishah ta hau yake a raye ba za a haramta hawansa a Shari'ah ba. Domin kuwa ko kafirai da suka hau dabbobi ba a haramta hawansu ba, balle cin namansu.

Kai, ta'assubancin 'yan Shi'ah ya kai ga suna qyamar lamba 10 don kauce ma mutane goma da Allah ya yi wa bushara da aljanna. Sai ka ji sun ce, tara da xaya. Suna qoqarin kada su yi komai ya dace da goma saboda haka.

Don tsananin ta'assubancinsu ma, in suka ga mai suna Ali ko Ja'afar ko Hasan da Husaini sai suna zanzari wajen girmama shi koda fasiqi ne. Dubi kuma yadda suka kafa ma Banu Umayyata qahon zuqa don wasu daga cikinsu sun kasance suna qyamar Ali. Alhali kuwa akwai mutanen kirki da dama daga cikin Banu Umayyata waxanda sun mutu tun kafin faruwar fitinar da ta gudana. Hasali ma babu wata qabila da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yawaita sanyawa cikin aikin gwamnati kamar su. Kamar yadda ya shugabantar da Attabu xan Usaidu akan Makkah. Ya kuma shugabantar da Khalidu xan Sa'idu da 'yan'uwansa Abanu da Sa'idu a wasu wurare daban. Haka kuma ya shugabantar da Abu Sufyan xan Harbu xan Umayyata ko xansa Yazidu akan Najran. Har Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya cika kuwa yana gwamna a wurin. Sannan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya aurar da 'ya'yansa mata uku ga dangin na Umayyata. Domin babbar 'yarsa Zainab ya aurar da ita ne ga Abul Asi xan Rabi'u, wanda Annabi ya yabe shi a lokacin da Ali ya so ya auri xiyar Abu Jahali. Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya nuna jin daxinsa da surukutar Abul Asi, kuma ya qara da cewa: "Ya faxa mani magana ya yi gaskiya, ya kuma yi mani alqawari ya cika". Sannan ya aurar da Ruqayyatu da Ummu Kulsumi ga sayyidina Usman. Duk waxannan 'yan gidan Umayyata ne.

Yana daga cikin jahilcin 'yan Shi'ah, qyamar da suke ma mutanen Sham gaba xaya, domin can farko an samu waxanda ba su son Ali *Raliyallahu Anhu*. To, ai ko Makkah an yi lokacin da kafirai ke a cikinta; waxanda ba su son Manzo. A Madina ma kuma an yi munafukai. Amma a halin da ake ciki yau, babu mai qyamar Ali ko xaya a Sham. To, don me suka tsane su?

Haka ma suna jin haushin duk wanda ya yi amfani da wani abu da ya rage na Banu Umayyata kamar shan ruwan rijiyar Yazid. Alhalin Yazidu bai ma gina rijiyar ba, ya dai yalwata ta ne kawai, sai aka kira ta da sunansa. Basu kuma son a yi sallah a masallacin Banu Umayyata. In don Banu Umayyata sun gina shi ne kuwa, ai Ka'aba mushrikai suka gina ta, amma Annabi *Sallallahu*

*Alaihi Wasallama* ya yi sallah a cikin ta. Kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai tava qin shiga gidajen da suka gina, ko ya qi shan ruwan rijiyar da suka haqa, ko sa tufan da suka saqa ko kashe kuxin da suka buga ba. To, wannan kafirai kenan fa; ina ga musulmi?!.

Wani amintacce ya bani labarin wanda yake da kare a cikinsu, sai aka kira karen nasa Bukairu, sai nan take ya fusata, wai an sa ma karensa sunan ‘yan wuta. Wal iyazu billahi. A dalilin haka suka yi ta faxa har abin ya kai aka zubar da jini. Wa ya fi mai yin wannan ta’assubanci da wauta?.

Su dai malaman Sunnah daxai ba su ce abar wani abu da shari’ah ta yarda da shi don wani xan bidi’ah ya aikata shi ba. Ka ga maganar daidaita qabari da ya yi. Mazhabar Abu Hanifa da Ahmad ita ce xaga shi ya fi. Hujjarsu kuwa ita ce, haka aka yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kuma suka ce, hakan ya fi nisantar da shi daga kama da gine-ginen duniya, kuma yana taimakawa wajen hana a zauna a kansa. Amma Imamus-Shafi’i sai ya so a shafe shi; ya ce mustahabbi ne. Domin akwai dalilai da suka nuna haka. Wasu daga cikin almajiransa suka ce, ai yin haka xabi’ar ‘yan Shi’ah ce, don haka suka karhanta. Amma akasarin almajiransa suka ce ba haka ba ne; mustahabbi dai ne ko ‘yan Shi’ah na yinsa.

Haka shi ma bayyana karatun bismillah shi ne mazhabar ‘yan-sha-biyu. Kuma a kan wannan ne da maganar qunutin asuba wasu suka yi magana akan Imamus-Shafi’i, saboda abin ya shahara a Iraqi garin ‘yan Shi’ah. Amma duk da haka, shi Imamus-Shafi’i bai daina ba tunda yana ganin shi ne Sunnah. To, ka ga ba wani malamin da ya tava barin Sunnah saboda wai wasu ‘yan bidi’ah irinku na yin ta.

### 2.9.2 Addu’a ga Halifofi Cikin Huxuba

Sannan xan Shi’ar ya ce: Su dai Ahlus-Sunnah sun qago bidi’oi da yawa a cikin addini alhlai suna sane. Kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Kowace bidi’ah vata ce. Kuma kowace vata makomarta wuta”. Ya kuma ce: “Duk wanda ya shigar da wani baqon abu a cikin addininmu to, ya yi ta banza”. Kuma ko an so a hana su waxannan bidi’oi ba su bari. Kamar addu’ar da suke ma halifofi a cikin huxuba, wadda ba ta da asali a cikin addini. Kuma ba a yi ta ba a zamanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da zamanin Sahabbai ko na Tabi’ai. Kai, ko ma zamanin Banu Umayyata da Banul Abbas ba a yinta. Sarki Mansur ne ya qago ta don ya musguna ma Alawiyyah sa’adda ya yi wata hatsaniya da su. Ga shi ko Ahlus-Sunnah na yinta har ila yaumina haza.

**Martani:**

Yana da kyau a rinqa ba ilimi da tarihi haqqinsu. Shi dai yin addu’a ga halifofi huxu a kan mimbari abu ne da tarihi ya tabbatar da an yi shi tun zamanin Sarkin Musulmi Umaru xan Abdulazizi. Dalilin yin sa kuwa shi ne, don kariyar martabar sayyidina Ali da wasu ‘yan kazagin Banu Umayyata suka

fara zagi a cikin huxubobinsau. Saboda adalcinsa sarki Umaru xan Abdulazizi ya ce a musanya wannan da yin addu'a da fatar alheri ga halifofi huxu shiryayyu, cikinsu har da Ali. Ya yi haka ne kuwa a matsayin wani salo na kawar da waccan mugunyar al'adar da ya ji tsoron yaxuwarta.

Kuma tuhumar da ya yi wa sarki Mansur ba ta da makama. Domin ba wata musgunawa ga Alawiyyawa don an yi ma Abubakar da Umar da Usman addu'a an haxa da Ali. Tunda daman sun riga shi yin halifanci kuma ban yi jayayya da su ba. Ba kuma wani Ahlus-Sunnah da ya ce yin wannan addu'a farilla ne a cikin huxuba. Bidi'ah kam sananna ita ce, yi wa Ali shi kaxai addu'a ko ambaton imamai goma sha biyu da 'yan shi'ah suka naxa. Kamar yadda zagin Ali ko duk wani magabaci a cikin huxuba yake bidi'ah mummuna.

Sanannen abu ne dai cewa, halifofi uku na farko al'umma ta haxu a kan naxinsu. Kuma a zamaninsu kafirai sun xanxana kuxarsu, musulmi sun zauna lafiya. Shi kuma na huxu ya zo bisa qaddarar Allah a lokacin fitina, musulmi basu haxu a kansa ba, ba su kuma zauna lafiya da juna ba. Don haka kafirai sun ci karensu babu babbaka a lokacinsa. To, ka ga faxinsa shi kaxai cikin huxuba a bar waxancan uku babu bidi'ar da ta wuce shi.

### 2.9.3 Shafar Qafa Wajen Arwalla

Xan Shi'ar ya ce: Ahlus-Sunnah sun canza nassin da Allah ya tabbatar na shafar qafafu a wajen arwalla madadin wanke su, inda Allah ya ce: *Sai ku wanke fuskokinku da hannayenku zuwa ga magincirori, kuma ku yi shafa ga kanunku da idanun sau. 5:6.* Kuma Ibnu Abbas ya ce: Gava biyu ake wankewa, biyu kuma ake shafawa. Amma suka canza suka wajabta wanke qafafu.

**Martani:**

Adadin waxanda suka ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yana arwalla, da waxanda suka koya daga wurinsa da waxanda suka yi a zamaninsa har ya gani da idonsa sun fi yawa akan adadin waxanda suka karantar da wannan aya. Domin duk musulmi suna arwalla. Kuma sun gan shi yana yin ta sau shurin masaqi. Kuma gaba xayansu sun gan shi yana wanke qafafu. Har ma sun ce, ya tsoratar da waxanda wankinsu bai yi ba da cewa, wuta zata wanke dugaduganšu.

Kuma su matsalar 'yan Shi'ah ita ce, ba su da cikakkiyar fahimtar Larabci. Don ita wannan aya sam bata sava ma aikin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba; ta yi daidai da shi. Sannan abin al'ajabi shi ne, duk bayan wannan 'yan Shi'ah su ce ba a shafa a kansafa wadda ta tabbata daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikinsunnah mutawatira. Wai suna ganin yin haka ya sava ma Alqur'ani, su da Harijawa. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuwa shi ne wanda yake fassara Alqur'ani.

## 2.9.4 Mutu'ar Hajji da ta Aure

Xan Shi'ar ya ce: Haka kuma Ahlus-Sunnah sun haramta mutu'a biyu da Alqur'ani ya zo da su; Mutu'a hajji da Allah ya ce: *To, wanda ya ji daxi da Umra zuwa Hajji, sai ya biya abin da ya sauqaq na hadaya 2:196.* Kuma da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rasa samun yin wannan mutu'a ba saboda ya yi qirani sai da ya yi nadama a kan haka. Sai kuma mutu'ar aure da Allah ya ce: *Kuma abin da kuka ji daxi da shi daga gare su, to, ku ba sadakinsu bisa farilla 4:24.*

Xan Shi'ar ya ce: Kuma waxannan mutu'oi biyu, musulmi sun ci gaba da gudanar da su tsawon zamani rayuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da halifancin Abubakar da Umar. Haka kawai watarana sai Umar xin ya hau mimbari ya haramta su. Kuma ya ce, duk wanda ya yi su zai to, jikinsa zai gaya masa.

**Martani:**

Ita dai mutu'ar Hajji da Umrah duk musulmi sun haxu a kan halalcinta. Kuma qarya ne a ce Ahlus-Sunnah sun haramta ta. Da yawan malaman Sunnah na ganin mustahabbi ce. Akwai ma masu rinjayar da ita da masu ganin ta wajibi.

Ita ko mutu'ar aure ba ta a cikin ayar da ya karanta. Ayar dai tana magana ne akan matar da aka xaura ma aure aka kuma ji daxi da ita ta cancanci sadakinta duka. Savanin wadda aka xaura ma aure ba a ji daxi da ita ba wadda ta cancanci kawai rabin sadakinta. Saboda haka ayar ba tana magana kan kowane irin jin daxi da macce ne ba, sai fa jin daxi na halas. Kuma malamai sun haxu a kan bata sadakinta duka idan aure ya tabbata koda vatacce ne. Amma wanda ya ji daxi da ita ta hanyar haram ba wani sadaki da Allah ya ce a ba ta.

Maganar cewa Umar ya haramta mutu'ar aure ba gaskiya ba ce. Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ya haramta ta bayan a da mutane na yin ta. Sayyidina Ali ne ma ya bayyana wannan Sunnah ga Ibnu Abbas da bai sani ba. Ya ce masa: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya haramta auren mutu'ah da cin jakin gida a ranar Haibara. Kuma ya tabbata a cikin Sahihu Muslim cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya haramta ta a ranar da aka ci Makka haramci na har abada.

Ita kuma cewar da sayyidina Ali ya yi: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya haramta auren mutu'ah da cin naman jakin gida a ranar Haibara. Wasu malamai kamar su Ibnu Uyainata na ganin yana nufin ranar Haibara ranar haramta jakin gidan ce. Amma shi auren mutu'ah a ranar buxa garin Makkah aka haramta ta. Wasu kuma na ganin ranar buxa Makkah haramtawa ta biyu ce. Don haka suke cewa, an haramta ta, sannan aka halalta, sai aka sake haramtawa daga qarshe. Akwai ma har masu cewa, an sake halalta ta kafin ranar Fatahu Makkah, sannan a ranar aka yi mata haramci na qarshe. Amma maganar can ta farko ta su Ibnu Uyainata tafi qarfi cewa, mutune suna yin

mutu'ah ba a kuma hana su ba sai ranar buxa Makkah. Daga nan kuma ba wani halalci da ya zo akan ta. Shi kuma Ibnu Abbas da ya yi fatawa akan halaccinta da na cin naman jakin gida bisa ga rashin sani, sai sayyidina Ali ya ankarar da shi ga haramcin da ya tabbata daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Don haka, Ahlus-Sunnah su ne suka bi Ali da sauran halifofi a cikin abin da suka cirato daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Su kuma 'yan Shi'ah sun sava ma Ali, sun bi wani ra'ayi na qashin kansu.

Ka ga ai a cikin Alqur'ani mata biyu Allah ya halalta; matar aure, da baiwa. Ita kuma matar mutu'a ba matar aure ba ce, don ba ta gado, ba a sakin ta, balle a ba ta rabin sadaki idan an yi shi kafin baiko. Sannan ba ta idda. Waxannan hukunce-hukuncen kuwa su ne Allah ya tabbatar ma matan aure cikin Alqur'ani. Sannan ita ba baiwa ba ce. Ka ga ta tabbata haramtacciya. Tunda Allah Ta'ala ya ce: *Kuma waxanda su masu kariya ne ga al'aurarsu. Sai fa akan matan aurensu ko abin da damansu ta mallaka (na bayi). To, su haqiqa ba waxanda ake zargi ba ne. To, duk wanda ya nemi (jin daxi) bayan wannan, to, su ne masu tsallake iyaka. Mu'minun:5-7.*

### 2.9.5 Ba a Cin Gadon Annabawa

Sai kuma xan Shi'ar ya zargi sayyidina Abubakar *Raliyallahu Anhu* yana mai cewa: Abubakar ya hana Fatima gadonta. Sai ta ce masa: Kai xan Abu Quhafata! Kai zaka gaji ubanka, ni ban gaji nawa ba? Wai sai Abubakar ya lava ga wata riwaya da kowa bai san ta ba in ba shi ba. Alhalin kuma shi ne abokin jayayyarta, don shi yana cin sadaka. Ya kawo mata hadisin da Alqur'ani ya qaryata shi. Ya ce wai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Mu Annabawa ba a gadonmu. Duk abin da muka bari sadaka ne". Alhalin kuwa Allah Ta'ala na cewa:

﴿ يُوصِيكُمُ ٱللَّهُ فِىٓ أَوۡلَـٰدِكُمۡۖ لِلذَّكَرِ مِثۡلُ حَظِّ ٱلۡأُنثَيَيۡنِۚ ﴾ النساء: ١١

*Allah yana yi maku wasicci a game da 'ya'yanku. (Idan kun mutu) namiji zai gadi rabon mace biyu 4:11*

Kuma Allah bai sanya wannan ga sauran al'umma banda Manzo ba. Sai ya qaryata riwayarsu. Kuma Allah ya ce:

﴿ وَوَرِثَ سُلَيۡمَـٰنُ دَاوُۥدَۖ ﴾ النمل: ١٦

*Kuma Sulaimanu ya gadi Dawuda*

Ya kuma ce:

﴿ وَإِنِّى خِفۡتُ ٱلۡمَوَٲلِىَ مِن وَرَآءِى وَكَانَتِ ٱمۡرَأَتِى عَاقِرً۬ا فَهَبۡ لِى مِن لَّدُنكَ

وَلِيًّ۬ا ۝٥ يَرِثُنِى وَيَرِثُ مِنۡ ءَالِ يَعۡقُوبَۖ ﴾ مريم: ٥ – ٦

*Kuma haqiqa ni, na ji tsoron dangi a bayana, kuma matata ta kasance bakarariya (maras haifuwa)! To,*

*ka ba ni wani mataimaki daga wajenka. Ya gaje ni, kuma ya yi gado daga gidan Yaquba 19:5-6*

**Martani:**

Cewar da ya yi wai, Nana Fatima ta ce wa Abubakar: "Kai za ka gaji ubanka, ni ba zan gaji ubana ba?". Ba maganar da aka san ingancinta ba ce. Da ta inganta kuwa, ba za ta zama hujja ba. Domin babu shakka babanta *Sallallahu Alaihi Wasallama* yana da nisan banbanci da nasa. Ya ko za a yi wannan gwaji? Ai su Annabawa Allah ya kare su daga a gaji duniya daga wurinsu. Don kada wannan ya zama marataya ga masu son zarginsu. Amma irin Abubakar sai ya gaji mahaifinsa lamui lafiya ba wata damuwa. Kamar yadda Allah ya kare Manzonsa daga iya rubutu ko tsara waqa, ba don hakan tana aibi ga sauran jama'a ba; sai don toshe qofar zargi.

Cewa kuma wai, Abubakar ya lava ga wata riwaya da shi kaxan ya zo da ita, zargi ne da ba shi da qamshin gaskiya. Domin hadisin da ya bayyana ba a gadon Annabawa ba Siddiqu ne kawai ya karantar da shi ba. An same shi daga Umar da Usman da Ali da Xalhatu da Zubairu da Sa'adu da Ibnu Aufi da Abbas da matan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Abu Hurairata. Kuma riwayoyinsu na nan cikin sanannun littafai ta hanyoyi ingantattu. Masana sun san da haka. Ya rage ma mai wannan zargi xayan biyu; jahilci ko katovara.

Ya kuma ce wai, Abubakar ne abokin jayayyarta. Ba kuwa haka ba ne. Don Abubakar bai ce shi zai ci gadon ko iyalansa ba. Cewa ya yi sadaka ce ga musulmin da suka cancanta. Ba shi kuma cikin masu karvar sadakar don ba shi da buqata da ita. Haka ma iyalansa ba su tava amfanuwa daga gare ta ba daxai saboda wadatarsu. Wannan yana daidai da wani attajiri ya yi shaida cewa, wani ya yi wasicci da wata sadaka ga talakawa. Ba abin da zai hana a karvi shaidarsa a nan, don shi ba abin tuhuma ba ne. Kai, koda yana da wani amfani a cikinta, in ya riwaito ana karva, don ba shaida ba ce; riwaya ce. Riwaya kuma hukunce ne da yake game kowa, a wannan mas'ala ko wata irinta har abada. To, ina kuma ga shi Sahabin Manzo! Ai wannan kamar ganin wata ne. Wanda zai gan shi yana cikin waxanda hukuncinsa zai hau kansu amma ba shi kaxai ba.

Kuma ka ga riwayar nan hukunci ne na Shari'a wanda ya haramta gado har ga matan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* cikinsu har da 'yar Abubakar. Ya kuma haramta a sayar ballantana ko shi Abubakar ko wani ya saya.

Sai maganar wai, wannan hadisi ya sava ma Alqur'ani. Ka ga dai ita ayar ba inda ta ce Manzo zai bar gado. To, tunda Sunnah ta tabbatar da ba a gadon nasa, ga kuma Sahabbai sun yi ijma'i a kan haka, ina rikici a nan? Ko ka ji wani cikin sauran magadan ya nace akan neman gadon? Gonar kuma ai ta kai zamanin Ali amma bai raba ta ba alhalin akwai sauran magada, da magadan magada. Ayoyin da ya kawo na gadon su Annabi Sulaiman da Annabi Yaqubu gadon ilimi da Annabta da mulki ake nufi. Ai daman ba wata fa'ida a ce xa ya gaji uba in dukiya ce ya gada. Daman kowa na gadon dukiyar ubansa.

Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Lalle Annabawa ba su gadar da dirhami, ko dinari. Suna gadar da ilimi ne. Saboda haka, duk wanda ya riqe shi to, ya yi riqo da babban rabo”. Abu Dawuda ya riwaito shi da wasu ba shi ba.

To, wannan shi ne. Ka ga ai gadon kuxi ba wani abin yabo a cikinsa. Ita kuma wannan aya ta zo ne da yabon Sulaimana *Alaihis Salamu.* Amma cewa, Sulaimana ya gadi dukiya daga mahaifinsa Dawuda kamar wani ya ce ne, wane ya ci abinci, ya yi bacci. Ba irin labaran Alqur’ani ba ne wannan.

### 2.9.6 Fatima ta Nemi Gonar Fadak

Xan Shi’ar ya ce: A lokacin da Fatima ta gaya masa cewa mahaifinta *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ba ta kyautar Fadak, sai ya ce, ki zo da wani mutum baqi ko ja don ya shede ki a kan haka. Sai ta zo da Ummu Aimana ta sheda cewa haka ne. Sai ya ce mata: Mace ce wadda ba a karvar maganarta. Ga shi kuma duk sun riwaito cewa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Ummu Aimana mace ce ‘yar aljanna”. Sai Ali ya yi sheda cewa maganar gaskiya ce. Sai Abubakar ya ce: Wannan mijinki ne. Yana son abin ya koma masa, ba za mu yi maki hukunci da shaidarsa ba. Ga shi ko duk sun riwaito cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Ali na tare da gaskiya, gaskiya kuma na tare da Ali, tana juyawa duk inda ya juya. Ba za su rabu ba har su zo wurina a qoramar Alkausara.

Xan Shi’ar ya ci gaba da cewa, sai, Fatima ta yi fushi a kan haka, kuma ta tafiyar ta. Ta rantse ba za ta sake magana da Abubakar ko abokinsa ba har sai ta haxu da babanta ta yi qarar su, gare shi. To, a lokacin da zata rasu, inji shi, sai ta yi wa mijinta Ali *Raliyallahu Anhu* wasicci cewa, ya rufe ta da dare, don kada xayansu ya yi mata sallah.

Xan Shi’ar ya ci gaba: Dukansu sun riwaito cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Ya Fatima! Allah Ta’alah yana fushi don fushinki, kuma yana yarda don yardarki”. Kuma duk sun riwaito cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Fatima sashena ce. Wanda ya cuta mata ya cuta mani, wanda ya cuta mani kuwa ya cuta wa Allah Ta’alah”.

Ya ci gaba da cewa: Da wannan labarin gaskiya ne, to, da bai hallata Abubakar ya bar alfadari da takobi da rawanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a wurin Ali *Raliyallahu Anhu* ba, a lokacin da Abbas ya nemi a ba shi su. Kuma da Ahlul-Baitin da Allah Ta’alah ya tsarkake su cikin littafinsa sun aikata abin da ba ya halatta, don an haramta masu sadaka amma sun neme ta. Bayan haka ne kuma Jabiru xan Abdullahi ya zo ya ce wa Abubakar: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce mani: Idan dukiya ta zo daga Bahraini to, zan xibar maka cikon tafina har sau uku. Sai Abubakar ya ce masa: Ka tafi Baitul-Mali ka xibi daidai abin da ya ce. Jabir ya je ya xiba daga cikin dukiyar musulmi ba tare da wani shedu ba; don kawai maganarsa shi kaxai.

**Martani:**

Wannan maganar dai ta qunshi qarairayi da qage mai yawa. Bari mu soma bayanin su:

Tun farko, a cikin maganarsa akwai tuqa da warwara, don da farko cewa ya yi Fadak gado ce. Yanzu kuma ya ce kyauta ce. Amma, bari mu bi shi a haka. Sai mu ce: Ita wannan kyautar yaushe ne aka yi ta? Mu mun san Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tsarkaku daga yin wasicci ga mai gado. Don hakan ya sava ma Shari'a. Idan kuma tun lokacin da yake cikin qoshin lafiyarsa ne ya yi mata kyautar, to, me ya sa ba ta karva ba sai yanzu? Idan mutum ya yi kyauta, ba a karve ta ba har ya mutu, kyauta ta tashi kenan. Ya ko za a yi Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ba da kyautar Fadak ga Fatima kuma matansa da sauran musulmi ba su sani ba, har ya zame cewa Ummu Aimana ko Ali *Raliyallahu Anhuma* ne suka kevanta da sanin hakan?

Danganta wannan neman Fadak shi kansa ga Fatima, qarya ne. Abul Abbas xan Suraiju ya soke maganar yana mai cewa: Hadissan Buhturi xan hassanu da ya karvo daga Zaidu xan Ali cewa Fatima ta gaya ma Abubakar *Raliyallahu Anhu* cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ba ta kyautar Fadak, kuma wai, ta zo da shedar mace da namiji sai ya qi karva, wannan maganar na da ban mamaki!! Lalle Fatima ta tambayi Abubakar gadonta, sai ya faxa mata cewa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Ba a gadon mu". Amma ba a ce Fadak ce ta nema ba, balle a ce ta shedar da wani a kan haka.

Amma Jarir ya riwaito daga Mugirata daga Umaru xan Abdulaziz cewa: "Fatima ta nemi Annabi ya ba ta Fadak, bai ba ta ba. Kuma Annabin ya kasance yana ciyar da wasu Banu Hashim, danginsa daga cikinta, yana taimakon masu rauninsu, ya aurar da marasa aure duk daga cikinta. Haka aka ci gaba har qarshen rayuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Fatima kuma ta karvi gaskiya". Sarki Umaru xan Abdulazizi ya qare da cewa: "Don haka, ina sheda maku cewa, ni ma na bar ta yadda take lokacin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*".

Ba wani ingantaccen hadisi da ya tabbatar da cewa Fatima ta ce an ba ta Fadak, ko wani ya yi sheda a kan haka. Da kuwa an yi haka da an riwaito shi, don abin jayyayya ne wanda ya shafi al'umma, kuma aka yawaita maganganu game da shi. Tun a lokacin ba xaya daga cikin musulmi da ya ce ya ji Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ba Fatima ita, ko ita Fatima ta ce an ba ta. Sai daga baya wannan Buhuturi xan hassan ya yo wannan riwaya.

To, ko da an qaddara cewa wannan hadisin ya tabbata, babu hujja a cikinsa. Don Fatima ba ta ce zata rantse tare da shedu aka hana ta ba. Kuma Abubakar bai ce ba shi yarda da shedu da rantsuwa ba.

Abin da tarihi ya bayyana shi ne, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* gonaki uku ne ya zava, waxanda suka haxa da gonar Banun Nadhir, da ta Haibara da Fadak. Sai ya keve ta Banun Nadhir don biyan buqatunsa da ke iya tasowa. Fadak kuma ya keve ta don matafiya masu buqata. Haibara

kuma sai ya raba ta kashi uku; kashi biyu daga ciki ya raba su a tsakanin musulmi, xayan kuma don ci da shan iyalinsa. To, duk abin da ya saura bayan an fitar wa iyalinsa sai a sake raba shi ga matalautan Muhajiruna.

A riwayar Laisu lokacin da Fatima *Raliyallahu Anha* ta aika ma Abubakar tana tambayar sa game da gadonta cikin dukiyar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* wadda ta haxa da abin da Allah ya ba shi a Madina ba tare da yaqi ba, da kuma Fadak, da abin da ya saura daga cikin humusin Haibara sai ya gaya mata cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Ba a gadonmu (Annabawa). Abin da duk muka bari sadaka ne. Kawai dai 'yan gidan Manzo suna iya amfani da ita dukiyar, amma ba mallaka ba". Abubakar ya qara da cewa: "Wallahi ba zan canza komai ba cikin dukiyar daga yadda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya saba yi da ita. Don haka sai bai ba Fatima komai na gado ba.

Duk wanda ya san farihin sayyidina Abubakar tare da duba riwayoyin da suka zo kan wannan al'amari ya san lalle Abubakar yana ganin girman Fatima kuma yana karvar maganarta. To, ina kuma ga a ce ta zo da shaidu irin waxanda suka ambata.

Bisa qaddara cewa, ana iya gadon Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama,* to, waxanda ke da haqqi su ne matansa da wan mahaifinsa Abbas. A irin wannan kuwa da an buqaci shedu mace xaya ko namiji xaya ba zasu wadatar ba bisa ga Alqur'ani da sunnah da haxuwar malamai. Don haka, in har jayayya ce ba Abubakar ne mai yinta ba.

Kafa hujja a irin wannan lamari da kasancewar Ummu Aimana 'yar aljanna jahilci ne da ya wuce wuri. Domin hujja ce a kansa. Ba wai sayyidina Abubakar ba, koda Hajjaju xan yusufa da Mukhtaru xan Abi Ubaid suka ce basu amsar shedarta ita kaxai ga haqqi, su faxi gaskiya, don qa'ida ce ta Shari'a cewa, ba a karvar shedar macce ga abin da ya shafi kuxi. Zamanta 'yar aljanna ko bai canza hukuncin Shari'a a wurin masu ilimi da hankali.

Ummu Aimana dai, ita ce uwar Usamatu xan Zaidu. Kuma ita ce wadda ta yi renon Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Tana kuma cikin muhajirai mata, masu daraja. Don girman darajarta ne 'yan Shi'ar suke so su lava gare ta suyi mata qarya. Kuma babu wani littafi na msulunci da aka yarda da shi wand aya kawo wannan magana.

Haka ma cewar da ya yi wai, Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi shaida cewa, an ba ta aka qi karvar shaidarsa don yana mijinta. Duk ba gaskiya ne ba. Amma bisa qaddara an yi hakan, to, ba aibi ba ne. Don shaidar miji ga matarsa ba a aiki da ita a wurin mafi yawan malamai. Wanda kuma suka yarda a karve daga cikin malaman cewa suka yi sai idan an samu qari akan mijin, kamar a samu wani namiji xaya ko kuma mata biyu.

Hadisin da ya kawo cewa, Ali na tare da gaskiya, ita ma gaskiya tana tare da Ali duk inda ya juya ba za su rabu ba har ya zo mani a wurin Alkausar. Wannan magana ce ta qarya da jahilci. Don ba ta da madogara ko daidai yanar gizo. Ka ga kuwa akwai muni matuqa, mutum ya qaga qarya ya jingina ga

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma ya ce wai, duk malaman Sunnah sun san da ita a matsayin gaskiya.

Sai maganar da ya jingina ga Fatima cewa ta fusata da Abubakar kuma ta rantse ba zata sake yi masa magana ba, shi da abokinsa. A zatonsa yana yabonta ne, alhalin kuwa suka ce mai girma a gare ta. Ina abin fushi a nan? Abubakar bai yi wani hukunci ba da ya sava ma gaskiya. Kuma gama-garin musulmi na iya haqurin karvar irin wannan gaskiya, to, ina ga Fatima 'yar gidan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*? Ba yabo gare ta a nan, ba aibantawa ga Abubakar.

A bisa imaninmu da iya saninmu, yawancin abubuwan da ake riwaitowa game da Fatima da wasu Sahabbai irin waxannan qarairayi ne. Wasu hikayoyin kuma suna da fassara mai ma'ana wadda ke fitar da su daga zargi. Idan kuma har xayansu ta tabbata cewa, ya aikata kuskure ko laifi, to, ai su ba ma'asumai ba ne, waliyyan Allah dai ne, 'yan aljanna da Allah Ta'ala ke gafarta ma zunubbansu.

Haka ma abin da ya ambata na cewa ta yi wasicci da Ali ya rufe ta da dare don kada xayansu ya yi mata sallah. Jingina wannan irin wasicci ga Fatima shi ma jahilci ne da wauta. Me zai sa Fatima ta yi wannan wasicci? Ai kowa ya san sallar musulmi qarin alheri ce da lada ga mamaci. Kuma mafificin halitta ba zai cutu ba koda mafi sharrin halitta ya yi masa sallah. Ga dai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama,* kowa ya yi masa sallah; muminai da fajirai. Kai har ma da munafikai. Irin wannan in bai amfane shi ba, ba zai cutar da shi ba. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuwa ya san cewa a cikin al'ummarsa akwai munafukai amma bai yi wasicci kada wani ya yi masa sallah ba.

Hadisin cewa, Allah na fushi da fushin Fatima, kuma yana yarda da yardarta. Shi ma qarya ne irin wancan. Babu shi a cikin ko xaya daga cikin littafan hadisi. Ba shi kuma da wani sanannen isnadi daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba. Mu dai mun sheda cewa Fatima yar'aljanna ce, kuma tabbas Allah ya yarda da ita. Muna kuma irin wannan shedar ga Abubakar da Umar da Usmanu da Ali da Xalhatu da Zubairu da Sa'adu da Sa'idu da Abdulrahaman xan aufu da Abu Ubaidata. Mun kuma aminta da abin da Allah Ta'alah ya ba da labari a wurare da yawa game da su; cewa ya yarda da su. Kamar in da maxaukakin Sarkin ya ce:

﴿ وَٱلسَّٰبِقُونَ ٱلْأَوَّلُونَ مِنَ ٱلْمُهَٰجِرِينَ وَٱلْأَنصَارِ وَٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُم بِإِحْسَٰنٍ رَّضِىَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُوا۟ عَنْهُ ﴾ التوبة: ١٠٠

> *Magabata na farko daga cikin Muhajiruna da Ansaru da waxanda suka bi su da kyautatawa, Allah ya yarda da su, su ma sun yarda da shi. Attauba 100.*

Da cewar da Allah Ta'ala ya yi:

﴿ ۞ لَّقَدْ رَضِىَ ٱللَّهُ عَنِ ٱلْمُؤْمِنِينَ إِذْ يُبَايِعُونَكَ تَحْتَ ٱلشَّجَرَةِ ﴾ الفتح: ١٨

*Haqiqa, Allah ya yarda da muminai a lokacin da suke yi ma ka mubaya'a a qarqashin itaciya. Suratul Fathi: 18.*

Mun kuma yarda da abin da ya tabbabata cewa, Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rasu yana mai yarda da Sahabbansa. Kuma mun san duk wanda Allah ya yarda da shi da Manzo, to fushin wani ko wane ne ba zai cutar da shi ba.

Hadisin da ya kawo cewa, Fatima sashen Manzo ce. Wanda duk ya cuta mata ya cuta masa. Duk da yake ya yi qari a cikinsa. Amma dai Annabi ya faxe shi ne a lokacin da Ali *Raliyallahu Anhu* ya nemi auren xiyar Abu Jahali. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya hau mimbari a kan haka, ya yi huxuba yana cewa: "Haqiqa mutanen gidan Hashimu xan Mugirata sun nemi in ba da izinisu aurar da 'yarsu ga Ali xan Abu Xalib. To, ba zan yi izini ba, kuma ba zan yi izini ba, kuma ba zan yi izini ba. Domin Fatima shashena ce; duk abin da ke damun ta yana damu na. Sai dai in Ali yana son ya saki xiyata ya Auri tasu.

Sai cewar da ya yi, in da gaskiya ne da bai halatta Abubakar ya bar alfadarin Manzon Allah da takobinsa da rawaninsa wurin Ali ya hana ma Abbas shi lokacin da ya nema. Sai a ce masa: Wa ya ce Abubakar da Umar sun ba Ali don ya mallaka? Ai sun bar su ne a hannunsa kamar yadda suka bar sadakarsa wurin Ali da Abbas don su ba da ita ga waxanda Shariah ta ce a ba.

Maganar tsarkake Ahlul-Baiti daga cin sadaka. Da farko, Allah Ta'ala bai ce ya tsarkake dukkan Ahlul-Baiti ba. Ku ma kun san cewa akwai daga cikin Banu-Hashim waxanda ba a tsarkake daga savo ba, musamman ma a gun ku 'yan-sha-biyu, da ke xaukar duk wani dangin Banu-Hashim da ke son Abubakar da Umar a matsayin wanda ba tsarkakakke ba.

Abin da dai Allah Ta'ala ya ce yana son haka gare su, kamar yadda ya ce yana son haka ga muminai cikin ayar taimama. Allah na son haka, kuma ya yarda da haka, ya yi umurni a kan haka. Wanda ya aikata, to, ya cimma muradin da aka so masa, wanda kuma bai aikata ba, to, ba zai sami muradin ba.

Sai maganar sadaka xin da aka haramta masu. Abin da aka haramta masu shi ne sadakar wajibi, ita ce Zakka. Amma sadaqoqi na ganin dama ba laifi ba ne a kansu in sun amfana da su. Ai suna shan ruwan rijiyoyin sadaka misali, waxanda ake ajiyewa tsakanin Makka da Madina. Da kansu kuma suna faxin cewa, sadakar farilla ce aka haramta mana, ba a haramta mana sadakar nafila ba. To, in ko haka ne, me zai hana su amfana da sadakar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ga jama'ar musulmi? Wannan dukiyar ba zakkar da aka farlanta wa Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba ce. Kuma na haramta masu zakka ne don tana dauxar mutane. Amma abin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bari na ganimar da Allah ya ba shi halal ce ga re shi, kuma ya sanya sashenta ya zama sadaka ga musulmi. Don haka Ahlul-Baiti na iya cin moriyarta kamar sauran musulmi.

Game da tsokacin da ya yi kan karvar da Jabir *Raliyallahu Anhu* ya yi ga alqawarin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi ma sa daga wurin

Abubakar. Jabir dai bai raya cewa yana son haqqin wani ba, ya dai nemi wani abu ne daga baitul-mali, shugaba kuma na da damar xaukar sa ya ba shi, ko da kuwa Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai yi masa alqawari ba. Ka ga ba a buqatar shedu a nan.

A gaskiya, duk maganganun da suke yi game da Fatima *Raliyallahu Anha* cewa ta nemi Fadak kuma ta kafa sheda akan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ba ta ita. Duk wannan suka ce suke yi gare ta a fakaice ba yabo. Kuma Allah ya raba ta da waxannan qazuffa nasu, ya nisantar da ita daga gare su.

### 2.9.7 Wai Don me Aka ce da Abubakar "Siddiqu"?

Xan Shi'ar ya ce: Malaman Sunnah duk sun riwaito hadisi game da cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya faxa game da Abu Zarri cewa: "Qasa ba ta taxa xaukar mafi gaskiyar magana fiye da Abu Zarri ba. Ita ma sama ba ta rufe wanda ya fi shi gaskiyar magana ba". Amma duk da haka ba su kira shi Siddiqu ba sai Abubakar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai yi masa irin wannan shedar ba.

**Martani:**

Hadisin da ya ambata cewa duk malaman Sunnah sun riwaito shi ba shi a cikin Buhari da Muslim ko littafan Sunan na Ahlus-Sunnah. Amma tun da yake an riwaito shi a wasu littafan Sunnah, to, zamu qaddara ingancinsa mu ba shi amsa.

Ba wani malamin da ya fahimci wannan hadisi a matsayin cewa, Abu Zarri ya fi duk mutanen da ke bisa doron qasa faxin gaskiya. Don wannan na fifita shi a kan Annabawa da Manzanni, cikinsu har da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da sayyidina Ali. Ka ga kenan ya sava ma ijma'in musulmi; Sunnah da Shi'ah baki xaya. Don haka ne aka san cewa ma'anar wannan kalimar ita ce, Abu Zarri mai gaskiya ne. Kuma waninsa bai fi shi neman yin daidai da gaskiya ba. Amma wannan ba ya lizimtar da cewa, babu wanda ya fi shi yawan gaskiyar da girmanta. Haka ma abin wani ya gasgata na iya zarce wanda shi Abu Zarri xin ya gasgata.

Abubakar dai ba a kira shi Siddiqu don kawai yana faxin gaskiya ba, a'a, don girman gasgatawar da ya yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. In aka lura da lafazin da kyau za a gane cewa, kowane Siddiqu mai gaskiya ne, amma ba kowane mai gaskiya ke zama Siddiqu ba.

### 2.9.8 Abubakar Halifan Manzo

Xan Shi'ar ya ce: Sun kira shi halifan Manzo ga shi kuma Manzo bai tava sa shi ya waqilce shi ba; a rayuwarsa ko bayan rayuwarsa, koda a wurinsu. Ba su kira Ali halifan Manzo ba, ga shi kuma Manzon ya sha sa shi ya waqilce shi a lokacin rayuwarsa kamar yadda ya wakilce shi a kan garin Madina lokacin yakin Tabuka, har ya ce masa: "Madina ba ta gyaruwa sai da ni ko kai.

Ba ka son ka zama a wurina kamar matsayin Haruna a wurin Musa? Sai dai fa babu wani Annabi bayana".

Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya shugabantar da Usamatu xan Zaidu akan rundunar yaqin da Abubakar da Umar ke ciki. Kuma bai sauke shi ba har ya rasu, ga shi kuma ba su kira shi halifa ba. A lokacin da Abubakar ya zama halifa sai Usamatu ya fusata, ya ce masa: "Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya shugabantar da ni akan ka, to wa ya shugabantar da kai a kaina? Sai ya tafi shi da Umar suka ba shi haquri. Kuma suka rinqa kiran sa Amir (sarki) har tsawon rayuwarsa.

**Martani:**

Halifan mutum shi ne wanda ya sa don ya maye gurbinsa ko kuma wanda ya maye gurbinsa koda ba da izininsa ba. A harshen Larabci wannan ma'anar ta biyu ita aka sani. Kuma shi ne ra'ayin mafi yawan malamai. Amma wasu daga cikin Zahiriyyah da kuma 'yan Shi'ah cewa suka yi sai in shi ya sanya wanda zai maye bayansa sannan za a kira shi halifansa.

To, a kowane ra'ayin dai Abubakar *Raliyallahu Anhu* halifan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne, don shi ne ya maye gurbinsa bayan rasuwarsa. Ko 'yan Shi'ah ma ba su jayayyar cewa shi ya zama shugaban musulmi bayan Manzo. Shi ke ba musulmi sallah, ya tsayar da haddi, ya yi jihadi, ya raba ganima, ya naxa sarakuna da alqalai. To, idan an ce halifa shi ne wanda wani ya sa ya maye gurbinsa, harwayau dai Abubakar ne. Domin daga cikin Ahlus-Sunnah akwai masu ganin cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ya ce Abubakar ya maye gurbinsa bayan rasuwarsa, ko dai ta hanyar nassi bayyananne ko wanda sai an yi tunani. Kamar yadda su ma 'yan Shi'ah ke ganin cewa akwai nassi a kan Ali. Wasunsu su ce bayyanannen nassi, wasu su ce mai buqatar nazari. Ra'ayin farko shi ne na 'yan-sha-biyu, na biyun kuma na Jarudiyyah, wani vangare na Zaidiyyah. Kuma ra'ayin Ahlus-Sunnah masu ganin akwai bayyanannen nassi game halifancin Abubakar ya fi qarfi nesa ba kusa ba a kan ra'ayin masu cewa akwai nasssi a kan Ali saboda yawan hadissai masu nuni ga Abubakar da ingancinsu.

Amma cewa ya saka Ali *Raliyallahu Anhu* ya kula da Madina ba ya cikin abin da Ali ya kevanta da shi. Domin duk lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yake fita daga Madina yakan sa wani daga cikin Sahabbansa ya kula masa da ita. Kamar yadda ya sa Abdullahi xan Ummu-Maktumi ya kula da ita a wani lokaci, da yadda ya sa Usmanu xan Affana ya riqa garin a wani lokaci na daban.

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya sa wani ba Ali ba a wasu lokutta ya kula da tsaron Madina da waxanda ke cikinta, sa'adda aka fi son a riqa ta don muhimmancin waxanda aka bari a cikinta. Amma dai duk wannan halifance ne qayyaddade ga wasu mutane da wasu lokuta, ba halifanci ne a kan duk al'umar Annabi ba. Ba kuma halifanci ne na bayan rasuwarsa ba. Idan har

aka Ali da sunan halifa da wannan ma'ana to, da yawa waxanda za su karva irin wannan sunan, don sun yi irin wannan halifancin a wasu lokutan su ma.

Halifanci na bai xaya shi ne wanda ake yi bayan cikawar Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Shi ne kuma wanda ya kamata mai yin sa ya zan ya fi sauran jama'a daraja. Amma halifanci a kan Madina kawai ba a cika kula da fifikon mutum a wajen yinsa ba. Domin masu fifikon a wannan lokaci duk suna can tare da Manzo. Don can ne suka fi amfani. Wanda za a bari kuwa ana barin sa ne don kula da iyali. Ka ga ta wannan fuska wanda aka tafi da shi ma ya fi fifiko.

Kamantawar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wa Ali da Haruna kuwa kan asali maye gurbin ne. Don ba ta ko ina suka yi kama ba. Ali *Raliyallahu Anhu* kuwa yana da waxanda suka yi tarayya da shi a wurin maye gurbin Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* idan ya fita daga garin Madina. Amma Haruna ba ya da shi. Kuma a lokacin da Annabi Musa *Alaihis Salamu* ya tafi ganawa da Allah shi kaxai ya tafi, ya bar duk jama'arsa. Amma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* lokacin da ya tafi yaqin Tabuka ya tafi ne da dukkan musulmi in banda masu uzuri. Bai bar Ali ga kowa ba sai qananan yara da mata. Sai ko maza masu uzuri. Don haka halifancin nasa bai kai kamar na Haruna ba. Amma ya yi daidai da shi ta fuskar kasancewarsa an ba shi amana a lokacin da maigidansa ba ya nan kamar yadda haruna ya yi wa Annabi Musa. Wannan shi ya sa Ali *Raliyallahu Anhu* ya nuna damuwa, sai Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya nuna masa cewa, barin sa tsaron bai nuna cewa don wani naqasu ba ne. A'a, an dai danqa ma sa amana ne kamar yadda Musa *Alaihis Salamu* ya yi wa xan uwansa Haruna.

Maganar cewa Madina ba ta gyaruwa sai da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ko Ali, qarya ce zunzurutunta. Kuma ba a san ta ba a cikin xaya daga cikin litaffan ilimi da ake dogaro a kansu. Kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi ta fita Madina tare da Ali *Raliyallahu Anhu*, ba abin da ya same ta sai alherin Allah. Wannan na cikin abin da ke bayyana tsananin jahilcin 'yan-sha-biyu. Sai su rafka qaryar da duk mai xan hasken karatu yana gane ta.

Sai maganar cewa, Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya sa Usamatu *Raliyallahu Anhu* ya shugabanci rundunar da Abubakar da Umar ke ciki. Wannan ma qarya ce da ba ta wuyar ganewa ga wanda ya san hadisi. Don kowa ya san cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya waqilta Abubakar ya maye gurbinsa wajen ba da sallah tun lokacin da ya fara rashin lafiya har zuwa rasuwarsa. Rundunar Usamatu kuwa an riwaito cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya shirya ta ne kafin rashin lafiyarsa. To, in har ma Abubakar na ciki, ka ga daga radda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce ya ba mutane sallah, shi an fitar da shi daga rundunar kenan. Ballantana ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai tava sa Abubakar qarqashin Usamatu ba.

Kuma cewar da ya yi har Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya cika bai cire Usamatu ba. Ai Abubakar xin ma bai cire shi ba, tare da yana da haqqin yin haka da ya fuskanci shi ne maslaha a wancan lokaci. Amma Abubakar ya zartar ta tafiyar rundunar Usamatu da barinsa a matsayin shugaba duk da kiraye-kirayen da aka yi ta yi ma sa daga musulmi na ya saurara kada rundunar ta je a wancan hali da ake ciki na tashin hankali da ruxuwa. Abubakar ya rantse ba zai fasa ci gaban abin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya soma ba.

Cewa kuma Usamatu ya yi fushi a lokacin da aka naxa Abubakar. Wannan qarya ce mai tsananin muni, domin son da Usamatu ke wa Abubakar da xa'arsa gare shi mashahurin abu ne da ba a iya musu. Usamatu ya fi kowa nisantar savani da rarraba. Ko lokacin fitina bai yaqi cikin kowace ruduna ba. Kuma shi ba Baquraishe ba ne, balle ya yi tunanin zama halifa. Bai ma zo masa a zuciya cewa zai iya zama halifa. To, in haka ne wace fai'da zai samu in dai ya yi irin wannan maganar ga wanda ya zama halifa, tare da ya san cewa duk wanda ya zama halifa, na da iko a kansa. Qaddara cewa Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya sa Abubakar qarqashin shugabancinsa. To, bayan rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ci gaban wannan shugabancin zai rataya ne ga yardar sabon shugaba bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.* Kuma lamarin zartar da runduna ko hana ta ya koma a hannunsa. Kuma ci gaba da shugabancin Usamatu da rashinsa ya koma hannun sabon halifa. To, idan an qaddara cewa Usamatu zai ce wa ya shugabantar da kai a kaina? Sai Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya ce: Wanda ya shugabatar da ni akan dukkan musulmi, cikinsu har da waxanda suka fi ka. In ya ce amma ni an shugabantar da ni a kanka, sai Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya ce wannan ya kasance kamin in zama halifa, amma bayan na zama halifa to, ka koma qarqashin shugabancina.

Shi dai Usamatu *Raliyallahu Anhu* mai hankali ne da ilimi da tsoron Allan da ba za su bari ya yi irin wannan magana maras ma'ana da xan Shi'ar ya jingina ma sa ba, ga mutum mai matsayi irin na Abubakar *Raliyallahu Anhu*.

Abin da yafi wannan ban mamaki shi ne cewa wai sayyidina Abubakar da Umar sun tafi wurin Usamatu suna neman ya yarda da su, tare da cewa su 'yan Shi'ah ne suka ce Abubakar da Umar da qarfi suka rinjayi Ali *Raliyallahu Anhu* da Banu-Hashim da Bani-Abdimanafi, ba su nemi yardarsu ba. Ga shi kuwa waxannan sun fi yawa da qarfi da xaukaka a kan Usamatu *Raliyallahu Anhu.* Wanda ya rinjayi qabilu kamar Bani-Hashim da Bani-Umayyata da sauran Bani-Abdimanafi da rassa daban-daban na Quraishawa, wacce yarda yake nema daga Usamatu xan Zaidu wanda ya kasance cikin mafi raunin talakkawansu, ba shi da wata qabila ko 'yan'uwa, ko kuxi ko wasu mutane tare da shi. Ba don son da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ke yi masa ba, da gabatar da shi da ya yi zai zama kamar sauran talakkawan musulmi masu rauni.

'Yan Shi'a na iya cewa, sun nemi yardarsa ne don Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* na sonsa. Wannan ko zai rosa ma ku aqida gaba xaya. Don ga shi kun ce sun musanya alqawarin Manzo, sun zalunci wanda ya yi wa wasicci, sun yi masa qwace. To, sai a tambaye ku: Wanda bai bi ingantaccen umurni ba, ya musanya bayyanannen al'amari, ya yi zalunci da wuce iyaka, ya sa qarfi, bai kula da xa'ar Allah Ta'ala da ta Manzonsa *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba, kuma bai kula da alqawalin 'yan gidan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da alfarmarsu ba, zai nemi yardar Manzo dangane da Usamatu? Kuma bayan haka kun ce bai nemi yardar Fatima ba, ya yi wa qwace, ya cutar da ita. Duk wanda ya aikata wannan to, lalle ba ya buqatar neman yardar Usamatu. Abin da ke sa mutum ya nemi yardarka shi ne don kana riqo da addini ko kuma don kana da duniya a hannunska. Ka ga a cewarsu, nan babu ko guda. 'Yan Shi'ah sun fi kowa yawan takin saqa a cikin maganganunsu saboda wautarsu da jahilcinsu.

### 2.9.9 Wai Don Me Aka Ce Da Umar "Faruqu"?

Xan Shi'ar ya ce: Kuma sun kira Umar Faruqu, mai rabe gaskiya ga shi kuma ba su kira Ali da wannan suna ba, kodayake Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Ali ne mai rarrabewa tsakanin mutanen gaskiya da mutanen banza". Umar da kansa ya ce: Ba mu kasance muna sanin munafukai a zamanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba sai wanda muka ga Ali na fushi da shi daga cikinsu.

**Martani:**

Da farko waxannan hadisan biyu malaman hadisi ba su shakkar cewa qarya ne. Kuma ba wani malami da ya riwaito su a cikin littaffan ilimin da ake dogaro a kansu. Ba kuma xaya daga cikinsu da ke da sanannen isnadi.

Ko ga mas'alar fiqihu, duk wanda ya kafa hujja da hadisin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* wajibi ne ya bayyana madogarar hadisinsa. To, ballantana mas'ala irin wannan? In ba haka ba don kawai mutum ya ce: "Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce", duk malamai sun haxu a kan cewa wannan ba hujja ba ne. In kuwa har yin haka hujja ne, kenan duk hadisan da Ahlus-Sunnah suka kawo su zama hujja kenan a kan 'yan Shi'ah. Mu dai a wannan babin muna gamsuwa da hadisin da duk wata qungiya ta musulmi ta riwaito idan dai isnadinsa na sanannun mutane ne masu gaskiya.

Amma idan hadisi ba shi da isnadi, kuma wanda ya cirato shi ya jingina shi ne ga littaffen wani, wanda bai riwaito shi ba, to, ba ya halatta ga mutum ya yi shaida a kan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ga abin da bai san madogararsa ba.

Sanannen abu ne ga duk mai masaniya cikakka cewa, malaman hadisi ne suka fi kowa qoqarin sanin maganganun Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* da ya faxa, kuma sun fi kowa kwaxayin bin maganarsa, da nisantar son zuciya. Inda ya tabbata cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya faxi

wannan game da Ali *Raliyallahu Anhu* da sun fi kowa cancanta ga bin wannan maganar, don suna bin maganarsa ne bisa ga imaninsu da shi, da son binsa, ba don neman wata buqata ga wanda aka yaba ba.

Da ya tabbata a wurin malaman hadisi cewa Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce wa Ali: "Wannan shi ne mai rarrabe ma al'ummata gaskiya" da sun karvi wannan sunan, sun riwaito shi kamar yadda suka riwaito maganarsa game da Abu Ubaidata *Raliyallahu Anhu* cewa: "Wannan shi ne amintaccen wannan alumma" da kuma cewar da ya yi game da Zubairu: "Kowane Annabi na da mataimaka. Ni ko Zubairu ne mataimakina". Kamar kuma yadda suka karvi abin da suka riwaito na cewar da ya yi ga Ali *Raliyallahu Anhu* "Lalle, gobe zan miqa wannan tutar ga wani mutum da Allah da Manzonsa ke so, kuma yake sonsu" da hadisin *Kisa'u* wanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wa Ali da Fatima da Hasan da Husaini addu'a yana cewa: "Ya Allah, waxannan iyalaina ne. Ka gusar da qazanta daga gare su, kuma ka tsarkake su tsarkakewa" da makamantan waxannan hadissan.

Duk hadisan nan biyu da marubucin ya kawo mun san cewa qarya ne bisa ga dalili. Ba ya halatta a danganta su ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.* Kuma ma mene ne ma'anar kasancewar Ali *Raliyallahu Anhu* ko waninsa mai rarrabewar alumma tsakanin gaskiya da qarya? In suna nufin cewa zai iya banbancewa tsakanin mumini da munafuki, to wannan babu mutumin da ke iya yin sa. Don Allah Ta'ala ya ce: *Daga cikin waxanda ke kewayenku akwai munafikai da kuma cikin mutanen Madina. Sun saba da munafucci, kai ba ka san su ba, mu ne muka san su. Attauba: 101.* To, idan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai san ainihin munafikai da fuskokinsu ba cikin mutanen da ke tare da shi a Madina da kewayenta, to yaya wani zai iya sanin su?

Son da 'yan Shi'ah ke cewa suna yi wa Ali *Raliyallahu Anhu* shi kansa babu shi. Domin wanda suke son babu shi. Shi ne imamin da ba ya kuskure, wanda kuma nassi ya zo da shugabancinsa, babu wani shugaba bayan Manzon face shi, wanda kuma ke da imanin cewa Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* azzalumai ne, 'yan qwace, kuma kafirai. To, ka ga in Ali ya zo ya bayyana gare su ranar alqiyama zasu san cewa ba shi ne wanda suke so ba. Wannan shi zai bayyana maka cewa, 'yan-sha-biyu maqiyan Ali ne, babu tanbaba.

Daga nan ne za ka fahimci hadisin da Muslim ya riwaito daga Ali *Raliyallahu Anhu* cewa: "Haqiqa Annabi ya tabbacin cewa, ba mai sona sai mumini, kuma ba mai qina sai munafiki.

Son da 'yan Shi'ah ke yi wa Ali ba shi da banbanci da son da Yahudawa ke cewa suna yi ga Annabi Musa da wanda Kirista ke cewa suna yi ga Annabi Isah. Kai 'yan-sha-biyu ma suna qin abin da ya sifofin gaskiya na Ali kamar yadda Yahudawa ke qin sifofin gaskiya na Annabi Musa, Kiristoci kuma suke qin sifofin gaskiya na Annabi Isah. Domin dukkansu suna qin wanda ya yarda da Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

## 2.9.10 A'isha Uwar Muminai

Xan Shi'ar ya ce: "Sun xaukaka lamarin Aisha ga shi kuwa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kasance yana ambaton Khadija 'yar Khuwailidu, har Aisha ta ce masa: "Ka cika ambaton ta ga shi kuwa Allah ya musanya maka waxanda suka fi ta". Sai ya ce: "Wallahi ba a musanya mani waxanda suka fita ba. Ta gasgata ni lokacin da mutane suka qaryata ni, ta karve ni lokacin da mutane suka kore ni, ta amfanar da ni da kuxinta. Allah kuma ya azurta ni da 'ya'ya daga wurinta, bai a ba ni daga wata ba ita ta.

**Martani:**

Ahlus-Sunnah dai ba su haxu a kan cewa Aisha *Raliyallahu Anha* ce ta fi duk matansa ba. Amma da yawa daga cikinsu na ganin haka, saboda hadisin da ya zo cikin Buhari da Muslim ta hanyar Abu Musa Al-Ash'ari da Anas Allah ya yarda da su cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce "Falalar Aisha a kan sauran mata kamar falalar *Saridu* ne a kan sauran abinci. *Saridu* shi ne tuwon alkama da miyar nama, kuma mafificin abinci. Domin alkama ta fi sauran dangin abinci, nama kuma ya wuce sauran abubuwan haxi a miya kamar yadda ya zo a hadisin da Ibnu qutaibata ya riwaito daga Manzon *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa: "Fiyayyar miyar da mutane ke sha duniya da lahira ita ce nama". To, ka ga da haka mai gaskiya abin gasgatawa ya fifita Aisha a kan sauran mata kamar yadda *Saridu* yake da fifiko a kan sauran abinci.

Ya zo a cikin hadisi ingantacce da Amru xan Asi *Raliyallahu Anhu* ya riwaito inda ya ce: "Na ce, ya Manzon Allah, duk cikin mutane wa ka fi so?" Sai ya ce: "Aishah". Sai na ce: "To, daga cikin maza fa?" Sai ya ce: "Babanta". Na ce: "Sai wa?" Ya ce: "Sai Umar". Sannan ya ambaci sunayen wasu mutane.

Cewar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi: "Wallahi ba a musanya mani waxanda suka fita ba". Idan ya inganta ba ya da shan kai. Domin Khadija ta amfane shi a farkon musulunci irin amfanin da waninta bai yi ma sa ba. Ta wannan fuska Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba shi da kamarta, don ta amfane shi lokacin buqata. Ita kuma Aisha ta kasance tare da shi ne a qarshen sha'anin annabta; lokacin da addini yake kammala. Wannan ne ya sa ta samu qarin imani da ilimin da mutanen da suka rasu tun farko ba su samu ba. Don haka sai ta zama mafi xaukaka ta wannan fuskar. Babu shakka kuma al'ummar musulmi ta amfana da ita fiye da yadda ta amfana da duk wata ba ita ba. Ta samu ilimi na Sunnah da wani ba ita ba bai samu ba, ta kuma karantar da mutane shi. Khadija ta amfani Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ga kansa, A'ishah kuma ta amfane shi ga al'ummarsa. Addini kuma ya kammala A'ishah tana raye, ita kuma Khadijah, Allah ya karvi ranta gabanin haka. Shi kansa yin imani da musulunci da yin aiki da shi a lokacin cikarsa yana da wani fifiko babu shakka.

## 2.9.11 Ina Laifin Nana A'isha?

Xan Shi'ar ya ce: Ta tona asirin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce mata: "Za ki yaqi Ali kina mai zaluntar sa". Sannan kuma ta sava wa umurnin Allah in da ya ce: *Kuma ku zauna a gidajenku. Al-Ahzab:33.* Ta fito fili tana yaqar Ali ba don laifin kome ba. Don duk musulmi sun haxu a kan kashe Usman, kuma ita kanta kowane lokaci tana umurni da a kashe shi, tana cewa: "Ku kashe tsohon banza. Allah ya kashe shi". Lokacin da kuma ta ji cewa an kashe shi sai ta yi murna, sannan ta tambaya: "Wane ne ya zama halifa?" Aka ce mata: "Ali". Sai ta fito don yaqar sa wai tana neman fansar jinin Usmanu. To, mene ne laifin Ali a cikin wannan? Ya aka yi Xalhatu da Zubairu suka halatta wa kansu yi mata xa'a a kan wannan? Da wace irin fuska za su sadu da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*? Ga shi kuwa da xayanmu ya yi magana da matar wani, ya fitar da ita daga gidanta, ya yi tafiya tare da ita, da ya zama mafi girman maqiyinmu. Ya aka yi dubun dubatar musulmi suka yi mata xa'a ga wannan, suka taimake ta ga yaqan Sarkin Muslumi? Su ne kuwa aka rasa wanda zai taimaki 'yar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikinsu koda da maganar fatar baki a lokacin da ta nemi haqqinta daga wurin Abubakar?

**Martani:**

Ahlus-Sunnah mutane ne masu tsayuwa da gaskiya, da yin sheda don Allah, kuma bisa ga adalci. Shi ya sa maganarsu a kodayaushe gaskiya ce da ba taqin saqa a cikinta. Amma 'yan-sha-biyu da sauran 'yan bidi'a maganarsu ba ta rabuwa da qarya da taqin saqa. A wurin Ahlus-Sunnah duk waxanda suka yi yakin Badar 'yan Aljanna ne. Haka ma matan Manzon Allah iyayen muminai; A'ishah da sauran matan duka. Haka Abubakar da Umar da Usmanu da Ali da Xalhatu da Zubairu su ne shugabannin 'yan aljanna bayan Annabawa. Sannan Ahlus-Sunnah ba su ganin sharaxi ne ga 'yan aljanna su kasance ba su kuskure ko ba su laifi. A'a, suna iya yin tuntuve ko su yi zunubi qarami ko babba sannan su tuba. Wannan maganar ita ce aqidar duk musulmi. Kuma in har mutum bai tuba daga qananan zunubbai ba, nisantar manya na kankare su. Kai, a wurin mafi yawansu manyan zunubbai ma na kankaruwa da aikata kyawawan ayyukan da suka fi su, sai ladarsu ta shafe zunubin waxancan. Haka ma musibun da ke sauka a kan musulmi, akan shafe zunubbai da su. Da sauran abubuwa dai.

A kan wannan tushe na aqida ne malamai ke cewa, mafi yawan abubuwan da aka ambata game da Sahabbai ba su wuce qarairayi. Wasu kuma ijtihadi ne suka yi, sai ya kasance mafi yawan mutane ba su gane ta inda suka vullo ma abin ba. In da aka qaddara sun yi zunubi kuma, Allah zai gafarta ma su shi, ko dai don sun tuba, ko don sun aikata manyan ayyukan lada, ko an jarabce su da wata musiba mai shafe zunubbai. Ko dai wani abu daban ba wannan ba. Amma tun da hujja ta tsayu a kan zamansu 'yan aljanna, to, ba zai tava yiwuwa su aikata abin da zai wajabta ma su shiga wuta ba, faufau. Kai ko

da ba irin waxannan bayin Allah da muke da tabbacin aljanna gare su ba, ba ya halatta a yi sheda a kan wani daga cikin xaixaikun musulmi da shiga wuta don abin da tabbas ba. Magana kuwa ba tare da ilimi ba haramun ce a Shari'a.

Sai cewar da ya yi wai, Nana A'ishah ta tona asirin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.* Sai mu ce, ku halinku kenan; ku kan farauto zunubban wani, ku take naku, sai ku rinqa fallasa shi kome darajarsa. Mu kam, a wurinmu, masu waxannan zunubai sun tuba, kuma Allah ya xaukaka darajarsu da yin tuban. Ba ka ganin Allah Ta'ala ya ce ma matan da suka yi wancan laifi: *Idan kun tuba to, zukatanku sun karkata. Attahrim:4.* Sai Allah Ta'ala ya kira su zuwa ga tuba. Kuma ba shi yiwuwa a yi zaton cewa ba su tuba ba duk da xaukakar da Allah Ta'ala ya yi masu, da kasancewarsu matan Annabinmu a aljanna. Ga shi har Allah ya ba su zavi tsakanin Allah da Manzonsa da gidan aljanna ko kuma duniya da qawace-qawacenta, suka zavi Allah da Manzonsa da gidan aljanna. Bisa ga haka har Allah ya haramta wa Manzonsa ya musanya wata daga cikinsu ya auro wata. Ya kuma haramta masu qara wani aure a kansu. Kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rasu ya barsu a matsayin iyayen muminai. Ba mu zaton ya zan ba su tuba ba bayan wannan aya kamar yadda ba mu zaton ya zan Ali *Raliyallahu Anhu* bai daina neman auren xiyar Abu Jahli da ya yi niyya ba koda a zuciyarsa bayan waccan ta Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* wadda a cikinta ya nuna damuwarsa akan haka, har ma ya ce: ".. Sai fa in xan Abu Xalib na son ya saki xayata ya auri xiyarsu".

Shi ko hadisin da xan Shi'ar ya kawo cewa; "Za ki yaqi Ali kina mai zaluntar sa". Ba a san shi ba a cikin littafan ilimi da ake dogara a kansu, ba ya kuma da sanannen isnadi. Kai ya ma fi kama da qarya don A'ishah ba ta fita ne don ta yi yaqi ba. Ta fita ne don sasantawa tsakanin musulmi, tana tsammanin cewa fitar ta fi alheri, sai ta gano daga baya cewa rashin fitar shi ne ya fi. Shi ya sa ta kasance idan ta tuna ta kan yi kuka har hawaye ya jiqa mayafinta.

Cewar kuma ta sava wa umurnin Allah, ta yi fita irin ta jahiliyyar farko. Wannan qazafi ne da Allah zai kama mai yinsa in bai tuba ba. Don Allah ya cewa su zauna cikin gidanjensu ba ya hana su fita idan akwai wata maslaha da ake yin umurni da ita kamar suka fita tare da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* wurin aikin hajji bayan saukar wannan aya, kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya aika ta tare da qanenta Abdurrahaman ta hau bayansa akan taguwa ta yi Umara daga wurin xaukar harama da ake kira *Tan'imu*

Abin da dai ya kamata a sani wanda kuma shi ne tarihi ya tabbatas, cewa Uwar Muminai ba ta fita a lokacin yaqin basasar Raqumi da nufin yaqi ba. Su ma Xalhatu da Zubairu *Raliyallahu Anhuma* ba su fita da niyyar su yaqi Ali ba. Kuma wannan shi ne yaqin da aka ambata cikin Alqu'ani inda Allah Ta'ala ya ce:

﴿ وَإِن طَآئِفَتَانِ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ٱقْتَتَلُواْ فَأَصْلِحُواْ بَيْنَهُمَاۖ فَإِنۢ بَغَتْ إِحْدَىٰهُمَا عَلَى ٱلْأُخْرَىٰ فَقَٰتِلُواْ ٱلَّتِى تَبْغِى حَتَّىٰ تَفِىٓءَ إِلَىٰٓ أَمْرِ ٱللَّهِۚ فَإِن فَآءَتْ فَأَصْلِحُواْ بَيْنَهُمَا بِٱلْعَدْلِ وَأَقْسِطُوٓاْۖ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلْمُقْسِطِينَ ۝٩ إِنَّمَا ٱلْمُؤْمِنُونَ إِخْوَةٌ فَأَصْلِحُواْ بَيْنَ أَخَوَيْكُمْۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمْ تُرْحَمُونَ ۝١٠ ﴾ الحجرات: ٩ - ١٠

*Kuma idan qungiyoyi biyu na musulmi suka yi faxa, to, ku yi sulhu a tsakaninsu. Sai idan xayarsu ta yi zalunci akan xaya, sai ku yaqi wadda ta yi zalunci har ta koma zuwa ga hukuncin Allah. Idan ta dawo, to, ku yi sulhu a tsakaninsu da adalci. Kuma ku daidaita. Haqiqa Allah na son masu daidaitawa. Haqiqa su dai musulmi 'yan'uwan juna ne. To, ku yi sulhu tsakanin 'yan'uwanku. Al-Hujura'at: 9-10.*

Ka ga duk da cewa sun yi yaqi da juna, amma sunan 'yan'uwantaka na nan a tsakaninsu. To, idan wannan hukunci ya tabbata ga waxanda ba su kai waxannan zama muminai ba, to, babu shakka ya fi cancantar ya kasance ga manyan Sahabbai.

Sai cewar da xan Shi'ar ya yi, wai duk musulmi sun haxu a kan kashe Usman *Raliyallahu Anhu*. Wannan na cikin bayyanar qarya. Don mafi yawan musulmi ba su yi umurni da kisansa ba, ba su kuma yarda da kisan ba. Kai da yawan musulmi ba su ma zaune a Madina lokacin da abin ya faru. Musulmi kowa na garinsa. Mutanen Madinar ma wasu duk sun tafi aikin hajji.

Sannan duk mafifitan musulmi ba su shiga cikin waxanda suka wannan xanyen aiki na kashe Usmanu ba, ba su kuma yi umurni da shi ba. Waxanda suka kashe shi wasu 'yan tsiraru ne mavarnata kuma qasqantattun daga wasu qabilu masu son fitina. Ali *Raliyallahu Anhu* ya kan ce a kowane lokaci yana mai rantsuwa cewa, shi bai kashe Usmanu ba, kuma ba shi da hannu cikin kisansa. Kuma yana cewa: "Allah ya la'ani duk wanda ke da hannu a cikin kisan Usman, a tudu da rafi duk inda su ke.

Wanda ba shi kusa a lokacin da abin ya faru na iya cewa, me ya sa su Alin ba su taimaka masa ba kamar yadda ya kamata? Amsa ita ce, su dai Sahabbai da su ke a Madina a lokacin irin shi kansa Ali ba su yi zaton cewa zai yiyuwa 'yan ta'addar su aikata haka ba. Da sun sani kuwa da sun toshe duk wata hanyar da za ta kai ga yin haka, kuma su gama da su.

Kuma ku 'yan-sha-biyu kun san cewa, haxuwar da mutane suka yi a kan yi wa Usmanu mubaya'a ta fi wadda aka yi a kan kashe shi. To, in har kun yarda da kafa hujja a kan haxuwar mutane ga yin wani abu, to, me yasa ba ku kafa hujja da haxuwarsu akan naxa shi, ku amince tun farko da naxinsa? Ku ne fa kuke cewa, waxanda suka yi ma sa mubaya'a tsorata su aka yi, suka yi ta a kan tilast. Ka ga da an so a yi irin wannan magana ta ku a wajen maganar kashe shi ta fi karvuwa. Don kuwa kowa zai iya yarda in aka ce, Sahabbai sun ji tsoron 'yan fitina ne shi ya sa suka qyale su, fiye da yardar da zai yi akan

cewa, tsoro ya sa aka naxa Usman tun da farko. Ina mai ba da tsoron? Wa kuma ake tsoratarwar? Akan me za a tsorata shi?

Wannan duk bisa ga qaddara cewar da suka yi wai duk musulmi sun yarda a kashe shi. Ballantana mafi yawan musulmi ba su yarda da yin hakan ba. Kuma ba su ma so faruwar hakan ba. Daga cikinsu ma har akwai waxanda suka kare shi a gidansa kamar Hasan da Husaini ‘ya’yan Ali da Abdullahi xan Zubair da sauransu .

In da wani zai yi irin wannan qarya ya ce, duk musulmi sun haxu a kan kashe Husaini, me ‘yan Shi’ah za su ce ma sa? Alhalin mafi yawan musulmi sun tashi tsaye don ramuwa a kan waxanda suka kashe shi Usman yadda ba su tashi tsaye wajen ramuwa a kan waxanda suka kashe Husaini ba. Wannan qaryar ta fi sauqin karvuwa ga hankali a kan ta ‘ya Shi’ah cewa wai, duk musulmi sun haxu a kan cewa a kashe Usman.

Kowa ya san cewa, ramuwar da mataimakan Husaini suka yi a kan maqiyansa ba ta kai wadda mataimakan Usmanu suka yi ba akan maqiyansa. Kuma fitina da sharri da varna da suka auku bayan kisan da aka yi wa Usmanu *Raliyallahu Anhu* sun fi girma nesa ba kusa ba a kan waxanda suka faru a dalilin kisan Husaini. Kuma kisan Usmanu ya fi girman zunubi a wurin Allah da Manzonsa da muminai a kan kisan Husaini. Don Usmanu yana cikin magabatan farko na muhajirai, irin su Ali da Xalhatu da Zubairu. Kuma ga shi, shi ne halifan musulmi wanda suka haxu a kan naxinsa. Kuma tsawon zamanin halifancinsa na shekaru 12 bai tava kashe kowa ba. Bai tava zare takobinsa don tsorata da wani musulmi ko kashe shi ba. Takobinsa a wancan lokaci ya yi amfani ne kawai wajen yaqar arna da isar da saqon musulunci, kamar yadda aka yi a zamanin halifancin Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* .

Sai cewar da ya yi wai, Nana A’ishah ta yi ta kira ga a kashe Usmanu, tana cewa ku kashe mugun tsoho, Allah ya kashe mugun tsoho. Kuma wai tayi murnar kashe shi. Da za a bar shi ya yi shekarun Abarshi yana neman madogarar wannan magana ba zai samu ba. Gaskiyar magana ita ce, Nana A’isah kamar sauran ‘ya’yanta muminai ba ta yarda da kisansa ba, kuma ta zargi waxanda suka kashe shi, har ma ta yi mummunar addu’a a kan qanenta Muhammad xan Abubakar da duk waxanda ke da hannu a cikin kisan.

Idan ma za mu qaddara cewa, xaya daga cikin Sahabbai Aisha ko wani ya ce haka a kan fushi don inkarin wani abin da ya kamata ayi inkarin sa, to maganarsa a nan ba ta zama hujja, ba ta kuma zama suka ga imanin wanda ya yi ta ko wanda aka wa ita. Domin dukkansu waliyyan Allah ne, ‘yan aljanna. Koda kuwa xayansu ya zaci halaccin kashe xaya, ko ma ya zaci cewa ya kafirta. Ba abin da zai hana ya zamo mai kuskure ga wannan zato, kuma kowannensu na nan a matsayin xan aljanna.

Ita dai magana duk wanda zai yi ta, wajibi ne ya yi ta akan ilimi da adalci, musamman in ta shafi mutuncin wani mutum musulmi kowane iri ne. Ba daidai ba ne a yi ta a kan jahilci da zalunci, kamar yadda ‘yan bidi’a ke yi a ko’ina. Dubi yadda ‘yan-sha-biyu ke bijirowa da mutane masu kusanci da juna

ta fuskar girma da xaukaka, da zamansu waliyyan Allah, amma sai su raba su; wasu su ce ma'asumai ne da ko rafkanwa xayansu ba ya yi. Sauran kuma su ce masu fajirai ko fasiqai ko kafirai. Kai tsaye kana iya gane jahilcinsu da taqin saqar maganarsu. Kamar Bayahude ne ko Kirista, duk sadda xayansu ya buqaci tabbatar da annabcin Musa ko Isah *Alahimas Salam*, tare da yin suka ga annabcin Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama,* ba zai iya ba, don nan take jahilcinsa da taqin saqar maganarsa zasu fito fili.

Sai maganar da ya yi cewa, Nana A'ishah ta tambayi wanda aka naxa, aka ce mata Ali*,* sai ta fito tana yaqarsa a kan neman fansar jinin Usmanu. Kuma ya qara da tambaya wai, wane laifi ne ga Ali *Raliyallahu Anhu* game da wannan?

Sai mu ce masa, duk wanda ya ce Aishah da Xalhatu da Zubairu sun yaqi sayyidina Ali a kan suna tuhumar sa da kashe Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya yi ma su qarya. Sun dai nemi Ali ya hannunta ma su waxanda suka kashe Usmanu, kuma wasunsu na nan saqe cikin rundunarsa. Amma sun fi kowa masaniya game da barrantar Ali daga jinin Usmanu kamar yadda suka san su ba su da hannu a ciki. Amma kowannensu; da su, da Alin ba wanda yake da haqiqanin iko a kan yin haka a wancan lokaci. Ita kuma fitina idan ta auku to, masu hankali na kasa shawo kanta. Sai ya kasance manya Sahabbai suka kasa kashe wutar wannan fitina da kange wawaye daga yin varna. Wannan ko shi ne sha'anin fitina duk inda ta kunna kai. Shi ya sa Allah mabuwayi ya ce:

﴿ وَٱتَّقُواْ فِتۡنَةً لَّا تُصِيبَنَّ ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ مِنكُمۡ خَآصَّةًۖ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ

ٱلۡعِقَابِ ﴿٢٥﴾ ﴾ الأنفال: ٢٥

*Ku ji tsoron fitina da ba za ta kevanta da waxanda suka yi zalunci cikinku kawai ba. Al-Anfal: l25.*

Don haka, idan fitina ta auku ba mai tsira daga dauxarta sai fa wanda Allah ya tsare.

Amma cewar da ya yi, menene laifin Ali *Raliyallahu Anhu* ga kisan Usman? Duk ya warware abin da ya yi can baya. Ba da farko ya ce Ali *Raliyallahu Anhu* na cikin waxanda ke halatta yaqar Usmanu ba har da kashe shi? Da yawa cikin mabiyan Ali da na Usman na da ra'ayin cewa, Ali na da hannu cikin wannan juyin mulki da ya kai ga kashe Usman. Waxannan sun ce Ali na da hannu don ba su son Usman. Suna son su ce ko Ali ma ba ya sonsa. Waxancan su kuma sun ce Ali na da hannu don ba su son Alin. Suna son su shafa masa kashin kaji. Amma mafi yawan musulmi sun san qarya vangaroran biyu ke yi.

Wannan fa shi ne rikicin. 'yan Shi'ah na ganin cewa, Ali *Raliyallahu Anhu* ya halasta kisan Usman, kai har ma da Abubakar da Umar. Kuma wai, wannan na cikin abubuwan da ake neman kunsanci ga Allah da yin su. To, sai ga wannan shi ko yana cewa, mene ne laifin Ali *Raliyallahu Anhu* a cikin wannan kisan? Ka ga babu wanda ya ke tsarkake Ali bisa adalci sai Ahlus-Sunnah.

Ka tuna kuma ya ce: “Ya aka yi Xalhatu da Zubairu suka halatta wa kansu yi mata xa’a a kan wannan? Da wace irin fuska za su sadu da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*? Ga shi kuwa da xayanmu ya yi magana da matar wani, ya fitar da ita daga gidanta, ya yi tafiya tare da ita, da ya zama mafi girman maqiyinmu”.

Wannan shi yake daxa bayyana jahilicin ‘yan Shi’ah da takin saqarsu. Su ne fa suke jifar Nana A’ishah da mafi munin abu a duniya ga ‘ya mace, bayan Allah ya tsarkake ta. Amma su faxi wannan magana, wai magana da matar wani ma laifi ce! To, ce ma ta karuwa fa? Qazafinsu kuma bai tsaya ga matar iyalin Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba, a’a, har da matan wasu daga cikin Annabawa. Kamar yadda suka ce matar Annabi Nuhu *Alaihis Salamu* mazinaciya ce, kuma wai, xanta da Annabi Nuhu ya kirazuwa shiga jirgin tsira bai karva ba, wai ba xansa ne ba, ta hanyar zina ta same shi. Sai suna karkatar da ayoyin Alqur’ani don su qarfafa son ransu, su samu mashiga ta yin suka ga iyayen muminai. Hakanan ita ma matar Annabi Ludu *Alaihis Salamu* ba ta tsira daga mugun bakinsu ba. Sun yi mata qazafi suna kafa hujja da ayar da ta ce, matar Nuhu da ta Luxu sun yaudare shi (Suratut-Tahrim:10). To, waxannan ne za su ce wani ya fita da matar Annabi kuma ya yi laifi?

‘Yan-sha-biyu dai sun yi kama da Munafukai da Fasiqai waxanda su ka jefi uwar muminai da alfasha, kuma ba su tuba ba. A kan irin su ne Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi huxuba yana cewa: “Wane ne zai yi mani uzuri ga mutumin da ya kai matuqa wajen cutarwa ga iyalina? Wallahi ban san wani abu game da iyalina ba sai alheri. Wanda kuma suka tuhumce da shi mutun ne da, wallahi ban san wani abu game da shi ba sai alheri”.

Ga al’ada duk mutumin da aka ce ma mijin mazinaciya an gama kai maqura ga cutata ma sa. Wannan kuwa shi ne abin da ‘yan-sha-biyu ke yi wa Annabawa. Wal’iyazu billahi.

Babu wani zargin da aka sa wa haddi sai qazafin zina. Don babu wani zargi da ya kai shi haxari. Kai ko kafirci aka zargi mutum da yi, yana iya qaryatawa ta hanyar bayyanar da ayyukan musulunci. Amma ita zina ya za a iya qaryata ta?

Sannan daga cikin jahilcin ‘yan-sha-biyu suna girmama nasabar Annabawa amma suna sukar matansu. Suna wannan ne don kawai tsananin ta‘assubanci da son rai, wai suna son girmama Fatima da Hasan da Husaini. Amma sai su soki A’isha Uwar Muminai. Don haka suke cewa Azara mahaifin Annabi Ibrahim mumini ne. Haka su ma mahaifan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Wai suna gudun in aka ce wani Annabi mahaifansa na iya zama kafirai, wani ya kafa masu hujja da cewa, ko ‘ya’yansa na iya zama kafirai. To, ka ji kai.

Shi dai Xalhatu ko Zubairu ko ma duk wani bare (ajanabi) ba su xauki uwar muminai ba. Don a cikin sansaninsu akwai muharramanta kamar Abdullahi xan Zubairu; xan yarta, wanda shari’a ta yarda ya kaxaita da ita bisa

ga nassin Alqur'ani da Sunnah da ijimain malamai. Haka ma tafiyar mace tare da muharramanta halal ne kamar yadda ya ke sanannen abu a shari'ah. Ko a sansanin Ali xan Abu Xalib *Raliyallahu Anhu* ba don qaninta Muhammad Xan Abubakar ya miqa hannunsa ya fito da ita ba, ai da an sami wani da ba muharrami ba ya yi hakan. Wannan ne ya sa Nana A'ishah ta yi masa mummunar addu'a da ya miqa hannunsa gare ta kafin ta gane shi. Ta ce: "Wannan hannun wa ne? Allah ya qona shi". Nan take sai qanenta ya ce: "A nan duniya ba a lahira ba". Da ta ji muryarsa sai ta ce: "A nan duniya ba a lahira ba". Haka kuwa aka yi, don an qona shi a Masar.

Game da maganarsa a kan goyon bayan da mutane suka ba A'ishah kuma wai, ba su taimaki Fatima a rikicinta da Abubakar ba, a cewarsa. Sai mu ce masa, ganwo ya jirkice ma dame kenan. Domin duk mai hankali ba ya shakkar cewa, Sahabbai na tsananin son Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da kuma girmama shi. Suna kuma ganin girman dangin Manzon Allah da 'ya'yansa fiye da yadda suke ganin girman Abubakar da Umar. Kuma babu shakka sun fi son Manzon *Sallallahu Alaihi Wasallama* a kan kawunansu da iyalansu. Ba mai hankalin da ka shekkar cewa, dukkan Larabawa na biyayya ga 'yan gidan Abdumanafi, dangin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* suna girmama su fiye da yadda suke girmama Tamimawa da Adiyawa waxanda Abubakar da Umar suka fito daga cikinsu. Don haka ne lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rasu aka ce wa Abu Quhafata, mahaifin sayyidina Abubakar: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rasu. Sai ya ce: "Babban abu ya auku. To, wa ya maye gurbinsa?" Aka ce masa: "Abubakar". Ya ce: "'Yan gidan Abdumanafi da Makhzumawa duk sun yarda?" Aka ce masa: "Qwarai kuwa". Sai ya ce: "Wannan falalar Allah ce, da yake bada ita ga wanda ya so".

Wannan ne ya sa lokacin da Abu sufyana ya zo wurin Ali ya ce masa: Kun kuwa yarda cewa shugabanci ya zamo cikin Tamimawa (qabilar su Abubakar)? Sai ya ce masa: Ya Abu sufyan! Lamarin musulunci ba irin na jahiliyyah ne ba.

To tunda yake ba'a samu wanda ya ce an zalunci Fatima ba daga cikin Sahabbai, ko ya ce tana da wani haqqi wurin Abubakar ko Umar da suka hana ma ta, ko ya ce su biyun azzalumai ne. Wannan ya nuna cewa musulmi basu xauki al'amarin a haka ba. Da ba abin da zai hana su su taimake ta.

To, yaya mutanen da suka tashi tsaye wajen fansar jinin Usmanu *Raliyallahu Anhu* har suka zubar da jinainansu sakamajon wannan za ace ba za su taimakawa wanda ya fi soyuwa gare su akan Usmanu ba, ina nufin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da iyalan gidansa?

### 2.9.12 Suna Jin Haushin a Kira ta "Uwar Muminai"

Xan Shi'ar ya ce: Sun kira ta "Uwar Muminai", amma ba su kira sauran matan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da wannan sunan ba. Ba su kira qanenta Muhammad xan Abubakar "Kawun muminai" ba duk da

xaukakarsa da ta babansa da kusancinsa ga ita A'ishar. Sai suka kira Mu'awiyah da wannan suna don kasancewarsa xan'uwan Ummu Habiba xiyar Abu Sufyana, ga shi ko Muhammad xan Abubakar da babansa sun fi xaukaka akan Mu'awiyah da 'yar'uwarsa.

**Martani:**

Babu qanshin gaskiya sam a cikin maganar cewa, A'ishah kaxai Ahlus-Sunnah ke kira "Uwar Muminai" ba da sauran matan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba. Ni ban sani ba, wannan mutum da ire-irensa da gangan suke qira qarya ko dai Allah ne ya taushe basirarsu don tsananin bin son zuciya ta yaddaba su iya gane qarya idan sun faxe ta? Wannan ya zan kamar yadda suke zargin wasu maqiyan Ali da cewa, sun musanta Husaini jikan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne a lokacin da za su kashe shi. Ya ko za ayi wani ya musanta nasabar Husaini in ba wanda Allah ya taushe wa basira don bin son zuciyarsa ba?

To, su 'yan-sha-biyu sun fi kowa inkarin gaskiya da gangan kuma sun fi kowa makanta. Ka ga a cikinsu akwai *Nusairiyyah* masu cewa Hasan da Husaini ba xiyan Ali ba ne, xiyan Salmanul-Farisi ne. Akwai daga cikinsu masu cewa Ali bai mutu ba. Akwai kuma masu cewa Abubakar da Umar ba su kwance tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin xakin A'ishah. Cikinsu kuma akwai masu cewa Ruqayyah da Ummu Kulthum ba xiyan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ba, don kawai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya aurar da su ga sayyidina Usmanu *Raliyallahu Anhu*. Suka ce 'ya'yan wani mushriki ne da Nana Khadija ta haifa ma sa kafin ta auri Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Banbance min jahilcin waxannan mutane da jahilcin wasu daga cikin waxanda suka kashe Husaini *Raliyallahu Anhu* waxanda suka ce sam, ba su yarda Husaini jikan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ba.

Musulmi dai a duk in suke sun san cewa, kowacce daga cikin matan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ana kiran ta "Uwar Muminai". Kuma wannan magana nassin Alqur'ani ce. Kamar yadda Allah Ta'ala ya ce: *Annabi ya fi cancantar gabaci ga muminai a kan kawunansu. Kuma matansa iyayen muminai ne. Suratul Ahzab:6.* Wannan sanannen abu ne. Saninsa bai kevanta da malamai ba. Kuma musulmi sun haxu a kan cewa, haram ne wani musulmi ya auri xaya daga cikin matan da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya aura. Haka kuma girmama su wajibi ne. Suna da alfarmar girmamawa da haramci, amma ba ya halatta wani musulmi ya kaxaita da su kamar yadda yake kaxaita da uwar cikinsa. Duk da yake hukuncisu hukuncin uwaye mata ne, amma kuma suna da banbanci ta wannan fuska. Don haka ne malamai ke savani game da kiran iyayensu kakannin muminai ko 'yan'uwansu kawunnan muminai. Wasu malamai suka ce ana iya kiran su haka. Kuma wannan hukunci bai kevanta da Mu'awiyah ba, a'a, ya haxa da Abdurrahaman da Muhammad 'yan'uwan A'ishah da Ubaidullahi da Asimu da Abdullahi

‘yan’uwan Hafsatu da Amru xan Haris ‘xan’uwan Juwairiyah da Utbatu xan Abu sufyana xan’uwan ita Ummu Habiba da Muawiyah.

Ra’ayi na biyu na malamai shi ne na masu ganin ba a iya kiran ‘yan’uwan matan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* maza ko mata da sunan kawunne ko innonan muminai, don rashin tabbatuwar haramcin aure a tsakaninsu da miminai. Nassi da haxuwar kan malamai sun nuna cewa, ana iya auren ‘yan’uwansu kamar yadda Abbas ya auri Ummul-Fadhli ‘yar’uwar Maimunatu ‘yar Harisu har ta haifa masa Abdullahi da Falalu. Abdullahi xan Umar da Ubaidullahi da Mu’awiyah da Abdurrahaman xan Abubakar da qaninsa Muhammad duk sun auri mata muminai. Da kuwa kawunnensu ne na nasaba da ba su aure su ba.

Waxanda ma suka ce masu kawunnen muminai daga cikin malamai ba jayayya suke akan wannan hukunci ba. suna dai nufin sun samu darajar surukuta da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Amma wannan ya fi shahara game da sayyidina Mu’awiyah, kamar yadda ya fi shahara da zama *Katibul Wahyi*, marubucin wahayi, duk da yake ba shi kaxai ya rubuta wahayi ba. Kuma Mu’awiyahn dai ne ya yi suna da *Radifu Rasulillah,* abokin hawan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, alhalin ba shi kaxai ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya hau dabba tare da shi ba. Duk waxannan abubuwa ba a faxe su ga Mu’awiyah don ya kevanta da su ba kamar yadda muka gani.

Sai cewa, Ahlus-Sunnah sun xaukaka darajarsa. Idan yana nufin darajarsa ta gida sai mu ce, ai wannan darajar ba ta da wani matsayi a gurinku. Don ga shi kuna sukar babansa da ‘yar’uwarsa matar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Su kam Ahlus-Sunnah ba su fifita kowa don kawai matsayin gidansu, sai dai don tsoron Allansa. Kamar yadda maxaukakin sarki ya ce:

﴿إِنَّ أَكْرَمَكُمْ عِندَ ٱللَّهِ أَتْقَىٰكُمْ﴾ الحجرات: ١٣

*Haqiqa mafi xaukakarku shi ne mafi tsoron Allanku. Suratul Hujurat:13.*

In kuma yana nufin Ahlus-Sunnah na girmama Mu’awiyah ta fuskar gabaci da hijira da taimakon Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da jihadi saboda Allah, to, ba su ce yana cikin magabatan farko ba. In kuma ma ta fuskar ilimi ne da riqon addini, Ahlus-Sunnah ba su ce ya fi kowa ba. To, ina laifin an faxi gaskiya ga mutum don kuna qin sa?

Kuma wai, inji shi, ‘yar’uwar Muhammad da babansa sun fi na Mu’awiyah. To, a wurin wa suka fi na Mu’awiyah? Su Ahlus-Sunnah, a wurinsu dangantaka ita kaxai ba ta fifita mutum, balle a ce ‘ya’uwantakar Muhammad ga A’ishah ta fifita shi. Kuma Mu’awiyah ba zai cuta wa Muhammad don ya fi shi asaba, kamar yadda magabatan farko irin su Bilalu da Ammar da Suhaibu da Khabbabu da ire-irensu ba su cutu da ‘yan girma irin su Abu Sufyana da suka fi su asaba ba, tun da su sun makara ga shiga musulunci a

kansu. Haka sauran waxanda suka shiga musulunci daga baya irin su Abu Sufyana xan Harisu da Aqilu xan Abu Xalib da Mu'awiyah da Yazidu, 'yan manyan gidaje ne, amma nasabarsu ba ta fifita su a kan su Bilal xin ba.

### 2.9.13 Sukar 'Yan Shi'ah ga Mu'awiyah

Xan Shi'ar ya ce: Tare da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya la'anci Muawiyah, 'yantacce xan 'yantacce, la'antacce xan la'antacce. Ya kuma ce: Idan kuka ga Mu'awiyah a kan minbarina, to, ku kashe shi. Ya kuma kasance cikin waxanda ake tausasa zukatansu. Ga shi kuma ya yaqi Ali wanda ko a wurin Ahlus-Sunnah shi ne halifa na huxu. Kuma shugaba ne na gaskiya. Wanda duk ya yaqi shugaba na gaskiya kuwa ya zama mai tsallake iyaka, azzalumi.

Xan Shi'ar kuma sai ya alaqanta wannan ga wai, son da Muhammad xan Abubakar ke yi wa Ali *Raliyallahu Anhu* da kuma cewa shi ya rabu da ubansa Abubakar *Raliyallahu Anhu* kuma wai, da kasancewar Mu'awiyah *Raliyallahu Anhu* na qin Ali *Raliyallahu Anhu.* Ya ce kuma, sun kira shi mai rubuta wahayi, ga shi bai rubuta ko kalma xaya ba ta wahayi. Wasiqu ne kawai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya sa shi ya rubuta. Kuma wai mutane goma sha huxu sun rubuta wahayi a gaban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Na farkonsu, inji shi, kuma mafi kusancinsu da Manzon Allah da kevantuwa da shi, shi ne Ali xan Abu Xalib *Raliyallahu Anhu.* Ya ce: Ga shi kuwa Mu'awiyah bai gushe mushriki ba tsawon lokacin da aka aiko Manzon Allah xin; yana qaryata wahayi yana izgili da shariah.

**Martani:**

Cewa wai, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya la'ani Mu'awiyah kuma ya ce a kashe shi idan a gan shi a kan mimbari. Wannan magana ba a iya samun ta a cikin littafan musulunci da ake dogara a kansu, kuma ma dai qarya ce zunzurutunta. Xan Shi'ar da ya riwaito ta kuma bai ambata mata isnadi ba balle a bincike shi. Abul Faraj Ibnul Jauzi ya ambace shi cikin hadissan qarya da aka jingina ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Daga cikin abin da ke tabbatar da qaryar wannan labari shi ne cewa, akwai mutane da dama da suka hau minbarinsa waxanda kuma Mu'awiyah ya fi su daraja bisa ga ijima'in musulmi. To, idan kisansa ya wajaba don kawai ya hau minbari, kenan wajibi ne a kashe duk waxancan. In kuma ya wajaba ne don ya yi shugabancin da bai cancanta ba, to wajibi ne a kashe duk waxanda shi Mu'awiyahn ya fiya, cikin waxanda suka zo bayansa. Wannan kuwa ya sava wa abin da hadissan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* suka tabbatar na hani ga kisan shugabanni. In da za ayi haka da zai zama sanadiyyar varna da yawaita kisann musulmi, sai an gwammace shugabancin azzaluman a kan wannan varna. To, ya ko za a yi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi umurni da abin da sharrinsa ya fi alherinsa?.

Xan Shi'ar dai zato ya ke ya aibata Mu'awiyah ne da ya ce masa "'Yantacce xan 'yantacce". Alhali wannan ba aibi ba ne, don waxanda aka 'yanta su ne waxanda suka shiga musulunci ranar da aka buxa garin Makka, waxanda adadinsu ya kai dubu biyar. Daga cikinsu kuwa akwai waxanda Allah ya xaukaka su har suka zama cikin mafifitan musulmi kamar Harisu xan Hishamu da Suhailu xan Amru da Safwanu xan Umayyata da Ikrimatu xan Abu Jahali da Yazidu xan Abu Sufyana xan Harisu, xan baffan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* wanda a da yake izgili da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yana yi masa zambo, sai daga baya ya musulunta, kuma ya kyautata musuluncin nasa. Haka ma Attabu xan Usaidu wanda Manzon Allah ya naxa shi gwamnan Makka na farko a musulunci. Duk waxannan da ire-irensu 'yantattu ne. To, ina aibi kenan ga zama 'yantacce?

Mu'awiyah xan Abu Sufyana yana cikin waxanda suka kyautata musuluncinsu. Wannan ne ya sa Umar *Raliyallahu Anhu* ya naxa shi kwamandan Jihadi a qasar Sham bayan rasuwar xan'uwansa Yazidu. Yazidun nan kuwa na daga cikin mafifitan musulmi waxanda Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* suka naxa a muqamai masu alaqa da yaqar kafirai, musamman a qasar Sham. Waxannan shugabanni su ne: Yazidu xan Abu Sufyana da Shuraihu xan Hassan da Amru xan Asi da Abu Ubaidata da Khalidu xan Walidu. A lokacin da Yazidu xan Abu Sufyana ya rasu sai Umar ya ba Mu'awiyah shugabancin Sham. Umar *Raliyallahu Anhu* kuma bai ji tsoron wani zargi ba. Kamar yadda ba a zargin sa da son rai wajen zaven shugabani. Ba ya kuma cikin masoyan Abu Sufyana. Abin da ma za a iya cewa shi ne, Umar na cikin waxanda suka fi kowa qin baban Mu'awiyah, wato Abu Sufyana kafin ya musulunta. Har ma lokacin da Abbas, baffan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kawo Abu Sufyana ranar buxa garin Makka, Umar ya yi kwaxayin kashe shi, sai da magana ta tsananta tsakaninsa da Abbas xin don qin da yake yi wa Abu Sufyana. Ka ga kuwa da Umar bai san ya cancanci shugabanci ba da bai shugabantar da shi ba. Don ba wani abin duniya da yake nema a wurinsa.

Sai cewar da ya yi Mu'awiyah na cikin waxanda ake kyautatawa don kwaxaita masu shiga musulunci. Haka ne. Kuma mafi yawan waxanda aka 'yantar kamarsa, su ma haka suka kasance. Daga cikinsu kuwa akwai mafifitan musulmi kamar Harisu xan Hisahamu da Ikrimatu xan Abu Jahali da Suhailu xan Amru da Safwan xan Umayyata da Hakimu xan Hizamu. Waxannan babu shakka suna cikin zavavvun musulmi. Kuma mafi yawan waxanda aka kyautata ma don kwaxaitar da su, sun yi kwaxayin musuluncin, sun kyautata shi ta yadda xayansu ya kasance yana shiga musulunci da safe don xan wani abu na duniya, amma kafin marece musulunci ya zame ma sa mafi soyuwar a duniya.

Yaqar Ali kuwa da ma duk wani shugaba na gaskiya tana iya kasancewa bisa ga tawili, ko bisa ga son zuciya, ko haxuwar abu biyun baki xaya, wanda shi ne ya fi yawan faruwa. To, kowanne ne ya kasance ba zai zama suka ga

fahimtar Ahlus-Sunnah ba, don ba su tsarkake Mu'awiyah ba balle wani wanda ya fi shi daga aikata savo ko kuskuren ijtihadi. Abin da suka ce shi ne, savo akwai abin da ke shafe shi, kamar tuba da istigfari da ayyukan alheri da musibun da ke zama kaffara ga mutum da sauransu. Wannan kuma ya haxa da Sahabbai da waxanda ba su ba.

Abu na biyu kuma shi ne: Ahlus-Sunnah suna kan turba guda xaya ne a nan. Amma ku a cikin takin saqa kuke. Domin kuwa maqiyan Ali *Raliyallahu Anhu* masu kafirta shi da masu fasiqantar da shi, Harijawa da Mu'utazilawa da Marwaniyyawa da ire-irensu masu shakka ga addininsa, in da za su ce maku: Minene hujjar da ke tabatar da imanin Ali *Raliyallahu Anhu* da shugabancinsa da adalcinsa? Ba ku da abin da za ku ce sai an samu labari mutawatiri mai nuna cewa ya musulunta. Nan take sai su ce maku, ai wannan ko sauran Sahabbai da Tabi'i da Umawiyyawa da Yazidu da Abdulmalik xan Marwan da sauransu duk an samu labari mutawatiri a kan musuluntarsu, amma kun kafirta su. To, me ya banbanta su da Ali? Ku kun kafirta su, mu mun kafirta shi. Sukar da ku ke yi game da imanin waxancan ta fi sukar da muke yi ga imanin Ali, don waxanda kuke suka sun fi waxanda muke suka yawa.

Idan kuma kuka kafa hujja da yabon da aka yi a cikin Alqur'ani, sai su ce ma ku, ayoyin Alqur'ani ba kan Ali xai suka sauka ba. Sun game muminai a lokacin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.* Kenan sun haxa da Abubakar da Umar da Usmanu da sauransu. Kamar yadda ayoyin suka haxa da Ali. To, ga shi kun kafirta sauran Sahabbai kun bar shi daga cikin waxanda Allah Ta'ala ya yaba duk da yawansu. To, mu ma mun fitar da Ali *Raliyallahu Anhu* daga cikinsu shi kaxai mun bar saura. Haka Hawarijawa za su ce muku.

In kuwa kuka ce za ku kafa hujja da abin da aka riwaito daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* game da falalolinsa, sai su ce maku, waxannan falalolin ai Sahabbai ne suka riwaito su kamar yadda suka riwaito sauran falalolin Abubakar da Umar da Usman. In kun yarda da adalcinsu da gaskiyarsu, to, ku karvi duk abin da suka riwaito mana. In kuma ba ku yarda da su ba to, duk hadissan falalar Ali sun zama wofi kenan.

Sai cewar da ya yi wai, don Muhammad xan Abubakar na son Ali ne da kuma rabuwar da ya yi da babansa, shi ya sa Ahlus-Sunnah suke qinsa da fifita Mu'awiyah a kansa. Wannan qarya a fili ta ke. Don Muhammad xan Abubakar bai ko san rayuwar babansa ba, don bai ma shekara uku ba a lokacin mutuwarsa. Da ya girma kuma yana cikin masu darajanta mahaifin nasa don da bazarsa yake rawa.

Sai cewar da xan Shi'ar ya yi, wai, an ce wa Mu'awiyah kawun muminai ba a ce wa Muhammad ba don yana son Ali *Raliyallahu Anhu* alhalin shi Mu'awiyah *Raliyallahu Anhu* yana qin sa. Wannan ma qarya ce. Don Abdullahi xan Umar duk ya fi su cancantar a ce masa hakan, ga shi kuwa bai taimaki Mu'awiyah ko Ali a wurin yaqi ba. Ya kasance yana girmama Ali *Raliyallahu Anhu* yana faxin darajojinsa, yana kuma son sa. Ya kuma yi wa Mu'awiyah mubaya'a a lokacin da mutane suka haxu a kansa. 'Yar'uwarsa

Hafsa kuma ta fi 'yar'uwar Mu'awiyah, haka ma mahaifinsa Umar ya fi na Mu'awiyah. Kuma mutane sun fi son sa da xaukaka shi a kan Mu'awiyah da Muhammad xan Abubakar, Allah ya yarda da su baki xaya. To, duk da haka shi shi xan Umar bai shahara da sunan kawun muminai ba. Saboda haka cewa an qi sa ma Muhammad xan Abubakar wannan suna don yana qin Ali zuqi ta mallau ce kawai.

Sai kuma cewar da ya yi, wai, an kira shi mai rubuta wahayi ga shi bai rubuta ko kalma xaya ta wahayi ba. Wannan magana ce maras-kai. Don ko ina dalilin cewa bai rubuta ko kalima xaya ta wahayi ba sai dai wasiqu?

Maganar da ya yi game da yawan marubutan wahayi, da cewa sun fi goma, kuma na farkonsu, mafi kusancinsu da kevantuwa ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne Ali. Babu shakka cewa, Ali *Raliyallahu Anhu* na cikin marubutan wahayi, kamar yadda ya rubuta yarjejeniyar da aka yi tsakanin musulmi da mushrikai a ranar Hudaibiyyah. Amma Abubakar da Umar ma na ciki. Don sun kasance suna rubuta masa wahayi su ma. Kuma babu shakka Zaidu xan Thabitu na cikinsu. Don shi ya rubuta ayar da ta ce: *Waxanda suka zauna gida daga cikin muminai ba su daidaita da waxanda suka fita jihadi. An-Nisa'i:95.* Haka shi ma Usmanu da Amiru xan Fuhairata da Abdullahi xan Arqamu da Ubayyu xan Ka'abu da Thabitu xan Qaisu da Khalidu xan Sa'idu xan Asi da Hanzalatu xan Rabi'u Al-Asadi da Mu'awiyah da Shurahabilu xan Hasanata, dukkansu Allah ya qara masu yarda.

Amma cewar da ya yi wai, Mu'awiyah musiriki a duk tsawon rayuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Amsar maganar ita ce, kowa ya san cewa, Mu'awiyah da xan'uwansa Yazidu da babansu duk sun musulunta ne a shekarar da aka ci Makka da yaqi kafin cikawar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da kusan shekaru uku. To, yaya zai masa mushriki duk tsawon rayuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*? Mu'awiyah ai qaramin yaro koda aka aiko Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama,* don lokacin uwarsa Hindu ke tawansa. Mu'awiyah ya musulunta a shekarar da aka ci Makka tare da xan'uwansa Yazidu da Suhailu xan Amru da Safwanu xan Umayyata da Ikrimatu xan Abu Jahali da Abu Sufyana xan Harbu. Duk waxanda sun fi nuna gaba da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kafin musuluntarsu fiye da Mu'awiyah.

### 2.9.14 'Yan Shi'ah Sun Tsani Mu'awiyah

Xan Shi'ar ya ce: Mu'awiyah ya kasance a qasar Yaman koda aka ci Makka. Yana can yana sukar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama,* har ma ya rubuta wa babansa Sakhru xan Harbu waqe yana aibanta shi don ya shiga musulunci yana ce masa: Ka karkace, tunda ka shiga addinin Muhammadu. Sai ya rubuta masa.

An dai buxa garin Makka ne a cikin watan azumi na shekara ta takwas bayan hijira. Mu'awiyah yana a kan kafircinsa, yan gudun Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* don ya ba da umurnin a kashe shi, inji xan Shi'ar. Sai ya

gudu zuwa Makka. Amma da ya ga ba wata mafaka sai ya tafi ala tilas wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce ya musulunta. Musuluntar tasa ta kasance ne watanni biyar kacal kafin rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Da zuwansa sai ya jefa kansa ga Abbas, wanda ya nema masa afuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma ya samu. Sannan Abbas xin ya nema masa aka ba shi damar yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* rubutu don ya samu girma. Sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yarda ya haxa shi da sauran mutane goma sha huxu. To wane rabo ya samu a cikin wannan aiki koda mun ba shi wannan suna na marubucin wahayi a cikin wannan xan qanqanin lokaci? Tattare da cewa Zamakhshari, xaya daga cikin malaman Hanafiyyah ya ce a cikin littafansa mai suna *Rabi'ul Abrar* : Daga cikin masu rubuta wahayi akwai Abdullahi xan Sa'adu xan Abu Sarhi, kuma ya yi ridda ya koma mushriki. A kansa ne ma aya ta sauka cewa:

﴿ وَلَٰكِن مَّن شَرَحَ بِٱلْكُفْرِ صَدْرًا فَعَلَيْهِمْ غَضَبٌ مِّنَ ٱللَّهِ وَلَهُمْ عَذَابٌ عَظِيمٌ ﴾ (١٠٦)

النحل: ١٠٦

*Amma wanda ya buxe wa kafirci qirjinsa, to, fushin Allah na kansu. Kuma suna da azaba mai girma. An-Nahli:106.*

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Abullahi xan Umar ya ruwaito yana cewa: Na zo wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, sai na ji yana cewa: Yanzu wani mutum zai zo muku wanda ba zai mutu a kan sunnata ba. Wai, sai Mu'awiyah ya shigo masallaci. Sai kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fara huxuba, shi kuma Mu'awiyah ya riqa hannun xansa Zaidu ko Yazidu ya fita bai saurari huxubar ba. Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Allah ya la'anci wanda ya ja, da wanda aka ja xin. Kaicon al'ummata a ranar da Mu'awiyah zai munana ma su.

Ya ci gaba da cewa: Mu'awiyah ya kai matuqa ga yaqar Ali, kuma ya kashe da yawa daga cikin zavavvun Sahabbai. Sannan ya la'anci Ali akan minbari. Aka kuma ci gaba da wannan zagi nasa har tsawon shekaru tamanin sai da Umaru xan Abdul'aziz ya yi sarauta sannan ya hana haka. Shi ne kuma ya kashe Hassan ta hanyar sa masa guba. Xansa Yazidu kuma ya zo ya kashe Husaini, ya qwace matarsa. Ubansa kuma shi ya karya wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* xaya daga cikin haqoransa, uwarsa kuma ta ci antar Hamza baffan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

**Martani:**

Cewar da ya yi Mu'awiyah ya kasance a qasar Yaman yana sukar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, wai har ya zargi babansa Sakhru a kan ya musulunta. Duk wannan ba gaskiya ba ne. Don yana a Makka ne aka ci ta da yaqi. Babansa kuwa ya musulunta kafin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya shiga garin, a daidai wurin da Manzon ya sauka, in da ake kira *Marruz-Zahran*, a wannan daren da Annabi ya sauka. Nan ne Abbas ya ce ma

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*: Ka ga Abu Sufyana yana son girma. Ka yi masa wani abu kan haka. Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Duk wanda ya shiga gidan Abu Sufyana ya tsira”.

Amma cewar da ya yi an buxe Makka a ranar takwas ga watan azumi. Wannan gaskiya ne.

Sai cewa Mu’awiyah yana a kan kafircinsa har ma ya gudu daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* don Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ba da umurnin a kashe shi, sai da ya ga ba mafaka sannan ya tafi tilas wurin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce ya musulunta a zahiri. Kuma wai an yi haka ne watanni biyar kacal kafin rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Duk wannan zulala ce da bayyanannar qarya. Mu’awiyah kam ya musulunta ne a shekarar da aka buxe Makka. Duk masana sun haxu a kan haka. To, ina cewar da ya yi can baya: “Mu’awiyah na cikin waxanda ake rarrashi, ana basu dukiya don a kwaxaitar da su ga musulunci”? Ai duk wanda aka rarrasa an yi masa haka ne daga cikin ganimar yaqin Hunainu wadda aka samu daga Hawazinawa. In ko har Mu’awiyah ya gudu, to, ta yaya aka yi rarrashinsa? In kuma ya musulunta ne watanni biyar kafin rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* to, kenan ba a ba shi komai ba daga cikin ganimar Hunainu. Kuma duk wanda manufarsa ita ce yin imani ko don ya kare kansa, to, ba ya buqatar kyautatawa.

Daga cikin abin da ke bayyana qaryar wannan xan Shi’ar shi ne abin da ya tabbata a tarihi cewa, ba wanda ya jinkirta musulunta daga cikin Quraishawa har zuwa lokacin da ya ambata. Kuma duk malaman tarihi sun haxu akan cewa Mu’awiyah ba ya cikin waxanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya halatta jininsu a shekarar da aka buxe Makka.

Kuma tuhumar da ya yi wa Ahlus-Sunna cewa, suna siffanta Mu’awiyah da marubucin wahayi shi kaxai ba da kowa ba, ba ta da qamshin gaskiya. A cikin Ahlus-Sunnah babu wanda ya ce Mu’awiyah ya kevanta da wannan siffar shi kaxai.

Game da riddar Abdullahi xan Sa’adu xan Abu Sarhi kuwa, wannan ta faru, amma ai ya sake tuba ya dawo musulunci. Ayar da ya faxa kuma ba kansa ta sauka ba. Ta ma sauka ne a Makka lokacin da aka tilasta wa Ammaru da Bilal yin ridda; su kafita. Shi ko wannan mutum ya yi ridda ne a Madina bayan hijira, sannan ya sake tuba. Kai ko an qaddara cewa a kansa ayar ta sauka, to, amma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya karvi tubansa, da mubaya’arsa.

Ruwayar da ya kawo daga Abdullahi xan Umar *Raliyallahu Anhu* kuma game da fitar Mu’awiyah daga masallaci don kar ya ji huxuba.. har zuwa qarshen maganarsa. Ba zai iya kare waxannan maganganu ba ballantana ya tabbatar da ingancinsu. Malaman hadisi kuma sun daxe da tada masu wannan qarya. Shi ya sa ba zaka same ta ba a cikin xaya daga cikin littafan hadisi da ake dubawa, balle a samu wani sannanen isnadi da ake jingina ta gare shi. Ka ga don cikar jahilcinsa sai ya jingina wannan magana ga Abdullahi xan Umar. Shi ko ya fi kowa nisantar zagin Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi*

*Wasallama.* Ga shi kuma ya tabbata cewa, Abdullahi xan Umar *Raliyallahu Anhu* ya yabi Mu'awiyah, in da ya ce: "Ban ga wanda ya fi Mu'awiyah iya tafi da shugabanci ba bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama".* Sai aka ce masa: "Har da Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma?"* Ya ce: "Abubakar da Umar sun fi shi, amma ban ga wanda ya fi shi iya shugabanci ba, bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama".*

Imamu Ahmad xan Hambali ya kira Mu'awiyah "Shugaba mai haquri". Ya ce kuma, ya kasance mai karimci da yawan kau da kai daga wautar jahilai.

Sannan huxubobin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba guda ba ne. Ya kan yi huxuba a ranaikun Jumu'a da idi da lokacin Hajji da dai sauransu. Kuma Mu'awiyah da babansa na halarta kamar yadda sauran musulmi ke yi. Ko kana nufin a kowane lokaci Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* zai yi huxubar su fita suke yi su tafiyarsu ba su saurarawa? Kuma duk aka qyale su? Wannan ai ba qaramar suka ba ce ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da sauran Sahabbansa.

Cewa ya kama hannun xansa Zaidu ko Yazidu, to Mu'awiyah dai ba ya da xa mai suna Zaidu. Shi kuma Yazidu malaman tahiri sun haxu a kan cewa, an haife shi ne lokacin halifancin Usmanu xan Affana *Raliyallahu Anhu.* Mu'awiyah bai haifu ba sam, a lokacin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.*

Hafizi Abul fadhli Ibnu Nasir ya ce: Mu'awiyah *Raliyallahu Anhu* ya nemi aure a lokacin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* amma bai samu ba saboda talauci. Sai zamanin Umar ya samu yi. Aka kuma haifar masa Yazidu a lokacin halifancin Usmanu xan Affana a shekara ta ashirin da bakwai bayan hijira.

Game kuma da yaqar Ali. Babu shakka cewa, rundunonin biyu sun yi yaqi a Siffin. Mu'awiyah *Raliyallahu Anhu* kuwa bai so yaqin ba tun da farko. Kai ya ma fi kowa gudun yaqin. Kuma an fi shi son yinsa.

### 2.9.15 Tuqa da Warwarar 'Yan Shi'ah

Daga abin da ya gabata, za mu fahimci cewa, maganar 'yan Shi'ah ta fi kowace magana zama maganar shirme da tuqa da warwara. Ga su suna ganin tsananin muni ga yaqar Ali *Raliyallahu Anhu*, amma kuma suna yabon waxanda suka kashe Usmanu *Raliyallahu Anhu.* A shariah kuwa zargi da zunubin waxanda suka kashe Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya fi tsanani a kan wanda ya kashe Ali *Raliyallahu Anhu* don Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya kasance halifan da duk musulmi suka haxu a kan yarda da shugabancinsa, kuma bai kashe musulmi ko daya ba. Suka kashe shi don su tilasta masa barin shugabanci. Don haka uzurinsa na son ci gaba da shugabanci ya fi uzurin Ali *Raliyallahu Anhu* qarfi shi da ya nemi sai an yi masa mubaya'a tun da farko. Usmanu *Raliyallahu Anhu* kuwa ya yi haquri har aka kashe shi bisa ga zalunci, ya yi shahada bai yi faxa don kare kansa ba. Ali *Raliyallahu Anhu* kuwa shi ya

fara yaqar jama'ar Mu'awiyah, ba su fara yaqarsa ba, sun dai yi masa mubaya'a ne.

Wani zai iya cewa, an kashe Usmanu *Raliyallahu Anhu* ne don ya aikata wasu abubuwa da ba a so. To, amma ai waxannan abubuwa ba su halatta tsige shi, ballantana kashe shi. Qorafin da mutanen Sham suka yi a kan Ali *Raliyallahu Anhu* wanda ya hana su yi masa mubaya'a, in aka auna su da qorafe-qorafen waxanda suka kashe Usman za a ga cewa, na mutanen Sham sun xara qarfi.

Hadissan da ke nuna cewa, halifanci zai yi shekaru talatin kuwa, ba mashahurai ne irin shaharar da za ta sa irin mutanen Sham duk su san su ba. Hadissai ne da mutane kevantattu suka riwaito. Ka ga ai ba su ko a cikin Buhari da Muslim da ire-irensa. To, idan hadisin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya shiga duhu ga mutum irin Abdulmalik xan Marwan, hadisin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce wa A'ishah: "Ba don kasancewar mutanenki (Quraishawa) suna sababbin shiga musulunci ba, da na sake gina Ka'aba, in saukar da qofarta qasa, sannan in yi mata qofofi biyu". Abdulmalik sai da ya rosa abin da Abdullahi xan Zubairu ya gina, sannan ya ji wannan hadisi na A'ishah. Sai ya yi fatar da ya san hadisin kafin haka don ya tabbatar da abin da Abdullahi xan Zubairun ya yi. Wannan hadisin na A'ishah kuwa tabbatacce ne a cikin Buhari da Muslim; malamai sun yarda da ingancinsa. To, ka ga cewa shi wannan hadisi na tsawon lokacin halifanci ya shige wa Mu'awiyah *Raliyallahu Anhu* da mabiyasa duhu ya fi sauqin yiwuwa. Ga shi kuma hadisin a farkon shugabancin Ali *Raliyallahu Anhu* ba ya nuna Ali xin shi kansa. An dai gano wannan ne bayan rasuwarsa. Kodayake wannan hadisi ba nassi ne yankakke ba mai kevance wani halifa na musamman. Su ko mutanen Sham cewa suke yi: Idan har Ali ba zai yi mana adalci wajen hannunta mana waxanda suka kashe Usman ba, saboda wani tawili ko don kasawa, to, ba wajibi ba ne mu yi mubaya'a ga wanda zai zalunce mu, ko ya kasa taimakonmu.

Sai cewar da xan Shi'ar ya yi: Wai Mu'awiyah ya kashe da yawa cikin fiyayyun Sahabbai. Sai mu ce masa: Waxanda aka kashe, an kashe su daga cikin vangarorin biyu. Kowane vangare kuma akwai Sahabbai a ciki. Kuma mafi yawan waxanda ke rura wutar yaqin daga cikin vangarorin ba su biyayya ga Ali ko Mu'awiyah. Ali da Mu'awiyah sun fi da yawan mayaqan neman kada a zubar da jini, amma an fi qarfin su. Daman ita don fitina idan da auku masu hikima daga cikin mutane na kasa kashe wutarta. Daga cikin masu hura wutar a vangaroran akwai irin Al-Ashtar An-Nakha'i da Hashimu xan Utbata da Abdurrahaman xan Khalid xan Walid da Abul A'awar As-Sulami da makamantansu. Waxannan na tsanantawa a kan neman fansar jinin Usmanu, waxansu na tsananin qin sa. Wasu kuma na tsananin taimaka wa Ali *Raliyallahu Anhu,* a lokacin da wasu ke qin sa.

Amma abin da ya faxa game da la'antar Ali *Raliyallahu Anhu*, to, kowane sashe daga cikin biyun sun rinqa la'antar junansu kamar yadda suka

yaqi juna. Sun kuma rinqa yin addu'oi akan juna. Kai yaqin da suka yi ma ai ya fi la'anta da harshe tsanani.

Sannan abin mamaki game da 'yan-sha-biyu shi ne ganin laifin an zagi Ali alhalin su, suna zagin sauran halifofi magabatansa, suna kafirta su da duk wanda ya so su. Mu'awiyah *Raliyallahu Anhu* kuwa da da masoyinsa ba su kafita Ali *Raliyallahu Anhu* ba. Harijawa ne dai su ka kafirta shi. Gara su kuwa da 'yan-sha-biyu.

A qashin gaskiya, zagin kowane Sahabi ba ya halatta. Ali ne ko Usmanu ko wani ba su ba. Wanda kuwa duk ya zagi Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhum* to, ya fi girman zunubi a kan wanda ya zagi Ali *Raliyallahu Anhu* koda kuwa ya aikata haka ne bisa tawili, to, tawilinsa ya fi na waxanda suka zagi Ali *Raliyallahu Anhu* muni.

Maganar sanya ma Hassan guba a cikin abinci na cikin abin da wasu mutane suka ambata, amma kuma bai tabbata ba ta hanyar shedu ko iqirarin da ake la'akari da shi. Ba kuma wata riwaya yankakkiya cewa hakan ta auku. Ga shi kuma wannan na cikin abubuwan da ba a iya sani. Sanin gaibu ko sai Allah.

Game da kisan Husaini da cewa Yazidu ya qwace masa mata. Gaskiyar magana ita ce, Yazidu bai yi umurni da kashe shi ba. Duk malaman tarihi sun haxu a kan haka. Amma shi ne ya rubuta wa Ibnu Ziyad cewa, kada ya bari Husaini ya kafa wata sabuwar gwamnati a Iraqi. Shi kuma Husaini *Raliyallahu Anhu* ya zaci cewa, mutanen Iraqi za su cika alqawarinsu da suka rubuta masa; su naxa shi. Sai ya aika masu da xan baffansa, muslim xan Aqilu sun ya samu tabbaci. Amma da ya san cewa, mutanen Iraqi sun yaudare shi, sun kashe Muslim, kuma sun yi mubaya'a ga Ibnu Ziyad, gwamnan Yazidu, sai Husaini *Raliyallahu Anhu* ya yi niyyar komawa. Amma rundunar nan azzaluma ta riske shi, ya kuma nemi su bar shi ya je wurin Yazidu ko wani wurin jihadi, ko ya koma gida, sai suka hana shi. Buqatarsu su kama shi a hannu, wulaqancin da shi kuma Husaini bai xauka ba. Da haka yaqi da su ya zame masa dole, kuma cikin haka ne suka kashe shi bisa zalunci, ya samu shahada. A lokacin da wannan labarin ya kai ga Yazidu ya nuna damuwa da jin ciwo ainun. Kuma an yi kuka a gidansa sosai. Ba a kuma tava matarsa ba, sam. A maimakon haka ya girmama iyalin Husaini, ya yi masu kyauta, ya sa aka mayar da su gida.

Sai kuma cewar da xan Shi'ar ya yi wai, Abu Sufyana ne ya karye wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* xayan haqoransa, ita kuma Hindu ta cinye antar Hamza baffan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Babu shakka cewa Abu Sufyana shi ne shugaban rundunar da kawo wa musulmi hari a yaqin Uhud. Kuma a nan ne aka karya wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* xayan haqoransa. Amma babu wani masanin tarihi da ya ce Abu Sufyana ne ya yi wannan xanyen aiki. Wanda aka tabbatar ya yi shi, shi ne Utbatu xan Abu Waqqas. Ita kuma Hindu ta tauna antar Hamza *Raliyallahu Anhu* sai ta kasa haxiye ta, ta tofar da ita. Duk wannan ya faru kafin musuluntarsu. Kuma bayan haka sun musulunta, suka kuma kyautata musuluncinsu da su da Hindu. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya

kasance ya na karrama ita Hindun. Musulunci kuma yana shafe abin da ya gabace shi. Allah maxaukakin Sarki kuma ya ce:

﴿ قُل لِّلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِن يَنتَهُواْ يُغۡفَرۡ لَهُم مَّا قَدۡ سَلَفَ ﴾ الأنفال: ٣٨

*Ka ce ma waxanda suka kafirta in suka bari, to, Allah zai gafarta masu abin da ya gabata. Al'Anfal:38.*

### 2.9.16 Khalidu Xan Walidu "Takobin Allah"

Xan Shi'ar ya ce: Sun kira Khalidu xan Walidu takobin Allah, kawai don tsaurin kai ga Amirul Muminina Ali, wanda shi ne ya cancanci wannan suna. Don shi ya kashe kafirai da takobinsa.

**Martani:**

Kiran Khalid xan Walid takobin Allah ba ya nufin shi ya kevanta da wannan suna. A'a, shi dai "xaya ne daga cikin takubban Allah akan mushrikai". Haka ya zo a cikin hadisi daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne wanda ya fara kiran sa da wannan sunan kamar yadda ya tabbata a cikin Sahihul Buhari ta hanyar Anas xan Malik *Raliyallahu Anhu* a wajen maganar yaqin Mu'utah da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ba da labarin shahadar Zaidu da Ja'afaru da Abdullahi xan Rawahata yana zubar da hawaye. Ya ce: "Har sai da wani takobi daga cikin takubban Allah ya xauki tutar, shi ne Khalid, har Allah Ta'ala ya ba su nasara".

Cewa Ali ne ya fi shi cancantar wannan suna. Sai mu ce masa wa ya musanta wannan? Wa ya ce Ali *Raliyallahu Anhu* ba takobi ne daga cikin takubban Allah ba? Shi kansa wannan hadisi na nuna cewa, Allah Ta'ala yana da takubba masu yawa. Kuma ba shakka cewa, Ali *Raliyallahu Anhu* na cikin mafi girma waxannan takubban. Ba wani musulmi mai fifita Khalid a kan Ali, balle har a ce ya keve Khalid da wannan suna. Wanda ya yi masa wannan kirarin kuwa shi ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da kansa.

Ai shi Ali *Raliyallahu Anhu* ya fi Khalid *Raliyallahu Anhu* xaukaka nesa ba kusa ba. Ya ma fi gaban a ce xaukakarsa ita ce kawai kasancewarsa xaya daga cikin takubban Allah, don matsayin imaninsa da martabar iliminsa da fasaharsa da riqon addininsa da kasancewarsa cikin musulmi magabata shi ya fi girma a kan kasancewa xaya daga cikin takubban Allah. Takobi ya kevanta ne da wurin yaqi kawai. Ali *Raliyallahu Anhu* kuwa yaqi xaya ne daga cikin falalolinsa. Savanin Khalid da yake yaqin shi ne falalar da ya ya fice da ita a kan sauran mutane. Ba za a sa shi cikin musulmin farko ba, ko cikin masu yawan ilimi ko zuhudu. Don haka ake yi ma sa kirari da takobin Allah.

Cewar da ya yi Ali ne ya kashe kafirai da takobinsa. Ai kowa ya san cewa, wasu kafirai ne ya kashe, haka ma sauran waxanda suka shahara ga yaqi daga cikin Sahabbai kamar Umar da Zubairu da Hamza da Mikdadu da Abu Xalha da Bara'u xan Malik da sauransu. Ba xaya daga cikinsu face ya kashe

wasu kafirai. Bara'u xan Malik shi kaxai ya kashe kafirai xari ta hanyar fito-na-fito, banda waxanda ya yi tarayya da wasu a wurin kashe su.

Sai kuma xan Shi'ar ya ce wai, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce ma Ali: "Kai ne takobin Allah kuma mashinsa". To, wannan hadisi ba a san shi ba a cikin littaffan hadisi sanannu. Kuma ba shi da isnadi. In ma har ya inganta a bisa qaddarawa, to, ma'anarsa mai kyau ce. Ba ya kuma nufin Ali ne kaxai takobin Allah da mashinsa.

Sai ya ce kuma wai, Khalid bai gushe ba maqiyin Manzon Allah mai qaryata shi. Wannan kuwa gaskiya kafin ya musulunta, kamar yadda dukan Sahabbai suka kasance masu qaryata shi kafin musuluntarsu.

Sai kuma xan Shi'ar ya ce: Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya aike shi wurin qabilar Bani Huzaifa don ya karvo zakkarsu, sai ya yaudare shi, ya sava wa umurninsa, ya kashe musulmi. Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tashi yana mai yin huxuba, ya yi inkarin abin da Khalid ya aikata yana mai xaga hannunsa zuwa sama har aka ga farin hamatansa, yana cewa: "Ya Allah! ina barranta zuwa gare ka daga abin da Khalid ya aikata". Sannan ya aika Amirul Muminina Ali don ya gyara abin da vata, ya umurce shi da ya nemi yardar matanen da aka yi wa hakan.

To, wannan labari nasa akwai jahilci da canza magana ga duk wanda ya san wani abu game da tarihin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, domin kuwa Manzo ya aike shi zuwa wurinsu ne bayan an buxe Makka don su shiga musulunci, sai suka yi amfani da kalimar da ake izgili da ita ga musulmin da suka shiga musulunci. Khalid kuwa ya qi karva masu wannan furuci. Ya ce wannan ba shi ne musulunci ba, ya kuma kashe su. Sahabban da ke tare da shi sun musanta masa, kamar su Salim na gidan su Abu Huzaifa da Abdullahi xan Umar da wasu ba su ba. To, lokacin da wannan labarin ya isa ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai ya xaukaka hannayensa zuwa sama ya yi wannan addu'a don kada Allah Ta'ala ya tambaye shi game da abin da khalid ya aikata na wuce iyaka. Haka Allah ya umurce shi da yi in da ya ce: *Idan sun sava maka, to, ka ce: Haqiqa ni barrantacce ne daga abin da kuke aikatawa. As-Shura:216.* Sannan ya aika Ali da dukiya, ya ba su rabin diyyar waxanda aka kashe, ya kum ranka masu abin da ya salwanta na dukiya har ma abin da kare ke shan ruwa cikinsa. Sannan abin da ya saura a hannunsa na dukiya ya bar masu don ya tabbata cewa kowa ya sami haqqinsa.

Duk da wannan, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai fitar da Khalid daga shugabancin rundunar ba. Kai bai gushe ba yana shugabantar da shi da gabatar da shi saboda wannan kuskuren. Don shugaba idan ya auka cikin kuskure ko zunubi akan umurce shi ne da tuba, a kuma bar shi a kan shigabancinsa. Khalid kuma bai kasance mai yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* tsaurin kai ba, mai xa'a ne. Sai dai bai kai ilimin wasu da riqon addininsu ba. Don haka hukuncin wannan lamari ya shige masa duhu.

Wasu cewa suke yi wai, akwai qiyayya tsakaninsa da su tun a lokacin Jahiliyyah. Kuma wai, wannan shi ya sa ya kashe su.

Amma cewar da ya yi wai an umurce shi ya nemi yardar mutanen. Ba maganar masani ba ce. Abin da ya sa aka aika shi shi ne don ya yi masu adalci, ya kuma ranka ma su abin da suka rasa, ba don kawai neman yardarsu ba.

Haka ma cewar da ya yi Khalid ya yaudari Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya sava umurninsa, kuma ya kashe musulmi. Wannan ba gaskiya ba ce. Domin Khalid bai yi gangancin sava ma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba, balle ya yaudare shi. Bai kuma kashe wanda ya san cewa musulmi ne mai haramtaccen jini ba. Ya dai yi kuskure kamar yadda Usamatu xan Zaidu ya yi sadda ya kashe wanda ya yi kalmar shahada don ya yi tsammanin yaudara ce kawai yake yi. Hakanan wata runduna ta musulmi a zamaninsa *Sallallahu Alaihi Wasallama* ta tava irin wannan kuskuren, suka kashe wani mai kiwon tumaki da ya ce ni musulmi ne, suka tafi da tumakinsa.

### 2.9.17 'Yan Shi'ah Suna Kariyar Murtaddai

Xan Shi'ar ya ce: Lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya cika sai Abubakar ya aika Khalid don ya yaqi mutanen Yamamah, sai ya kashe mutum dubu da xari biyu duk da kasancewarsu suna amsa sunan musulmi. Ya yi wa Maliku xan Nuwairata kisan gila ga shi kuwa musulmi, sannan ya kwana da matarsa. Suka kira Banu Hanifata murtaddai don ba su kai wa Abubakar zakka ba, saboda rashin yardarsu da shugabancinsa. Aka halatta jinainansu da dukiyarsu da matansu har sai da Umar ya yi masa inkari.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Sun kira wanda bai ba da zakka ba murtaddi, amma ba su kira waxanda suka halatta jinin musulmi da waxanda suka yaki Amirul Muminina murtaddai ba, tare da sun ji cewa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce wa Ali *Raliyallahu Anhu*: "Yaqinka yaqina ne, kuma zaman lafiyarka zaman lafiyata ne". Wanda ya yaqi Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ko kafiri ne. Duk an haxu a kan haka.

**Martani:**

Allahu Akbar! Sannunku magoya bayan murtaddai masu bayyana qin Allah da Manzo da addini da Qur'ani. Waxanda suka fice daga addinin musulunci suka yi watsi da shi, suka sava wa Allah da Manzonsa da muminai, suka jivinci mutanen ridda da 'yan-a-ware. Ire-iren waxannan bayanai na tabbatar mana da cikakken qawancenku da kafirai don tsananin adawarku ga sayyidina Siddiqu; adawar da ba ta da wani dalili.

Mutanen Yamama dai su ne qabilar Bani Hanifa, mabiyan Musailamatu sarkin qarya wanda ya raya cewa shi Annabi ne tun a zamanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, ya kuma zo Madina ya nuna musulunci a zahiri. Amma a voye sai ya ce, idan Muhammadu ya naxa ni magajinsa zan ci gaba da yin imani. Da ya koma Yamama sai ya raya cewa ya yi tarayya da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ga annabci. Ya ce kuma wai, Annabi Muhammadu ya gasgata shi a kan haka. Ya samu wani fajiri irinsa mai suna Rajjalu xan Unfuwata ya yi masa sheda a kan wannan qarya.

Haka kuma musailamu ya rubuta nasa Alqur'ani wanda yake cike da tsabar rashin kunya da shirme. A lokacin da aka karanta ma sayyidina Abubakar wannan shirmen sai ya ce: "Kaiconku! Ba ku da hankali ne? Ina wannan maganar ta ta yi kama da maganar annabta?"

Wannan maqaryacin na Yamama har wasiq ya rubuta wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* wadda ya buxe ta da cewa: "Wasiqa daga musailamatu Manzon Allah zuwa ga Muhammadu Manzon Allah. A cikinta kuma yake raya cewa ya yi tarayya da Annabi a cikin annabta. Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rubuta amsa yana cewa: Daga Muhammadu Manzon Allah zuwa ga musailamu sarkin qarya. To, ka ji asalin wannan sunan da ya bi shi, Manzon Allah ne ya sa masa shi, saboda girman qaryar da ya yi wa Allah. Bayan rusuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma sai Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya aika Khalidu xan Walidu don yaqar sa, bayan da Khalid ya gama da wani annabin qarya irinsa mai suna Xulaihatul-Asadi da ya bayyana a qasar Najadu. Allah Ta'ala kuwa ya ba Khalid nasarar gamawa da duk waxannan mutanen. A can ne aka kashe fitaccen Sahabin nan Ukashetu xan Muhsinu, xaya daga cikin waxanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce, za su tsallaka siraxi ba tare da sun gamu da ko wace irin wahala ba. Bayan haka ne shi wancan annabin qaryar, Xulaihatul-Asadi ya musulunta. Sai aka wuce zuwa Yamama wurin musailamu wanda kuma sojojin musulunci sun sha fama mai yawa a kansa. Kuma a can ne a ka kashe wasu baraden Sahabbai irin su Zaidu xan Khattabi, qanen Umar da Thabitu xan Qaisu da Usaidu xan Hudhairu da wasu da dama.

A taqaice dai lamarin musailamatu da 'yan qabilarsa Bani Hanifa da suka bi shi ba a voye yake ba. Abubakar Siddiqu *Raliyallahu Anhu* kuwa ya yaqe su. Wannan a tarihi ya fi zama gama-gari a kan yaqin da Ali ya yi na Raqumi da na Siffin. Don ba a tava jin wanda ya musanta faruwar hakan ba. Amma daga zaqaquran magana *Ahlul-Kalami* akwai waxanda suka musanta faruwar yaqin Raqumi da na Siffin. Ka ga kodayake shirme ne suke yi, amma mai cewa bai san mutanen Yamama sun bi annabin qarya; musailamatu ba, kuma cewa a kan haka aka yaqe su ai ya fi wancan zama sarkin shirme.

Amma su 'yan-sha-biyu don tsananin qin gaskiya da jahilcinsu sukan yi fiye da haka. Tunda yake an samu a cikinsu masu qaryata cewa Abubakar da Umar ne ke kwance kusa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama,* kuma wai, tun can ba su tare da shi a lokacin rayuwarsa. Da masu cewa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya naxa Ali a matsayin halifansa. Kai har ma daga cikinsu akwai masu cewa, Ruqayya da Zainab da Ummu-Kulthumi ba 'ya'yan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ba, wai 'ya'yan khadija ne na wani mijinta kafiri. Da masu cewa sayyidina Umar ya yi qwacen 'yar sayyidina Ali har ta haifa masa 'ya'yan da suka samu. Da masu cewa Sahabbai sun fasa cikin Fatima har ta zubar da abin da ke ciki, kuma wai, an rusa gidanta ya faxa a kan waxanda ke ciki. Da qarairayi ga su nan marasa makama da ko mai qaramin sani na iya warware su.

Mun dai riga mun saba da jin irin waxannan daga wurinsu. Domin su kodayaushe qoqarin suke su ga abubuwan da suka tabbata, waxanda babu shakka a cikinsu, sai su ce sam, ba su auku ba, su zo ga abubuwan da ba a tava yi ba, su yi qoqarin tabbatar da su. Shi ya sa 'yan-sha-biyu na da babban kaso cikin ayar da Allah Ta'ala ke cewa a cikinta:

﴿ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَوْ كَذَّبَ بِٱلْحَقِّ لَمَّا جَآءَهُۥٓ ﴾ العنكبوت: ٦٨

*Shin wane ne ya fi zalunci a kan wanda ya qira wa Allah qarya, ko ya qaryata gaskiya a lokacin da ta zo masa.*

*Al-Ankabut: 68.*

Suna raya cewa Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* sun yi ridda alhali babba da yaro kowa ya san cewa su ne suka yaqi waxanda suka yi ridda. Kasancewarsu suna bai wa masu ridda hanzari, suna zargin Abubakar da zaluntar su, dalili ne babba na xayantakar tafarkinsu, da cewa Abubakar da Ahlus-Sunnah mabiyansa har abada suna cikin yaqi da masu ridda.

Maganar hana zakka kuwa, wasu mutane ne daban ta shafa ba na Yamama ba. Kuma wasu Sahabbai sun yi ciris kan lamarinsu, wasu sun yi shakkar halalcin yaqar tasu. Cikinsu har da sayyidina Umar, amma nacewar da Abubakar ya yi, da qarfin hujjar da ya kafa ta sanya kowa ya gamsu. Su xin ma yana da kyau a sani cewa, ba an yaqe su ne don kawai ba su ba da zakka ga Abubakar *Raliyallahu Anhu* ba. A'a, don dai ba su yarda da fitar da ita ba suka ba da ita ga masu haqqi. In da sun aminta da bayar da ita da kansu ga waxanda suka cancanta da ba za a yaqe su ba. Don haka, sanannen abu ne cewa, Siddiqu bai yaqi kowa ba akan sai ya yi masa xa'a, ko ya yi masa mubaya'a. Don haka ne lokacin da Sa'adu ya yi jinkirin yi masa mubaya'a bai tilasta shi ba.

Sai hadisin da xan Shi'ar ya jingina ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* don ya kafirta waxanda suka yaqi Ali. Hadisin dai kamar sauran ire-iren hadissan da ya saba kawowa ne, waxanda ba su a cikin sannannun littafan hadisi, balle ko a ce suna da isnadi da za a duba a yi hukunci a kansu. Kuma ko bisa ga qaddarawa in har gaskiya ne Manzon Allah ya faxe shi, ba lalle ne waxanda suka yaqi Ali su kasance sun ji shi ba.

Lokacin da Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi yaqin Raqumi da na Siffin bai ce Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ya umurce shi da yin hakan ba. Ijtihadi dai ne ya yi. Abu Dawuda ya ruwaito daga Qaisu xan Abbad cewa: Na tambayi Ali game da fitarsa daga Madina zuwa yaqi, na ce ma sa: Shin umurni ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ba ka, ko kuwa ra'ayinka ne? Sai ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai umurce ni da komai ba cikin wannan lamari. Ra'ayina ne kawai.

Ka ga da gaskiya ne cewa wanda ya yaqi Ali *Raliyallahu Anhu* ya yaqi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, kuma ya zama murtaddi, to, da Alin ya yi masu abin da ake yi wa murtaddai. Ga shi kuwa abokan faxansa a

yaqin Raqumi da na Siffin duk hanawa ya yi a bi wanda ya juya a cikinsu. Masu rauni kuma ya hana a gama da su. Ya kuma ce, kada a xauki ganimar dukiya ko iyali ko ‘ya‘ya. Waxannan ko ba hukunce-hukuncen yaqar murtaddai ne ba. Hasali ma cikin waxanda ke xaya vangaren yaqin akwai uwar muminai A’ishah. Wa zai ce ba uwarsa ce ba ya kafirta? Kuma wa zai bautar da uwarsa?

Kuma in da abokan faxan Ali kafirai ne, da Hassan *Raliyallahu Anhu* bai miqa lamarin musulmi ga hannun kafiri, murtaddi ba. Ga shi kuma ma’asumi ne; ba ya kuskure a wurinku. Miqa akalar musulmi zuwa ga kafirai ba aikin mumini ba ne balle ma’asumi.

Shi dai Allah Ta’ala bai kafirta kowane vangare ba. Cewa ya yi: *Idan qungiyoyi biyu na muminai suka yi yaqi to, ku yi sulhu a tsakaninsu. Al-Hujurat:9.* Sai Allah ya tabbatar da cewa suna nan a matsayinsu na muminai ‘yan’uwan juna ne koda yake sun yaqi juna.

Kuma ya tabbata cikin ingantaccen hadisi daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa: “Wasu ‘yan-a-ware za su fice a lokacin rarrabuwar musulmi, sai wata qungiyar da ta fi kusa da gaskiya ta kashe su”. Ya kuma ce: “Haqiqa jikan nan nawa shugaba ne. A nan gaba Allah zai sasanta wasu manyan qungiyoyi biyu na musulmi ta hayarsa”. Ya kuma ce ma Ammar: “Wata qungiya mai ta’addanci za ta kashe ka”. Sai ya sifaita ta da savo ba kafirci ba.

Duk waxannan hadisan ingantattu ne a wurin malamai. Sai ta tabbata cewa, gaskiya ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ba da labarin cewa qungiyoyi biyu masa savani da juna musulmai ne. Kuma ya yabi wanda Allah zai sa ya sulhunta su. Ya kuma bayyana cewa wata qungiyar ta fi wata kasancewa kusa da gaskiya, wacce kuma ita ce za ta kashe Ammar.

Bari yanzu mu haxa ‘yan Shi’ah da wasu maqiyan Ali *Raliyallahu Anhu* su tattauna don mu ji amsar da za su ba su. Maqiyan Ali sun ce, ya halatta jinin musulmi, ya yaqe su ba bisa umurnin Allah da Manzo ba, don kawai kariyar muqaminsa. Ga shi kuwa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Zagin musulmi fasiqanci ne, yaqarsa kuma kafirci ce”. Ya kuma ce: “Kada ku juya bayana ku koma kafirai; sashenku na kisan sashe”. Suka ce, bisa ga qaxannan hujjoji Ali *Raliyallahu Anhu* ya kafirta.

To, faxa min wace amsa ce ‘yan-sha-biyu za su bayar? Duk hujjar da za su bayar ba za ta fi hujjar waxancan ba, don hadissan da suka kafa hujja da su ingantattu ne.

Sannan kuma Nasibawan, maqiya Ali na cewa: Kashin rayuka varna ne. Don haka duk wanda ya kashe rayuka don a yi masa xa’a to, yana neman xaukaka ne a bayan qasa, da yaxa varna. Suka ce, wannan shi ne halin Fir’auna da ire-irensa. Kamar yadda Allah Ta’ala ya ce: *Waccan gidan lahira ce (Aljanna) muna ba da ita ga waxanda ba su neman xaukaka a bayan qasa, ba su kuma son varna. Kuma qarshen qwarai na masu tsoron Allah ne. Al-Qasas: 83.* Suka ce duk wanda ya nemi xaukaka a bayan qasa ta hanyar yin varna

kamar kisan mutane, to, ba ya cikin masu rabo a ranar lahira saboda wannan aya. Kuma suka ce Ali na cikinsu. Suka ce, amma Abubakar ya yaqi waxanda suka hana zakka ne da waxanda suka yi ridda don mayar da su zuwa ga xa'ar Allah da Manzonsa, ba don a yi shi a yi masa xa'a ba.

### 2.9.18 Wai Iblisu Ma Ya Fi Mu'awiyah.. Inji shi!

Xan Shi'ar ya ce: Wani malami na kirki ya kyauta inda yake cewa: "Wanda ya fi iblis sharri shi ne wanda bai wuce shi ga xa'ar da ya tava yi ba, sannan ya tafi tare da shi a cikin fagen savonsa". Babu wata shakka a tsakanin malamai cewa, Iblisu ya kasance ya fi mala'iku ibada, kuma yana xauke da Al'arshi shi kaxai har tsawon shekaru dubu shidda. Amma lokacin da Allah ya halicci Adam, ya sanya shi halifa a bayan qasa, an umurce shi da ya yi sujuda sai ya yi girman kai, sai ya cancanci la'ana da kora. Haka Mu'awiyah bai gushe ba yana shirka da bautar gumaka tsawon lokaci bayan bayyanar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Sannan kuma ya yi girman kai da aka sa Ali ya zama shugaba, kowa ya yi masa mubaya'a bayan an kashe Usmanu sai shi Mu'awiyahn ya yi zamansa a inda yake. Don haka gara ma iblis da shi.

**Martani:**

Wannan maganar inda mafaxinta ya yi tunani zai gano ta qunshi jahilci da vata da fita daga cikin musulunci, kai har ma da dukan addinai da kuma fita daga aikin hankali irin wanda ko kafirai na da shi.

Da farko dai ba a haxa kafircin Iblis da na kowa. Kuma duk wanda ya shiga wuta to, yana cikin mabiyansa ne. Don haka Allah Ta'ala ya ce masa: *Wallahi zan cika wutar jahannama da kai da duk wanda ya bi ka gaba xaya. Sad: 85.* Duk laifin da aka yi a duniya shi ne ya yi umurni da shi, ya qawatar da shi, ya sa ayi shi. To, yaya wani zai fi shi sharri, musamman daga cikin musulmi, kuma daga cikin sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*?

Cewa wanda ya fi iblis sharri shi ne wanda bai yi irin xa'ar da Iblis ya yo can baya ba, sannan ya bi shi a wajen savo. In aka bi wannan magana tana nuna cewa duk wanda ya sava wa Allah ya fi Iblis sharri kenan. Don bai kai shi ga waccan xa'ar da kuka ce ba, sannan suka yi tarayya a fagen savo. A haka, kenan Annabi Adamu da zurriyarsa sun fi Iblis sharri, don Allah Ta'ala ya ce: *Kuma Adamu ya sava wa Ubangijinsa, sai ya vata. Suratu Xaha 121.* Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma ya ce: "Duk 'yan Adam masu yawan kuskure ne. Mafi alherin masu kuskure su ne masu tuba".

Akwai kuwa wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira da ke iya qarfin halin cewa gara Iblis da musulmin da ya yi savo? Ashe wannan ba ya cikin abubuwan da aka san cewa vata ne da kaucewa daga tafarkin addinin musulunci? To, bisa ga wannan maganar, 'yan Shi'ah ma gara Iblis da su, don koyaushe suna cikin zunubi.

Idan Kharijawa suka ce maku: Ali *Raliyallahu Anhu* ya aikata savo, don haka gara Iblis da shi. Me za ku ce mu su? Ba abin da za ku ce sai shi ma'asumi ne da ba ya kuskure. Ku da ba za ku iya tsayar masu da hujjar da ke tabbatar da imaninsa da shugabancinsa da, ina maganar ma'asumancinsa? Duk abin da 'yan-sha-biyu ke kafa hujja da shi sokakke ne kuma yana karo da dalillai irinsa daga gefen Kharijawa, don haka bai inganta a kafa hujja da shi. Amma Ahlus-Sunnah na iya tabbatar da imanin Ali da shugabancinsa da hujjojin da 'yan-sha-biyu ba su da hannu gare su, don suna warware aqidarsu.

Abu na biyu kuma shi ne: Wannan magana bayan dai ba ta da hujja, kuma ba ta da ma'ana. Don ina dalilin cewa, wanda bai yi irin aikin da shaixan ya yi ba kafin kafircinsa ya fi shi sharri in sun tafi tare a savo? Akwai daga cikin 'yan Adam wanda zai iya tafiya tare da shaixan cikin dukan savonsa? Don ba shi yiwuwa a sami mutumin da zai kai Iblis wajen savo, ta yadda zai iya vatar da dukan mutane, ya ruxe su.

Idan Iblis ya gabatar da wata xa'a kome yawanta, ta riga ta rushe da kafircin da ya yi bayanta. Saboda ridda tana vata aiki. Sannan savon da yake yi har abada kowa bai iya yin sa. To, ta yaya za a sami wanda ya fi shi sharri?

Idan mun tafi a kan wannan qa'idar da xan Shi'ar ya kafa, kenan magoya bayan Ali *Raliyallahu Anhu* waxanda suka yi yaqi tare da shi kuma suka kasance a wasu lokutta suna sava masa, sun fi sharri a kan waxanda ba su yi masa mubaya'a ba cikin Sahabbai. Don su, suna da xa'a da ta gabata sannan waxancan sun tafi tare da su a fagen savo.

To, sannan ina hujjar cewa, Iblis ya fi Mala'iku ibada? Da kuma cewa ya kasance yana xauke da al'arshi tsawon shekaru dubu shidda? Ko ma cewa yana cikin masu xaukar al'arshi? Ko shi ne xawusun Mala'iku? Ko ba wani bigire a sama ko a qasa face ya yi wa Allah sujada ko ruku'i a cikin? Da makamantan waxannan maganganu da wasu mutane ke faxa. Irin wannan lamarin hanyar saninsa kawai ita ce ingantacciyar riwaya. To, ba a faxi wani abu mai kamar haka ba a cikin Alqur'ani, kuma ba a riwaito wani ingantaccen hadisi daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba game da shi. To, in ba jahili ba wa zai kafa hujja da irin wannan ga manyan mas'aloli haka?

Abin da duk ya fi ban mamaki shi ne cewarsa wai, babu savanin tsakanin malamai cewa Iblis ne ya fi dukan mala'iku ibada. Wane ne ya ce haka cikin malaman Sahabbai ko Tabi'ai da wasunsu daga cikin malaman musulmi, ballantana ya kasance malamai sun haxu a kan sa? Wannan maganar ba wanda ya tava yin ta cikin malaman musulunci da ake karvar maganarsu. Kuma abu ne wanda ba shi yiwuwa a san shi sai ta hanyar riwaya, kuma ba a riwaito wannan daga kowa ba, koda da isnadi mai rauni. To, idan wasu masu wa'zi ne suka faxe shi, ko masu rubutu game da tarbiyyar zuciya, ko masu xauko labaran da aka riwaito daga Yahudawa cikin wasu littaffan tafsiri ba tare da isnadi ba. Wannan ba a kafa hujja da shi ga abin da ya shafi kwandon albasa. To, yaya zai kafa mana hujja da shi a kan cewa, Iblis ya fi duk wani

wanda ya savawa Allah cikin ‘yan Adam, kuma ya sa Sahabbai cikin waxannan da Iblis ya fi su?

Allah Ta’ala bai tava siffanta Iblis da alheri ba, haka ma Manzonsa *Sallallahu Alaihi Wasallama*, to, balle cewa ya tava yin wata xa’a ko wace iri ce. Tattare da in ya yi to, ta vaci saboda riddar da ya yi da kafircinsa.

Wani abin al’ajabi daga cikin maganar xan Shi’ar, wai babu wani savani tsakanin malamai cewa, Iblis ya kasance yana xauke da al’arshi shekaru dubu shidda shi kaxai! Tsarki ya tabbatar ma Allah. Shin akwai kuwa wanda ya tava furta wannan magana daga cikin malaman musulmi da ke ganin girman Allah? Idan ma har wannan labarin gaskiya ne, to, ai ba a iya saninsa sai ta hanyar Annabawa. Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuwa bai faxi komai ba game da wannan batu. To, ta ina suka san shi?

Shi dai Mu’awiyah *Raliyallahu Anhu* musuluncinsa ya tabbata. Kuma musulunci na shafe duk abin da ya gabace shi. Sannan bai tava yin ridda ba bayan ya musulunta. Amma wanda ke raya cewa Abubakar *Raliyallahu Anhu* da Umar *Raliyallahu Anhu* da Usmanu duk sun yi ridda, ina mamaki don ya haxa da Mu’awiyah *Raliyallahu Anhu*? Kuma ina banbancin hujjarsa da ta waxanda suka ce Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi ridda shi ma, Harijawa kenan? In dai ta vangaren hujja ne to, Harijawa sun fi hasken hujja a kan ‘yan-sha-biyu.

In da kuma har wayau za mu xauki maganar xan Shi’ar a yadda ya yi ta, ba wanda take suka gare shi kamar Ali da xan Al-Hassan. Don kenan murtaddai sun samu galaba a kansa shi Ali., Hassan kuwa ya miqa shugabancin musulunci ga murtaddai. Kuma kenan taimakon da Allah ya yi wa Khalid akan kafirai ya fi wanda ya wa Ali *Raliyallahu Anhu*. Da yake Allah Ta’ala mai adalci ne da ba ya zaluntar kowa, ya ba Khalid xan Walid abin da ya cancanta na taimako. Shi kuma Ali bai cimma Khalid ba, tun da Allah bai taimake shi a kan waxanda ya yaqa ba. Khalid dai kenan ya fi xaukaka a wurin Allah sama da Ali.

Maganar mubaya’ar da ya ce kowa ya yi ma sa bayan kisan Usmanu. Idan wannan hujja ce, to, mubaya’ar da aka yi wa Usmanu *Raliyallahu Anhu* ta fi girma. Ga shi ko ku ba ku ganin wanda ya qi wa Usmanu mubaya’a a matsayin kafiri. Kuna ma ganin cewa, shi ne musulmin qwarai mai tsoron Allah.

Kuma bisa wannan maganar taku, sai mu ce, haxuwar kan mutane a lokacin yi wa Abubakar mubaya’a ta fi kammaluwa. Ga shi ko ku da wasu ba ku ba na cewa Ali *Raliyallahu Anhu* bai yi mubaya’a ba sai bayan wani lokaci. To, wannan yana kai mu ga cewa ya yi girman kai ga yi wa Allah Ta’ala xa’a bisa ga wannan qa’idar taku. Wannan yana kai wa ga kafirta Ali *Raliyallahu Anhu* bisa wannan hujjar taku in da ta kasance gaskiya. Amma mu mun san hujjarku vatacciyar hujja ce, ba mu kafirta Ali *Raliyallahu Anhu* ko waninsa da ita. Ku dai da ke amfani da ita in kun gane sai ku tuba.

Fita batun qaryar da ya shara wajen cewa, kowa ya yi ma Ali mubaya’a bayan Usmanu. Don da yawa daga cikin musulmi; rabi ko abin da bai kai haka

ba, ko wanda ya fi haka basu yi ma sa mubaya'a ba. Manya irin su Sa'adu xan Abu Waqqas da Abdullahi xan Umar na cikin waxanda ba su yi ba.

Daga qarshe, cewar da ya yi, wai, Mu'awiyah ya zauna wurinsa, babu adalci a ciki. Don can farkon lamari Mu'awiyah bai nemi shugabanci ga kansa ba, bai kuma tafi wurin Ali *Raliyallahu Anhu* don ya karve masa mulki ba, amma yaqi yi masa mubaya'a ne shi da mabiyansa. Ya kuma ci gaba da shugabancinsa na gwamna wanda tun lokacin Umar da Usman yake yi. Ko lokacin da aka nemi sasantawa, aka sanya mutum biyu su yi hukunci, Mu'awiyah ya kasance yana shugabantar waxanda ke qarqashinsa ne kawai. In kuma xan Shi'ar na nufin ne Mu'awiyah ya haye mulkin Sham xin ne, bai bar Ali *Raliyallahu Anhu* ya naxa wani ba, to, wannan gaskiya ne. Amma abin da Mu'awiyah *Raliyallahu Anhu* ke cewa shi ne, ba zan yi jayayya da shi a cikin abin da ke hannunsa ba, kuma ban ga abin da ke wajabtar da shigata qarqashin xa'arsa ba. Wannan maganar kuwa sawa'un in gaskiya ce ko qarya, ba ta isa ace wanda ya yi ta ya fi Iblis sharri ba.

Wanda ya mayar da Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* matsayin waxanda suka fi Iblis sharri, to, bai raga ma Allah da Manzo ba. Ya kuma yi shisshigi, ya wuce iyaka ga mafi alherin qarni da aka tava yi na 'yan Adam. Allah Ta'ala zai taimaki Manzanninsa da waxanda suka yi imani a rayuwarsu ta duniya da ranar qiyama, sa'adda shaidu za su tsayu, su ba da shaida a gabansa. Shi kuma son zuciya idan ya kai mai shi zuwa ga irin wannan madatsa yakan fitar da shi daga cikin hankalinsa, fita batun ilimi da doka. Allah muke roqo ya kiyashe mu daga miyagun fitinu.

Tabbas, Allah Ta'ala zai qasqantar da wanda ke furta irin wannan magana, kuma zai taimaki bayinsa muminai, waxanda suka haxa da Sahabban Annabinsa da masoyansu a kan waxannan azzalumai masu qiren qarya.

### 2.9.19 Yazidu Ya Zama Sarki, Husaini Ya Samu Shahada

Xan Shi'ar ya ce: "Duk da miyagun ayyukan da Yazidu xan Mu'awiyah ya aikata, waxanda suka haxa da yi wa Husaini kisan gilla, tare da wasashe dukiyarsa, da ribace matansa, da sukwane lungu–lungu na garuruwa da su a kan raqumma; haka nan babu ko siridda a kansu. Suna kuma jaye da shugabanmu Zainul Abidina sun zuba masa sarqa a hannu kamar bawa.

Wannan wulaqanci da suka yi wa Zainul Abidina bai ishe su ba. A qarshe dai suka aika shi lahira. Kuma duk da haka hankalin su bai kwanta ba, sai da suka tattaka haqarqarinsa da dawaki suka sare kansa tare da soka shi a kan tsinin mashi, tare da na waxanda ke tare da shi, suka ratsa gari tsaye suna murna da annashawa.

Duk waxannan abubuwa ba su hana wani sashe na Ahlus–Sunna imani da cewa Yazidu ya karva sunan shugaba a musulunci ba, saboda tsananin qabilanci.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: "Kuma wani abin ban mamaki shi ne, waxannan mutane sane suke da cewa malamansu sun riwaito cewa; ranar da

Yazidu ya yi wannan aika–aika ta aika Husaini lahira sai da aka yi mamakon ruwan jini daga sama. Wannan magana da nake gaya ma, Rafi'i ne ya kawo ta a cikin littafin: *Sharhul Wajizi,* haka nan kuma Ibnu Sa'ad ya faxa a cikin littafin: *Ax-Dabaqat* cewa; a wannan rana sama'u tayi ja jawur. Abin da ba a tava gani ba. Ya kuma ci gaba da cewa; babu wani dutse da za a tava a duniya, saboda wani dalili a wannan rana, face an taras da ruwan jini a qarqashinsa. Haka kuma an yi wani irin ruwan sama da ya zama takalmin kaza a jikin tufafin mutane.

Kuma Imamuz-Zuhri ya ce; babu wanda ya tsira daga azaba tun nan duniya daga cikin waxanda ke da hannu kai tsaye a cikin kisan Husaini. Gaba xayansu mummunan qarshe suka yi. Wasu daga cikinsu karkashe su aka yi. Wasu kuma aka jarabce su da makanta ko baqin jini ko kubcewar mulkinsu, duk a cikin xan qanqanin lokaci.

Kuma sau da yawa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ke yi wa musulmi wasiyya da su raga wa jikokin can nasa guda biyu, wato Hasan da Husaini. Yana mai cewa: "Waxannan sune amanar da na bari hannunku".

Kuma wai ma a kan haka ne Allah ya saukar da ayar da ke cewa: "Bani tambayar ku wata ijara a kansa face dai soyayya ta cikin zumunta" (42:23).

Tirqashi! Gwanin abu mai yin sa, kai ka ji.

**Martani:**

Bismilahi. Mun fara.

Ina fatar dai baka mance da farkon maganar xan Shi'ar ba. Don ta ita ne zamu fara mayar masa da martani.

Muna son mu gane abin da yake nufi da cewar da ya yi; wai, tsananin qabilanci yasa wasu Ahlus – Sunnah imani da cewa Yazidu xan Mu'awiyah ya karva sunan shugaba (Imamu) a musulunci.

Ixan xan Shi'ar na nufin waxannan Ahlus-Sunnah sun yi imani da kasancewar Yazidu xaya daga cikin shiryayyun halifofi da nagartattun shugabanni a musulunci. Kamar su Abubakar da Umar da Ali *Raliyallahu Anhum*. to, muna tabbata masa cewa babu wani malami daga cikin malaman musulunmi da ya yi imani da haka. Amma dai muna jin labarin cewa akwai wasu jahilai daga cikin qurdawa da makamantansu da sukayi imani da cewa Sahabbai ba su fi Yazidun da komai ba; shi ma Sahabi ne. Kai! Wasu ma daga cikinsu na jin cewa shi Annabi ne. A ya yin da wasu suka tsaya kusa-kusa; suka ce a a, yana dai kafaxa-da-kafaxa da shiryayyun Halifofi.

To, amma irin waxannan mutane ba su daga cikin ma'abuta ilimi, balle a yi guzurin maganarsu.

Amma kuma duk da haka, sun fi jahilai da zindiqai daga cikin 'yan-Shi'ah sauki. Waxanda ke jin cewa sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* Allah ne, ko Annabi. Kuma wai shari'ar musulunci ba komai ba ce illa yaudara, saboda zahirinta na takin saqa da baxininta. Kai! qarewa da qarau ma *Isma'iliyyah* da Nasiriyya da wasunsu daga cikin qungiyoyin Shi'ah na .jin cewa salla da

azumi da zakka da hajji, sun faxi daga kan malamansu. Kuma wai tashin qiyama qarya ne. Wal'iyazu billahi. Can ga bakinku.

Amma ka sani, babu wani daga cikin malaman ahnlus –sunna, irin waxanda ake shiga xaka da maganarsu, da ya yi imani da cewa Yazidu da makamantansa na kafaxa-da-kafaxa da halifofin Manzon Allah, irin su Abubakar da Umar da Usmanu da Ali. *Raliyallahu Anhum* a daraja da xaukaka. Ko alama. Hasali ma ahlus- sunna riqe suke da hadisin nan da ke cikin: As – sunanu, wanda ke cewa: "Halifancin annabta zai qare bayan shekaru talatin, mulkin gargajiya ya maye gurbinta."

Wannan kenan. Idan kuma xan Shi'ar na so ne ya ce waxannan mutane da ya kira sashen Ahlus-Sunnah sun yarda da Yazidu, har quryar zukatansu, a matsayin Sarkin Musulmi kuma halifa a zamaninsa, mai wuqa da nama. Kamar yadda suka aminta da sauran halifofi; Umawiyyawa da Abbasiyyawa, to, babu wata jayayya a cikin haka. Duk wanda ma ya ce ba zai yarda da haka ba, to ya tabbata kangararre. Domin kuwa gaba xayan duniyar musulunci ta ji kuma ta yarda da bai'ar da aka yi wa Yazidu bayan rasuwar mahaifinsa Mu'awiyah. qasashen musulmi da suka hada da Sham da Masar da Iraqi da khurasan da sauransu duk, suka kasan ce qar qashin ikonsa.

Ka ga da haka ne ya zama shugaba kuma halifa kuma Sarkin Musulmi. Babu kuma wani dalili da za a iya riqo dashi, a hana shi zama haka. Yadda kasan dole ne a kira mai ba mutane salla da sunan liman; ko anqi ko anso. Domin dazarar kowa ya yalla ido ya ga mutum ya rungume hannuwa gaban sahu, to wautace wani ya qi yarda da kasancewarsa liman gare su. Shi kuwa zancen kasancewarsa mutumin kirki ko asharari, wata maganace daban.

To, a kan wanan ma'auni ne Ahlus-Sunnah suka yi imani da kasan cewar Yazidu da Abdulmalik da Mansur da wasunsu sarakunan musulunci. Shi kuwa duk wanda ke musun haka, dai-dai yake da wanda ke musun halifancin Abubakar da Umar da Usmanu. Da mulkin kisra da qaisar da Najjash, da wasu sarakuna.

Amma cewa xaya daga cikin waxannan halifofi da sarakunan musulunci ma'asumi ne. Ko kuma adali ne a cikin gaba xayan al'amurransa; baya sava wa Allah fai da voye, wannan ba aqidar malamai da shugabanin musulunci ba ce.

Sanya wannan mala tukuna.

Shi kuwa Husaini *Raliyallahu Anhu* a wurin Ahlus-Sunnah, ko shakka babu kisan da aka yi masa zalunci ne. Kuma Allah *Subhanahu Wa Ta'ala* ya karvi shahadarsa. Wannan kisa nashi a wurinmu daidai yake da na duk wanda aka kashe bai ji bai gani ba, sai don kawai ya ce Allah! Kuma duk wanda ya aikata wannan mugun aiki ko ya taimaka cikin tabbatuwarsa ko ya yi farin ciki da haka, to ya sava wa Allah ya kuma cutar da Manzo. Don ya yi tarayya da maqiya Allah a cikin jefa musulunci cikin fitina.

Amma kuma a wuri xaya, kamar yadda muka faxa, hakan ta zama sanadiyyar samun shahada da daraja da xaukaka ga Husaini *Raliyallahu Anhu.*

Allah Ta'ala ya nufi cewa shi da xan'uwansa za su sami irin wannan babban rabo, da ba a samu sai da zufan goshi. Eh! Tsuntsu ne daga sama gasashshe suka samu. Don ba su ga abubuwan da wasu daga cikin mutanen gixansu suka gani ba na hawa da gangara. Domin kuwa ko da aka haife su yabanyar musulunci ta qetare siraxin fari. Suka rayu cikin girma da aminci, sai ga shi cikin ikon Allah xayansu yara su ta hanyar shayar da shi guba. Xayan kuma ta hanyar kisan ga-ni-ga-ka. Da haka ne kuma suka sami shiga sahun manyan shahidai.

Amma kuma daxa, duk da haka, zunubin wannan kisan gilla da aka yi wa Husaini da 'xan'uwansa, bai kai girman zunubin kisan gillar da waxansu al'ummomi suka yi wa Annabawa ba. Ka tuna irin yadda Allah Ta'ala yake ba mu labarin irin yadda bani'isra ila ke karkashe Annabawa ba li ba la. To, musiba da zunubin da ke cikin kashe ba annabe sun yi wa wanan fintinqau. Kai! Ko kisan gilar da aka yi wa halifa Ali da Halifa Usmanu *Raliyallahu Anhuma* duk sun fi wannan girman zunubi da musiba.

To, tunda kuwa har haka ne. Ashe ka ga kenan babu abin da ya wajaba a kan musulmin qwarai a cikin waxannan lokuta na sabkar musibu, sai haquri da mayar da al'amari a wurin Allah. Kamar yadda Allah da Manzonsa ke so,

Amma a maimakon haka, sai gashi wannan kisa na Husaini *Raliyallahu Anhu* ya sa wasu mutane sun biye wa qixan shexan. Inda hakan ta zama sanadiyar tsiruwar waxansu bidi'oi guda biyu: bidi'ar zama cikin baqin ciki da jimami tsawon yinin ranar Ashura, tare da mare maren kai da kai, da hargowa da koke- koke da bege da rera wakokin ta'aziyya. Tare da wannan kuma, sai ka taras sun buge ga: Bidi'a ta biyu wato zagin magabata da la'antar su, tare da shafawa waxanda ba su ji ba su gani ba daga cikinsu kashin kaji. Wanda hakan kan kai su ga zagin uwayen tafiya (Assabiqunal auwaluna) A qarshe kuma su zauna xandali suna qaranta yadda al'amarin abin ya faru wai. Wanda mafi yawan labarun da suke faxa wa mutane a kan hakan qarya ce tuburan.

Kuma kar ka daxa kar ka qara.'Yan Shi'a sun tsiri waxannan abubuwa ne tare da mayar da su wata sunna tasu, don kawai su haifar da fitina a cikin musulmi tare da raba kanunsu. Gaba xayan musulmi sun yi itifaqi a kan cewa, ko ga matsayin mustahabbi waxannan abubuwa da suke yi a wanan rana ba su kai ba balle wajibi. Kai! Hasali ma fita hayyaci da jimami saboda wasu musibu da suka daxe da faruwa a rayuwa, na daga cikin manyan abubuwan da Allah da Manzonsa suka haramta. Kamar yadda suka haramta matsanacin xoki da annashawa tare da fita hayyaci saboda wani abu na farin ciki.

Ita kuwa cewar da xan Shi'ar ya yi wai an ribace mata da 'ya'ya matan Husaini *Raliyallahu Anhu* An kuma xauke su a kan raqumma babu ko siridda, aka zagaya qasa da su, qarya ce lafiyayyarta.

Alhamdu lillahi. A iya saninmu da tarihin musulunci, musulmi ba su tava ribace wata Bahashima ba. Hasali ma babu wani lokaci da aka tava jin al'ummar Muhammadu *Sallalahu Alaihi Wasallama* ta halatta ribantar wani Bahashime. Amma dai muna jin qarya ce – qarya cen da wasu jahilai ma'abuta

son zuciya ke yaxawa. Kamar yadda muka ji wata qungiya daga cikinsu na cewa wai Hajjaju, ya tava kashe sharifai (Banu Hashim).

Haka kuma cewar da ya yi wai babu wani dutse da za'a xaga, a kan wata lalura a duniya, a ranar da aka kashe Husaini face an taras da jini qundum a qarqashinsa, ita ma qarya ce bayyananna.

Amma ka ga cewar da ya yi imamu Az-zuhri ya ce: Babu wan da yara ge daga cikin waxanda ke da hannu a cikin kisan Hussai *Raliyallahu Anhu* face Allah ya azabtar da su tun duniya.

Wannan abune mai yiyuwa. Domin ta tabbata cewa zalunci shi ne zunubin da Allah ke gaggauta azabtarda wanda ya yi shi tun duniya.babu kuwa zaluncin da ya kai kisan Husaini *Raliyallahu Anhu* girma.

Amma kuma ko shakka babu, cewar da ya yi wai, a kan Hassan da Husaini ne ayarda ke cewa: *Ka ce, Bani tambayar ku wata ijara a kansa face dai soyayya ta cikin zumunta. (42:23)* ta sauka qarya ce lafiyayya.

Dalili kuwa shi ne; ita dai wannan aya tana cikinsurar shura ne. Ita kuwa wannan surar ko shakka babu a Makka ne ta sauka; wato tun kafin a aurar wa Ali da Fatima *Raliyallahu Anhama* har su haifi Hasan da Husainin. Tarihi ya tabbatar da cewa an yi wannan aure ne bayan anyi Hijra zuwa Madina da she karu biyu. Kuma ba suyi baiko ba sai bayan yaqin Badar, wanda akayi a cikin watan azumi na sheqarar.

Abin da wannan aya ke nufi, kamar yadda xan Abbas yabayyana, Imamul Buhari kuma da waninsa suka riwaito, shi ne; Allah (S W A) na magana ne da harshen Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da cewa ; ka ce musu ba ka neman wani sakamako daga wurin su a kan alherin da ka zo masu dashi na musulunci,face su dubi abin da ke tsakaniku na zumunta;kada su cutar da kai.

Xan Abbas ya qara da cewa, hakan kuwa ta faru ne: saboda babu wata qabila daga cikin qabilun Quraishawa, wadda Manzon Allah ba yada zumunci da su. Ka ji xan xangi.

Amma kuma duk da haka munji wasu marubuta daga cikin Ahlus-Sunnah wal jama'a da 'yan Shi'a, daga cikin muqarraban imamu Ahmad da wasunsu na yayata wani qagaggen hadisi, wanda kecewa wai: A lokacin da wannan aya ta sauka, Sahabbai sun tambayi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa: su waye ma kusantan naka? Wai sai ya ce: Ali da Fatima da 'Ya'yansu guda biyu.

To, malamai ma'abuta ilimin hadisi sun yi ittifaqi a kan cewa, wannan hadisi qagagge ne.

### 2.9.20 Yazidu Bai Cancanci La'anta ba

Xan Shi'ar ya zargi wasu daga cikin Ahlus-Sunnah, waxanda hankalinsu bai natsu da cancantar Yazidu da shiga sahun sarakunan musulunci ba. Amma kuma tattare da haka ba su yarda da a la'ance shi ba. Amma kuma

wai, A cewar xan Shi'ar, sun yarda da kasancewarsa azzalumi. Tunda ya kashe Husaini ya kuma yi awon gaba da duk abin da ya mallaka.

To, wai ko sun manta da faxar Allah Ta'ala: *To, La'anar Allah ta tabbata a kan azzalumai. (11:18)?*

Kuma ga shi Abul-Faraji Ibnul-Jauzi, xaya daga cikin malaman mazhabar hanbaliyyah ya ce: An samo daga xan Abbas *Raliyallahu Anhu* wanda ya ce wai: Allah Ta'ala ya yi wahayi zuwa ga Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa: Na karvi rayukan mutum dubu saba'in akan kashe Annabi Yahya xan Zakariyya. Zan kuma karvi rayukan mutum dubu xari da arba'in akan kashe jikanka.

Haka kuma As-suyudi, xaya daga cikin mutane masu girma a wurin Ahlus-Sunnah ya bayar da labarin cewa: "Watarana na sauka karbala ina xauke da kayan abinci na na kasuwanci a inda wani mutun ya karvi baqunci na. Bayan mun qare cin abincin dare, sai muka xauko hirar kisan gillar da aka yi wa Husaini a wannan wuri. Sai ni da fatake yan uwana muka ce: " Ka ko ga babu wanda bai yi mutuwar qasqanci ba, daga cikin waxanda ke da hannu a cikin kisan Husaini." Sai mai masaukinnan namu ya kada baki ya ce: "Lallai kune sarakunan qaryar duniya! To, ni xin nan dake gabanku tare da ni aka kashe shi, Amma kuma gani daram". Ah! Ai dare na tsalawa; alfijiri na gab da ketowa, sai kawai muka ji ana cewa kai baqi ku tashi ba lafiya. "Muka ce me ya faru?"

Sai aka karva mana da cewa: Ai jiya da dare mai masaukin nan namu yana gyaran a-ci-bal-bal xinsa, sai kawai yatsansa ya lashi wuta. Nan take wutar ta bi ta jinin sa ta kone shi qurmus. Wallahi haka muka taras da gawarsa baqi qirin kamar gawayi.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: kuma Muhammad xan Yahya ya tambayi Ahmad xan Hambali watarana, a kan Yazidu. Sai ya karva masa da cewa: Shi ne wanda ya aikata aika-aikan nan.ya ce: "sai na ce masa; meya aikata?" sai ya karva mani da cewa: Keta alfarmar Madina ya yi.

Kuma wai watarana Salihu, xaya daga cikin 'ya'yan Ahmad xan Hambali ya ce wa mahaifin nasa: Baba naji wasu mutane na cewa muna daga cikin waxanda suka yarda da jivintar Yazidu. Sai wai shi kuma ya karva masa da cewa: Haba Salihu, ai ba wanda ke yarda da jivintar Yazidu, sai wanda bai yi imani da Allah da ranar lahira ba. Ko me kace? Sai Salihun ya ce masa: To baba me ya sa ban ji kana la'antar sa ba? Sai wai shi kuma ya karva masa da cewa: Me ko zai hana in la'anci wanda Allah ya la'anta a cikin littafinsa? Ba ka dai dace da hakan ba ne. Sai kuma ya sake ce wa uban: To, baba a ina Allah ya la'ance shi? Sai ya karva masa da cewa a cikin faxar sa: *To, shin kuna fatar idan kun juya (daga umurnin) za ku yi varna a cikin qasa, kuma ku yanke zumuntarku? Waxannan su ne waxanda Allah ya la'ane su, sannan ya kurumtar da su, kuma ya makantar da ganinsu (47:22-23).*

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: To, akwai zalunci da varnar da ta kai kamar kisan kai da keta alfarmar birnin Madina tsawon kwana uku tare da

ribance mutanen da ke cikinta? Tare kuma da kashe wasunsu da dama, da suka haxa da Quraishawa da Ansaru da Muhajiruna, waxanda adadinsu bai kasa xari bakwai. Da wani adadin na bayi da 'ya'ya da mata da ba a san iyaka ba. Aika-aikar da tasa sai da gawawwaki suka yi iyo a cikin gulbin jini. Wanda kuma ya kai har ga qabarin Manzon Allah *Sallalahu Alaihi Wasallama*; raudarsa ta cika maqil da jini. A qarshe kuma suka koma suka harbi Ka'aba da manjaniqu, ya roshe, suka kuma liqa mata wuta; ta ci ta canye. Akwai varnar da ta kai ga haka?

Me zai sa waxannan mutane su yi shayin la'antar mai irin wannan aiki? Ko sun manta da cewar da Manzon Allah *Sallalahu Alaihi Wasallama* ya yi: Allah zai sanya duk wanda ya kashe Husaini a cikin wani akwati na wuta, ya kuma yi masa rivin azabar da zai yi wa 'yan wuta. Ta hanyar xaure hannuwansa da qafafunsa da wata sarqa ta wuta, a tungumi akwatin a jefa wuta ya yi qasa.Ya dinga wani wari da ko 'yan wuta sai sun roqi Ubangiji tsari daga gare shi. Haka zai tabbata cikinta har abada, yana shan azaba mai raxaxi. Duk lokacin da fatar jikinsa ta nina ta kware, sai Allah ya mayar da ita sabuwa fil, don azabar ta shigeshi sosai; da minti xaya ba za'a sassafta masa ba.Ana yi ana shayar da shi ruwan zafin jahannama.Kaico qaryar maqaryata ta qare sun shiga hannun Allah.

Xan Shi'ar ya rufe da cewa: Kuma wai Manzon Allah *Sallalahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Hushin Allah da nawa sun tsananta a kan wanda ya zubar da jinin zuri'ata ya kuma lave da su ya cutar da ni".

**Martani:**

Babu wani dalili da zai sa a la'anci Yazidu shi kaxai domin kuwa bai cancanci hakan ba; duk kuwa wanda ya dage akan tabbatar da la'ana a kansa to kamar yana cewa ne takwarorinsa daga cikin wasu sarakuna da halifofin musulunci duk la'anannu ne, kai sun ma fishi zama haka. Domin kuwa duk wanda ya san tarihin musulunci, ya san cewa akwai dayawa daga cikin shugabanni waxanda Yazidu yafisu dama-dama, kamar: Mukhtar xan Abu Ubaidu as-saqafi, sarkin Iraqi.Wanda ya tsaya kai da fata akan xauko wa Husaini fansa ta hanyar azzabtar da waxanda suka kashe shi.Wanda qarshe yai da'awar cewa Jibirilu ya zo masa da wahayi .haka kuma Yazidu yafi Hajjaju xan yusuf dama.

Domin kuwa gaba xayan mutane sun yi ittifaqi a kan cewa zaluncin Yazidu bai ko kama qafar nasa ba.

To, kuma dai duk da tabbatar haka,qololuwar hukuncin da ake iya yanke wa Yazidu da waxannan sarakuna takwarorinsa da makamantansu, shi ne na kasancewa "fasiqai" amma ba a la'ance su ba.Domin kuwa babu inda shari'a tayi umurni da la'antar wani fasiqi.

Nau'in mutanen da Sunnah ta zo da lafuzzan la'antar su sanannu ne. Kamar cewar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya yi: Allah ya la'anci varawon da zai saci qwarar qAai har a yanke masa hunnu. Da cewar da ya

yi:Allah ya la'anci wanda ya qirqiro bidi'a ko ya daurewa mai qirqiro ta gindi. Da kuma cewar da ya yi: Allah ya la'anci mai cin riba da kuma mai bayar da ita da mai rubuta ta da mai shaida akan ta. Da kuma cewar da ya yi: Allah ya la'anci mai auren xibar wuta da wan da akeyinsa don shi. Haka kuma da cewar da ya yi: Allah ya la'anci giya da mai shirya ta da kayan haxinta da xan dakon ta da abin da ake xaukar ta a ciki, da mai rarraba ta ga mashaya, da wanda yaci kuxinta.

To, ka ga ba zancen la'anta kenan,ga wanda ba xaya da ga cikin waxannan mutane ba.

To, kuma kowancan abu da mutane ke ta yakutar Yazidu a kansa. Wato abin da ya aikata wa mutanen Al-harrah, ai akan hujja ya yi shi. Domin kuwa bai xauki wani mataki a kansu ba bayan sun yaya ta yimasa tawaye da qorar xan ginsa da ke wakiltarsa a can, sai da ya aika masu Manzo bayan Manzo, yana neman su dawo suyi masa da'a. Amma hakan ta ci tura. A qarshe dai ya yanke shawarar aika Muslimu xan uqbata al-mariyyu, ya kuma umurce shi da keta alfarmar Madina tsawon kwana uku waxanda ya halatta yaqi a cikin ta idan ya yi nasara a kansu. Haka kuwa akayi. To kaji abin da mutane ke qyama matuqa a cikin al'amarin Yazidu. Wanda har watarana aka cewa Ahmad: ko zaka iya karvar hadisin da aka samo da ga Yazidu? Ya ce Allah ya sawwaqe. Ashe ba shi ne ya yi wa mutanen Madina abin da ya ga dama ba?!

Wannan kam gaskiya ne ya tabbata.Amma bai sa aka qarar da irin sharifan ba. kuma adadin waxanda aka kashe bai .kai dubban xaruruwa ba. Kuma jini bai malala har hubbaren Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba, balle ya maqare raularsa. Artabin da aka yi ma a lokacin ba a cikin masallaci aka yi shi ba.

Wannan kenan. Ita kuwa Ka'aba da ya ce wa an rusa an qona, wannan ba gaskiya ba ne. Domin kuwa Allah ya riga ya xaukaka ta ya girmamata, ya bata cikakar kariya, ta hanyar sakata qarqashin kulawar sa.

Babu wani lokaci; kafin musulunci ko bayansa, da Allah ya taba yar darwa wani tozarta wannan xaki nasa mai alfarma. Ai ka dai ji irin yadda ya yi biji-biji da ashabul fili, A lokacin da suka yi nufi tava dakinsa. Duk duniya babu wanda bai ji har gowar su ba.

Kuma tarihi ya tabbatar da cewa, ba a tava samun wani daga cikin sarakunan musulunci ba. Tun daga Umawiyyawa har Abbasiyawa da hakimansu, wanda ya tava nufar Ka'aba da wani mugun nufi; Babu wani daga cikin wakillan Yazidu ko Abdulmalik; Hajjaju xan Yusuf ko waninsu da ya tava nufatar haka.

Abin da ya tabbata shi ne, gaba xayan musulmi, na matuqar girmama wannan daki na Allah. Abida ma yakawo Ka'aba a cikin wannan mas'ala shi ne shigar da Ibn Zubairu ya yi a cikinta, wanda shi ne dakarun Yazidu suka so datsewa, har suka har ba masa manjariqu. Amma ba a Ka'abar sukayi niyyar harbi ba.

Wani abu da kuma zai qara tabbatar maka da cewa ba Ka'abar ce sukayi niyyar harbi ba shi ne, shigar da sukayi cikin masallacin bayan sun kashe xan Zubairu, suka yi xawafi. A matsayin hajjin wannan shekaara, a qarqashin jagorancin Hajjaju wanda ya gudanar da ibadar akan tafarkin xan Umar, ba tare da ya sava masa ko da a mas'ala xaya ba, kamar yadda Abdulmalik xan Marwanu ya hore shi da yi.

Ka ga a hankalce, da a ce sun zo ne da nufin tozarta Ka'aba da keta alfarmarta, da sun mayar da ita labari,tunda sun sami galaba da iko a kan haka. Kamar dai yadda suka aika da Zubairu lahira da ya shiga hannun su.

Haka kuma hadisin da xan Shi'ar ya kawo, wanda ya bayyana halin da wai, wanda ya kashe Husaini zai sami kansa a ranar qiyama, qar ya ce lafiyayya, tun daga far kon sa har qarshe  ( ina fatar baka manta da hadisin ba).

Ko shakka babu wannan hadisi maganace irin ta shaqiyyan mutane maqaryata, waxanda basu jin kunyar yi wa Manzon Allah *Sallahu Alaihi Wasallam* yaye-yayen qarya. Ah! To, idan ba haka ba,ya za'ace a hukunta wa wani mutum xaya xaukar rabin azabar gaba xayan 'yan wuta kan wani laifi? Wa ma ke iya kimanta rabin azabar ta su? balle Kadubi irin azabar da Allah ya tanadar wa Alu Fir'auna da Alu ma'idata da munafukai da sauran kafiran duniya. Haxa da wadda ya tanadarwa waxanda suka kashe Annabawa ba li ba la, da waxanda suka kashe nagartattun bayi magabata. Al'amarinfa na da matuqar  girma.

Na kuma tabbata cewa baka musun kasancewar zunubin waxanda suka kashe halifa Usmanu, ya fi na waxannan da suka kashe Husaini *Raliyallahu Anhu* girma nesa ba kusaba. To, irin wannan wuce gona da iri a cikin sha'anin Husaini ta wannan fuska, daidai yake da azarvavin Nasibawa da suke raya cewa matsayin Husaini daidai yake dana Harijawa ('yan tawaye) sa boda haka in an kashe shi an kashe banza. Dalilinsu kuwa a kan haka wai shi ne cewar da Annabi *sallallahu Alaihi Wasallam* ya yi: duk wanda ya taras da ku qar qashin jagorancin mutun xaya,ya so ya xaixaitaku, to ku sare kansa da takobi, ko xan waye. Muslimu ne ya riwaito hadisn, kai ka ji.

To, amma mu Ahlus-Sunnah wal jama'a, mun yi Allah wadai da waxannan ra'a yoya guda biyu na 'yan Shi'a ('yan Shi'ah) da Nasibawa; ba mu tare da kowannensu.

Mu a wurin mu, Kisan gillar da aka yi wa Husaini zalunci ne, kuma ya yi shahada. Waxanda kuwa sukayi karen aikin mutanen banza ne tantirai. Sannan kuma hadissan da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya yi umurni cikinsu da kashe duk wanda ya yi nufin xaixaita al'ummarsa, ba su shafi Husaini ba.

Ah! Ta yaya ko za su shafe shi  *Raliyallahu Anhu* tun da bai yi nufin fasa taron jama'ar Amada ba. Kuma ko da aka kashe shi yana bisa niyyar xayan abubuwa guda uku ne: ko dai ayar de masa ya koma inda yafi to, wato garin su. Ko ya yi sansani a wani wuri, a matsayin mai ribaxi. Ko kuma abashi dama ya yi tozali da Sarkin Musulmi Yazidu.

Ka ga babu xaya daga cikin waxannan abubuwa uku, da za'a iya fahimta a matsayin wariya da yuqurin basa garke, ko da akan tawili. Tafi munji waxanda ya nemi xaya daga cikin waxannan da mamaki daga gare su, adadin su bai tava kara ya karya ba, idan akayi la'akari da gaba xayan jama'ar Yazidu, na gida da dawa. Amma duk da haka, tunda har ya roka, to ya zama wajibi a karva masa.
Babu wani dalilin da zai sa ayi kunnen uwar shegu da shi, a matsayinsa na jikan Manzon Allah. Domin kuwa a hankali da shari'a, ko wanda bai kai darajarsa ba, ya nemi alfarmar xaya daga cikin waxancan abubuwa, ba ya halatta aqi saurarensa, Balle abashi baya ko a tage shi, Daxa balle a aikashi lahira.
Wannan ita ce aqidar Ahlus-Sunnah wal jama'a a kan wannan mas'ala.
Wannan kenan, haka kuma cewar da xan Shi'ar ya yi wai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Hushin Allah da nawa ya tsananta a kan duk wanda ya zubar da jinin wani daga cikin dangina ko ya lava ga zuri'a ta ya cutar da ni. qar ya ce.

Magana ce da babu wan da zai yarda da ta fito daga bakin ma'aiki *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai jahili. Domin kuwa imani da tsoron Allah *Subhanahu WaTa'ala* ne ya kamata agindaya a matsayin garkuwa da gambun tsari ga ran Hasan da Husaini, da ma kowane musulmi, ba dangantaka ba, ina fatar ka gane. Ah! Yau da wani daga cikin mutanen gidan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* zai aikata wani laifi, da hukuncinsa kisa ne ko datse hannu sai a ce: a'a tunda Ahlul baiti ne shi ya sha! Halas ne bisa haxuwar musulmi, Kai! Wajibi ne a zartar masa da hukuncin yadda za'a zartar wa kowa. Ko banza ingantattar magana ta zo daga shi Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yana cewa: Haqiqa abin da ya halakar da waxanda suke a gabanin ku shi ne kasancewar suna qyale wanda ya yi sata daga cikinsu idan xan wane ne. Amma idan ya-ku-bayi ne, nan take za su zartar masa da haddi. To, ku sani wallahi da yau Fatima 'yar Muhammadu za ta yi sata (Allah ya tsare) wallahi sai na yan ke hannunta.

Subhanallahi! Allah ya daxa tsira gare ka da aminci.

Ka ga shugaban talikai ya tabbatar maka da cewa da Fatima za ta faxa cikin wannan tarko, ba zai tsamo ta ba don tana 'yar cikin sa. Ka kuwa san, babu wanda Annabi ke so a cikin iyalansa kamarta.

Kuma idan baka sani ba. A kan haka ne malaman musulunci suka haxu a kan wajabcin jefe Bahashime har lahira, da zai yi zina, yana kuma da aure ko ya tava yi, da kashe shi, da zai kashe wani akan ganganci, babu sixixi ba saxaxa. Ko da kuwa wanda ya kashe bahabashe ne, ko barume ko baturke ko badaulame.

Kuma ai ta tabbata cewa: Annabi *Sallalahu Alaihi Wasallama* ya ce: Farashin jinanen musulmi xaya ne.

Wato ma'aiki na cewa ne: jinin bahashime baifi na waninsa tsada ba. Matuqar dai sun yi tarayya a qarqashin lemar xiyauci da musulunci. Kuma a kan haka ne gaba xayan al'ummar musulunci ta sandare. Ka ga kenan

hukuncin da za'a zartar wa wanda ya zubar da jinin bahashime shi za'a zartar wa wanda ya zubar da na wanda ba shi ba, matuqar dai ba da alhakinsu ba.

To, idan kuwa haka ne, ka ga ba wanda ya isa, ko xan uban waye. Ya ce mana wai Annabi *Sallalahu Alaihi Wasallama* ya ware mutanen gidansa da wata daraja, ta tsanantar hushin Allah a kan wanda ya zubar da jininsu. Ai adinin musulunci ba shegantaka ne ba.

Abin da Allah Ta'ala ya haramta shi ne kashe wata rai ba akan haqqi ba. Amma duk wanda za'a kashe a kan wani haqqi na shari'a, ko shi xan waye ko jikan wa, Bahashime ne ko waninsa, ba ruwan Allah balle har hushinsa ya tsananta a kan wanda ya zartar da hukuncin kisan a kansa.

Wanda Allah ke hushi, ya kuma ya la'anci wanda ya kashe shi, tare da tanadin azaba mai girma ga makashi, da yanke masa hukuncin dawwama cikin wutar jahannama, shi ne muminin da aka aika lahira bai ji bai gani ba.

Abin da ke sa jinin mutum ya tsira ko ya halatta a shari'ar musulunci, abu ne da ya kundume bani hashim da wanda ba su ba.

Irin waccan magana ta banza, babu wanda ke jingina ta ga Manzon Allah *Sallalahu Alaihi Wasallama* sai munafuki. Wanda ke son gurvata tsarkaken ruwan annabcinsa. Idan kuwa har ba munafuki ba ne, to lalle kuwa jahili ne, wanda bai san irin adalcin da Allah Ta'ala ya aiko Muhammadu don tabbatarwa ba.

Cewar da xan Shi'ar ya yi, hushin na Allah da manzon sun haxa da: wanda ya lave ga zuri'ar manzo ya cutar da shi.

To, duk da yake gaba xayan hadisin bai ingantaba. Amma ai ana iya lavewa ga al'ummar Manzon Allah *Sallalahu Alaihi Wasallama* ko sunnar sa a cutar da shi domin kuwa ko shakka duk wanda ya keta alfarmar waxannan abubuwa biyu, dai dai yake da wanda ya keta ta zuri'arsa, kuma duk cutarwa ce gareshi *Sallalahu Alaihi Wasallama* yin haka kuwa haramun ne tabbas.

## 2.10 Garin Neman Qiba an Samo Rama

A qoqarin 'Yan Shi'ah na ganin jikinsu yafi na musulmin duniya yin vul-vul, sai gashi sunfi kowa rama, wanda hakan ta sa mazahabarsu zama cibiyar vata da varnace-varnace. Bari kaji..

Xan Shi'ar ya ce: Muna son masu hankali da su sa idon basira su gane mana waxanda sukafi cancanta da amincin Allah, tsakanin waxanda su ka tsarkake Allah da mala'ikunsa da Annabawansa da imamansa. Suka kuma tsarkake shari'ar sa daga duk wata qazanta. Da waxanda suka vata sallar su sanadiyar qin yin salati ga imaman da Allah ya zavar masu. Suka koma suna ambaton imaman wasunsu, shin waxannan ne suka fi ko waxanda suka tsaya kan zavin Allah suka watsar da wanin sa?

Kaji tambayar mutumin naka!

Martaninmu a nan shi ne: qoqarin da kuka yi na kore wa Allah Ta'ala waxancan siffofi na kamala, waxanda suka hada da: Rayuwa, ilimi, qudura, magana, cikakken iko, so, qi, yarda da fushi. Sai ka ce Allah yafi qarfin

waxannan siffofi balle ya siffanta da su. Kuma wai za'ayi su dace dashi tunda sandararrun abubuwa da siffofi ma na da su?.

To ku sani wannan ba wani abin mazan gwari ne ba. Nakkasa alqaxarin Ubangiji ne da Annabawansa kuka yi. Kuma zance ne kuka yi irin na jahamiyawa. Waxanda ke cewa: Tsarkake Allah daga kama da wanin sa, na wajabta kore waxancan siffofi daga gare shi. A kan haka sukace Allah Ta'ala ba ya da rai, jahili ne, kasasshe, kurma, kadar kasuwa. Bai so bai qi, bai yarda bai fushi. Ba a ganin sa, kuma ba ya da hannu a cikin komai. Kuma a karansa, ba ya iya sukkuna komai.

To ka ga haka, sun kamanta Allah da sandararrun abubuwa nakkasassu; adai dai lokacin da suka kore masa siffofin cika da kamala. Ka ga kenan wannan ba tsarkakewa ce ba. Qazantawa ce da gurguntawa.

Abin da ake cewa tsarkakewa a wannan babi, shi ne: kore wa Allah duk wata naqasa da ke takin saqara da wata siffa ta kammala ta yarda ba ta yiwuwa su sha innuwa xaya. Wato a kore masa: mutuwa, da angaje, balle barci. A kore masa: kasawa, jahilci, da bukata, kamar yadda ya kore wa kansa su a cikin littafinsa. Wato a lokaci xaya, tabbatar masa da duk wata siffa ta kamala, tare da kore masa kishiyoyinsu; na naqasa. A kuma tsarkake shi da ga yin kama da wani abu daga cikin halittarsa, ta kowace fuska, tare da kore masa duk wata naqasa, ba tare da iyakancewa ba. Haka kuma a tsarkake shi daga yin kama da wani abu a cikin waxancan siffofi da aka tabbatar masa na kamala.

Wannan kenan. Ta vangaren Annabawa kuma, sai aka wayi gari kun kore masu abin da Allah Ta'ala ya tabbatar masu na kamala da xaukakar daraja. Waxanda ke samuwa garesu ta hanyar tuba da neman gafara. Wanda hakan ke xaukaka darajar su ninkin-ba-ninkin. Da wannan mugun aiki naku, sai aka wayi gari kun qaryata abin da Allah Ta'ala ya fadawa duniya ta wannan fuska; kuka canza wa tuwo suna. Kuka ce wai ciratar xan Adamu daga duniyar jahilai da vata da zalunci zuwa ta ilimi da shiriya da adalci, naqasa ne gare shi.

Kun jahilci kasancewar haka wata ni'ima da qudura mafiya girma daga wurin Allah. A inda yake xaukaka darajar wasu bayi nasa daga matakin naqasa zuwa na kamala. Ta yadda xayan su zai iya kasancewa mai iko akan xanxana alheri da sharri, da tantance banbancin su. Har a wayi gari son da yake na ganin alheri ya tabbata, sharri ya gushe, ya shafe na wanda alheri kawai ya sani. Kamar yadda Umar xan Haxxabi *Radiyallahu Anhu* ya ce: Ba za a iya yi wa musulunci sukuwar salla, a yi wa xan mansa dai dai ba. Sai an wayi gari al'umma ta haifi wanda bai son komai na jahiliyya ba.

Wannan kenan.Shi kuwa zancen tsarkake imamai, wani abu ne na kunya da bai kamata mai hankali ya fada ba,musaman ixan akayi la'akari da wancan imamin mai taken "Malam Babu",wanda baya da wani amfani duniya da lahira.

Haka kuma zancen tsarkake shari'ah daga qazanta da qasqanci, wani abu ne tuni an riga an rufe littafinsa. Domin kuwa bayani ya riga ya gabata akan cewa a cikin mas'alolin da Ahlus-Sunnah suka yi ittifaqi a kansu a matsayin

shari'ah, babu xaya da keda ko da amon qazanta balle qasqanci. Savanin 'yan Shi'ah waxanda mazahabarsu ke maqil da qazantattu kuma qasqantattun mas'aloli irin waxanda ba mai su a duniyar musulunci.

Bari kuma mu koma ga cewar da ya yi:.........ko waxanda su ka bata sallarsu sakamakon qin yin salati ga imaman da Allah ya zabar masu. Suka koma suna ambaton imaman wasunsu.

To, a nan xayan biyu. Ko dai ya kasance xan Shi'ar na nufin yi wa imamai goma sha biyunan nasu salati wajibi ne. Koko a'a, wajibi dai ne a yi wa wani kevantacce daga cikinsu, ko kuma wani can baqon haure; wanda dai ba Annabi *Sallalahu Alaihi Wasallama* ba. Ko kuma ya kasance yana nufin yin salati ga mutanen gidan Annabi *Sallalahu Alaihi Wasallama* kacokwan wajibi ne.

Idan xan Shi'ar na nufin fassara ta farko, to, ko shakka babu hakan ta tabbatar da kasancewarsu kwatarnen vata da varna, da yi wa shari'ar Muhammadu *Sallalahu Alaihi Wasallama* tawaye. Domin kuwa da mu da su babu wanda tilas ba ta sa ya san cewa Annabi *Sallalahu Alaihi Wasallama* bai umurci musulmi ya yi wa wani daga cikin imaman nasu goma sha biyu salati ba, daxa ko a cikin sallah ne ko wajen ta. Kuma babu wani musulmi ma da aka samu yana aikata haka a zamaninsa. Babu kuma wanda ya riwaito haka daga Annabi *Sallalahu Alaihi Wasallama,* ta hanya ingantatta ko mai rauni. Kai! Hasali ma ba wajibi bane a kan wani musulmi ya riki xaya daga cikin imaman goma sha biyu shugaba, alhali ga Annabi raye, balle har yi masa salati acikin sallah ya zama wajibi.

Duk kuwa wanda ya ce yi wa waxannan imamai salati cikin sallah wajibi ne, har kuma ya vata sallar wanda bai yi haka ba, to ya canza alqiblar addinin Muhammadu*Sallalahu Alaihi Wasallama* ya mayar da shi wani abu, kamar yadda Yahudawa da nasara suka sauyawa addinin Annabawansu fasali.Wannan abun da 'yan Shi'ah ke qoqarin tabbatarwa, baya tabbatuwa. Domin kuwa sallar da musulmi suka yi zamanin rayuwar Annabi, ingantattace bisa haxuwar kan al'umma tabbas. Tattare kuma da rashin yin salati ga imaman a cikinta.

Idan kuwa xan Shi'ar ya ce a'a muna nufin fassara ta biyu ne, wato wajabcin yin salati wa mutanen gidan su Annabi *Sallalahu Alaihi Wasallama* saboda matsayin da suke da shi.

To, sai mu ce masu: Mutanen gidan su Annabi yawa ne da su. Matansa kaf, da gaba xayan banu Hashim, har ma da banu Abdul-muddalibi, a bisa wani zance, duk Ahlun-nabiyi ne. Kuma Shi'ah imamayya ba su ganin mafi yawan waxannan bayin Allah da gashi a kai. Domin a wurin su abbasiyyawa ba kowa ba ne. Musamman halifofi daga cikinsu. Ga shi kuwa suna daga cikin Ahlu Muhammadin. Haka kuma suna sukar lamarin duk wanda ya yarda da shugabancin Abubakar da Umar *Radiyallahu Anhum*. Ga shi kuma mafi rinjayen banu Hashim sun yarda da shugabancinsu, Duk wanda yake xan halas daga gidan Hashim yana tare da Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhumam* sai

fa ‘yan qwarori. Amma in ban da su, duk wani ma’abuci ilimi da kishin addini a wannan gida baya qyamar Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhumam.*

Babban abin ban mamaki ko ince ban ta kaici da waxannan ‘‘yan Shi’ah, duk bai fi tattare da irin tinqahon da suke yi na so, da girmama mutanen gidansu Annabi *Sallahu Alaihi Wasallama.* Sai gashi kuma sune a gaba, a lokacin da Tatar suka far wa bagadaza, Hedikwatar Hilafar musulunci a lokacin. Su dai ‘yan Shi’ah nan sune suka yi masu jagora suka salwantar da rayukan musulmi Hashimawa. Waxannan Allah ne ka xai yasan adadinsu, balle daxa waxanda ba su ba. Suka kuma kashe kusan mutum dubu xari da goma sha takwas da xari tara da saba’in a cikin sasannin Bagadazar. Suka kuma kashe Halifan lokacin, Ba abbase. Suka ribace mata da kananan yaran Hashimawa; Aka hada kan ‘yan matan Hashimawa da wasunsu duk aka kai wa Yazidu da takwarorinsa sarakuna. Duk haka ta farune da taimakon ‘rafelawa.

Ka ko ga babu wata qiyayya da za’a nuna wa Alu Muhammadin *Sallalahu Alaihi Wasallama* wadda ta kai haka. Ko shakka babu.

Kai! In ta kaice maka labari, babu wani abu da ‘yan Shi’ah za su soki lamirin wani da shi, a wannan babi, face hakan tafi cancanta da su ,nesa ba kusa ba.

### 2.11 Na Gaba ya yi Gaba

Xan Shi’ar ya yi qoqarin karkata akalar wasu darajoji na Sayyidina Ali, tare da kafa hujja dasu, don tabbatar da fifiko da imamancinsa. Ga abin da yake cewa:

Abu na shida: Ai ba da banza jama’ar Shi’ah ‘yan-sha-biyu suka zavi Sayyidina Ali a matsayin shugaba abin yi wa da’a ba gare su, sun yi haka ne saboda ganin irin darajoji da martabobin da basu qidayuwa. Waxanda masoya da magabatansa su ka riwaito, waxanda kuma ke tabbatar da kasancewarsa xan goma.

Bayan wannan kuma sun ga iri aibubban da wai junansu su ka riwaito a kan wasu Sahabbai waxanda yawansu ya zarta hankali amma ba su samo aibi ko xaya ta a kan sayyidina Ali. To wai a kan haka ne su ka sakakance da babu wanda ya cancanci saurarawa da shiga gaban sahu sai shi, wai saboda ya sami shedar tsarki daga bakin masoya da maqiya.

Sun kuma yi watsi da duk wanda ba shi ba, saboda ganin waxanda ma suka yarda da shugabancin nasa, sunyi masa raxan-raxan ta hanyar riwaito abun kunya a kansa. Wanda hakan ke hana shugabancinsa karvar sunansa a shari’a.

Xan Shi’ar ya ci gaba da cewa, kuma yanzu za mu ambaci kaxan daga cikin darajojin Alin, waxanda suka inganta a wurin Ahlus-Sunnah. Domin kuwa littafai da zantukan da suka aminta tare da dogara a kansu duk sun naqalto su. Za mu kuma yi haka ne, don ta zama hujja a kansu ranar alkiyama. Inji shi.

Daga cikin waxannan darajoji akwai abin da Abul-Hasan Al-Andalusi ya riwaito a cikin littafin: Al-jam'u Bainas-sihahis-sitta, da: Muwaxxa Maliku, da ingantattun littafan Buhari da Muslimu, da sunanu Abu Dawuda, da sahihu Tirmizi, sahihu Nisa'i, daga Ummu–Salmata matar Annabi *Sallalahu Alaihi Wasallama* wadda tace: Ayar da Allah Ta'ala ke cewa: Allah na nufin ya tafiyar da kazanta kawai daga gareku, ya ku mutanen babban Gida! kuma ya tsarkake ku, tsarkakewa.(33:33) ta sauka ne ga Manzon Allah *Sallalahu Alaihi Wasallama* a lokacin da yake xakinta. Ta ce: a lokacin ina zaune daura da kofa. Sai na ce ya Manzon Allah! ina fatar dai ni ma ina daga cikin mutanen gidanka xin nan, sai ya karva mata da cewar: Anya? Ina dai yi maki fatar alheri ki na dai daga cikin matar  Annabin Allah. Taci gaba da cewa: A lokacin da wannan abu ke faruwa, Ali da Fatima da Hassan da Husaini *Radiyallahu Anhum* duk suna cikin xakin nawa. Sai kuwa ma'aiki ya yafa masu mayafinsa, ya ce: Ya Ubangiji waxannan su ne mutanen gidana. Allah ka tafiyar da kazanta daga garesu, ka kuma tsarkake su tsarkakewa.

To abin da za mu gayawa wannan xan Shi'ar a matsayin martani, a kan wannan magana shi ne: Na farko dai ya sani, Nagaba ya yi gaba. Domin kuwa darajojin halifa Abubakar da Umar *Radiyallahu Anhum* waxanda suka tabbata a cikin ingantattun hadisai, sun fi waxanda suka tabbata na darajojin halifa Ali *Radiyallahu Anhu* yawa da kabri.

Kuma waxannan hadisai da ya ambata. Ya ce kuma suna kunshe a cikin ingantattun littafan hadisan Jumhurun musulmi, kuma wai amintattun littafai da zantukan su duk sun nakalto su, qarya ce yake yi wa Jumhurun. Domin kuwa masana ilimin hadisi sun yi ititfaqi a kan kasancewar mafi yawan waxancan hadisai da ya ambata qarya, ko masu rauni. Su ku wa waxanda suka inganta daga cikinsu ba su xauke da wani abu da ke nuna imamancin Ali, ko fifikon darajar sa a kan Abubakar da Umar. Hasalima bai kevanta da darajojin da hadisan suka qunsa ba; ya dai yi tarayya da wasu ne daga cikinsu. Savanin darajojin da suka tabbata na Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhu* waxanda babu wanda ya yi tarayya da su, a cikin mafi yawan su. Musamman ma dai Abubakar *Raliyallahu Anhu* wanda bai yi tarayya da kowa ba a cikin gaba xayan darajojin da ya kevanta da su.

Su kuwa abubuwan kunyar da ya ce an riwaito na waxannan halifofi uku, wai ya sani sun fi qarfin haka. Idan ma har wani abu ne, sai dai a ambace shi "qorafi". Amma ba abin kunya ba. Sannan kuma, babu wani qorafi da za'ayi kan su, face akwai kwatankwacin sa ko wanda ya fi shi, da za'a iya yi kan Ali *Raliyallahu Anhu*.

Ka ga da haka, ta tabbata duk abin da ya faxa a wannan fasali kar ya ce cas. Nan gaba kaxan kuma za mu tona asirinsa a kan haka, dalla-dalla, in Allah ya so.

Wannan kenan, idan kuma ba ka manta ba, xan Shi'ar ya ce wai: Shi'ah 'yan-sha-biyu sun riki imamu Ali shugaba a gare su. Saboda ganin irin yadda masoya da magabata suka yi masa wankan tsarki, tare kuma dayin biris da duk

wanda ba shi ba. Saboda kasancewar har waxanda ma suka yarda da shugabancinsu nada qaiqayi a zukatan su a kansu.

To, kafin muje ko ina, muna tabbatar wa 'yan Shi'ah cewa wannan magana qarya ce. Domin kuwa waxanda ba su yarda da Ali *Raliyallahu Anhu* ba, su ne kan gaba wajen sukar sa. Hasali ma yawan QungIyoyin da ke sukar lamirin sa su ne mafiya rinjaye, idan akayi la'akari da masu qorafe-qorafe a kan Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhu* da kuma waxanda suka wuce wurin cikin girmama Alin kansa; wato "Gulatu".

Ka ga dai tumun fari, Harijawa sun yi ittifaqi a kan kasancewar Ali kafiri. Wai Kuma duk da haka sun fi Gulatu daraja a idon musulmin qwarai; saboda su Gulatun, a wurinsu Sayyidina Ali Allah ne. Sukan kuma sassafta wani lokaci su ajiye shi matsayin Annabi.

Ba wannan kawai ba. Jamhurun musulmi sun fi ganin Harijawa da sauran Sahabban da suka shaya daga da Ali tare da su, da gashi aka, a kan ''yan Shi'ah masu aqidar biyar imamai goma sha biyu. Waxanda ke kan aqidar kasancewar Alin imami ma'asumi.

Wani abun kuma da zai qara tabbatar wa ka da irin yadda halifofin can uku na kafin Ali, suka yi masa fintinqau a wannan fage, shi ne irin gaba xayan al'ummar Amada ke saka masu bakin albarka, idan ka cire 'yan Shi'ah la'anannu. Duk da kuwa Harijawan can da ke kafirta Ali *Raliyallahu Anhu* da Marwaniyawa da suka xauke shi matsayin wani qasurgumin azzalumi. Suka kuma sa qafa sukayi fatali da halifancinsa. Duk waxannan mutane sun yarda da shugabancin Abubakar da Umar, har ma da na Usman *Raliyallahu Anhu* tare da zama qarqashin tutocinsu, tattare kuwa da kasancewar babu zumunci a tsakaninsu da su ko na anini. To, ta yaya za a ce wai masoya da magabata su yi wa Ali *Raliyallahu Anhu* wankan tsarki, tare da yin kunnen uwar shegu da waxancan halifofin uku. Alhali kuwa wannan ingantattar magana da muka fada ta cika kunnen duniya?

Haka kuwa tabbataccen abu ne cewa mutanen da ke sa wa waxancan halifofi uku bakin albarka daga cikin wannan al'umma, su ne mafi yawa da girman daraja a cikinta. Su kuwa masu yi wa Ali *Raliyallahu Anhu* kwarar vawan kalgo, ta hanyar naxa masa rawanin kafirci da fasiqanci da varna, qungiyoyi ne sanannu kuma tantantattu. Amma kuma tattare da ha akan sun yi wa ''yan Shi'ah ko-ta-kwana a fagen ilimi da kishin addini, da qarfin tuwo. Ko alama ''yan Shi'ah ba su kai su ba a wannan fage. Balle su yanke su da takobin hujja ta hankali da basira, ko su goga a kaifunsu a kan fandun dutse ranar fama.

Kuma kasan wani abu? Babu qungiya xaya daga cikin qungiyoyin can da ke kafirta Ali ko ganinsa azzalumi, da aka sheda da wani aiki na ridda. Savanin waxanda ke kuxa da kwarzanta shi tare da sukar lamirin waxancan duwatsu guda uku na daular musulunci. Wato kamar Nusairiyya (Al-Galiyah) waxanda ke jin shi Allah ne. Da Isma'iliyah (Al-Mulhidah) waxanda har gwamma Nasiriyya da su. Da kuma Galiya, waxanda ke jin shi Annabi ne. Duk

waxannan qungiyoyi kafirai ne murtaddai. Bisa shaidar Allah da Manzonsa da duk wani malamin musulunci na gari.

Ko shakka babu duk wanda ke da masaniya da addinin musulunci komai qanqantarta, ba ya musun kafirci duk wanda ya naxawa wani mutum rawanin ubangizantaka. Ko ya yi imani da wani Annabi bayan muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* koko a'a anabcin ba nasa ba ne, na Aliyu ne mala'ika Jibrilu ya kai masa a kan kuskure.

Haka kuma ba ya musun musulncin Harijawa. Waxanda ke kafirta Ali *Raliyallahu Anhu*da la'antarsa. Da kuma na waxanda suka yaqe shi suka kuma la'ance shi daga cikin Sahabban Mu'awiyah da Bani Marwanu da wasunsu. Waxannan mutanen gaba xayan su musulmi ne. Domin sun yarda da musuluncin da shari'o'insa; suna salla, suna azumi, suna zakka, suna hajji. Suna kuma haramta duk abin da Allah da Manzonsa suka haramta. Babu mutum xaya daga cikinsu wanda kafircin sa ya bayyana. Duk wanda ya san tarihin musulunci ya san waxannan mutane na matuqar girmama musulunci da shari'o'insa.

Ka ga hakan ta tabbatar mana da cewa,cewar da xan Shi'ar ya yi wai gaba xayan magabata sunyi wa Sayyidina Ali wankan tsarki, savanin waxancan halifofi uku, qarya ce kawai.

## 2.13 Hadisin Mayafi ba Hujja ba ne

Shi kuwa hadisin mayafi ko shakka babu ingantacce ne. Domin kuwa Ahmada da Tirmizi sun riwaito shi da ga cikin hadisan Ummu Salma. Haka kuma Muslimu ya riwaito shi a cikin ingantaccen littafinsa, daga cikin hadissan Aisha, wadda tace: Watarana da hantsi Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya fita yafe da wani mayafi mai faxi na baqin gashi. Sai ga Hasan xan Ali ya iso, sai ya gayyace shi ciki. Sai kuma ga Husaini ya iso,shi ma ya gayyaceshi, sai kuma ga Fatima ta iso, ita ma ya gayyace ta, qarshe kuma sai ga Ali ya iso, shi ma ya gayyace shi ciki. Sannan ya ce: Allah na nufin kawai ya tafiyar da qazanta kawai daga gare ku ya ku mutanen Babban Gida! Kuma ya tsarkakeku tsarkakewa (33:33).

Abin da muka son tabbatarwa anan shi ne,wannan hadisi tattare da ingancinsa, ba ya zama hujja akan imamancin Ali,kamar yadda xan Shi'ar ke qoqarin tabbatarwa.

Dalininmu shi ne: Kasancewar ba Ali kawai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya gayyata a cikin mayafin ba,balle ace ya gayyaci Fatima, Hassan da Husaini, ka kuwa san mace bata shugabanci, ka ga kenan wannan falalar bata nufin tabbatar da lasisin shugabanci ga waxannan mutane.A'a abu ne da wasu keda hakki a kansa.

Iyakar fassarar da wannan hadisi ke iya xauka itace: Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya roi Allah ya tafiyar da kasanta daga waxannan mutane, ya kuma tsarkake su tsarkakewa. Wato su zama mutane masu tsoron Allah a dalilin tsarkin can da tsarkakewa.

Shi kuwa nisantar qazanta da Allah ya yi alkawali abu a kan kowane mumini, kamar yadda aka ambaci gaba xayan mumine da tsarki. Dubi abin da Allah ke cewa: *Allah baya nufin domin ya sanya wani kunci a kanku kuma amma yana nufin domin ya tsarkake ku, ya kuma cika ni'aimar sa a kanku (5:6).*

A wata ayar kuma ya ce: *Ku karvi sadaka da dukiyoyinsu kana mai tsarkake su, sanan kana mai tabbatar da kirkinsu. (9:103).*

A wata ayar kuma ya ce: *Haqiqa, Allah yana son masu tuba, kuma yana son tsarkakewa (2:222).*

To, ka ga iyakar abin da wanan hadisin ke nufi, shi ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya roi Allah *Subhanahu Wa Ta'ala* akan aikata alheri da nisantar sharri, Amma ba imamanci ba.

Ka kuwa ba afi Abubakar siddiqu *Raliyallahu Anhu* ba a fagen aikata alhairi. Tun da har Allah Ta'ala ya bayar da labarinsa da cewa, *shi mafi taqawa ne wanda yake bayar da dukiyarsa, alhali yana tsarkaka. Alhali babu wani mai wata ni'ima wurinsa wanda ake neman sakamakonta. Face dai neman yardar Ubangijinsa mafi xaukaka. To, lalle ne zai yarda (da sakamakon da za a ba shi) (92:17-21).*

Haka kuma cewar da Allah ya yi: *Kuma masu tserewa na farko daga Muhajirun da Ansar da waxanda suka bisu da kyautatawa, Allah ya yarda daga gare su, kuma ya yi masu tattalin gidajen aljanna: qoramu suna guxana a qarqashinsu. Suna madawwama a cikinsu har abada. Wancan ne babban rabo mai girma (9:100)* na tabbatar da cewa waxannan bayin Allah sun tsaya tsayin daka akan aikata abin da Allah ya yi horo dashi, da nisan tar abin da Allah ya yi hani da shi. Domin sai da haka ne suke iya samun wannan sakamako na yar dar Allah.

Ka ga kena a haka, kanfa, kazantar da samun cikakken tsarki daga zunubi sun zama daga cikin siffofin su. Kuma sun yi tarayya da mutanen can huxu (ahlul baiti) a cikin wancan bakandamin du'a'i da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya yi masu.

Ba wannan ma ka wai ba, tarihi ya tabbatar da cewa akwai mutane da dama; ba waxancan huxun ba. Waxanda Manzon Allah ya roi Allah ya yi salati a kansu. Ya kuma rokar wa wasu masu yawa aljanna da gafarar allah da wasu muhimman abubuwa daba waxannan ba. Waxanda suka fi waccan du'a'i girma. Amma kuma hakan ba ta wajabta zaman waxanda ya yi wa du'a'in na biyu mafiya girma a kan sabikunal auwaluna.

Kuma dalilin da ya sa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya yi wa Ahlul- kisa'i wannan du'a'i, shi ne kasancewar nisantar qazanta da zankake wajibi a kansu. Saboda haka ya roi Allah ya taimakesu a kan tabbatar da haka. Don kada kashinsu ya bushe; su wayi gari ana Allah waddai da su, kuma cikin azaba.

Wannan du'a'i da Annabi ya yi masu, da kasancewarsa karvabbe a wurin Allah, zai sa waxannan mutane su zama abin madalla da lulluvewa da rahama.

## 2.13 Tilas Mai Hawan Ruwa ya yi Babban Masaki

Xan Shi'ar ya yi qoqarin kafa hujja a kan fifikon darajar Ali *Raliyallahu Anhu* da imamancinsa, da ayar da Allah Ta'ala ke cewa a cikin ta:

﴿ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓا۟ إِذَا نَـٰجَيْتُمُ ٱلرَّسُولَ فَقَدِّمُوا۟ بَيْنَ يَدَىْ نَجْوَىٰكُمْ صَدَقَةً ۚ ذَٰلِكَ خَيْرٌ لَّكُمْ وَأَطْهَرُ ۚ فَإِن لَّمْ تَجِدُوا۟ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ﴿١٢﴾ ﴾ المجادلة: ١٢

*Ya ku waxanda suka yi imani! Idan za ku ganawa da Manzon Allah, to ku gabatar da 'yar sadaka(58:12)*

Xan Shi'ar ya kafa hujja da cewa, Sarkin Musulmi Ali xan Abu Xalib *Raliyallahu Anhu* ya ce: Babu wanda ya yi aiki da wannan aya daga cikin Sahabbai sai ni. Kuma albarkaci na ne Allah ya sassautawa wannan al'umma al'amarin wannan aya.

**Martani:**

Ya kamata xan Shi'ar ya fahimta cewa wannan ummarni da Allah *Subhanahu Wata'ala* ya yi, na gabatar da wata 'yar sadaka don gana wa da manzon. Bai zama wajibi a kan kowane musulmi ba. Balle wanda bai yi ba yayi laifi. Wajabcin ya ta kaita ne a kan wanda lalurar ganawa da manzo ta kama. To, kuma sai akayi sa'a, a lokacin da wannan ayar ta sauka Ali *Raliyallahu Anhu* ne kawai wannan bukatar ta ganawa da manzo ta kama. Bai kuma yi wata-wata ba sai ya gabatar da sadakar. Kamar yadda dai malamai suka yi ittifaqi.

Ka ga kenan, wannan ummarni dai- dai yake da ummarnin da Allah ya yi da yanka hadaya, ga wanda ya hada hancin aikin hajji da na umara lokaci xaya. Ko kuma wanda aka datse.

## 2.14 Ayar:

﴿ ۞ أَجَعَلْتُمْ سِقَايَةَ ٱلْحَآجِّ وَعِمَارَةَ ٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ ﴾التوبة: ١٩

Xan Shi'ar ya ce an samo daga Muhammad xan ka'abu al-kwrari, wanda ya ce: Watarana Xalhatu xan Shaibata; xan Bani Abdud-xari, da Abbas xan Abdulmuddalibi, da Aliyu xan Abu xalib sun yi musanyyar alfahri wa junansu wai. Na farkon ya ce: In na ga dama sai in buxe Ka'aba in kwana ciki tun da a hannuna mabuxanta suke. Na biyun kuma ya ce: Ni kuma tunda ni ke shayar da Alhazzai ruwa, in na so sai in kwana a cikin masallacin. Shi kuwa na ukun, wato Sayyidina Ali, wai sai ya ce: To duk kusaurara. Ni nayi malinku. Don na share tsawon wata shida ina fuskantar Ka'abar ina sallah, kafin kowa ya yi. Kuma nine Antaru sarkin yaqin Manzon.

Wai rufe bakunan su keda wuya sai Allah ya saukar da ayar da ke cewa:

*Shin kun sanya shayar da mahajjata da ruwar da masallaci mai alfarma kamar wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira, kuma ya yi jihadi a cikin hanyar Allah? Ba su dai-dai ta a wurin Allah. Kuma Allah ba ya shayar da mutane azzalumai( 9:19).*

**Martani:**

Martanimu a kan wannan magana shi ne: Wannan hadisi dai qarya ne. Domin babu wani littafi daga cikin littafan hadisi da ya zo da shi. Kuma kayan cikin hadisin na daxa tabbatar da haka. Bari ka ji:

Mutumen can na farko da xan Shi'ar ya ambata; wato Xalhatu xan Shaibatu, babu shi a cikin kundin tarihin musulunci. Shaibatu xan Usmanu xan Xalhatu shi ne wanda aka sani mai hidimar xakin Ka'aba. Ka ga wannan kawai ya isa tabbatar da rashin ingancin hadisin.

Sannan cewar da ya yi wai xan Abbas ya ce: in na ga dama sai in kwana a cikin masallacin (Ka'aba) To, xan saurari wannan magana da kyau. Ka kuma tambayi kanka, wace daraja ce kega wanda ya kwana a cikin masallacin Ka'aba, balle har ya kafa wa wani hujja da shi?

Haka kuma cewar da ya yi Ali *Raliyallahu Anhu* wai ya ce: Na share wata shidda ina fuskantar Ka'abar ina sallah kafin kowa.

Wannan magana ce da babu mai musun kasancewarta karya. Domin kuwa tarihi ya tabbatar da cewa tsakanin musuluntarsa da ta Zaidu da Abubakar da Khadijah *Raliyallahu Anhu* bai fi kwana xaya ba ko qasa ga hakan ba. To ya ya za'a ce ya riga kowa sallah da wata shiddah? Ko a ce ya ce shi ne gishirin yakokan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* Tunda tare da dubban mutane akayi su, ba shi kadai ba?

## 2. 15 Hadisin Wasiyya Qagagge Ne

Xan Shi'ar ya kafa hujja a kan cewa wai, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wasicci ga Ali *Raliyallahu Anhu* da ya zama magadin halifarsa kai tsaye ba yan ya wuce, da hadisin da ya ce wai, Ahmad xan Hambali ya riwaito daga Anas xan Maliku. Wanda ya ce: watarana mun nemi salmanu ya tambayar mana Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* shin waye yarima mai jiran gadon sa? Sai kuwa ya tambaye shi.

Wai sai Manzon Allah ya mayar wa Salmanu da tambayar da cewa: waye ka ji ance shi ne yariman da ya gaji gadon Musa? Sai Salmanu ya karva masa cewa: Yusha'u xan Nunu ne. Daga nan manzon ya ce masa: To ni, Yariman da ke jiran gadona, ya biya bashin da ke kaina, ya kuma cika arqawurra na shi ne Aliyu xan Abu Xalib.

**Martani:**

Ka ga wannan maganar qarya ce lafiyayyarta bisa haxuwar malamai masana hadisi. Kuma ko alama babu shi a cikin musnadin Imamu Ahmad xan Hambali. Eh! Gaskiya ne Ahmad xin ya wallafa littafi akan darajojin Sahabbai. A inda ya ambaci darajojin Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhu* da na wasu Sahabbai. Amma kuma ka sani ba duk abubuwan da fada a kansu suke ingantattu ba; ya ambaci har yaye-yaye a cikin don a san su, a yi hattara da su.

Kuma ka sani shi wannan littafi nasa cike ya ke makil da abubuwan da al-kaxai'i ya riwaito da ga malamansa. Waxanda mafi yawansu qaryayyaki ne. Kamar yadda za mu fexe Biri har wutsiya a kan haka nan gaba in Allah ya so, ta hanyar ambato wasu daga cikinsu.

Wani abin da ya kwabe wannan lamari shi ne, kasancewar malaman can qadai'i kan riwaito hadissai daga tsararrakin Ahmad. Su kuwa ''yan Shi'ah saboda tsabar jahilci, da sun yalla ido sun ga irin wannan hadisin qadai'in ya riwaito daga waxancan malamai nasa, ya kuma cusa shi cikin wancan littafi na Ahmad, sai suce Ahmad ya ce. Ahmad din ma xan Hanbali. Alhali kuwa zancen kudai'i ne ba na shi ba. Shi kuma wanda aka riwaito zancen daga gare shi xaya ne daga cikin malaman kudai'in. Waxanda ke yowar riwaya daga tsararrakin Ahmad din.

Bayan wannan ma, a cikin wannan littafin akwai qare-qaren da da Ahmad xin; wato Abdullahi ya yi. Musamman a kan masaniya na Aliyu xan Abu Xalib *Raliyallahu Anhu* Abubuwan da wannan yaro ya qara a wannan wuri na da yawa sosai.

## 2.16 Bai Isa Kayan Gabas Ba

Xan Shi'ar ya kawo wata magana mai kama da hadisi. Wadda ya so ya yaudari mutane da ita a qoqarin fitowa da darajar Ali *Raliyallahu Anhu*. Ga abin da ya ce:

An samo wai da ga Yazidu xan Abu maryam daga Ali *Raliyallahu Anhu* wanda ya ce: Watarana ni da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* mun kama hanya tinki-tinki har muka isa xakin Ka'aba. Ya ce in duka. Sai ya taka kafa xuna. Na yunqura inyi sama da shi. Abun ya fasqara. Ganin haka sai ya sauko ya duka a gabana. Ya ce: Taka kafaxuna. Taka wata keda wuya sai ya yi sama dani. Sai na ji da zan so a lokacin zan iya tavo sama'u. Sai dai na kama saman Ka'aba na xale, a in da wani gumki na azurfa yake. na kama shi ina ta girgizawa hagu da dama, gaba da baya har na tizge shi.

Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce mani: Jefo shi qasa. Ni kuma na wurgo shi. Nan take ya far fashe shi kamar yadda qarau ke fashewa. Sannan na sauko. Daga nan sai muka sheqa ni da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam* muna rigyangyanto, muka vuya cikin gidaje, don tsoron kada wani mutum ya ganmu.

To, martaninmu a nan shi ne: muna tabbatar wa wannan barafilin da cewa, wannan hadisi, ko da ya inganta bai isa wani kayan gabas ba. Don babu

wani abu na falala a cikinsa da ta ke banci Imamai ko Ali *Raliyallahu Anhu*. Idan kuwa har baka yarda da haka ba. Ya za ka ce a kan Umamatu 'yar Abul-Asi xan Rabi'u wadda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* kan dora a kan kafadunsa yana kuma salla? Idan ya mike tsaye ya xauketa a hannu, idan kuma ya yi sujada ya ajiye ta?

Ya kuma za ka yi da sayyidina Hassan da kan zo ya xale wuyan Manzon Allah idan ya yi sujada. Har yakan ma ce: Ai xanane ya hau wuyana. Har kuma ya qara da sunbutar sa?

To, ka ga ixan dai har Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* zai xauki wani yaro ko wata yariya a kan kafadunsa, xaukar da ya yi wa Ali ba zata wajabta kasancewarsa wani gagarabadau ba. Domin kuwa ba shi ne kawai wanda Annabi ya taba yi wa hakan ba. Kuma shi xin ma da ya xauka a kafaxar ta sa, ya xaukeshi ne domin kasawar da ya fahimci Alin nada ita ta xaukar sa shi.

Ka ga kenan a haka, abin alfahari a nan na Manzon Allah ne, shida ya yi xaukar. Ka kuma san darajar wanda ya xauki Manzon Allah, ta fi ta wanda Manzon Allah ya xauka *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kamar yadda irin wannan darajar ta tabbata ga wani daga cikin Sahabbai, da ya xauki Manzon ranar yaqin Uhudu; wato Xalhatu xan Ubaidullahi da waninsa. Ina fatar ka gane banbancin. Ka ga wannan shi ya amfanar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* wancan kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ya amfanar da shi. kuma tabbataccen abu ne cewa wanda ya amfanar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da jinkinsa da dukiyarsa, ya fi wanda ya amfana da jiki da dukiyar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*

## 2.17 Siddiqai Basu Qidayuwa

Haka kuma xan Shi'ar ya yi amfani da wani hadisi na qarya, a qoqarinsa na tabbatar da imamancin Ali *Raliyallahu Anhu*. A inda yake cewa wai: An samo daga Abu Laila, wanda ya ce Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Siddiqai a duniya guda uku ne kawai. Na farko Habibu an-Najjar; muminin nan na Ali Yasin. Na biyu kuma Huzkilu; muminin nan na Ali firaun. Sai kuma na qarshensu kuma mafi xaukakarsu; wato Ali xan Abu Xalib.

To, martaninmu a nan shi ne: Wannan magana dai qarya ce aka qagawa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* Domin kuwa ta tabbata a cikin wani ingantaccen hadisi, Manzon Allah ya tabbatar da siddiqancin Abubakar *Raliyallahu Anhu*.

Haka kuma akwai wani ingantaccen hadisi, wanda aka samo daga xan Mas'ud *Raliyallahu Anhu* daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Wanda ya ce: ina horonku ku tsare gaskiya. Domin gaskiya ma shiriya ce zuwa ga da'a da nagarta. Ita kuwa nagarta ta farki ce na shiga Aljannah. Mutum ba zai gushe ba yana aiki da gaskiya tare da kirdadon ta, face ya karva sunan mai gaskiya, a wurin Allah. Ina kuma yi muku kashedi da karya. Domin karya na batarwa zuwa ga fajirci da kangara. Ita kuwa kan gara tafarki ce ta shiga wuta. Mutum

ba zai gusheba yana karya tare da kirdadonta, face ya karva sunan makaryaci a wurin Allah.

Ka ga wannan hadisin kawai ya ishi mai hankali ya gano cewa siddiqai ba su kidayuwa.

Wannan kenan. Wani dalili kuma da ke tabbatar da kasan cewar wannan hadisi qarya shi tabbtarwar da Allah Ta'ala ya yi cewa, maryamu 'yar Umrana "Siddiqa ce" tattare da kasancewarta mace.

Kuma a wani wurin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* na cewa: Girma da xaukakar mazaje da yawa sun kai. Mata kuwa sai kwara huxu kacal.

Ka ga kenan wannan hadisin ma na tabbatar da cewa yawan adadin siddiqai. Domin kuwa duk yadda aka yim girma aka sami xaukaka ba a kamar "siddiqi" balle a fi shi.

## 2.18 Ba Aliyu ne Farau ba

Daga cikin hadissan da wannan xan Shi'ar ke wasa da hankalin fararen fulla da shi, a qoqarinsa na samar wa tatsuniyar imamancin Ali *Raliyallahu Anhu* gindin zama a soron aqidar musulunci, akwai hadisin da aka samo daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* inda ya ce wa Ali *Raliyallahu Anhu* : kaza da kwai sune misali na da kai.

**Martani:**

Eh! Ko shakka babu wannan hadisi ingantacce ne. Domin .kuwa Buhari da Muslim duk sun kawo shi a cikin ingantattun littafansu, a cikin jerin gwanon hadisan Bara'u xan Azibu, wanda ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yan ke hukuncin zaman wata 'ya ta sayyidi Hamza a hannun gwaggon ta, a sakamakon jayayyar da Sayyidina Ali da Ja'afaru da Zaidu *Raliyallahu Anhu* suka yi a kan wanda zai rike ta. A qarshe ya lallashi Ali *Raliyallahu Anhu* da cewa : kar ka damu, kaza da kwai sune misali na da kai. ya juya ya ce wa Ja'afaru: kai ma kar ka damu, ganin ka gani na a hali da siffa. Ya kuma juya ya ce wa Zaidu: kai ma kada kada mu kai xan'uwa ne kuma abin so a wurimu.

Amma duk da haka muna son xan Shi'ar ya san cewa, wannan al'amari ba Aliyu *Raliyallahu Anhu* ne farau ba. Domin kuwa waxancan kalmomi: "Anta minni wa ana minka" Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fade su ga wasu daga cikin Sahabbansa a cikin siga daban-daban. Bari ka jita daga bakin da baya karya ko ana ruwan harshashi.

Ya zo a cikin littafin Buhari da Muslim daga Abu Musa Al-Ash'ari, wanda ya ce Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Idan ash'ariyawa suka rasa mazaje a wurin yaki, ko shekara tayi musu barkwanci, abicinsu ya qaranta, yunwa ta dafafi iyalansu a Madina; sai kowanen su ya kawo abin da ya mallaka a yamutse a raba dai-dai wa daida, kowa ya samu. Kaza da kwai su ne misali na da su. Kaji wannan ko?

Haka kuma manzon ya fadi irin wannan babbar magana ga Julaibibu, a wani hadisi da Muslim ya riwaito a cikin sahihinsa, daga Abu hurairata, wanda ya ce: mun kasance tare da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a wajen wani yaki wanda Allah ya bashi gagarumar nasara. A inda ya ce wa Sahabbansa wa-dawa muka rasa? Muka ce masa: wane da wane. Ya sake cewa: Wa-dawa muka rasa kuma bayan waxannan? Muka karva masa da cewa: sai kuma wane da wane, da kuma wane. Ya kuma sake cewa: sai wa kuma? Muka ce masa sukenan.

Sai ya ce: Amma ni ban ga Julaibibu ba. Ku gano mani shi. Sai muka fantsama cikin gawawwaki muna nema. Kwanfa, sai ga gawar sa tsakiyar wasu dakarun kafirai guda bakwai, waxanda ya kashe kafin su kashe shi. Nan take muka kyafato Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya iso wurin. Tsayawar sa ke da wuya sai ya kalli yana yin da Julaibibu yake ciki, sai ya ce: Ko shakka babu shi ya kashe bakwan nan kafin su kashe shi. Kaza da kwai sune misalin wannan (Julaibibu) da ni.

Sai Manzon Allah ya ciccive shi, shi kaxai qarshe aka haqa qabari aka saka shi.

Mai riwayar ya ce: Mai bayar da labarin bai ce mana an yi masa wanka ba.

Ka ga kenan a haka, ta tabbata ba Ali *Raliyallahu Anhu* ne farau a wannan kirari na manzo ba, balle ya qare kansa, domin kuwa gashi ya yi wa ash-ariyyawa da Julaibibu irin sa, waxanda ma ba halifofi ba.

To, idan kuwa har waxanda ba su kai darajar halifofin can uku ba, sukayi tarayya da Ali *Raliyallahu Anhu* a cikin wannan kuxa, babu dalilin da zai sa hakan ya zama dalilin kasancewarsa mafi xaukaka a kansu. Balle wajabcin imamancin sa.

## 2.19 Fixar Hadisin Amru Xan Maimun

Daga cikin waxancan hadissai da xan Shi'ar ke sojan gona dasu, akwai wani hadisi misali, na Amru xan Maimun, wanda wai ya ce, inji xan Shi'ar: Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* nada wasu darajoji guda goma waxanda babu mai su a Duniya: Shi ne wanda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce a kansa: Zan aika wani mutum, wanda har aBadar Allah ba zai kunyatar ba. Wanda kuma ke son Allah da manzon sa, su ma suke so sa. Wai jin hake ke da wuya sai sai Sahabbai suka yo ca, sukayi dako- dako. Kowa na jiran ace shi.

Sai Annabi wai ya kayar da baki ya ce: ina Aliyu xan Abu Xalib? Aka ce masa yana fama da ciyon ido, wanda ya tsayar da shi gidin dutse yana niqa. Sai wai ya ce: Bai kamata irin sa ace yana niqa ba.

Amru ya ce: Aka kira shi ya taho yana dundumi. Nan take Annabi ya yi masa addu'a idon ya warke. Ya kuma girgiza tutar yaqi har sau uku, sannan ya danqa masa. Kuma wai a wannan yaki ne ,ya taho da Safiyyatu 'yar Huyaiyu.

Bayan haka ne kuma wai, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya aiki Abubakar *Raliyallahu Anhu* da suratul- Tauba. Bai samu isar da ita ba, kuma Manzon ya tura Ali *Raliyallahu Anhu* ya karve ta daga hannunsa. Ya kuma kafa hujja da cewa: bai kamata dama wani ya isar da irin wannan sako daga gare ni ba. Sai wanda ni da shi kamar kaza da kwai ne. Daraja ta farko kenan.

Ta biyun kuma. Watarana tarayyar 'ya-yan Ammin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na zaune, a cikin ma har da Aliyun. Sai Annabi ya dube su ya ce: waye daga cikin ku zai jibince ni duniya da lahira? Wai sai kawai suka dube shi biris. Sai Aliyu ya karva masa da cewa: Ni zan jibince ka duniya da lahira. Sai Annabi yaqi kula shi. Daga nan kuma sai ya bisu xaya bayan xaya, yana yi musu waccan tambaya. Su kuma kamar farko, suna yi masa kallon haxarin kaji. Shi kuma Ali bai daddara ba . ya sake karva masa da irin waccan amsa ta farko. Ganin haka sai wai Annabi ya kula shi da cewa: kai ne majibincin al'amarina duniya da lahira.

Daraja ta uku kuwa: Aliyu ne wanda ya rufa wa sayyida khadija baya wajen mika wuya ga addinin Allah.

Ta huxu kuma : Aliyu ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya lulluvawa mayafin sa, tare da Fatima da Hassan da Husaini. Ya kuma ce: *Allah na nufi ne ya tafiyar da qazanta kawai daga gare ku, ya ku mutanen babban gida, ya kuma tsarkake ku tsarkakewa (33:33).*

Daraja ta biyar kuma: Aliyun ne wanda ya saxaukantar da rayuwarsa. Ta hanyar saka tufafin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* tare da kwantawa a kan shimfixarsa. Ga kuma mushrikai na ruwan wutar duwatsu a kansa.

Ta shida kuma: Aliyu ya nemi iznin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a kan ya bishi zuwa yaqin Tabuka tare da rundunarsa da zai fita da ita. Manzon Allah ya ce masa: A'a. Jin haka sai Aliyu ya fashe da kuka. Sai wai Annabi ya ce masa: Ba zaka so matsayinka a wurina ya zamo kamar matsayin Haruna a wurin Musa ba? Duk da yake kai ba Annabi ba ne. Ba ta yiwuwa in tafi face na bar ka a matsayin wakilina.

Daraja ta bakwai kuma: wai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya ce ma Ali: "Kai ne madadina ga kowane mumini bayan na bar duniya"..

Ta takwas kuma: Manzon ya ce babu wata qofa ta masallaci da ke buxe sai ta Ali.

Daraja ta tara kuma: Babu lokacin da masallaci baya shiguwa ga Ali *Raliyallahu Anhu* ko yana da janaba.

Daraja ta goma kuma: Itace cewar da manzon Alla *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi a kan Ali: "Duk wanda ya yarda da ni a matsayin majivinci, to, ya riqi Aliyu a matsayin haka".

An kuma samo daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* marfu'an. Cewa ya aika Abubakar *Raliyallahu Anhu* da surar Bara'atu zuwa Makka. Bayan kwana uku da haka kuma sai ya tashi Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce masa ya yi gaggawa ya riski Abubakar xin, ya karvi sakon ya kai, shi kuma ya dawo.

Dawowar Abubakar ke da wuya, sai ya iske Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya na kuka. Ya ce: Ya Manzon Allah, Allah yasa ba wani laifi na yi ba? Manzon ya ce: ko alama. An dai umarce ni ne da kada in aika wani da wannan sakon sai jini na. Bisa ga na riga na baka shi.
Wannan duk inji Xan Shi'ar.

To, ga martaninmu: Na farko dai wannan hadisi ba masnadi ba ne, mursali ne. Wannan kuwa ko da ya tabbata daga Amru xan Maimun xin.

Bayan wanna kuma, akwai maganganmu da dama a cikin sa, waxanda tabbas qarya ce aka yi wa ma'aiki *Sallallahu Alaihi Wasallama* kamar cewar da a kayi ya cewa Ali *Raliyallahu Anhu* Ba ka fatar matsayinka a wurina ya zama kamar matsayin Haruna a wurin Musa? Duk da yake kai ba Annabi ba ne. Ba ya kamata in tafi face na barka a matsayin wakilina.

Ka ga wanna magana, qarya ce shararra. Domin kuwa akwai tafiye-tafiye da dama da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi, ya kuma bar wani,wanda ba Ali ba, matsayin wakilinsa a Madina. Kamar tafiyar da ya yi don Umratul Hudaibiyya, da yaqin Haibara, da yaqin Fathu, da na Hunainu da Da'ifa, da Hajjin ban kwana, da yaqin Badar.

Duk waxannan tafiye-tafiyen da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi, duk ya yi sune tare da shi Alin *Raliyallahu Anhu*. Wani Sahabi na wakiltarsa a Madina. To, in ji?!

Kuma wannan magana da nake gaya maka, tabbata ce kuma sananna. Don bana kwai ni da xai sai da zaqara. Ingantattun riwayoyi waxanda malamai masana hadisi suka haxu a kansu, sun tabbatar da cewa, mafi yawan gumurzun da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi da kafirai, ya yi shi ne tare da Alin, ko da Allah bai kaddari aka gwabza a wurin ba.

To, ka ga a kan haka, idan muka tafi akan fassarar xan Shi'ar. Wadda ke qoqarin nuna cewa, duk wanda manzo ya bari ya wakilce shi a Madina, don wata tafiya, to, ya zama mafi xaukakar Sahabbai a lokacin. Kenan fara shin alkaxarin Ali ya faxi warwas, a waxancan lokuta da manzon ya wakiltar da wani a Madinar bashi ba. Musamman idan aka yi la'akari da waqilcin da aka bar wa Sahabban a lokutan na kula da mazaje ne kuma Muminai. Shi kuwa waqilcin da manzo ya bar Ali ya yi a lokacin yaqin Tabuka, na kula ne da mata da kananan yara da ashararan munafikan musulmin nan guda uku. Waxanda suka yi raggon kaya da gangan a lokacin yaqin, suka darewa ma'aiki.

Kuma ma wannan lokaci ne na aminci ga birnin na Madina, ba a fargabar faruwar wani abu na illa gareshi. Ta yarda har wanda aka wakilta xin zai yi amfani da qarfin tuwo balle. Savanin sauran lokutan, da a mafi yawansu magajin garin na Madina keda bukatar yin jan ido da murza gashin baki.

Ita kuwa ce war da xan Shi'ar ya yi wai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Babu wata kofa ta masallaci da ke buxe sai ta Ali. Magana ce da 'yan Shi'ah suka qaga don su daidai ta tsawon darajar Ali da ta Abubakar *Raliyallahu Anhu*. Domin kuwa abin da ya tabbata ya kuma inganta a wannan babi, Shi ne abin da ya zo daga Abu Sa'id, daga Annabi *Sallallahu Alaihi*

*Wasallama* cewa, ya ce a lokacin da yake jinyar ajali: Babu wani mutum da dukiyar sa da abokantakarsa suka amfane ni kamar Abubakar. Da na kasance mai riqon wani a matsayin badaxayi koma bayan Ubangijina, da na riqi Abubakar. Amma dai ku sani bani da masoyi kuma xan'uwa na musulunci kamar sa. Babu wata qofa da haske ke shigowa tata a wannan masallaci da ta rage face ta Abubakar.

Xan Abbas kuma ya riwaito hadisin a cikin Buhari da Muslim.

Haka abin yake a cikin cewar da xan Shi'ar ya yi Annabi ya ce wa Ali: kai ne majivincin kowa ne mumini bayan na qaura. Magana ce qagagga bisa haxuwar malaman hadisi. Domin kuwa lafazin da ya inganta na wannan magana bai kevanci imamai ko Ali ba *Raliyallahu Anhu*; wani wanda ba shi ba ya yi tarayya da shi a cikin haka. Kamar kasancewar sa masoyin Allah da manzon sa kuma mai sonsu. Ko wakila shi da manzo ya tava yi ya tsare birnin Madina. Ko lalla shin sa da ya yi da yi masa bushara da zama kamar Haruna a wurin Musa, shi kuma a wurinsa. Ko kasancewar sa majibincin kowane mumini matuqar ya yarda da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama,* a matsayin majibinci.

Duk waxannan wasu mukamai ne da babu muminin da bai cancanci riqawa ba.

Ko kuma surar bara'a, da manzon ya ce: ba ta kamata wani ya isar da ita saqo ba, wanda ba jinin sa ba, wato Bani Hashim. Ka ga ai wannan magana ta qundume gaba xayan Hashimawa. Tun da ba Aliyu ne kawai Bahashime ba.

Kuma abu ne tabbatacce a tarihin Larabawa cewa, a al'adance ba wanda ke da isar walwale wani arqawari sai xaya daga cikin 'ya'yan qabilar wanda aka qulla arkawarin da shi a matsayin shugaba.

### 2.20 Mafi Yawan Hadisansu na Qarya ne

Babu wani hadisi da wannan xan Shi'ar zai kafa hujja da shi a kan fifikon Ali *Raliyallahu Anhu,* a kan sauran Sahabbai. Musamman guda ukun nan; halifofi kafisa, face ka taras da hadisin ya xauki matsayin xaya daga cikin matsayai biyu:

Wato ko dai ya kasance qarya ce tun daga maxigarsa har babban yatsar kafansa. Ko kuwa:

Ya kasance ingantacce, amma ya kar kata akalarsa. Ta hanyar yi masa qare - qare ko wani abu mai kama da haka.

Ga guda goma daga cikin waxanda gaba xayan su qarya ne:

Xan Shi'ar ya ce: Daga cikin hadissai kuma akwai wanda Akhxabu ya riwaito, wanda ya ce wai Annabi *Sallalahu Alaihi Wasallama* ya ce: ya kai Ali! da wani mutum zai bautawa Allah *Subhanahu WaTa'ala* tsawon shekarun da Annabi Nuhu ya yi a cikin mutanensa yana kira , ya kuma kasance ya mallaki zinarin da ya yi tulin dutsen Uhudu, ya kuma ciyar da da shi kaf, a kan tafarkin Allah , a kuma tsawaita rayuwar sa yaje aikin hajji sau dubu a qasa, a kuma kashe shi a ta qarshe tsakanin safa da marwa, bai ji bai gani ba. To ba zai ji ko qanshin aljanna ba, balle ya shige ta. Matukar bai rike ka abin jivinta ba.

Na xaya kenan.

Na biyu kuwa: Wai wani mutum ya tambayi Salmanu cewa: Me ya sa naga ka na tsananin son Ali? sai wai ya karva masa da cewa: Na ji manzon Allah ne *Sallalahu Alaihi Wasallama* na cewa: Duk wanda yaso Ali, haqiqa ya so ni. Duk wanda kuma yaqi shi haqiqa ya qini.

Hadisi na ukku kuma, wai shi ne: abin da aka riwaito daga Anas wanda ya ce: Manzon Allah *sallahu alaihi wa sallam* ya ce wai: Allah ya halicci mala'iki dubu saba'in daga hasken fuskar Ali *Raliyallahu Anhu* waxanda aikinsu kawai yi wa Ali istigfari da masoyansa, har Allah ya naxe qasa.

Na huxu kuma wai an samo daga xan Umaru, wanda ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* wai ya ce: Allah na karvar sallar da azumi da tsayuwar daren duk wanda ke son Ali, ya kuma jabi du'a'insa. Ku saurara! Allah zai bayar da birane a cikin aljanna ga duk wanda ke son Ali, gwar gwadon yawan digaggen zufan da jikinsa ya zuba a duniya. Ku saurara! Allah zai amintar da duk wanda ke son iyalan gidan Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* daga tashin hankalin Hisabi da mizani da siradi. Ku saurara! Ni da sauran Annabawa za mu zama maga'isa ga duk wanda ya mutu a kan son iyalan Muhammadu, a gixan aljanna. Ku saurara! Duk wanda ke kin iyalan Muhammadu, a gidan aljanna. Ku saurara! Duk wanda ke qin iyalan Muhammadu zai tashi ranar qiyama, a goshinsa an rubuta: "Ya yanke qauna daga rahamar Allah".

Hadisi na biyar: Wai an karvo daga Abdullahi xan mas'udu, wanda ya ce: na ji Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na cewa: wai duk wanda ke jin ya yi imani da ni, da abin da nazo da shi. alhali baya son Ali to yana yaudarar kansa ne kawai, shi ba mai imani ne ba. Maqaryaci ne.

Na shida kuma wai shi ne, wanda aka samo daga Abu Barzata, wanda ya ce: watarana muna zaune sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Na rantse da wanda raina yake hannun sa. Babu wani bawa da zai xaga kafarsa ranar qiyama face Allah Tabaraka wa Ta'ala ya tambaye shi a kan wasu abubuwa guda wato

: Shekarun sa da yadda ya qarar dasu. Jikinsa da yadda ya miqe shi. Dukiyarsa, yadda ya same ta yadda ya kashe ta. Da kuma son da ke tsakaninsa damu (mutanen babban gida) wai sai Umar ya ce: Ya za'a gane mutum na son ku bayan kun qaura? Sai wai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya xora hannunsa a kan Ali xan Abu Xalib, wanda alokacin yake gefen sa. Ya kuma ce: Soyayyar mutum gareni bayan na qaura ita ce ya so wannan.

Hadisi na Bakwai kuma wai: shi ne wanda aka samo daga Abdullahi xan Umar, wanda ya ce wai: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce; a lokacin da aka tambaye shi cewa: da wane yare ne Ubangijinka ya yi magana da kai daren mi'iraji? Sai ya karva da cewa : ya yi magana dani ne da yaren Ali. Sai kuma ya yi mini ilhami na samu ikon ce wa: Ya Ubangiji shin kaine ke magana da ni ko Ali? Sai kuma yayi mini irhami da sanin ikon cewa: ya Ubangiji shin kai ne ke magana da ni ko Ali? Sai kuma ya karva mani da cewa:

Ya kai Muhammadu! Ka sani babu wani abu da ke zama da ni. Ba ni miisaltuwa da mutane ko siffan tuwa da wasu abubuwa. Na halicce ka daga haske na, na kuma halicci Aliyu daga haskeka. Amma da na leqa kariyar xakin birnin zuciyar ka, naga babu wanda kake mutuwar so kamar Ali, sai na zavi inyi maka magana da yaren sa don ka sami natsuwa.

Na takwas kuma shi ne wai aka samo daga xan Abbas, wanda ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Da duk gandunan duniya za su zama alqaluma, gulabenta su zama ruwan tawada, aljannu su zama masu kididdiga, mutane su zama marubuta, ba za su iya lissafe darajojin Aliyu xan Abu Xalib ba.

Ga yadda warwarar bakin hadisan zata kasance idan muka koma ta kan isnadinsa:

wai cewa xan Abbas ya yi: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Allah Ta'ala, haqiqa ya tanadi lada wadda ba ta iyakantuwa saboda yawanta, a kan abin da ya shafi darajojin Ali.

Daga nan wai sai Manzo ya shiga lissafi da rattafawa: Duk wanda ya ambaci wata daraja daga cikin darajojin Ali, yana mai kudurce imani da ita. Allah zai gafarta masa gaba xayan zunubansa; na farko dana qarshe. Duk kuma wanda ya rubuta darajarsa xaya a kan takarda. Mala'iku ba za su gushe suna yi masa istigfari ba, matuqar rubutun nan na wanje. Duk kuma wanda ya saurari ambaton darajarsa xaya, Allah zai gafarta masa gaba xayan zunuban daya xauka ta kunne. Duk kuma wanda ya kalli wata daraja tasa dake rubuce, Allah zai gafarta masa gaba xayan zunuban da ya xauka ta ido.

Sannan kuma wai ma'aiki ya ce: kallon fuskar Sarkin Musulmi Ali *Raliyallahu Anhu* da ambaton sa duk ibada ne. Kuma wai Allah ba ya karvar imanin bawan da bai riki Aliyu majibinci ya kuma yi wa magabansa bara'a ba.

Na tara kuma wai shi ne wanda aka samo daga Hakimu xan Huzama, daga mahaifinsa shi kuma daga nasa mahaifin wanda ya ce wai: Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Wallahi fito na fiton da Ali ya yi da Amru xan Abdu wuddin ranar yaqin kadarko(khandak) ta fi duk aikin da al'uma ta zata yi girma a wurin Allah, har ranar qiyama.

Hadisi na goma kuma wai shi ne: wanda aka samo daga Sa'ad xan Abi Wakkas, wanda ya ce: Mu'awiyah xan Abu Sufyanu ya umarce ni watarana da in zagi Ali *Raliyallahu Anhu* sai na qi. Sai ya tambayeni dalili, sai na ce masa: Saboda naji wasu Abubuwa guda uku na falala da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya faxa a kansa. Waxanda da zan sami xaya daga cikinsu. Da na fi wanda kakarsa ta yanke saka damawa.

Na farko naji watarana Aliyu na yi wa Annabi qorafin barinsa da ya yi gida tare da qasan shi; wato mata da qananan yara. Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce masa: Ba ka fatar matsayinka a wurina ya zama kamar matsayin Haruna a wurin Musa? Duk da yake dai babu wani Annabi baya na.

Na biyu kuma. Na ji manzon, a ranar yaqin Haibara, yana cewa: yau zan xanka tutarmu ta yaqi hannun wani jarumi. Wanda ke son Allah da manzon sa, suke kuma son sa. Sai kowanen mu ya fara zura wuya. Sai manzon ya ce: kai! Ku kiran man Aliyu. Sai gashi ya taho da ciyon ido. Nan take manzon ya yi masa tohi a idon ya kuma xanka masa tutar. Allah kuwa ya yarda akayi nasara a yaqin albarkacinsa. Kuma ya saukar da ayar da ke cewa: To ka ce: " ku zo mu kira yi 'yayanmu da 'ya'yanku....(3:61) A inda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya gayyato Ali da Fatima da Hassan da Husaini *Raliyallahu Anhu* ya kuma ce: Waxannan sune iyali na.

**Martani:** Eh! Gaskiya ne Akhdabu Khawarazumi ya yi wallafa a cikin abin da ya shafi darajojin Ali *Raliyallahu Anhu* sai dai masana hadisi sun dade da fahimtar cewa mafi yawan hadisan da ya riwaito a wannan babi ka gaggu ne. Wanda hakan ke tabbatar da cewa shi ba malamin hadisi ba ne da dai, balle har a iya riqon shi Hujja ko wata madogara.

Wani kuma abin da ke tabbatar da rashin cancantarsa da taka wanna rawa da yake ta qoqarin takawa a fagen hadisi, shi ne cewar da ya yi babu wani hadisi da zai riwaito face wanda ya inganta a idon waxannan mazaje. Wanda kuma suka riwaito a cikin nagartattun zantuka da littafansu. Sai kuma ga shi hakan ta faskara. Domin kuwa babu wani daga cikin malaman da ya riwaito wani hadisi daga cikin waxannan hadisai, a cikin litafai a cikin dogaro, balle ya inganta shi . hasali ma kansu haxuwa ya yi a kan kasancewar hadisan qarya.

Da haka ne kuma gaba xayan waxancan hadisai tara da muka ambata suka tabbata qarya; har zuwa kar shensu.

Amma hadisi na goma, wanda Mu'awiyah ya umarci da Sa'ad da la'antar Ali *Raliyallahu Anhu* shi kuwa yaqi. Da muhawarar da ta gudana tsakanin su har ya kafa masa dalilai a kan haka. Hadisi ne .ingantacce. domin imamu Muslimu ya riwaito shi a cikin ingantaccen littafinsa. Sai dai darajojin da aka ambata na Ali *Raliyallahu Anhu* a cikinsa, ba su kevanta da shi ba.

Xauki misalin daraja ta farko: wato barinsa a birnin Madina da manzo ya yi a matsayin waqili, da abin da ya gudana tsakaninsu qari da busharar da manzon ya yi masa. Ka ga ai ba Ali *Raliyallahu Anhu* ne kawai wanda ya tava waqiltar birnin na Madina ba.

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya sha barin wasu su waqilce shi a Madina, waqilci kuma irin wanda yafi wanda aka bar Ali *Raliyallahu Anhu* yi xaukaka; domin shi mata da qananan yara aka barshi tsaro. A kan haka ma ne ya koka wa Annabi, har waccan busharar ta biyo baya.

Ga al'ada babu wani yaki da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* zai fita, face ya bar wasu dakarru muminai daga cikin Muhajiruna da Ansaru a Madina, ya kuma na xawa garin magaji kafin ya dawo. A lokacin da zai tafi yaqin Tabuka ne kawai ya tabbata wa Sahabbai cewa yau kan ba a xauke wa kowa fita ba. Sai masu kunnuwan qashi da mata da qananan yara da masu wasu lalurori. To kaji dalilin da ya sa Ali *Raliyallahu Anhu* ya kyamaci wannan waqilci, har ya koka wa ma'aiki *Sallallahu Alaihi Wasallama* A kan

haka ne Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi masa bayani da cewa: Bai wakilta shi a wannan karo don ya tozarta shi, ko qasqan tashi ba. A'a ya yi haka ne, saboda gamsuwa da irin amanar da yake da ita. Kamar yadda Musa ya kiltar da Haruna saboda yarda da amanar sa. Duk da yake wanda Musa ya wakilta xin Annabi ne. Amma ni babu wani Annabi da zai zo baya na.

Amma idan ka dubi wannan salon na kamantawa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi amfani da shi tsakanin shi kansa da Musa zuwa ga Haruna da Ali, abu ne da ya ta kaita akan "waqilci" kawai. Amma ba gaba xayan mas'aloli ba.

Eh! Ba gaba xaya ba mana. Tunda ai ka ga gaba xayan Bani Isra'ila ne Haruna ya tsare a matsayin waqilin Musa *Alaihis Salamu*. A ya yin da shi kuwa Ali *Raliyallahu Anhu* wasu 'yan tsiraru ne daga cikin musulmi ya waqilci Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* tsarewa. Adai - dain lokacin da ya fita tare da mafi yawansu. Ka gani ko.

Wannan kenan. Wani kuma abin da ke qara tabbatar da rashin kasancewar wannan. kamanta wani abin godoro ko alfahri ga Ali *Raliyallahu Anhu* da 'yan Shi'ah, shi ne irin yadda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kamanta Abubakar *Raliyallahu Anhu* da Annabi Ibrahim da Annabi Isa *Alaihis Salamu* Umar *Raliyallahu Anhu* kuma da Annabi Nuhu da Annabi Musa *Alaihis Salamu* ka kuma san darajar waxannan Annabawa huxu tafi ta Haruna nesa ba kusa ba. Kuma kasancewa ma'aiki ya kamanta Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* da biyu daga cikin Annabawa kowannen su, ta sa salon kamanta war nasu zama mafi xaukakar daraja a kan na Ali *Raliyallahu Anhu* a matsayinsa na wanda aka kaman ta da mutum (Annabi) xaya kacal. Wannan kuma tattare da kasancewar Alin ba farau ba daga cikin Sahabbai, a cikin wannan aiki da muqami na "magaji Gari" mai taqaitaccen wa'adi, balle ya zama qarau.

## 2.21 Yamutsa Hazon Hadisin Ranar Shura

Idan baka manta ba. A baya kaxan na gaya maka cewa xan Shi'ar nan yana da hanyoyi biyu, da ya kan bi don tabbatar da fifikon Ali *Raliyallahu Anhu* a kan Sahabbai, wato hanyar kawo hadissan qarya ko yamutsa hazon wasu ingantattu tare da karkata akalar su.

To anan zan kawo maka wani hadisi da ya inganta a cikin Buhari da Muslimu, a kan yadda Usmanu ya zama halifa, ka ga irin yadda xan Shi'ar ya yamutsa hazon sa. Amma kafin haka sai ka fara da gurbataccen, don a qarshe ka she she baki da nagartacce.

Xan Shi'ar ya ce: An samo daga Amiru xan wasilata, wanda wai ya ce: Na kasance tare da Ali *Raliyallahu Anhu* ranar shura. Sai na ji yana cewa Sahabbai: zan kafa muku hujja a kan fifikona, da wasu abubuwa da babu wani daga cikin ku; Xan Shi'a ko Bobawa da ke iya karkare shi. Sannan wai ya ci gaba da cewa:

Ya jama'a tsakanin ku da Allah, ko akwai wani daga cikinku, da ya kaxaita Allah Ta'ala kafin na?

Suka wai karva masa da cewa: wallahi babu.

Ya ce: tsakanin ku da Allah ko akwai wani daga cikinku, da ke da xan'uwa irin Ja'afaru, wanda ke shawagi a cikin Aljanna kamar tsuntsu, tare da Mala'iku in ba ni ba?

Suka ce: wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah ko akwai wani daga cikinku da ke da Ammi kamar Ammi na Hamza; zakin Allah da manzonsa kuma limamin shahidai.

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakaninku da Allah ko akwai wani daga cikin ku da ke da mata kamar matata Fatimatu; 'yar Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* shugaban matan aljanna?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah ko akwai wani daga cikinku, da ke da 'ya'ya biyu kamar nawa; Hassan da Husaini, shugabannin samarin aljanna?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah ko akwai wani daga cikinku daya tava ganawa da Manzon Allah *sallahu alaihi wa sallam* sau goma, kowace da manzon sadaka kafinta kamar yadda nayi?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah, ko akwai wani daga cikinku, da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce wa irin yadda ya ce mani: Duk wanda ya yarda dani abin jibinta to ya riqi Ali abin jivinta. Ya Allah ka jivinci al'amarin duk wanda ya jivinci Ali. Ka kuma qi duk wanda ya qishi. Wanda ya ji ya sanar da wanda bai ji ba?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah ko akwai wanda addu'ar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* wadda ya ce: Ya Ubangiji ka koxo mani mafi soyuwar halitta a wurin ka, mu yi kalaci da wannan tsuntsu tare da shi. Ta faxa kansa; ya faxo suka ci tare in ba ni ba?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah ko akwai wani daga cikinku, wanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya shelartawa duniyar Sahabbai cewa: yau zan danqa tutarmu ta yaqi a hannun wani mutum da ke son Allah da manzonsa suke kuma sonsa. Wanda ba zai dawo ba sai da guxar nasara. Ashe ni yake nufi. Hakan kuma ta tabbata. Bayan wasu sun kutsa fagen famar suka dawo suna tavavvi. Ko akwai shi?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakaninku da Allah ko akwai wani daga cikinku, da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce wa bani waki'ata: ku bari. Ko wallahi in aiko muku da aradu; wani dakare daga cikin dakarruna. Wanda ni da shi ba

banbanci; yi masa biyayya kamar yi mani ne. Kuma sava masa kamar sava mani ne; wanda zai shiga tsakanin ku da kaifin takobi. qarshe ya aika ni?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah, ko akwai wani daga cikinku, da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce a kansa: Duk wanda ya ce yana so na ba ya son wannan (Ali) makaryaci ne. In ba ni ba?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah, ko akwai wani daga cikinku, da mala'iku dubu uku suka yi wa sallama a lokaci xaya, wato; Jibrilu da Mika'ilu da Israfilu. A lokacin da suka kawowa Manzon Allah ruwa daga wata rijiya. In ba ni ba?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah, ko akwai wani daga cikinku, da aka gwarzanta daga sama'u da cewa: Yau duk wani takobi in ba "zul-kifaru" ba labari ne. [hadari mai kashe qarfi rana, goga mai kashe qarfi molo] In ba niba?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah, waye daga cikinku, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce zai yaqi Baqaqe da jajaye da kore-koren musulmi a kan umarnin sa, in ba ni ba?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakani ku da Allah ko waye daga cikinku, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce zai yi yaqi don tabbatar da ingantattar fassarar Alqur'ani. Bayan shi ya yi yaqi don samar masa gindin zama, in ba ni ba?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah, waye daga cikin ku Allah *Subhanahu WaTa'ala* ya dawo wa da rana bayan ta faxi don ya sallaci sallar la'asar cikin lokacinta, kamar yada aka yi mani?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah ko akwai wani daga cikinku, da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya umarta da karvar sakon surara bara'atu daga hannun Abubakar. Har da Abubakar xin ya tambaye shi cewa: ko an saukar da wani abu ne a kaina? Manzon ya tabbatar masa da cewa: ko alama. Na dai ga babu wanda ya kamata ya isar da irin wannan saqon sai Ali kawai, kamar yadda ya umarce ni?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah, waye daga cikin ku, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce wa: Babu mai son ka sai mumini, babu kuma mai qinka sai munafuki. In ba ni ba?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah, ashe ba kune Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi umarni da'a rufe qofofinku, a buxe tawa ba. Har kuka yi qorafi a kan haka. Ya tabbata maku cewa; ba shi ne yake da sha'awa a kan haka ba. umurnin Allah ne? Ko kun manta?

Suka ce: Wallahi bamu manta ba.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah, Ashe ba kune kuka kalubalanci Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba, a kan ya xauki lokaci yana ganawa da ni, ranar yaqin Xa'ifa; savanin irin yadda yake ganawa da mutaane. A qarshe ya tabbatar maku da cewa, Allah ne ke ganawa da ni a lokacin ba ni ba. Ko kun manta?

Suka ce: Wallahi bamu manta ba.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah, kun manta da cewar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi: Ali na tare da gaskiya; gaskiya kuma na tare da shi, duk in da ya yi tana biye da shi?

Suka ce: Wallahi bamu manta ba.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah kun manta da cewar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi: Haqiqa na bar muku waxansu abubuwa guda biyu masu nauyi; Littafen Allah da mutanen gidana. Ba za ku vata ba matukar kuna rike dasu. Kuma su, ba za su saki hannun juna ba. Ko sun isa gabar kogina?

Suka ce: Wallahi bamu manta ba.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah waye daga cikinku, ya saxaukar da rayuwarsa, saboda kariya ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* daga mushrikai. Ta hanyar kwanciya a kan shimfixarsa *Sallallahu Alaihi Wasallama* kamar yadda na yi?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah, waye daga cikinku, ya yi gum da Umar xan Abdul-Widdi a lokacin da yakewa musulmi kuce. Ashe bani ne nace masa cas ba?

Suka ce: Wallahi kai ne.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah, ko akwai wani da cikinku wanda Allah *Subhanahu WaTa'ala* ya saukarwa ayar tsarkakewa a kansa, wadda ke cewa: kuma Allah na nufin ya tafiyar da qazanta kawai daga gare ku, ya kuma tsarkake ku tsarkakewa (33:33) kamar yadda ya saukar a kai na?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: Tsakanin ku da Allah ko akwai wani daga cikinku, wanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce wa: Kai ne shugaban sahun muminai, kamar yadda ya ce mani?

Suka ce: Wallahi babu.

Ya ce: tsakanin ku da Allah ko akwai wani daga cikinku, da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tava cewa: Ban tava roqon Allah wani abu ba face na roqa maka kwatankwacin sa; kamar yadda ya ce mani?

Suka ce: Wallahi babu.

Akwai kuma daga cikin irin waxannan hadisai na qarya da xan Shi'ar ke dogaro dasu, hadisin da wai aka samo daga Abu Amru Azzahidu, daga kuma xan Abbas, wanda wai ya ce: Ali *Raliyallahu Anhu* nada wasu darajoji guda huxu da babu wanda ke dasu daga cikin mutane; Shi ne mutum na farko daga cikin Larabawa da Bobayi, wanda ya yi sallah tare da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne kuwa wanda tutarsa bata tava faxuwa a kowane yaqi. Shi ne

kuma gagarraren damon yaqin hunainu. Shi ne kuma wanda ya yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* wanka, ya kuma saka shi cikin kabarinsa.

Ka ji kai! Allah da iko shi ke.

Haka kuma xan Shi'ar ya ce wai, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Ni da Jibrilu mun taras da wasu mutane, a daren da akayi mi'iraji dani, ana shatar naman jikinsu. Sai na tambayi Jibrilu ko suwaye? Ya ce sune waxanda ke cin naman mutane ta hanyar giba. Can kuma muka taras da wasu an shashshavesu kamar daudawa. Na tambayi Jibrilu kosu waye? Ya ce kafirai ne. Daga nan sai muka sake hanya.

Isarmu sama ta huxu keda wuya sai ga Ali na sallah. Sai na cewa Jibrilu: Ah! Kai ji Ali har ya riga mu isowa. Sai ya ce mani: wannan ba Ali ne ba. Na ce: To waye? Sai ya ce: wani mala'ika ne Allah *Subhanahu WaTa'ala* ya halitta a cikinsurar Alin. Wai dalili kuwa mala'ikun da ke hidma faxar Allah ne, da shugabannin su, suka sami kansu cikin matsanancin shauqi da begen Ali, a sakamakon yawan jin darajojinsa da suke ji. Musamman cewar da wai Annabi Allah*Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi: Matsayin Ali a wurina kamar matsayin Haruna ne a wurin Musa. Duk da yake babu wani Annabi bayana.

Saboda haka a duk lokacin da shauqin Ali ya motsowa mala'kun sai suzo su kewayi wannan mala'ika mai siffar Ali; an huta dasu kenan.

Kai ka ji magana kamar irinta mata da qananan yara.

Kuma wai xan Abbas ya ce: watarana Almusxafa *Sallallahu Alaihi Wasallama* na jin nishaxi. Sai kawai muka ji ya ce: Ni bajini ne, xan bajina kuma xan'uwar bajini.

Xan Abbas xin wai sai ya ce: Annabi na nufin: Shi bajinin Larabawa xan bajinin Annabawa Ibrahim. Saboda cewar da Allah Ta'ala yayi: Munji wani saurayi (bajini) yana ambatar su. Anace masa Ibrahim (21:60) kuma shi ne xan'uwan bajinin sahabbi Ali.

Kuma wai wannan magana da kirari da koxa da manzo yayi, ita ce fassarar guxar da Jibrilu ya tashi sama'u yana yi a ranar yaqin Badar yana cewa: Duk takobi yau idan ba "zul-qifari" neba labari ne, kuma duk dakare (bajini) in ba Aliyu ne ba labari ne.

Wai kuma an samo daga xan Abbas xin dai, wanda ya ce: Na ga Abu Zarrin, watarana riqe da labulayyen Ka'aba yana cewa: Wanda ya sanni cikinku ya sanni. Wanda kuma bai sanni ba, to ni ne Abu Zarri. Kuma ku ji ta daga bakina: Da za kuyi azumi ku rame kamar tsarkiya, kuyi ta sallah har ku yi doro kamar baka. Hakan ba zata amfane ku da komai ba. Matuqar baku son Ali.

Tammat! Magana ta qare. Kai ka ji. Wasu dai Allah ya hore masu iya qarya. Kai kasan wannan ko Musailamatul-kazzabu albarka ko?!

To, martanin mu kan zaqaqarun malamai a fagen ilimin hadisi ya haxu a kan cewa gaba xayan abin da xan Shi'ar ya ce an riwaito daga Amru xan wasilatu dan gane da wannan rana ta shura da abin da ya faru a cikinta qarya

ne; babu wani abu da Ali *Raliyallahu Anhu* ya fada mai ko kama da wannan a wannan rana.

Iyakar abin da ya tabbata a wannan rana shi ne, Abdurrahman xan Aufi ya ce wa Ali *Raliyallahu Anhu* : ina fatar da Allah zaisa in zaveka a matsayin halifa da zaka yi adalci? Ali ya ce: ko shakka babu, da yardar Allah zan yi iyakar qoqarina. Abdurrahman ya kuma sake ce masa: To da Allah zai nufi inyi mubaya'a ga Usmanu a matsayin shugaba fa, za ka yi masa xa'a? Ali *Raliyallahu Anhu* ya sake karvawa da cewa: Tabbas zan yi.

Kuma irin wannan muhawara ce ta gudana tsakanin Abdur-Rahman xin da Usmanu a kan Ali *Raliyallahu Anhu*.

A qarshe sai Abdur-Rahman ya fahimci cewa matsayin su duka xaya ne; wato babu wanda keda nufin qin yin adalci da zai zama halifa. Ko yaqi yarda da hukuncin Allah, da xan'uwansa zai zama. Saboda haka, ba abin da ya rage wa shi illa shawara. Sai ya kwashe kwana uku ya na gudanarda tattaunawa da dai-dakin musulmi a kan wannan mas'ala.

Bari ka ji yadda Buhari da Muslim suka kawo wannan waqi'a a cikin ingantattun littafansu.

Buhari ya ce: An samo daga Amiru da Maimun, a kan abin da ya faru na kashe Umar xan Khaxxabi. Ya ce: qare hidimar kawar da Umar keda wuya sai waxannan manyan Sahabbai suka haxu. Sai Abdur-Rahman ya ce: To, ku zavi mutum uku daga cikinku ku fice masu nauyin jagorancin nan. Nan take zubairu ya ce: Ni na jaye na zavi Ali. Xalhatu kuma ya ce: Ni kuma na jaye na zavi Usmanu. Shi kuwa Sa'ad ya ce: Ni kuma na jaye na zaveka kai Abdur-Rahman.

Sai kuma Abdur-Rahman ya sake cewa: To, waye daga cikinmu zai ba wannan al'amari baya. Mu kuma mu yarda da shi, ya zavi wanda ya ga ya fi dacewa daga cikin biyun, bisa sharaxin kiyaye alfarmar Allah da addinin musulunci. Sai Usmanu da Ali suka yi tsit. Sai Abdur-Rahaman ya ce: ko za ku yarda dani a kan haka? Ni kuma ina tabbatar maku ba zan kasa zabar mafi cancanta daga cikinku ba, da yar dar Allah. Nan take suka karva masa da cewa: mun amince.

Daddale wannan magana a kan haka keda wuya, sai Abdur-Rahman ya kama hannun xaya daga cikinsu (Ali) ya ce: kai dai xan'uwan Manzon Allah ne na kusa. Kuma kana daga cikin na farko-farko na shiga musulunci. Ka kuma san haka. Kuma ka riga ka tabbatar mini, tsakanin ka da Allah cewa, da Allah zai baka halifancin nan, za ka yi adalci. Kuma da zai ba wanin ka zaka yi xa'a. Ko ba haka ba?( Ali ya ce tabbas haka ne) Sai kuma ya kevace da xayan (Usmanu) shima ya tuna masa irin wannan yarjejeniya da suka yi. Shi kuma ya qara tabbatar masa da haka.

Qare wannan shiga da fita keda wuya sai Abdur-Rahaman ya xaga hannun Usman, a matsayin wanda Allah ya zava.

Wannan kenan. Shi kuma wancan hadisi da wannan xan Shi'ar ya yamutsa hazon wannan da shi, cike yake fal da qarya ce qarya ce, irin waxanda

Allah ya tsarkake Ali daga furtawa. Kamar hujjar da ya ce Alin ya kafa da matsayin xan'uwansa dana Amminsa da na matarsa. alhali kuwa duk ya fisu girman daraja. Ka ga gaba ta koma baya kenan, inji xan tanoma.

Ko alama Aliyu ba zai yi haka ba, don ya daxe da sanin cewa mafificin mutane a wurin Allah shi ne wanda ya fi kowa jin tsoronsa.

Yan da Abbas zai kafa hujja da cewa: babu wanda ya kai darajata daga cikinku, don ni keda 'ya'yan 'yan'uwa da suka haxa da: Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Ali da Ja'afar *Raliyallahu Anhu* , ka ga babu abin da ya banbanta wannan hujja ta sa da wacan ta Ali.

kuma da abi zai tsaya nan ma da sauqi. Don alfahari da 'ya'yan 'yan'uwa yafi zama xaukaka, bisa yinsa da 'ya'yan ammi.

Abin kamar dai Usmanu *Raliyallahu Anhu* ne ya tashi ya bugi qirji ya ce: Akwai wanda ya auri 'ya'yan Annabi mata biyu kamar yadda na yi? Ka ga babu wani abin alfahari da dogaro a nan. Kuma da shi da wanda ya ce: ko akwai mai mata irin tawa a cikinku, duk jirgi guda ya xauko su. Domin kuwa da Fatima da waxancan 'ya'ya na manzo mata biyu da Usmanu ya aura duk ba wanda ke raye a daidai wannan lokaci na "shura". Musanman ma Fatimatu da Allah ya karva bayan kamar wata shidda da rasuwar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Haka kuma cewar da xan Shi'ar yayi, wai alin *Raliyallahu Anhu* ya ce: ko akwai daga cikinku mai 'ya 'ya irin nawa? Da cewar da ya yi wai, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Ban tava roqon Allah wani abu ba face na rokar wa Ali irin sa. Da kuma wai cewar da ya yi: Ba wanda ya isa ya isar da wannan saqo daga gare ni sai Ali.

Duk waxannan maganganu qaryayyaki ne da ba su da tushe balle makama.

Ita wannan magana kuma ta qarshe, ta cewa babu wanda ya kamata ya isar da wannan saqo daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai xan cikin gidansa, Alkhixabi ya ce a cikin littafinsa: 'Shi'arud-dini': magana ce mutanen Kufa suka yayata daga bakin Zaidu xan Yazidu. Wanda yake kuma ana tuhumar sa da shi'anci, da rashin gaskiyar zance. Kuma ta tabbata duk waxanda sukayo riwaya daga gare shi, ba su san komai ba a kansa.

Sannan kuma wannan malami, wato Al-khixabi ya kalli waccan 'sako' da ake qoqarin kore cancantar isar da shi ga kowa in ba ahlu Baitin na biyu ba, a matsayin sakon musulunci. Ta wannan mahanga ne ma, ya kafawa 'yan Shi'ah hujja da cewa: Suna ina Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya aika As'ad xan Zurarata zuwa Madina don ya isar wa jama'ar can da saqon musulunci, tare da koyawa Ansaru karatun Alqur'ani da sanin makamar addini. Ya kuma aika al-Ala'u xan Al- Hadharami zuwa baharaini da irin wancan saqo. Abu Musa da Mu'azu kuma zuwa Yaman. Utba xan Asidu kuma zuwa Makkah?

Ka ga da haka malamin ya tabbatar masu da cewa, zancen rashin cancantar wani wanda ba Ahlul baiti ba, ga isar da saqon musulunci ya tashi.

Wani abu kuma wanda ke tabbatar da kasancewar wannan xan Shi'a limamin maqaryata shi ne: hadisin daya ce an samo daga xan Abbas. Wannan hadisi ko shakka babu qarya ce lafiyayya. Xauki misalin cewar da ya yi wai mai riwayar ya ce: Babu lokacin da tutar musulunci ta faxi daga hannun Ali *Raliyallahu Anhu* a dukkan yaqoqan da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi. Alhali kuwa babu wanda baisan cewa Mu'ab xan Umari ne, ke riqe da wannan tuta ta Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a lokacin yaqin Uhudu ba. A ranar yaqin Falhu Zubairu ne xan Auwamu ne ke riqe da ita. Wanda har Manzon Allah ya umarce shi da ya kafata a wani wuri da ake kira Al-ityan. Har Abbas yake tambayar sa da cewa: Anya kuwa nan ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya umarceka da kafa wannan tutar?

Buhari da muslimu duk sun riwaito wannan hadisin.

Haka nan kuma cewar da xan Shi'ar ya yi wai xan Abbas ya ce: Aliyu *Raliyallahu Anhu* ne ya ari tutar haquri da juriya a ranar yaqin Hunainu, a inda ya tsaya tare da Manzon Allah .

Itama wannan magana qarya ce kamar sauran. Domin kuwa tarihi ya tabbatar da cewa Abbas xan Abdul-mudallib ne da Abu Sufyanu xan Harisu xan Abdul-mudallibi ne suka kasance gidin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a wannan rana. Abbas na riqe da ragwamar jakar ma'aiki, a yayin da Abu sufyanu ke riqe da shimfixar da yake kanta, a matsayinsu na hurrasu. Wanda a wannan lokaci ne ma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya umarci Abbas xin da ya xaga murya ya kira masa "masu faren kaya da bakar karraba".

Xan Abbas ya ce: Nan take nayi kururuwa na kiransu. Kuma wallahi irin yadda suka danno zuwa wurina, kai kace saniya ce taji kukan lavovon xanta; suna isowa suna faxar: Ga mu ya Manzon Allah, ga mu. Shi kuwa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a lokacin ya xau kyarma, ya na kirari yana cewa: Ni Annabi ne haqiqa kuma xan Abdul-mudallibi ne ubana.

Yana qare faxar haka sai ya sauko daga kan jakarsa, ya xibi tsakwankwani da hannun sa, ya watsawa abokan gaba, yana cewa: Allah ka karya su don girman Ka'aba. Abbas ya ci gaba da cewa: Wallahi wannan aiki na Manzon Allah keda wuya sai naga bangonsu yana darewa suna juyawa da baya, har Allah ya kunyata su.

Buhari da Muslim duk sun riwaito wannan hadisin. Amma Buhari cewa yayi Abu Sufyanu xan Harisu ne ke riqe da ragwamar jakar ta Ma'aiki ba Abbas ba. Kuma a wannan martani nasa, cewa Buhari yayi: Abbas ya ce: Ni da Abu Sufyanu mun kafe gindin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ranar yaqin Hunainu, har akaci aka suxe.

Ka ji wannan. Shi kuwa zancen cewa, Ali *Raliyallahu Anhu* ne ya yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* wanka ya kuma saka shi cikin kabarinsa, magana ce dake da bukatar 'yar kwarye - kwaryar garan fuska. Domin kuwa babu wani daga cikin: Abbas da 'ya'yansa da barorin sa shakran. Da wasu Ansaru, wanda bai sa hannunsa a cikin wannan al'amari ba. Illa dai

Ali *Raliyallahu Anhu* shi ne wanda ke wanka jikin ma'aiki kai tsaye, Abbas na bashi umarni a matsayin sa na kan gida, da kuma kasancewar Aliyu mafi cancanta daga cikinsu da xaukar wannan nauyi kai tsaye.

## 2.22 Wata Sabuwar Tatsuniya Tasu

Shi kuwa hadisin da xan Shi'ar ya kawo. Inda ya ce: Allah Ta'ala ya halicci wani mala'ika a cikin siffar Ali *Raliyallahu Anhu* don ya kashe wa wasu manyan mala'iku (Jibrilu, Israfilu da Mika'ilu) kwandar shauqin da suke yi wa Ali *Raliyallahu Anhu* wanda ya zamar masu kamar ciwo, sanadiyar jin irin falalolin da yake dasu. Da cewar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi ma shi: Baka fatar matsayin ka a wurina ya zama kamar matsayin Haruna a wurin Musa?

Ka ga wannan magana, tatsuniya ce da jahilai irin waxanda ko qarya ta gagare su iyawa kan yi. Domin kuwa babu wani musulmin kirki wanda bai san cewa mi'irajin da a kayi da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, anyi shi ne ba, tun ana Makka; kafin ayi hijra zuwa Madina kamar yadda Allah Ta'ala ya ce: Tsarki ya tabbata ga wanda ya yi tafiyar dare da bawan sa, da dare daga masallaci mai alfarma zuwa ga masallaci mai nisa,wanda muka sanya albarka a gefensa domin mu nuna masa daga ayoyinmu. Lalle shi, shi ne maiji, mai gani (17:1)

Ka ga kenan daga masallacin Makka ne aka yi wannan tafiya.
Haka kuma Allah Ta'ala ya ce: Ina rantsuwa da taurarον, a lokacin da ya faru. Ma'bucin ku bai vata ba kuma bai qetare haddi ba. Kuma baya yin magana daga son zuciyar sa.(maganarsa) ba ta zamo ba, face wahayi ne da ake aikowa (53:1-4). Har zuwa inda ya ce: Shin za kuyi masa musu a kan abin da ya gani? Kuma lalle ya ganshi, haqiqatan, a wani lokacin saukarsa. A wurin da magaryar tukewa take(53:12-14). Har kuma zuwa inda ya ce: Shi kunga lata da uzza? (53:19)

Ka ga duk waxannan ayoyi a Makka suka sabka bisa haxuwar kan malamai da almajiran sanin makamar Alqur'ani da tafsirinsa.

Kuma ka ga cewar da ya yi manzon ya ce wa Ali: Ba ka fatar matsayinka a wurina ya zama kamar matsayin Haruna a wurin Musa? Magana ce da manzon yayi alokacin yaqin Tabuka; yaqi na qarshe a shekara ta tara bayan hijira. Shi kuwa mi'iraji in baka mantaba kafin hijira aka yishi. To ta yaya za'a ce mala'iku sunji wannan magana shekaru da yawa kafinta. Ko sun san gaibi ne?

## 2.23 Bajini Xan Bajini Xan'uwan Bajini

Haka kuma daga cikin irin waxannan hadisai na wofi, da xan Shi'ar ke tuma goda dasu, akwai wanda ya ce wai: An samo daga xan Abbas, wanda wai ya ce: Watarana Al-Musdafa *Sallallahu Alaihi Wasallama* na cikin nishaxi, sai muka ji yaqata ya ce; Ni bajini ne xan bajini kuma xan 'uwan bajini.

Kuma wai sai xan Abbas xin ya ce: Annabi na nufin shi ne bajinin Larabawa, xan bajinin Annabawa; wato Annabi Ibrahim *Alaihis Salamu* wai saboda Allah ya ce:

قَالَ تَعَالَى: أَعُوذُ بِٱللَّهِ مِنَ ٱلشَّيْطَٰنِ ٱلرَّجِيمِ ﴿ قَالُواْ سَمِعْنَا فَتًى يَذْكُرُهُمْ يُقَالُ لَهُۥٓ إِبْرَٰهِيمُ ﴿٦٠﴾ ﴾ الأنبياء: ٦٠

*Munji wani saurayi yana ambatar sa. Ana ce masa Ibrahim (21:60).* Xan'uwan nasa kuwa shi ne Ali. Wanda shima wani bajinin ne. Wai kuma wannan magana ta ma'iki itace fassarar abin da Jibrilu ya ce a lokacin yaqin Badar, daidai lokacin da yake kutsa hatson samaniya. Inda ya ce: Duk wani takobi yau idan ba "zul-qifani" ne ba, labari ne. Duk kuma dakaren da ba Ali ba, shi ma labari ne.

To bari ka ji.

Na farko dai, kan malaman hadisi ya haxu a kan cewa wannan hadisi qagagge ne. Kuma kasancewar sa qarya na tabbatar da bayyana ta fuskoki kamar haka:

**Fuska ta farko**: duk da yake kalmar "al-fata" Balarabiyar kalmar ce wadda aka ce manzon yayi amfani da ita a cikin wannan kirari na nufin "bajini" a babin. Wadda kuma ke nuna "yabo". Sai dai a harshen al-qur'ani da Hadisi; (sunnah) da abin da harshen Larabci ya al-adanta(?) kalmar bata nufin "yabo" ko " suka". A kan yi amfani da ita ne kawai a waxannan wurare da nufin alamta: matashi ko saurayi ko dattijo, ko wani abu mai kama da haka. Domin ai waxanda suka cewa Ibrahim *Alaihis Salamu* " al-fata" a cikin wanccan aya, kafirai ne. Ka kuma san ba yabonsa suke nufin yi ba.

Ka ga a nan kalma ta "al-fata" na nufin "saurayi" ko " matashi".

Wata fuskar kuma itace: Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yafi qarfin yin alfahari ( kirari) da ka kansa da xan ammin sa.

Kuma ko alama Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai qulla zumunci da Ali *Raliyallahu Anhu* ko wani ba. Hadissan dake nuna haka, da waxanda ke nuna qulla zumunci tsakanin Abubakar da Umar duk ka gaggu ne. Abin da dai ya tabbata shi ne, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya qulla zumunci ne tsakanin Muhajiruna da Ansar. Amma bai qulla shi tsakanin Muhajiruna da xan'uwansa Muhajiri ba.

Kuma cewa wannan abu ( kirarin) ya faru ne a ranar yaqin Badar, yama fi komai zama qarya.

Kuma. Aliyu bai tava mallakar wani takobi mai suna "zul-qafari" ba. Abin da ya tabbata a tarihi shi ne, shi wannan takobi yana daga cikin takubban Abu Jahil. Wanda ya faxa a cikin ganimar da musulmi suka samu a wurin yaqin na Badar. Ka ga kenan takobin a wannan rana ba mallakar musulmi ba ne. Na kafirai ne. Kamar yadda Ahlu-sunan: Imamu Ahmad, Tirmizi, xan Maja suka riwaito daga xan Abbas cewa: takobin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* na ganawa na abu Jahil (zul-qafari) azaba, ta hanyar yi masa giyavu, idan sukayi karon battar karfe (majaz).

Kuma. Xan Shi'ar ya manta cewa shekarun Annabi na bayan Annabta, shekaru ne na manyanci; ya wuce a ce masa "saurayi" a lokacin, balle ya cewa kansa, tunda ba magori bane shi.

### 2.24 Son Ali Da Sauran Sahabbai Duk Wajibi Ne

Shi kuwa hadisin da xan Shi'ar ya riwaito daga Abu Zarri, hadisi ne mai gajeren asali (maukit) ; nan zariyarsa ta tuqe ga Abu Zarri xin. Darajar sa ba ta kai ta marfu'i ba (hadisi mai cikakken asali) saboda haka ba a shiga xaka da shi, balle kafa hujja watarana.

Kuma cewa ma an riwaito shi daga Abu Zarri, magana ce da keda xan mirtsi-mirtsi.

To kuma ma duk aje wannan. Ko da hadisin ya inganta, to abin da ya qunsa xin can bai kebanci Ali ba. Domin kuwa son sauran Sahabbai, da suka haxa da: Abubakar da Umar da Usman *Raliyallahu Anhu* da Ansaru wajibi ne, yadda son Ali *Raliyallahu Anhu* yake wajibi a kanmu.

Wani abu dake tabbatar da wannan magana tamu shi ne ingantaccen hadisin da ya ce Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Son Ansaru shi ne alamar imani. Kamar yadda qin su yake alamar manafucci.

Haka kuma wani ingantaccen hadisi a cikin sahihu Muslim ya ce; Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce: Annabin nan da bashi da malami sai Allah ya yi mini busharar cewa: duk wanda yaso ni mumini ne. Wanda kuma duk ya qini munafuki ne.

### 2.25 Son Aliyu Bai Isa Shinge

Xan Shi'ar ya ce daga cikin darajojin Ali *Raliyallahu Anhu* wai akwai hadisin da marubucin littafin: al-fiddausi ya riwaito daga Mu'zu xan Jabalu, wanda ya ce wai: Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Son Ali wani kyakkyawan aiki ne mai silke. Wanda mugun aiki ba ya hudawa, balle ya cutar da mai shi. Haka kuma qinsa, wani mugun aiki ne mai sida, wanda ran mai shi bai daxa shi da komai ba.

**Martani:** Muna tabbatar wa da wannan xan Shi'ar cewa wannan hadisi qarya ne. Kuma wannan littafi na: al-fiddausi cike yake makil da ka gaggun hadisai. Tattare kuwa da kasancewar mawallafinsa; Shirawahi xan Shahradaru ad-Dailami xaya daga cikin mafarauta hadisi da riwayarsa. Hakan bata hana wannan littafi nasa zama maqoshin kolo ba, ta hanyar tarkata duk hadisin da yaci karo dashi a ciki, tare da share isnadinsa, ba kuma tare da kula da kasancewar sa ingantacce ko mai rauni ko qagagge ba. Saboda haka ne ma su gizo da qoqi suka sami ranar shanya jikakken garin su a cikin littafi, barkatai.

Babu wani musulmi na qwarai da zai yarda cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya furta wannan magana. Domin kuwa sanin kowane son Allah da manzonsa sun fi son Ali falala nesa ba kusa ba. Amma duk da haka ba su hana a kama mai su da laifin mugun aikin daya aikata. Ka ga ashe kenan son Ali baya isa shinge.

‘Yan Shi’ah suna ina, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* kansa a yi wa Abdullahi xan Hammaru xan karan duka, saboda yasha giya, tattare kuwa da shaharar da ya yi da son Allah da manzonsa? Son Allah da Manzonsa kuwa wajibi ne a kan kowane mumini. Amma kuma hakan ba zata hana a kama shi da laifin wani mugun aiki ba; za’a kama shi da shi harma a hukunta shi .

Kuma abu ne sananne ga xaukacin jama’ar musulmi; sani na lalura, a sakamakon kasancewarsu musulmi, cewa duk wanda ya rayu ya kuma mutu yana shirka, kashin sa ya bushe; Allah ba zai gafarta masa ba, ko da kuwa yana lasan dugadugan Ali *Raliyallahu Anhu* saboda tsananin so da qauna.

Ai ka ga son da mahaifin Ali; wato Abu Xalib, da Shi’ah al-Galiyya ke yi wa Alin bai hana su shiga wuta ba a matsayin kafirai.

A ta kaice wannan aqida kafirci ce bayyananne , irin wanda Allah ke sauraron mai ita idan ya tuba. Kuma haramun ne ga duk wanda ya yi imani da Allah da ranar qarshe ya kudurta haka, balle furta shi.

Wannan kenan. Haka nan kuma cewar da ya yi wai Annabi ya ce: qin Ali wani mugun aiki ne mai sida, wanda wani aiki na mai shi, ba zai amfane shi da komai ba. Magana ce da ke son a kalleta sau biyu.

Ah! Sau biyu mana. Ai ko shakka babu, sai dai kafircin kafirin da yaqi Ali, ya zame masa qarqiya daga shiga Aljannah, ba kin Alin ba. Kamar yadda imanin mai imani zai zame masa sanadin shiga aljannar, ko yana qin Alin kuwa. Don ba shi ne ma’auni ba.

Haka kuma malaman hadisi sun yi itifaqi a kan cewa hadisai biyu da xan Shi’ar ya riwaito daga xan Masa’udu inda ya ce wai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: ladar son Alu Muhammadin ta yini xaya ta fi alheri bisa ga ibadar shekara xaya. Kuma wai duk wanda ya mutu a kan sonsu xan aljanna ne.

Da kuma xayan da ya ce a cikin sa: Ni da wannan (Ali) hujjar Allah ne a kan halittar sa. Duk hadisai ne ka gaggu. Domin ai ibadar shekara xaya ba wasa bace; dubi girman imani da sallah biyar kowace rana da azumin watan Ramadana, har na tsawon shekara xaya. Ko a kansu xai aka tsaya. Waxanda saboda girmansu ne kan masulmi ya haxu a kan cewa sun fi qarfin son Alu Muhammadin na tsawon zamani, balle kwana xaya, a lada.

Sannan kuma ai hujjar Allah akan bayinsa , ta riga ta tabbata sakamakon aiko manzanni kawai. Dubi abin da Allah Ta’ala ke cewa:

قَالَ تَعَالَى: أَعُوذُ بِاللَّهِ مِنَ الشَّيْطَانِ الرَّجِيمِ ﴿ رُّسُلًا مُّبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ لِئَلَّا يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَى ٱللَّهِ حُجَّةُۢ بَعۡدَ ٱلرُّسُلِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمًا ١٦٥ ﴾ النساء: ١٦٥

Domin kada wata hujja ta kasance ga mutane a kan Allah bayan manzanni (4:165)

Ka ga bayan manzanni Allah bai lava imamai ko waliyyai ko wasunsu ba ko?

Haka kuma nagartattun malamai; ma’abuta ilimi da kishin addini sun haxu a kan cewa, cewar da xan Shi’ar ya yi wai Annabi *Sallallahu Alaihi*

*Wasallama* ya ce: Da gaba xayan mutane za su haxu suso Ali *Raliyallahu Anhu* da Allah *Subhanahu WaTa'ala* ya shafe wuta. qarya ce gangariya. Suka kuma qara tabbatar da cewa da mutane za su haxu suso Alin baki xaya. Hakan ba zata amfane su da komai ba ranar qiyama. Matukar ba su yi imani da Allah da mala'ikunsa da littafansa da manzaninsa da Ranar lahira, suka kuma aikata aikin qwarai ba.

Da zarar haka ta samu daga gare su, to aljanna gare su har quryar xaki, ko dako basu tava sanin ko waye Ali ba, balle su soshi ko su qishi.

## 2.26 Hadisan Gizo Da Qoqi

Kusan mafi yawan hadisan da wannan xan Shi'ar yake shawagi dasu, a sararin samaniyar qoqarin tabbatar da fifikon Ali *Raliyallahu Anhu* hadisai ne na gizo da qoqi.

Daga cikin waxannan hadisai, akwai wanda xan Shi'ar ya ambaci wani arqawari da Allah ya yi a kan Ali *Raliyallahu Anhu*. Da cewa shi tutar shiriya ne kuma shugaban sahun masoya Allah (waliyai) kuma wai Ali shi ne abu xaya da Allah ya wajabtawa masu tsoronsa so a matsayin wata xaya-xayan kalma... har dai qarshen hadisin.

To, malamai masana sirrin hadisi da makamar sa sun yi itfaki a kan cewa wannan hadisi qagagge ne. Kuma baya zama ingantacce don kawai mawallafin littafin al:Hilyah ya riwaito shi, ko wani mai kama dashi. Domin tabbataccen abune shi wannan malami ya riwaito hadisai masu yawa a cikin wannan aiki nasa. Waxanda kusan duk masu rauni ne, a kan darajojin, Abubakar da Umar da Usmanu da Ali da wasu waliyai da wasunsu. Kai! Wasunsu ma ka gaggi ne bisa haxuwar malamai. Duk da yake shi da takwarorinsa daga cikin "huffaru" amintattu, ma'abuta hadisi, amintattu ne a karan kansu, a kan duk abin da za su riwaito daga shehunninsu. Illar tare da su shehunan.

Haka ma hadisin Ammaru da na xan Abbas, waxanda xan Shi'ar ya kawo duk na gizo da qoqi ne.

## 2.27 Sun Mayar Da Sahabbai Dalga

Sahabbai a wurin 'yan Shi'ah ba kowa bane. Saboda haka suka mayar da su dalga. Ta hanyar kai masu ko wacce irin suka, da zuba masu kowacce irin qazanta kamar salga.

A qoqarin tabbatar da wannan manufane , xan Shi'ar ya ce wai: Jumhurun malamai sun riwaito abubuwan kunya da basu kida yuwa a kan Sahabbai. Wanda har wani marubuci mai suna al-qalibi ya wallafa littafi mai suna. Ababen kunyar Sahabbai wai. Amma bai ambaci wani abun kunya ko xaya ba, ko wata naqasa dangane da Ahlul-Baiti a cikin littafin.

To ka ga irin wannan xanyen aiki na 'yan Shi'ah abin yayi hattara ne da.

**Martani:** To, kafin mu shiga walwale wannan qullin maqodo filla - filla, muna tabbatar wa xan Shi'ar da cewa, duk wani abu da wani zai ga

la'arin Sahabban Manzon Allah a kansa, bai kamata a kira shi abin kunya ba. Sai dai wata qila ko qorafi.

Amma daxa ga dalilai na:

Qorafe-qorafen da a kanyi kan Sahabbai nau'i biyu ne:

Ko dai su kasance: 1) qarya zalla. Wato an qaga masu ne; ba su ji basu gani ba. Ko kuma 2) lauje cikin naxi. Wato abubuwan sun faru a cikin nagartattar sura. Amma sai magabata suka sake masu fuska. Ta hanyar rage wasu abubuwa daga cikinsu ,da qara wasu. Ta yadda za su bayyana a matsayin miyagun ayukka ga idon duniya. Waxanda a qarshe za su tsirar da itatuwan suka da zargin waxannan bayin Allah.

To mafi yawan korafe - korafen da ake riwaitowa a kansu, na qarqashin wannan kashi na biyu ne. Kuma za ka taras da cewa, waxanda ke riwaito sun, mutane ne da suka shahara da qarya; kamar su Abu Mukhnif; Lud xan Yahya, da Hisham xan Muhammad as-Sa'ibi al-kalibi, da wasu maqaryata takwarorin su. Kuma ka ga dashi wanna al-kahbin ne xan Shi'ar ya kafa mana hujja. Alhali kuwa limami ne daga cikin limaman qarya a duniyar Shi'ah. Kuma duk abin daya riwaito kan biyo takan mahaifisa ne daga hannun abu Muhnif xin can. Waxanda dukansu biyun ba a shiga xaka da maganarsu.

Nau'i na 3), kuma daga cikin waxannan qorafe - qorafe, shi ne, : Tantagaryar gaskiya. Wato abubuwa waxanda tabbas Sahabbai sun aikatasu a matsayinsu na 'yan adamu. Amma kuma suna da uzuri a kan haka. Wanda la'akari dashi, ke xauke ayyukan daga zama tantagaryar zunubi, zuwa matsayin ijtihadi. Irin wanda mai shi ke samon lada biyu idan ya yi muwafaka. Yake kuma samun xaya idan yayi kuskure.

To gaba xayan abin da ya inganta, daga cikin qorafe - qorafen, na qarqashin wannan inuwa ne.

Kuma duk ma qorafin da aka qaddara wa wani tantagaryar zunubi, za ka taras ba wata alka da yake iya yi wa Sahabban, idan akayi la'akari da darajojinsu da kyawawan ayukkansu, da kasancewarsu 'yan aljanna tun duniya. Domin ba garesu kawai ba. Ga kowa ma, tantagaryar zunubai kan zama labari a lahira, a yayin da mai su ya sami xaya daga cikin waxannan lanbobi ko masu kama dasu, tun duniya:

(a) Tubar wankan tsarki. Kamar yadda ta tabbata daga bakin malaman Shi'ah 'yan-sha-biyu cewa, waxannan Sahabbai sun yi irin wannan tuba ga Allah *Subhanahu WaTa'ala* a kan duk kurakuran da suka aikata.

(b) Kyawawan ayyuka. Kamar yadda ta tabbata cewa kyawawan ayyuka na wanke zunubai. Kuma Allah Ta'ala ya ce: Idan kuka nisanci manyan abubuwan da ake hanaku aikatawa, to, za mu kankare muna nan ayukanku daga gare ku (4:31)

(c) Manyan musibu. Waxanda ta tabbata suna kankare zunubai

(d) Addu'ar muminai waka junansu. Da kuma ceton da Allah zai ba su damar yi wa junan nasu gobe qiyama.

Kai! Babu wani abu dake zaman dalilin kwaranyewa, wani daga cikin al'ummar nan wani zunubi ko wata azaba, face waxannan Sahabbai sun fi cancanci da shi a kan kowa. Sune kuma ya kamata su zama sha yabon masu yabo, varin varin masu vari kafin kowa.

Bayan xan Shi'ar ya qare waccan dunqulallar maganar, sai kuma ya ce: Al-Kalbi ya ambaci waxancan abubuwa na kunya masu yawa. Bari in xan gutsuro maku kaxan daga ciki. Sai ya ce: An riwaito cewa watarana Abubakar *Raliyallahu Anhu* na kan munbari sai ya ce: haqiqa Annabi ya kasance yana samun gudunmuwar wahayi a kan duk abin da yake aikatawa. Ni kuwa shexan na iya dagula mani lisafi. Ina fatar za ku mara mani baya a duk lokacin da kuka ga na kama hanya shararra. Za ku kuma kevo ni, idan na kama daji.

Ka ji qarshen maganar Siddiqu.`

To sai xan Shi'ar ya ce: To ta yaya za'a yarda da shugabancin wanda ke da buqata da taimakon talakawa, alhali kuma su suna da bukata da nasa taimakon? An yi haihuwar guzuma kenan.

**Martani:**

Ai wannan hadisi aya ne, dake tabbatarwa da nuna xaya daga cikin manyan darajojin Abubakar Sidiku *Raliyallahu Anhu*. Kuma ba wani abin da ke nuna kasancewarsa wanda ba ya nufin homa da varna a bayan qasa kamar wannan magana da ya yi. Dama kuma bai nemi shugabancin ba, bai kuma tava sha'awar zalunci ba. Bai kuma da nufin yin mulkin mallaka a halifancinsa. Saboda haka ya kama hannun mutane ya haxa dana Allah da manzonsa; ya ce subi su.

Tabbas abida yake nufi kenan. Don fassarar waxancan kalmomi da ya yi amfani dasu itace: idan kun ga na tsayu a kan xa'a ga Allah, to ku agaza mani a kan haka. Idan ko kun ga na bar tafarkin gaskiya to (don Allah) ku ceto ni. Kamar yadda wata magana daya tava yi ke tabbatarwa, in da ya ce: kubi ni matuqar na bi Allah, idan kuma nayi kuskure daga yi masa xa'a ku yi ta kanku.

Allahu Akbar!!! Ka ji baraden musulunci.

Kuma cewar da halifan yayi, shexan na iya dagula masa lissafi, magana ce da bai kamata mai hankali da ilimi ya yi wa kallo biyu ba. Saboda abu ne dake iya faruwa ga kowane xan Adam. Don babu wanda Allah bai sawa abokin zama daga cikin mala'iku da shexanun (aljannu) kowane xaya-xaya ba.

Ka ga a nan Siddiqu na sone ya faxawa duniya tun da asuba, cewa fa shi ba ma'asumi ne kamar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba. Wannan kuma gaskiya ne.

Wannan kenan. Ita kuma cewar da xan Shi'ar ya yi wai: ya za'a amince da shugabancin wanda keda bukata da agajin talakawansa don ya dawo ga hanya. Maganace irinta waxanda suka jahilci tantagar yar manufa da ma'anar shugabanci (Imama)

Ai a tsarin musulunci shugaba ba Ubangijin talakawansa ne ba, balle ya kasance baya da bukata dasu. Kuma ba Manzon Allah bane, zuwa gare su, balle ya zama hamzatul-wasali tsakanin suda Allah. A'a, ko alama. Shi, shugaba ne, kuma abokin tarayyar talakawa cikin duk abin da zai tabbatar da nagartar rayuwar su ta addini da duniya; dolene su yi masanyar hannuwan gudunmuwar alheri a tsakaninsu. Wato ya zama kamar dai madugun tafiya, wanda ayari zaibi baki alaikum, idan ya kama lafiyayyar hanya. Su kuma faxakar da shi idan yaci tuwon gigi; su dawo dashi a kan hanya madaidaiciya. A qarshe kuma idan wani abu; mutum ko dabba ya kawo masu hari, to sai ayi ba babba ba yaro; dashi dasu duk sun tuve ayi ta katakka. Idan an qare lafiya, ya koma ya nax a rawaninsa ya fike amawali ya buxe mahuta.

Amma kuma tattare da haka akwai bukatar duk wanda zai shugabanci jama'a ya kasance mafificinsu kamala a ilimi da kudura da jinqai, don ya zama masu rariya matatar komai.

### 2.28 Tawali'u Ne Ba Rashin Cancanta Ba

Daga cikin abubuwan da xan Shi'ar ke sukar lamarin Sahabi Abubakar *Raliyallahu Anhu* dashi akwai cewar da ya yi wai, Abubakar *Raliyallahu Anhu ya yi*qoqarin butsewa a lokacin da aka zave shi matsayin halifa, saboda sanin da ya yi cewa bai cancanci muqamin ba; Don ba haqqin sane ba. Wai sai ya ce: (Don Allah) ku fita ba tuna, tunda ga Aliyu na raye, ai ba ni da wani matsayi. Balle a dage a kan sai Ni.

Daga nan ne xan Shi'ar ya ce: Idan dai har Abubakar na jin cewa ya cancanci wannan shugabanci, kuma haqqinsa ne, to qoqarin bultsewar nan da ya yi savo ne. Idan kuwa har kamuyamiya ce zai faxa wa; kamar yadda shi da kansa ya hango haka, har yayi qoqarin bultsewa. Kuma tattare da haka ya ci gaba da riqe mukamin, to abin kunya ya tabbata a kansa.

Lalle, kai kasan kafiri dai bai san kunya ba!!!

**Martani:** Babu inda wannan magana ta fito a cikin littafan hadisi ingantattu. Babu kuma mai cewa ga isnadinta. Saboda haka qarya ce kawai.

Abubakar *Raliyallahu Anhu* baice: "Tun da Aliyu na raye---ba") Ingantattar maganar da dai ta tabbata itace, cewar da ya yi a ranar da sukayi taro a "saqifa": ya ku jama'a ina kiranku ga ku naxa xaya daga cikin: Umar xan khaxxabi da Abu Ubaidatu xan Al-Jarrar . yana qare faxar haka sai Umar ya yi kazazam ya ce: A'ah! Kai dai za'a naxa. Ko banza mun daxe da gamsuwa da zaman ka shugaba a gare mu, kuma mutum mafi alheri da soyuwa a wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma wallahi da za'a rataye ni a sare kai na, in tafi wurin Allah ina tsarkakakke, ya fi soyuwa gareni. Bisa ga a naxani shugaban mutanen da kake cikinsu.

Kaji iyakar abin da ya gudana a wannan taro ta wannan haujin.

To kuma tafi naji. Muqaddara cewa Abubakar xin *Raliyallahu Anhu* ya ce: "kuma Aliyu na raye" kamar yadda xan Shi'ar ke son ya ce. To ai wannan

shedar da Umar ya bayar a kansa ta isa ta cancantar da shi ga halifancin fiye da kowa. Haka kuwa akayi, ka gani ko?!

To kuma mu dawo ga cewar da xan Shi'ar ya yi wai: Da Abubakar na jin halifancin haqqinsa ne, ya kuma nemi ya butse, to ya aikata savo.

To abin da za mu cewa a nan shi ne: Mu qaddara cewa Abubakar xin *Raliyallahu Anhu* ya nemi ya butse. Hakan bata nuna rashin kasancewar ta haqqi gare shi. Domin kuwa zaman abu haqqi ga mutum na nufin ko dai 1) halas ne gare shi. Ko kuma 2) Wajibi. Babu kuwa inda barin halas don kunya (fillanci) ya zama laifi, balle a ce. Na farko kenan. Kuma ka ga zancen aikata sabo bai taso ba.

Na biyu kuma, halifanci na zama wajibi a kansa, idan sauran Sahabban suka qi janye naxin da suka yi masa balle su naxa wani. Rashin yin haka kuwa da suka yi ya tabbatar da shi a haka.

Kuma ai ka ga da yawa mutum ka qulla ciniki ko jinga, ta yadda wanzar da su zai wajaba, amma kuma ya iya fasawa. Kamar haka ne. Abu ne mai yiwuwa ya kasance Abubakar ya nemi ya butsewa shugabancin ne saboda tawali'u da irin nauye - nauyen dake kansa. Tattare da kasancewar babu wanda yafi shi cancanta da ita a wurin dama wani wuri. Kuma ai tawali'u bai tava kayar da haqqi ba.

## 2.29 Abu Ne Daga Allah

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa wai: Umar ya ce: Mubaya'ar da suka yi wa Abubakar *Raliyallahu Anhu* a matsayin halifa baqar qaddara ce. Wadda ba don da Allah ya tsare ba. Da hakan ta saukar da wata alloba. Saboda haka, duk wanda ya sake irin wannan gigi ku kashe shi.

Xan Shi'ar yaci ka da cewa: Ka ga inda shugabancin Abubakar ba baqar qaddara ce ba, Umar bai cancantarwa wanda ya sake irinta da kisa. Idan kuwa ya yi haka to abin kunya ya tabbata gare shi. A yayin da tabbatar zamanta baqar qaddarar, da rashin cancantar Abubakar da ita, zai tabbatar da abin kunya a kansu su biyu.

Kai ka ji magana kamar ta mai ilimi da imani.

**Martani:** Za mu kawo wa mai karatu cikakken martanin wannan hadisin, mu kuma fexe shi har wutsiya. Saboda gaskiya ne abu ya faru, amma mutumin naku (Xan Shi'ar) ya yi halin nasa.....

Kafin haka ga dai ingantaccen abin da Umar xin *Raliyallahu Anhu* ya ce a cikin hadisin: kada in qara jin wani daga cikinku yayi varin bakin cewa ba Abubakar ne aka shirya yi wa bai'a ba, illa dai abune daga Allah. Eh! Ko shakka babu haka ne. Kuma sai ga shi Allah ya sa ta zama alheri ga mutane. Don babu wanda mutane ke goyon bayansa daga cikinsu kamar Abubakar.

Wato yana bayyana irin yadda mutane suka yi ta yin tururuwa suna kai caffa ga Abubakar *Raliyallahu Anhu* ba tare da wata inda - inda ba.

Babu wani abin mamaki ko kaxan a cikin haka. Domin kuwa Sahabbai sun riga sun sallama wa Abubakar fai da voye, tun Annabi na raye. Musamman

ganin irin yadda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ke gabatar da shi ga al'amurran zahiri da baxini. Saboda haka Sahabbai a wannan lokaci ba su bukatar wata shawara ko jinkiri kafin suyi wasa bai'ar. Savanin wani, wanda ba shi ba, da ba ta yiwuwa (halatta) a yi masa mubaya'a haka nan ba tare da an xanyi wani batun zucci ba, da 'yan shawarwari.

Saboda haka duk wanda ya yi wa Abubakar mubaya'a, a wannan lokaci, ba tare da wata ida-inda ba, daidai yake. Saboda ai nuni ya ishi mai hankali.

## 2.30 Halifa Abubakar Bai Damu Ba

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa wai: A lokacin da ajalin Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya qaraso, halifan yayi nadamar karvar halifancin da ya yi, inda ya ce: kaicona! Na so ace na samu damar tambayar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*; shin ko Ansaru nada wani haqqi a cikin wannan al'amari( halifanci)?

Xan Shi'ar ya kammala da cewa wai: Wannan shi ke nuna cewa ko da Abubakar ya karvi halifacin yana cike da kokwanton cancantarsa da shi; yana kuma jin naxa shi da aka yi kuskure ne.

**Martani:** Wannan magana qarya ce xan Shi'ar ya yi wa Abubakar; ko ban za bai ambaci isnadin ta ba. Kuma sannen abune cewa wajibi ne ga duk wanda ya kafa hujja da wata riwaya, ya kawo isnadinta matukar yana son hujjarsa ta zama karvavva. Balle wanda ke son tabbatarwa duniyar musulmi da cancantar keta alfarmar Sahabbai. Sai kuma ya buge ga kafa hujja da wata shegiyar hikiya; maras uba balle kaka da kakanni.

Sannan kuma muna tabbatarwa da xan Shi'ar cewa, da yana da hankali da wayo da bai kawo wannan magana ba. Domin .kuwa tana qaryata iqirarin da suke yi ne, na cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bar sallahun Ali ya gaje shi, a nassance. Ka ga kenan da akwai wancan nassi da suke tutiya, da Abubakar *Raliyallahu Anhu* bai nemi sanin ko Ansaru nada wani haqqi cikin al'amarin ba. Wannan idan mun qaddara tabbata da ingancin wannan shegiyar riwaya keNan.

Wannan magana tabbas ce.

## 2.31 Tsananin Tsoron Allah Ne

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa wai: wani abu kuma dake nuna cewa Abubakar *Raliyallahu Anhu* ba kowa bane shi ne cewar da ya yi lokacin daya kai gargara : kaicona! Ina ma ace mahaifiyata bata haifeni ba, ina ma ace buntu aka yoni a yi dawun kungu da ni.

Xan Shi'ar ya ce: kaji abin da Abubakar ya ce: Tattare da kuma kasancewar Ahlus-Sunnah sun riwaito daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* wanda ya ce: babu wanda zai kai gargara daga cikin mutane face Allah ya nuna masa mazauninsa na aljanna da wuta.

**Martani:** Cewa halifan ya faxi wannan magana a wannan lokaci abu ne ba a tava ji ba. Saboda haka ko shakka babu wannan ba gaskiya ba ne.

Amma dai ya inganta cewa, nana Aisha *Raliyallahu Anhu* tazo wurinsa. Yana gargara, tana mai maita wani baitin waqa dake cewa:

Wadata ba tada wani amfani ga mutum,

Idan qirjinsa ya buwayi numfashinsa zuwa,

Ya dawo yana gargara a maqogwaro.

Tana faxar haka sai halifan *Raliyallahu Anhu* ya kware fuskarsa ya ce: bari wannan magana kamata yayi ki ce: Kuma mayen mutuwa yaje da gaskiya. Wannan shi ne abin da ya kasance daga gareshi kana bijirewa (50:19)

Wannan alokacin da ya kai gargara kenan. Amma alokacin daya ke lafi yayye, an tava jin yana cewa: kaicona! Ina ma a ce mahaifiyata bata haife ni ba. Wannan kuwa tsananin tsoron Allah ne, in har ta tabbata ya ce hakan.

Kuma irin wannan kalami dake nuna tsoron Allah mai shi, ba Abubakar *Raliyallahu Anhu* ne farau ba. An riwaito mutanen kirki da dama, sun furta irin haka, saboda tuna irin tashin hankali da firgita da ranar tashin qiyama ta qunsa. Har wani daga cikinsu ya ce: Da za'a bani zavi, tsakanin in mutu ayi min hisabi, tare da lamanar shiga aljanna, ko a mayar dani turxa? Dana zama turxa.

Imamu Ahmad ma ya riwaito cewa Abu Zarri ya tava cewa: Wallahi na so ace ni wata itaciya ce da ake taunawa a furzar.

## 2.32 Ja Da Baya Ba Tsoro Ba

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya kuma ce: Kaicona dana sani dana marawa xayan mutanen nan biyu baya ( Umaru xan Haxxabi da Abu Ubaidat xan al-Jarraru) a ranar taron sa'idata, ya zama shugaba. Ni kuma inzama wazirinsa.

Xan Shi'ar ya ce: To ka ga wannan magana, tana tabbatar da cewa Abubakar bai cancanci halifancin ba. Tunda gashi; da kansa yana da ya sani; da bai karva ba.

**Martani:** A hankalce, wannan magana, idan ma har ta tabbata cewa Abubakar xin yayi ta. To tana kawai nuna cewa ba Ali *Raliyallahu Anhu* ne ya cancanci halifanci ba. Kuma ya faxe tane, shi abubakar *Raliyallahu Anhu* xin, saboda tsoron kada alfarmar halifancin ta tozarta kuma ko da Allah zai kaddari haka, to shi dai ya fi son haka ta kasance hannun wani ba shi ba. Wannan kuma na nuna irin yadda ya san girman shugabancin. Kuma wannan abu da ya yi, jada baya ne ba tsoro ba.

Wato ya fi son ko da zai kasance da hannu a cikin shugabancin, to kada ya wuce na wazirci. Ta yadda nauyin ba zai tattara a kansa ba. Kuma haka baya nuna wani tsoro ko kasawa. Domin kuwa qarshen ta dai nauyi kansa ya qare.

Kuma ka ga inda nassin halifancin Aliyu *Raliyallahu Anhu* ya inganta, Abubakar *Raliyallahu Anhu* ba zai kudurta marawa waxancan mazajen baya ba. Don yin haka tare da sanin waccan masaniya tozarta alfarmar halifancin ne. Kuma kenan shi zai kasance wazirin halifa mai shigar kutse. Wato ya sayarda lahirarsa kenan, saboda duniyar waninsa ta gyaru.

Ka kuwa san ba irin Abubakar *Raliyallahu Anhu* ba. Duk wanda ke tsoron Allah, yake kuma fatar gamawa lafiya ba zai yi haka ba.

### 2.33 Wani Jihadin ne ya Tsayar Da Siddiqu

Wani qoqarin kashe isa, da xan Shi'ar yayi ga Siddiqu, shi ne cewar da ya yi wai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce, watarana yana jinyar ajali. Yayi yana maimaitawa: ku tabbata da ganin rundunar Usamatu ta xaga. Kuma Allah ya la'anci duk wanda ya bari jirgin wannan rundunar ya bar shi tasha.

Kuma wai a wannan lokacin halifofin can uku na kafin Ali *Raliyallahu Anhu* na tare da Manzon Amma wai qarshenta Abubakar ya hana Umar *Raliyallahu Anhu* halartar yaqin.

**Martani:** Gaba xayan masana tarihin musulunci da mazajensa, sun yi ittifaqi a kan cewa wannan magana qarya ce. Kuma babu wani daga cikin ma'abuta ilimi da ya riwaito cewa Abubakar da Usmanu *Raliyallahu Anhu* na daga cikin waxanda Manzo ya umarta da fita tare da rundunar Usamatu. Abin da dai aka riwaito shi ne ya umarci Umar da yin haka.

To, yama kamata duk mai hankali ya tambayi kansa cewa: yaya za a yi Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tura Abubakar xin *Raliyallahu Anhu* tare da waccan runduna ta Usama, Alhali ya riga ya xaura masa nauyin ba musulmi sallah. Matuqar shi ba zai iya ba saboda rashin lafiyar da yake fama da ita?! Kuma ingantattun riwayoyi mutawatirai sun tabbatar da cewa sai da manzon ya share kwana goma sha biyu kwance yana jinya. Bai kuma sa wani Sahabi bayar da sallar ba, baya ga Abubakar*Raliyallahu Anhu*.

Ka ga kenan ba wai sallah xaya ce ko biyu, ko ta yini xaya ko biyu ba, Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya waqilci Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bayarwa balle a zaci yiwuwar faruwar wannan dama lissafin da 'yan Shi'ah ke qoqarin haifarwa. Har ma suna qarawa da cewa; wai 'yarsa ce Aisha, don dai hilqon tsiya ta tura mahaifin nata ga bayar da sallar; Annabi bai ji bai gani ba.

To ba haka al'amarin ya kasance ba. Manzo ne da kansa ya hore shi da hakan. Kuma tsawon kwanukan jinyar sa.

Ko ka gane. Gaba xayan mutane sun yi ittifaqi a kan cewa tsawon kwanakin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi yana jinya, Manzon bai samu fitowa limanci ba. Babu kuma wanda ke waqiltarsa a kan haka sai Abubakar *Raliyallahu Anhu* kuma ya share tsawon kwanaki yana wannan waqilci. Lokaci da malamai suka kimanta mafi qaramcin sallar da Siddiqu ya jagoranta a cikinsa da sallah goma ce; sallar isha'i ta daren Jumu'a. Aka wayi gari kuma ya jagoranci juma'a, tare da yin khuxubar ta.

Wannan shi ne abin da ingantattun hadisan mutawatirai suka tabbatar:
Haka kuma Siddiqu Ya ci gaba da ba musulmi sallah, bayan wannan salla ta jumu'a, har safiyar ranar litinin. Ranar da yana cikin limancin sallar subahi dinta Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yaye labulensa, yayo

dogon haske; ya dubi tsayuwar sahun almajiran da ya yaye, a jami'ar farko ta musulunci, suna koyi da jami'insu Siddiqu.

A lokacin da Sahabbai suka ji a jikinsu cewa ana kallon su. Suka kuma daga kai suka ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kaxan ya rage hankalin su ya rabu biyu. Shi kuma ma'aiki daya fahimci haka sai ya saki labulen.

Wannan shi ne gani na qarshe da suka yi wa Manzon, yana raye hantsi na gab da qarewa a wannan rana ya ce ga garinku nan.

### 2.34 Ba Rashin Yarda Ba Ne

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa kuma wai: Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai tava wakilta Abubakar ba a kan wani al'amari, tsawon ra yuwarsa. A maimakon haka ma sai dai ya shugabantar da Umar xan Asi a kansa, wani lokaci. Wani lokacin kuma yasa shi qarqashin jagorancin Usama. Qarewa da qarau ma, ko lokacin da Manzon ya tura shi isar da saqon surar Bara'a,ba afi kwana uku ba, Allah ya yi wa manzon wahayi da ya karvi saqon daga gare shi ya ba wani (Ali RA). Wai haka kuma aka yi.

Xan Shi'ar ya kammala da cewa wai: to ya za a yi mai hankali ya yarda da shugabancin wanda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai yarda da shi ba. Kuma ma har Allah da kansa yayi horo da dakatar da shi daga isar da saqon ayoyi goma kacal daga cikinsurar Bara'a? Wai ya za a yi mai hankali ya yarda da irin wannan mutum a matsayin shugaba?!

**Martani:** Ko shakka babu wannan magana qarya ce feqaqqa. Domin masana tarihin musulunci, da malaman tafsiri, dana sira, da na hadisai da fikhu, da wasunsu duk sun tabbatar da cewa Abubakar *Raliyallahu Anhu* ne ya waqilci Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a hajjin sheqara ta tara; hajji na farko a tarihin musulunci, wanda musulmi sukayi daga birnin Madina. Idan a kwai wani, hajji da za'a ce musulmi sunyi kafin wannan, sai fa wanda suka yi bayan anci garin Makka da yaqi nan take, a qarqashin jagorancin Asyad xan Abilt-Asi xan Umayyata, mutumin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya shugabantar a kan mutanen Makka, bayan wannan nasara. Wannan hajji da aka yi a qarqashin jagorancin wannan Sahabi anyi shi ne a cikin shekara ta takwas. Shekara na dawowa kuma sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tura Abubakar *Raliyallahu Anhu* bayan sun dawo daga yaqin Tabuka, don ya jagorancin hajjin wannan shekara. Ya kuma Umarce shi da shedawa kafiran Makka cewa: daga wannan shekara an haramta wa da wani mushriki aikin hajji, balle xawafi uryan.

Ta kuma tabbata cewa babu wani daga cikin Sahabbai da Manzon Allah ya tava naxawa irin wannan waqilci sai Abubakar *Raliyallahu Anhu* ka ga wannan abin godiya ne ga Allah. Wani abin ma shi ne, Ali *Raliyallahu Anhu* na cikin waxanda Abubakar xin *Raliyallahu Anhu* ya jagoranta a lokacin. Wanda ma a lokacin da ya isa Makka, sai Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya

tambaye shi: kazo ne a matsayin shugaba ko talakka? Shi kuwa ya ce: A‘a na zone a matsayin talakka.

Haka wannan aikin hajjin ya guda na; Aliyu na sallah bayan Abubakar *Raliyallahu Anhu* tare da sauran musulmi, ya na kuma sauraron umurninsa kamar yadda kowa ke saurare; babu wani abu da musulmi suka yi wa Abubakar *Raliyallahu Anhu* a wannan lokaci face ka ji amon muryar Ali *Raliyallahu Anhu* a ciki.

Haka kuma Abubakar *Raliyallahu Anhu* ne mutum xaya kwal daga cikin Sahabbai , wanda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya waqilta ya riqa bawa musulmi sallah tsawon kwanakin jinyarsa ta ajali.

Ka ga waxannan waqilce- waqilce biyu da Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya yi wa manzo, darajoji ne guda biyu daya kevanta dasu. Savanin irin waqilcin da wasu Sahabbai suke yi masa; irin su Ali *Raliyallahu Anhu* da wasunsa; Babu wani nau’i na waqilci da Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi wa manzon, face wasu Sahabbai sun yi masa irinsa ko wanda ya fishi.

Wannan kenan. Haka nan kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai tava shugabantar da Usamatu ko Amir xan Asi a kan abubakar ba *Raliyallahu Anhu* a matsayin waqillai. Nagartattun malamai sun yi itfaqi a kan haka.

Ita kuwa qissar jagorancin Amir xan Asi ga Abubakar da sauran Sahabbai *Raliyallahu Anhu* Xan Shi’ar yasa son zuciya a ciki.

Yadda al’amarin ya faru a haqiqa shi ne: Watarana ce Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tura Amru xin ya jagoranci yaqin zatis-salasilu, wanda za a yi da Bani uzurata; kawunnan shi Amru xin. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi haka ne don wataqila, hakan ta zama sanadiyar musuluntarsu, ganin xansu gaba-gaba.

Tafiyar su keda wuya kuma sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi shawarar qara kabrin jagorancin rundunar. A inda ya tura Abubakar da Ubaidatu harma da Umar *Raliyallahu Anhu* da wasu Sahabbai daga cikin Muhajiruna. Ya kuma yi masu gargaxin cewa: ku haxa kai dashi kada ku bari a ji ku.

Bayan sun isa, Ubaidatu madugun wannan ayari na biyu ya cewa Amru: Manzon Allah ya turomune mu kama muku wannan daga. Saboda haka idan lokacin sAllah ya yi, sai kowanenmu; ni da kai, ya jagaranci rundunarsa Salla. Don gashin kanmu muke ci. Sai Amru ya ce: A’a, ashe ba cewa kayi manzo ya turoku ne ku kama mana daga ba? Ya ce : Eh, haka ne.

Sai Amru ya ce: To ai, ba batun cin gashin kai kenan za ku yi Sallah ne a bayana. Sai Ubaidatu, ganin irin yadda Amru ya kafe, ya ce: To ba komai, da ma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya umarce ni da cewa, kada inyarda ajimu da kai. Nan take Abubakar ya qara daddale wannan magana ta haxa kai tare da qarawa Ubaidatu qwarin gwiwa a kanta. Wannan ra’ayi kuwa na Abubakar shi ne mafi dacewa.

Daga nan sai suka ci gaba da Sallolin su bayan Amru a matsayin liman. Amma kuma kowa yasan cewa darajarsa ba ta kai tasu ba.

Amma cewar da xan Shi'ar ya yi wai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya karve isar da saqon suratul bara'a daga hannun Abubakar *Raliyallahu Anhu* bayan kwana ukku, wai saboda rashin yarda da aminci. Kuma wai ma Allah *Subhanahu WaTa'ala* ya yi masa wahayi da hakan.

Wannan magana ko shakka babu qarya ce, da kowa ya san qarya ce. Amma kuma babu mai musun cewa xauke saqon waccan sura (ayoyi) daga hannun abubakar zuwa na Ali *Raliyallahu Anhu* umurni ne daga Allah, amma ba rashin yarda ba ne. Bari kaji yadda abin yake, ya kai jahili uban jahilai.!

Sayyidi Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya waqilci Manzo a hajjin wannan shekara ta tara kamar yadda ya ummarce shi. Bai dawo garin Madina ba sai da anka qare aikin hajji. Ya kuma shelantawa kafiran Makka saqon manzo na shekara; cewa kada mushrikin daya sake aikin hajji daga wannan shekara ,balle yayi xawafi uryan; abin da suka al'adanta. Abubakar ya shelanta wannan saqo kowa naji, sauran Sahabbai na yi masa amshi, har ma da Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* a cikinsu.

To dama akwai daddalallin arkawwura tsakanin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da mushrikan Makka. Dawowarsu Abubakar *Raliyallahu Anhu* daga wannan aiki na hajji keda wuya, sai nan take Manzon ya sake tayar da Ali *Raliyallahu Anhu* don ya koma ya walwale waxancan arqawwulla, tunda mushrikan sun kasa tsare alfarmarsu.

Dalilin kuwa da ya sa Manzon, bai bari Abubakar *radiyallahu anhu* ya qarqare ayyukan wannan shekara na sakwanni a matsayin waqilinsa ba shi ne: da ma a al'adar Larabawa babu wanda ya isa a kulla wani arqawari da shi ko ya walwale shi, daga cikin wasu mutane, sai shugabansu ko wani daga cikin danginsa na jini. Saboda haka ne Manzon ya tura Ali *Raliyallahu Anhu* ba don komai ba; kuma iyakar abin da ya tura shi yayi kenan. Saboda haka ne ma Alin ya kasance yana Salla bayan Abubakar *Raliyallahu Anhu* yana kuma biyar sawunsa a cikin ayukan hajji kamar yadda sauran musulmi keyi saboda shi Abubakar xin ne waqilin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na wannan shekara.

### 2.35 Siddiqu Ba Jahili Ba Ne

Sai kuma xan Shi'ar ya ci gaba da cewa wai: kuma saboda tsabar jahilci Abubakar ya tava sa aka yanke hannun hagun wani varawo; saboda bai san na dama ne ake yankewa ba.

**Martani:** ko shakka babu cewa Siddiqu jahili ne, bai san cikin da wajen wannan mas'ala qanqanuwa ba, qarya ce bayyananna. Inda ma har cewa aka yi yana ganin yanke hannun hagun varawo shi ne mafi dacewa, bisa ga na dama. Da maganar tafi xan shiga. Domin kuwa babu inda Alqur'ani ya bayyana cewa lalle ne idan za'a yanke hannun varawo a yanke na dama, balle.

Xan Mas'ud ne, a salon qira'arsa ya tafi a kan yanke hannun dama; ba na hagu ba. Kuma sai kawai daga nan abin ya zama "sunna". Shi a wurinsa, maimakon a karanta ayar kamar haka: "Faqda'u Aidihima"( ku yanke

hannayensu) sai ya karanta ta da: “Faqda’u Aimanahuma” ( ku yanke hannayensu na dama). Ka ga kenan mas’alar ta ijtihadi a salon qira’a ce.

Kuma ma duk aje wannan jerangiya. A wane littafi, ko daga bakin waye xan Shi’ar ya naqalto cewa, Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya yanke hannun hagun varawo. Ya faxa masa asalin maganar da isnadinta. Mu dai mun bi diddigin littafan masana tarihin musulunci na haqiqi, amma ko misali mislin wannan magana babu a ciki. Kai! Ko malaman da suka shahara da tattara wandararrun maganganu (al-ikhwabat) basu naqalto wannan magana ba. Su ne kuma gaba-gaba a fagen jinjinawa Abubakar da ganin girmansa *Raliyallahu Anhu* .

## 2.36 Aliyu Mai Wuta Aljihu

Xan Shi’ar ya ci gaba da cewa: Wani abin kunya kuma da Allah waddai da Abubakar ya yi, wai shi ne qone Fuja’atis-salami da ya yi a wuta. Alhali Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya hana horo da wuta.

**Martani:** Idan dai har qone wanda ya cancanci qonewar, kunya ne da Allah waddai to Ali *Raliyallahu Anhu* ya fi cancanta da qunyar. Don shi ne mai wuta aljihu a jerin Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* Domin kuwa akwai ingantattar magana da ke tabbatar da cewa ya qone wasu mutane masu yawa daga cikin Shi’ah Gullatu. Harma da labarin haka ya kai kunnen xan Abbas, Sahabin yayi Allah waddai dashi har ya ce: Da nine shi, ba zan qone su a wuta ba. Saboda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya hana yin azaba da abin da Allah ke azaba dashi. A maimakon haka sai dai in sare kawunansu. Saboda cewar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi: ku kashe duk wanda ya canza addinin sa.

Da wannan magana ta kai kunnen Alin, Sai ya ce: kash! Yanzu xan Ummul-fadhli zai yi wannan magana?!

Ka ga kenan Ali *Raliyallahu Anhu* shi ya fi dacewa da wannan suka da xan Shi’ar ya yi wa Abubakar *Raliyallahu Anhu* Don shi ne ya qone dubban jama’a da wutar dake aljihunsa. Idan kuwa har ‘yan shi’a za su iya shafe shi da mai su haxe tattare da haka, to kuwa Abubakar *Raliyallahu Anhu* yafi cancanta su fara shafawa suhaxiye. Domin kuwa kowanensu ya xauki matakin da ya xauka ne, a matsayinsa na shugaba mai wuka da nama.

## 2.37 Barewa Ba Ta Gudu Xanta ya yi Rarrafe

A nan kuma xan Shi’ar ya soki lamarin Abubakar Siddiqu *Raliyallahu Anhu* da cewa, wai masaniyar da yake da ita da hukunce-hukuncen shari’a ba ta taka qara ta qarya ba.

Ga abin da yake cewa: mafi yawan hukunce-hukuncen shari’a sun gagare shi (Abubakar) sani; don bai san hukuncin kalalah ba. Don riwaito shi (Abubakar) da kansa yana cewa: A kan abin da ya shafi kalalah, sai dai in faxi

ra'ayina kawai. Idan nayi muwafaqa, to nufin Allah. Idan kuma na kuskure to sharrin sahaixan ne.

Xan Shi'ar ya ce: saboda haka ne, sau saba'in yana bawa kaka haqqin kalalah. Ka ga wannan, na nuna tatatarsa(Abubakar) a faqon dimi.

Ka ji kai!

**Martani:** ko shakka babu, wannan magana qarya ce hamshaqiya.

Da gaskiya ne Abubakar ya jahilci mafi yawan hukunce- hukuncen shari'a, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba zai ba shi damar yin fatawa da Alqalanci a gabansa ba, ba tare da kuma ya ba wani Sahabi irin wannan dama ba. Har kuma ya kasance yana shawara da ganawa da shi fiye da kowa daga cikin Sahabbai, Umar na rufa masa baya.

Abubakar *Raliyallahu Anhu* nefa, da yawa daga cikin malamai, irin su: Mansur xan Abdul Jabbar as- Sam'ani da wasunsa, suka riwaito cewa kan malamai ya haxu a kan kasancewarsa mafi ilimi a cikin wannan al'umma. Wannan kuwa tabbas ne. Domin kuwa a lokacin halifancinsa, babu wata mas'ala da musulmi za su shiga tajin- tajin a kanta, face ya walwale masu zare da abawarta. Ta hanyar amfani da iliminsa da kafa masa hujjoji daga cikin Alqur'ani da sunna.

Misalin wannan shi ne irin yadda ya tabbatar masu da rasuwar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*; ya ceci imaninsu, ta hanyar kafa masu hujja da ayar Alqur'ani. Sannan ya bayyana masu inda ya kamata a yi wa Manzon makwanci. Ya kuma wayar masu da kansu a kan halacci da wajabcin yaqar waxanda suka hana zakka. Wanda kafin haka har ruxani ya kama Umar *Raliyallahu Anhu* shi ne kuma, a taron da aka yi a saqifafatu Bani Sa'idu, ya tabbatar wa Sahabbai da cewa: lallai idan ba Quraishawa aka danqawa halifanci ba; kowa an kaba shi da sakal. Wannan, a yayin da wasu kejin cewa ana iya bayar da shi ga waxanda ba Quraishawa ba. Ko ma sune suka fi su cancanta da haka.

Wannan kenan. Kuma ai da Abubakar *Raliyallahu Anhu* jahili ne, da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai waqiltar da shi ga aikin hajjin farko a tarihin musulunci, daga birnin Madina ba. Ka kuwa san mas'alolin aikin hajji sune mas'aloli mafi sassarqiya a cikin mas'alolin ibada. Da kuwa bai naqalcesu nakalta ba, ba abin da zai sa Manzon ya shugabantar da shi a ibadar. Haka kuma waqilcin daya sa shi na limanci. Ka ga shi ma ba a sa jahili. Ta kuma tabbata cewa shi ne kawai Sahabin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya waqilta ga jagorancin aikin hajji da limancin salla.

Bayan wannan kuma. Littafin da Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya wallafa a kan sanin makamar zakka, shi ne littafi mafi inganta a wannan hauji. Shi ne kuma wanda Anas ya karva daga hannunsa. Shi na kuma madogarar malaman fikhun musulunci a kan sha'anin zakka. To in ji.

A taqaice babu wanda zaice ma, komai iliminsa, ga wata mas'ala ta shari'a da Abubakar *Raliyallahu Anhu* yaci tuwon gigi a cikinta, kamar yadda wasu Sahabbai suka ci.

Za mu yi wannan magana idan lokacin ta yayi.
Ita kuwa cewar da xan Shi'ar yayi, wai Abubakar bai san hukuncin kalala ba. Saboda haka ne yayi amfani da ra'ayinsa...

To sai muce: ai barewa bata gudu xanta yayi rairahe; A matsayin Abubakar *Raliyallahu Anhu* na xan hannun daman Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma babban almajirin makarantarsa, hukuncin kalala ya yi masa kaxan.

Amfani da ra'ayinsa da ya yi a cikin wannan hukunci, na daga cikin abubuwan dake nuna zurfin iliminsa. Kuma haka ne tasa junhurun malamai suka karvi ra'ayin nasa da hannun biyu- biyu, ba yan rasuwarsa, a matsayin tsayayyen hukunci a kan al'amarin kalalah; wato wanda ba yada mahaifa ko 'ya'ya raye.

Kuma amfani da ra'ayi (hasashe) a cikin hukuncin shari'a ba gare shi farau ba. Umar da Usman da Ali kansa, da xan Mas'ud da Zaidu xan Sabitu da Mu'azu xan Jabalu *Raliyallahu Anhu* duk suna amfani da hasashensu a cikin hukunce- hukunce. Kuma a duk lokacin da hasashen mutum ya dace da gaskiya, Allah zai bashi lada biyu; kamar dai irin wannan hasashe na Abubakar *Raliyallahu Anhu*. Shi ne kuma mafi alheri bisa ra'ayin da mai shi zai kafe kansa, tattare kuma da sanin qundin ladarsa xaya ce. Wato kamar dai ra'ayin da Ali *Raliyallahu Anhu* ya kafe kansa na neman tilastawa Mu'awiyah ya yi masa bai'a a matsayin halifa. Ra'ayin da a qarshe ya yi sanadiyar zubar da jini da rasa rayuka .

Eh! Ra'ayinsa ne shi kadai tallin tal. A kan haka nema aka riwaito cewa Karsu xan Ubaidu ya ce masa, kafin wuta ta kama: ina son in gane ya Ali, shin wannan ra'ayi da ka yi tsaye kyam a kansa, Umurnin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne koko dai ra'ayin qashin kanka ne? Sai ya karva masa da cewa: Ra'ayina ne dai.

Abu Dawuda da wasunsu duk sun riwaito wannan magana.
To ka ga idan har irin wannan ra'ayi daya zama sanadiyar salwantar rayuka, bai hana jama'a yarda da kasancewar mai shi halifa ba. To qaqa za'ayi da jumhurun malamai suka karva hannu biyu-biyu, kuma bai zama sanadiyar kashe ko kiyashe ba, ya zama dalilin qin yarda da mai shi, ko abin suka a kansa?!

Ita kuwa cewar da ya yi wai sau saba'in Abubakar na hukuntar da hukuncin kalalah ga kaka, maganace ta qarya Xan Shi'ar ya yi. Wadda kuma ke tabbatar da kasancewarsu ('yan Shi'ah) imaman jahilai da maqaryata.

Wannan hukunci bana Abubakar *Raliyallahu Anhu* ne ba, babu wanda ya tava riwaito shi daga gare shi.

## 2.38 Mafi Yawan Mutanen Kufa Jahilai Ne

A qoqarin wannan xan Shi'a ne, na fifita Ali *Raliyallahu Anhu* Ya ci gaba da cewa: Ina Abubakar ina imamu Ali! Ai lizami yafi qarfin bakin kaza. Imamu Ali ne fa ya cewa mutane: ku tambayeni duk abin da kuke so, kafin ku

nemeni ku rasa. Ku tambaye ni a kan duk abin da keda alaqa da sama'u. Ni kuwa in baku amsa daga nan qasa.

Xan Shi'ar ya kafa hujja a kan wannan magana tasa da cewa: Abul-Buhtari ya ce: Na ga Ali watarana a Kufa; a kan mimbari yana sanye da sillken Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na yaqi. Yana kuma rataye da takobinsa, naxe da rawaninsa kuma sanye da zobensa *Sallallahu Alaihi Wasallama* a hannu. Nan take sai ya zauna ya kware cikinsa, ya kuma cewa jama'a: ku tambayeni duk abin da kuke so, kafin ku nemi ni ku rasa. Domin haqarqarina cike suke da tarin ilimi. Kuma cikin nan nawa salkar ilimi ce. Ni ne sirrin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne ya tsatsageni da ilimi; ba wahayi ne aka yi mani ba. Wallahi da za'a shimfixa mani darduma in zauna a kai. Zan iya yi wa mutanen Attaru fatawa da Attaurarsu. In kuma yi wa mutanen linjila da linjilar su. Har Allah ya hukunci Attaura da magana, tace: lallai Aliyu yayi gaskiya. Haqiqa fatawar da ya yi maku dai dai take da abin da Allah ya saukar a cikina. Amma kuka kasa ganewa sai kace ba ku karanta al-qur'ani?!

**Martani:** Ba musun cewa, Aliyu ya ce: ku tambaye ni. Amma ai yana magana ne da mutanen Kufa. Kamar yadda riwayar ta nuna. Ya kuma ce masu haka ne,don su cika shi da tambayoyi, har yayin amsa su, shi kuma ya cika su da ilimin Addini , saboda mafi yawansu jahilai ne; ba suyi tozali da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Amma ka ga mutanen da ke kewaye da mimbarin Abubakar *Raliyallahu Anhu* sune manya - manyan Sahabban Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* waxanda kuma suka sha suka ya tatil da ilimi mai kabri na addini a hannun manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* wanda hakan ta sasu kasance mutane mabiya ilimi da kishin addini a cikin wannan al'umma.

A yayin da waxancan mutane da Ali *Raliyallahu Anhu* ke waccan magana dasu ya ku bayi ne, tabi'ai kawai. Kuma mafi yawansu ashararu ne ko a cikin tabi'an. Wanda hakan ta sa Alin kodayaushe yake yawan kuka da su, tare da xebe masu albarka. Hakan tasa aka wayi gari tabi'ai daga cikin mutanen Makka da Madina da Sham da Basara suka fisu nagarta.

Sannan kuma idan xan Shi'ar ba yada labari: Ai matsayin kowane daga cikin waxannan halifofi huxu a fagen ilimi ba abu ne voyayye ba. Domin kuwa malamai a wancan lokaci da sauran almajiran ilimi, sun hada hancin fatawowi da hukunce- hukuncen da kowane xaya daga cikinsu yayi. Qarshe dai aka jinjina na kowane, sai aka taras da cewa na Abubakar *Raliyallahu Anhu* sun fi haxuwa. Wanda hakan ke nuna irin yadda ya yi wa sauran fintinqau a fagen ilimi.

Bayan na Abubakar sai na Umar suka biyo baya *Raliyallahu Anhu* kuma shi ne dalilin da ya sa xan takin saqar da ake samu tsakanin fatawowin Umar da na Abubakar, idan aka xorasu akan ma'aunin nassi, bai taka qara ya qarya ba. Idan aka yi la'akari da yadda kodayaushe na Ali ke yin yamma a lokacin da na Abubakar xin *Raliyallahu Anhu* suka yi gabas maxauka lada. Da wuya

matuqa a samu wani nassi da yaqi amincewa da wata fatawa ko wani hukunci da Abubakar *Raliyallahu Anhu* yayi.

Kuma ai Xan Shi'ar sanine bai yiba. Abubakar *Raliyallahu Anhu* ne wanda kodayaushe ke warwarewa waxannan Sahabbai (halifofi) zare da abawa duk wata mas'ala mai rikitarwa. Ba a kuma tava samun wanda ya tava bijire masa a kan haka ba, tsawon rayuwarsa. Sai bayan rasuwarsa ne aka fara jinsu, ana kuma ganin su rana a kan hukunce-hukunce. Don mai kwance daragar, Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya kwanta dama.

Wannan kenan. To amma cewar da ya yi wai Ali *Raliyallahu Anhu* zai yi wa mutanen Attaura da Linjila hukunci da littafansu, magana ce da ke son nazari. Domin kuwa abu ne sananne kuma tabbatacce cewa al-qur'ani da hadisi da ijma'i sun haramta yin hukunci tsakanin Yahudawa da nasara; wa-su-wa-su sai da abin da Allah ya saukar wa Muhammadu. Ko da kuwa hukuncin bai yi daidai da abin da ke cikin littafin nasu ba.

To ka ga ashe kenan duk wanda ya ce Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi waccan magana, har ya kwarzanta shi da ita. Ko dai ya kasance qaton jahilin addini. Wanda kuma bai san abin da kamata a ajinginawa lamirin Ali *Raliyallahu Anhu* a matsayin yabo. Ko kuma ya kasance zindiqi ne., da ya yi nufin sukar lamarin Alin. Ta hanyar jingina masa wannan magana da ke jawa wanda ya yi ta zargi da azaba maimakon yabo da lada.

## 2.39 Girma Ya Kai !

An dai gama ta xan Shi'ar nan ya cimma gavar abin da yake son tabbatar. Don ga shi yaba Ali *Raliyallahu Anhu* muqamin "shafe zane" ta hanyar amfani da wani qagaggen hadisi:

Bari ka ji abin da ya ce:

Wai baihaqi ya riwaito, da isnadinsa daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* wanda ya ce wai: duk wanda yake son yaga Adamu a cikin rigarsa ta ilimi da Nuhu a cikin rigarsa ta tsoron Allah, da Ibrahim a cikin rigarsa ta haquri, da Musa a cikin rigarsa ta kwarjini, da Isa a cikin rigarsa ta ibada, to yakalli Aliyu xan Abi Dalib. Wai Allah ya tarkata masa duk waxannan siffofi da ya rarraba wa waxannan. Annabawa

Ka ji kai. Lalle girma ya kai!

**Martani:** kafin komai muna son muja hankalin xan Shi'ar a kan cewa fa, ya manta ya ambaci isnadin wannan hadisi. Kuma idan bai sani ba Imamul-Baihaqi kan riwaito raunana, kai harma da ka gaggun hadisai, a kan abin da ya shafi falaloli. Kamar dai yadda takwararorinsa ma'abuta ilimi suka al'axanta.

Sannan abu na biyu: ko shakka babu wannan hadisi qarya ce aka yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kamar yadda ma'abuta ilimi suka tabbatar. Saboda haka nema duk da irin kwaxayin da suke dashi ga tattara darajojin Ali *Raliyallahu Anhu* ba su riwaito wannan hadisi ba.

Ka ga nisa'i, a cikin littafinsa mai suna: "Al-khasais", da Tirmizi a cikin tarin hadisan daya ambata a kan darajojin Ali, duk da kasancewar akwai masu

rauni da qagaggu a cikinsu. Amma duk basu ambaci wannan hadisi da makamancinsa a cikin ayyukan nasu ba.

### 2.40 Ba Dai A Madina Ba

Bayan wannan kuma sai xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: kuma Abu Umar Az-zahidi ya ce: Abu Abbas ya ce: Ba musan wani daga cikin Sahabbai ba, da ya bugi qirji saboda tarin iliminsa, ya ce wa musulmi, bayan Annabi ya kaura: ku tambaye ni duk abin da kuke so; na tun daga zamanin Annabi shisu har zuwa zamanin Annabi Muhammadu. Sai Ali *Raliyallahu Anhu* kuma a kan wannan dama ce da ya bayar, manyan Sahabbai irin su Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* da makamantansu, suka dinga yi masa ruwan bama - baman tambaya, yana ba su amsa, har ya shaqe su. Sannan ya ce: ya kai Kumailu xan Zayyad, ka sani tsatsage nake da tarin ilimin da, da zan sami mazaken qwarai da ke iya xaukar sa, da anga abu.

**Martani:** Wannan magana ba ingantatta bace. Domin kuwa ko shi Sa'alabu wanda ya riwaito ta asalatan bai ambaci isnadinta ba, balle ta cancanci zama abin kafa hujja. Kuma hasali ma, Sa'alabu baya cikin malaman da suka san kabli da ba adin hadisi, balle ya iya gane gangariyarsa da mai sanqara. Wanda hakan za ta iya ba wani damar iya bugun qirji ya ce: hadisi kaza ya inganta a wurin Sa'alabu. Kamar yadda ake iya yin garkuwa da riwayar Ahmad ko Yahya xan Mu'inu ko Axuwa uba Buhari, da matara kama da su.

To ko waxannan malaman, da makamantansu daga cikin waxanda suka yi malin sa'alabu a wannan fage. Kan ambaci hadisan da ba su da tushe. Balle makama, a cikin ayyukansu, balle shi. Muna iya yi wa Sa'alabu uzuri domin wannan magana, ya riwaito tane daga bakin irin mutanen nan da suka kware a fagen halin hankaka, na mayarda xan wani nata; don ba sukan ambaci sunayen waxanda suka samo magana daga gare su ba.

Wannan kenan. To kuma tafi, mu xauka cewa gaskiya ne Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi wannan magana. To ba ko a Madina ba; daidai lokacin halifancin Abubakar ko Umar ko Usmanu *Raliyallahu Anhu* Ali *Raliyallahu Anhu* ya na da dama da sararin faxin haka amma a Kufa, lokacin da yake halifa. Don hakan ta zama wani qarani da salon jawo hankalin mutanenta zuwa ga qaratu da neman sanin duk abin daya kama ce su sani, daga wurinsa. Saboda asalatan su mutane ne masu tsananin ragganci da kasawa fagen neman ilimi.

Wani abu dake qara tabbatar da ingancin wannan fixa da muka yi wa wannan magana, shi ne, kasancewar kumailu nan tabi'i. Bai yi tare da Ali *Raliyallahu Anhu* ba sai a Kufa. Ka ga wannan na tabbatar mana da cewa leke su da Ali *Raliyallahu Anhu* yayi; ya gama fahimtar kasawarsu a fagen ilimi tasa ya yi waccan magana. Ko alama Ali *Raliyallahu Anhu* ba zai 'iya buxa baki ya fadi irin wannan magana a cikin Muhajiruna da Ansaru ba. Allah ya daxa yarda da su, amin.

Sannan kuma cewa Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya tava tambayar Ali *Raliyallahu Anhu* wani abu na ilimi wala. Amma da an tsaya ga Umar *Raliyallahu Anhu* to maganar na sauraruwa. Don shi ya kan yi shawara da Sahabbai irin su Usman da shi Aliyun da Abdurrahman da xan Mas'udu matsayinsu na 'yan majalisar shawara.

Ka ga ko a haka akwai magana.

### 2.41 Akwai Abin Da Siddiqu Ya Gani

Har yau dai mutumin naku; sarkin jahilai bai gaji da xaukar zunubi ba a cikin haqqin Sahabbai. A nan kuma cewa ya keyi wai, Siddiqu ya yi wa hukuncin Allah zinbire tunda bai kama Khalidu xan Wahdu ya aika shi lahira, saboda ya kashe malik xan Nuwairatu, tattare da kasancewarsa musulmi ba. Wanda hakan har tabawa shi Khalidun damar aure matar Malikun, ya kuma yi baiko da ita a daren da tsohon mijin ta ya baqunci lahira. Kuma ma wai har sai da Umar ya jawo hankalin Abubakar xin *Raliyallahu Anhu* a kan wajabcin kashe Khalidun. amma wai saboda tsabar qin Allah, Abubakar *Raliyallahu Anhu* yayi shayulatin vangare da maganar tasa. Duk inji xan Shi'ar.

Farkon abin da za mu fara faskarawa xan Shi'ar a ka, a matsayin martani kan wannan magana shi ne: idan har akyale wanda ya kashe wani ba bisa haqqin shari'a ba, wani abin kunya da ashane ga shugabanni, to, lalle kuwa dangin Halifa Usmanu nada babbar hujja akan qayar bayan da suka tayarwa Ali *Raliyallahu Anhu* akan lalle ya bimasu kaxin jinin xan'uwansu. ya kuma qi. Ka kuwa san a matsayin Usmanu *Raliyallahu Anhu* na halifa ga musulunci. Wanda kuma aka yi wa kisan gilla; bai ji bai gani ba. Darajarsa ta linka ta Maliku xan Nuwaira ta fiye da sauran yawan qasa. Amma kuma duk da haka Aliyu yaqi kashe makasansa. Wanda hakan ya zama qwaqqwaran dalilin da dangin na Usmanu *Raliyallahu Anhu* suka riqa a kan qin yi wa Aliyu mubaya'a.

To. Idan kuwa har kuna ganin akwai wani uzuri na shari'a daya hana Alin kashe maka shin Usmanu *Raliyallahu Anhu* kashe makashin maliku shi ne mafi qarfi. Idan kuwa kuna ganin cewa abubakar *Raliyallahu Anhu* baya da wani dalili a kan haka, to ko, Ali *Raliyallahu Anhu* shi ne mafi zama marashin dalilin a kan yarda wa makasan Usmanu *Raliyallahu Anhu* ci gaba da rayuwa.

Ka ga kenan a haka, ta tabbata cewa jahilci ne daya yi wa 'yan Shi'ah riga da wando, da kuma tinka da walwala, suka sa suna zargin Abubakar *Raliyallahu Anhu* tare da qorafi a kansa, a wannan 'yar kankanuwar matsala. Alhali ga wata qasaitacciyar matsala can ta kewaye Ali *Raliyallahu Anhu* amma sun sa qafa sun taushe; kamar ba a yiba. Tattare da cewa duk mai hankali da basira isassa ya san cewa, lalle akwai abin da Siddiqu ya gani.

Ba a kan Abubakar *Raliyallahu Anhu* kawai suka tsaya ba. Sun soki lamarin halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* shi ma. A kan wai yaqi kashe Ubaidullahi xan Umar saboda kisan gillar da ya yi wa Hurmuzanu.

To, duk wannan martani, ya isa kariya ga waxannan halifofi biyu masu girman daraja.

Wannan kenan. To idan kuwa har 'yan Shi'ah za su yi qarfin halin ce mana: To ai Ali *Raliyallahu Anhu* nada Uzuri a kan rashin kashe makasan Usmanu, kamar yadda muka qaddara yiwuwar su ce. Qarshe kuma suce mana uzurin kuwa shi ne: Rashin cikar sharuxxan dake wajabta qisasi; koko a'a, Aliyun bai san waxanda suka yi mugun aikin ba. Ko kuma ya sansu, amma sun fi qarfinsa saboda kasancewarsu buwayayyi. Ko kuma dai wani dalili mai kama da wannan.

To sai mu ce masu mu kuma: Eh! To mun ji, mun kuma yarda. Sai dai, su ma makasan Maliku da Hurmuzanu, duk babu wanda dalilan da za su wajabta qisasi a kansa suka cika. Saboda akwai shubuha (ruxani) a cikin mas'alolin nasu. Shubaha kuwa dalilice mai kwari da ke tunkuxe haddi.

Na san kuma saboda tsananin qarfin hali da kangara, suna iya sake cewa: Bawata shubuha dake ciki. Tunda har sai da Umar da Ali suka tabbatar wa Abubakar da Usmanu *Raliyallahu Anhu* rashinta, tare da wajabcin kashe makasan; wato Khalidu da Ubaidullahi. Amma suka qi.

To amsarmu a nan itace: Idan wannan na zama dalili, me ya hana Ali *Raliyallahu Anhu* kashe makasan Usmanu, tunda har sai da Xalhatu da Zubairu da wasu Sahabbai suka tabbatar masa da wajabci da yiwuwar haka? Me ya hana shi?

Kuma aje ma duk wannan. idan tonon silihi kuke so a yi, bisimillah...!

Kun mace cewa, Abubakar *Raliyallahu Anhu* bai kyale waxanda suka ba shi shawarar kashe khalidu haka nan ba; sai da ya kafa masu hujjar da ta gamsar da su, da cewa: qisasi bai wajabta kan khaladu. Saboda abu ne mai yiwuwa qwarai ya kasance a kan haqqin Allah na ya kashe Malikun. Saboda a mafi rinjayen zato dakare kuma barden musulunci irin Khaladu, ba zai kashe musulmi haka kaxai ba; saboda haka lalle ne akwai wani ijtihadi daya dogara a kansa, kafin ya aika shi lahira.

Amma rashin gamsuwar da Ali *Raliyallahu Anhu* yayi da waxanda su ka ba shi shawarar kashe makasan Usmanu, mummunan yaqi ta haifar tsakaninsu. Wanda muninsa yafi na kisan da aka yi wa Usmanu. Kowa yasan irin nauyin abin da ya faru a yaqin sibbaini da Jamalu.

To idan kuwa har za'a iya yi wa Ali uzri a nan, to yi wa Abubakar *Raliyallahu Anhu* uzuri a can shi ne mafi cancanta da dacewa. A matsayinsa na waxanda suka dogara a kan wani karvavven ijtihadi.

Na daxe da sanin cewa 'yan Shi'ah na iya izgilin cewa, maganar kisan gillar da aka yi wa Usmanu, ba wata matsala bace, domin jininsa halattace ne. Saboda yadda ya tozartar da alfarmar dukiya da halifancin musulunci.

To, harwayau dai. Mu qaddara cewa waxancan abubuwa sun halatta jinin Usman xin *Raliyallahu Anhu* Amma babu mai hankali da musun cewa jinin Maliku xan Nuwairatu yafi cancanta da halatta. Domin kuwa, hasali babu

wanda ke iya tabbatar da rashin cancantar Malikun da wancan kisa da khalidu ya yi masa ta fuskar shari'a; mu dai a wurinmu babu wannan dalili.

Amma halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* dalilai da nassosa daga cikin al-qur'ani da sunna sun tabbatar da cewa kisan da aka yi masa zalunci ne. Kuma kowa ya san fifikon da Usmanu yake dashi a kan xan Nuwairata, Allah kadai ne ya san iyakarsa.

Kuma babu ta yadda za a yi wanda ya halatta jinin Usmanu, ya iya haramta na Ali ko Husaini *Raliyallahu Anhu* Domin kuwa dalilan dake tabbatar da haramcin jininsa sun fi qarfi da bayyana bisa waxanda ke haramta nasu. Abubuwan da ke kaiwa ga sa a zubar da jinin mutum, qalilan ne matuka a cikin al'amarin Usmanu, idan sha'anin Ali da Husaini *Raliyallahu Anhu* kuma ruvavvun dalilan da makasan Usman suka lave bayansu, sun fi waxanda makasan Ali da Husaini suka lave bayansu nuqa da ruva.

Fara lissafi.

Ka ga dai halifa Usmanu bai kashe musulmi ko xaya ba. Bai yaqi kowa a kan rashin yi masa muba a ba; ko niyar haka bai kulla ba. Mu tsaya ma anan.

To ka ga renin hankali da ilimi ne, a ce wanda ya shaya daga da musulmi don neman shugabanci, jininsa haramtace ne. Don abin can da ya yi ijtihadi ne. Amma wanda bai yaqi ko sauro ba, a ce jininsa ya halatta, ko shakka babu Usmanu *Raliyallahu Anhu* shi ne mafi cancanta da kasancewa mai haramtaccen jini, kuma mujtahidi a cikin irin yadda ya riqa dukiya da halifancin al'umma.

Wannan kenan. Sannan kuma mun yarda da cewa jinin Malilku xan Nuwairata haramtacce ne asalatan. Amma khalidu ya halatta shi a kan wani tarihi, har ya aika shi lahira. To ai, wannan ba komai ba ne balle har ya halatta ko wajabta kashe khalidun.

Ah! Kun manta da Usamatu xan Zaidu ya kashe wani mutum a wurin yaqi, bayan ya furta kalamar shahada. Har Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ga laifinsa;. Ya ce: ya zaka kashe mutum bayan ya ce: La'ilaha illal-lahu?. Ya maimata haka ga Usama har sau uku.

Amma duk da haka Annabi bai nemi Usama da biyan wata diyya ko kaffara ba a kan haka, balle ramuwa, tunda ya yi kisan ne a kan wani tawili. Ya kuma yi nadama a qarshe.

Sannan zancen auren matar Maliku da yin bai ko da ita a daren da yabar duniya, da shi Xan Shi'ar ya ce khalid yayi, magana ce da bata inganta ba. Ko da kuma Allah yasa ta ingantan, to babu wani dalili da zai wajabtar da haddin jifa a kansa. Domin kuwa malaman fiqihu sun qara wa junansu ilimi ta hanyar kasuwa gida biyu a kan wajabcin iddar mutuwar miji kafiri tantagarya ko na tawili. Wasu suka ce wajibi ce, wasu suka ce ba wajibi ba ce. Kamar yadda ta faru tsakaninsu a kan wajabcin iddar a kan zawariyyar da mijin ta ya rasu. Sabanin iddar saki, wadda take wajabtarwa. Ita kan babu wani ka-ce-na-ce a kanta. Lalle ne sai an tsalkake mahaifa kafin ayi wani aure.

Amma ita iddar mutuwa, ta na wajabta ne, daga lokacin da aka tofa fatiha anka daura aure. Amma da mijin zai mutu a dai - dai lokacin da kuma yake kafirta asalan, iddar na ci gaba da zama wajibi kan matar ko qaqa? A nan ne malamai suka xan wasa kwakwalwa. Kamar yadda suka yi akan wajabcinta kan matar da irin wannan miji yayi baiko da ita bayan xaurin auren kuma ta yi wanki xaya bayan haka.

To amma idan qaddarar ridda ce ta fada masa, sai kuma ga mutuwa kwaram. A mazhabar Shafi'i da Ahmad da Abu Yusuf da M uhammad za ta yi idda, amma ba ta wadda mijinta ya rasuba, ta dai wadda aka rabu da ita, rabuwa ba'ina. Saboda aure na vaci da zarar miji yayi ridda. A wurin Shafi'i da Ahmad kuwa irin wannan rabuwa da ke faruwa saboda ridda, ba a ce mata saki. Saboda haka ne ma suka qi wajabtawa matar iddar rasuwa, sai dai ta rabuwa ba'ina.

Idan kuma dama bai yi baiko da ita ba, ya rasu to ba kowace irin idda a kan ta, a wurinsu. Kamar yadda ba zata yi iddar ba ko da sakin ta yayi, matukar dai bai .kusance ta ba.

Amma irin waccan rabuwa ta mutuwa, kamar rabuwa ce ta saki a wurin Maliki.

To, idan har ka fahimci wannan qullin makodo na malaman fikhu, zaka yarda da cewa lalle akwai abin da Siddiqu ya gani ya qi kashe khalid. Domin kuwa bai kashe maliku ba sai da ya gama yanke masa hukuncin ridda. Ka ga idan har anyi sa'a bai kusanci matar ba, shi Maliku. To ba za tayi wata idda ba, a matsayin gaba xayan malamai. Idan ma har koya kusance ta, to wanki xaya ya isa tabbatar da tsarkin mahaifarta, da ba dole sai ta yi cikakkar idda ba, bisa xayan zancen malaman; wanda xayan sun ke wajabta mata wanki uku.

Idan kuwa asalatan kafiri ne, matar ba za tayi idda saboda mutuwar sa ba, bisa xayan zancen waxannan malamai. Idan kuma har tsarkin mahaifar tata ba zai tabbata ba, sai idan tayi wanki bayan mutuwar mijin, to haka ba zata wajabta akan taba, sai idan ta tava wanki kafin baikon.

A haka ma, akwai malaman da ke jin wani sashe na kwanakin wanki ya isa tabbatar da tsarkin mahaifa.

A ta kaice dai mu a iyakar saninmu, duk yadda aka kixa kuma aka raya, ba yadda za a yi wannan mas'ala ta kasa karvar sallamar ijtihadi karvavve a idon shari'a. Kuma sukar wani da irin wannan al'amari xabi'a ce ta jahilai. Kuma abune da Allah da Manzonsa suka haramta.

### 2.42 Gadon Fatima Da Laqabin "Halifa"

Daga nan kuma sai xan Shi'ar ya ci gaba da cewa wai: kuma Abubakar ya savawa umurnin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* tunda har ya hana Fatima gadon mahaifinta, da Fadak. Kuma ya qaqabawa kansa laqabin "halifatu Rasulullahi" alhali ba Annabin ne ya zave shi halifansa ba.

**Martani:** Bari mufara da matsalar gadon Fatima. Wannan batu mun riga munyi magana a kansa. Mun kuma tabbatar wa duniya da cewa matakin da

Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya xauka a kansa shi ne madaidaici. Wanda saboda haka ne ma gaba xayan musulmi suka marawa baya a kai, in ban da wasu ‘yan Shi’ah. Haka kuma mun tabbatar wa ku da cewa matsayin nasa hukunci ne da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi. Kuma abin da ‘yan Shi’ah nan ke yayatawa a kan wannan matsala, da ta Fadak, babu gaskiya a cikin ko kaxan.

Kuma halifancin da suka biyo bayan Abubakar *Raliyallahu Anhu* babu wanda ya tayarda wancan hukunci nashi. Kuma babu wani abu; ko da kwatankwacin Allura, da Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* suka xaukar wa kansu, ko suka ba iyalinsu daga Fadak xin, balle a ce. Kuma Fadak ba kome ba ce, idan aka yi la’akari da irin abin da waxannan halifofi suka mallaka wa Banu Hashim.

Kuma yau da wani daga cikin musulmi zai yi qorafi, da kafa hujja da cewa, ai Ali *Raliyallahu Anhu* ma ya hana wa xan Abbas da sauran Bani Hashim ko sisi daga cikin Baitil mali, har hakan ta sa xan Abbas xin ya dahe wasu kuxaxe a Busra yasa su mala. Na san ba abin da za kuce, a qoqarin bawa Alin kariya illa cewa, ya yi haka ne saboda tabbatar da gaskiya da riqon amana, a matsayinsa na shugaba adili; saboda haka bai kamata a zarge shi ba.

To ku sani Abubakar *Raliyallahu Anhu* shi ya fi dacewa da cancanta da irin wannan kariya. Domin kuwa son da yake yi wa Fatima da qoqarin tsare alfarmarta, sun fi waxanda Aliyu *Raliyallahu Anhu* ke yi wa xan Abbas. Kuma matakin da xan Abbas ya xaukarwa Aliyu *Raliyallahu Anhu* na nuna kasancewarsu qare ba a tsaga ba. Savanin Fatima ga Abubakar *Raliyallahu Anhu*. ko alama abin arzikin da ke tsakanin Ali da xan Abbas, bai kai wanda ke tsakanin Abubakar da Fatima ba *Raliyallahu Anhu*.

Shi kuwa laqabin “Halifa” da xan Shi’ar ya ce wai, Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya qaqalawa kansa, qaryar banza ce. Duk wanda ya san tarihin musulunci yasan cewa musulmi ne suka yi wa shi wannan laqabi a qaran kansu.

Kuma idan kalmar “Halifa” na nufin wanda anka halifantar, kamar yadda maganar xan Shi’ar tazo, to ai cewa Abubakar *Raliyallahu Anhu* halifa ba laifi bane, don Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne da kansa ya halifantar dashi. Kamar yadda Ahlus-Sunnah suka yi imani. Idan kuwa kalmar na nufin wanda ya maye gurbin wani, ko da shi wanin bai yi umurni da hakan ba. kamar yadda jumhuru suka yi imani, to ai kuma babu sunan da ya kamata a ambaci Abubakar xin da shi in ba “Halifa” ba *Raliyallahu Anhu* .

Wannan ma’ana ta biyu kuwa, itace abin da Alqur’ani da sunna ke tabbatarwa. Bari ka ji. Allah Ta’ala na cewa: Sannan muka sanya ku masu mayewa (halifa) a cikin qasa daga bayansu, domin muga yaya kuke aikatawa (10:16).

## 2.43 Ya Kuma Dira A Kan Umar

Bayan kuma da wannan xan Shi'ar ya gaji da cin mutun cin Abubakar *Raliyallahu Anhu* sai ya dira a kan Umar *Raliyallahu Anhu.*

Ga alama haka zai bi manyan halifofi xaya bayan xaya.

Farkon abin da ya fara da shi, shi ne cewa wai; Daga cikin abubuwan dake tabbatar da cewa halifofin nan uku ba kowa bane, a wurin Allah, akwai abin da aka riwaito a cikin littafin: "Hilyatul-auliya'u". Marubucin littafin; Abu Nu'aimi al-Hafiz ya ce wai anji Umar na cewa, a lokacin da ya kai gargara: kaicona ina ma dai rago Allah ya yi ni, daga cikin ragunan dangina. Su yi ta kiyona har kitse ya rufe mani qoda. Qarshe su yanka ni liyafa ga mafi soyuwa daga cikin baqinsu. Su soya rabin namana rabi kuma suyi romo. A taru ayi mani kaf, in zama turoso ba mutum.

Xan Shi'ar ya ce: To ka ga wannan magana ta Umar, wai tayi dai - dai da ta kafircin da zai buxa baki gobe lahira ya ce: kaitona dama dai na zama turxaya (79:40).

Daga nan kuma sai ya koma kan xan Abbas, ya ce wai shima ya ce, a lokacin da ya kai gargara: wallahi dana mallaki zinarin da ya yi yawan qasa da na bayar dashi, don in tserewa tashin hankalin ranar lahira.

Mutumin naka ya ce ita kuma wannan magana wai dai - dai take da cewar da Allah Ta'ala ya yi: kuma da waxanda sukayi zalunci suna da abin da ke cikin qasa gaba xaya, da misalinsa a tare dashi, lalle da sun yi fansa dashi daga mummunar azaba (39:47).

Sannan ya ce: To don Allah muna son masu hankali su dubi waxannan maganganu, na waxannan mutane biyu, su kuma auna su dacewar da Ali *Raliyallahu Anhu* yayi:

- "Wai yaushe ne mutuwa zata xauke ni, in sadu da masoyana;... Muhammadu da rundunarsa.
- Wai yaushe ne zan yi tozali dasu ... in kuma ga yadda za a yi tawayya da marasa arziki daga cikinsu"

Da kuma kalimar da ya yi a lokacin da xan Muljamu ya xora shi kan godaben zuwa lahira wadda ya ce:

- "Wallahi na taki sa'a"

Wato xan Shi'ar naso ne ya ce, Umar kafiri ne. Xan Abbas kuma azzalumi ne *Raliyallahu Anhu.* wal'iyazu Billahi.

Martanin mu a kan wannan magana shi ne; ko alama wannan zance bai kai lasaba kuma wata alama ce, da ke nuna kabrin jahilcin xan Shi'ar. Domin kuwa ba Aliyu *Raliyallahu Anhu* ne aka tava jin ya furta irin waxancan kalmomi dake nuna jaruntaka da rashin fargaban zuwa lahira ba. Wasu Sahabbai da ba su kai darajar sa, balle ta Abubakar ko Umar ko Usmanu *Raliyallahu Anhu* har ma da wasu daga cikin masu kafirta Alin, daga cikin Harijawa, sun furta irin waxancan kalmomi.

An riwaito cewa Bilalu, Sahabin da Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya yi wa hidima da karimcin "'yanci", an ji yana yin aras da matarsa, a lokacin da ya kai gargara. Hankalinta ya tashi tana cewa: yau mun shiga uku mun lalace!. Shi

kuwa yana cewa: can gareki ni kam farin ciki nake yi. Gobe zan haxu da masoyana; Muhammadu da rundunarsa

Bilalu kenan. Sahabin da Umar *Raliyallahu Anhu* ya yi wa "Allah ya isa" shi da wasu Sahabbai, saboda sun fitine shi, a kan lalle sai ya raba ko rayen tuxxan Iraqi ga mayaqa. Shekara kuwa bata zagayo ba sai da Allah ya karvi rayuwarsu gaba xaya.

Amma ka ji kalmomincan da Ali *Raliyallahu Anhu* ya furta basu fi waxannan da shi ya furta zaqi da qarfi ba.

Wani kuma abu dake qara tabbatar da cewa, ba Ali *Raliyallahu Anhu* ne farau a irin wannan baiwa ba shi ne abin da Abu Nu'aimi xin ya riwaito a cikin wanna littafi nasa "al-Haya" inda ya ce: kudai'i da Hasan xan Abudullahi da Amir xan Sayyaru da Abudul-Hamid xan Hushub, daga Abdur-Rahman xan Ganami, daga kuma Harisu xan Umairin, wanda ya ce: watarana an soki Mu'azu da Abu Ubaidata da Shuraihabilu xan Husnata da Abu Malik al-Ash'ari, a wurin yaqi. Sai Mu'azu ya ce: Ai wannan ba abin mamaki ne ba. Wannan suka da aka yi mani a rana xaya, muna kuma dangin juna, wata rahama ce daga wurin Ubangijinmu, wadda Annabinmu ya roqar mana. Kuma nagartattun bayi waxanda suka gaba cemu suka ce"Amin" a lokacin da Annabi ya ce: ya Ubangiji ka yanka wa mutanen gidan su Mu'azu babban rabo daga cikin irin wannan rahama.

Mu'azu Ya ci gaba da cewa; marece na gaba dayi, bayan wannan adu'a sai kuwa aka kaiwa xana Abdur-Rahmanu Bikrah; xaya daga cikin 'ya'yana da nafi so, suka. Ina dawowa masallaci na same shi murtut da fuska, yana cikin zilla. Na ce masa me ya faru ne Abdurrahman? Sai ya ce: Bari baba. Gaskiya ta tabbata daga Ubangijika, kada kuma ka zama cikin mutane masu ruxani.

Sai ni kuma nace masa: Ni kuwa da yardar Allah zan kasance daga cikin mutane masu haquri.

Mai riwaya Ya ci gaba da cewa: Haka Mu'azu Ya ci gaba da rungume wannan xa nasa, har zuwa lokacin da ransa ya fita. Safiya nayi aka yi jana'izarsa.

Anan kuma shiga ta kawo ga Mu'azu, shi ma aka soke shi. Ya shiga cikin wani irin magagi; ransa na zuwa yana dawowa. Amma hakan ba tasa ya fita hayyacinsa har yamanta da Allah. Duk lokacin daya farko za a ji yana cewa: Ya Ubangiji! A shirye nake mutuwa ta xauke duk lokacin daka shata. Kuma ka sani, wallahi ina matuqar son ka, har cikin quryar xakin birnin zuciyata.

Mu'azu kenan.

Haka ita ma cewar da xan Shi'ar yayi Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce: "wallahi na taki sa'a" ba gare shi farau ba. An riwaito cewa Amiru xan fuhairiyatu; barwan Sahabi Abubakar *Raliyallahu Anhu* A wannan matsayi nasa, da bai kai na Aliyun ba. Shi ma ya faxi irin wannan kalma a lokacin da yake gab da xauke shexa, a wani wuri gab da Najdu, a sanadiyar sukuwar sallar da magabata suka yi kansa da makamai, a wannan wuri da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tura shi tare da wata runduna.

Malaman tarihi suka ce, a wurin ne wani kafiri da ake cewa Jabbaru xan Salimi, ya kai masa suka ta qarshe, wadda ta kama jikinsa sosai, ya kuma tabbata lalle tashi ta qare. To a lokacin ne ya ce: " wallahi na taki sa'a." jin haka sai Jabbaru xin ya ce: me yake nufi da wannan magana? Sai Urwatu xan Zubairu ya ce: wannan sa'a ta tabbata domin kuwa mun ga mala'iku sun halarto jana'izarsa.

Haka kuma an riwaito cewa a lokacin da aka kaiwa Shubaibu al-Hariji suka, ta kama jikinsa sosai, shi ma ya ce: Allah ka karvi wannan shahada tawa.

To ba waxannan magabata ba. Ni xin nan na san wani mutum daga cikin amitattu, wanda a lokacin daya kai gargara sai aka ji yana cewa: ya masoyina ga ni nan isowa don mu sadu.

Wannan kalami ne Ya ci gaba da maimaitawa har ransa ya fita. Irin waxannan misalai akwai su da yawa.

Sannan kuma wancan tsoro da fargaba da suka kama Umar *Raliyallahu Anhu* a lokacin gargararsa, ba wani abu hakan ke tabbatarwa ba illa tsananin tsoron Allah, wanda ke tsatsage da birnin zuciyarsa. Wanda kuma ke nuna cika da kamalarsa a fagen ilimi. Saboda Allah Ta'ala ya ce: Malamai kawai ke tsoron Allah daga cikin bayinsa(35:28)

Kuma tsoron Allah da bayyanarsa sunna ce da ta samo asali daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* Domin da yawa idan yana salla, ake jin qirjinsa na zavarvaka kamar tukunya ta tafasa, saboda tsananin kukan da yake shara.

Ita kuwa waccan magana ta Umar *Raliyallahu Anhu* da xan Shi'ar ya ce wai, daidai take da abin da kafiri zai ce gobe qiyama: Kaicona da ma turxaya aka yoni (79:40)

Wannan zumuncin da xan Shi'ar ya qulla tsakanin waxannan kalamai biyu, aiki ne irin na jahilai. Domin kuwa babu abin da ya haxa wannan magana da waccan saboda ta farko an yi tane a duniya; gidan da ake neman lahira a cikinsa. Kuma maganar na nufin tabbatar da tsoron Allah ne a cikin zuciyar Umar *Raliyallahu Anhu* ka ga kenan zai sami ladar haka daga wurin Allah. A yayin da ita kuma magana ta biyu za a yi tane a ranar qiyama; ranar da ba a karvar tuba kuma wani aiki mai kyau ba ya da wani anfani.

Ka ga ashe hanyar jirgi daban ta mota daban.

Kuma a irin wannan tafarki Sayyida Maryam tace: kaitona, da dai na mutu a gabanin wannan kuma na kasance wani abu walaqantacce wanda aka manta (19:23)

Ka ga babu mai hankali da ilimin da zai daidaita matsayin wannan gurin mutuwa da Maryam ta yi, a duniya, da wanda wani kafiri zai yi a lahira; kamar cewar da 'yan wuta za suyi goben: Ya maliku! Ubangijinka ya kashe mu mana (maliku) ya ce, " lalle ku mazauna ne (43:77) Da kuma gurin da waxanda sukayi zalunci a duniya za suyi a goben kamar yadda Allah Ta'ala ke cewa: kuma da waxanda suka yi zalunci suna da abin da ke cikin qasa gaba xaya, da misalinsa a tare dashi, lalle da sunyi fansa dashi daga mummunan azaba, a

Ranar qiyama. Kuma abin da basu kasance suna zato ba, daga Allah ya bayyana gare su (39:47)

Ka ga waxannan ayoyi suna ba mu labarin halin da waxannan mutane za su kasance ne a ciki gobe qiyama ne kawai; ranar da tuba da tsoron Allah ba su da wani amfani.

Amma a nan duniya, sanannen abune cewa, a duk lokacin da bawa yayi tsoron Ubangijinsa, to yayi ibada. Wadda kuma Allah zai bashi lada a kai, Ya kuma amintar dashi gobe qiyama. Duk kuwa wanda ya daidaita matsayin wannan tsoron Allah da wancan, to, daidai matsayinsa yake dana wanda ya daidaita matsayin haske da duhu, ko inuwa da rana, ko na rayayyu da matattu.

## Sayyidina Umar:
## 2. 44 Umar: Mai Gani Da Hasken Allah

A wani yunquri kuma da xan Shi'ar yayi na bice haske da martabar Umar *Raliyallahu Anhu*, sai ya xauko zancen rubuta wasiyya, a matsayin makami, inda ya ce: Mawallafan ingantattun littafan hadisan na shida, sun riwaito daga Musnadin xan Abbas, wanda ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya nemi Sahabbai, a lokacin da yake jinyar ajali, dasu kawo masa alqalami da farar takarda don ya rubuta masu abin da idan suka yi riqo da shi, ba za su vace ba a bayansa. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na bayar da wannan umurni, sai Umar ya ce: ina sa ran magagin mutuwa ne ya kama shi. Kuma ai littafin Allah ya ishe mu.

Umar na qare faxin haka sai wuri ya kece da hayaniya. Jin haka sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: ku watse ku ba ni wuri, bai kamata kuna rikici gaba na ba. Daga nan kuma sai xan Abbas ya ce: Amma dai ba mu ji daxin hana Manzon Allah ya rubuta mana wannan wasiyya ba.

Abu na farko kenan.

Abu na biyu kuma inji xan Shi'ar shi ne, wai a lokacin da labarin rasuwa Manzon Allah ya bazu Umar *Raliyallahu Anhu* bai yarda ba, har ya ce: Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba zai mutu ba sai ya yanke hannaye da kafafun wasu mutane. A nan ne Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya ce ya kama bakinsa, ya kuma karanta masa ayar dake cewa: lalle kai mai mutuwa ne, kuma suma lalle masu mutuwa ne (39:30) da kuma wadda ke cewa: ashe idan ya mutu ko kuwa aka kashe shi, za ku juya akan dugaduganku? (3:144)

Qare karanta waxannan ayoyi da Abubakar *Raliyallahu Anhu* yayi ke wuya, sai Umar ya ce: Na ji kamar ban tava jin su ba .

Kafin mu shiga walwale bakin zaren wannan magana a matsayin martani, bari mu fara shimfida darajojin Umar *Raliyallahu Anhu* waxanda suka tabbata a cikin ingantattun hadisai. Waxanda za su sa mai karatu ya gane matsayinsa na wanda ke gani da hasken Allah. Kuma cewar da ya yi "wata qila magagin mutuwa ne ya kama Manzon Allah" hasashe ne irin na masu ilimi da hangen nesa.

Sayyidina Umar nada darajojin da babu wanda keda irinsu daga cikin Sahabbai in ba Abubakar *Raliyallahu Anhu* ba.

Ya zo a cikin sahihu Muslimu daga Aisha *Raliyallahu Anhu* wadda ta ce: Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kasance yana cewa: An yi mutane masu kyakykyawan hasashe a cikin al'umomin da suka gabace ku. Idan akwai irinsu xaya a cikin al'umma ta, to, Umar ne.

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi amfani ne da kalmar "muhaddisuna" a cikin wannan hadisi da wanda zai biyo bayansa. Kalmar Larabci wadda muka fassara da "kyakykyawan hasashe". Mun yi haka ne ta hanyar shiga rigar arzikin malam da Wahabi, wanda ya ce: kalmar na nufin "waxanda Allah ke yi wa ilhamu".

Haka kuma Buhari ya riwaito daga Abu Hurairata, wanda ya ce Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: An yi mutane masu kyakykyawan hasashe a cikin al'ummomin da suka gaba ce ku. Idan akwai wani irinsu a cikin wannan al'umma tawa to Umar xan Haxxabi ne.

A wani matakin kuma Buhari cewa yayi Annabi ya ce: An yi wasu mutane a cikin Bani Isra'ila; waxanda suka gabace ku, waxanda ke magana ta zama kata'un, tattare kuma da cewa su ba Annabawa ba ne. Da akwai xaya daga cikinsu cikin al'ummata , to Umar ne.

Haka kuma yazo a cikin wani hadisi ingantacce hadisi daga xan Umar, wanda ya ce, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: watarana yayi mafarkin an zo mani da wata kwarya cike da nono. Na sha na qoshi, har a kaihuna suka nuna. Da na rage sai na miqawa Umar xan Haxxabi.

Sai Sahabbai suka ce: To da me ka fassara wannan nono ya Manzon Allah? Ya ce: Da ilimi.

A wani hadisi kuma sahihi, wanda aka samo daga Sa'id, wanda ya ce, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: watarana nayi mafarkin wasu mutane sanye da 'yan guntayen tagguna da basu wuce qirazansu ba. Wasu kuma nasu sun xan gota nan. Can sai ga Umar xan Haxxabi tasa rigar har tana jan kasa.

Sai Sahabbai suka ce: To da me ka fassara wannan riga ta Umar ya Manzon Allah? Ya ce: Da faxaxxiyar addini a hannunsa.

Wannan kenan. To mu koma kan asalin wannan magana kuma. Wato abin can da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yaso ya rubuta wa Sahabbai a matsayin wasiyya. Wannan abu sananne ne baga Umar kawai ba. Domin kuwa Aisha *Raliyallahu Anhu* ta faxa a cikin wani ingantaccen hadisi, cewa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce mata a liqacin da yake jinyar ajali: kira mani mahaifinki (Abubakar *RALIYALLAHU ANHU*) da xan'uwanki. Zan rubuta masu wata takarda. Don ina tsoron wani mai guri yayi guri, kuma mai cewa ya ce: Ni ne mafi cancanta. Amma Allah da muminai su qi kowa sai Abubakar.

Ya kuma zo a cikin sahihul Bukari daga Kasim xan Muhammadu, wanda ya ce: Aisha *Raliyallahu Anhu* ta xaga murya watarana tace: Boni ko zai ci

fatun lihidda! Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: idan ina raye zan yi maki istigfari in kuma yi maki addu'a. Sai tace: kaicona! Wallahi ina zaton dai kana sone in mutu. Ina tabbata maka idan haka ta faru zan ci gaba da zama rataye ga wasu daga cikin matanka. Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: kenan ni bonin zai ci ba fatun lihidda ba. Haqiqa nayi nufin in aika wurin Abubakar da xansa don in danqa masa amana. Don kada gobe wani mai faxa ya faxa ko mai guri ya gurata. Qarshe kuma Allah da muminai Abubakar za su zava.

Ka ga kenan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya riga yayi ishara da abin can da yake son rubutawa, tare kuma da bayyana dalilansa a kan haka.

Wannan darga ta qare qarau ga mai hankali. Shi kuwa Umar kokwanto ne ya kama shi a kan haqiqanin matsayin waccan magana da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi; shi yayi ta ne a sakamakon zafin ciwo da kusantowar ajali, koko yana cikin hayyacinsa?!

Wannan hasashe da Umar *Raliyallahu Anhu* yayi ba laifi ba ne. Domin tabbas Annabawa na arashin lafiya. Kuma ko ba komai halin da Manzon ke ciki ya isa tabbatar da haka. Kuma kalmar "ina sa rai" wadda ya yi amfani da ita a lafazin nasa, na nuna cewa bai yanke wa matsalar hukunci ba; a'a yana dai kokwanto da hasashe ne. Ka kuma sani Umar bai fi qarfin kokwanto ya kama shi ba, tun da shi ba Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ba, wanda Allah ya ba lasisin ma'asumanataka. Kuma wannan kokwanto daya kama shi, an yi sa'a yana wurin zama a cikin al'amarin, tunda ga Annabi kwance kuma ribxe a cikin zafin masassara. Saboda haka yayi hasashen ko zafin ciwo ne yasa shi maganar, ta yadda ake iya yin wani xan batun zucci kafin a saurareta kai tsaye. Koko karvar ta nan take wajaba, ba tare da wani nazari ba?! Kamar dai yadda ya yi kokwanton tabbacin mutuwarsa daga baya, har sai da ya gama gane lalle dai ya rasun, sannan ya miqa wuya.

Kuma ka ga cikin ikon Allah, sai abin can da Umar *Raliyallahu Anhu* ke hasashe ya tabbata. Wato abin can da manzo yaso rubutawa, ya riga ya faxawa Nana Aisha *Raliyallahu Anhu* shi. Saboda haka ne ma daya ga ruxani ya shiga tsakanin Sahabbai a kan abun, ya kuma san ko da ya nace a kan sai ya rubuta maganar, hakan ba zai kawar da ruxanin ba, tunda ya riga ya faru, sai ga fita batun hakan. Ya kuma san cewa Allah zai haxa kansu a kan abin da ya yi niyyar rubuta masun. Kamar yadda ya riga ya faxa cewa: qarshe kuma Allah da muminai Abubakar za su azaba *Raliyallahu Anhu*.

Ita kuwa cewar da xan Abbas yayi: Bamu ji daxin hana Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rubuta mana wannan wasiyya ba..... magana ce dake nuna rashin jin daxin zai tabbata cikin qirazan waxanda ba su yarda da halifancin Abubakar *Raliyallahu Anhu* ba samsam. Ko kuma suka yi shakkunta. don tabbas da rubutun ya yiwo, da abin da ya farun nan bai faru ba.

Amma duk wanda ke da masaniya da barwa Abubakar *Raliyallahu Anhu* amanar al'umma, da Annabi yayi, ba wani rashin jin daxi gare shi.

Alhamdu lillahi

Rashin jin daxi na nan ga waxanda ke zaton cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yaso ne ya rubuta cewa Ali *Raliyallahu Anhu* ya gade halifarsa kai tsaye bayan ya qaura. Kuma vattatu ne bisa haxuwar kan gaba xayan malaman sunna da na Shi'ah.

Eh! Tabbas haka wannan magana take. Domin kuwa malaman sunna sun haxu a kan cewa Abubakar *Raliyallahu Anhu* shi ne mafifici a cikin Sahabbai, kuma shi ne mafi cancanta da halifanci a lokacin. A yayin da su kuwa malaman Shi'ah, waxanda ke ganin cewa Ali shi ne mafi cancanta da kujerar a lokacin, cewa suke yi Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya riga ya daddale maganar kasancewar Alin yazama mai jiran gadon manzanci, da yankakken "nassi" tun kafin wannan lokaci na jinyar. Ka ga kenan ba bukatar wani rubutu.

To ina suka ga makama? Babu

Kuma da 'yan Shi'ah za su ce: A'a akwai buqatar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rubuta waccan naxi da ya yi wa Ali *Raliyallahu Anhu* duk da yake yayi shi ne a cikin dubu; Don gudun kada al'umma ta musa nan gaba.

To shi mu karva masu da cewa, duk al'ummar da ke iya musanta abin da aka yi (magana) cikin dubu, to musa wanda aka yi (rubutu) cikin 'yan kwarorin mutane yafi sauqi da cancanta gare ta.

Kuma muna nan akan bakar mu, na cewa in dai har wancan nassi (magana) ya inganta, to babu buqatar wannan rubutu yanzu. Saboda baya halatta ga Annabawa su jinkirta wata magana (saqon Allah) har sai lokacin mutuwasu. kuma da wajibi ne a kan manzon ya rubuta waccan wasiya, shakku da kokwanto da hayaniyar da Sahabbai suka sami kansu a lokacin ba ta hana ya dage a kan sai an kawo kayan rubutun ya rubuta; maganar Umar *Raliyallahu Anhu* ko wani daga cikinsu duk ba za ta hana shiba, a matsayinsa na mafi xa'a ga Allah daga cikin bayinsa.

Ka ga fita batun rubutun da *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi ya tabbatar da cewa ba wajibi ba ne. Ba kuma wani abu ne mai muhimmanci a addini ba, wanda rubuta shi a lokacin ke wajaba. Don da haka ne, da ya yi.

Kuma shi Umar ya riga ya gama leqen cewa abin ba wani abu bane. Don inda wani abu ne, kuma Annabi ya zartar da hukuncin lalle sai ya rubuta shi, lalle Umar *Raliyallahu Anhu* a matsayinsa na mai hasashe (ijtihadi) kawai ba zai yi gangancin wandarewa ba. Kokwanton da ya aure shi a kan gaba xayan lamarin ko sashensa; daga baya, ba zai ba shi damar yin haka ba. Ko banza kokwanto a kan kasancewar abin da yake gaskiya gaskiya, ya fi sauqi bisa ga yanke masa hukuncin zama qarya.

Ina fatar dai ka gane.

To kuma tafi naji. A matsayin Umar *Raliyallahu Anhu* na mai ijtihadi iyakar abin da za'a iya cewa yayi na rashin sa'a shi ne, kuskure. Allah kuwa ba ya kama mai ijtihadi da wani laifi don ya kuskure daidai. Kamar yadda ba zai kama Ali *Raliyallahu Anhu* da kuskuren da ya yi a cikin ijtihadi, ya wajabta ma wata mata da mijinta ya rasu yin iddar mutuwa ta tsawon mafi tsawon iyakoki biyu ba. Tattare kuma da abin da ya tabbata ya kuma inganta daga

Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne cewa a lokacin da aka ba shi labarin cewa Abus-Sanabilu ya yi wa Subai'atul-Aslamiyyah irin wannan fatawa. Sai Annabi ya ce: Qarya Abus-Sanabilu ke yi. Jeki ki auri duk wanda kike so kin halatta.

Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya qaryata Abus-Sanabilu ne, saboda bai isa yin ijtihadi ba. Musamman ma da yake Manzo na kusa.

Amma ka ga ba za'a qaryata Ali da xan Abbas *Raliyallahu Anhuma* ba, saboda sun bayar da irin wannan fatawa. Domin sun bayar da ita ne bayan rasuwar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma ba su da masaniya da wannan qissa ta Subai'atu.

### 2.45 Halifa Umar ba Azzalumi ba ne

A wani qoqari kuma na cin mutuncin Umar *Raliyallahu Anhu* da tozarta shi, sai xan Shi'ar ya yi masa qazafin zalunci, da wasu siffofi da halaye na naqasa. Inda ya ce wai, bayan da nana Fatima *Raliyallahu Anha* ta yi wa Abubakar *Raliyallahu Anhu* gargaxi a kan abin da ya shafi Fadak, sai halifan ya rubuta takarda, wadda ke nuna ya mallaka ma ta qasar; ta fita hannun kowa daga wannan lokaci. Wai kuma fitowarta daga wurinsa ke da wuya, sai ta yi kicivis da Umar *Raliyallahu Anhu* wanda ya qwace takardar daga hannunta ya qona. Wannan abu ya dugunzuma ranta sosai. Nan take ta yi ma sa baqar addu'a da "Allah ya isa". Wai kuma sakamakon wannan addu'a ne, Abu Lu'alu'ata ya yi wa Umar abin da ya yi masa.

Kuma xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Haka kuma saboda rashin sanin hukunce-hukuncen shari'a, Umar ya yi wa haddin Allah wanda ya hau kan Mugiratu xan Shu'ubata targazo, ta hanyar qin hukunta shi. Kuma ya kasance yana bai wa sauran matan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* fiye da abin da suka cancanta daga Baitul-Mali. Amma sai ya ba wa Aisha da Hafsatu *Raliyallahu Anhuma* dirhami dubu goma kowace shekara. Ya kuma canza hukuncin Allah a kan waxanda aka kora.

## Martani:

Ko shakka babu wannan magana baqar qarya ce, irin wadda ba masanin da zai kokwanton ta. Domin babu wani malamin hadisin da ya tava riwaito ta, balle a iya gane isnadinta. Kuma tabbataccen abu ne, Abubakar *Raliyallahu Anhu* bai tava tabbatar wa Fatima *Raliyallahu Anha* ko wani mallakar qasar Fadak ba. Kuma ba ta yi wa Umar wata baqar addu'a ba.

Kuma ko shakka babu abin da ya faru ga Umar *Raliyallahu Anhu* na kisan gillar da Abu Lu'alu'ata ya yi masa, wani karamci ne daga wurin Allah Ta'ala irin wanda Ali da Husaini *Raliyallahu Anhuma* ba su samu ba. Eh! Ba su samu wannan karimci ba mana. Tunda xan Muljamu da Yazidawa waxanda suka kashe su, musulmi ne 'yan'uwansu. Shi kuwa Abu Lu'alu'ata, makashin Umar *Raliyallahu Anhu* kafiri ne baqin. Ka kuwa san ba abin mamaki ba ne

kafiri ya kashe musulmi, balle ma halifa sukutum. Ai ko banza babu abin da ke tsakanin mumini da kafiri sai yaqi.

Saboda haka ne shahadar wanda ya rasa ransa hannun kafiri ta fi ta wanda ya rasa nasa hannun musulmi xan'uwansa girma da karvuwa a wurin Allah. Kuma ta yaya ne ma za'a iya gane cewa addu'ar da Fatima wai ta yi wa Umar xin *Raliyallahu Anhu* ce sanadiyyar kisan nasa, tunda sayyidar ta rasu ne bayan halifancin Abubakar da wata shidda kafin qarewar na Umar *Raliyallahu Anhu* ka ga abin na da kamar wuya.

To, kuma ko qaddarawar muka yi Nana Fatima ta yi wa Umar xin waccan baqar addu'a, ta fatar ajalinsa ya kasance hannun kafiri. Ai wannan abin alheri ne da alfahari ta roqa ma sa. In kafiri bai kashe shi ba sai rayuwarsa ta xore? Ai irin wannan addu'a ce Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* kan yi ga Sahabin da matsayinsa ya kai gare shi, wato ya roqar masa shahada. Har ma Sahabbansa suka gano cewa, da zaran sun ji Manzo ya ce: "Allah ka yi gafara ga wane". To sun san shahadarsa ta kusa. Saboda haka ne ma, wani lokaci sukan katsi nunfashinsa, idan ya yi wa wani Sahabi irin wannan addu'a, su ce: ya Manzon Allah! Ba mu gaji da ganinsa ba.

Haka kuma a da 'yan Shi'ah za su dage a kan cewa lalle sakamakon zaluncin da Umar *Raliyallahu Anhu* ya yi wa Fatimar ne da baqar addu'ar da ta yi masa, wancan abu ya faru gare shi. To, sai mu ce masu: Idan dai har hankalin masu hankali zai karvi wannan magana taku, to, ba zai kasa karvar ta wanda ya ce: kisan gillar da xan Muljam ya yi wa Ali *Raliyallahu Anhu* ya faru ne sakamakon zaluncin da ya yi wa mutanen Siffin da Harijawa da "Allah ya isa"r da suka yi masa. Kuma Abu Sufyana da Harisu ne suka yi wa Husaini baqar addu'a, ta zama sanadiyyar kashe shi a karbala.

Ita kuma cewar da xan Shi'ar ya yi, wai Umar ya yi wa hukuncin Allah targazo, ta hanyar qin yi wa Mugiratu xan Shu'ubata haddi, qarya ce. Domin kuwa jumhurun malamai sun karvi abin da halifan ya yi a cikin wannan sha'ani da hannu bi-biyu; wato yi wa sauran shedu haddin qazafi, idan suka kasa cika. Kuma sauran malaman da ke ganin ba haka ya kamata hukuncin ya kasance ba, sun gamsu da cewa mas'alar ta ijtihadi ce.

Sannan kuma, kamar yadda muka faxa a baya; abin da Ali *Raliyallahu Anhu* yayi na qyale makasan halifa Usmanu ba tare da ya hukunta su ba. Shi ne yi wa hukuncin Allah targazo, ba wannan ba. Idan kuwa kuna ganin mai wannan ra'ayi; na ganin laifin Ali, ya yi varna. To, wanda ke ganin laifin Umar *Raliyallahu Anhu* a cikin waccan mas'ala shi ne babban mavarnaci, bisa la'akari da matsayi da banbancin mas'alolin biyu.

Haka kuma, xan Shi'ar ya soki halifan da cewa, yana ba wa sauran matan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* fiye da abin da suka cancanta daga Baitil-Mali. Amma Nana Aisha da Hafsatu sai ya ba su dirhami dubu goma-goma kowace shekara...

**Martani:** Da Allah ya sa xan Shi'ar nan na cikin masu hankali, to da ya fahimci cewa, ai wannan abu da halifan ya yi, wani abu ne da ke nuna cikar

taskai da adalci. Tare da haxuwarsa da Allah, ta hanyar hana zuciyarsa abin da take so.

Kai ka san in ba haka ba, babu abin da zai sa ya fifita wata a kan ‘yar cikinsa a cikin wannan sha’ani na dukiya. Shi a hankali da tunaninsa Hafsatu ‘yarsa da Abdullahi xansa, ba su isa su yi kafaxa-da-kafaxa da sauran matan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da mutanen gidansa ba, balle su karvi daidai abin da su suke karva. Daxa balle ma su wuce su, don Ubansu ne halifa.

Tirqashi ka ji masu tuqen dabaibiya malam.

A fahimtar halifa Umar *Raliyallahu Anhu* arzikin qasa ana raba shi ne ga jama’a gwargwadon girma da xaukakarsu. Saboda haka ne shi, a duk lokacin da ya tashi rabo, sai ya fifita matan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a kan sauran mata. Kamar yadda yake fifita Banu Hashim; wato Aliyu xan Abu Xalib da Abbas da sauransu, a kan sauran qabilun da ba su ba.

Duk wanda Umar *Raliyallahu Anhu* ya fifita a cikin wannan al’amari na rabon arzikin qasa, to za ka taras makusancin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne. Ko kuma yana daga cikin na sahun farko a shiga musulunci. Ko kuma yana da wani abu na bajinta ko mai kama da haka, wanda zai sa ya cancanci wannan fifiko. Har ma an riwaito yana cewa: Babu wanda ya fi wani cancanta da wannan arziki a cikinmu; ina dai la’akari ne da buqatar mutum, ko hidimarsa ga addini, ko sammakosa a cikinsa, ko wadatarsa.

Waxancan mata na Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da xan Shi’ar ke zargin Umar *Raliyallahu Anhu* da basu kuxi mai yawa. Halifan bai yi hakan don tsoron wani abu ko rojin wani ba. Don babu wata dangantaka tsakaninsa balle a ce. Kuma ka ji irin ma yadda ya yi da ‘ya’yan cikinsa, da makaman tansu. Ba ya fifita mutum sai don wani dalili na addini tsantsa. Kuma ko a hakan ma yana fifita mutanen gidan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* tare da farawa dasu, a kan mutanen sauran gidaje. Kuma babu wanda ya bi sawun Umar *Raliyallahu Anhu* a cikin wannan kyakyawan aiki, daga cikin Usman da Ali *Raliyallahu Anhu* halifofin da suka zo bayansa, ko wasunsu.

Idan kuwa har za’ayi wani qorafi a kan Umar, kan fifita waxancan mata na Manzo, to sai a kuma yi qorafi a kan fifita Ahlul-Baiti da ya yi a kan wanda ba su ba, tare da gabatar da su. Koko?

### 2.46 Gargaxi ne ba Haddi ba

Xan Shi’ar ya ci gaba da cewa wai kuma: Umar *Raliyallahu Anhu* ya canza hukuncin Allah a kan waxanda ake kora saboda aikata wata kaba’ira.

**Martani:** Da xan Shi’ar nan ya san cewa, canza hukuncin Allah na tabbata ne a lokacin da aka xauke shi, aka kuma maye gurbinsa da abin da ke walwale shi. Kamar haramta abin da Allah ya wajabta ko halatta abin da ya haramta. Da bai faxi wannan magana ba.

Shi kuwa korar da shari’a ta yarda a yi wa wanda ya sha giya misali, gargaxi ne ba haddi ba. Kuma gargadi a shari’a wani fage ne na ijtihadi. Musamman a kan shan giya. Domin kuwa har Annabi *Sallallahu Alaihi*

*Wasallama* ya kwanta dama, bai daddale haddin mashayin giya ba ta fuskar yawan abin da za a yi ko siffarsa. Iyakar abin da aka san ya bar wa musulmi a matsayin sunna, shi ne; dukan mashayin da ganyen dabino da takalmi da wutsan tufafi, har ya yi tivis. A yayin da ake bulale mai qazafi da mazinaci.

Abin da Sahabbai suka gada kenan a wannan vangare. Wato "dukan" mashayin giya. Amma vangaren adadin dukan (buloli) Sahabban sun yi amfani da basira, ilimi da gogewarsu, a matsayin ijtihadi. Wasu daga cikinsu suka yi bulala arba'in, wasu kuma tamanin.

Kuma hadisi ingantacce ya tabbata cewa, Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce: kowane adadi aka xauka an yi Sunnah.

### 2.47 Allah Ne Kawai ba ya Mantuwa ba ya Kure

A nan kuma Xan Shi'ar cewa yake yi, wai Umar *Raliyallahu Anhu* kamar Abubakar ne. Shi ma masaniyar da yake da ita da hukunce-hukuncen shari'a 'yar qanqanuwa ce; saboda wai ya yi umurni da a jefe wata mata da ke da juna biyu, saboda kama ta da laifin zina da aka yi. Sai wai Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce ma shi, idan kana da hujjar sa a kashe ta, to ba ka da hujjar sa a kashe xan da ke cikinta. Wai saboda haka sai Umar *Raliyallahu Anhu* ya janye umurnin, har kuma ya ce: "Wallahi ba don Ali ba yau da Umar ya halaka".

**Martani:** Babu wani abu qasa, da ke tabbatar da kasancewar wannan qissa gaskiya. To kuma ko da mun qaddara kasancewarta hakan, to lalle ne xayan biyu; ko dai ya kasance Umar bai san matar na da juna biyu ba, sai da Ali ya labarta masa *Raliyallahu Anhu,* ka ga kenan rashin sani ya shiga. Kuma faxakar da shi, da Ali ya yi a kan haka, kamar abin da aka saba ne na, muqarraban shugaba su faxakar da shi a kan abubuwan da suka shige masa duhu, na halayen talakawansa. Ko kuma irin abin da shedu zai bayyana a gabansa. Babu kuwa wani Annabi ko shugaba da ba ya da buqata da irin wannan gudunmawa ta alheri. Hakan kuma ba ya daga cikin hamshaqan hukunce-hukuncen shari'a.

Na farko kenan. Ko kuma a'a ya san da matar na da juna biyu. Amma ya sha'afa da cewa ba a jefe irinta sai ta sauka. Da kuma Ali *Raliyallahu Anhu* ya tunatar da shi, sai ya gamsu. Ka ga ba zancen rashin sani a nan, sai dai sha'afa. Don da ace ya riga ya gamsu da halaccin jefe irinta, to, babu wanda ya isa ya hana shi zartar da hakan, a matsayinsa na mujtahidi. Tattare da masaniyar da yake da ita da cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya umurci Gamidiyyah da ta je sai bayan ta sauka, ta dawo a zartar ma ta da haddin zinar da ta yi iqirarin ta yi har ta xauki ciki.

To, kuma ai ba abin mamaki ba ne, don wannan mas'ala ta shige wa Umar *Raliyallahu Anhu* duhu. Kuma ba abu ne da ya kamata a soke lamarinsa a kai ba. Domin kuwa Allah ne kawai ba ya mantuwa ba ya kure, *Subhanahu WaTa'ala*. Kuma halifa irin Umar, barde, jarumi uban jarummai, kamata yayi a yi masa kyakkyawan zato. Musamman idan aka yi la'akari da yadda ya shugabanci musulmi da kafiran amana. Ta hanyar ba wa kowa haqqinsa, da

zantar da haddoda. Da zama Alqalin gaba xayan jama'a, da irin yadda musulmi ya sami ranar baje garinsa a zamaninsa, irin yadda bai samu ba kafinsa.

Babu wani lokaci da za ka taras da halifa Umar *Raliyallahu Anhu* face, ko dai yana fatawa, ko yana Alqalanci. Ka kuwa san mai cikin cokalin ilimi ba zai iya haka ba ko alama ko?!

To tunda kuwa haka ne, ashe ba aibi ba ne don mai irin wannan fama, ya manta mas'ala xaya daga cikin mas'aloli dubu xari ko fiye, sai da aka tuna masa. Kai! xauki ma bai san ta ba sai da aka sanar da shi. Ai duk xan Adamu ajizi ne.

Kuma ai tabbataccen abu ne, cewa mas'alolin da suka shige wa Ali *Raliyallahu Anhu* duhu, daga cikin sunnar Manzon Allah, sun fi a qirga. Wasu ma har ya mutu bai san su ba.

Ina fatar baka jahilci haka ba?

### 2.48 Halifa Umar ba Jahili ba ne

Wata sukar lamirin kuma, mai kama da waccan itace cewar da xan Shi'ar yayi kai tsaye, wai halifa Umar jahili ne. Saboda ya yi umurni da a jefe wata mahaukaciya saboda samunta da laifin zina da aka yi. Sai da Ali *Raliyallahu Anhu* ya faxakar da shi cewa, an xauke Alqalami daga kan mahaukaci, har sai ya warke. Jin haka sai Umar ya janye umurnin, kuma ya ce: "Wallahi ba don Ali ba da Umar ya halaka".

**Martani:** kafin mu shiga fashin baqin wannan magana a matsayin martani, muna tabbatar wa xan Shi'ar da cewa; Eh! Wannan mas'ala, gaskiya ne ta faru. Amma wannan magana ta cewa Umar xin ya ce ba don Ali ba da ya halaka qari ne; babu ta a cikin lafiyayyar ruwaya.

Nan kenan. Kuma lalle ne Umar *Raliyallahu Anhu* bai san waccan mata mahaukaciya ce ba. Ko kuma ya sani amma ya sha'afa. Saboda haka ya yi umurni da zartas ma ta da haddin. Amma da aka faxakar da shi ya gamsu ka ga ba abin sukar lamiri a nan.

Koko a'a, halifan ya fahimci cewa haddodin da ake zartarwa a kan masu lafiya, ana zartar da su ne, don alqinta rayuwar duniya, ta hanyar hana wani cutar da wani. Saboda haka babu dalilin da zai hana a hukunta mahaukaci, matuqar ya zo da wani mugun aiki da ke iya cutar da jama'a; waxanda suka haxa da masu hankali da mahaukata. To, tunda kuwa zina mugun aiki ce, da ke cutar da al'umma, lalle, idan mahaukaci ya yi ta a hukunta shi. Amma daga baya sai aka faxakar da shi cewa, irin wannan haddi na zina, haddi ne da Allah Ta'ala bai yi umurni da zartarwa ba, sai a kan mukallafai.

Wannan kenan. Wani abu kuma da ke iya zama madogara, ga halifan a kan wannan ijtihadi nasa, shi ne horon da shari'a ta yi na ladabtar da qananan yara, ta hanyar duka idan suka qi yin sallah. Har Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Ku hori yara da yin sallah suna 'yan shekara bakwai. Ku kuma doke su, idan suka qi, in sun shekara goma. Ku kuma rabe masu shinfixun bacci".

Bayan wannan kuma, ai ba mutumin da ba ya da hankali ba, ko dabba, a shari'a idan tana fitinar jama'a, daidai ne a kashe ta. Haka idan mahaukaci na fitinar jama'a shi ma aka rasa yadda za ayi da shi a yi maganinsa, sai ta hanyar kisa, ya halatta.

Kuma, waccan dabba da za'a kashe bisa wancan dalili, idan ta gida ce kuma mallakar wani, ba za'a biya shi diyyarta ba, bisa ra'ayin Jumhurun malamai, irin su: Maliku da Shafi'i da Ahmadu da wasunsu.

A taqaice, duk abubuwan da xan Shi'ar nan ya ambata na suka ga Umar *Raliyallahu Anhu* ko waninsa daga cikin Sahabbai, na kawai tabbatar wa mai hankali da ilimi, xayan abubuwa biyu ne: 1) ko dai ya kasance xan Shi'ar ya faxe su, sakamakon fama da ciwon qarancin ilimi. Ko 2) tsanar wannan bawan Allah da qarancin kishin addini.

Dalili kuwa shi ne, ya xauka cewa halifan ya hana Fatima haqqinta, ya kuma yi son zuciya a cikin rabon arzikin qasa, ya kuma yi wa hukuncin Allah tasgaro da makamantan wannan.

Ka ga a taqaice yana so ne ya ce halifan ba adili ba ne. Alhali kuwa babu inda labarin adalcin Umar *Raliyallahu Anhu* bai kai ba a faxin duniya. Ta yadda har ma ake buga misali da shi; ana cewa: A yi koyi da rayuwar Umarora biyu. Maganar da malamai irin su Ahmad xan Hmbali da wasu malaman hadisi suka fassara da cewa; ana nufin Umar xan Haxxabi ne da Umar xan Abdulaziz. A ya yin da Abu Ubaidata da wasu malaman Lugga da Nahawu, suka ce: Umarun na biyu na nufin Abubakar ne *Raliyallahu Anhu.*

A taqaice dai, Umar xan Haxxabi ya tabbata adali.

### 2.49 Wannan Shi Ne Halin Bayin Allah Na Gari

Daga nan kuma sai xan Shi'ar ya lalubo zancen qayyade sadakin aure, da halifa Umar *Raliyallahu Anhu* ya yi, ya soki lamirinsa da shi. Bari ka ji abin da ya ce:

Wani abu kuma da ke nuna kasancewar Umar jahili shi ne, watarana yana huxuba sai ya ce: Daga yau duk wanda ya sake bulbula wa mata kuxin sadaki, to zan karve toliyar in saka ta Baitil-Mali. Yana faxar haka sai wata mace, can daga cikin sahun mata ta xaga murya ta ce: Ya halifan Manzon Allah! Ya za ka hana a ba mu abin da Allah ya yi umurni da a ba mu a cikin littafinsa? Inda ya ce: *Alhali kuwa kun bai wa xayarsu qinxari (4:20).* Dasa ayarta ke da wuya sai Umar ya ce: Kai madalla da aka samu waxanda suka fi Umar sanin makamar addini har a cikin mata. Na kuma janye wannan magana.

**Martani:**

Ko shakka babu wannan qissa, na tabbatar da kamalar Umar *Raliyallahu Anhu* ne kawai, da kishin addini da tsoron Allansa. Da kuma irin yadda yake shirye kodayaushe, ya bar ijtihadinsa ya koma yana saurare da karvar gaskiya, ko da kuwa daga bakin mace ta fito, har ma ya cire hula ya sara mata. Kuma a

shirye yake yayi tawali'un tabbatar da fifikon wani a kansa, a cikin irin wannan qanqanuwar mas'ala. Wannan kuwa shi ne halin bayin Allah na gari.

Kuma Alhamdu Lillahi, da ya zan ba sharaxi ba ne, sai mafi girman mutane ya zama wanda babu mai iya faxakar da shi a kan wani abu daga cikinsu, kafin ya karva sunansa. Kuna ina tsuntsun Hudahuda ya ce wa Annabi Sulaiman: *Na san abin da ba ka sani ba, kuma nazo maka daga Saba'i da wani labari tabbatacce (27:22)?.* Kuma kuna ina Annabi Musa *Alaihis Salamu* ya ce wa Haliru: *Ka yarda in bi ka a kan ka sanar da ni daga abin da aka sanar da kai na shiriya (18:66)?.* Ka kuma san abin da ke tsakanin Annabi Musa *Alaihis Salamu* da Haliru na fifikon daraja ya fi wanda ke tsakanin Umar *Raliyallahu Anhu* da na takwarorinsa Sahabbai, balle wata mace. Kuma hakan ba ta wajabtar da kasancewar Halirun ko kusa da darajar Musa ba *Alaihis Salamu* balle yayi kafaxa-da-kafaxa da shi. Kai! Ba Musa ba, ko Annabawan da suka zo bayansa. Irin su: Haruna da Yusha'u da Dawuda da Sulaimana da wasunsu, duk sun fi Halirun girman daraja; ko an xauke shi a matsayin Annabi.

Kuma tabbataccen abu ne cewa Sahabbai su ne mafificiyar al'umma. Imamus Shafi'i ya ce: Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* sun yi mana ko-ta-kwana a fagen kowane irin ilimi da fiqihu da riqon addini da shiriya. Kuma ijtihadinsu shi ne mafi alhairi gare mu, bisa ijtihadinmu a kan kansu.

Imamu Ahmad xan Hambali ko cewa ya yi: Tuwasun Sunnah a wurinmu shi ne riqo da abin da Sahabban Manzon Allah suke a kai.

Abdullahi xan Mas'udu, ya ce: Ya ku mutane! Duk wanda zai yi koyi da wani daga cikinku, to ya yi da waxanda suka riga mu gidan gaskiya. Saboda babu fitinar da ba ta iya faruwa ga wanda yake raye. Ku yi koyi da Sahabban Muhammadu. Don su ne mafiya girma daga cikin wannan al'umma, mafiya kuma nagartattun zukata da zurfin ilimi da sauqin kai. Su ne kuma mutanen da Allah ya zavar wa Annabinsa a matsayin abokai. Kuma mataimaka don tabbatar da addininsa. To, saboda haka ku kiyaye alfarmarsu, ku kuma yi koyi da su. Ku yi kwaikwayon duk abin da kuke iyawa daga cikin halayensu da kishinsu ga addini. Don suna kan tafarkin madaidaici.

Haka kuma an riwaito Huzaifatu na cewa: Ya ku gardawa ku shiga taitayinku. Ku dawo kan tafarkin waxanda suka gabace ku. Idan Allah ya taimake ku a kan haka, to wallahi kun sami babban rabo. Idan kuwa kuka bar tafarkin nan nasu madaidaici kuka dinga mashalo, ba ku gidan Ango ba ku gixan Amarya, to, haqiqa sai magenku ta sha qasari.

### 2.50 Halifa Umar Bai Jahilci Haddin Shan Giya ba

Daga nan kuma sai xan Shi'ar ya ce kuma wai halifa Umar *Raliyallahu Anhu* bai san haddin shan giya ba. Saboda ya sa wa Qudamatu na shafin kwalli a lokacin da ya sha yayi tatil, bisa dalilin ayar da ya karanta masa. Wadda Allah Ta'ala ke cewa a cikinta: *Babu laifi a kan waxanda suka yi imani ga abin da suka ci, idan sun yi taqawa kuma suka yi imani (5:93).* Sai da Ali

*Raliyallahu Anhu* ya ce wa Umar: Ai Qudamatu ba ya daga cikin mutanen da wannan aya ke magana a kai. Wai sai Umar ya yi sakabo, saboda bai san hukuncin wanda ya sha giya ba. Balle ya zartar wa Qudamatu. Ganin haka sai Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce: ka yi masa bulala tamanin. Saboda shan giya na sa maye da fita hankali da yin qazafi da qaga karya.

Ka ji abin da mutumin ya kafa hujja da shi.

**Martani:**

Ko shakka babu wannan magana ba haka take ba. Domin kuwa ilimin da Umar *Raliyallahu Anhu* ke da shi a kan wannan mas'ala, ya fi qarfin a tsaya ja-in-ja don tabbatar da shi. Kafin wannan mas'ala ta Qudamatu, ta tabbata a tarihin halifancin Abubakar da shi Umar xin *Raliyallahu Anhu* cewa sukan yi wa mashayin giya bulala arba'in ko tamanin wani lokaci. Wani lokacin ma, idan al'amarin bai hayaqa ba, Umar *Raliyallahu Anhu* kan sa a aske kan mashayin ko a kore shi daga Madina a matsayin gargaxi. Sukan kuma yi amfani ne da kabar dabino wani lokaci, idan za su bulale mashayin. Wani lokaci kuma su sa takalmi ko hannayensu ko wutsan mayafansu, su faffalke sa.

Ita kuwa waccan qissa ta Qudamatu, gaskiya ne ta faru. Amma xan Shi'ar yayi son zuciya a cikinta, irin yadda dai ka san ya saba yi. Ga kuma haqiqanin yadda al'amarin ya faru:

Abu Ishaka al-Jauzajani da wasu malamai sun riwaito daga xan Abbas, wanda ya ce: watarana Qudamatu xan Maz'unu ya sha giya ya yi tatil. Sai Umar ya ce ma sa: Ya aka yi haka? Sai shi kuma ya karva ma sa da cewa: Ai Allah Ta'ala ya ce: *Babu laifi a kan waxanda suka yi imani, kuma suka aikata ayyukan qwarai, a cikin abin da suka ci. Idan sun yi taqawa kuma sun yi imani, kuma sun aikata ayyuka na qwarai (5:43).* Ka kuwa san ina daga cikin Muhajiruna na farko-farko, waxanda kuma suka halarci yaqin Badar da na Uhudu.

Daga nan sai Umar ya kalli sauran Sahabbai ya ce: "Ku ba shi amsa mana". Sai suka yi tsit.

Ganin haka sai ya dubi xan Abbas ya ce: "Ba shi amsa". Sai ni kuma na ce masa: "Qudamatu ka ci tuwon gigi. Ai wannan aya ta sauka ne a matsayin uzuri ga magabatanmu waxanda suka sha giya kafin Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya haramta ta ka suka kwanta dama. Ya kuma haramta ta da cewar da ya yi: Ya ku waxanda suka yi imani! *Abin sani kawai, giya da caca da refu kiban quri'a qazanta ne daga aikin shaixan. Sai ku nisance su (5:90).* Kuma ka sani wannan aya hujja ce a kanka".

Sannan sai Umar *Raliyallahu Anhu* ya nemi shawarar Sahabban a kan bulolin da ya kamata a yi masa a matsayin haddi. Sai Ali xan Abu Xalib *Raliyallahu Anhu* ya ce: Tunda idan mutum ya sha giya tana sa shi maye, idan kuma ya yi maye hankalinsa kan goce har ya yi wa wani qazafi, ai sai a yi masa bulala tamanin (haddin qazafi). Sai Umar ya sa aka sha shi tamanin.

Wannan shi ne haqiqanin abin da ya faru. Kuma ka ga shawara ce kawai Ali *Raliyallahu Anhu* ya bayar ta a yi bulala tamanin. Kuma duk da haka akwai yar magana a wurin.

Abin da ya sa na ce akwai 'yar magana a wurin shi ne, saboda ta tabbata a ingantaccen hadisi cewa Abdurrahaman xan Aufu ne ya ba Umar *Raliyallahu Anhu* waccan shawara ta bulala ku dama tamrin ba Ali ba. Hasali ma shi Alin *Raliyallahu Anhu* ijtihadinsa a kan haddin shan giya bai tava wuce bulala arbain ba. Kuma su ne ya yi wa Walidu xan Uqubata a lokacin da ya sha giyar, a zamanin halifancin Usmanu *Raliyallahu Anhu*, tare da faxar cewa bulala tamanin Umar *Raliyallahu Anhu* kan yi. Amma kuma an sami wata riwaya da ke cewa, bayan Alin *Raliyallahu Anhu* ya zama halifa, ya kawo wancan ijtihadi nasa, na bulala arba'in ya koma ga na Umar, wato bulala tamanin. Kamar yadda Sahabi Abdurrahaman ya bayar da shawara. Ka ga kenan ya haxa haddodi biyu.

Amma duk da yake babu wani daga cikin Sahabban da malaman fiqihu da ya mara wa Ali *Raliyallahu Anhu* baya a cikin waccan magana ba musamman idan hakan ta faru a cikin bulala arba'in ko qasa ga haka, bai kamata a xauki maganar tasa a matsayin ficewa daga ijma'i ba.

## 2.51 Ba Ta San Zina Haramun Ce Ba.

A nan kuma matsala biyu ce xan Shi'ar ya soki sawun Umar *Raliyallahu Anhu* da su; matsalar diyyar vari da ta haddin zina. Ga abin da yake cewa:

Watarana Umar ya aika a kira ma sa wata mata mai juna biyu. Isar saqon ke da wuya sai cikin nata ya zuba, saboda tsoron abin da zai biyo baya idan ta yi ido huxu da halifan. Da aka dawo aka ba shi labarin, sai ya samu damuwa. Sai Sahabban suka ce masa: "Kar ka damu. Ba ka da wani laifi a wurin Allah, tunda a kan haqqin shari'a ce haka ta faru".

Amma dai duk da haka Umar bai gamsu ba. Sai ya tambayi Ali *Raliyallahu Anhu* shi kuma ya ce lalle sai dangin Umar sun taru sun biya diyyar cikin da ya zuba.

Wai a haka inji xan Shi'ar, fifikon Ali *Raliyallahu Anhu* a kan Umar da sauran Sahabban ya tabbata.

Matsala ta biyu kuma ya ce wai: Watarana an zo da wata mata da aka kama da laifin yin zina, a wurin Umar *Raliyallahu Anhu* gaba xayan Sahabbai suka yi ittiffaqi a kan a jefe ta.Amma Umar xin ya yi biris da su, ya qyale ta.

**Martani:**

Ita waccan matsala ta farko, kamata ya yi a jinjina wa Halifa Umar *Raliyallahu Anhu* a kanta.saboda nacewar da ya yi sai ya samu wani abu da zai ba ya ntsu a kan sha'anin. Tunda matsala ce ta  ijtihadi.

Kuma neman shawarar Ali *Raliyallahu Anhu* da ya yi bayan ya gama jin ta bakin sauran Sahabbai, ba wani abin qumaji ba ne. Domin kuwa da ma al'ada ce ga Umar xin, ya shawarci Sahabbai a kan al'amurra. Ya saba da haka.

Ya kan shawarci Usmanu da Ali da Abdurrahamanu xan Aufu da xan Masu'du da Zaidu xan Sabitu da waxansu daga cikin Sahabbai. Wani lokaci ma har xan Abbas ya kan shawarta. Wannan kuwa na nuna kammalar darajarsa da hankalinsa da kishin addininsa. Wanda hakan tasa ya fi kowa daidaitaccen ra'ayi da ijtihadi.

Ita kuma waccan mata da yake faxa, an zo masa da ita ne akan ta furta cewa ta yi zina. Sai Sahabbai suka yanke mata hukuncin jifa, sayyidina Usmanu bai ce qanzil ba. Ganin haka sai halifa Umar *Raliyallahu Anhu* ya ce ma sa: Na ji ba ka ce komai ba, don me? Sai ya karva ma sa da cewa: Na yi shiru ne saboda na ga yadda take taka qasa da kallon mutane kamar wadda ta aikata wani abin alheri. Saboda haka nake jin ko shakka babu, ba ta san zina haramun ce ba.

Jin wannan magana ta dattijo Usmanu *Raliyallahu Anhu* sai halifa Umar ya fasa zartar ma matar da haddi. Ko banza yayata labarum ta yi zinar da take ta yi da kanta, ya sa aka kame ta a matsayin wadda ta yi iqirari. Kuma har aka gurfanar da ita gaban halifa Umar *Raliyallahu Anhu* ji take yi da ita da wanda ya ci wani abinci ko ya sa wata kuyangarsa xaka duk xaya.

**2.52 Annabi Sulaimana ne ba Halifa Umar ba**

A lalabe-lalaben da wannan xan Shi'ah ke yi, na kashin kajin da zai shafa wa halifa Umar, ya lalubo wata qissa da ta faru ga Annabi Sulaimana *Alaihis Salamu*, amma saboda cikar jahilci ya yava ta ga sayyidina Umar *Raliyallahu Anhu*.

Ga abin da xan Shi'ar ya ce: Watarana wasu mata biyu sun yi jayajjar wani jariri kowace daga cikinsu na cewa nata ne. qarshe suka xunguma sai gaban halifa Umar. Amma wai saboda zamansa kidahumi, sai ya rasa yadda zai raba gaukar. Saboda haka ya garzaya wurin Ali *Raliyallahu Anhu* sai Alin ya sa aka kira matan nan gaban Umar *Raliyallahu Anhu* ya yi masu nasiha. Amma abin ya faskara. Sai ya ce a kawo masa zarto zai raba ma su jinjirin. Jin haka sai xaya daga cikinsu ta ce: Don Allah, baban Hassan kar ka yi haka, idan ma har wajibi ne sai ka raba mana shi biyu, to na yafe ma ta. Sai Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce; Allahu Akbar! Ko shakka babu wannan yaro naki ne, ba na waccan ba, don lalle da xanta ne da ta yi yadda kika yi. Nan take kuma sai xayar can ta tabbatar wa Alin da cewa, xan dai na waccan ne.

Wai ganin haka, inji xan Shi'an sai hankalin Umar ya tashi ya kuma qara sakar wa Ali *Raliyallahu Anhu* har ma ya yi masa addu'a.

**Martani:**

Kasancewar xan Shi'ar bai ambaci madogarar wannan qissa ba, balle a binciki didiggin ingancinta. Kuma ni ban san wani malami da ya ambace ta ba. Duk hakan na tabbatar da cewa ba ta faru ga waxannan Sahabbai ba. Domin ko shakka babu, da ta faru da sun faxe ta.

Amma dai ta tabbata a wurinmu cewa Annabi Sulaimana *Alaihis Salamu* ya yi irin wannan hukunci.

### 2.53 Ra'ayin Shiryayyaun Halifofi Ne

Daga nan kuma sai xan Shi'ar ya ce: kuma jahilcin Umar bai tsaya nan ba. Watarana ya yi umurni da jefe wata mata wai don ta haihu da wata shida bayan aure. Sai Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce ma sa: Ya za ka yi da ita idan ta kawo maka hujja da cewar da Allah Ta'ala ya yi a cikin littafinsa: *Kuma cikinsa da yayensa wata talatin ne.* Da kuma cewar da ya yi: *Kuma masu haifuwa suna shayar da abin da suka haifa shekaru biyu cikakku, ga wanda ya yi nufin ya cika shayarwa (2:233).*

**Martani:**

Kamar yadda muka ambata a baya, babu wani abu da zai fuskanci halifa Umar *Raliyallahu Anhu* ba tare da ya shawarci manyan Sahabbai ba, kuma a mafi yawan lokuta ba yakan tsallake shawarwarin Usman *Raliyallahu Anhu* ba. Ya kan kuma shawarci Ali *Raliyallahu Anhu* wani lokaci. Wani lokacin kuma Abdurrahaman xan Aufu ko waninsu. Kuma a kan wannan kyakkyawan hali na waxannan magabata ne, Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yabi muminai da cewa: *Kuma al'amarinsu shawara ne a tsakaninsu (42:33).*

Bayan kuma wannan daraja da ta daxe da tabbata ga Umar *Raliyallahu Anhu* malamai sun qara wa junansu sani, a kan cewa shin ko macen da ciki ya bayyana gare ta, ba miji, ba Ubangida, ba ta kuma kafa hujja da wani ya take ta a kan kuskure ba, ta cancanci jifa? Sai malaman Madina suka tafi a kan cewa lalle za a jefe. Kuma a kan wannan hukumci ne Ahmad yake, a xaya riwayarsa. A yayin da Hanafawa da Shafi'awa suka tafi a kan cewa ba za a jefe ta ba. Wannan hukunci kuma shi ne riwaya ta biyu daga Ahmad. Dalilin waxannan malamai na biyu kuwa, a kan ijtihadin nasu shi ne, a tasu fahimta, abu ne mai yiwuwa qwarai ya kasance ta sami cikin ne saboda wani taki da aka yi mata na dole, ko na kuskure. Ko kuma Allah ne kawai ya hukunce ta da samun cikin ba tare da an take ta ba, a'a ta wata hanya dai daban.

Shi kuwa wancan ijtihadin na farko, wanda ke cewa ana jefe wannan mata, ra'ayin shiryayyun halifofi ne, dukansu a kansa suke. Har an riwaito cewa a qarshen rayuwar Umar *Raliyallahu Anhu* halifan ya hau mimbari ya yi wa mutane huxuba da cewa: Jefe mazinaci hukunci ne da ya tabbata a cikin littafin Allah, a kan maza da mata. Da zarar an samu shedu ko ciki ya bayyana, magana ta qare.

Ka ga kenan Umar ya daidaita bayyanar ciki da shedu a cikin tabbatar da laifin zina.

### 2.54 Ijtihadi ne Wannan

Sai kuma xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: kuma Umar ya kasance yana nuna banbanci idan yana rabon ganima, tattare da cewa Allah Ta'ala ya wajabta raba-daidai a cikinta.

Wato xan Shi'ar na so ne ya ce Umar ya qi bain umurnin Allah.

**Martani:**

Tarihin musulunci ya tabbatar da cewa ba halifa Umar *Raliyallahu Anhu* ne ke raba ganimar yaqi da kansa ba. Mayaqan ne dai da kansu ke rarraba ta tsakaninsu, bayan sun debe zumunci.karon da suke aika wa Umar din *Raliyallahu Anhu* kamar yadda ake aika wa kowane halifa. Wand shi ne zai warware wa mutanensa.iyakar abin da muka sani tabbatacce kenan.amma ba a taba jin Umar ko waninsa ba ya ce wajibi ne a fifita wasu da kansu a kan wasu, idan aka zo rabon ganinsa. Amma sane muke da cewa malamai sun dayi tsokace-tsokace a kan cewa, shin ko shugaba nada dammar kara wa wani daka ce wani abu idan ana rabon ganinsa. Saboda wani kwazo da aka ga ya nuna fiye da kowa?

Iyakar maganar kenan.kar ka dada kar ka kara.

Kuma a ta kaice, ya kamata kafin in kirein sheda wa mai karatu cewa wannan matsala ta ijtihadi ce.da Umar *Raliyallahu Anhu* zai ga dacewar nuna banbancin ta wannan hanya, akan waccan tsakaci da malamai suka yi. Ba wanda ya ba ya ce masa do me? Ko waye shi ko. Yana da dammar yin haka, a matsayinsa na shugaba wanda Allah ya sa zuciyarsa da harshensa, suka zama wani labaron hangen gaskiya komai nisanta,

Amma zancen rabon arzikin kasa, wanda baya da alaka da ganina, ko shakka babu Umar *Raliyallahu Anhu* na nuna banbanci a cikinsa, amma ban a son kai da son zuciya da ko da ba. Yakan fifita fifita wasu mutane nne a kan wasu, gwargadon girman darajarsu, kamar dai yadda muka yi bayani baya kadan. Kuma shi kansi ya so ya bar wannan salo, ya koma ga akasirinsa.don an riwaito yana cewa: idan Allah ya kai ranmu badi zan yi wa mutane bugu guda.

Wannan kenan. Ita kuwa cewar da xan Shi'ar ya yi wai: Allah ya wajabta da daitawa a cikin rabon ganina. Magana ce da ya bari haka nan, bai kafa wani dalili a kant ba, balle mu kacaccala tada shi. Kamar yadda mukan yi a cikin al'amuran da ke karvar ijtihadi.

### 2.55 Ra'ayin Sahabbai Hujja ne

Daga nan kuma sai xan Shi'ar ya ce: Kuma Umar na aiki da ra'ayi da zato da hasashe.

**Martani:**

Bayyana hukuncin wani abut a hanyar aiki da ra'ayi, bag a Umar *Raliyallahu Anhu* bawan ba.hasali ma tarihi ya tabbatar da cewa Ali *Raliyallahu Anhu* shi ne Sahabi mafi amfani da hasashe da ra'ayi a surin yanke hukunci. Haka Abubakar da Usman da zaidu dad an mas'udin da wasunsu daga

cikin Sahabbai, duk sukan yi amfani da hankali da basirarsu da gogewar da suke da ita a rayuwar musulunci su bayyana ra'ayinsu a kan wani hukunci.

Kuma ma ra'ayin da Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi amfani da shi ya halatta jinin masallata, ya fi komai ban mamaki.

Kamar yadda kaisu dan ubbadu ya tabbatar a cikin wani ingantaccen hadisi, wanda aka riwaito daga Hasan, a cikinsunanu Abu Dawuda da waninsa. Inda kaisun ya ce: Na ce wa Ali: don Allah muna son mu gane shin Manzon Allah ne *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya alkawanta maka wannan al'amari, ya kuma umurci ka da yi haka.koko dai ra'ayinka ne? sai ya karva masa da cewa: babu wani abu da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya alkawanta mani. Ra'ayina ne kawai.

Wannan magana tabbatatta ce. Don haka ma ne ka ji Ali *Raliyallahu Anhu* bai riwaito wani abu gane dayakin basasar raqumi da siffan ba, kamar yadda ya riwaito game da yakin da ya yi da Harijawa.

Wannan kenan. Sannan kuma idan dai mutum nada hankali da sanin ya kamata komai kakantarsu, to bai kamat ba ya yi ko kwantontsarkin tarihin Umar da umurninsa da adalansa da darajojinsa ba, balle har ya soki umurnsa, har ma yah ado da halifa Abubakar *Raliyallahu Anhu* don sun yi amfani da hasashen su a cikin wani hukunci. Ai ra'ayin Sahabbai hujja ne.

Duk kuwa wanda ka ji yana sukar lamarin waxannan bayin Allah, a kan wannan al'amari, to xayan biyu:

Ko dai ya kasance munafuki ne, zindiqi, mulhidi, maqiyin musulunci. Wanda ke son ya yi amfani da sukar lamirinsu, ya soki lamirin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da addinin musulunci kamar yadda malamin 'yan Shi'ah na farko, wanda ya kafa qungiyar ya kasance. Wanda ya yi daidai da matsayin 'yan Baxiniyyah.

Ko kuma ya kasance jahili mai biyar son zuciya. Kamar yadda mafi yawan 'yan Shi'ah suke. Ko da a cikin zukatansu musulmi ne su.

Amma na san xan Shi'ar na iya cewa: To ai Ali *Raliyallahu Anhu* ma'asumi ne. wanda duk abin da zai faxa ba ra'ayinsa kawai ne ba, wahayi ne daga wurin Allah. Kamar yadda ake yi wa Manzon Allah, kuma shi ne wanda manzon ya tabbatar da imamancinsa a nassanace.

Da zai mana haka, sai mu kuma mu ce masa: Da kai da Harijawa duk jirgi xaya ya xauko ku, kowanenku motar bidi'arsa ce ya take har kwano. Ku kun kai Ali *Raliyallahu Anhu* inda Allah bai kai shi ba. Su kuma sun ce kafiri ne ma.

Banbancin da ke tsakaninku da su kawai shi ne, su mutane ne masu ilimi da son gaskaiya da kishin addini fiye da ku. Don haka sun fi iya kare bidi'arsu da hujjoji masu dama. Duk kuwa wanda ya san ku ya san su ba ya shakkar wannan magana.

## 2.56 Shawara Ba Laifi Ba Ce.

Bayan wannan kuma sai xan Shi'ar ya soki lamirin halifa Umar *Raliyallahu Anhu* da cewa: Ya sava wa sunnar halifa Abubakar *Raliyallahu Anhu* tunda ya kafa kwamitin da zai zavi halifa daga cikinsa, tun yana raye. Alhali, shi ba kwamiti aka naxa kafin ya zama halifa ba.

Ya ci gaba da cewa: Halifa Abubakar bai ce ga wanda zai zama halifa bayansa ba. Iyakar abin da ya yi dai shi ne, ya faxi alherin Salimu bawan Abu Huzaifa. Inda halifan ya ce: Da Allah ya sa Salimu na raye, ba zan yi shakkun komai a kansa ba.

Kuma ya faxi wannan magana ne gaban Sarkin Musulmi Ali *Raliyallahu Anhu*. Kuma a taqaice, inji xan Shi'ar wai, Umar ya riga ya gama zaven magadinsa. Tun da a cikin wancan kwamiti na shawara da ya kafa, ya haxa hancin waxanda ya san ba yadda za a yi su yi kafaxa-da-kafaxa da sauran, balle su shiga gabansu. Sannan kuma wai sai ya biyo da dasisar sukar 'yan kwamitin, da cewa ya yi haka ne don ba ya son wani bara gurbi ya hau karagar sai dai nagari. Qarshe kuma sai ya damqa ta ga bara gurbin. Saboda yanke hukuncin da ya xaya daga cikin 'yan kwamitin ya yi.

Ya dawo kuma ya bar ta tsakanin huxu daga cikinsu. Ya kuma mayar da su. Har sai da ta kama hanyar zuwa ga xaya daga garesu. Kuma a haka sai ya damqa ragamar zave na qarshe a hannun Abdurrahaman xan Aufu. Bayan kuma can ya siffanta shi da rauni da kasawa. Sannan kuma ya ce: Idan Ali *Raliyallahu Anhu* da Usman *Raliyallahu Anhu* suka rage a faifai, to duk shawarar da suka yanke a kansu tayi. Idan kuwa suka kai uku, to duk hukuncin da waxanda Abdurrahman xan Aufu ke cikinsu suka yanke shi ne abin karva. Kuma wai Umar ya yi haka ne, inji xan Shi'ar saboda ya san har abada Ali da Usmanu *Raliyallahu Anhu* ba su haxuwa qarqashin inuwa xaya. Kuma babu yadda za a yi Abdurrahman ya bar Usman a matsayinsa na xan amminsa, ya zavi Ali.

Sannan kuma wai sai Umar, don tsananin iya makida, inji shi, ya yi umurni da shace kan duk wanda ya kwana uku bai yi bai'a ga wanda aka zava ba. Alhali kuwa sun yarda da kasancewar sauran manbobin kwamitin daga cikin waxanda Allah ya yi wa albishirin aljanna tun duniya. Ya kuma yi umurni da kashe wanda ya sava wa ra'ayin huxu daga cikinsu, da wanda ya sava wa na uku daga cikinsu, waxanda Abdurrahaman ke cikinsu. Kuma gaba xayan wannan shiri da Umar ya yi ya sava wa addini. Inji xan Shi'ar.

Ya ci gaba da cewa: Kuma a qarshe da aka bar Abdurrahaman da Ali da Usman, wai sai Abdurrahaman ya ce wa Ali: Da za a zave ka a matsayin halifa, kana ganin zaka iya jagorancin al'ummar nan bisa tafarki madaidaici? Ka ga, wai kai tsaye wannan magana, na nuna ba su da niyyar zavensa. Sannan kuma ya ce wa Usmanu: Ka yarda da, da za a naxa ka a matsayin halifa, kuma ka bautar da mutane ga 'yan gidanku a kashe ka? Ka ga wai kai tsaye wannan magana na nuna, an riga an shirya kashe shin da haka za ta faru. Inji shi.

**Martani:**

Da farko, abin da za mu ce a matsayin martani a kan wannan magana shi ne: tabbatar xayan abubuwa biyu a kan wannan zance, wajibi ne: Ko dai mu yanke mata hukuncin kasancewa qarya ta fuskar naqali. Ko kuma qoqarin canza wa tuwo suna, ta hanyar bice hasken gaskiya da qarfi da yaji. Wannan wajibi ne, saboda haxuwar hakin tantagaryar qarya, da na bobawan birni a cikin maganar.

Eh! Gaskiya ne. Akwai abin da yake tabbas ne ya faru, xan Shi'ar bai yi qarya ba a ciki. Amma babu wani abu a ciki da ke wajabta sukar lamirin halifa Umar *Raliyallahu Anhu* a ciki. Hasali ma kamata ya yi a qididdiga wannan mataki da ya xauka daga cikin manyan karamomi da kyawawan ayyukansa.

Amma a maimakon haka, sai 'yan Shi'ah suka karkata akalar wannan aiki da ya cancanci yabo, suka mayar da shi abin suka. Saboda su halinsu na jahilci da qoqarin tabbatar da kasancewar abin da bai kasance ba, da kore wanda ya tabbata. Tare da saka wa alheri rigar sharri da yi wa balbela baqin fenti. Hakan ta sa su rasa tsuntsu da tarko, ba su ga hankali balle karatu. Suka zama daidai da waxanda Allah Ta'ala ke bayar da labarinsu da cewa:

﴿وَقَالُوا۟ لَوْ كُنَّا نَسْمَعُ أَوْ نَعْقِلُ مَا كُنَّا فِىٓ أَصْحَٰبِ ٱلسَّعِيرِ ١٠﴾ الملك

*Kuma sukka ce: "Da mun zamo muna saurare ko muna da hankali, da bamu kasance a cikin 'yan sa'ira ba (67:10).*

Wannan kenan. To mu dawo kan nassin maganar tasa daki-daki.

Xan Shi'ar ya ce: kuma Umar *Raliyallahu Anhu* ya kafa kwamitin da zai yi shawara ya zavi wanda zai zama halifa bayansa. Wannan kuwa ya sava wa abin da Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya yi kafinsa.

To, savawa na xaukar ma'ana biyu: Ko dai: 1) savani na taho-mu-gama; wanda zai haifar da gaba da rashin ga-maciji tsakanin juna. Ko kuma, 2) savani na yaxuwa, wanda zai haifar da kaurin arziki da yalwa, ta yadda zai ishi kowace matsala da darga.

Misalin nau'in savani na farko shi ne, kamar: wannan ya ce: abu kaza wajibi ne. Wancan kuma ya ce: A'a haramun ne. Shi kuwa nau'i na biyu shi ne, kamar banbance-banbancen da ke tsakanin makarantar Alqur'ani wanda, a sanadiyyarsu, suka sassava a wasu wurare. Amma kuma duk da haka, kowace qura'a daga cikinsu karvavva ce a idon shari'a. Kamar yadda ingantattun hadissai suka tabbatar daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma ta dubun dubutar hanyoyi.

Wani abin da ke tabbatar da cewa wannan banbancin fahimta (savani nau'i na biyu) halas ne, ko ma wajibi, kuma yana da asali a shari'ar musulunci, shi ne abin da Ibnu baxxata ya riwaito, ta hanyar wani gagarabadan isnadi, cewa: Watarana Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce wa Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma*: "Ba don da kuna ra'ayi biyu a wasu lokuta ba, da ba zan sava ma ra'ayinku ba".

Ka ji wannan magana. Kuma gaba xayan salaf har da magoya bayan Ali *Raliyallahu Anhu* sun yarda da fifikon waxannan Sahabbai biyu. Kar ka yi wani mamaki, don jin na ce, magoya bayan Ali *Raliyallahu Anhu* wato ‘yan Shi’ah san yarda da fifikon Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* a kan gaba xayan Sahabbai, har ma da Alin kansa.

Ko shakka babu, ‘yan Shi’ah na farko a kan wannan aqida su ke. Daga baya ne al’amarin ya xauki sabon salo, lokacin da vata gari suka kunno kai. Abin da zai tabbatar maka da wannan magana shi ne abin da Ibnu baxxata ya riwaito daga cewa: Watarana Abu Ishaqas-Sabi’i ya zo Kufa. Sai Shamir xan Axiyyah ya ce: Mu je mu gaishe shi. Qare gaisawarmu ke da wuya, sai suka shiga zance. A cikin haka ne muka ji Abu Ishaqan na cewa: Wai ya aka yi ne? Ko da na bar Kufa ban san akwai wani mutum xaya a cikinta ba, da ke shakkar kasancewar Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* mafifita daraja a cikin Sahabba. Amma ga shi yanzu da isowata na ji mutane na wasu ‘yan maganganu da ban gane kansu ba.

Kuma Ibnu baxxata xin ya ruwaito daga Laisu xan Abu Sulaimu cewa: Na tarar da ’yan Shi’a na farko ba su ganin girman kowa a kan Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma.*

Kuma Imamu Ahmad xan Hambali ya ruwaito daga Masruq, xaya daga cikin mafi girman Tabi’ai, yana cewa: “Son Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* da kiyaye alfarmarsu na cikin sunna. Haka shi ma Xawisu ya faxa da Ibnu Mas’ud.

Ah! To, me ko zai hana ‘yan Shi’ah na farko su yarda da fifikon darajar Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* a kan sauran Sahabbai, tunda sane suke da cewa hanyoyi kusan tamanin na riwaya, sun tabbatar da cewa, Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce: Mafi girma da alheri a cikin wannan al’umma bayan Annabinta, su ne Abubakar da Umar.

Imamul Buhari ma ya riwaito wannan magana cikin ingantaccen littafinsa, daga bakin Hamdaniyyawa, waxanda su suka fi kowa kusanci da Ali *Raliyallahu Anhu*. Su ne fa Alin yake ce wa: “Da an ba ni mabuxin qofar aljanna, da na fara sa Hamdanawa a ciki”.

Buhari ya riwaito Muhammadu xan Hanafiyya, ya ce, na ce wa mahaifina (Ali *Raliyallahu Anhu*): Don Allah wa ye mafifici a cikin mutane bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*? Sai ya karva mani da cewa: Af! Kai ba ka sani ba? Na ce: Wallahi ban sani ba. Sai ya ce: Abubakar. Na ce: Sai kuma wa? Ya ce: Umar.

Haka kuma an riwaito Alin *Raliyallahu Anhu* na cewa: Duk wanda ya kuskura ya shigo hannuna, yana fifita ni a kan Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* sai na yi masa bulalar qazafi.

Kuma a cikin Sunan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Ku yi koyi da mutum biyu a bayana: Abubakar da Umar”.

Mu koma kan qorafin da xan Shi’ar ke.

Bismillahi!

A matsayin Umar *Raliyallahu Anhu* na shugaba, yana da cikkakiyar damar zavar wa musulmi halifa mafi dacewa daga cikinsu. Kuma abin da ya yi qoqarin yi kenan. Wanda ijtihadinsa ya tabbatar ma sa da cewa babu wanda ya cancanci wannan nauyi fiye da xayan waxannan Sahabbai shida. Ba a kuma samu wani mutum xaya a lokacin da ya musa masa ba.

Wani abin ban sha'awa ma da qayatarwa, da tabbatar da kaiwar halifa Umar *Raliyallahu Anhu* qololuwa a fagen ijtihadi da adalci da nagarta, da kauce wa son zuciya, shi ne barin wannan kwamiti ya zavi halifa daga cikinsa. Don gudun shi ya zavi xaya daga cikinsu kawai ya tabbatar, tunda duk ya yarda da su. Amma hakan ta sava wa ra'ayin sauran manbobi. Kuma ya kasance akwai wanda ya fi shi cancanta a cikinsu.

Tattare da cewa, ba a rasa wanda yafi kwanta masa a rai daga cikinsu. Amma kuma ya rinjayar da burin kwamitin yayi zaven, ko da zai zavi wanda ba shi ne, shi a zuciyarsa ba *Raliyallahu Anhu*.

Kuma ai shawara ba laifi ba ce. Musamman ga musulmi, balle manyan Sahabbai.Tunda cewa Allah Ta'ala yayi: *Kuma al'amarinsu shawara ne a tsakaninsu (42:38).* Ya kuma ce: *Kuma ka yi shawara da su a cikin al'amarin (3:159).* Kuma ko shakka babu, wannan kwamiti na shawara da halifan ya kafa, shi ne mafi dacewa da tabbatar maslaha ga al'umma a wannan lokaci. Kamar yadda abin da Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya yi a lokacinsa na zaven Umar xin *Raliyallahu Anhu* a matsayin halifansa ba tare da ya kafa wani kwamitin shawara ba, shi ne abu mafi zama maslaha a wancan lokaci. Domin kuwa halifan bai yi haka ba, sai da ijtihadinsa ya gama tabbatar ma sa da cewa Umar xin shi ne mafi cancanta, kuma lalle gadon bayansa na iya xaukar nauyin. Kuma babu buqatar kafa irin wannan kwamiti. Kuma hakan ta tabbata. Don abin can da Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya kyautata zato ga Umar ya tabbata, duniyar musulmai ta sheda.

Kuma babu mai hankalin da bai san cewa, 'yan kwamitin can, da halifa Umar *Raliyallahu Anhu* ya kafa, da suka haxa da: Usmanu da Ali, Xalhatu da Zubairu, Sa'adu da Abdurrahaman xan Aufu kowannensu na iya cike gurbin Umar ba, kukkukkuf. Saboda haka zaven cancantar da Abubakar ya yi wa Umar *Raliyallahu Anhu* daidai yake da mubaya'ar da Sahabbai suka yi wa Abubakar xin *Raliyallahu Anhu* a matsayin mafi cancanta a wancan lokaci.

Saboda haka ne ma aka riwaito xan Mas'ud *Raliyallahu Anhu* na cewa: Mutanen da suka fi kowa dacewar hasashe a duniya uku ne: 1) 'Yar Sarkin Madayana, da tace: *Ya baba! Ka ba shi aikin ijara, haqiqa mafi alherin wanda ka bai wa aikin ijara shi ne mai qarfi amintacce (23:26).* Da 2) Matar Fir'auna, da tace: *Akwai yiwuwar ya amfane mu, ko mu riqe shi a matsayin xa (28:9).* Sai kuma 3) Abubakar *Raliyallahu Anhu* da ya zavi Umar a matsayin halifa.

Gaba xayan hasashen da waxannan mutane uku suka yi a duniya, ya zama gaskiya.

Abin da ijtihadin Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya nuna masa kenan. Shi kuwa Umar *Raliyallahu Anhu* sai nasa ijtihadi ya nuna masa, kusan babu

wanda bai iya riqe muqamin halifa daga cikin waxannan mutane guda shida. Duk kuwa da yake akwai daga cikinsu waxanda suka fi wasu xaukaka da alfarma. Amma idan aka duba da kyau, za'a taras cewa suma waxanda aka fi xin suna da wasu martabobi da waxanda suka fisu ba suda. Ka ga an yi tangan kenan.

Bayan wannan kuma halifa Umar mai gani da hasken Allah, ya hangi cewa da zarar ya zavi wani daga cikinsu kai tsaye. To fa, duk abin da hakan ta haifar na tajin-tajin shi zai zama abin zargi. Saboda haka sai ya kauce, don gudun talalaviya ta kwashe shi amma kuma kafin haka, sai ya tattara waxanda suka fi kowa cancanta da matsayin ya danka masu al'amarin. Ka ga a hakan ya jefi tsuntsu biyu da dutse xaya kenan. Wato ya zavi halifan a kaikaice, amma a kai tsaye ba shi ne mai zaven ba, ya xauke haqqin Allah ya kuma xauke nauyin mutane kenan.

Kuma ko shakka babu mutanen nan shida da Umar ya xauka wa wannan al'amari, sun sami yardar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* har qarshen rayuwarsa. Babu wanda ya kai darajarsu daga cikin Sahabbai. Duk kuwa da kasancewar Manzon ya qyamaci wani abu a cikin kowannensu. Amma kuma ai duk xan Adamu xan tara, banda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma ko shakka babu da za'a xora su a kan sikeli tare da waxanda ba suba, to za su rinjaya.

Babban abin da zai tabbatar maka da haka kuwa, shi ne kasancewar rawar da halifa Usmanu ya taka, ta fi ta wanda yazo bayansa qayatarwa. Shi (Ali *Raliyallahu Anhu*) kuwa tasa ta fi ta na bayansa. Kuma babu wani Sarki a tarihin musulunci da ya taka nagartattar rawa irin wadda Mu'awiyah ya taka *Raliyallahu Anhu* abun da mutane da dama suka tabbbatar.

To, a haka, idan har za'a ce ga wani zunubi da xaya daga cikin waxannan Sahabbai keda, lalle wanda waninsu keda yafi girma da duhu. Kuma kyawawan ayyukansa ba za su kama qafar nasu ba. Wannan na daga cikin abubuwan daya kamata a sani a kuma kiyaye. A kuma fahimci cewa da wuri mai qazanta. Shi kuwa mai hankali, kodayaushe yakan auna al'amurra ne ta hanyar la'akari da qwansu da qwarqwatarsu.

To, waxannan 'yan Shi'ah da kake ji, sune mutane mafiya jahilci a cikin wannan al'umma. Suna aibanta wanda ba su so, da wani abin da wanda suke so da yavo, ya daxe da yin dumudumu da abin da yafi shi. Kuma da za'a dawo a kafa ma'aunin adalci, za'a taras da cewa wadda suke sukar da kushewa, shi yafi cancanta da yabo da sarawa, in ba don da suke manyan jahilai ba.

Wannan kenan. Shi kuwa zancen Salimu bawan Abu Huzaifata, da xan Shi'ar yayi, kamar yadda ake riwaitowa, magana ce qarama. Domin kuwa sanannen abune cewa Umar da sauran Sahabbai *Raliyallahu Anhu* sun san da cewa, babu wanda ya dace da shugabancin al'ummar sai baqwaishe. Kamar yadda littafan sunnan suka cika suka katse da haka, daga bakin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kamar yadda Buhari da Mushini suka riwaito daga Abdullahi xan Umar *Raliyallahu Anhu* wanda ya ce: Manzon Allah

*Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Wannan al'amari (halifaci) ba zai gushe daga hannun Quraishawa ba. Matuqar akwai ko da mutum biyu a bayan qasa. Wani martanin kuma ya ce: matuqar akwai mutum ko da biyu daga cikinsu a raye.

Sannan kuma cewar da xan Shi'ar ya yi wai, kwamitin can da Umar ya kafa ya haxa masu manya da qananan darajoji. Kuma a al'adance kamata yayi mai babbar daraja ya shige gaban mai qanqanuwa a komai.

To, da farkon abin da za mu cewa a nan shi ne: Xan banbancin da ke tsakanin waxannan Sahabbai na daraja, ko alama bai kai yadda xan Shi'ar ya xauke shi ba. Idan ma mutum bai kwantar da hankali da kyau ba, ba zai gane komai ba. Don fifikon darajar ba kamar wanda kega Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* ne a kan sauran Sahabbai ba. Wanda ko makaho ya sani. A kan wannan dalili ne ma, idan aka zauna tarihin shawari ake karvar ta Usmanu wani lokaci. Wani lokacin kuma a karvi ta Ali, ko Abdurrahman *Raliyallahu Anhu* domin kowane daga cikinsu nada wata daraja da waninsa baya da.

Abu na biyu: idan har abu ne mai yiwuwa daga cikin 'yan kwamitin can a samu mai babbar daraja da mai qanqanuwa, kamar yadda xan Shi'ar ya faxa, tunda zavo su aka yi, ba tare da ance wane shi ne gulbi, wane shi ne qorama ba. Wane dalili kega xan Shi'ar na cewa Ali *Raliyallahu Anhu* shi ne teku, ba ma gulbi ba shi kuwa Usman *Raliyallahu Anhu* da sauran fadammu ne, ba ma qorammu ba? Alhali kuwa muhajuruna da Ansaru, sun haxu a kan cewa Usmanu na gaban Ali *Raliyallahu Anhu* a falala. Kamar yadda Abu Sakhtayani, xaya daga cikin jigajigan malamai ya ce: duk wanda ya fifita Ali a kan Usmanu *Raliyallahu Anhu* haqiqa ya tozarta Muhajiruna da Ansaru.

Ya kuma tabbata a cikin Buhari da Muslimu, daga Abdullahi xan Umar, wanda ya ce: Mun kasance a zamanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* muna fifita Abubakar, sannan Umar, sannan Usmanu *Raliyallahu Anhu* a wani martanin kuma ya ce: Sai kuma mu qyale sauran Sahabban na Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba tare da mun fifita wani a kan wani ba.

Ka ga wannan magana babba ce matuqa, saboda tana gaya mana, yadda Sahabbai a lokacin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ke fifita darajar Abubakar *Raliyallahu Anhu* a kan sauran Sahabbai. Sannan ta Umar da Usman *Raliyallahu Anhu*. Kuma Annabin na sane bai ce kanzil ta hani ba.

Kenan wannan daraja tasu tabbatatta ce nassance ko kuma tunda Manzo bai hana ba tattare da sanin Muhajiruna da Ansaru na kan haka. Ko kuma saboda tattarar gaba xayansu su yi wa Usamanu *Raliyallahu Anhu* bai a bayan rasuwar Umar ba tare da an tilasta su, ko don rashin samun wani abu ba: ba a sami wanda ya wandare daga cikinsu ba.

Kamar yadda imamu Ahmad ya tabbatar da cewa: Babu bai'ar da mutane suka haxu a kanta kamar ta Usmanu *Raliyallahu Anhu.* Haka kuma da aka tambaye shi a kan halin da halifancin Annabta ya kasance. Sai ya ce: Duk

wanda aka yi wa bai'ar a Madina. Kuma rayuwar Sahabbai da sauran musulmi ta bunqasa, a qarshen halifancin Umar fiye da yadda take kafinsa matuqa.

Wani babban abin da ke tabbatar maka da cewa bai'ar da Sahabbai suka yi wa halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* sun yi ta ne khalisan li wajhillahi. Ba kamar yadda xan Shi'ar ke son nuna cewa akwai wata gane-ta-kai a ciki ba, shi ne, kasancewar duk da Abdurrahman, farkon wanda ya yi masa bawar, halifan bai bashi wata dukiya ko sarauta ba daga baya. Hasali ma shi ne mafi nesa-nesa da abin duniya a tsawon halifancin Usmanu *Raliyallahu Anhu* tattare da kasancewarsa wanda ya shawo kan al'amurra, a matsayin shugaban shawara, a daidai lokacin da babu Umayyata xin ba su da wani tsimi ko wata dabara. Kuma baya ga shi Usmanu xin *Raliyallahu Anhu* ba su da kowa a cikin wancan kwamiti na shawara.

Kuma duk wanda ya san irin halin Sahabbai, ya san inda ba su gamsu da cancanta da fifikon Usmanu *Raliyallahu Anhu* ba wanda ya isa ya tilasta suyi masa bai'a. Ka tuna fa Allah Ta'ala ya sifanta su da cewa: *Yana son su kuma suna son sa, masu tawalu'i ne a kan muminai, masu izza a kan kafirai. Suna yin jihadi a cikin hanyar Allah, kuma basu jin tsoron zargin mai zargi (5:54).* Bayan wannan sheda kuma, sun yi wa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai'a da alqawarin faxar gaskiya ko waye shi. Matuqar an ci iyakar haqqin Allah. Amma tattare da haka, tarihi ya tabbatar da cewa babu xaya daga cikinsu da ya qi yi wa Usmanu *Raliyallahu Anhu* bai'a, balle ya yi wani korafi.

Ka tuna dakaru, 'yan zafi masu jiran ko-ta-kwana, irin su: Ammaru xan Yasiru da Suhaibu da Abu Zar da Khabbabu da Miqdadu xan Aswadu da xan Mas'udu duk sun yi masa bai'a suna murna da xoki da Annashawa. Har xan Mas'udu ke cewa: Mun yi wa mafi girman daraja daga cikinmu bai'a. Ba mu kangare ba.

Kuma ka tuna manyan mutane irin su Abbas xan Abdul-Muxxalib, da Ubaidatu xan Samitu da makamantansu, irinsu Abu Ayyub al-Ansari da ire-irensu, duk fa sun yi wa Usmanu *Raliyallahu Anhu* bai'a.

Babu shakka a duk lokacin da masu hankali da basira suka yi wa wannan al'amari nazari qwaqwaf sai sun qara ilimi da hankali da basira, bisa waxanda suke dasu. Duk kuwa mai ilimin da ka ji yana ko karanton wani abu a cikin sha'anin, to lalle Allah bai ba shi ikon nazarinsa da kyau ba. Sai kuwa idan jahili ne wanda baisan makamar zaren ilimi da rayuwar duniya ba.

Ita kuwa cewar da xan Shi'ar ya yi wai: Umar ya soki lamirin kowane xaya daga cikin 'yan wannan kwamiti daya kafa. Ya kuma bayyana cewa yana gudun ne alhakin abin da ka iya biyowa baya idan shi ya zavi mutum xaya, ya bi shi har lahira. Saboda haka ne ya bar aikin hannun wannan kwamiti. Amma kuma wai, sai ga a kaikaice kamar shi ne wanda ya zavi halifan. Tunda ya sharxanta wa kwamitin zaven xayansu a muqamin. Ka anyi ba a yiba kenan, inji xan Shi'ar.

Matani: Eh! Gaskiya ne Umar ya yi xan qorafin a kan waxannan manbobi. Amma abin bai kai ga ace ya soki lamirinsu ba, ta yadda hakan zata

sa waninsu ya fi su cancanta da karagar. Hasali ma shi a wurinsa, babu kamarsu a wannan sha'ani, balle a fi su kamar dai yadda shi da kansa ya tabbatar. Abin da kawai yayi, wanda xan Shi'ar ke kira sukar lamiri wai,shi ne bayyana dalilin da ya sa yake tsoron zavar xayansu a matsayin halifan, balle har alhakin haka yahau kansa. Amma baya ganin wani abu na haufi, idan ya zavi mutum shida xin ya kuma yi masa muni irin wanda ya ishi mai hankali. Ya kuwa yi haka ne saboda yaqinin da yake da shi a kan cewa, kowanensu taqarqari ne daya isa xaukar kaya. Kuma ijtihadinsa ya tabbatar masa da cewa yin haka shi ne mafi zama salama, ko da wasu na ganin hakan can shi ne sawaba. Shi kuwa salama yake nema, ba don yana kyamar sawaba a karan kanta ba. Kuma haka shi ne mafi zama alheri gare shi, da al'umma baki xaya.

Wannan irin hikima na daxa tabbatar da cikar hankali da kishin addinin da halifa Umar ke dasu *Raliyallahu Anhu*.

Sannan kuma xan Shi'ar ya ce: sai kuma wai ga Umar ya yi qasa a gwiwa ta hanyar shatawa kwamitin yadda alhakin zaven zai koma hannun mutum huxu daga cikinsu, sannan uku. Har dai ya koma ga xaya tal. Wanda kuma zai kasance Abdurrahman xan Aufu. Bayan kuma shi Umar xin ya siffanta shi da rauni da kasawa.

Ka ji wannan qulli da kyau ko?

**Martani:**

Da farko dai, muna tabbatar wa xan Shi'ar cewa wannan magan irin ta 'yan sandace. Musamman da yake bai faxi yadda ta inganta ba. Baya kuwa kamata ga mutum mai hankali, ya kafa hujja da abin da ba yada toshe balle makama. Don nan take ne za'a iya kwashe masa kafafu. Kamar yadda za mu yi masa yanzu…

Abin da ya tabbata a cikin sahihul Buhari da wasu littafai, ya tabbatar da cewa wannan magana qarya ce. Domin kuwa waxannan 'yan kwamiti, su ne a qashin kansu, uku daga cikinsu suka zavi salama daga xaukar wannan nauyi suka bar uku. Sannan sauran ukkun kuma suka xorawa Abdurrahman xan Aufu fitar da gwani daga cikin biyunsu, tunda shima ya bi sawun ukkun can na farko kuma Umar *Raliyallahu Anhu* ba yada hannu a cikin wannan tsari.

Abin da zai tabbatar maka da wannan magana shi ne tabbataccen hadisin da aka riwaito daga Amru xan Maimun, wanda ya ce: kafin shexar Umar *Raliyallahu Anhu* ta qarshe ta kai ga bugawa, a lokacin da aka soke shi, ya ce: tun kafin yau wasu mutane ke neman in nada magaji, don kada a sami tajin-tajin bayan na wuce. To na danqa wannan al'amari hannun sababban nan shida. Waxanda ko da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rasu yayi matuqar yadda da al'amarinsu, wato: Ali da Usman da Xalhatu da Zubairu da Abdur-Rahmanu xan Aufu da Sa'adu xan Maliku *Raliyallahu Anhu* sannan Abdullah xan Umar ya zama Alqali. Amma kada su kuskura su zave shi a matsayin halifa.

Idan Allah ya sa Sa'adu ne suka zava, daidai. Idan kuwa wani ne, to ina horonsa da ya yi aiki da shi. Domin kuwa ba wata kasawa ko yaudara ce tasa na tuve shi ba.

Daga nan kuma sai ya ce: ina yi wa duk wanda Allah ya xorawa wannan nauyi, bayan na wuce, wasiyya da tsoron Allah Ta'ala. Kuma don Allah ya tsare alfarmar muhajiru na. mutanen nan na farko da aka zava da gidajensu da dukiyoyensu don kawai sunce Allah, ya kuma ba su haqqinsu. Haka kuma don Allah ya kula da Ansaru. Mutanen nan da suka saxaukantar da gidajensu, suka kuma yi imani tun gabaninsu, duk abin da suka yi na kyautatawa ya qarva, ya kuma yafe kura - kurarsu haka kuma ina yi masa wasiya daya kula da mutanen sauran garuruwa, yayi tayi man alheri. Domin kuwa ba don su ba, da musulunci bai kai labari ba, sun turawa magabata haushi. Suna kuma tsaye haiqan ga tara haqqin Allah na dukiya. Kada ya kula da wani abin da suka yi ko za su yi, sai na alheri kuma ya jira sai sunci sun raga, sannan a nemi yardarsu a kan saura. Haka kuma Larabawan qauye, suma don Allah ya kyautata masu. Don sune tushen Larabawa da makamashin musulunci. Idan aka tashi karvar zakka daga gare su, a kuma raba ta ga talakawa daga cikinsu. Haka kuma kafiran amana, don Allah ya tabbata ya cika duk arqawarin dake tsakaninmu dasu, bisa yardar Allah da Manzonsa. Ya kuma yaqi duk wanda ke dagagensu. Kada kuma ya xora masu duk abin da basu iyawa.

To ka ji iyakar abin da Umar *Raliyallahu Anhu* ya ce, gab akin wanda ba ya qarya.

Mun qare da wannan. Bari mu koma ga cewar da xan Shi'ar yayi, kuma wai Umar ya ce: idan bakin Ali da Usman *Raliyallahu Anhu* ya haxu to, duk wanda suka zava ya zavu. Idan kuma suka kai su uku, wato kwamitin ya rabu gida biyu, to duk wanda inda Abdur-Rahman, yake suka zava ya zavu. Kuma wai inji xan Shi'ar Umar *Raliyallahu Anhu* ya yi haka ne don ya san ba yadda za a yi bakin Ali da Usman *Raliyallahu Anhu* ya haxu a kan wani al'amari, haka suke kamar Annabi da kafirci. Kuma wai halifan ya san da cewa Abdur-Rahman ba zai kasa zaven xan Amminінsa Usmanu ba.

To a nan, muna son xan Shi'ar ya gaya mana wanda ya ce Umar *Raliyallahu Anhu* ya ce haka. To kuma tafi. Ko da ta tabbata ya ce haka xin, baya halatta da dacewa a yi masa irin wannan fassara, cewa ya kutsa haka ne don yana son a zavi Usman, yana kuma kyamar a zavi Ali *Raliyallahu Anhu*. Ai inda wannan itace manufarsa, to kai tsaye tun farko, zaice na zavi Usman ya gaje ni. Kuma babu wanda zai yi gigin musa - masa. don kuwa gashi bayan ma ya qaura xin Usman xin ne aka zava. Wanda hakan ke nuna suna son sa fiye da kowa. Kuma inda ma hakan yayi, to alqadarin Usman xin zai fi fitowa, don xa'arsu gare shi za tafi kauri a matsayinsu na mutane masu son addini da rajen aikata alheri da tabbatar da adalci. Kamar yadda muminai suka shede su. Kai I ko da akasin haka suka kasance. Kamar yadda munafukai ke zarginsu, ba za su kasa fesawa wannan zave na Umar turaren xa'a ba.

Ko shakka babu, da wannan itace manufarsa, kamar yadda na faxa a baya kaxan. To babu abin da zai hana shi tabbatar da ita, kai tsaye ba tare da wasu kewaye - kewaye ba. Tunda ba wanda yake tsoro. Wanda har hakan tasa 'yan Shi'ah nace masa: Fir'aunan al'ummar Muhammadu.

Kai kasan idan dai har halifa Umar *Raliyallahu Anhu* ba zai ji shakkun miqewa ba shi kaxai, ya zavi Abubakar *Raliyallahu Anhu* a matsayin magaji Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba. Ba kuwa zai ji shakkar tabbatar wani, ko ba Usmanu *Raliyallahu Anhu* ba, da halifanci bayansa ba. A lokacin da mutane suka riga suka saba da biyayya, musamman gare shi.

Ka ga a hankalce Umar *Raliyallahu Anhu* ba yada buqatar shirya irin wannan qungiya - qungiya don tabbatar da irin wannan sassauqar manufa. Kuma tafi na ji. Wai ma me zai ba Umar yaqi Ali saboda Usman *Raliyallahu Anhu*? ai babu wata alaka dake tsakaninsa da Usman fiye da Alin *Raliyallahu Anhu* wadda zata wajabtar da faruwar haka. Babu wata kariya tsakaninsu ta qabilanci ko akasin haka balle a ce.

Ko harma a ce wai: Umar *Raliyallahu Anhu* ya san ba yadda za a yi bakin Ali da Usman *Raliyallahu Anhu* ya haxu a kan wani al'amari xaya. Wai Shi ya sa ya shirya waccan munqisa.

Haba! Wace irin qiyayya ce wannan?

Wannan magana qarya kawai aka yi wa halifa Umar *Raliyallahu Anhu* domin kuwa ba a tava ganin halifofin a rana biyu ba, tsawon rayuwar halifan. Hasali ma dangantakar dake tsakaninsu, babu ta tsakanin xayansu da wani daga cikin sauran manbobin kwamitin gida huxu. Domin duka su biyun bani Abdulmunafi ne. Mutanen da kodayaushe kansu haxe yake tsawon tarihi.

Haka kuma cewar da xan Shi'ar ya yi wai halifa Umar *Raliyallahu Anhu* ya san cewa Abdurrahman ba zai kasa zaven Usmanu *Raliyallahu Anhu* ba, a matsayinsa na xan ammininsa, qarya ce kawai.

Na farko dai Umar bai da alaqa da wannan magana. Na biyu kuma babu wani zumunci tsakanin Abdurrahman da Usman *Raliyallahu Anhu* balle ya zama xan ammininsa. Kai i hasali ma ba 'yan qabila xaya bane. Abdurrahman xan qabilar bani Zahrata ne. shi kuwa Usman xan qabilar bani Umayya ne. kuma ma hulxar jakadancin dake akwai tsakanin banu zahrata da banu hashim tafi wadda ke tsakaninsu da banu Umayyata nesa ba kusa ba. Domin su banu Zahrata xin kawanni ne ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma daga cikinsu ne shi Abdurrahman yake. Har ma da Sa'ad xan Abi Wakkasin, wanda har watarana Annabi yayi alfahari da shi, da cewa: Sa'ad xaya ne daga cikin kawannina, mutum ya gwada mani nasa kawon.

Kai ba wannan dangantaka ta jini ba. Ko da irin zumuncin nan na musulunci babu shi tsakanin Usman da Abdurrahman. Domin kuwa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai qulla irin wannan zumunci tsakanin Muhajiruna ko Ansaru wasu - wasu ba. Ya dai qulla shi ne tsakanin jinsunan mutanen biyu. A inda shi Abdur-Rahman a matsayinsa na muhajiri ya zama xan'uwan Sa'adu xan Rabi'u Ansari. Sahabin da keda hadisi shahararre a cikin

Sihahu da wasu littafai. Babu wani malami a cikin wannan fanni da bai san da shi ba. Amma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai qulla irin wannan zumunci tsakanin Usman da Abdur-Rahman ba. Balle ace ko don shi ya zave shi. Kai! Hasali ma, ko irin wanan hulxa ta rayuwar duniya Usman bai cika yi dashi, balle.

Sannan kuma idan tsawon wannan mujadala bai sa ka manta ba. Xan Shi'ar ya ce wai kuma: Umar ya yi umurni da a kashe 'yan kwamitin idan suka kasa yi wa xayansu bayi'a har tsawon kwana uku.

Ina fatar ka tuna.

To da farko dai wannan magana qarya ce. Ko kuma idan xan Shi'ar na musu, to ya gaya mana wanda ya inganta ta. Ko tabbataccen asalinta.

Abin da kawai ya tabbata a tarihi shi ne, halifan ya hori Ansaru da cewa kada suyi nesa da kwamitin har sai an zavi wanda aka zava an kuma yi ma sa bai'a.

Sannan kuma abu na biyu: Wannan magana kamar yadda muka faxa, qarya ce. Babu wani ma'abuci ilimi daya riwaito ta. Kuma ma dai ai abin ya savawa hankali Umar *Raliyallahu Anhu* ya yihoro da kashe waxannan Sahabbai. Alhali ya san babu kamarsu a wannan al'umma. Kuma idan aka kashe su, lalle sai an yi da an sani irin matsanancin fasalin da zai faru, dalilin haka. Kuma inda gaskiya ne ya bayar da wannan umurni, to lalle ne a samu ko ya ce: bayan kun kashe sai ku naxa wane da kowane. dole ne a samu haka. Don bata yiwuwa mai hankali ya karva wa makaho sanda, ba tare da ya ba shi wata ba. Daxa ko ko ta raga ce.

Ka ga a haka wannan xan Shi'ar ya tabbata maqryaci, irin wanda bai san abin daya kamata ya rubuta ba, shar'ance da al'adance.

Kuma ma wani abin ban mamaki dake kasa tabbatar maka da cewa rashin kunyar fafilawa ya vaci shi ne, cewa suka yi wancan kisa da Umar *Raliyallahu Anhu* ya yihoro da shi ayi wa 'yan kwamitin. Hukuncin ya dadare dasu amma banda gogan nasu Ali *Raliyallahu Anhu*.

To mu qaddara cewa gaskiya ne ya bayar da umurnin. To ya za a yi da cewar can kuma da suka yi wai yana matuqar son sune ban da Ali don haka ya taqaita halifancin a da'irarsu?

Ka ga a haka kamar suna sone su haxa ruwa da wuta ne wuri xaya.

Wannan kenan. Amma kuma na san saboda tsananin kangara. 'yan Shi'ah na iya cewa, Umar *Raliyallahu Anhu* ya bayar da wancan umurni ne kawai. Amma Ali *Raliyallahu Anhu* kawai yake nufin a kai.

To sai mu ce masu: wannan ma ba ta savo, wai bindiga a ruwa. Yau da gaba xayan 'yan kwamitin za su yi mubaya'a ga wanda suka zava. Amma Ali *Raliyallahu Anhu* ya qiyi, hakan ba zai hana naxin yiwuwa ba. Balle har a nemi kau da shi. Ga al'adar irin wannan sha'ani na shugabanci ana gafartar da wanda ake jin yana iya kawo tsagaro gare shi ne idan ya wandare. Ai ka ga Sa'adu xan Ubaidata bai yi wa Abubakar *Raliyallahu Anhu* bai'a ba amma ko jan ido ba a yi masa ba. Balle xauri ko duka. Daxa balle kashi.

Ka dai sake vulo mun daddale wannan.

Kuma ai ka ga akwai masu cewa Ali *Raliyallahu Anhu* da gaba xayan banu Hashim, duk ba su yi wa Abubakar *Raliyallahu Anhu* bai'a ba sai bayan wata shida. Amma kuma kafin haka babu wanda ya yi masu ko jan ido balle duka, ko tilasta su bai'ar. To bai'ar Abubakar *Raliyallahu Anhu* kenan wadda gaba xayan Sahabbai ke jin wajibi ce a kansu. Ka ga ya savawa hankali matuqa wannan bai'a ta Usmanu. Wadda ko shi kansa Umar xin bai wajabtawa kansa balle wani.

To, aje ma duk wannan. Tarihin musulunci ya tabbatar da cewa tsawon lokacin halifancin Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* sahabba na matuqar karrama Ali *Raliyallahu Anhu* da sauran bani Hashim, fiye da yadda suke karrama sauran mutane. Harma an riwaito Abubakar *Raliyallahu Anhu* kan ce: ya ku mutane! ku kiyaye alfarmar Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* ta hanyar tsare mutuncin mutanen gidansa.

Kuma yakan taka da kafafunsa har gidan Ali *Raliyallahu Anhu* a inda yakan taras da banu Hashim anjin. Ya zauna suyi taxi: ya ba su girman suna kasancewa dangin Manzon Allah. Su kuma su bashi nashi na kasancewa halifa kuma shugabansu, harma suyi masa jinjina. A irin wannan haxuwa ce suka bashi haquri a kan rashi yi masa bai'a cikin dubu. Nan take kuma suka yi ta xaga su sai shi.

Bayan haka kuma dubban dalilai, sun tabbatar da cewa akwai matuqar qauna da fahimtar juna tsakanin Ali *Raliyallahu Anhu* da waxannan sabahabbai biyu. Abin da kuma ire-iren wannan shaqiyin xan Shi'a ke faxa qarya ne. Ah! qarya ne mana. Kai ka san da Sahabban na da qudurin cutar da Alin *Raliyallahu Anhu* a lokacin da suke halifofi suna da wannan iko. Ba sai sunyi qoqarin yin haka ta kure shi daga halifancin ba. Abun bai kai can ba.

Qarya ce da rennin hankalin mutane 'yan Shi'ah ke yi, suce wai Sahabban sun zalunci Ali *Raliyallahu Anhu* a daidai lokacin da yake iya yi wa kansa faxa. Amma kuma sun kasa zaluntarsa a lokacin ba su da wani qarfi ko iko a kan haka, ko da sun so. Ka ga a hankalce, lokacin da suka yi qarfi ne, mutane na sauraransu ya kamata ace sun zalunce shi xin, da suna da kudurin haka ko?

Haka kuma ita ma cewar da xan Shi'ar ya yi wai Umar xin ya yi wani umurnin da kashe duk wanda ya savawa mutum huxu ko uku da bakinsu yazo xaya, kuma cikinsu da Abdurrahman, qarya ce.

To muma qaddara ya ce hakan, to sai me kuma? Ai hakan ba ta savawa addini ba. Hakan ma yafi dacewa. don a kashe wanda ke son tayar da fitina ibada ne. kamar yadda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: duk wanda ya taras daku tsintsiya maxaurinki xaya, kuna da'a ga mutum xaya, ya nemi raba kanku, to ku sare kansa da takobi ko xan waye.

Abin da kawai ya tabbata shi ne Umar *Raliyallahu Anhu* ya yi umurni ne da kashe duk wanda ya yi wa wani bai'a, ba tare da ya shawarci sauran musulmai ba. Kuma ya dogara ne akan wannan hadisi da ya gabata.

Amma kashe wani don xai ya qi yin bai'a, bai kuma nemi tayar da wata fitina ba, balle raba kan musulmai. Umar *Raliyallahu Anhu* bai yi wannan umurni ba. Hasali ma kashe irin wannan mutum ba ya halatta.

Haka kuma isharorin da xan Shi'ar ya ambata wai na kashe Usman da qin zaven Ali *Raliyallahu Anhu* duk qarya ne, Umar bai qulla haka ba.

Cewar da Abdur-Rahman yayi : idan ka aikata (kaza) wallahi suna kashe ka. Labari ne kawai yake bayarwa, ko ya riga ya bayar ba. Kamar yadda cewar da ya yi: ba za su zave shi ba. Ita ma labarin abin da yake ganin zai faru ne kawai yake bayar wa. Ba wai umurni ne yake bayarwa da aikata hakan ba.

Duk da yake gaba xayan waxannan lafuzza, a cikin irin wannan siyaki basu tabbata daga bakin halifa Umar *Raliyallahu Anhu* ba. qarya ce aka yi masa.

Allah Ta'ala shi ne mafi sani.

### 2.57 Xan Shi'ar ya Dira A Kan Usman

Dama na gaya maka cewa ina zaton xan Shi'ar nan zai ta kan halifofin nan uku ne, xaya bayan xaya. Ga shi tako tabbata. Ya qare da Umar bayan Abubakar *Raliyallahu Anhu* yanzu kuma ya dira kan Usmanu *Raliyallahu Anhu* inda ya fara sukar lamarin halifan da cewa:

shi kuwa Usmanu, babban laifinsa shi ne xaukar muqami ya danqawa waxanda ba su dace dasu ba. wanda hakan tasa a qarshe, babu abin da suka sukkuna wa jama'a, in banda yaxa fasiqanci da varna a bayan qasa. Wani kuma daga cikinsu suka xaure wa zalunci gindi. Kuma abin ban ta kaici, inji xan Shi'ar duk waxanda yaba muqaman nan 'yan'uwansa ne na kusa. Saboda haka, da mutane suka yi qorafi a kansa, yayi kunnen uwar shege dasu.

Ka ga Walidu xan Ikibata, wanda halifan ya naxa gwamna, babu abin da ya aje sai shan giya. Har watarana ta kai shi gaba mutane salla yana lage. Shi kuwa Sa'idu xan Asi wanda halifan ya kai Kufa, aika - aikar da ya yi bata faxuwa. Wadda har tasa mutanen garin suka kore shi. Sai Abdullahi xan Sa'ad xan Abi Sarhu, wanda ya kai masar. Shi kuwa saboda tsanancin zaluncinsa saida talakawansa suka kawo qararsa wurin halifan. Amma saboda qin Allah, sai halifan ya aika masa a rubuce, cewa wannan ba komai bane, Ya ci gaba da mulkinsa yadda ya saba. Ya aika masa da wannan saqo ne asirce, savanin abin da ya rubuta masa a bayyane. Ya kuma yi masa umurni da kashe wani mutum da ake kira Muhammad bin Abubakar.

Haka kuma dai inji xan Shi'ar, Usman ya naxa Mu'awiyah gwamnan sham, inda yaje ya shimfixa maqaqiyar tabarmar fitina, haka kuma ya kai Abdullahi xan Amru a busra. Shima yayi ganin damarsa a can. Qarewa da qarau ma, sai ya danqa wa Marwanu ragamar gudanar da komai. Har da tasarrafi da hatiminsa na halifanci. Wanda a qarshe hakan ta zama sanadiyar kashe Usmanu *Raliyallahu Anhu* wutar fitina ta kama sosai a cikin al'umma. Kafin haka inji xan Shi'ar, halifan ya kasance yana xibar dukiya mai yawa daga baitil mali yana ba 'yan'uwansa da iyalinsa. Wanda har watarana ya xibi

dinari dubu xari huxu yaba wasu kuraishawa huxu dake auren ‘yayansa mata. Ya kuma ba Marwanun can dinari dubu biyu.

Ya ci gaba da cewa: Usmanu ne, bayan yahau gadon halifanci, yasa aka yi wa xan mas’ud dukan tsiya, har saboda yana suka tare da kafirtarsa har ransa ya fita. Haka yasa aka yi wa Amru har fatar jikinsa ta farfashe. Alhali kuwa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Amru wata fata ce daga cikin fatun idona. Kuma ina jin wasu la’ananni ne za su kashe shi. Waxanda nake fatar Allah ba zai sasu cikin cetona ba, ranar qiyama. Shi ma Amru ya sami wancan xanyen hukunci ne saboda sukar halifan da yake yi.

Haka kuma wai kafin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kwanta dama, sai da ya kori ammin halifan, Hakamu xan Abilas, tare da xansa Marwan daga birnin Madina. Birnin da ya yi masu qarshen xan goma tsawon rayuwar manzon da halifa Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* amma wai hawan Usmanu karagar keda wuya sai ya dawo dasu birnin. Ya kuma naxa Marwanun magatakardansa, kuma sarkin fada. Alhali Allah Ta’ala ya ce: *Ba zaka sami mutane masu yin imani da Allah da Ranar lahira ba suna soyayya da wanda ya sava wa Allah da manzonsa, ko da sun kasance ubanninsu ne, ko xiyansu (58:22).*

Kuma inji xan Shi’ar, Usman *Raliyallahu Anhu* xin dai ne wanda ya kori Abu Zarrin daga Madina ya koma Rabzata, bayan shima ya yi masa xan Karen duka. Alhali kuwa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: kasa bata tava xaukar wani mutum mai faxin gaskiya inuwa ba kamar Abu Zarri. Ya kuma ce: haqiqa Allah ya yi mani wahayin cewa akwai wasu Sahabbai nawa da yake matukar so. Saboda haka ni ma ina so su. Sahabbai suka tambaye shi su waye waxannan ya Manzon Allah? Sai ya ce : limaminsu shi ne Ali, sai Salmanu da Miqdad da Abu Zarri.

Kuma wai halifan ya keta alfarmar hukuncin Allah. Saboda yaqi kashe Ubaidullahi xan Umar wanda ya kashe Hurmazanu bawan Ali *Raliyallahu Anhu* wai Alin ne ya tashi tsaye yana qarsheta dai wurin Mu’awiyah ya fake . kuma wai halifan yaso yaqi zartar da hukuncin shan giya ga Wahdu xan Ukbata, saida Ali *Raliyallahu Anhu* ya karvi aikin a hannunsa ya zartas, yana mai cewa: bata yiwuwa a tozarta hukuncin Allah ina nan kuma raye.

Haka kuma wai Usman *Raliyallahu Anhu* xin ne ya bidi’ar da kiran salla na biyu a ranar juma’a. har aka wayi gari hakan ta zama sunna a yau. Kuma wai saboda waxannan halaye ne nasa, gaba xayan musulunci suka juya masa baya har suka aika shi lahira, tare da yin Allah waddai da ayyukansa. Suka yi masa rakiya da cewa : kaqi fita yaqin Badar, ka fita na Uhudu ka gudo. Kuma bada kai aka yi bai’atur - Ridhwan.

Xan Shi’ar ya kamala da cewa: irin waxannan miyagun labarai a kan Usmanu ba su da iyaka.

Martan: kafin mu shiga fixar wannan magana dalla-dalla tare da warwarar zare da abawarta, muna tabbatarwa xan Shi’ar da cewa, ai ba lalle Sarkin mugun ba faxa ya zama mugu. Kuma daga tai dahakimai su cuci sarkinsu, a

tarihin musulunci bag a halifa Usmanu aka fara ba. Cutar da wakilan Ali *Raliyallahu Anhu* a garuruwa suka guma masa, tare da yin yamma a duk lokacin da ya yi gabas, tafi wadda wakilan Usman *Raliyallahu Anhu* suka yi.

Akwai rubuce-rubuce da dama da aka yi a kan wasu waqilai da Alin *Raliyallahu Anhu* ya naxa suka kwashe dukiyar talakawansu. Wasu kuma suka bar shi, suka koma gindin Mu'awiyah. Kuma ta tabbata Alin *Raliyallahu Anhu* yayi aiki tare da Zayyadu xan Abu sufyanu, baban Abdullahi xan Zayyadu, makashin Husaini, a matsayin waqilinsa. Haka kuma yayi da Al-ashtar An-Nakh'i da Muhammad xan Abubakar da makamantarsu. Duk a wannan matsayi. Kuma kai kasan Mu'awiyah xan Abu Sufyanu *Raliyallahu Anhu* yafi duk waxannan zama mutumin kirki ga duk mai hankali.

Sannan kuma naxa 'yan'uwa da makusanta muqamai baga halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* ne karau ba. Balle 'yan Shi'ah su addabe shi damu. ai tarihi ya gaya mana cewa a lokacin da Ali *Raliyallahu Anhu* ya zama halifa shima ya naxa nasa 'yan'uwa da makusanta, na wajen uwa da uba. Kamar irin su: Abdullahi da Ubaindullahi ''ya'yan Abbas. Ya kai Ubaidu a yaman, Qasimu xan Abbas xin kuma Makka da Daya. A Madina kuma ya naxa Sahlu xan Hunaifu a matsayin gwamna. Wasu malaman tarihi kuma suka ce: a'a Samamatu xan Abbas ne ya kai can. A yayin da ya kai Abdullahhin can xan Abbas, harwayau, Barra. A masar kuma ya kai xan 'yaye da renonsa, wato Muhammad xan Abubakar.

Kuma qarewa da qarau ma, saboda tsananin mamaya, handama da babakere, Aliyun *Raliyallahu Anhu* bai bar duniya ba saida ya yi wasicci a kan kada a fitar da halifanci daga hannun zu'arsa, xaya bayan xaya. Kamar yadda Shi'ah 'yan-sha-biyu ke faxawa duniya.

Ina fatar xan Shi'ar ya san wannan tarihi:

Kuma kai mai karatu, ka san idan wanda ya naxa danginsa sarautu da muqamai ya yi wani abin qi da kyama. To abin da waninsa yayi a qaqaice masu uwar muqamai, wato halifancin yafi zama laifi. Musamman kuma idan aka taras 'ya'yansa da jikokinsa ne, ya yi wa wancan qaqacin ba danginsa ba a wajen Uba kamar yadda wancan yayi. Kuma ma a kan wannan ma'auni ne wasu malaman fiqihu suka yanke hukuncin cewa, duk wani waqili ko waliyin da baya isarwa kansa ga wata hulxa ta ciniki, to baya halatta ya waqilci xansa a irin wannan mu'amala. Kuma ko da dukiya ce aka ba shi don yayi kyauta da ita ga duk wanda yaga dama, to wanda yaba shi ba zai karvarwa kansa ko xansa ita ba, a xayan zantukan.

Haka kuma malaman sun karu da junansu sani, a kan halacci da yiwuwar halifa ya yi wasicci da xansa ya gade shi. Wasu suka yarda da ha kan wasu kuma suka ce, faufau. Kuma a wurin mafi yawan malamai, ba a karvar shedar mahaifi ga dansa. Amma shedar mutuma ga amminsa karvavva ce. Haka hukuncin yake a cikin sauran hukunce-hukunce.

Wato abin da muke son fitarwa a nan shi ne, a shar'ance, xa da mahaifi abu xaya ne ya rabu biyu. Haka kuma abin da ke tsakaninsu na haqqoqi. Kamar

yadda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: da mutum da dukiyarsa duk mallakar mahaifinsa ce. Ya kuma ce: babu wanda keda xamar tayar da kyamutar da ya yi. Sai fa idan xan cikinsa ya yi wa.

Wannan kenan. Amma kuma da 'yan Shi'ah za su ce: Ai Ali *Raliyallahu Anhu* yayi abin da ya yi ne da umurnin Allah da Manzonsa.

To sai mu ce masu: Eh! To, ba mu musun kasancewar Ali *Raliyallahu Anhu* halifa nagartacce, kamar yadda Usmanu *Raliyallahu Anhu* yake. Amma kuma koba musan dalilin kowanensu ba, a kan abin da ya yin. Duk mai hankali zai fi shakku da zargin Ali fiye da Usman *Raliyallahu Anhu*.

Amma kuma na san 'yan shi'ah za su kawai qale ni biris ne, suce wata qila ko ban gane abin da suke nufi ba. Alhali kuwa na gane.

Suna sone suce: Ali na da hujja a kan wancan aiki da ya yi.

To naji na kuma yarda. Amma ina tabbata masu hujjar da Usmanu *Raliyallahu Anhu* keda ita tafi tasa nesa ba kusa ba. Don na san iyakar abin da za suce shi ne, ai Ali *Raliyallahu Anhu* Ma'suni ne, duk abin da ma ya aikata daidai ne a shari'a. saboda haka sai a kame baki daga sukar sa haka nan. To wannan ma naji kuma na yarda. Amma kuma ina tabbatar masu da cewa hujjar da kega Usman *Raliyallahu Anhu* ta kasancewarsa mujtahidi, tafi iya sa masu sukar sa su saurara, ta kuma fi zama kusa ga hankali da naqali.

Allah dai ya sawwaqa.

Idan ka kwantar da hankali , za ka fahimci cewa iyakar abin da xan Shi'ar ke guri da wannan aiki nasa tun farkonsa, shi ne ya shafawa mutanen da lafiyayyen hankali da ingantaccen naqali suka tabbatar da fifikonsu a kan takwarorimu qashin kaji. A lokaci xaya kuma ya yi wa waxanda ake bin wancan tsarki. Duk ta hanyar sukar wadancan da yabon waxannan, kamar yadda Nasara suka yi tsakanin Annabawan Allah. Suka qasqanta darajar waxanda Allah ya xaukaka daga cikinsu, tare da nuna darajarsu bata ko kai ta Sahabban Annabi Isa *Alaihis Salamu* ba. Shi kuwa Isan Allah ma sukutum.

Babban abin ban ta kaici da mamaki ma duk bai fi yadda suka naxawa Sahabban na Annabi Isah *Alaihis Salamu* rawanin ma'asumanci ba. Tattare da kasancewar darajarsu ko gata Annabawa ba ta kai ba. A lokaci guda kuma suna sukar lamirin Annabawan. Kamar Annabi Sulaimanu da waninsa.

Kai! Ba Sulaimanu kawai ba. A wajen nasara darajar Sahabban Annabi Isah *Alaihis Salamu* tafi ta Annabi Ibrahim da Muhammad *Alaihis Salamu* ka kuwa san dalilai da yawa na shari'a sun tabbatar da fifikon darajar waxannan Annabawa biyu a kan Isan kansa, balle Sahabbansa. Amma kaji aqidar nasara a kansu.

Irin wannan aiki na jahilci kuwa, da shishshigi na daga cikin abubuwan da Allah Ta'ala ya hana nasara yi. Inda ya ce: *Ya mutanen littafi! Kada ku zurfafa a cikin addinku. Kuma kada ku faxa ga Allah face gaskiya. Abin da aka sani kawai, Al-Masihu Isah xan Maryama Manzon Allah ne, kuma kalmarsa, ya jefa ta zuwa ga Maryama, kuma ruhi ne daga gare shi (4:171).*

To yadda ka ji haka, haka 'yan Shi'ah suke, su da Nasara ba wani banbanci.

Eh! Ba wani banbanci mana a tsakaninsu. Tunda su ma shishshiginsu yasa sunce Ali *Raliyallahu Anhu* Allah ne. to ka ga a nan ma har gwamma Nasarawa dasu. Don Isa Annabi ne, to Ali fa. A yayin da wasu ragilawan ke cewa Annabi dai ne shi Alin ba Allah ba. To ka gasu waxannan dai- dai suke da mabiyan Musailamatul-Kazzabi, waxanda suka yarda da wani Annabi bayan Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* illa dai shi Ali *Raliyallahu Anhu* ba yada wani laifi cikin wannan al'amari. Don ba shi ne ya kira kansa Allah ko Annabi ba. Savanin Musailamatu da takwarorinsa.

Su kuwa Shi'ah 'yan-sha-biyu abin da suke iqirari shi ne, imamancin Ali *Raliyallahu Anhu* tabbataccen abune bisa nasu. Kuma shi da, da yawa daga cikin zuri'arsa duk ma'asumai ne. Kuma wai sauran Sahabbai sun zalunce su.

Ma'asumancin nan da kake ji, ma'anarsa a wurinsu daidai take da ta Annabci. Domin kuwa wajibi ne wai a yi wa ma'asumi xa'a a cikin duk abin da ya faxa, sava masa haramun ne. Ka kuwa san Annabawa kawai ne keda wannan matsayi. Saboda sune Allah Subhanahu WaTa'ala ya umurce mu da yin imani da abin da aka saukar masu, inda ya ce: ku ce: "mun yi imani da Allah, da abin da aka saukar zuwa gare mu, da abin da aka saukar zuwa ga Ibrahim da Isma'ila da Ishaka da yaqubu da Jikoki, da abin da aka bai wa Musa da Isah, da abin da aka bai wa Annabawa daga Ubangijinsu, bamu rarrabewa a tsakanin kowa daga gare su, kuma mu a gare shi masu salamawa ne (2:136).

Ka ga a nan Allah ya umurce mu damu ce: mun yi imani da abin da aka ba Annabawa. Kuma gaba xayan musulmi sun yi ittifaqi a kan cewa imani dakowane Annabi wajibi ne. duk kuwa wanda ya kafirce wa waninsu to kafuri ne. idan da kuma izgilin zagin xaya daga cikinsu wani yayi to jininsa ya halatta inji malamai.

Wannan matsayi kuwa na Annabawa ne kawai, babu wani wAliyu ko shugaba ko fasihi ko malami ko waninsu da keda irinsa. Duk kuwa wanda ya ce ga wani mutum wai shi ma'asumi ne da imani da duk abin da ya faxa yake wajibi, bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* to yana aufin shi ma Annabi ne.

Eh! Haka yake nufi mana ko da kuwa bai ambace shi da sunan ba. Kuma babu wani banbanci tsakanin wannan da Annabawan bani Isra'ilu.Waxanda aka umurta biyar shari'arttawa.

Wannan kenan. Sannan kuma sanannen abune cewa irin waxannan kudurce - kudurce na wuce gona da iri, da qoqarin samarwa da wani gunki a haxa shi da Allah da manzonsa a bauta, ya savawa Addinin Musulunci, Alqur'ani da Sunna da ijma'in al'umma da malamanta duk ba su yarda da haka ba. Ga kuma abin da Allah Ta'ala ke cewa: *Ya ku waxanda suka yi imani! Ku yi xa'a ga Allah, kuma kuyi xa'a ga manzonsa, da ma'abuta al'amari daga cikinku. Idan kun yi jayayya a cikin wani abu, to ku mayar dashi zuwa ga Allah da manzonsa (4:59).*

Ka ga ashe kenan duk wanda ya samar da wani mutum ya kuma ce ma'asumi ne, bayan Manzon. Wanda kuma duk abin da ya faxa gaskiya ne. to yana nufin kenan wajibi ne a mayar da abin da ya faskara gare shi. Wannan kuwa ya savawa umurnin Alqur'ani.

Domin kuwa Manzo ne kawai Alqur'ani ya wajabta yi wa xa'a maras adadi, ba ma'asumi ba kamar yadda Shi'ah 'yan-sha-biyu ke cewa, ya kuma tabbbatar da alwashin farko ga duk wanda ya sava masa. Tabbataccen wannan magana. Shi ne abin da Allah Ta'ala ke cewa: *Kuma waxannan da suka yi xa'a ga Allah da Manzonsa, to, waxannan suna tare da waxanda Allah ya yi ni'ima kansu daga Annabawa da masu yawan gaskiya, da masu shahada, da salihai. Kuma waxannan sun kyautatu ga zama abokan tafiya (4:69).* Ya kuma ce: *to, wanda ya savawa Allah da Manzonsa, to, lalle yana da wutar jahannama, suna masu dawwama a cikinta har abada (27:23).*

Ka ga anan da wurare da dama Alqur'ani ya nuna cewa gidan aljanna shi ne sakamakon wanda ya yi xa'a ga Manzo. Amma bai sharxanta haka ga wani don yayi xa'a ga wani wai shi ma'asumi ba duk kuwa irin yadda zai yi xa'a ga ma'asumi to makomarsa ita ce wuta, matuqar bai yi xa'a ga Manzo ba.

Domin Manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne Alfijirin da Allah ya ware 'yan aljanna daga 'yan wuta da shi. Ya kuma sa shamaki tsakanin fajirai da nagatattun bayi da albarkarsa. Ya kuma yi katangar qarfe tsakanin qarya da gaskiya, da bata da shirya, da sanadarinsa. Wanda kuma tahowarsa ce ta kafawa shaqiyai tasu bukka daban, ta kuma kafa wa Sa'idai tasu. Shi ne wanda ake yi wa xa'a a rabbanta, a saba masa a vakita. Babu kuma mai irin wannan daraja sai shi *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

A kan haka ne, kan gaba xayan malaman da suka naqalci sirrin Alqur'ani da sunna, ya haxu a kan cewa babu wanda yafi qarfin a xauki maganarsa in anso, ko a saka ta kwandon shara in anso sai mijin Khadija baban Zainab *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi kan wajibi ne duk abin da ya faxa a gasgata, duk abin da ya yi umurni kuma a aikata. Saboda shi ma'asumi ne da komai ya faxa umurni ne daga Allah Subhanahu WaTa'ala ba son zuri'arsa ba. Don baya dashi. Shi ne kuma wanda Allah zai tambayi mutane a kan yadda suka xauke shi, ranar qiyama. Kamar yadda Allah Ta'ala ya faxa mana: sa'annan lalle ne muna tambayar waxanda aka aika zuwa garesu, kuma lalle muna tambayar manzanni (7:6) .

Shi ne kuma wanda Allah zai jarraba mutane a kansa, a cikin qaburburansu yasa ace wakowannensu: waye Ubangijinka? Mene ne kuma Addininka? Kuma wanene Annabinka? Wace irin sheda kake iya bayarwa a kan manzon da aka aika maku? A nan ne Allah zai taimaki masu imani na gaskiya, ya ba su ikon cewa: Annabinmu dai shi ne xan Abdullahi (Muhammadu) bawan Allah ne kuma Manzonsa. Ya zo mana da walihahhen abubuwa da shirya kuma munyi imani dashi mun bishi.

Da mutum zai kuskure ya ambaci wani ba Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba, kamar wani Sahabi ko tabi'i. Ko wani malami, to kashinsa ya bushe. Don lokacin ba a son jin sunan kowa in ba shi ba.

A taqaice dai, kada inji ka da nisa. Abin da kawai muke son tabbatar da wannan dogon karatu shi ne, duk uzurin da wani zai iya kawowa, don ya ceci wuyan Ali *Raliyallahu Anhu* a kan abubuwan da ake qorafi a kansa, to akwai dubunsu da qari, da ake iya kawowa don a daxa gyara wuyan rigar Usman *Raliyallahu Anhu* a kan shigen waxannan abubuwa.

A taqaicen taqaitawa ma ka ga, Ali *Raliyallahu Anhu* ya yaqi musulmi tantagarya saboda kujerar halifanci, har aka salwantar da rayukan jama'a da dama. Kuma tsawon halifancinsa bai yi yaqi da kafirai balle yaci garuruwansu, xaukar musulunci ta faxaxa ba. Babu wani ci gaba da musulmi suka samu a lokacinsa. Kuma ya ba waxanda ya ga dama daga cikin makusan tansa muqamai, kamar yadda Usman *Raliyallahu Anhu* yayi. Illah dai hikimar Usman sun fi nasa xa'a da misantar sharri.

Ita kuwa dukiyar da ake zargin Usmanu *Raliyallahu Anhu* wai da Almubazzarantarwa, halifan yana da hujja a kan haka (tawili) kamar yadda wai Ali *Raliyallahu Anhu* keda tashi hujja (Tawuli) a kan zubar da jinin musulmi. Ka kuwa san jinainai sufi dukiya haxari ko?!

Sannan abu na biyu kuma shi ne, wannan nassi kuke ta gogogo dashi, a matsayi hujjar Ali *Raliyallahu Anhu* a kan wannan abu da ya yi, ku kanku kun kasa haxa kanku a kansa, idan wasunku suka yi gabas sai wasu suyi yamma. Wannan kuwa shi ke tabbatar da cewa gaba xayanku baku da wata taqammar hujja. Tunda 'yan kame - kame ne da kurin qarya kowannen ku keyi. Kuma jumhurun malamai sun tabbatar da haka.

Wannan kenan. sannan abu na ukku kuma, da za'a kalli abin da halifa Usmanu yayi a bawa banu Umayyatu muqamai, da idon taura, to za'a fahimci cewa wani abune kamar sunna. Kamar yadda shi halifan kan kafa hujja a duk lokacin da aka qalubalance shi, da cewa: ai bani na fara ba: ko Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi aiki dasu a lokacin da yake raye. Kuma halifa, Abubakar *Raliyallahu Anhu* ma yayi aiki dasu. ba kuwa don suna danginsa ba, balle a tuhumce shi. Kai har Umar ma bai ki suba.

Hasali ma iya saninmu ba musan wata qabila da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yawaita aiki tare da 'ya'yanta, daga cikin qabilun Larabawa, kamar banu Abdush-shams. Ko banza qabilace mai tsananin yawa da gabaci. Wanda hakan tasa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya naxa Uttabu xan Asyad dan Abi Aisu xan Umayyata gwamnan qasa mafi daraja, wato Makka. Da fatar hakan ta taimaka ga bunqasa musulunci. Ya kuma kai Abu sufyanu xan Harbu xan Umayyata a Najiranu. Khaddu xan sa'id xan Asi ya kai shi Wan'a'al-yaman bayan yasa shi karvar zakka daga banu mazhajin. Yana yamen din ne a matsayinsa na gwamna Allah ya karvi ran manzo *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Haka kuma manzon ya kai sa'id xan Asin taima'a da Haibara da sauran Alkaryun Uraibah, don ya rike su. Ya kuma sa

Abban dan sa'idun kula da balahyoyi.daga nan kuma ya yi masa canjin aiki zuwa Bahrain, bayannan xauke Ala'u dan Hadhrami daga can. A can ne Abbanun ya ci gabada aiki har qarshe rayuwar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* haka kuma manzon ya yi aiki da walidu dan ukubata. Wanda a kansa ne ma Allah Ta'ala ya saukar da: idan fasiqi ya zo muku da wani babban labari, to, ku nemi bayani, domin kada ku cuci wadansu mutane a cikin jahilci (49:6).

Ka ga a haka halifa Usman nada cikakar hujja ta cewa: ai na raya sunnar Annabi ne. Don na yi aiki da waxanda ya yi aiki dasu.

Kuma irin wannan aiki da Usman *Raliyallahu Anhu* ya yine Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* suka yi kafinsa. Don Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya yiaiki da Yazid xan Abu Sufyanu xan Harbu a yaqin da aka ci sham, a matsayi shugaba. Kuma da Umar *Raliyallahu Anhu* yazo bai canza masa wurin aiki ba. Bayansa ne kuma Umar xin *Raliyallahu Anhu* ya maye gurbinsa da xan'uwansa Mu'aiwiyya.

Wannan magana da muke gaya maka ta aikin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi da waxannan mutane tabbatattace. Matsayinta ma a wurin marubutan ilimi ya kai na mutawatura. Wani sashe nata ma har malaman hadisi sun karvetada hannu biyu - biyu a wannan matsayi. A yayin da sashenta ma daga bakinsu ne malamai suka jita. Kuma a jumlance ma dai babu wani daga cikinsu dake musun kasancewarta gaskiya.

### 2.58 Mu Zuba Zuwa

Wannan Martani da muke yiga wannan xan Shi'ar a kan cin mutuncin halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* da ya yi bai tsaya nan ba. Mun xan yaxa zango ne mu sha ruwa mu koma daga. Yanzu kuma tunda mun nunfasa, to mu zuba zuwa.

Xazu kaxan mun yi qoqarin bayyana dalilan halifan ne a kan wadancan abubuwa da xan Shi'ar ke qorafi, tare da suka. To yanzu kuma, tattare da waxancan dalilai da muka bayyana, mu qaddara halifan bai dace da sawaba. To ko a hakan bai cancanci cin mutunci da tozartawa ba ga duk mai hankali da ilimi.

Domin kuwa a shari'ance babu wanda yafi qarfin kuskure baya ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Wannan ita ce qa'ida, halifofi da waxanda basu ba, duk na iya faxawa a cikin kuskure. Wannan abune ja'izi a haqqinsu. Amma kuma abune mai sauqi ga Allah (subhanahu wa ta;ala) ya gafarta masu zunuban kurakuransu, ta hanyar la'akari da xinbin kyawawan ayyukansu. Ko kuma ya jarabce su da waxansu musibu irin waxanda ke karkare kantar zunubai da iznin Allah. Ko kuma ta wata hanya da ba wannan ba.

To duk kuwa wani laifi da za'a iya cewa halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* yayi bai wuce masa yin kuskure ba. Kuma a waje xaya yana da wasu sanadaran gafara da malalonsu ke iya shafe zunuban har gaba. Xauki misalin zamansa da sahun farko a shiga musulunci, da qarfin imaninsa, da irin jihadin da ya yi, da

sauran ayyukan xa'arsa zuwa ga Allah, ta kuma tabbata cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi masa kyakkyawar sheda tare da albishirin shiga Aljanna a kan waxansu Bala'o'i da za su faxa masa.

To kuma abune tabbatacce cewa halifan ya tuba ga Allah, tuba irin ta cikon sunna, a kan duk abubuwan da ake zarginsa da aikatawa. Kuma ga jarrabawar da Allah Ta'ala ya yi masa da gwagwarmayar musulunci. Wadda ta zama sanadiyar rasa ransa ba tare da ya yi wani fargaba ko zarewa ba. Wannan kisan gilla da aka yi masa da sauran bala'o'i da ya haxu dasu kafin haka na daga cikin nau'o'in sanadaran da Allah kan karkarwa bawansa zunubai saboda su. Gashi kuma ya mutu shahidi.

Ba halifa Usman *Raliyallahu Anhu* kawai ba. Ko imamu Ali *Raliyallahu Anhu* qololuwar abin da Harijawa da sauran magabatansa ke zarginsa dashi, bai wuce zama kuskure ba ko zunubi. Kuma shima a wuri xaya yana da tarin ayyuka na alheri, irin waxanda haskensu yafi qarfin duhun zunubi komai girmansa ya bice. Waxanda suka haxa da kasancewarsa xan gaban goshin musulunci, da qarfin imaninsa, da jihadin daya zuba, da wasu ayyuka na xa'a waxanda ba waxannan ba. Kuma shi ma gashi Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi masa kyakkyawar sheda, tare da busharar shiga Aljanna. Kuma ta tabbata shi ma ya nemi gafarar Allah ta gaba xaya, ya kuma yi nadammar abubuwan da suka faru sanadinsa ga shi kuma shima ya mutu shahidi.

Ka ga wannan qa'ida bakandamiya, ta isa sa mai hankali kame bakinsa daga abubuwan da dai - daikun Sahabban nan suka aikata, balle har ya yanke masu hukuncin zama wajibi ko mustahabbi. Matuqar buqatar hakan bata taso ba.

Ka ga kenan, a kan haka, ko dai cewar da xan Shi'ar ya yi wai halifa Usman *Raliyallahu Anhu* ya naxa waxanda ba su cancanta. Ko kuma ya kasance basu cancanta xin ba. Wato ijtihadin nasa ya kuskure kenan. To ko a haka bai cancanta sukar lamiri ba. Don yana da lada a wurin Allah a matsayinsa na mai ijtahidi.

Kuma ba halifa Usman ba, ko Annabawa sukan zaci abu, ya kuma kasance ba hakanan ba.

Xauki mi'salin Wahdu xan Ukubatu, wanda ake ta ganin laifin halifan, saboda ya bashi muqami. Ai tafsirai da hadisai da dama, da littafan sura sun tabbatar da cewa, watarana Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tura shi karvo zakka daga wajen wasu Larabawa. Isarsa kusa da tungarsu keda wuya, sai suka yo tururuwa don su haxu dashi. Shi kai gogan naka sai ya zaci sun fito ne don su gama dashi. Nan take sai ya aikawa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da signal cewa gasu nan za su yaqe shi. Nan take sai ya aika wa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi shirin aikawa da runduna don ta kama masa. Sai Allah Ta'ala ya saukar masa da ayar da ke cewa: yaku waxanda suka yi imani! Idan fasiqi yazo muku da wani babban labari, to ku

nemi bayani, domin kada ku cuci waxansu mutane a cikin jahilci, saboda haka ku waye gari kuna abin da kuka aikata kuna masu nadama (49:6).

To ka ga, idan har wani abu na iya shigewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* duhu, to waye Usman *Raliyallahu Anhu* da hakan ba za ta iya faruwa gare shi ba?

Amma duk da haka na san fitsararrun ('yan Shi'ah) na iya cewa, ai bayan faruwar haka ne Usmanun ya naxa shi.

To, sai mu karva masu da cewa, ai qofar tuba buxe take kodayaushe. Ai ta tabbata a zamanin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa Abdullahi xan sa'ad xan Abu Sarhu yayi ridda. Amma kuma yazo gaban Manzo ya faxi yana ahi yana tuba. Kuma Manzon ya karvi tubansa bayan ya riga har ya yanke masa hukuncin kisa.

Idan ba a karvar tubar mai laifi, meyasa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya karvi ta wannan?

Wannan kenan. Kuma ko da bayan naxa shinne, ta bayyana cewa shi ba mutumin kirki ba ne. Hakan baza tasa a zargi halifan da komai ba. Don ai ko Ali *Raliyallahu Anhu* daga baya, wasu hakimansa sun bayar daba yada ake zato ba. Kuma haka bai zama abin suka da qorafi a kansa ba. Iyakar abin da ake iya cewa halifa Usmanu yayi shi ne, naxa wasu mutane, alhali kuma yasan akwai waxanda suka fisu cancant. To ko a hakan bai cancanci suka ba, don al'amari na ijtihadi ne.

Ko kuma a ce, son da yake wa danginsa yaba shi karkata gare su, har hakan tasa ya zaci sun fi kowa cancanta da mukaman. Kuma hakan lalle laifi ne. to ko a hakan ba a binda ya gano shi. Domin kuwa mun riga mun yi bayanin yadda Allah ya wanke laifukansu.

Sannan kuma cewar da xan Shi'ar ya yi wai daga baya, sai hakiman na halifa Usmanu suka cika qasa da fasiqanci da varna, maganar banza ce, daba ta isa hujja ba. Domin kuwa faruwar abin bayan naxasu da aka yi, baya nuna cewa ansanda haka kafin naxin. Koma halinsu ne fil'azal. Domin tabbataccen abune cewa, lokacin da halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* yaji labarin Walidu xan Ukabatu ya sha giya. Bai yi wata - wata ba yasa aka kamo shi ya bulale shi haddi. Haka kuma halifan kan tuve duk wanda ya cancanci tuvewa daga cikin hakiman. Ya kuma tsayar da haddi a kan wanda ya cancanci hakan.

Sannan kuma xan Shi'ar ya zargi halifa Usman *Raliyallahu Anhu* da arzulta danginsa da dukiyar musulmi. To tafi munji wannan laifi ne, ai halifan gafartacce ne a wurin Allah. Balle ma mas'ala ce ta ijtihadi.

A ta kaice ma dai kai, babu wanda yahau wannan karaga ta halifanci, bayan halifa Umar *Raliyallahu Anhu* face ya fifita ko kevance danginsa makusanta da wani abu na muqami ko dukiya. Kamar yadda ta tabbata Ali *Raliyallahu Anhu* ya kama da makusantarsa.

Shi kuwa zancen shan giyar da Walidi yayi bayan naxa shi, kamata yayi ta zama abun yabo ga Usman *Raliyallahu Anhu* ba suka ba. Domin ya zartar masa da hukuncin Allah. Kamar yadda muka faxa a baya. Kuma Ali

*Raliyallahu Anhu* ne sheda. Don halifan ya umurta da bulala hamsin. Shi kuma ya umurci Hassan a cikin. Da Hassan ya kasa, sai ya umurci Abdulllahi xan Ja'afar. Wanda ya tashi yayi ta zabga wa Walidu bulala baji ba gani. Yana daga kannunsa daga ta azba'in sai Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce masa: ya isa haka nan. Su Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Sahabi Abubakar *Raliyallahu Anhu* suka yi wa mashayin giya. Amma Umar *Raliyallahu Anhu* har tamanin yayi. Kuma kowanensu sunna ne. Amma dai ni nafi gamsuwa da arba'in.

Muslim da waninsa duk sun riwaito wannan hadisi.

Ka ga a hankalce da shar'arce halifan ne ya zartar da hukuncin, ba Ali *Raliyallahu Anhu* ba tunda shiya bashi umurni.

Sannan kuma xan Shi'ar ya ce wai mutanen Kufa har sai da suka kori Sa'id xan Asi gwamnan da Usman *Raliyallahu Anhu* ya tura masu, saboda mugun halinsa.

To ka ga wannan magana, tana tabbatar maka da cewa xan Shi'ar nan xan soke ne a kasuwar karatu.

Eh mana! Xan soke ne. domin kuwa fitinar mutane Kufa sananna ce. Korar da suka yi wa wannan gwamna, bata tabbatar da cewa ya yi wani abu da zai cancantar masa da haka. Halinsu ne duk gwamnan aka tura masu haka suke yi masa, sun yi wa Sa'ad xan Abu Wakkas tawaye. Wanda shi ne yaci garin da yaqi, ya karya lagon rundunonin qasar. Yana kuma daga cikin majalisar shawara. Kuma basu tava samun gwamna irinsa ba. Haka kuma sun yi ta qorafi a kan Amru xan Yasir da shi Sa'ad xin da Mugirata xan Shu'ubata da sauran gwamnonin da aka aika masu. Harma da abin yayi yawa, saida Umar xan Khaxxabi ya yi masu mugunyar addu'a da cewa: ya Ubangiji ka dagula lissafin mutanen Kufa yadda suka dagula mani lissafi.

To kuma, mu qaddara cewa wannan gwamna ya aikata zunubin da zai sa mutanen Kufa su kore shi. To meye laifin halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* a nan. Ai ko daga cikin waqilan Ali *Raliyallahu Anhu* har ma dana Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* an samu da yawa, waxanda suka aikata ayyuka na zunubi. Abin da zai sa a kalli shugaba a matsayin mai laifi a wannan hauji, shi ne, idan ya kasa gurfanar da irin waxannan mutane a gabansa, balle ya hukun tasu. Ko ya kasa kwatowa wani haqqinsa, ko wani abu mai kama da wannan, daga ma'aikatansa.

In ma har dai akwai wani laifi a nan, daya hau kan halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* mun riga mun baje shi. Balle ma babu shi.

Haka kuma idan baka manta ba. Xan Shi'ar ya ce wai, gwamnan da Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya tura Masar, wato Abdullahi xan Sa'ad xan Abu Sarhu, ya shakewa mutanen qasar zaiti, har sai da suka kai qarar zaluncin da yake masu ga halifan. Amma maimakon ya kwatar masu haqqinsu, sai ma ya qara xaure mashi gindi. Ta hanyar rubuta masa takarda a asirce a kan Ya ci gaba da aikinsa yadda ya saba. Alhali kuwa yaja kunnensa a rubuce bainar jama'a.

To mu ba duk mai hankalin daya dubi wannan magana ya san qarya ce aka yi wa Usman *Raliyallahu Anhu* kuma da aka zarge shi da haka, saida ya sha billahil - lazi a kan bai ji bai gani ba. Kuma kasan a qa'ida duk abin da ya faxi gaskiya ne, ko bai rantse ba. Iyakar abin da ya tabbata dai shi ne, magatakardarsa Marwanu xan Hakamu ne ya rubuta wannan takarda ta biyu, bada saninsa ba. Su kuwa Misirawa, suka ce: to in gaskiya ne ya ba su Marwanun su kashe. Shi kuwa ya ce: atafau.

To ka ga kashe Marwanu a matsayinsa na kawai wanda ya yi sojan gona bai halatta baza shari'an ce, bai cancanci kisa ba. Kenan qin bayar dashi da halifan yayi dai – dai ne. Kai! Wajibi mane. idan kuwa akwai wani tawili da zai halatta kashe shi, ba wajabtawa ba… to shima qin bayar dashi xin halas ne. babu kuwa wani dalili da zai wajabta kashe shi, in ba ijtihadi ba.

To tafi ma, mu qaddara cewa halifan ya hana a tabbatar da wani abu daya wajabta. Ai idan baka manta ba kuma shi halifan ga vatacce ne a wurin Allah tabbas.

To sai me kuma?

Wata shahararrar qarya kuma da xan Shi'ar ya tafka a cikin wannan magana, itace cewa da ya yi wai halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya yi umurni da kashe Muhammad xan Abubakar. Ka ji kai.

Wannan magana ko shakka babu qarya ce. Domin kuwa duk wanda ya san Usman da irin dattako da adalcin daya shahara dashiya ba zai yi horo da irin wannan aiko kan wani ma, ba Muhammad ba. Kai ba a tava jin yayi irin wannan aika- aika ba.

To tafi ma halifan ya ce a kashe shi. A matsayin Usman *Raliyallahu Anhu* na nagartaccen shugaba, yana da damar yin haka. Don wajibi ne a kansa, yakare mutuncin talakawansa. Ta hanyar kashe duk wanda, ba a iya hutawa daga fitinarsa sai ta haka. Kuma wannan ba abin suka bane. kuma shi yafi cancanta da a yi wa xa'a idan yayi horo da hakan ba waxanda suka so kashe mansuranu ba. A matsayinsu na 'yan tawaye. Kuma mavarnata, waxanda ba suda ikon kashe kowa, ko zartarwa kowa da hukunci. Waxanda kuma iyakar hujjarsu ita ce, an zalunci tane, keda haqqin haninta wanda ya zalunce shi ba. Balle har ya kashe shi daxa.

Ko shakka babu Muhammadun nan da kake ji, ya dace da kisa sosai, savanin maroranu. Don fitina da sharri da matsalolin da koyaurshe a gindinsa babusu a na muh'd. Kuma irin shaharar da Marwanu yayi a fagen ilimi da kishen addini shi bayyi taba. tunda har hadisai da dama ke akwai a cikin shihalu na Marwanun. Kuma ma har fatawa malamia kan yi da wasu maganganunsa. Wasu ma na jin yayi tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Qarya ta farko a wannan magana, itace cewa halifa Usman ne *Raliyallahu Anhu* ya kai Mu'awiyah sham bayan rasuwar xan'uwansa Yazidu xan Abu Sufyanu. Wanda ke gwamna a qasar. Shi kuwa halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* da yazo, sai ya barshi a sham xin a matsayinsa na gwamna. Kuma

Mu'awiyah yayi abun a zo a gani, a wannan qasa ta sham. Don tarihin rayuwarsa ya tabbatar da cewa yana daga cikin gwamnonin da talakawansu ke matuqar godewa, da tsananin so.

A gaida sarkin sarakuna xan Abu Sufyanu. Baban Yazidu hafizin qur'ani.

Ta tabbata a cikin ingantaccen hadisi cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: zavavvu daga cikin shuga banninku, sune waxanda kuke so, suke kuma son ku. Kuma kuna yi masu addu'ar alheri suma suna yi maku. Kuma mafi sharrinsu, sune waxanda kuke qi suna kuma qinku. Kuna la'antar su, su ma suna la'antar ku.

Duk abin da za ka ji ance Mu'awiyah yayi, to ya faru ne bayan kisan gillar da aka yi wa halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* ita kuwa wannan fitina ruwan dare ce game duniya, ba shi kaxai ta shafa ba. Hasali ma Mu'awiyah shi mafi neman salama da zaman lafiya, fiye da sauran waxanda abun ya shafa. Don baka haxa shi da Ashtar An-nakha'I ko Muhammadu xan Abubakar ko Abdullahi xan Umar xan Khaxxabi ko Abul-a'awar as-sulami, ko Hashim xan Hashim al-Murkali, ko Ash'asu xan kasu al-qiniki, ko Busru xan Abu Azda'ata da wasunsu daga cikin magoya bayansa da magoya bayan Ali *Raliyallahu Anhu* duk yafi dama sosai.

Haka kuma xan Shi'ar ya ce, halifa Usman ya kai Abdullahi xan Amir Basra, inda gwamnan ya aikata miyagun abubuwa yadda yaso.

**Martani:**

Duk abin da wannan gwamna ya aikata na zunubi, ai yana kansa. Mi ya gano halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu*? tunda babu wanda ya ce ya yarda da ayyukan Abdullahi. Kuma tattare da hakan rayuwar gwamnan cike take da kyawawan ayyuka, waxanda suka sa mutane na matuqar sonsa iyakar zarafi.

Haka kuma xan Shi'ar ya soki lamirin halifan da naxa Marwanu da ya yi, tare da xauko masa wuqa da nama, a sha'anin mulki. Har ya daka masa hatiminsa. Wanda wai a qarshe hakan ta zama sanadiyar kashe shi halifan. Tare da jefa al'umma cikin fitina.

**Martani:**

Marwanu, shi kaxai, ba shi ne sanadin kashe halifan ba. Abubuwa ne da dama suka haxu. Waxanda suka haxa da qorafe-qorafen da ake yi kan shi Marwanun, da kuma kasan cewar halifan ya sha ruwa sosai shekaru sun miqa. Wanda hakan taba su gwamnonin damar yin wasu abubuwa ba tare da saninsa ba musamman waxanda ake qorafi a kansu amma sanda yawa yake ba Marwanun umurnin canzawa wasu daga cikinsu wuraren aiki ko tuve ma wasu. Shi kuma wani lokaci ya zartar. Wani lokcin kuma ya doje. Mun riga mun fexe buru'I wannan magana har wutsiya.

Sannan kuma wani abu da zai qara tabbatar maka da cewa cin amanar Usman *Raliyallahu Anhu* aka yi har aka kashe shi, shi ne, yayin da 'yan inna da suke qorafi a kansa, saida ya wayar masu da kai a kai. Kai! Har saima da a

qarshe, ya yarda da zai tuve duk wanda ba su so . kuma zai danqa mabuxan Baitul'mali hannun wanda suke so. Ya kuma tabbata masu cewa babu kwabo xaya daya tava xauka daga Baitil malin yaba wani, face ya nemi yarda da shawarar sauran Sahabbai. Kai har dai suka yi kwatakyas. Hakan tasa Sayyida Aisha *Raliyallahu Anha* cewa: basu kashe shi ba saida suka matseshi kamar yadda ake matse tufa, suka raba shi da komai.

Allah ya isa!

Iyakar abin da ake cewa shi ne wai, sun kama wata takarda ne, a kan hanya dasa hannun halifan, inda a ciki wai ya yi umurni da a kashe su. A qarshe kuma halifan ya rantse masu da Allah a kan cewa baida masaniya da wannan takarda. Suka ce to, lalle ko maruranu ne ya rubutata. Saboda haka lalle abasu shi su kashe. Shi kuwa halifan, ya ce, atafau.

Wai a kan haka ne suka kashe shi.

To, mu qaddara cewa wannan labari gaskiya ne, marwanu ya rubuta takardar, kuma halifan yaqi bayar da Shi a kashe. To,ai wannan bai isa halatta jininsa ba, balle a kashe haka kaddan. Don ko shi Marwanun zunubinsa kawai na shirya a kashe sune, in har ta tabbata ya yi hakan, amma ai gurin nasa bai cika ba, balle. Niyar kashe mutum ba tare da wanzarwa ba, bata wajabta kashe mai ita. Ka ga kenan ko Marwanun bai cancanci kisa ba balle halifan.

Amma, eh! Gaskiya ne irin wannan ya kamata a ladabta shi, a kore shi, a kuma yi kaffa - kaffa dashi. Ko wani abu mai kama da haka. Amma a ce a kashe shi, wala.

Haka kuma xan Shi'ar ya soki lamirin halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* da cewa yana kwasar dukiyar Baitul-mali yana ba danginsa da makusantansa. Wai akwai ma lokacin da yaba wasu Quraishawa dake auren 'ya'yansa mata dinari dubu.

**Martani:**

Ina xan Shi'ar ya samo wannan magana? Ba muna musun irin kyautar da halifan ya shahara da ita ne ba. Domin kuwa ko tauraruwar sarfa ta sanda zamansa. Gaskiya ne halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* na cikawa makusantansa aljifansu. Amma kuma da kowa yake, shi ba indararo bane, kaba daji ruwa gida bai sha ba. A'a shi a duk lokacin daya ba Albasa ruwa sai ya ba yalo. A'a ba musu muke ba. Wannan adadi da xan Shi'ar ya faxa, shi muke son mu ji maqaryacin malamin daya gaya masa shi.

Wannan magana ko shakka babu qarya ce. Ba Usmanu *Raliyallahu Anhu* ba, babu wani halifa daga cikin shiryayyun halifofin Manzo, daya tava kyautar irin wannan maqodan kuxi. Halifa Mu'awiyah shi ne tarihi ya tabbatar da cewa ya bi sawun halifa Usmanu a fagen kyauta. Toko shi iyakar adadin abin da aka riwaito, daya kan ba waxanda yake lallashi don su bi shi bai tava wuce dirhami dubu xari ko dubu xari uku ba. Kamar yadda ya tava ba Hassan xan Ali *Raliyallahu Anhu* an kuma riwaito cewa ma Hassan xin kawai ne ya tava

dacewa da irin wannan babbar riba. Wasu malama na jinma Mu'awiyah ya sha gaban Usmanu *Raliyallahu Anhu* a irin wannan kyauta ta lallashi.

Eh! Gaskiya ne halifa Usman *Raliyallahu Anhu* na irin wannan kyautawa makusantansa, wadda har taja masa fitinu. Amma kuma mun riga mun kawo hojjojunsa a kan haka. Za mu kuma qara warware matsalar nan gaba kaxan.

To kuma duk aje ma wannan. A taqaice dole ne kowane shugaba ya gyara tsakaninsa da wasu mutane, don su ji daxin bashi kariya daga duk wanda ke son cuta masa. Musamman idan bai sami irin yadda Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* suka samu ba, na kasancewar talakawansu tare dasu fai da voye.

Wannan shi ne uzuri na farko daya kamata a yi wa halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* idan ana yi wa Allah.

Uzuri na biyu kuma da ake iya yi wa halifan shi ne: a matsayinsa na ma'aikacin gwamnatin musulunci, kuma wanda ke hidimar dukiyarta,to yana da haqqi na musamman a ciki. Don cewa Allah Ta'ala yayi: da masu aiki a kansu (9:60) a kan wannan dalili ne gaba xayan musulmi suka yi ittifaqi a kan cewa komi wadatar wanda ke hidimar irin wannan dukiya, to yana da haqqi a cikinta. Kuma ba laifi bane don ya karve shi.

Haka kuma xan Shi'ar ya ce wai: xan Mas'ud na ganin la'anin halifa Usman *Raliyallahu Anhu* saboda irin waxannan xabi'u nasa, harma yana kafirta shi.

To duk mai hankali da ilimi yasan wannan magana qarya aka yi wa xan Mas'ud babu wani malami daga cikin malamai manaqalta sirrin riwaya daya tava riwaito irin wannan magana. Hasali ma, abin da suka riwaito xan Mas'ud xin na cewa, a lokacin da aka naxa halifa Usmanun *Raliyallahu Anhu* shi ne: mun naxa mafi girman daraja. Bamu bayar ba.

Wani kuma abin da ke qara tabbatar da kasancewar wannan magana ta xan Shi'ar qarya, shi ne, kasancewar shekarun farko na halifancin Usman *Raliyallahu Anhu* babu wanda aka ji yana sukar lamuransa a cikinsu. Sai da aka kai ga kashin qarshe na shekarun, sannan aka fara jin qorafe -qorafe a kansa dangane da wasu abubuwa, da masu qorafe -qorafen keda uzuri a cikin wasu daga cikisu. A yayin da kuwa halifan ne keda uzuri a cikin mafi yawansu.

Wannan qorafi da xan Shi'ar ke son mayar wa wani abu, wanda xan Mas'ud keyi a kan halifa Usmanu, na daga cikin waxannan qorafe - qorafe. Abin da ya faru kuwa shi ne xan Mas'ud ya daxe yana hushi da halifan, saboda danqa aikin sake rubuta Alqur'ani da ya yi ga Yazidu, maimakon ya danqa masa. Bayan haka kuma ya umurci Sahabbai da shafe nasu Qur'anan, su bar aiki dasu, su dawo ga wanga da Yazidu ya rubuta daga baya. Kuma sai mafi yawan Sahabbai suka goyi bayan halifan: suka bar xan Mas'ud. Ka ji iyakar abin da ya faru. Amma zancen kafirtawa, bamu da wannan labari: kai, babu shi sam.

To kuma idan dai har ana son gaskiya, zancen halifan shi ne abun xauka. Bana xan Mas'ud ko Amru ko Abu Zarri ba, ko waninsu. Don babu wanda

darajarsa daga cikinsu ta kai ta Usman *Raliyallahu Anhu* kamar yadda dalilai da dama suka tabbatar.

Wannan ta vangaren su kenan. To vangaren kuwa wanda abin bai shafa ba. Amatsayinsa na xan kallo, kamata yayi ya fahimci, halifa ne ya kamata ace yana fushi da xan Mas'ud, ba shi yayi da shi ba. Amma saboda dattakonsa bai yiba, balle a riwaito. Ko kuma idan ya tashi bayar da labarin mas'ala, ya tsetsefeta, tsetstsefewa irin ta masu ilimi da adalci. Idan kuwa matsayinsa bai kai na haka ba, to ya tsaya ga faxar darajojinsu da kishen addininsu, ya fita batun yin alqalanci tsakaninsu. Don yayi kaxan. Sauran abin da ya gudana tsakaninsu na yaya da ja-in-ja, kuma, ya barwa Allah sani.

Kuma bisa wannan dalili nema, malamai su kayi umurci musulmi dasa ido kawai, da kame baki daga duk abin da ya gudana a tsakanin Sahabbai. Domin kuwa Allah ba zai tambaye mu a kan al'amarin ba.

Kuma a qoqarin qarfafa wannan mataki na kame baki ne, Umar xan Abdul'aziz ke cewa: tunda Allah ya sabani da hannu cikin zubar da wadancan jinane na musulmi, toba kuwa zan tsoma halshena cikinsu ba.

Wani magabancin kuma abin da yake cewa shi ne, abin da Allah Ta'ala ya ce: waccan, wata al'umma ce,ta riga ta shige, tana da abin da ta sana'anta, kuma juna da abin da kuka sana'anta. Kuma baza a tambaye kuba daga abin da suka kasance suna aikatawa(2:134).

Amma kuma ka sani, haka ba zata hana, idan wani xan bidi'a ya tsiru yana sukar lamirin wadancan magabata, da abin da basu jiba basu gani ba, a tashi a yaqe shi, ta hanyar amfani da ilimi da adalci, har a karya lagonsa.

Haka nan kuma abin da xan Shi'ar ya ce, wai Amru ya ce: Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya kafirta, kafirci mabayyani. Har kuma Hassan xan Ali *Raliyallahu Anhu* ya kwave shi. A qarshe kuma wai Alin *Raliyallahu Anhu* ya cewa Amrun " sai dai idan kaine ka kafirce wa Ubangijin da Usman *Raliyallahu Anhu* ya yiimani dashi.

Duk waxannan maganganu, qarairayi ne, da basu tava faruwa ba a tarihin musulunci.

Wannan kenan. Haka kuma cewar da ya yi wai, hawan Usmanu *Raliyallahu Anhu* keda wuya sai yasa aka yi wa xan Mas'ud dukan tsiya har ransa ya fita. Wannan magana qarya ce bai sa ittifaqin ma'abuta ilimi.

Babu abin da ke tsakanin halifa Usmanu da xan Mas'ud *Raliyallahu Anhu* sai alheri. Domin haka ne ma a lokacin da Usmanun *Raliyallahu Anhu* ya zama halifa, bai xauke shi daga Kufa ba, inda yake, har sai da hukuncin Allah ya gudana kansa. Amma ba Usmanu ne *Raliyallahu Anhu* ya kashe shi da duka ba.

To kuma ko da ta tabbata cewa halifan yasa an yi wa xan Mas'udun dama Amru dukan, wannan ba zai zama abin suka gare suba, har shi halifan. Domin dukansu 'yan aljanna ne tun duniya. Mun kuma shedi haka. Kuma suna daga cikin manya -manyan waliyan Allah masu taqawa.

Kuma ko bayan haka, mun riga mun yi bayanin cewa abu ne mai sauqi sosai waliyen Allah ya aikata laifin da zai cancantar masa da wata azaba ta shari'a, balle gargaxi (ta'azur).

Tomu dawo ga zancen Ammru. Wanda xan Shi'ar ya ce wai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce shi wata fata ne daga cikin fatun idonsa *Sallallahu Alaihi Wasallama* da kuma yake jin wasu la'ananu 'yan tawaye za su kashe. Waxanda ke fatar Allah ba zai sasu cikin jirgin cetonsa ba a ranar qiyama.

Ina son ka xan kalli wannan magan da kyau.

Iyakar abin da ya inganta daga cikinta shi ne, cewa Annabi ya ce: Ina jin wasu la'anannu ne 'yan tawaye za su kashe shi to kuma ko ita wannan kalma wasu malamai sun raunana ta, a matsayin hadisi. Daga cikin malaman kuwa akwai: al-Husaini al-Karabisi da wasunsu. An kuma riwaito imamu Ahmad shima ya raunana hadisin. Ka ga da sakal kenan.

Sauran abin da kuma ba wannan magana ba, a cikin hadisin, duk qarya ce, karanta aka yi a matsayin toliyar zamba. Babu wani malami daga cikin malamai masana isnadi da ya riwaito ta.

To kuma majata ta tabbata Manzon ya faxi duk tarkacen da xan Shi'ar ya faxa. Hakan ba zata daxa Ammarun da komai ba. Balle ta hana a hukunta shi, idan ya yi wani laifi.

Dubi matsayin da nana Fatima keda shi a wurin mahaifinta *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Wanda harta tabbata a cikin ingantaccen hadisi cewa ya ce: ko shakka babu Fatima jinina ce. Duk abin da ya tava ta ya tava ni.

Amma kuma tattare da ha kan manzon ya tabbatar wa duniya, a cikin wani ingantaccen hadisi, da cewa: da Fatima 'yar Muhammadu zata yi sata wallahi sai na yanke hannunta.

Haka kuma ta tabbata Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na matuqar son Usamatu, wanda har ya ce a wani ingantaccen hadisi: ya Ubangiji kasan inason Usamatu. Saboda haka ya Allah kaso shi. Ka kuma so duk wanda ke sonsa.

Amma kuma tattare da haka Manzon yayi matsananci hushi tare da kakkausan kashedi gare shi, a lokacin daya dahe wani mutum bayan ya furta kalmar shahada. Ya ce masa: ya kai Usamatu! Ya zaka kashe shi bayan ya ce: la'ilaha illal-lah?

Usamatu ya ce: haka Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya riqa maganar nan yana ta konkoma ta a kaina, har saida naji ina ma dai a ce sai a ranar ne na musulunta!.

To haka abin yake, babu wanda halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya zartar wa wani haddi ko gargadi bisa jahilci ko zalunci. kuma shi yafi cancanta da a yi masa uzuri, a kuma bashi kariya.

a cikin waxannan masallolin bias ga Ali *Raliyallahu Anhu*

Bayan wannan kuma xan Shi'ar ya soki lamirin halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* da cewa wai, ya dawo da Hakamu xan Abdul-Abi a wurinsa,

da xansa Marwanu a garin Madina. Bayan manzo Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya koresu tsawon rayuwansa. Kuma halifa Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* suka qi maikar dasu, sai shi. Har ma ya naxa Marwanu a matsayin magatakardansa. Alhali kuwa Allah Ta'ala ya ce: Ba zaka sam mutane masu yin imani da Allah da ranar Lahira suna soyaya da wanda ya savawa Allah da Manzonsa (58:22).

Wannan magana ko kaxan babu qanshin gaskiya a cikinta. Domin dai Hakan xin nan xan Abi, na xaya daga cikin mutane dubu da suka Musulunta ne, ranar da aka ci garin da yaqi. Kaji wanan ko? Sannan shi kuma Marwanu, xansa, shekarunsa a lokacin basu wuce bakwai ko aqalla ko akasansa ba da kaxan. Ka ga yazo ne matuqa. Wanda ba wani zunubi kansa da zai sa har Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kore shi a kauran kanoli. Kuma a wannan lokaci ba a ba fursunoni yaqin da aka sallama damar zama cikin garin Madina, balle ace an kore Hakim daga cikinta. In har korace, sai dai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*, ya kore shi daga Makka ba Madina ba. Idan kuwa har kaddarata sa aka bashi damar zama Madina. Kuma kora tazo, to sai dai a kora shi zuwa Makka. Amma da mafi yawan ma'abuta ilimi babu yarda da koransa akayi. Abin da suka ce dai ya tafi ne a ra'ain kansa.

Ka ga dawowa da shi bisa wannan lokaci ba lafi bane.

Sannan shi kuma Marwanu mun riga mun gaya muku cewa yaro ne qarami a wannan lokacin ko da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rasu Marwanu bai balaga ba, bisa litaffin ma'abuta cikin qololuwan shekarunsa a wannan lokacin ba sufi goma ba to ya za'ace Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kori shi wannan lokaci.

To a kan me?

Kuma tarihi ya tabbatar da cewa qoriya da samartakar Marwanu duk na musulunci ne bai da voye; mutun ne mai yawan karatun al-qurani da neman ilimi fiqihun addini. Haka rayuwarsa ta xore a kan nagarta har lokacin da fitinoni suka kuma kai. To don Allah meye laifin wanda ya haxamu na wannan matsayin magatakardarsa?

Wani abin la'akari kuma shi ne ko da wannan fitina ta faru, ba a kan Marwanu kawai ta tsaya ba; tabi ta kan har waxannda suka fi shi daraja. Kuma baya cikin waxanda suka savawa Allah da Manzonsa. Shi kuma Mahaifinsa yana daga cikin fursunoni da aka saka masa in gantacen imani. Wasu kuwa abin nasu gashi nan dai. Duk kuwa zunubin da ake yi wa mai shita'aziri, ba wajabta kasancenwarsa munafiki a voye.

Haka kuma idan baka manta ba xan Shi'ar ya ce wai halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* ne ya kori Abu Zarri zuwa Rabzah, bayan ya yi masa dukan tsiya. Alhali kuwa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce shi ne mafi gaskiyar zance a duniya. Kuma Allah ya yi wa Manzon wahayi da cewa yana son wasu Sahabbansa guda huxu, kuma yana horonsa dashi ma yaso su. Kuma na qarshen waxannan Sahabbai shi ne Abu Zarri.

Allah da iko shike. Kai ka ji wannan tsari.

To mu dai iyakar abin da muka sani, kuma wanda za mu mayarwa 'yan shi'an nan martani dashi, shi ne: Abu Zarri shi ne a qashin kansa ya bar birnin Madina ya koma Rabza. Saboda rikittan dake faruwa tsakaninsa da mutane. Sakamakon qoqrin da yake yi na tilasta masu zama zahidai. Shi mutum ne salihi mai zuhudu. Wanda kuma ke jin zuhudu wajibi ne. kuma duk abin da mutum ya rage hannunsa bayan buqatarsa ta yini ta biya. Allah zai yi masa azaba dashi gobe qiyama. Harma da Allah ya karvi na Abdulrahamu xan Aufu. Aka samu ya bar dukiya. Sai Abu Zarri ya yanke hukunci cewa Allah zai yi masa lalas da ita gobe qiyama a wuta. To ashe kai ka je.

To kuma da yawa halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* ke qoqarin ganar da Abu Zarri, ta hanyar ilimi cewa al'amani ta ba haka ba. A haka har watarana ka'abu ya tsoma baki ya kuma goyi bayan lafiya, har Abu Zarri xin ya kai masa duka. Kuma wani abu mai kama da haka ya tava faruwa tsakaninsa da Mu'awiyah a kan haka a sham.

Sannan kuma wannan ra'ayi na Abu Zarri ya savawa abin da gaba xayan halifofi shanyayyu da sauran Sahabbai da tabi'ai suke a kai.

To kuma uwa uba ya savawa abin da ingantattar sunnar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ta tabbatar. Kamar inda Manzon ke cewa: babu zakka a cikkin abin da ba kai auziqi ko zandi ko awaki biyar ba.

Ka ga a nan Manzon ya tabattar da halarcin aje abin da bai kai xayan biyu ba, ba kuma tare da an fitar masa da zakka ba. Kuma ko da mai shi baya da buqata dashi. ai buqatar ba sharaxi bace a nan.

Bayan wannan kuma jumhuran Sahabbai sai suka fasara waccan kalmar ta "kanzin" dukiyar dake jawo azabar Allah gobe qiyama ga mai ita, da cewa itace. Dukiyar da ba a fitar da haqqin Allah daga cikinta. Komai yawan ta ko qanqancita.

Ka ga kenan Abu Zarri ya jefa kansa a wannan lokaci, a cikin matsalar son wajabta wa mutane abin da Allah bai wajabta masu ba. Ya kuma ga laifin mu a kan abin da Allah bai ga yayi ijtihadinsa ne. kuma Allah zai bashi lada a kai, kamar yadda zai bayar ga takwarorinsa ijtahidai.

To a kan wannan dalili ne Abu Zarri ya ga bari ya batse kansa, ya koma Rabza. Ba don Usmanu *Raliyallahu Anhu* nada wani mugun nufi a kansa sannan kuma maganar kasancewar Abu Zarri xin alfahari ne ba. Kuma hakan bata nuna cewa darajarsa ta fita kowa. Hasali ma, a ingantacen hadisi, shi mumini ne mai rauni kamar yadda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tabbatar, inda ya ce: ya kai Abu Zarri! Na riga na gane kai mutum ne mai rauni. Duk da yake kuma ina so maka abin da nake sowa kaina. Amma ina ganin bai kamata a shugabantar da kai ko da a kan mutum biyu ba. Ko a baka dukiyar maraya.

Wani hadisin kuma dake qara walwale wannan, tare da fitowa da matsayin Abu Zarri na haqiqa, savanin wancan da xan Shi'ar ke son qaraba mana shi ne, cewar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a wani igantacen

hadisi: mumini mai kaza da kaza shi ne mafi alheri da soyuwa a wurin Allah, bisa ga mumini raunana. Amma kuma akwai alheri aikin kowanensu.

To ka ga idan haxa hancin waxannan hadisai biyu wuri xaya, sai kace: muminai 'yan majalisar shura, irinsu Usmanu da Ali da Abdurahama xan Aufu, waxanda suka cancanji zama halifofi da sonransu, shi ne muminai kafata kuma masu kazar - kazar. Shi kuma Abu Zarri da takwarorinsa, masu cikin hali da halittarsa sune raunana. Kenan waxannan sunfi shi falala.

Shi kuwa wannan hadisi, a cikin wannan lafazi da xan Shi'ar ya kawo, hadisi ne mai rauni. Kai! Qagagge ma, don babu wani isnadi da zai iya xaga darajarsa.

Ka ji wannan!

To yanzu kuma mu dawo ga cewar da ya yi wai halifa Usmanu ya keta alfarmar shari'ar Allah, tunda bai kashe Ubaidullahi xan Umar ba, wanda ya kashe Hurmuzanu, bawan Ali *Raliyallahu Anhu* bayan kuma ya musulunta. Kuma wai saboda haka Alin (Sarkin Musulmi) yayi tsaye a kan shi ko sai ya zartar wa Ubaidullahi da hukuncin Allah. Amma wai a qarshe Mu'awiyah ya bashi mafaka.

Sannan kuma wai, inji xan Shi'ar, halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* yaso yayi ko oho da hukuncin shan giya. Wanda ya hau kan Walidu xan Uqbata. Sai da Ali *Raliyallahu Anhu* ya xaukarwa abin matakin soja; ya zartar da hukuncin a kansa, ya kuma rufe caftar da cewa: Ai ba ta yiwuwa a tozartar da hukuncin Allah ina raye.

**Martani:**

Wannan magana ko shakka babu bakar qarya ce. Domin kuwa ba haka kawai halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya ki kashe Ubaidullahi makashin hurmuzanu ba. Akwai dalili a kan haka, da kuma hujja karvabba. Bari ka ji yadda al'amrin ya kasance. Wanda na yi imani da Allah, ba ni ba, ko kai za ka yi wa halifa Uzuri.

Abu na farko da ya kamata ka sani shi ne: shi dai Hurmuzanun nan, xaya ne daga cikin Farisawa da Kisra ya waqilta su yaqi musulmi. A qarshe Allah ya nufi aka kama shi a matsayin fursunan yaqi. Da aka zo dashi gaban zakin halifofi Umar xan khaxxabi sai ya musulunta. Halifan ya ce: mun karvi musuluncinka, mun kuma 'yanta ka. Kana ji da kyau ko?

To a lokacin da bamajushen nan, Abu lu'ulu'ata bawan Mugirata xan Shu'ubata ya yi wa halifa Umar *Raliyallahu Anhu* kisan gilla. Musulmi suka zurfafa bincike, sai aka gano cewa akwai abota mai kauri tsakaninsa da hurmuzanu. Harma an gansu, suna kus-kus-kus kafin kashe halifan. Aka kuma tabbatarwa Ubaidullahi xin da haka. A haka sai Hurmuzanu ya zama babban wanda ake tuhuma da hannu a cikin kisan halifan.

Wannan tuhuma ta kara qarfi matuqa, da aka yi la'akari da labarin da Abdullahi xan Abbas ya bayar cewa, kafin shexar Umar ta fita *Raliyallahu*

*Anhu* ya ce masa: Ai ga irinta nan. Kai da mahaifinka kun fi kowa son a sakarwa illiyin Farisa mara sa cika birnin Madina.

Jin haka sai Abdullahi xan Abbas xin ya cewa halifan: To in ka yarda yau muna aika gaba xayan su lahira. Umar ya ce: Ai bata yiwuwa tunda har an wayi gari sun ari harshen ku sun kuma shiga addinin ku.

To ina son kaxan dubi wannan magana da kyau. Ka ga idan dai har xan abbas, a matsayinsa wanda ya yi wa Abdullahi xan Umar fintinqau a fagen sanin makamar addini da kishinsa. Ya kuma fi shi martaba, zai nemi iznin yi wa gaba xayan illiyin Farisa dake Madina kisan qare dangi, saboda kawai ana tuhumarsu da fasadi. Me zai hana Ubaidullahi sakankancewa da hallaccin kashe Hurmuzanu a kan abin da ya aikata? Babu.

Bayan da aka gama tabbatar da hannun Hurmuzanu a cikin aika -aikar, sai halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya shawarci mutane a kan dacewar yin layya dashi. Sai wasu Sahabbai suka ce, hakan bai dace ba
a halin yanzu. Saboda jiya - jiya ne aka aika mahaifinsa lahira. Idan shi kuma aka aika shi yau, to hakan na iya zama abun faxi ga musulmi.

Ka ga kenan a taqaice, kamar wata shubha ta kama zuqatan waxannan Sahabbai, har suke jin jinen Hurmuzanu bai gama halatta ba, takwana. Wato rasa gane matsayinsa tunda tuhuma ce ake masa; shin yana kawai cikin 'yan hadin baki waxanda jininsu baya halatta, koko cikin 'yan damu aka yi, waxanda suka cancanci kisa?

Ka ji bilinbiton da waxannan Sahabbai suka sami kansu a ciki. Amma dai sauran mafi yawansu sai suka tafi kan cewa jininsa ya halatta. Domin wannan kisan 'gilla da aka yi wa halifa Umar *Raliyallahu Anhu* duk malamai sun sakasu a cikin babin tawaye. A qa'ida ko da 'yan hadin baki da 'yan damu akayi, a wannan babi duk hukuncinsu xaya.

A kan haka duk wanda ya taimaka, ko da da magana ne, a cikin wannan kisa da aka yi wa halifa Umar *Raliyallahu Anhu* to a wurin waxannan Sahabbai (jumhuru) wajibi ne ya baqunci lahira. Ta kuma tabbata cewa hadin baki a cikin kisan halifan. (Umar *Raliyallahu Anhu*)

To ka ga a haka kisan Hurmuzanu ya wajaba illa dai shugabanin jama'a ne keda haqqin zartar masa da hukuncin. Sai Ubaidullahi yayi azarbabi ya riga malam masallaci ya gama dashi. Amma kuma duk da haka halifan nada cikakkar dama ta yafewa wanda ya riga sarkin yankansa ga mai laifi.

Ka ji yadda al'amarin ya faru a haqiqa.

Bayan wannan sai kuma xan Shi'ar ya ce wai sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* ya xaura niyar kashe ubaidullahi saboda kashe Hurmuzanun da ya yi.

To ka ga wannan magana, ko da ta inganta, bai kamata 'yan Shi'ah su buga taba, da suna da hankali. Domin zata fito da gwarzon nasu ne (Ali *Raliyallahu Anhu* a matsayin wanda bai san makamar addini ba (fikhu) Dama haka halinsu yake; sawa zagi rigar yabo.

To kuma ma wai, ina suka samo cewar Alin *Raliyallahu Anhu* yayi niyar kashe Ubaidullahi, koma har ya kashe shi? Yaushe Aliyu *Raliyallahu Anhu* ya samu wannan faraga? Wanda bai fita ruwa bana matsar ragga?

Kuma ya za a yima Ali *Raliyallahu Anhu* ya iya kashe Ubaidullahi a matsayinsa na wanda ya sami goyon bayan dubban musulmi harma da Mu'awiyah. Wadanda kuma ke jin Ubaidullahi ya cancanci kowace irin kariya a matsayin mayar da hannun baiwa ga wanda ya miqo shi. Kuma kasawar da Alin *Raliyallahu Anhu ya yi*ta tunvuke Mu'awiyah kawai, ta tabbatar da cewa ba kofar da zai iya bi balle ya isa ga Ubaidullahi balle ya kashe shi. Bama zai fara wannan tunani ba.

Kuma wani abin mamaki, da zai tabbatar maka da cewa 'yan Shi'ah na qaryar kare hukuncin Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* suke yi shi ne yin kunnen uwar shege da suka yi da maganar jinin halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* tare da halatta shi. Tattare da kasancewarsa jagoran musulmi (Imamu) kuma wanda aka yi wa bushara da aljanna. Wanda kuma shi da danginsa su ne mafifitan halitta bayan Annabawa.'yan Shi'ah suka xauki kashe sa da aka yi kamar an kashe kare. Amma sai gashi suna qoqarin kifar da duniya a kan kawai an kashe Hurmuzanu. Kuma a matsayin wanda ake tuhuma da nifaqa da yi wa Allah da Manzonsa tawaye, da xaurewa fasadi gindi a duniya.

Halifa Usmanun nan da kake ji *Raliyallahu Anhu* Sahabin da 'yan Shi'ah suka yi wa wannan riqon sa kainar kashi, dattijo ne na qarshe. Riwayoyi mutawatirai sun tabbatar da cewa ya fi kowa gudun zubar da jinin wani. Shi ne kuma mutum mafi haquri da yafewa wanda yaci mutuncinsa. Kuma irin yadda ya kau da kai tare da tsare alfarmar waxanda suka kai masa takakka don su kashe, tattare kuma yasan nufinsu, ba duk mutum ke iya haka ba.

Sai da musulmi suka yo angaya daga ko ina, suka bashi shawarar lalle ya xaura yaqi da waxannan mutane. Amma gogan naka; salihi uban dattijai, ya kafa kai ga kasa ya ce, atafau, kada wanda ya yaqe su; duk wanda ke jin maganarsa ya kauda kansa. Harma an riwaito cewa ya ce wa bayinsa duk wanda ya kama kansa na 'yanta shi.

Ganin cewa halifa Usmanu baya da niyyar sassautawa daga wannan mataki daya xauka sai musulmin dake tare dashi, suka ce to yayi hijira mana ya koma Makka. Ya ce: Allah ya sauwake. Ba zai zama wanda ya keta alfarmar xakin Allah ba. Suka ce to ya tafi sham. Ya ce: Barin Madina; garin hijira baya yiwuwa gare ni. Suka ce: To lalle koka yaqe su ya ce: ina! Ko alama. Ba zan yarda in zama farkon wanda ya raka Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* da fasa garken al'ummarsa da takobi ba.

Ko shakka babu, wannan haquri da jaruntaka da halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya nuna, ta hanyar yi gaba da gaba da mutuwa, na daga cikin manyan darajojin da musulmin duniya ke girmama shi a kai. Duk kuwa wanda ya soki lamarinsa da cewa wai ya halatta zubar da jinin musulmi tunda yaqi kashe Ubaidullahi. Duk wanda ya ce haka, to a taqaice yana sone ya buxe kofar sukar lamarin Ali *Raliyallahu Anhu* da abin da yafi wannan girma. Domin idan

magatta Ali *Raliyallahu Anhu* suka qirdadi wannan magana, suka kuma hankalto cewa kyale Ubaidullahi da halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* yayi, abune dake da madogara a shari'a. To sai suce ba kowa ne ya keta alfarmar hukuncin Allah ba, banda Ali *Raliyallahu Anhu* tunda shi ne yaqi hukunta makasan halifa sukutum (Usman *Raliyallahu Anhu)* waxanda babu wani tawili da zai kasa halatta, jininsu. Wanda ko shakka babu keta alfarmar hukuncin Allah a cikin yin biris da wannan haddi tafi zama varna bisa ga yin biris dashi acikin wancan. Domin ko alama alfarmar Hurmuzan bata kai ta halifa Usmanu ba *Raliyallahu Anhu.*

To idan kuwa har za a yi wa Ali *Raliyallahu Anhu* uzuri, a kuma ba shi kariya. Ta hanyar la'akari da kasancewarsa mujtahidi kuma maras wuqa a hannu tare da nama. Babu abin da zai hana a sakawa Usman *Raliyallahu Anhu* irin wannan riga. Don ya mafi cancanta da ita.

Haka kuma cewar da xan Shi'ar ya yi wai halifa yaso yin biris da haddin da yahau kan Walidu xan Ukbata. Wai sai da Ali *Raliyallahu Anhu* yayi tsaye ya zartar da hukuncin a kansa. Qarya ce yake yi wa duka su biyun.

Abin da ya tabbata a ingantaccen hadisi, kamar yadda muka ambata a baya, shi ne; halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* shi ya umurci Ali *Raliyallahu Anhu* da bulale Walidu haddi. Qarshe kuma shi Alin *Raliyallahu Anhu* ya hana a yi masa bulala tamanin. Aka tsaya ga arba'in. Ka ga da ya bari an yi tamanin xin halifa ba zai ce uffan ba. Don hakan ma sunna ne. Ka ga kenan Ali *Raliyallahu Anhu* ya tausayawa Walidu a matsayinsa kuma na wanda ya savawa Allah.

Wannan kenan. Wani abin kuma dake qara tabbatar maka da jahilcin wannan xan Shi'a, da kasancewarsa mugun maqaryaci, shi ne cewar da ya yi wai bayan tsayar da wancan haddi da Ali *Raliyallahu Anhu* yayi, sai ya ce: Bata yiwuwa a tozarta hukuncin Allah ina raye.

Tumun fari, wannan magana qarya ce.

To kuma ko da mun qaddara kasancewarta gaskiya, to za ta zama wani babban abunda ya kamata a yabi halifa Usmanu dashi ba Ali *Raliyallahu Anhu* ba. Domin halifan bai yi girman kan qin karvar shawarar Ali ba *Raliyallahu Anhu* balle ya hana shi zartar da hukuncin. Tattare da kuma yana da ikon yin haka. Kuma a matsayinsa na halifa idan yaga dama, Ali *Raliyallahu Anhu* bai isa yasa ko hana shi abin da yaga damar yi ba.

Wannan magana tabbas haka take. Don Ali *Raliyallahu Anhu* nada irin wannan iko a a kan halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* da bai bari ya aikata abubuwan da 'yan Shi'ah suka xauka abubuwan kunya ba. Amma ka ga bai hana shi ba. Tattare da kasancewar sa Ma'asumi, mai iko a kan komai. Kamar yadda 'yan Shi'ah suka yi imani. Ka ga kenan reshe ya juye da mujiya; sukar lamirin ta koma kan Ali *Raliyallahu Anhu.*

Saurarawa Ali da Usman zaiyi *Raliyallahu Anhu* idan har hakan ta tabbata, don zartar da wannan hukunci, na kawai tabbatar da dattako da kishin addini da adalci da halifan ke dasu ne, amma ga mai hankali.

Haka kuma halifa Usmanu ya naxa Walidun nan gwamnan Kufa. Abin da 'yan Shi'ah ke ganin bai halatta ba. To ka kuwa ga inda hakan haramun ne, kamata yayi ace Ali *Raliyallahu Anhu* ya hana halifan yin haka. Tunda har yana da ikon yin haka ko? Tunda kuwa har bai hana shi ba, kenan ya yarda da naxin a matsayin halas. Ko kuma bai da ikon hana shi xin. In har hakan bata halasta, a nasa gani.

Idan kuwa haka ta tabbata, kenan Ali *Raliyallahu Anhu* bai zartar da hukuncin can ba, bayan Usmanu *Raliyallahu Anhu* yayi biris dashi, in har hakan ta tabbata. Tunda ta tabbata bai iya hana shi komai, don yana ji yana gani ya naxa Walidun.

Ka ga kenan a hankalce, da halifa Usmanu bai so ba, bata yadda za a yi Ali *Raliyallahu Anhu* ya iya zartar da hukuncin. Idan kuwa ya zartar dashi ne, tare da yardar halifan. Ka ga halifan ya tabbata mai kishin addini. Wanda ba zai tozartar da wani hukunci daga cikin hukunce - hukuncen Allah ba.

Karka yi mamaki yadda 'yan Shi'ah nan ke tafe suna qwangaba qwanbaya. Haka sunka saba.

Bari kaji wata wautar da tunqa da walwala. Xan Shi'ar ya ce wai: haka kuma halifa Usmanu ne *Raliyallahu Anhu* ya qirqiro da bidi'ar kiran sallar, da wanka na ranar jumu'a. Har aka wayi gari ya zama kamar sunna.

Ka ji magana kamar ta ilimi.

**Martani:**

Idan dai wannan ijtihadi da halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* yayi bidi'a ne, to Ali *Raliyallahu Anhu* ko na daga cikin waxanda suka goya masa baya a kanta, a lokacin rayuwar halifan da bayan rasuwarsa. Don haka ne ma da Alin *Raliyallahu Anhu* ya zama halifa bai kashe wannan kiran sallar ba.

Kamar yadda ya tuve waxanda bai yarda da su ba, daga cikin ma'aikatan Usmanu *Raliyallahu Anhu* wanda har Mu'awiyah na daga cikinsu. Amma abin ya faskara. Ka kuwa san kashe kiran sallah, da wasu ayyuka masu kama da shi, da ake jin bidi'a ne, a Kufa yafi sauqi matuqa bisa ga qoqarin tuve wadancan ma'aikata, daxa balle yaqar su. Abin da ya gagari Alin *Raliyallahu Anhu*

Kuma ko shakka babu, da Ali *Raliyallahu Anhu* ya kashe irin wannan kiran sallah a Kufa, da duniyar musulunci taji. Ka ga kenan ba bidi'a bane har a cikin littafin fiqihun Ali *Raliyallahu Anhu.*

Nasan kangararrun ('yan Shi'ah) na iya cewa: to ai dole ya bari aci gaba da yi nai. Don ko cewa yayi a daina mutane baza su yarda ba.

Ka ji wawaye.

To ai hakan, dalili ne dake nuna cewa mutane harda magoya bayan Ali *Raliyallahu Anhu* waxanda suka taya shi yaqi, irin su: Ammaru da Sahlu xan Hanifu, da wasunsu daga cikin 'yan sahun farko a musulunci, duk sun goyi bayan halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* a cikin ganin dacewar wannan kiran sallah, da tahowarsa a kan qari.

Wani abun ban mamaki ma duk, bai fi cewa mutanen nan (‘yan Shi’ah) dake sukar lamarin halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* a kan wannan kiran sallah da ya taho dashi. Kuma gaba xayan musulmi; da suka haxa da Muhajirun da Ansaru, suka mara masa baya. Sune mutanen da suka kara lafazin “Hayya Ala Haril Amal” a cikin kiran sallar. Abin da ba a tava ji zamanin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya furta ko ya yi umurni dashi ba. Kuma babu musulmin da baisan cewa kiran sallar da Sahabi Bilalu da xan Ummu Makatum keyi a masallacin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a Madina. Da wanda Abu Mahazura keyi a Makka, da Sa’adu al-Kurzu a Quba a, duk bai qunshi wannan xan Shi’ar lafazi ba.

Ka ga kenan wannan qari nasu shi ne bidi’a kuma vatatta, ba kiran wanka ba. Don gashi musulmi ba riwaito lafazin nasu ba, amma sun riwaito wanda ya inganta.

Haka kuma xan Shi’ar ya ce wai gaba xayan musulmi sun raba gari da halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* wanda hakan ta zama sanadiyar ya rasa ransa. Kuma wai ma sukan yi masa arashi da cewa, bai halarci yaqin Badar ba. Kuma ya gudo daga na Uhudu. Kuma ba tare dashi aka yi Bai’atur - Ridhwanu ba. Kuma wai labari a kan haka sufi qarfin kididdiga.

Maratani: Idan xan Shi’ar na nufin raba gari na gama gari. Waton gaba xayan mutane sun juya wa halifa baya. Suka halatta jininsa, ta hanyar haxa waccan yar qungiya, da bata kowane irin taimako don xaukar ran halifan, to babu wanda bai san wannan magana qarya bace. Domin wasu ‘yan kwarorin mutane ne, azzalumai suka yi masa tawaye, suka kuma kashe shi. Kuma da sauran musulmi sun sami goyon bayan halifan a kan yaqar Makosan da Mussarsu ta kyankyami kasari.

Kuma wani abin da ke tabbatar da cewa wannan magana qarya ce, shi ne cewar da xan Zubairu yayi: Allah dai ya la’anci makasan Usmanu *Raliyallahu Anhu* sun masa shigar sauri ne kamar yadda varayi keyi. Amma duk da haka nan wasunsu basu shaba. Sauran kuma suka nemi sa’ar hasken taurari.

Wato yana sone ya ce: ‘yan tawayen sun kai kutsa kai ne suka kashe halifan cikin dare. Bayan mafi yawan musulmi sun sallame shi. Amma sauran mutanen gari sun ga shigowar su. Sai dai ba su yi tsammanin kashe shi za su yiba. Don babu wata alama tare dasu da ke nuna hakan.

Ka ga ashe kenan wasu ‘yan tsiraru ne suka raba garin dashi ba kowa ba.

Idan kuwa xan Shi’ar na nufin gaba xayan musulmi su raba gari ne da halifan, rabawa irin wadda ta taqaita ga qin amincewa da duk abin da ya aikata kawai. Ko kuma ga abubuwan da ake sukar lamarinsa a kansu kawai. To ko a hakan ya shara shegiyar. Domin kuwa tarihi ya tabbatar da cewa babu wani abu da wasu musulmi suka savawa halifan a cikinsa, face adadin da yafi nasu yawa ya amince dashi a kai. Kai harma daga cikin nagartattun malaman su kan mara masa baya. Haka kuma tarihi ya tabbatar da cewa waxanda suka yarda da halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* a kan abubuwan da wasu ke qi nasa, sun fi

waxanda suka yarda da Ali *Raliyallahu Anhu* a kan abubuwan da ake ganin lamarisa a kai yawa da girman daraja, ta fuskoki da dama.

Haka kuma ta tabbata cewa waxanda suka yi wa halifan arashi da cewa bai halarci yaqin Badar da Bai'atar-Ridwanu ba, ya kuma gudo daga yaqin Uhudu, wasu 'yan tsiraru ne kawai daga cikin musulmi, waxanda ba su cika yatsun hannu ba a adadi ba. Kuma halilfan da biyu, shaixan kawai ne ya talalabantar dasu, saboda sashen abin da suka tsirbata. Kuma lalle ne, haqiqa Allah ya yafe laifi daga gare su. Lalle ne Allah mai gafara ne mai haquri (3:155).

To ka ga wannan aya ta hutar da duk mai tsoron Allah. Tunda sarkin ya yafewa duk ma wanda ya kaye a ranar yaqin; ba Usman *Raliyallahu Anhu* kawai ba. Ga kuma tarin falala da kyawawan ayyukan da halifan yake dasu *Raliyallahu Anhu.*

### 2.79 Maganar Shaharastani Ba Hujja Ce Ba

A wani qoqarin kuma na samar wa soke-soken da xan Shi'ar ya yi wa waxannan manyan halifofi, sai ya lalabu maganar shahraxani ya kafa hujja da ita, da cewa: Duk da tsananin kyamar da shahraxani ke yi wa Shi'ah 'yan-sha-biyu inji xan Shi'ar, wai an samu yana cewa: Babu wata fitina data gurvata al'ummar musulmi bayan fitinar shexan (Iblis) kamar savanin daya shiga tsakanin Sahabbai a lokacin rashin lafiyar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama.*

Farkon wannan savani kuma inji shahraxani, wai shi ne, abin da Buhari ya riwaito, da isnadinsa, daga xan Abbas, wanda ya ce: Ya yinda rashin lafiyar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya qaura aikinta ta tsananta, sai ya cewa Sahabbai ku kawo mani tawada da farar takarda in rubuta muku wasiyyar da baza ku vace ba bayan na qaura. Sai Umar ya ce: ina ganin zafin ciwo ne ya tsananta gare shi. Kuma ai littafin Allah ya ishe mu.

Daga nan sai wuri ya kacame da yaya. Sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Bai kamata kuna irin wannan yaya da jayayya gabana ba. Kai! Ku dai watse.

To farkon abin da za mu ce a nan, a matsayin martani shi ne: Maganar shahraxani ba hujja bace. Saboda mafi yawan abin da yake faxa, shi da takwrorinsa mawallafa, a cikin: Al-milal Wan-Nihal, maganganu ne da sashensu ke riwaitowa daga sashe. Kuma mafi yawansu, ba a riga an tace jirwayen zantukan waxanda aka riwaito su daga gare suba, aka zubar. Kuma ma mafi yawan su ba su da isnadi. Wani abin la'akari ma shi ne da yawa yakan tsakuro maganganu daga cikin littafan marubuta 'yan Shi'ah da suka wallafa maqalu kafinsa. Wato irin su: Abu Isah al-Warrak, shahararren marubucin nan na 'yan Shi'ah. Waxanda basu jin kunyar qarya. Sai kuma Abu Yahaya da waninsa. Haka kuma ya kan tsakuro wasu abubuwa daga cikin littafin Shi'ah Zaidiyya da Mu'utazilawa. Waxanda suka shahara da sukar lamirin da yawa daga cikin Sahabbai saboda haka maganarsa bata isa hujja ba.

To amma mu bamu yi mamakin wannan abu da xan Shi'ar yayi na riqon gurvataccin maganganun malamin a matsayin hujjojinsa ba. Domin kamar an tunkuxi icce ne inda yake son faxuwa. Dama kuma ma'abucin son zuciya na kodayaushe lalaben abin da ya dace da itane ya karva ido rufe. Ba tare da wata kwakwarar hujja dake wajabta masa hakan ba. Nan take kuma ya yi watsi da duk abin da bai dace da ita zuciyar tasa ba, ba bisa wani dalili kwakwara ba.

'yan Shi'ah kenan. Babu wata qungiya daga cikin qungiyoyi a duniya da tayi sunan qaryata gaskiya da gasganta qarya kamar su. Domin waxanda suka kafa marhabar tasu, da malamanta duk munafukai ne zindikai. Kamar yadda malamai da dama suka tabbatar, take kuma bayyana ga duk wanda ya yi masu kallon tsaf.

A kan haka, kenan ba za ta yiwu ba mu saki samu kama abin da ko ga tozo bai kai ba. Abubuwan da al-qur'ani da sunna da mutawatiran riwayoyi suka daddale, na kyawawan ayyukan Sahabbai da darajojinsu sun yafi qarfin wata gurguwar magana maras asali. Ko burkutu - burkutu su kawar dasu. Balle wadda ke kan turva madaidaiciya. Domin a qa'ida, shakka bata kawar da yaqini. Kuma mu mun riga mun miqa wuya ga duk abin da al-qur'ani da sunna da ijma'in magabata suka tabbatar. Haka kuma duk wata riwaya mutawatira, ko wata dalili na kaifin hankali da zai zo ya marawa waxannan abubuwa da muka yarda da su baya; ya daxa karfafa su, ta hanyar tabbatar da cewa Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* sune mutane mafiya daraja a cikin halittar Allah bayan Annabawa. To za mu karvi irin waxannan riwayoyi da hannu biyu - biyu. A waje xaya kuma sukar da za a yi masu ta hanyar amfani da wasu abubuwa da ingancinsu bai tabbata ba, ba zata razana mu ba, balle wadda aka tabbatar da kasancewarta qarya.

Wannan kenan. Sannan kuma cewar da xan Shi'ar ya yi wai, Shahrastani na daga cikin mutane masu tsananin kyamar Shi'ah 'yan-sha-biyu. Ba gaskiya bane. Kuma ya kawo wannan magana ne don ya yaudari hankalin mai karatu.

Abin da yake gaskiya shi ne: Shahrastani na daga ma cikin mutanen da ake zargi da kasancewa 'yan Shi'ah *Isma'iliyyah*. Saboda da yawa yake goyon bayan wata hujja da wata magana tasu. Duk da yake, a haqiqanin gaskiya shi ba xan Shi'ah bane. Tattare kuwa da waxanda ke zargin shi da ita sun kafa hujjoji daga cikin maganganunsa da tarihin rayuwarsa. Amma idan akace malami ne daka tava qida kaxan ya tava karatu; yau Ba ash'are gobe Bashi'e babu laifi.

Daga nan kuma sai cewar da xan Shi'ar yayi, shahrastani ya ce: Babu wata matsala data girka xumar fasadi da varna a duniya bayan wadda Iblisu ya girka, kamar savanin daya shiga tsakanin Sahabbai a lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ke jinyar ajali.

Ka ji.

To duk yadda aka kaxa aka raya wannan magana ba ta zama gaskiya; Idan xan Shi'ar na nufin wannan savanin fahimta daya shiga tsakanin Sahabbai a wannan lokaci; shi ne farkon laifin da aka yi wa Allah, to qarya yake yi.

Haka kuma ko cewa yayi;  a'a, yana dai nufin shi ne savani na farko da aka samu bayan waccan matsala ta Iblisu. Duk dai har yau bai daga ko kaxan daga matsayin maqaryaci ba, saboda dalilai kamar haka:

a) abin nan daya faru tsakanin Sahabbai a wannan lokaci, ya sha banban da wanccan daya faru ga Iblisu kwata - kwata. Domin wancan batun zuci da iblisu yayi, har ya kasa miqa wuya ga umurnin Allah kai tsaye, bai sa mala'iku suka shiga cikin wani bilinbito ba. Kuma al'amarin bai kai kunnen 'yan Adamu ba, balle suma su afka cikin koyin rikici da savani.

b) Banbancin fahimta tsakanin 'yan 'Adamu abune mai daxaxxen tarihi; tun zamanin Annabi Nuhu. Hasali ma banbancin fahimta da savani da ake samu tsakanin musulmi, ko kaxan bai kama qafar wanda ya yi ta faruwa a tsakanin al'ummomin da suka gabace mu ba.

C) Idan aka kai wannan abu da ya faru a lokacin wannan jinya ta Manzo, bai kai can ba. Domin babu wani abu mai rikitarwa acikinsa balle; abu ne mai matuqar sauqi da zama ga – ta - sarqi. Domin kuwa ya tabbata a cikin ingantaccen hadisi cewa, kafin wannan lokaci Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya cewa Sayyida Aisha *Raliyallahu Anhu*: kiraman mahaifinki da xan'uwanki. Ina son in rubuta wa Abubakar *Raliyallahu Anhu* wata takarda don kada mutane suyi wata shakka, balle su sava a kansa, bayan na qaura. Sannan Manzon ya cika da cewa: Alhali kuwa shi ne zavin Allah, wanda kuma muminai za su zava.

Ka ji tushen wancan al'amari.

Kamawar ranar Alhamis keda wuya sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi tunanin rubuta wannan magana don qara daddale ta. Har ya ce a kawo masa kayan rubutu. Umar *Raliyallahu Anhu* ya ce: Anya ba zafin masassara ne ya tsananta a kansa ba.

Ka ga Umar *Raliyallahu Anhu* bai yanke hukunci a kan matsayin maganar ba, tunda ya yi amfani da kalmar "anya" wadda ke alamace ta "shakku", da tabbatar da cewa al'amarin ya shige masa duhu ne. Kamar yadda rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ta shige masa duhu, har kaxan ya rage ya musanta ta.

Daga nan sai wasu Sahabbai suka ce, kai! Ku samo abun rubutu. Wasu kuma suka ce, kar a kawo. Ganin wannan magana ta Umar *Raliyallahu Anhu* tayi wannan tasiri a cikin Sahabbai. Kuma ma ba wani muhimmanci wannan rubutu keda shi ba. Ko banza ma ya riga ya faxi abin da yake son rubutawa tun shekaranjiya. Ga kuma wannan kokwanto daya sami Sahabbai daga wurin Allah. Sai Manzon ya fita batun rubutun.

Ka ga kenan abin da wannan ke tabbatar wa, shi ne; wannan wasiyya bata cikin abin da Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya wajabta wa Manzon rubutawa Sahabbai a wannan lokaci, a matsayin sakonsa. Don da wajibin ce,

babu abin da zai hana Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fita batunta, a matsayinta na abin da Allah ya umurce shi dayi. Abu dai ne da shi a karan kansa, yaga ya dace, don yayi maganin wani rikici da kan iya tasowa a kan bakin daya bari na Sahabi Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya gaji halifancinsa.

Wannan itace gaskiyar al'amarin. Amma saboda jahilcin daya yi wa 'yan Shi'ah kanta, sai sukace wai Manzon yaso ne ya rubuta wasiyyar a kan Ali *Raliyallahu Anhu* ya maye halifarsa, bayansa kai tsaye. Alhali kuwa babu wani abu a cikin wannan qissa dake nuna haka ta kowane hali. Kai! Ko wancan hadisi sannane a wurin malaman riwaya, baya xauke da wani abu mai ko kama da wannan. Amma ingantattun hadisan dake tabbatar da halifancin Sahabi Abubakar suna da yawa.

Wani abun kuma dake qara tabbatar da jahilcin waxannan mutane, shi ne cewar da suka yi wai itama halifar Ali *Raliyallahu Anhu* Manzon ya riga ya tabbatar da ita a nassance, ta yadda wanda ya kauce mata ba zai sami wani uzuri ba. Ah! To idan kuwa har haka ne, to rubutu na me? Idan kuwa har yaso ne ya rubuta don kada waxanda suka ji wancan nassi su fandare. To rubutun ba zai yi amfani ba. Don shi ma suna iya fandare masa. Ka ga kamar yadda muka faxa, idan dai har ta tabbata Manzon ya furta waccan magana, to amfani me rubutun zai yi masu? Babu.

Savani na biyu a wannan lokaci, a cewar sharastanin shi ne, rabuwar kan da aka samu tsakanin Sahabbai, bayan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce musu: ku kimtsa rundunar Usamatu. Kuma Allah ya la'anci duk wanda ya bari ta bar shi tasha.

Wai kuma tattare da wannan babbar magana da Manzon yayi, sai Sahabban suka shiga ka-ce-na-ce; wasu na cewa: Lalle ne a aiwatar da wannan umurni. Wasu kuma na cewa: A'a a dai saurara. Ba ku ganin yadda masassarar nan ta tsananta gare shi? Bai kamata mu tafi mubarshi ba. Kuma wai a lokacin da suke wannan muhawara har Usamatu ya sha xamara.

**Martani:**

Eh! Gaskiya ne wannan abu ya faru. Amma malamai masana sirrin riwaya sun tabbatar da cewa qarya ce, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai ce: Allah ya la'anci duk wanda wannan runduna ta bari tasha ba. Kuma babu wani isnadi dake tabbatar da cewa ya ce haka. Babu wani littafi na hadisi daya sanda wannan magana asalata. Kuma tarihin musulunci ya tabbatar da cewa imanin Sahabbai ba zai bari su qi fita tare da Usamatu ba, daya fitar. Shi ne da kansa ya ga bai dace su fita a lokacin ba, saboda ganin halin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ke ciki na rashin lafiya. Har ya ce masa. Ya Manzon Allah! Ya zan fita in barka cikin wannan hali? In koma ina tambayar fatake yadda ka kwana? Daga nan sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi masa izinin lalle sai Usamatun ya tafi, ba abin da zai hana shi zuwa. Da kuwa sauran Sahabban da aka shirya subi shi sun bishi. Don ta tabbata babu wanda ya bari jirgin rundunar ya bar shi tasha, lokacin da ya

tashi, bayan rasuwar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai fa wanda shi Usaman ya yi wa izinin tsayawa saboda wani jihadin.

Sannan kuma kan malamai ya haxu kan cewa babu sunan Abubakar *Raliyallahu Anhu* cikin jerin sunayen waxanda ya kamata su fita yaqin tare da Usama. Amma an riwaito cewa na Umar *Raliyallahu Anhu* na ciki. Kuma tuni Barden ya xaura tamantaka yayi shirin fita, da lokacin ya yi.

Amma sai Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya nemi izinin Usaman a kan ya bar masa Umar *Raliyallahu Anhu* don ya kama masa wani jihadin. Aka kuma yi sa'a kwamandan ya amince. Amma kuma karka manta zaman Sahabi Abubakar halifa ke da wuya, ya dage a kan lalle wannan runduna ta tafi. Amma sauran Sahabbai suka nuna masa haxarin daka iya faruwa a cikin fita tunda wuri haka. Don magabata sun koxa wuqaqensu da jin rasuwar Annabi. Amma duk da haka halifan ya nace a kan wannan Umurni nasa, yana mai cewa: Wallahi ba zan saukar da tutar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya xaga ba. Sai dai kome ke tafasa ya kone.

Tirqashi ka ji maza. A gaida Uban Aisha saxaukin fama.

Haka kuwa aka yi, sai da rundunar ta tafi.

Wannan shi ne ingantaccen tarihin abin da ya faru. Amma sai gashi sarakunan qaryar duniya na yayata cewa wai Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* anga daga cikin waxanda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya shata su tafi yaqin tare da Usama. Kuma wai dasisa ce Manzon ya killa masu, don kada su hana Ali *Raliyallahu Anhu* kaiwa ga halifanci, idan ya cika suna kusa. Ka kuwa san fa mai kera irin wannan qarya sai mafi jahilcin mutane da tarihin Manzon da Sahabbansa.

Abin da ya tabbata shi ne; tsawon kwanukan jinyar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* Abubakar *Raliyallahu Anhu* ne keba mutane sallah, da Umurninsa. Kuma kowa ya san haka. Da Annabi yaga dama, yana iya naxa wanda zai gade shi a lokacin. Kuma Sahabbai ba za su qiya masa ba. Kuma ko shakka babu Muhajiruna da Ansaru na yin layya da duk wanda yaqi bin umurnin Allah da Manzonsa. A matsayinsu na waxanda suka yi gwagwarmayar kafa addinin har ya kai gaci.

Umurnin Manzon Allah ba zai tava faxuwa ba matuqar waxannan na raye. Da Manzon yasa Ali *Raliyallahu Anhu* ya waqice shi ga limancin sallah, ko aikin hajji, ya kuma sa Abubakar da sauran Sahabbai qarqashin ikonsa. Ko ya ce masu: Ga Aliyu nan shi ne na zava ya zama shugabanku (halifa) idan na qaura. Babu wanda ya isa ya ce masa a'a. Kai ka san haka.

A shirye gaba xayan musulmi da Muhajiruna da Ansaru suke suyi masa xa'a da zai ce haka. Saboda babu wanda Ali *Raliyallahu Anhu* ya kashe wa xan'uwa daga cikinsu balle yaqi shi.

Ah! Kuma inda Manzon na sone ya korewa Ali *Raliyallahu Anhu* su, don haka ya tura su yaqi tare da Usama. To da abin ya faskara, sai ya ce wa musulmi: kada wanda ya yi wa xayan su bai'as. Shikenan ba mai yi. Babu wani tsoro da zai ji a cikin faxar haka. Saboda tabbacin samun taimakon Allah da

yake da shi. Kuma ga Muhajiruna da Ansaru kewaye dashi. Waxanda da zai hore su da kashe iyayensu da 'ya'yansu, nan take ne.

Kuma ma me yayi zafi tsakanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* wanda tarihi bai sani ba, balle ya faxa, har da haka zata kasance? Ai surar bara'atu ta sauka daga wurin Allah. Ta tona asirin munafukai, ta fito dasu a fili, musulmi kowa ya sansu. Manzo da gaba xayan al'umma suka yi tir da Allah waddai dasu.

Amma aka ci aka suxe, Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* na nan a kan matsayinsu na mafiya zama kusanci ga manzon. Mafiya girma, soyuwa da cuxanya dashi dare da rana. Kuma waxanda suka fi kowa qaunarsa, da biyar umurninsa, da yarda da ra'ayinsa da xaukaka martabar addinin da yazo da shi.

Ka ga a wannan matsayi nasu, ya savawa hankali a ce kuma, suna daga cikin waxanda mutane da surar Bara'atu ta tonawa asiri. Kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yanke kowace irin hulxa dasu bayan saukar surar. Amma kuma har Allah ya karvi rayuwarsa babu wanda ya keso daga cikin mutane, da girmamawa kamar Abubakar *Raliyallahu Anhu* .

Bayan wannan kuma sai shaharastanin ya ce: Savani na uku kuma shi ne wanda ya faru a kan rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* .

**Martani:** Eh! Ko shakka babu al'amarin rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yaya shige wa Umar *Raliyallahu Anhu* duhu a farkon lamari, amma safiya nayi, ya dawo cikin hayyacinsa, ya kuma sakankance cewa dai lalle Manzon Allah ya qaura. Bayan haka kuma ya tabbatarwa sauran musulmi da cewa, matakin da ya hau jiya kuskure ne. Kuma daga nan sai kura ta kwanta komai ya koma daidai. Kuma lafazin hadisin na haqiqa ya savawa yadda shahrastani ya shimfixa al'amarin.

Abin da yazo a cikin Buhari da Muslim, a hadisin da aka riwaito daga xan Abbas, wanda ya ce: Umar na cikin magana, sai ga Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya fito, ya ce: saurara Umar, zauna. Umar yaqi ya zauna. Sai ganin haka, mutane suka mayar da hankali ga Abubakar *Raliyallahu Anhu* don suji abin da zai faxa. Suka fita batun Umar *Raliyallahu Anhu* sai Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya ce: Bayan haka, ku sani, duk wanda ke bautawa muhammadu, toya sani Muhammadu ya rasu. Duk kuwa wanda ke bautawa Allah to ya sani Allah baya mutuwa. Kuma Allah Ta'ala ya ce: kuma Muhammadu bai zamo ba face manzo, lalle ne manzani sun shuxe a gabaninsa. Ashe idan ya mutu ko kuwa aka kashe shi, za ku juya akan duga - duganku? (3:144)

Xan Abbas ya ce: Wallahi kai kace mutane basu tava sanin Allah ya saukar da wannan aya ba, sai yau da Abubakar ya karanta masu ita. Nan take kuma sai kowa ya riqe ta yana maimaita a zuci, lavvansa na mui –mui - mui.

Ya ce kuma : xan masayyibi ya bani labarin cewa Umar *Raliyallahu Anhu* ya ce: wallahi qarewar Abubakar karatun wannan aya keda wuya sai gavvaina suka yi sanyi., har kafafuna suka kasa xauka ta. Nan take na faxi zaune na kuma tabbata lalle dai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rasu.

Ka ji haqiqanin abin da ya faru.

Sannan kuma savani na huxu, kamar yadda Shahrastanin ya ce, wai shi ne wanda ya faru a kan halifanci. Ya ce kuma shi ne savani mafi muni a tarihin musulunci, daya tarwatsa kan al'umma. Domin babu wata qa'ida ta musulunci da aka zare takubba aka ba hamata iska saboda ita, a tsawon zama, kamar yadda aka yi a kan halifanci.

**Martani:** Wannan magana babban kuskure ce. Domin kuwa –Alhamdu -Lilahi- babu wani yaqi da aka yi a kan halifancin Abubakar ko Umar ko Usmanu *Raliyallahu Anhu* kai! Ko cacar baki har hanci ya yi zafi, ba a tava yiba a zamaninsu a kan halifanci, balle a kan wani abu na addini. A sane muke da cewa Ansaru sunyi waxansu 'yan maganganu. Amma kuma da manyan mutane suka yi masu kashedi, nan take kowa ya nabba a. Ka ga ba wani rikici a nan. Don babu mai musun cewa girman darajar mutane irin su Ubaidu xan Huzairu da Abbadu xan Bushrin da wasunsu tafi ta Sa'ad xan Ubaidata, a tsurar ruwan zatin kansu da girman gida. To sune suka sa baki magana ta kare.

Babu wani mutum xaya daga cikin manyan gidajen Ansaru, waxanda Buhari da Muslimu suka riwaito, ta fuskoki da dama cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tabbatar da girmansu da cewa: mafi alheri daga cikin gidajen Ansaru, sune:

1. Gidan bani Najjar
2. Gidan bani Abdul-As'hal
3. Gidan bani Hashi
4. Gidan bani Sa'idata

Amma kuma akwai alheri a cikin gaba xayan gidajen Ansar inji Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* to babu wani daga cikin gidaje uku masu daraja ta farko (1-3) da aka ji ya yi wata jayayya a kan halifancin. Hasalima manyan mutane daga cikin Bani Najjar, irin su: Abu Ayyuba al-Ansarida Abu Xalhatu, da Ubayyu xan Ka'abu da wasunsu duk Abubakar suka a zava.

Haka kuma Usandu dan Hudhainu, barden da ya jagoranci rundunar Ansaru a ranar da aka ci garin Makka da yaki, yana hagu ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* Abubakar *Raliyallahu Anhu* na dama. Wanda kuma daya ne daga cikin Gidan Bani Ashhal, shina daya daga cikin Ansarun da suka hada kan al'umma a kan yi wa Abubakar *Raliyallahu Anhu* bai'a.

Waxanda kawai suka yi cijiya; suka ki yin wannan bai'a a lokacin da kowa ya yi, s;u ne: Sa'ad dan Ubbadata da Hubbatu dan munzir, da wasu 'yan tsirarun mutane. Ko su kuma sun gano sun yi kuskure. Daga baya suka dawo suka yi wa Siddiqu mubaya'a, ban da Sa'adu dan Ubbadata shi kam cewa ya yi, atafau.

Amma kuma wannan abu da Sa'ad ya yi, ba abin mamaki ba ne. Domin shi ba ma'asumi bane balle. Amma dai mutum ne salihi. Kuma yana da laifuka, waxanda wasunsu sananni ne ga musulmi. Kuma ana fatar Allah ya gafarta masa su. Musamman tunda ya sami shiga sahun ansaru na farko ga shiga musulunci. Waxanda kuma Allah ya yi wa albishirin aljanna tun duniya. Kari a kan yarda da amincewa da ya yi da su.

Kuma cewar da shahrastani ya yi wai gaba xayan Ansaru sunyi ittifaqi a kan Sa'ad din ya walkice su, ya zama halifa, maganace maras tushe balle makama. Domin abin ada ya tabbata daga bakin ma'abuta ilimin riwaya, da kuma tabbataccin hadisai duk sun tabbatar da kasancewar maganar karya bisa ittifaqi. Duk da yake shahrastani da ma kantansa ba maqaryata ba ne a karan kansu. Amma tabbas suna tsakuro abubuwa daga cikin littafan manyan maqaryata ba tare da sun sani ba.

Haka nan kuma abin da wasu ke yaya tawa, an cewa duk wannan rikici da ake ta yi a kan halifanci, wai Ali *Raliyallahu Anhu* bai da labari. Don yana can ya shagalta da abin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya umarce shi da yi na yi masa wanka da saka masa likkafani da rufe shi da kuma zaunawa wurin kabarinsa. Wannan magana tabbas qarya ce. Kuma maganar ma ta yi ban hannun smakaho da abin da su kansu suka yi imani da shi. Na cewa a cikin daren ne ankayi jana'izar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba da rana ba wasu kuma suka ce a'a, sai da wani dare  ya yi sannan aka rufe shi. Kuma bai umurci kowa da zaunawa wurin kabarinsa ba. Kuma tarihi bai fadi cewa Alin *Raliyallahu Anhu* ya zauna wurin ba, ko a ra'ayin kansa.

Ya ma za a yi haka ta faru, tunda an nufe Manzon ne a cikin dakin Aisha *Raliyallahu Anhu* kuma ba ajanabace ga alin?

Sannan kuma ai 'yan Shi'ar sun gaya mana cewa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya riga ya gaya wa Ali shi ne magadin halifarsa. Kuma lalle ne ya yi qoqarin ganin haka ta tabbata. To ya za a yi wanda ke da irin wanna aiki; kuma a ce manzon ya umurce shi da tsare kabariunsa. Ko ya yi me? Oho.

Kuma a haqiqanin gaskiya ba Ali *Raliyallahu Anhu* ne kawai ya yi hidmar jana'izar Manzon ba. Abin da ya tabbata shi ne, shi da Abbas da 'ya'yan Abbas din, da barwansa Shakran ne da wasu ansaru suka yi masa wanka da saka masa likkafani. Abubakar da Umar da wasunsu kumas suna bakin kofar dakin har aka ci aka sude. Ka ga da su aka yi kenan. Cewar da ake yi suna Bani Sa'adata a lokacin qarya ce kawai.

Abin da kuma ya hana su shiga a kimtsa gawar ta Ma'aiki tare da su shi ne; kasancewar sunna ta tanadi ta kaita irin wannan hidma ga dangin mamaci. Saboda haka ne Ali *Raliyallahu Anhu* da makamntansa suka rabauta da wannan alheri. Da kumas aka karkare, sai aka ba musulmi dama suka shiga dakin; daya bayan daya don su yi masa salla da ganin ban kwana. Haka suka yi ta yi, maza da mata. Taron da jama'a musulmi suka yi don wannan ibada, sai ta sa dole aka jin kirta rufe gawar har zuwa ranar alhamis.

To kuma ba halifancin halifofi uku na kafin Ali *Raliyallahu Anhu* wanda aka yi lami lafiya, ko yakin da aka yi lokacin halifa Ali *Raliyallahu Anhu* ba yaki ne na neman shugabanci ba. Domin mutanen da ke bayan Sayyida Aisha da Mu'awiyah *Raliyallahu Anhu* a yakokan Basasar da aka yi na Jamalu da siffain da Nahrawan, ba su saxaukantar da rayukansu ne ba, don nada wani halifa ba, Ali *Raliyallahu Anhu* kamar yadda Mu'awiyah da Xalhatu da

Zubairu babu daya cikinsu da ya ce shi ne shugaba ba Ali *Raliyallahu Anhu* ba. Kamar yadda kuma ba ba qarqashin jagorancion wanimutum da suke jin shi ne halattaccen shugaba, suka yi yakokin mba, kafin sasantawar da aka so yi bisa girman Allah.

Haka kuma babu daya daga cikinwaxannan yakoka na basasa, da aka yi, a kan wata ka'ida ta shugabanci da ake cece-kuce a kanta don tabbatar da sukar lamiri da rashin goyon bayan halifofi uku magabata, da shelantawa duniyar musulunci cewa ba su ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bar wasiya a nassance da cewa su gaji shi ba. Haka kuma su dayan vangaren, ba suna yakin ne don suna jin Ali *Raliyallahu Anhu* bai cancanci zama halifan ba. Ko alama ba haka al'amurran suka gudana ba.

'yar ja yayyar da ta shiga tsakanin mutane a kan wannan al'amari, kamar wadda ke tsakaninsu ce da 'yan Shi'ah da Harijawa da mu'utazilawa da sauransu. Amma babu wani sahaboi da ya shiga ytakin;don kawai jayayyar shugabanci. Babu wanda ya kushe shugabancin Ali *Raliyallahu Anhu* ko ya kafirta shi, ko ya kafirta duk wanda ya jibince shi, shi da Usman *Raliyallahu Anhu*.

Ka ga kenan, idan ka fahimci wannan karatu da na shinfida maka, zaka fahimci cewa duk wanda ya ce farkon damtsen da aka ware, aka ba hamata iska a tsakanin musulmi wa-su-wa-su, har anka hada da kaifin takobi, ya faru ne kawai saboda kokuwar shugabanci, makaryaci ne na kinkarawa. Wanda leka kundin tarihin Sahabban kawai, ba tare da an shiga cikinsa ma sosai ba ke tabbatar da haka.

Kuma duk wanda ya kalli waxannan yake-yake da idon basira da tsoron allah, zai tabbatar da cewa yake-yake ne na Basasa, da Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya jarabci Sahabban da su a matsayin "fitina" kuma a kan haka ne mafi yawan malamai masu tsoron allah suka kwana. Kuma idan har ta kama sauran su yi wani sharhi a kai, ba su kan wuce cewa: Yakoka ne da suka faru tsakanin 'yan santsi da 'yan tabo a cikin Sahabban ba.

Ka ga a ta kai ce an yi yakokan ne bisa karvabben tawili, na garin dacewar saurara wa wanda bai gama zama shugaba ba. Amma ba don wata ka'ida ta addini ba.

Iyakar fassarar wannan lamari kenan. Kamar yadda da a ce lokacin da aka nada halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* wasu Sahabbai sun ja daga har haka ta sa ya yake su. To matsayin yakin dazai yi da su din daya da wanda Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi da wadannasn. Eh! Matsayinsu daya mana, tattare kuwa da kasancewar babu wata rashin jituwa tsakaninsu a kan wata ka'ida ta addini.

Ka ji matsayin waxannan yakoka. Amma yaki na farko da aka yi a tarihin musulunci, a kan wata ka'ida ta addini shi ne wanda Harijawa suka tayar tsakaninsu da Sahabbai. Sanadiyar wasu akidu da suka qirqira waxanda suka saba wa akidar musulunci, kuma wannan yaki na daya daga manya-manyan yakoka a tarihin musulunci. Kuma da ma nassosa mutawatirai sun ambace shi

kamar cewar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi: wasu ‘yan tawaye za su yi amfani da wata tsaga da za ta faru a garin musulmi, su yi wa musulunci tawaye. Amma vangaren da ya fi gaskiya daga cikin musulmin ne za su kashe su.

Haka kuma shi Ali *Raliyallahu Anhu* a karan kansa, bai yaki kowa don ya kwaci shugabanci ba. Kuma babu wanda ya yake shi don ya kwace shugabanci daga hannunsa. Kamar yadda babu daya daga cikin: Sayyida Aisha ko Xalhatu ko Zubairu ko Mu’awiyah da Sahabbansa, ko Harijawa, da ke jin shi ya fi cancanta da halifanci a kan Ali *Raliyallahu Anhu* Hasali ma gaba xayan al’umma na matukar ganin girmansa da zamansa mafificin daraja bayan halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya kaura. Haka kuma suna jin babu wani Sahabi da bai zama wajibi gare shi, ya cire wa Ali *Raliyallahu Anhu* hula ba,a lokacin Usman *Raliyallahu Anhu* babu gagarabadau a cilkin Sahabban sai shi. Wanda hakan ta sa babu wanda ya ji wani kaikayi, da aka ce shi ne halifa, balle ya yi wata jayayya, da husuma don qoqarin nuna fifikon cancantar wani a kansa. Ba a sami ko daya daga cikin irin wannan ba, balle dada zancen shaya daga. Kamar dai yadda Akayi halifancin Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* cikin lumana da kwanciyar hankali.

A ta kaice dai, abin da muke son tabbatar  wa da wannan jeka-ka-dawo shi ne: duk wanda ke da masaniya da tarihin Sahabbai ingantacce, tabbas ya san cewa babu wani rikici da ya faru tsakaninsu a kan halifancin Abubakar da Umar da Usmnu *Raliyallahu Anhu* balle yaki .

Haka kuma ba a sami waxanda suka yi wata jayayya ba, don qoqarin jtabbatar da akwai wanda ya fi Ali *Raliyallahu Anhu* cancanta da halifanci a lokacin sa. Duk da yake akwai wasu mutane da aka tilastawa yi wa dayan halifofin huxu bai’a. Wannan dole na, kuma ba abun mamaki ba ne. Domin ko annabcin Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai da aka tilasta wasu karvar sa, balle halifancin wani Sahabi.

Haka kuma ta tabbata cewa Sahabbai ba su yaki junansu a kan halifancin Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhu* ba. Kai! Ko cacar baki ba su yi ba. Halifancin dai da aka zubar da jini a kasa shi ne na Ali *Raliyallahu Anhu* ka ga idan har zubar da jini a kan shugabanci abun kunya ne, to ba wanda hakan za ta shafa sai wanda hakan can ta faru tsakanin al’umma kan shugabancinsa.

To kuma wannan ita ce hujjar hawarijawa a kan matsayin da suka xauka na kin yaarda da al’amarin Ali *Raliyallahu Anhu* kuma wannan hujja tasu, ta fi ta ‘yan Shi’ah qarfi, su kuma a matsayin da suka xauka na kai Sahabi inda Allah bai kai shi ba. Haka kuma takubbansu sun fi sauka madaidaicin wuri bisa ga na ‘yan Shi’ah. Kamar yadda addininsu ya fi nasu inganci. Saboda su Harijawa ba maqaryata ba ne kamar ‘yan Shi’ah. Amma kuma duk da haka ta tabbata daga bakuna da daman gaske, daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bisa kuma ittifaqin Sahabbai cewa Harijawa batattu ne, kuma abin da suke kansa bidi’a ne. Dada Balle ‘yan Shi’ah waxanda hauka da jahilci da

rashin kishin addinin su, da jaruntakarsua fagen kiren karya da rashin kuzarinsu da rashin tsentseni, kai da suffan tuwarsu da duk wasu miyagun halaye, suka tabbata.

Ko shakka babu Harijawa su ne qungiya mafi yaji, da wasu da takobi a kan wuyan mutane. Amma duk da haka ba su yaki kowa a kan halifancin Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* ba. Hasali ma suna daga cikin duban jama'ar da suka yarda da shugabancinsu, suks kuwa bi su.

Wannan kenan.

Sannan kuma Shaharastani ya ce: Matsala ta biyar wai ita ce ta Fadak da abin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bari na kayan gado a duniya.

To, ita wannan mas'ala ba matsala ba ce. Domin kuwa ta tabbata cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Mu Annabawa ba a gadon mu. Duk abin da muka bari duniya sadaka ne".

To, abin da ya kamata a sani a kan wannan mas'ala shi ne; mas'ala ce ta banbancin fahimta a farfajiyar shari'a. Kuma ba ma wani savani da za a iya cewa akwai a cikinta. Don bai kai wanda ke cikin gadon 'yan'uwan juna tare da kaka namiji ba. Ko na kaka mace tare da danta ba. Ko kuma wanda ke cikin shamakance Uwa da 'yan'uwa biyu ke yi. Ko xaukar matsayin kaka namiji da Uwa kamar na Uba. Da kuma wasu mas'aloli na gado, masu kama da waxannan, da malamai suka sami banbancin fahimta a kai.

Sannan kuma ita ma mas'alar Fadak, mas'ala ce ga-ta-sarai. Domin kuwa ai Ali *Raliyallahu Anhu* ya zama halifa bayan haka nan, Fadak da sauran garuruwan musulunci duk suka koma qarqashin ikonsa. Amma bai damqa ta hannun 'ya'yan Fatima ba, a matsayin wani abu da 'yan Shi'ah ke iqirarin wai Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya ba mahaifiyarsu. Haka kuma bai karvo wani abu da aka bai wa matan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da 'ya'yan Abbas ba, da sunan gado.

Ka ga ke hakan na nuna cewa shi kansa alin *Raliyallahu Anhu* bai tare da 'yan Shi'ah a cikin wannan zargi da suke yi wa halifofin. Domin da yana jin cewa abin da suka aikata da abin da Manzon ya bari zalunci ne, lalle da ya walwale shi. Domin kuwa yana da ikon yin haka. Kuma hakan ma shi ne abu mafi sauki gare shi, bisa ga fuskantar Mu'awiyah  da rudunarsa da sunan yaki. Ko shakka babu Alin *Raliyallahu Anhu* ba zai yaki Mu'awiyahn ba, tattare da irin sharrin da hakan za ta haifar. Kuma a lokaci xaya ya kasa qwato wa magadan Annabi wannan xan abin duniya ba. Abin da yake iya yi cikin qyaftawa da bisimillah.

Bayan wannan kuma sai malamin ya ce wai kuma matsala ta shida ita ce: Yaqar waxanda suka hana zakka da halifa abubakar ya yi. Wannan ma ya vata wa al'ummar Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* suna. Wai ma saboda tsinkayo haka ne da halifa Umar *Raliyallahu Anhu* ya hau gado ya dage kai da fata ya mayar ma su da waxanda aka kamo daga cikinsu a lokacin yaqin. Ya kuma saki gaba xayan waxanda aka xaure a dalilin haka.

Ka ji abin da Shahrastani ya ce, kuma xan Shi'ar ya riwaito.

To duk wanda ya san tarihin musulunci ya san wannan magana shegiyar qarya ce. Domin kuwa halifa Abubakr *Raliyallahu Anhu* bai yaki waxannan mutane ba, sai da Umar *Raliyallahu Anhu* ya yarda da shi, bayan sun kara wa juna ilimi a kan mas'ala. Kamar yadda Buhari da Muslimu suka riwaito daga Abu Hurairata cewa:

Umar ya ce Abubakar *Raliyallahu Anhu*: ya kai halifan Manzon Allah! Ya zaka yaki waxannan mutane, alhali Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: An umarce ni da in yaki mutane, matukar ba su yi imani da babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah ba, kuma ni Manzon ne. Amma idan suka furta wannan kalima jinai nai da dukiyoyinsu sun haramta gare ni. Sai fa a kan wani hakki na shari'ah. Hisabinsu kuma na wurin Allah?

Sai Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya ce masa: Ah! To ai cewa ya yi: sai fa a kan wani hakki na shari'ah ko? Ti ai zakka hakki ne na shari'ah. Tunda kuwa haka ne. Wallahi da za suki ba ni ko da ragwamar Raqumi da sukan ba Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* zan yake su a kan haka.

Daga nan sai Umar *Raliyallahu Anhu* ya ce: wallahi, daga nan ne na fahimci Allah ya gama haskaka qirjin Abubakar a kan wannan yaqi. Na kuma sakan - kance da cewa lalle bisa hanya yake.

Ka ga kenan wannan hadisi ya tabbatar mana da cewa Umar *Raliyallahu Anhu* yayi itifaqi da halifa Abubakar *Raliyallahu Anhu* a kan wannan yaqi. Haka kuma sauran Sahabbai ma sun yarda da shi a kai. Kuma yaqin yayi amfani matuqa . saboda mutanen sun dawo sun yarda da kasancewar ci gaba da fitar da zakkar wajibi a kansu. Bayan can dauri sun fandare. Sannan kuma a ingantaccen tarihin yadda yaqin ya kasance, ba a kama kowa daga cikinsu aka ribace ba. Ba a kuma xaure kowa daga cikinsu ba. Kai hasalima babu wanda aka tava xaurewa a zamanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kona Abubakar *Raliyallahu Anhu* a Madina. Balle har a ce halifan ya mutu ya bar 'yan fursuna. Qarya ne.

Daga nan kuma sai shahashtanin ya ce wai, matsala ta bakwai itace: zaven Umar *Raliyallahu Anhu* da halifa Abubakar *Raliyallahu Anhu* yayi a matsayin wanda zai zama halifa bayansa. Wai har wasu mutane suka qorafa cewa: Abubakar ka naxa mana mutum mai kaushi hali da hushi!

**Martani:**

Harwayau dai, wannan mas'ala ba ta isa a kira ta mas'ala ba domin kuwa ba ga Umar *Raliyallahu Anhu* aka fara ba. Wasu Sahabbai sunyi irin wannan qorafi a kan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a kan ya shugabantar da Zaidu xan Harisata da xansa Usamatu a kansu, a wasu lokutta. Kuma wasu mutane da yawa sun yi qorafi da suka a kan wasu da halifa Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* suka ba riqon wasu kasashen musulmi.

To kuma shi wannan qorafi, da waccan magana da malamin ya ce an faxa a kan Umar *Raliyallahu Anhu* ai ba kowa ne ya yi ba banda Xalhatu. Shi ma

daga baya yayi nadama. Har ma aka wayi gari yana cikin sahun mutanen da ke matuqar girmama halifa Umar xin *Raliyallahu Anhu* kamar yadda masu qorafin can a kan jagorancin Zaidu da Usamata suka yi nadama a kai, kuma suka gyara saboda girman Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Bayan wannan kuma sai malamin ya ce, wai kuma matsala ta takwas ita ce kafa kwamitin da halifa Umar *Raliyallahu Anhu* yayi, don ya zavi halifa bayansa. Wanda wai kuma a qarshe bayan an yamutsa gashin baki, manbobin suka haxu a kan Usmanu *Raliyallahu Anhu* a matsayin halifa.

**Martani:**

Wannan magana na xaya daga cikin maganganun da malamai masana sirrin riwaya, suka haxu a kan kasancewarsu qarya tuburan. Domin kuwa babu wanda ya nemi tayar da hankali a kan halifancin Usmanu *Raliyallahu Anhu* saboda wai bai yarda ba. Illa dai Abdurrahamanu xan Aufu ya xauki tsawon kwana ukku yana tattaunawa da mutane. Inda yabi har matan Sahabbai a gidajensu, yana neman shawarar su. A qarshe aka tabbatar masa da cewa an gamu da Usman ya zama halifa *Raliyallahu Anhu*. To kuma ko da akwai wanda ke qyamar halifan a zuciyarsa, ba a samu wanda ya riwaito hakan ba. Kai! Hasali ma dai babu abin da aka faxa a kan wannan al'amari, da ya kawo kunnenmu.

Amma kuma duk da haka, ba mu cewa wani bai yi wani qorafi ba, koda a zuci. Tunda irin wannan al'amari na neman shawara wurin jama'a ya gadi haka.

Sannan kuma malamin ya ce wai ko bayan waxannan matsaloli. Wasu matsalolin sun faru da dama. Waxanda suka haxa da: Mayar da Hakamu xan Umayyata da halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya yi a Madina, bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kore shi. Wanda har mutane ke yi masa laqabi da "Zakkar Manzo". Kuma wai halifan ya yi haka ne, tattare da neman halifa Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* da ya yi, a lokacin halifacin da su yi wa Hakamu xin afuwa. Amma abun ya faskara. Kuma ma wai halifa Umar *Raliyallahu Anhu* bai tusaya ga qin yi masa Afuwa ba. Har qarawa yayi da shi gaba, daga inda yake zaune a Yamen, da tsawon zango arba'in.

To abin da za mu ce a nan shi ne: Wannan mas'ala ba ta isa a kira ta savani ba. Abin da har za'a xauka a kai shi da nisa. Balle a ambace ta matsala. Idan kuwa har aka yi haka. To kenan, duk wani hukunci da wani halifa ya yanke, wasu Sahabbai suka saba da shi a fahimtar abun ya zama "matsala" kenan ko?

To dama irin wannan, har gwamma a ambaci banbance-banbancen fahimtar da aka samu tsakanin Sahabban, a kan wasu mas'alolin gado da saki da wasu mas'aloli irinsu. Waxanda suka fi inganci a riwaya, da amfani ga mutane. Eh! Waxannan mas'aloli da ire - irensu su ne mafi inganci mana, da tabbata. Saboda ma'abuta ilimi sun riwaito su. Wanda kuma har yau mutane na

bitar su, tare da amfanuwa da taskokin da ke cikinsu na ilimi, a matsayinsu na duwatsun murhun shari'a, da ake iya qara wa juna ilimi a cikinsu.

Savanin irin waxannan qananan abubuwa, daba su isa a kalli banbance - banbancen fahimta a cikinsu, a matsayin wani abu daya cancanci tautaunawa don qara wa juna ilimi ba.

Amma fa duk wannan sharhi da muke yi muna yin sa ne, tattare da yaqinin da muke da shi a kan cewa duk waxannan abubuwa da ya faxa game da Hakam, qorarsa, laqabinsa, nemar masa afuwa, qiyawa da qarawa dashi gaba, duk qarya ce.

Idan kuwa xan Shi'ar ko shi shahrastanin naji zancen gaskiya ne, to su gaya mana asalin wanda ya riwaito shi, da isnadinsa, da lokacin da ya tafi yeman xin, da dalilin da ya sa aka iza qeyarsa can. Alhali Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi masa mazauni a Xa'ifa, kamar yadda suke cewa. Gashi kuma ya tafi Yemen xin zama kusa ga Makka da Madina.

Eh mana! A gaya mana dalilin da zai sa a matsa dashi can bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya aje shi kusa dashi. A gaya mana.

To kuma duk aje wannan. Ma'abuta ilimi sun tabbatar cewa, wannan magana da 'yan Shi'ah ke yayatawa, ta cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ya kore Hakamu zuwa Xa'ifa ba gaskiya ba ne, shi ne ya tafi a son ransa. Sannan kuma wani abu da zai tabbatar ma ka da cewa maganar tatsuniya ce. Shi ne kasawar waxanda suka ce Manzon ya yi masa korar, daga ambaton wani isnadi ingantacce, a kan yadda al'amarin ya faru dalla-dalla.

Sannan kuma malamin ya ce, wai daga cikin matsalolin, akwai korar da halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya yi wa Abu Zarri zuwa Rabaza. Da aurar wa Marwanu xan Hakamu 'yarsa da ya yi. Tare da dunqule wasu ganimomi biyar da aka samo daga Afrika, ya danqa masa. Waxanda qimarsu ta kai dinari dubu xari biyu.

**Martani:**

Ita maganar Abu Zarri da barin garin Madina da ya yi, mun riga mun yi bayani a kanta dalla-dalla a baya kaxan.

Wannan kenan. Sannan kuma me ya haxa aurarwa Marwanu da 'yarsa da al'amarin musulmi, balle ace hakan ta haifar da wata matsala a tsakaninsu? Sannan zancen ganima biyar ta Afrika da yaba shi, daga ina aka samo ta? Abin da suke faxa can farko shi ne halifan yaba shi dinari dubu biyu. Ka ga an sami savani nan take. To kuma ko a haka, ai kowa ya san waccan ganima ba ta kai wannan qima ba.

Bayan wannan kuma sai ya ce: Kuma daga cikin matsalolin akwai bayar da mafaka da halifa ya yi ga Abdullahi xan Sa'adu bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya halarta zubar da jininsa. Wai ma kuma halifan ya naxa shi gwamnan Masar bayan haka.

**Martani:**

Idan xan Shi'ar na nufin har zuwa lokacin da halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya tura Abdullahi xan Sa'ad xin Masar a matsayin gwamnansa, jinin nasa na nan halattace. Kamar yadda maganar tasa ke nunawa, to qarya yake yi. Kuma hakan ta qara tabbatar da kasancewarsa jahilin tarihin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Domin kuwa gaba xayan mutane; soja da farar hula a fagen sani sun yi ittifaqi, a kan cewa, an karvi tubar Abdullahi xan Sa'ad. Suka ce bayan da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya shelanta halartar zubar da jinin waxansu mutane da dama, a ranar da aka ci garin Makka da yaqi. Kuma a cikin mutanen nan har da Abdullahin nan. Bayan xan lokaci sai Usman *Raliyallahu Anhu* ya taho dashi wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya roqar masa afuwa. Shi kuma yayi mubaya'a. A qarshe kuma ya kulle amana da musulmi; ta a faxi a tashi tare. Daga nan sai jininsa ya koma haramtacce.

Sannan kuma malamin ya ci gaba da cewa: Kuma halifa Usmanu ya naxa kwamandan Askarawansa, Mu'awiyah xan Abu Sufyanu gwamnan Sham. Ya kuma kai Sa'ad xan Abu waqqasi Kufa. Ya kuma maye gurbinsa da Abdullahi xan Amru daga baya. Ya kuma tura Walidu xan Uqubata Busrah.

To abin da za mu tabbata wa xan Shi'ar a nan shi ne, halifa Umar xan Khaxxabi ne farkon wanda ya naxa Mu'awiyah gwamnan Sham bayan rasuwar xan'uwansa Yazidu xan Abu Sufyanu, wanda ke gwamna a can. Iyakar abin da halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya yi shi ne tabbatar ma sa da ci gaba da riqon Sham xin tare da haxe masa baki xayan sassanta. Kuma Mu'awiyah ya zauna da mutanen wurin zama na madalla; tarihin zamansa dasu cike yake da abubuwa masu faranta rai. Wanda hakan ta sa talakawan nasa ke matuqar girmama shi, da qaunar shi.

Ka ga ashe Mu'awiyah ya sami babban rabo musamman idan aka yi la'akari da abin da ya tabbata a cikin Buhari, a ingantaccen hadisin da aka samo daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* wanda ya ce: Zavavvu daga cikin shugabaninku sune waxanda kuke so, suke kuma son ku. Kuke kuma yi masu fatar alheri, suma suke yi maku.

Kuma tabbas tarihi ya tabbatar da cewa talakawan Mu'awiyah *Raliyallahu Anhu* suna matuqar sonsa tare da yi masa addu'a da fatar alheri. Haka shima, son da yake masu ne yasa ya riqa su da aminci, har ma yake masu fatar dauwama cikinsa ko bayansa.

Shi kuma zancen abin da ya faru tsakanin Sa'id xan Asi, wanda halifa Usman *Raliyallahu Anhu* ya naxa gwamnan Kufa, da talakawan nasa, abu ne sababbe. Mun riga mun faxa maku cewa su miyagun mutane ne asalatan. Babu gwamnnan daya tsira daga qorafe - qorafensu. Sa'ad xan Abu Wakkas, da Abu Musa al-Ash'ari da Ammaru xan yasir da Mugirata xan Shu'ubata duk sun zauna da mutanen Kufa, a matsayin gwamnoninsu. Amma babu wanda ya kwashe lafiya dasu. Sun shahara da irin wannan matsala. Illa dai abin nasu yafi qamari a lokacin halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* amma kuma ko Ali

*Raliyallahu Anhu* bai tsira daga sharrin suba. A matsayinsa na wanda shima yaba makusantansa muqamai kamar yadda Usman *Raliyallahu Anhu* yayi.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: kuma shahrastani ya ce: matsala ta tara kuma ita ce wadda ta faru a zamanin Sarkin Musulmi Ali *Raliyallahu Anhu* wadda ta haxa da: Tashin da Xalhatu da Zubairu suka yi zuwa Makka, bayan an zaxi Ali *Raliyallahu Anhu* a matsayin halifa har kuma an yimasa bai'a, da kuma xaukar sayyida Aisha *Raliyallahu Anhu* da suka yi kan Raqumi zuwa Busra. Da kuma dagar da suka shiga da halifan. Wadda aka sani da suna "Yaqin Basasar Raqumi". Da kuma savanin da ya shiga tsakaninsa da Mu'awiyah *Raliyallahu Anhu* wanda a qarshe ya haifar da "Yaqin basasar Siffin". Da kuma warewar da Amiru xan Asi ya yi wa Abu Musa al-Ash'ari.

Sai kuma savani daya faru tsakanin halifan da la'anannin Marikawan nan a Nahrawan.

Amma dai a taqaice, duk waxannan abubuwa da suka faru, Ali *Raliyallahu Anhu* shi ne mai gaskiya. Sai gashi kuma mutane irin su: Ash'as xan Kaisa da Mus'ir da Fadqi at-Tamini da Zaidu xan Huswain ad-da'i da wasunsu dake tare dashi, sun yi masa tawaye da sunan Harijawa. Bayansu kuma, duk a zamanin nasa aka sami "Gulatu" irin su Abdullahi xan Saba'i. Waxannan qungiyoyi biyu sune mafarkacin kowace irin fitina da varna. Kuma a haka sa maganar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi a kansa ta tabbata. Inda ya ce: mutum biyu za su halaka a kanka; wanda ya wuce wuri a cikin sonka da wanda ya zurfafa a cikin qinka.

Xan Shi'ar ya kammala wannan magana da cewa: don Allah ka dubi maganar wannan mutum (Shaharastani) da idon basira. Za ka fahimci cewa waxannan tsoffin bariki (halifofi uku kafin Ali *Raliyallahu Anhum)* su ne ummul-haba'asin duk wata fitina da ta faru a tarihin musulunci. Kar ka daxa kar ka qara.

**Martani:**

Eh; to. Wannan ra'ayinka ne. Amma a qashin gaskiya, duk wanda ya dubi wannan magana ta Shahrastani da idon adalci. Zai fahimci cewa marubucin ya shirya littafin ne kawai don ya tallata Shi'ah. Kamar yadda muka riga muka vulguta maku tun farko. Ah! To idan ba haka ba. Ai ya ambaci Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhu* fiye da sau shurin masaki. Amma baice "suke da gaskiya ba". Amma nan take, daya kawo kan Ali *Raliyallahu Anhu* sai ya yanke hukuncin cewa shi ne mai gaskiya. Kamar dai an naxa shi Alqalin alqalai.

Ka kuwa san ga al'ada, idan ba wata manufa kega marubuci ba, a matsayinsa kuma na mai bayar da labari, to baya wuce faxin abin da kowa yayi, da abin da aka yi masa. Amma duk wanda kaji ya kutsa wannan duhun daji, daga cikin musulmi. A qarshe kuma ya buye ga cewa: Gaskiya na tare da Ali, yana kuma tare da ita *Raliyallahu Anhu* su kuwa Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhu* to!---. Ka tabbata xan Shi'ah ne.

Kuma wani abin da ke tabbatar maka da cewa wannan magana qarya ce shi ne, cewar da Shahrastanin ya yi wai: Sai da aka daddale magana a kan zaven Ali *Raliyallahu Anhu* har aka yi masa bai'a. Sannan qura ta muske. Alhali kuma a haqiqanin gaskiya mafi yawan musulmi, har daga cikin mutanen Makka, ba su yi masa mubaya'a ba. Fita batun waxanda ke nesa. Irin mutanen Sham da Masar da Magrib da Iraqi da Khuransa.

Irin wannan magana ta haxuwar kan jama'a gaba xaya, bata faxuwa a kan Ali *Raliyallahu Anhu* kamar yadda take faxuwa a kan halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* wanda ba a sami mutum xaya daya qi goyon bayansa ba.

Wani abun kuma dake tabbatar da rashin gaskiyar Shahrastani a cikin wannan magana shi ne, sukar lamirin daya yi wa xalhatu da Zubairu da Aisha *Raliyallahu Anhu* ta hanyar wanka da kamar jirwaye. Ba tare da ya fito da al'amarin fili yadda ya faru ba. Alhali kuwa ma'abuta ilimi na qwarai, sun kwana da sanin cewa Xalhatu da Zubairu basu fita da nufin su yaqi Ali ba *Raliyallahu Anhu* Abin ya zamar masu dole ne, a matsayin kariyar kai. Haka suma mutanen Sham basu fita da niyar yaqar saba. Allah kawai ya qaddara haka ta faru. Shi Alin *Raliyallahu Anhu* ba nufinsa ne ya yi yaqi da waxancan ko waxannan ba. Qaddara ce kawai ta riga fata.

Malaman da suka naqalci zahiri da baxinin tarihin musulunci, sun bayyana cewa yaqin Raqumi ba yaqi ne ba. Rikici ne kawai na cikin gida. Koka ce masa "Yaqin Basasa" kamar yadda muka ambace shi a farko.

Dalili kuwa inji malaman shi ne; gaba xayan vangaroran biyu sun haxu ne, domin daddale yarjejeniyar da suka yi. Da shata yadda za a yi a kama makasa halifa Usmanu a hukunta su. Don a sami zaman lafiya; kowa yabar jin qaiqayi a ransa. A cikin wannan dufulomasiyya, sai makasan nasa, dake cakuxe cikin musulmi, suka tabbata cewa, idan suka yarda aka zartar da wannan yarjejeniya, lalle kashin su ya bushe. Saboda haka bari su sake tayar da wata fitina kamar yadda suka tayar da ita farko.

Sai nan take, suka kai farmaki kan Xalhatu da Zubairu da mutanensu. Su kuma suka yo kukan kura don su kare kansu. Sai makasan suka yi tururuwa, daga cikin jama'ar Ali *Raliyallahu Anhu* da cewa ga su Xalhatu nan za su far ma su. Nan take sai kuma Ali *Raliyallahu Anhu* ya sa qaimi, mutanensa, har da su makasan, suka rufa masa baya, a matsayin su ma masu kariyar kai, aka yi karon battar qarfe.

Subhanallahi. Allah ka kiyashe mu da halin munafukai.

Iyakar guri da niyyar kowane vangare kenan; kariyar kai. Amma ba yaqi ba.

To tunda ko har haka ne. Ka ga al'amarin sai hamdala da hauqala. Kuma kame baki daga gareshi shi yafi. Tunda Alqur'ani da Sunnah sun bayyana cewa, su zavavvu ne a wurin Allah, na kirki ne, 'yan aljanna.

## 2.60 'Yan Shi'ah na Taimakon Kafirai a Kan Musulmi

Bari mu fara da inda xan Shi'ar ke cewa: "Ka dubi maganar wannan mutum da idon basira da adalci. Za ka tabbatar cewa waxannan tsoffin bariki, yana nufin halifofi uku na farko, su ne ummul haba'isin wannan fitina".

**Martani:**

Zancen fitina a cikin musulunci, ko na-goye ya kwana da sanin cewa, 'yan Shi'ah ne mafarinta. Babu wata fitina ko wani sharri da ya faru ga wannan al'umma, face ka taras da cewa su ne kanwa uwar gami a ciki. Domin kuwa ai wutar fitinar farko da ta kama a tarihin musulunci, su ne suka hasa ta, don su ne suka kashe halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu.*

Imamu Ahmad ya riwaito daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa: "Fitinu uku, duk wanda ya tsira daga cikinsu to, shi ne tserarre. Mutuwata, da kisan wani halifa a kan zalunci, da kuma Dujjal".

Wannan kenan. Wani abu kuma dake tabbatar da kasancewar maganar wannan xan Shi'ah qarya shi ne, duk wanda ya bibiyi diddigin tarihin qungiyoyi a duniya, zai tabbatar cewa, Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* mutane ne da Allah *Subhanahu WaTa'ala* ya shaida a cikin Alqur'ani da kasancewa mafiya alheri daga cikin halitta, kamar inda yake cewa:

﴿كُنتُمْ خَيْرَ أُمَّةٍ أُخْرِجَتْ لِلنَّاسِ تَأْمُرُونَ بِالْمَعْرُوفِ وَتَنْهَوْنَ عَنِ الْمُنكَرِ وَتُؤْمِنُونَ بِاللَّهِ ۗ وَلَوْ آمَنَ أَهْلُ الْكِتَابِ لَكَانَ خَيْرًا لَّهُم ۚ مِّنْهُمُ الْمُؤْمِنُونَ وَأَكْثَرُهُمُ الْفَاسِقُونَ ﴿١١٠﴾﴾
آل عمران: ١١٠

*Kun kasance mafi alherin al'umma, wadda aka fitar ma mutane; Kuna umurni da Alheri, kuma kuna hani daga abin da ake qi, kuma kuna imani da Allah (3:10).*

Su ne mutanen da suka fi kowa son zaman lafiya. Domin kuwa ba a tava samun jama'a wadda kanta ya haxu a kan shiriya, da faxaka da nisantar fitina da savani da rarrabuwar kai, a tarihin duniya kamar su ba.

Haka kuma kundin tarihin ya tabbatar da cewa 'yan Shi'ah sun fi kowa nisa daga shiryayyar qungiya wadda Allah ke taimako.[1] Hakan kuwa ta faru ne a sakamakon kasancewarsu mafiya jahilci da zalunci daga cikin qungiyoyin shexan, waxanda ke iqirarin kasancewa cikin musulmi masu mayar da gaba gabas su yi sallah.

[1] Yana nuni zuwa ga hadisin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce, har abada akwai qungiyar shiryayyu wadda Allah ke taimako. 'Yan Shi'ah kuwa sun fi kowa nisa da ita. Daga Masu Fassara.

Haka kuma ya tabbata cewa, zavavvun wannan al'umma su ne waxancan Sahabbai. Sun kuwa samu wannan sheda da matsayi a sakamakon kasancenwarsu shafe zane a fagen zama tsintsiya maxaurinki daya, a cikin shiriya da addinin gaskiya. Tare da yin matukar nesa-nesa daga xai-xaicewa da zaman 'yan marina. Duk kuwa wani abu na tasgaro da kasawa, da wani zai ce ya faru daga waxannan mutane, ba zai wuce ajizanci irin na xan Adamu ba. Kuma da za a kwatanta shi da wanda ya faru daga wasunsu, za a taras da bai taka kara ya karya ba.

Fita batun duk wani abu da mutum zai qaddara a cikin zuciyarsa, ya kuma nace a kan kasancewarsa, alhali Allah *Subhanahu WaTa'ala* bai halicci mai irin wannan abu a cikin qanana da matsa kaita da manyan bayinsa ba. Kamar abin da waxansu ke cewa, wai lallai ne shugaba ya kasance ma'asumi. Wasu kuma su ce, a'a, ko dai bai kai ma'asumi ba, ya kasance xan qwarya-qwarya. Kai wasu ma za ka taras suna jin cewa, ya kamata duk yadda malami ko shehi ko shugaba ko sarki ya qasura, tattare da yawan iliminsa da kishin addininsa da yawan ayyukansa. Duk da haka su a wurinsu lalle ne ya kasance ya san komai, ta yadda ba ya kure a cikin kowace irin mas'ala. Ya kuma fita daga layin mutane, ta yadda babu abin da zai vata masa rai balle ya yi fushi. Kai da yawa daga cikin irin waxannan mutane ma ke gurin shugaba ya siffanta da wata sifa da ko Annabawa albarka.

Ka ga wannan ya sava wa hankali. Domin kuwa ai Allah *Subhanahu WaTa'ala* umurtar Annabi Nuhu da Muhammadu *Alaihimus Salamu* Ya yi da su ce:

﴿ وَلَآ أَقُولُ لَكُمۡ عِندِي خَزَآئِنُ ٱللَّهِ وَلَآ أَعۡلَمُ ٱلۡغَيۡبَ وَلَآ أَقُولُ إِنِّي مَلَكٞ ﴾ هود: ٣١

*Kuma ba ni ce muku a wurina taskokin Allah suke, kuma ba ina sanin gaibi ba ne. Kuma ba ina cewa ni mala'ika ne ba. (11:31).*

Amma kuma tattare da wannan magana, sai ka taras da jahilai daga cikin mabiya na gurin shugabansu ya kasance masanin duk abin da za'a tambaye shi, mai iko a kan duk abin da za'a nemi ya yi. Ya kuma wadatu daga duk wasu buqatu irin na 'yan Adamu; wato ya dai zama kamar mala'ika. Irin wannan guri da fata da wasu mabiya ke yi wa shugabanninsu, daidai yake da fatar da Harijawa ke yi wa al'umma baki xaya, wato kada wani ya aikata wani zunubi daga cikinsu. Wanda kuwa duk ya aikata, to a wurinsu ya kafirta kuma xan wuta ne har abada.

Da wannan matsayi na Harijawa da wancan na 'yan Shi'ah da wasunsu daga cikin qungiyon bidi'a, duk vata ne. Allah *Subhanahu WaTa'ala* bai halacci irin waxannan mutane ba, balle ya shari'anta irin waxannan siffofi.

Harwayau kuma dai, muna qara nanatawa. ‘Yan Shi’ah su ne matattarar vata da danbarwa, fiye da kowace qungiya daga cikin qungiyoyin da ke jingina kansu ga wannan al’umma. Kamar yadda su kuma ma'abuta hadisi da tantagaryar Sunnah, su ne matattarar shiriya da sawaba da rahama fiye da kowace qungiya daga cikin qungiyoyin wannan al'umma. Wanda hakan ta sa duk motsin da za su yi, lalle ne ya kasance taimako ga sunnar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* don ba su da kowa sai shi. Shi ne shugaba a garesu na qarshe. Ba su sauraren maganar kowa, sai idan ta yi muwafaqa da tashi. Kuma fatarsu kodayaushe ita ce taimakon addinin Allah da sunnar Manzo.

To, ka ga a hankalce, idan Sahabbai da ma’abuta hadisi da tantagaryar sunnah, sun kevanta da kasancewa ma’abuta shiriya da addinin gaskiya, mafiya nisantar qungiyoyi daga shiriya su ne masu zagin su.

A haka kenan, ta bayyana ga dukkan mai hankali cewa, maganar wannan xan Shi’ah shirme ne kawai irin wadda babu mai kafa hujja da shi sai jahili. Haka kuma ta bayyana cewa marubucin, son rai ne yake bi, illa iyaka. Ga shi kuma bai san kome ba a cikin fannin riwaya. Matsayinsa bai wuce na masu bada qissoshi a cikin masallaci ba.

Su dai ‘yan Shi’ah an sani cewa, munafukai ne da suka shigo musulunci da nufin gurvata shi. Saboda haka suka qirqira qarairayi, suka haifar da miyagun ra’ayoyi don cimma wannan manufa tasu, ta qasqanta duk wanda ke kan tafarki madaidaici. Saboda haka suka fara da kashe halifa Usmanu, wanda shi ne xaya mafarin qirgar fitina. Bayan haka sai suka koma suka kewaye Ali *Raliyallahu Anhu* da sunan so da qauna gare shi da 'yan gidan Manzon Allah, alhali kuwa manufarsu ita ce girka sanwar fitina a tsakanin musulmi.

Wannan dalili ya sa za ka taras da 'yan Shi’ah kodayaushe suna goyon bayan kafirai da waxanda suka yi ridda. Kamar yadda suka goyi bayan *Banu Hanifata* mabiyan Musailamatul-Kazzabi, suka ce wai musulmi sun zalunce su, a qarqashin shugabancin Abubakar *Raliyallahu Anhu* kamar yadda marubucin ya ce. Haka kuma za ka same su suna goyon baya da jin-jina wa kasurgumin kafirin nan Abu lu’uluatal Majusi wanda ya kashe sayyidina Umar.

Bari kaji yadda abin ya kasance: An riwaito cewa, Abu lu’uluata ya nemi halifa Umar ne da ya sa baki tsakaninsa da masu karvar haraji, don a sassafta ma shi. Halifa Umar ya yi niyyar sa bakin, amma kafin haka sai qiyayyar da ke kimshe cikin zuciyar Bamajushen zuwa ga musulunci da musulmi ta yunquro masa. Sai kawai ya kashe halifa Umar, saboda ya xaukar wa kafirai fansar fatattakar da Umar xin ya yi masu lokacin da ya ci qasashensu, inda ya karkashe shugabanninsu ya kuma rarrabe dukiyoyinsu a tsakanin musulmi.

Ka ji aika-aikar da Abu Lu'ulu'ata ya yi. To, don Allah kai kana ganin akwai wanda zai kalli irin wannan bawa da gashi a ka, balle har ya koxa shi, in ba mafi girman kafirce wa Allah da Manzo daga cikin mutane, da qiyayya da musulunci, da kai matuqa ga jahiltar al'amurransa ba?.

To, mu fita batun ma wannan, da duk wani abu da a ke ji ko ake karantawa wanda ya faru tsawon shekaru, duk mai hankali da ya dubi abin da ke faruwa yau a zamaninsa, da wanda ya faru jiya kaxan na fitinu da sharri da varnace-varnace a cikin musulunci, zai taras da cewa 'yan Shi'ah ne suka haddasa mafi yawansa. Zai kuma tarar da cewa aikinsu kenan: duk abin da zai jefa wannan al'umma cikin wutar fitina da sharri da varna, to suna lale marhabin da shi.

Mu mun sheda, mun kuma ji ta lafiyayyun hanyoyi, abin da ya faru a wannan zamani namu. Mun ga irin yadda *Jankizkhan* sarkin kafiran Turkawa ya danno, da irin mugun abin da ya faru ga musulunci, na mamayewar da kafirai mushrikai suka yi wa qasashen musulmi. Suka taka dangin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* Hashimawa da Banul Abbas yadda suke so. Suka kashe na kashewa, suka raunata na raunatawa. Suna da ribaci mata muminai suka halatta farjojansu. Qananan yara kuwa suka shigar da su cikin addininsu, tare bautar da su.

Wannan duk ban da karkashe malamai da suka yi da fitattun makarantan Alqur'ani da wargaza masallatai. Daga sai suka samu damar xaukaka darajar gidajen gumaka waxanda suke yi wa laqabi da *Al-Bazkhanat*, da wuraren ibadar Yahudawa da 'yan mishan. Kai da waxansu abubuwan da dama, waxanda ba su da daxin faxi.

Kuma duk mai hankali ba ya shakkun cewa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* zai dawo duniya, ya ga wannan illa da ta faru ga al'ummarsa lalle zai yi baqin ciki fiye da wanda zai yi, a kan musulmi biyu da suka shaya daga tsakaninsu saboda tabbatar da mulki na gari. Dalili kuwa shi ne su waxannan yaqe-yaqe na basasa, babu wani vangare daga ciki da aka ribace matansa, ko aka keta alfarmarsa. Kuma ba su qari wani kafiri da komai ba. Kamar kuma yadda ba su rosa wasu shari'o'i mutawatirai, bayyanannu na musulunci ba.

Ka dubi girman wannan al'amari. Ya kuma faru bisa ga gayyata da tallafi na musamman daga 'yan Shi'ah. Haka kuma mutane sun sheda a lokacin da *Holaku* Sarkin kafiran Turkawa ya shiga qasar Sham a shekara ta 658H. 'Yan Shi'ah da ke cikin Sham a birane da qauyuka, waxanda suka haxa da mutanen *Halab* da maqwabtanta da na Dimashqu da kewayenta, su ne suka zama manya-manyan dakarun da waxannan kafirai suka yi amfani da su ga tabbatar da mulkinsu, bayan sun roshe na musulmi.

Haka abin ya kasance a lokacin da Holakon ya isa qasar Iraqi, ya kashe halifa da musulmin da Allah ne kaxai ya san adadinsu. Babba da yaro, kowa ya san cewa a wannan lokaci, wazirin halifan ne, wato Ibnul-Al-qami xan Shi'ah da mutanensa suka mara wa wannan kafiri baya, suka taimake shi ta hanyoyi daban-daban, na voye da na bayyane. Waxanda faxarsu ba za ta yiwu ba, ko wani sarki ya ci ya fita.

Haka kuma an tabbatar mana da cewa, 'yan Shi'an sun ci gaba da kasancewa tare da Jankizkhan, don musulmi na ganin su tare kodayaushe, a cikin sasannin Sham da sauran garuruwa.

Kai! Babu wani lokaci da musulmi za su shaya daga da Nasara, face 'yan Shi'ah sun yi qawance da Nasaran, tare da ba su kowace irin gudunmuwa gwargwadon ikonsu. Suna baqin ciki da qyamar su ji an ci wani gari na Nasara da yaqi. Kamar yadda suka qyamaci cin garin Akka da ire-irensa. Kai kama hannun Nasaran ma suke yi suna nuna masu inda musulmi suke. Akwai ma wani lokaci da aka yi qanfar rudunar musulmi a Sham, a shekara ta 599H. Ganin haka sai 'yan Shi'ah suka bazu a cikin garuruwa suna ta varna da masha'a ta hanyar kashe Ahlus-Sunnah da qwace dukiyarsu. Tare da kaxa tutar da ke xauke da hoton kuros a sama, da kururuta fifikon Nasara a kan musulmi. Qarshe ma har ribace musulmi da dukiyoyinsu da makamansu suka xora yi suna kai wa Nasara abokan gaba, a *Qubrus* da wasu garuruwa.

Mutane da yawa sun shedi waxannan abubuwan da makamantansu. Wanda kuwa bai ganar wa idonsa ba, ya ji ta hanyoyi mutawatirai. Wallahi da zan ambaci gaba xayan abin da na gani da wanda na ji a kan wannan lamari da wannan littafi ya gagari kundila. Na kuma tabbata mutane da yawa sun san wasu abubuwa filla-filla na wannan labari, waxanda ban sani ba.

Taimakon da 'yan Shi'ah ke yi wa kafirai a kan masulmi da irin yadda suka fi qaunar ganin kafirci da kafirai sun bice hasken musulunci da musulmi abu ne da ya fi rana bayyana idan ta fito.

Mu qaddara cewa musulmin da 'yan Shi'ah ke wannan matsananciyar gaba da su, azzalumai ne kuma fasiqai, waxanda kuma ke bayyanar da nau'o'an bidi'o'i waxanda suka fi zagin Ali da Usmanu *Raliyallahu Anhuma* nauyi. Duk da haka, da a ce 'yan Shi'ah mutane ne masu hankali, kamata ya yi su auna irin sharrin da wannan aiki nasu zai haifar, da alherin da ke cikin rashin yin sa.

Ai ka ga su Ahlus-Sunnah, da yake mutane ne masu cikar hankali, tattare da abin da suke faxa na kasancewar Harijawa da 'yan Shi'ah da wasunsu daga cikin mutanen bidi'a karkatattu, ba su tava taimakon kafirai a kan xaya daga cikinsu ba, balle su guraci rinjayen kafirci da kafirai fiye da yadda wata 'yar qaramar bidi'a za ta bayyana. Don sun san haka rosa kai ne.

Su kuwa 'yan Shi'ah da xai haka suke. Idan suka sami sa'a ba su iya ba. Dubi abin da suka haifar na varna a zamanin daular sarki *Khudabandah*, wanda aka rubuta wa wannan littafi, da muke martani a kansa. Sharrin da waxannan mutane suka qulla a wannan lokaci, da ya tabbata ya kama qasa sosai, da gaba xayan shari'o'in musulunci sun kwanta dama! Sai dai da yake ta Allah ba tasu ba; kullum suna qoqarin bice hasken Allah ta hanyar amfani da kaifin halsunansu, amma Allah na daxa tabbatar da haskensa, ko da kafirai sun qi.

Su kuwa halifofi da sauran Sahabbai su ne tushen duk wani alheri da musulmi ke ciki a yau har Allah Ya naxe qasa. Su ne suka yi jihadi fi sabillillahi, har hasken imani da musulunci da Alqur'ani da sauran fannonin ilimi, da ibadodi suka kammala, dashensu ya haxu ya yi kyau ya barbaje. Musulmi suka yi galaba a kan kafirai, kalmar Allah ta xaukaka, aljanna ta tabbata ga musulmi wuta ta nisanta daga gare su. Gaba xaya aikin da Sahabban can suka yi na yaxa addini, shi ne ya tabbatar da wannan.

A kan haka babu wani mutum da ya yi imani da Allah face Sahabbai nada kamisho da falala a cikin haka har rana ta qarshe. Kai su kansu 'yan Shi'ah, duk wani abu na alheri da suke cikinsa, sun same shi ne albarkacin waxannan Sahabbai. Su kuma halifofin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* shiryayyu, su ne kan gaba a sahun wannan alheri da aka samu ta hanyar Sahabbai. Domin kuma a duniya da lahira babu wani Sahabi da ya kamo qafarsu a fagen aikata alheri da dasa shi. To, ta yaya za a wayi gari yau a ce mana su ne mavuvvugar sharri, su kuma 'yan Shi'ah wai su ne mavuvvugar alheri?

Alhali kuwa sanannen abu ne cewa, shi wannan xan Shi'ah yana bisa turbar waxancan 'yan Shi'ah ne, ta qin jinin Sahabbai. Ashe wannan ba yana nuna kasancewarsu mafi sharrin waxanda Allah Ya toshe wa basira ba?:

﴿فَإِنَّهَا لَا تَعۡمَى ٱلۡأَبۡصَٰرُ وَلَٰكِن تَعۡمَى ٱلۡقُلُوبُ ٱلَّتِي فِي ٱلصُّدُورِ ٤٦﴾ الحج: ٤٦

> *Domin haqiqa makanta ba ta idanu ba ce, amma makanta (ta gaskiya) ita ce makantar zukata waxanda ke cikin qiraza (22:46).*

## 3.0 ZANGO NA UKU:
## DALILAI NA HANKALI

Xan Shi'ar ya ce: Fasali na uku wanda zai yi magana a kan dalilan da ke tabbatar da cancantar sarautar Sarkin Musulmi Aliyu xan Abu Xalib, shugaba bayan wucewar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Duk da yake waxannan dalilai na da matuqar yawa, ta yadda ba za a iya qididdige su ba. Saboda haka za mu ambaci mafi muhimmanci daga cikinsu, ta hanyar karkasa su gida huxu. Inji shi:

Waxannan dalilai guda biyar ne. Na Farko: Lalle ne duk wanda zai shugabanci al'umma bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a matsayin Imamu, to, ya kasance ma'asumi. Wannan dalili kuwa shi zai tabbatar da cancantar Aliyu *Raliyallahu Anhu* da wannan kujera.

"Dalilinmu a kan goshin wannan magana inji xan Shi'ah, wato wajabcin samar da shugaba ga jama'a da zancen kasancewarsa ma'asumi shi ne: Kasancewar mutun wata halitta da Allah *Subhanahu Wa Ta'ala* Ya sa wa son zama cikin taro, ta yadda rayuwarsa za ta yi qunci da tasgaro matuqa, idan ya ce zai rayu shi kaxai. Saboda buqatunsa na samun abin ci da sha, da sutura da wurin bacci kodayaushe, ba za su samu tabbatuwa ba, matuqar ya yi tsinbirin gata. Dole ne yana da buqata da gudunmawar wasu mutane irinsa, waxanda kowane daga cikinsu, har da da shi kansa, zai tsare wa xan'uwansa wata daga ta waxancan buqatu. Ta wannan hanya ce kuwa kawai jinsin xan adam zai iya ci gaba da wanzuwa a bayan qasa".

"Irin wannan haxuwa kuwa, wuri xaya da nufin zama, ta gadi haifar da qeta da son kai. Ta yadda wasu daga cikin mazaunan za su yi qyashin abin da ke hannun wasu har ma su yi gurin gushewarsa ko dawowarsa a hannunsu ta hanyar qwace ko yaudara. Wanda hakan kan haifar da qunci da tajin-tajin da tashin fitinu. Ka ga a irin wannan yanayi, dole ne a samar da shugaba ma'asumi wanda zai hana mutane zaluntar juna da wuce iyakoki. Ya tabbatar da ganin kowa ya tsaya wurinsa tare da qwato wa wanda aka zalunta haqqinsa daga wanda ya yi zalunci da kuma sadar da kowane haqqi ga mai shi. Duk kuwa wanda zai hau wannan matsayi, lalle ne ya kasance ba ya kuskure ko mantuwa ko savo. Idan kuwa ya kasa cika waxannan siffofi, to zaune ba ta qare ba. Don har yau dai al'ummar na da buqata da wani shugaban ba shi ba. Domin kuwa toshe kafafen kurakuran a cikin al'umma ne dalilin da ya sa aka naxa shi, To, idan har kuwa shi ma irinsu ne, an yi faxuwar guzuma kenan ka ga dole a nemo wani shugaba wanda ba ya kuskure. Idan shi ma ya bi hanyar na gabansa, to babu hus. Haka al'amarin zai ci gaba da tafiya yana kwan-gaba kwan-baya".

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: "Shi kuwa abin da qirjin wannan magana ya qunsa, wato ma'asumancin Aliyu *Raliyallahu Anhu* a matsayin

shugaba abu ne bayyanane. Domin kuwa babu xaya daga cikin Abubakar ko Umar ko Usmanu wanda ma’asumancinsa ya tusgo bisa haxuwar malamai. Amma ta tabbata cewa Ali *Raliyallahu Anhu* ma'asumi ne. Saboda haka shi ne ya kamata ya zama magajin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na farko”.

**Martani:**

Gaba xayan waxannan maganganu; goshin da qirjin, vatattu ne. Bari mu fara da farko, inda ya ce: Dole ne a samar da shugaba ma'asumi wanda zai hana mutane zaluntar juna da wuce iyakoki, ya tabbatar da ganin kowa ya tsaya wurinsa, tare da qwato wa wanda aka zalunta haqqinsa daga wanda ya yi zalunci, da kuma sadar da kowane haqqi ga mai shi. Ya kuma ce, duk wanda zai hau wannan matsayi, lalle ne ya kasance ba ya kuskure ko mantuwa ko savo.

To a nan sai mu ce: Mu ma Ahlus-Sunnah mun yarda da wannan dalili da ke wajabtar da samar da shugaba ga jama’a. Amma inda gizo ke saqa shi ne, wane ne ma'asumin? Amsa a nan ita ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kuma wajibi ne a kan kowane mutum a kowane zamani ya yi xa'a da biyayya gare shi. Kuma Alhamdu lillahi, abin da ke hannunmu na horo da hani, waxanda ya yi wa al’ummarsa, ya fi cika da kamala a kan abin da xaixaikun shugabanninku suka sani na horo da hani, waxanda voyayyen imaminku ya yi.

Ko shakka babu, shugabanci da ma'asumancin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* su ne mafiya bayyana da tabbata. Kuma ga shi babu wani daga cikin al’ummarsa wanda ya jahilci horace-horace da hane-hanen da ya yi. Magana ta qare. Wannan shi ne matsayinmu.

Su kuwa ‘yan Shi’ah, qololuwar abin da za su gaya maka a kan sha’anin nasu ma'asumin shi ne har yanzu bai riga ya bayyana ba, ana nan ana ta dakon isowarsa. To, ba wannan ma kawai ba. Babu wani mutum a duniya ko da kuwa daga cikin ‘yan Shi’an, da zai bugi qirji ya ce ya san wani horo ko hani daga wannan imami na voye, kamar irin yadda gaba xayan al’umma suke da cikakkar masaniya da shari’o’in da Manzonsu Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya zo masu da su. Ta yadda ba su da buqata da wani shugaba wanda ba shi ba. Ko wani Wanda zai yi labu da wasa da abubuwan da wannan addini nasu ya qunsa. Domin kuwa duk abin da suke da buqata da shi, don gudanar da ayyukan addini, Manzon ya riga ya zazzage masu shi. Ba kamar xaixaikun masu da’awar wancan shugaba ma'asumi ba, waxanda ba su san komai dangane da shi ba ko da an qaddara samuwarsa. Har yau dai baya ga Aliyu *Raliyallahu Anhu* babu wani daga cikin imaman can da ake wa gogen

ma’asumanci, da ya tava jagorantar mutane a zahiri. Sai ko Al-Hasan da ya yi na wata shida.

Muna da cikakkar masaniya kuma yankakka, cewa akwai mabiyan wannan imami voyayye, a qasar Yaman da Khurasana da waxansu qasashe, da ba su san abu xaya wanda ya yi umurni ko hani da shi ba. 'Yan korensa ne kawai ke wasa da hankalin mutane.

Amma ka ga waxanda suka gaji ilimin da Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya zo wa duniya da shi, sun san komai a cikinsa filla-filla. Kuma suna sanar da sauran mutane shi tsakani da Allah; ba ragi ba qari, fiye da yadda waxanda ke waqen bin Ali *Raliyallahu Anhu* suka san matsalar da irin yadda suke isar da ita ga duniya. Iyaka kawai abin da suke qoqarin tabbatarwa shi ne wajabcin samar da shugaba ma'asumi a raye.

To, muna tabbatar masu da cewa, wannan magana tasu vata ce, ta fuskoki kamar haka:

**Fuska ta farko**: Ba a tava samun wani shugaba, a inda aka fito, da waxannan sifofi da suka zayyana ba. Haka kuma a wannan zamani namu. Wanda dai ke da waxannan sifofi shi ne wanda ko a wurin mabiyansa sunansa Malam-na-Voye, balle a wajen masu hankali a cikin al’umma. Su a wurinsu sunansa Malam-babu.

To duk kuwa wanda yake haka, babu wani abu daga cikin manufofin shigabanci, da ke iya tabbatuwa ta hanyarsa, asalatan. Kai duk wanda ma za a shugabantar wa mutane, ko da kuwa iliminsa da adalcinsa ba su taka kara sun karya ba, matuqar dai ga shi a sarari, to ya fi fa’ida gare su bisa ga irin wannan da babu wata hanya da zai iya amfanar da su da ita da komai.

Ko da kuwa mabiyan shi wannan ma'asumin voye, sai sun nemi gudunmawar wasu mutane a kan wasu al’amurra nasu. Waqen kasancewarsa majivincin al’amuransu kawai suke yi. Amma idan suka tashi neman wani agaji sai su nema daga wani qasurgumin kafiri ko azzalumi. Idan kuwa har wannan ma'asumi da ake jira ya kasa amfanar da ko waxanda suka yi imani da shi a cikin wani sha’ani nasu na duniya ko lahira, ba ta yadda za a yi ya iya tabbatar da wani abu na gallar shugabanci da manufofinsa ga wani.

To, idan ko har babu wata manufa daga cikin waxannan manufofi na shugabanci da ke iya tabbata ta hanyar Malam-na-Voye, to, kuma ba mu da buqatar tabbatar da hanyoyin rashin yiwuwar haka. Domin kuwa ba don guga tana guga ake sayenta ba. A’a sai don a jawo ruwa da ita. To idan kuwa har ta tabbata cewa babu wata rijiya a gari da ke da ko xigo na ruwa, to zancen guga vata lokaci ne. Kamar dai a ce ne ga mutane na buqatar agajin abinci da abin sha masu kama kaza. Kuma qabila kaza ce kawai ake iya samun su daga gare su. Amma kuma tarihi ya tabbatar da cewa ko veran masallaci ya san da zaman wannan qabila saboda tsananin rashi da talauci. Ka ga ai ba magana.

To kamar haka ne babu wata fa'ida da za'a samu a cikin neman duk wani abu da ake da masaniyar babu shi. Ko kuma biyayya ga wanda ba ya da amfani ko masoso. Ai ana buqatar shugaba ne don xayan abubuwa biyu: Ko dai don wani ilimi da ya kevanta da shi, don ya isar da shi ga mutane ta hanyar karantarwa. Abu na xaya kenan. Na biyu Kuma, ko don ya taimaki mutane da qarfin mulkinsa a kan aiki da wani ilimin da suka riga suka sani.

To, shi wannan Malam-na-Voye da ake jiran bayyanarsa, ba ya iya amfanar da al'umma da xayan waxannan abubuwa biyu. Duk ma abin da suke da shi na ilimi, sun same shi ne daga cikin zantukan waxanda suka gabace shi. Ta fuskar aiki kuwa, sukan nemi gudunmawar musulmi ne, a cikin abubuwan da kansu ya haxu da nasu a ciki. Idan kuwa ba su sami haka ba, sai su nemi gudunmawar kafirai da zindiqai da makamantansu.

Kar ka yi mamakin wannan magana tawa. Idan ba ka sani ba, Allah bai halicci mutane mafiya ragganci da jahilci kamar waxannan mutane ba, tattare kuwa da gogen da suke yi na kasancewa mabiyan ma'asumi. Alhali kuwa ita wannan kalma ta ma'asumi na nufin siffantuwa da cikakken ilimi da qarfin iko na aiwatarwa. Amma su, da ilimin da ikon ba su da ko xaya. Hakan kuwa ita ke tabbatar da koruwar duk abin da suke waqa. Kuma babu xaya daga cikin shugabannin da aka yi, wanda manufofin shugabanci suka tabbata ta hannunsa albarkacin xaya daga cikin waxancan imamai goma sha biyu. Idan kuma ka cire Ali *Raliyallahu Anhu* ka yi qasa da lissafi, za ka taras cewa, babu wani abu na ilimi ko kishin addini da suka qarar da mutane da shi, fiye da yadda takwarorinsu ke iyawa da yi. Abin da Zainul Abidina da xansa Baqiru da jikansa As-Sadiq suka kasance suna karantar da mutane a zamaninsu, daga cikin abin da Allah ya sanar da su, bai fi wanda sauran malaman zamaninsu ke karantarwa ba. Kai akwai malaman da ma suka fi su ilimi da amfanar da jama'a a wancan zamani. Babu wani ma'abuci ilimi da bai san haka ba.

To, ko da ma za a qaddara cewa sun fi kowa ilimi da kishin addini a wancan zamani, ai wannan ba wani abu ne ba. Domin tarihi bai ambaci wani tasiri da ma'abuta ilimi da kishin addini suka yi, a fagen tabbatar da mutane a kan gaskiya da hana su varna, ta hanyar amfani da qarfin iko ba, kamar yadda ma'abuta mulki suka yi.

To, sauran imamansu bayan ukun da muka ambata, musamman ma dai biyun na qarshe, ba su da wani ilimi da tarihi ya tabbatar da al'umma ta qaru da shi, ko wani qarfi da ta yi shinge da shi. Matsayinsu bai fi na sauran Hashimawa ba, waxanda mutane ke gani da gashi a ka don kusancinsu da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da fuskar dangantaka. Ilimin da su ke da shi na abubuwan da suke da buqata da su a musulunci, bai fi na sauran takwarorinsu ba. Shi ne kuma irin ilimin da fararen hula daga cikin musulmi ke da shi.

Amma abin da ma'abuta ilimi suka kevanta da shi na sannai, su ba su sami wani rabo daga cikinsa ba. Saboda haka ne ma ba a yi almajircin ilimi a wurin su ba, kamar yadda aka yi ga waxancan uku na farko. Da kuwa mutane a lokacinsu sun san akwai abin, da sun je nemansa. Amma ka san ba wanda ya san abin da ya ke buqata kamar mai neman ilimi

Wani abu da zai tabbatar maka da haka shi ne, duk wanda ke da ilimi da girman asali, za ka tarar da asalin ya taimaka ga kwararowar mutane zuwa gare shi don su qaru. Ai ka ga da yake xan Abbas na da tarin ilimi, al'umma ta ji ta kuma fa'idantu da shi. Kuma babba da yaro kowa ya ji sunansa.

Haka Imamus-Shafi'i, nasabarsa ta Quraishawa ta qara fitowa da shi fili, ilimin da ya ke da shi na fiqihu da sauran fannona ya bayyana, aka qaru da shi.

Amma da zarar mutum ya tarar da babu abin da yake nema a wurin da ya yo qarere, ko tashen batun ba zai yi ba. Yau da za a cika duniya da waqen cewa ai wane qwararren malami ne a fannin likitanci ko Nahawu, aka cicciva shi har wasu daga cikin masana likitanci ko Nahawu suka ziyarce shi. Amma suka tarar da cewa bai san abin da suke nema a cikin waxannan fannoni ba. za su koma inda suka fito ne. Ka ga koxa shi da xaukaka sunansa da jahilai suka yi bai daxa shi da komai ba.

Wannan kenan. Kuma sai Shi'ah 'yan-sha-biyu suka tsallaka suka je wurin Mu'utazilawa suka aro wasu aqidu da suka danganci siffofin Allah da makamantansu. Ita kuma matsalar shugabanci sai suka azizita ta har ta fi Annabta matsayi a wurin su.

Suka ci gaba da cewa: Al'adu da shuxewar kwanuka sun tabbatar mana da sanin cewa, a duk lokacin da jama'a suke qarqashin jarumin shugaba wanda ake tsoro, ake kuma yi wa biyayya ko ba don Allah ba. Sai don iya shugabancinsa da shinfixa hannayensa. Haka ta fi sa su kasancewa mafi zama kusa ga shiriya da nisantar varna. Balle daxa idan babu shugaban baki xaya, sai a wayi gari qunci da yamutsi sun mamaye su, su kuma zama nesa qwarai daga shiriya.

To, ka ga wannan matsala ita ce kanwa uwar gami, a cikin sha'anin sa hankali gaba a cikin addini. Sanannen abu ne da ba mai musun sa, sai wanda ya jahilci halin rayuwa, bai kuma san qa'idar xorewar zaren tunani a cikin kai ba. Daga nan sai suka ce: Idan kuwa har hakan za ta taimaka ga xauke nauyin hukunce-hukunce, ai kuwa tabbatar da wanzuwarsa ya zama wajibi. Don haka sai suka ambaci siffofin shugaban, waxanda suka haxa da ma'asumanci da waninsa.

Wasu daga cikinsu suka tambayi kansu da cewa: Ah, to idan mun ce shugaba rahama ne da taimako ga xauke nauyin shari'a, to ai ba mu tare da shi yanzu! Ba kuwa yadda za a yi luxufi da taimakon wanda ba ya nan ya wanzu. Idan kuwa har ta tabbata ba za a iya samun wannan luxufi ba matuqar dai

imamin yana fake, ga kuma nauye-nauyen shari'a sun tabbata, kenan cewar da muka yi shugaba luxufi ne a cikin addini ta tashi. Kuma ba mu da bakin sake sharxanta ma'asumancin wani shugaba.

Sai kuma suka ba junansu amsa da cewa, a'a, ai muna nufin ne luxufin wancan shugaba da ke fake, na samuwa ne ga waxanda suka san da zamansa, suna nan bayyane. Waxanda kawai wannan luxufi ba zai sama ba, su ne waxanda ba su yarda da kasancewarsa imaminsu ba. Kamar dai yadda luxufin sanin Allah ba zai samu ga wanda bai san shi ba.

A qarshe suka ce: Qaryar waccan tambaya ta qare, sanadiyyar wannan bayani. Saboda haka suna nan kan bakarsu na kururuta wajabcin ma'asumancin shugaba.

Kawowarsu nan ke da wuya sai aka ce masu: To, idan kuwa luxufinsa na iya saduwa da ku yana faken kamar yadda zai sadu da ku idan ya bayyane, kenan wajibi ne ku wadatu daga bayyanarsa, don ba ta da wani amfani. Sai kawai ku ci gaba da biyayya gare shi yana faken har ku mutu. Mun kuwa san wannan ba shi ne manufarku ba.

Sai suka sake karvawa da cewa, ai abin da muke nufi da saduwar luxufinsa ga waxanda suka yi imani da kasancewarsa shi ne ta hana su kusantar miyagun ayyuka. Kamar yadda kuma za su ci gaba da kasancewa idan ya bayyana. Amma ita bayyanar tasa za ta wajabtar da wani abu da ba wannan ba. Wato bayyanarsa za ta kwave hannuwan azulumai daga taushe muminai da suka yi. Ta kuma karve dukiyoyin da masu iko suka qwace ta mayar wa masu su da abinsu. Ba wannan kawai ba, za ta kuma kawar da azzulaman daulolin da mu ba mu iya kawarwa, sai da taimakon wannan imami na voye.

To a nan sai a tuna wa 'yan Shi'ah cewa: Kar fa ku manta, shugaban nan da kuka ce luxufi ne, shi ne wanda hankulla da al'adun rayuwa suka sheda. Wanda kuma kuka ambata da cewa duk lokacin da jama'a suke qarqashin mulkin jarumin  shugaba wanda ake tsoro, ake kuma yi wa xa'a ko ba don Allah ba. Hakan za ta sa su kasancewa mafi zama kusa da shiriya, da nesa-nesa da varna. Bayan wannan kuma kuka sharxanta kasancewarsa ma'asumi. Kuka kafa hujja da cewa, saboda da ita ne kawai shugabancin nasa zai iya tasiri. Amma kuma sai ga shi gaba xayan imaman da suka kasance kafin wannan da ake jira, babu xaya daga cikinsu da ya taka wannan rawa; babu wanda ya kasance mai qarfin iko da zartarwa daga cikinsu. To qaqa kenan? Kun ga maganar can taku ta zama sharholiya.

Tsawon kwanukan da Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi yana halifa, abubuwan da ya gudanar na halifanci da zartarwa ba su kai na waxanda suka gabace shi ba. A yayin da sauran waxanda da suka biyo bayansa daga cikin imaman naku babu wanda ya gudanar da wani abu na iko da zartarwa.

To, daxa balle shi wancan bawan Allan na voye, wanda babu ko harafi xaya na abin da ya gudanar, domin ko ganin sa ba a tava yi ba.

Yau da waxanda suka yi imani da samuwarsa, za su ji cewa, fiye da shekaru 460 kenan da ya faku, kuma saboda jin tsoro ne ba zai iya bayyana ba, balle ya gudanar da hukunce-hukunce. Kuma kodayake can fake xin ba ya da ikon bayar da wani umurni ko hani, to, za su fahimci cewa ashe saboda haka ne qunci da varna suka yi kanta a cikinsu. Kuma a qashin gaskiya haka ne; babu wani bananci a cikin wannan magana.

A kan wannan dalili ne kake ganin qungiyoyin 'yan Shi'ah sun fi kowace qungiya kasancewa cikin qunci da varna, da yawan savani ta hanyar kace-nace, da bankaura. Irin yadda kashe-kashe da savani da zaluntar juna ke gudana tsakaninsu, ko tsakanin waxanda ke qarqashin jagorancin kafirai albarka. Daxa balle waxanda ke cikin taragon musulmin direba. To idan ka dubi wannan sai ka ga wane luxufi ne waxannan mabiya na wannan "Malam-na-Lave" suka samu?

Shi dai imani da kasancewar Allah Ta'ala samamme, rayayye, mai iko a kan komai, yana kuma horo da yin xa'a gare shi tare da tanadin lada ga wanda ya yi, yana kuma hani daga savo, tare da shirin azabtar da wanda bai ji bari ba. Imani da waxannan abubuwa na daga cikin manya-manyan abubuwan da ke sa tsoron Allah da kwaxayin rahamarsa a cikin zukata. Ta yadda sanin zai kasance tafarkin samun lada da jinqayinsa. Daga nan sai ka ga an dage a kan aikata abubuwan da ya yi umurni da su, da nisantar waxanda ya hana. Za ka taras da duk wanda ya kai wannan matsayi yana samun tashin hankali a duk lokacin da ya savi Allah ko a kan kuskure ne. Saboda ya kwana da sanin cewa Allah masani ne kuma mai iko. Kuma sunnarsa ta riga ta gudana a kan saka wa masu biyayya da alheri da azabtar da waxanda suka kangare. To, ya za a kwatanta wannan sani na Ubangiji da yake da wannan xinbin fa'ida da sanin Malam-na-Boye?

Duk mutumin da aka san babu shi fiye da shekaru xari huxu, kuma bai iya azabtar da kowa ko da da baqar magana, ba ya kuma da abin da zai ba wani na lada. Hasali ma tsoron mutane yake yi, saboda haka yake fake; ba zai iya fitowa ba, balle ya bayar da wani umurni ko hani. Sanin akwai irin wannan mutum ba zai sa a aikata abin da ya yi horo da shi, ko a bar abin da ya hana ba. A maimakon haka ma sanin da ake da shi na kasancewarsa da tsoron da yake da shi, za su sa ne kawai a daxa kutsa kai cikin miyagun ayyuka. Musamman ma kasancewa an xauki tsawon lokaci ba a ji ya karrama wani ko ya gyara wa wani zama ba.

To mu qaddara ma yakan bayyana sau xaya bayan kowace shekara dari ya xan zartar da wani xanyen hukunci. Ba zai kama qafar xaya daga cikin shugabanni a fagen luxufi ba, ko da kuwa bayan kowace shekara goma ce yake bayyana, ko ma ce bayan kowace shekara xaya. Ba dai zai kama qafar

shugabannin da ke tare da jama'a kodayaushe ba a fagen amfanarwa, tattare kuwa da abin da ke tuzgowa daga gare su na zunubbai da zalunce-zulunce a wasu lokutta. Sun dai tsayar da shari'ar Allah, ta hanyar zartar da hukunce-hukunce na horo da zuba qoqari a cikin kwaxaitar da jama'arsu ga yin ayyukan xa'a, fiye da yadda wanda ba ya ko bayyana gare su daga bana sai baxi. To daxa balle wanda ya salwanta sukutum; masu hankali suka tabbatar da rashin wanzuwarsa. Waxanda ke waqen akwai shi xin ma, suna da yaqinin cewa, kasasshe ne, matsoraci; bai ma tava tavuka wani abu irin wanda xaixaikun mutane ke tavukawa ba, daxa balle irin abin da shugabanni ke yi.

To wace irin jaruntaka ce ko kwarjini irin wannan mutum ke da su, da har za a shakkarsa? Wane iko ke ga irin wannan balle har ya shimfixa hannunsa a kan mutane, ko ya zama mai taimaka masu ga kasancewa mafi zama kusa ga shiriya!

Duk wanda ya yi xan batun zuci a cikin wannan lamari, zai tabbatar cewa jahilci da girman kai da wautar waxannan mutane sun isa. Ganin irin yadda suka sakankance da kasancewar samun luxufin wannan mahaluqi na voye, tattare kuma da kasancewarsa kasasshe, kamar yadda wai za su sami luxufin nasa ko da bayyana ya yi. Kuma wai sakamakon amincewa da kasancewarsa samamme a cikin halin nasa na kasawa da tsoro, a can faken, daidai yake da kasancewarsa a fili, kuma a cikin halin maza kuta da aminci. Wai kuma tsurar ruwan zatin wannan masaniya luxufi ce a karan kanta ga wanda ya siffanta da ita, kamar sanin Allah *Subhanahu WaTa'ala*. Tirqashi wani aiki sai jahili.

**Fuska ta biyu**:

Muna son mu ji ta daga bakinku ku 'yan Shi'ah. Shin cewar da kuka yi, dole ne a samar da shugaba ma'asumi wanda zai tsare aikata waxancan abubuwa da kuka ce kalmar luxufi ta qunsa, na nufin wajibi ne ga Allah *Subhanahu WaTa'ala* Ya halicci mutum mai waxancan siffofi ya kuma tabbatar da samuwarsa. Ko ko a'a wajibi ne ga mutane su yi masa bai'a a matsayin shugaba bayan Allah Ya samar da shi?

Idan kuna nufin wajabci na farko, to qaryarku ta sha qarya. Domin kuwa Allah *Subhanahu WaTa'ala* bai halicci mai irin waxancan siffofi ba. Qul xin abin da kuke iya cewa shi ne, ai Ali *Raliyallahu Anhu* ma'asumi ne. Amma ai ko shi xin, tarihi ya tabbatar da cewa Allah *Subhanahu WaTa'ala* bai arzutta shi da wata halitta a cikin jikinsa ko rundunarsa ba, wadda za ta iya ba shi damar aikata irin waxancan abubuwa da kalmar ta luxufi ta qunsa a wurin ku.

Ku da kanku ma, kuna faxa wa duniya cewa sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* ya kasance mai rauni kuma audugar kasuwa, wanda aka zalunta a zamanin halifofi uku na kafinsa. Kuma a daidai lokacin da ya haxa runduna don xaukar fansa, sai aka sami wata runduna daban, ta yaqe shi. A qarshe ma

dai ko irin abin da waxancan halifofi uku suka gudanar na alheri, waxanda kuke xauka azzalumai, Allah bai ba shi ikon gudanarwa ba.

Ka ga kenan waxancan halifofi uku ne, suka dace da taimakon Allah har suka shimfixa waxancan alherai, irin waxanda shi Ali *Raliyallahu Anhu* ya kasa aikatawa. Kenan dai, a haka ta tabbata Allah bai halicci irin wannan ma'asumi da kuka ba shi shawarar halittawa ba.

Idan kuma kuka ce, muna nufin wajabci na biyu ne. Wato ai Allah Ya riga ya halicce shi. Muna dai cewa ne ya zama wajibi kan mutane su yi masa bai'a, su kuma taimake shi.

A nan sai mu ce maku kun ci tuwon gigi. Babu wasu mutane daga cikin mabiya ko magabta da aka samu sun yi haka. Wato babu wani daga cikin waxancan ma'asumai da kuke tutiya, wanda mutane suka mara wa baya, ko Allah Ya taimaka. Kun kuma san ba yadda za a yi waxancan nasarori na luxufi su tabbata a hannun shugaba sai tare da haxuwar hancin waxannan gudunmuwowi guda biyu. Da zarar kuwa an rasa su, to, ba magana. Don hangen dala ai, ba shi ne shiga birni ba.

**Fuska ta uku:**

Idan dai gaba xayan abubuwan da ke iya tabbatar da waccan galla ta shugabancin ma'asumi, sun kasa samuwa. Da yawa ma daga cikin sharuxxan samuwarsu sun shuxe, me zai hana mu qaddara cewa ma'asumancin ne aka rasa? Idan kuwa har ta tabbata an rasa ma'asumancin, ko dai saboda rashin cancantar shi wanda ake gani ma'asumin, da iya xaukar rawanin, ko babu ma'asumacin ma samsam. Duk dalilin da ya tabbata daga cikin waxannan dalilai biyu, xaya ne.

To a kan haka, ta yaya aka samo wajabcin halittar shugaba ma'asumi a ma'aunin hankali, a kan Allah *Subhanahu WaTa'ala*?

Kuma ko da wannan wajabci ya tabbata a kan Allah, to ai zai halicci ma'asumin ne domin ya zama sanadin kyautatuwar rayuwar al'umma duniya da lahira. Amma sai ga shi wannan ma'asumi naku, Allah ya halacce shi kasasshe, ta yadda ba zai iya tabbatar da wannan guri ba. Hasali ma varnace-varnacen da suka afku, da babu shi da ba su afku ba. Fuska ta gaba za ta qara tabbatar da wannan.

**Fuska ta huxu:**

Tabbas, ko da Allah bai halicci wannan ma'asumi naku ba, sharrin da ke gudana a bisa doron qasa ba zai wuce haka ba. Domin kuwa babu mai musun cewa samuwarsa ba ta daxa duniya da komai ba, ta fuskar raguwar sharrora. Babu wata illah qwaya xaya tal, da za a iya cewa, samuwarsa ce ta kawar da ita. Hasali ma samuwar tasa, ta sa mafi yawan al'umma sun qaryata shi, sun

qulla gaba da magoya bayansa, sun kuma wai zalunce shi da mabiyansa, kamar dai yadda kuke faxa. Kuma ma wai a kan haka ne sharroran da Allah kaxai ne ya san iyakarsu suke ta faruwa.

Harwayau, a hankalce kasancewar sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* da sauran imamai goma sha biyu da makamantansu ma'asumai, ta kasa hana abin da ya faru ya faru. Domin kuwa ai kun ce zamanin halifancin magabatansa da na waxanda suka biyo bayansa cike yake da zalunci da sharri. Kenan akwai ayar tambaya a kan ma'asumancinsu. Qoqarce-qoqarcen da su waxancan ma'asumai naku suka yi na kawar da sharri daga bisa doron qasa, abu ne da ko wanda ba ma'asumi ba yake iyawa. Ka ga kenan kasancewarsu ma'asumai, kamar yadda kuke waqantawa, ba ta haifar da alheri ba, sai sharri.

Ka ko ga hikimar Allah *Subhanahu WaTa'ala* ba za ta bari ya halicci wani abu, don tabbatar da alheri ba, amma a qarshe ya kasance bai tabbatar da shi ba, sai sharri.

To a nan 'yan Shi'ah na iya cewa, ai wannan sharri ya faru ne a sanadiyyar zaluncin da mutane suka yi wa wancan ma'asumi. Sai mu ce: Idan dai har Allah *Subhanahu WaTa'ala* a cikin hikimarsa, ya san manufar da ya halicci ma'asumin naku domin ta, wato tabbatar da alheri ba za ta tabbata ba, sai dai ma sharrin ya qara qamari, kenan babu wata hikima a cikin halittar tasa. Allah kuwa ba zai yi haka ba. Domin kuwa yin haka, kamar mutum ne ya xauki xansa ya danqa hannun wani don ya koya masa tarbiyya, alhali ya san haka ba za ta samu ba. A maimakon haka ma qara vata shi zai yi. Kai ka ga akwai mutum mai hikima da zai aikata haka?

**Fuska ta Biyar**:

Eh, gaskiya ne Allah Ta'ala ya halicci mutum da qwandar son zama cikin jama'a. Kamar yadda kuka ce. Amma cewar da kuka yi wajibi ne a samar da shugaba ma'asumi a cikin irin wannan zama, don ya hana mutane zalunci da cutar da juna, na nufin lalle ne a samar da shi a kowane gari daga cikin garuruwan duniya. To, ma'asumi nawa ake buqata kenan? Kuma har a garuruwan kafirai da mushrikkai akwai irin waxannan ma'asumai? Kenan har a Sham inda Mu'awiyah *Raliyallahu Anhu* yake akwai ma'asumi ko?

Na san ga wautarku za ku ce, kuna nufin ne akwai ma'asumi xaya a kowane babban birni. A sauran garuruwa kuma akwai waqilansa. To, tambayarmu a nan ita ce: Shin waqilan nan sun haxa gaba xayan garuruwan duniya ne, ko sashensu?

Idan kuka ce, ai akwai su a cikin gaba xayan garuruwan duniya. Mun san wannan irin fankamar da kuka saba da ita ce. Idan kuma kuka ce, a'a, a waxansu sassa ne kawai ake da su, to sai mu tambaye ku, don me haka za ta faru idan dai har cewar da kuka yi samar da ma'asumi wajibi ne a kan Allah ta tabbata? Babu dalilin da zai sa a kevance wasu garuruwa da wannan alheri, a

bar wasu. Domin kuwa ai buqatar da suke da ita da wannan ma'asumi duk xaya ce.

**Fuska ta Shida**:

Muna son mu gane, shin ita wannan martaba ta ma’asumantaka ta taqaita ne ga babban kawai, koko su ma waqilan nasa ma'asumai ne? Mun san ba za ku yi kuskuren cewa su ma ma'asumai ne ba. Domin kun san za mu jefe ku da ‘Girman kai’. Domin kuwa ai ko a cikin waqillan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* babu ma'asumi ko xaya, balle daxa daga cikin waqilan Ali *Raliyallahu Anhu* waxanda ma tarihi ya tabbatar da irin yadda suka cutar da shi, alhali waqilan Ma’awiyah *Raliyallahu Anhu* ba su cutar da shi haka nan ba. To ina zancen ma’asumanci yake a nan?

Wohoho! Na san kuna iya sake salo, ku ce, ai sharaxin ma’asumantaka a kan babban kawai yake. To, haka ba za ta raba mu da ku ba. Harwayau, idan haka ne, mene ne makomar sauran mutane da ke zaune a garuruwan da ke nesa da babban birnin da ma'asumin yake? Musamman a irin lokacin da ma'asumin ba ya iya tanqwara waqilan a sakamakon kasancewarsa kasasshe? Kenan irin waxannan mutane ba za su qaru da komai ba na gallar luxufin ma'asumin. Domin kuwa wanda ke ba su sallah, yake hunkuci tsakanin su, yake karvar dukiyoyinsu a matsayin khumisi, suke kuma tsananin biyayya gare shi ba ma'asumi ba ne.

Kuna iya cewa ai gaba xayan waxannan abubuwa waqillan na yin su ne a matsayin babban nasu. Sai mu ce: Da a ce shi wannan ma'asumi naku ya yi jaruntaka da qarfin iko kamar na Umar da Usmanu da Mu’awiyah *Raliyallahu Anhu* ba zai iya cusa imanin tsayar da adalci a cikin zukatan gaba xayan waqilansa ba, kamar yadda shi yake yi. Iyakar abin da yake iya yi shi ne ya zavi wanda yake ganin yana iya kwatanta adalaci fiye da wasu, ya naxa shi. Idan kuwa ya kasa samun kowa sai  kasasshe, kuma azzalumi, ba yadda zai yi dole shi zai naxa.

A nan ba ku da wata ta cewa, illa ku ce, idan har Allah bai halicci kowa ba sai irin waxannan rubabe-rubaben, to, ba lalle ne a kan babban ma'asumin ya nemo shi ba. Sai ya yi da abin da ya samu.

Da wannan magana taku kenan, kun yarda da cewa Allah bai halicci wani mahaluki da ke da iko a kan komai, wanda kuma ba ya kuskure ko zalunci ba. Abin da kawai Ya wajabta wa shugaba shi ne ya aikata iya abin da yake da ikon aikatawa. Kamar yadda iyakar abin da yake wajibi a kan mutane shi ne su zavi mafi zama kusa ga shiriya a matsayin shugaba, ko da kuwa akwai wata ‘yar tangarxa tare da shi ta fuskar ikon zartarwa da tsayar da adalci.

Wannan ita ce gaskiya. Domin an riwaito cewa Umar *Raliyallahu Anhu* yakan ce: “Ya Ubangiji a wurinka nake koken jaruntakar fajiri da kasawar nagari”.

Ka ji. Kowa kuwa ya san ba a tava yin wani shugaba a duniya kamar Umar ba. Domin kasancewarsa zuma; ga dafi ga zaqi. To, ya kake zaton yadda halin wanda ba shi ba zai kasance?

Sannan kuma, shi kasasshen ma'asumin, wanda aka tabbatar da babu shi, wa zai tsare kaiwa da komowa tsakaninsa da waqilansa, balle ya san halin da suke ciki? Waye zai tursasa su su yi masa xa'a? Idan daga cikin waxanda ya waqilta xin, wani ya yi laho ya nuna kamar na Allah ne shi, sai bayan da ma'asumin ya naxa shi ta bayyana shi kure ne; ya tattara dukiyar mutane ya haye ya nemi mafakar siyasa a wajen wasu sarakuna. Yaya wannan kasasshen ma'asumin zai yi da shi?

Ka ga a haka ta tabbata, komai irin qarfin ikon da ma'asumin yake da shi, ba zai iya tabbatar da abin da ake buqata na zaman jama'a ba, shi kaxai. To, ina ga wanda yake kasasshe kuma audugar kasuwa? Ga shi kuma a fake, a vace, ta yadda ba zai iya ce wa mutane uffan ba. Balle daxa a lokacin da ya karva sunan da masu hankali da ilimi suka yi masa na Malam-Babu?

**Fuska ta Bakwai**:

Rawar da ta kamata wannan ma'asumi naku ya taka, da Allah Ya sa akwai shi, ta hana masu qarfi su zalunci na qasa gare su, da qwato haqqin da suka riga suka ci na wani, da ba wa kowa haqqinsa. Duka wani yanki ne na toshe qofar zalunci, da tabbatar da adalci. Sai kuma ga shi ya kasance kasasshe kuma audugar kasuwa, ta yadda ba ya iya kare kansa daga kowane irin zalunci, qo kwato wani haqqin nasa na shugabanci ko dukiya, ko haqqin matarsa na gado. To, wanda ya kasance haka, wane irin zalunci zai iya kawarwa balle har ya sadar da wani haqqi ga mai shi? Balle daxa a irin wannan hali da aka tabbatar da rashin kasancewarsa a zahiri, yana dai can fake, ta yadda ba ya iya bayyana a wata al-qarya ko qauye don tsoron wai kada azzalumai su kashe shi. Haka yake lave fiye da shekaru 460. Alhali kuma ga duniya ta cika ta batse da fasadi da zalunci. Shi kuwa ko ya fito ya ce ga shi shi ne wane, abin ya faskara. Ka ga kenan babu yadda za a yi har abada ya iya kare faruwar wani zalunci ko ya sadar da wani haqqi ga mai shi. Kai, babu wanda ya fi su dacewa da faxar Allah Ta'ala, inda yake cewa:

﴿ أَمْ تَحْسَبُ أَنَّ أَكْثَرَهُمْ يَسْمَعُونَ أَوْ يَعْقِلُونَ ۚ إِنْ هُمْ إِلَّا كَالْأَنْعَامِ ۖ بَلْ هُمْ أَضَلُّ سَبِيلًا ﴿٤٤﴾ ﴾ الفرقان: ٤٤

*Ko kana zaton cewa, mafi yawansu suna ji, ko kuwa suna hankali"? Su ba su zama ba face dabbobin gida suke. A'a, su ne mafi vacewa ga hanya (25:44)*

**Fuska ta Takwas**:

Ku sani ya ku 'yan Shi'ah, buqatar da mutum yake da ita ta sarrafa jikinsa da ikon kansa, ta fi girma da matuqar muhimmanci bisa ga buqatar da yanayin zaman jama'a a matsayin birane suke da ita, ta samun shugaba. Amma kun ga tattare da haka Allah bai halacci ran mutum ya sa ta ma'asumiya ba. To, yaya zai zama wajibi a kansa ya halicci wani shugaba ya kuma sa shi ma'asumi?

Abin lura a wannan magana tawa shi ne, ai kun san mutum na iya fanxare wa birnin zuciyarsa ya aikata wani savo a voye. Har ya shahara da aikata wasu zalunce-zalunce da varna, amma ma'asumin da ke tare da shi bai sani ba. Ko da kuma ya sani ba yadda zai yi ya hana, tunda kasasshe ne. To, idan kuwa har Allah ya qyale shi bai yo shi, shi kansa ma'asumi ba, to, ba wata buqatar samar da wani ma'asumi don ya kula da shi.

**Fuska ta Tara**:

Tambaya ce za mu yi a nan. Shin kuna nufin samuwar waxannan imamai ma'asumai ta sa shiriya ta fi varna yawa a bayan qasa? Ta yadda kowane mutum zai kasance mafi zama kusa ga shiriyar, mafi kuma zama nesa daga varna, ta yadda da za a rasa Imaman babu mai iya maye gurabunsu? Koko a'a, kuna nufin kasancewarsu za ta kai qarshen sake faruwar wata varna? Ko akwai dai wani miqdari na shiriya da kuke nufin kasancewarsu ta samar?

Idan kuna nufin damen farko na wannan magana; wato shiriya ta rinjayi varna. To, ai wannan shi ne abin da mafi yawan shugabannin musulunci suka tabbatar a kwanukansu. Haka ta kasance a zamanin halifancin Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhum* fiye da yadda ta kasance a zamanin halifancin Ali *Raliyallahu Anhu* kamar kuma yadda ta kasance a kwanukan mulkin halifofin Umawiyyawa da Abbasiyawa, fiye da yadda ta kasance sanadiyar imamai goma sha biyu xin nan naku.

Bari ma ta zancen waxannan, yadda irin haka ta kasance a zamanin mulkin Rumawa da Turkawa da Indiyawa ta fi yadda ta kasance da kasancewar Malam-na-Voye wanda kuke yi wa laqabi da *Sahibuz-zamani.* Kuma dama yadda matsalar take ai, babu wani shugaba da za a naxa, daga baya a qaddara gushewarsa ba tare da mamayi ba, face varnar da za ta faru a lokacin da aka qaddara gushewar tasa, ta fi wadda ka iya faruwa idan yana nan. Amma kuma duk da haka abu ne mai sauqi wani shugaba ko mutum ya fi shi kasancewa shiryayye. Kamar yadda ake jin an ce, shekara sittin qarqashin fajirin shugaba ta fi alheri bisa ga dare xaya ba shugaba.

Idan kuma kuka ce, a'a muna nufin dame na biyu na maganar, wato samuwar shiriya ta har abada tsintsa; wadda ba varna tare da ita. Sai mu ce maku: Har abada haka ba za ta samu ba, domin Allah bai shirya haka ba. Kuma ko kokwanto babu a kan cewa bai halicci dalilan da ke iya tabbatar da samuwar

haka ba. Duk kuwa wanda ke jin wajabcin kasancewar haka, har ya wajabta samar da hanyoyin samuwar haka a kan Allah, lalle ne ko dai yana yaudarar kansa ne, ko kuma ya rena Allah Ubangijinsa. Domin kasancewar Allah Ya halicci abin da ke iya taimakawa ga samuwar haka, ba za ta samar da hakan ba, idan bai halicci abin da lalle sai da shi ne hakan ke iya kasancewa ba.

Wannan magana ma taku, ku sani ta taqaita a kan ayyukan bayi ne na al'ada. Abin duk da kuwa ya shafi zancen ma'asumanci, to, sai hattara. Domin kuwa ba shi ne ke da ikon samar wa kansa ganbun tsari da ikon da ke tare da shi ba. Wannan sai Allah. Kai 'yan Shi'ah daga cikin Mu'utizilawa ma na jin hakan ta sha qarfin ikon Allah.

To, wajabta wa Allah *Subhanahu WaTa'ala* halitta wani mutum wai shi ma'asumi wanda zai shafe savo daga doron qasa kwata-kwata, ya fi zama varna a kan wajabta masa halittar kyawawan ayyukan bayi gaba xaya.

**Fuskar ta goma:**

Yanzu kuma za mu koma ga cewar da xan Shi'ar ya yi wai, da kuwa shugaban al'umma bai kasance ma'asumi ba, da hakan ta sa ta buqatuwa ga samun wani shugaban ba shi ba. Domin kuwa kuskuren da ke da yiwuwar faruwa a cikin al'umar ne, dalilin da ya sa ake da buqatar irin wannan shugaba. To, idan kuwa har shi ma akwai yiwuwar ya yi kuskure, to, sai a buqaci wani shugaba ba shi ba, don da shi da su ba a san gwani ba.

**Martani:**

Me zai hana ku yarda da kasancewar wasu mutane a cikin al'ummar, waxanda za su riqa faxakar da shugaban a duk lokacin da ya saki hanya bisa kuskure? Ta yadda ba za ta yiwu gaba xayan xaixaikun al'ummar su haxu a kan kuskuren ba. Wato ya kasance a duk lokacin da wani sashe na jama'a ya yi kuskure, sai shugaba ko mataimakinsa ya faxakar da su. A lokaci xaya kuma idan shi shugaban ne ya yi kuskuren, ko mataimakin can nasa, sai a sami wasu mutane su faxakar da shi. A haka sai suturar ma'asumancin ta tabbata a jikin gaba xayan al'ummar har da shugaban, ba a jikin kowane daga cikinta a xaixaice ba. Kamar yadda Ahlus-Sunnah ke cewa.

Kamar yadda hukuncin yake a cikin xaixaikun masu bayar da wani labari mutawatiri, wato kasancewa tana yiwuwa ga kowane xaya daga cikinsu ya yi kuskure a matsayinsa na tilo. Ko ma ya qiri qarya da gangan. Amma a lokacin da suka haxu wasu-wasu a kan labari xaya, al'ada ba ta yarda da yiwuwar su haxa baki a kan qarya ba. Kamar yadda abin yake a cikin sha'anin ganin jinjirin wata ko wasu qananan abubuwa. Wanda tana yiwuwa ga mutum xaya wani abu ya qyafta masa ya faxi savanin abin da yake shi ne gaskiya. Amma idan taron jama'a ya cure, hakan kan wuyata.

Haka wannan lamari yake a cikin nazarin lissafi da zane-zane. Tana yiwuwa qwarai, mutum xaya ya kasa tantance matsala xaya ko biyu a wannan fage. Amma a yayin da ma'anbuta ilimi suka haxu a zauren qara wa juna sani, suka yi wa matsalar taron dangi, yana da wuya a al'adance su kasa tantance mas'alolin kamar yadda suke asalatan

Kuma ma ai sanannen abu ne cewa, rigar ma'asumantaka ta fi dacewa da wuyan taron jama'ar da bakinsu ya haxu a kan kalima xaya. Saboda hakan ya fi zama kusa ga abin da hankali da duniya ke karva, fiye da wuyan mutum xaya. Idan kuwa har rigar ta qi shiga wuyan irin wannan taro da suka haxu a kan wani ayyanannen abu guda xaya, to bai ko kamata a iske ko sunsunar wuyan mutum xaya, wanda ya kevanta da wani abu ta yi ba. Idan kuma har ta kuskura ta shiga wuyansa har ta zauna, to lalle ne kuwa ba makawa, a iske ta daxe da zaunawa wuyan irin wancen taro har ta yi annakiya saboda jimawa; ana batun tuve ta a wanke.

Kuma idan ka duba da kyau, za ka ga hakan ta tabbatar da fin cancantar wuyan taron jama'a da rigar can ta ma'asumanci a kan wuyan tilo. Kuma hakan ya haxa har da shi shugaban, don xaya ne shi daga cikin jama'ar. Illa dai kawai ya kasa zama gudagudan ma'asumi: Wahadahu la sharika lahu. Ka ga ta haka an huta.

Amma saboda jahilcin da ya yi wa 'yan Shi'ah kanta, sai suka wajabtar da kasancewar xaya daga cikin musulmi ma'asumi. A lokaci xaya kuma suka yardar wa gaba xayan ragowar musulmi yiwuwar faxawa a cikin kuskure, matuqar babu wani ma'asumi xaya tare da su. Amma ka ga a fahimta ta hankali, duk lokacin da kan malamai da yawa ya haxu a kan wani zance xaya, to, ya fi kasancewa mafi kusa ga zama daidai, bisa abin da wani malami tilo yake a kai can gefe. Wannan kuwa ko da savanin da ke tsakanin malaman a waxansu mas'aloli ya wuce misali. Domin kuwa idan dai ana iya kama maganar wani tilo ta zama ilimi, to kuwa maganar taron jama'a ta fi cancanta da zama haka.

Wani abin da zai qara tabbatar maka da haka shi ne, ai shugaba abokin tarayyar mutane ne a cikin gaba xayan aikinsa wanda ya shafe su, domin kuwa shi kaxai ba ya iya gudanar da wannan hidima, sai idan sun tallafa masa. Misali, ai ka ga idan ba su ba shi haxin kai ba, ba ta yadda za a yi ya iya zartar da hukunce-hukunce, ko ya tabbatar da cikar mudun haqqoqa. Ba zai iya karo da abokan gaba ba, sai da sa hannunsu. Kai, ko sallar juma'a da ta jam'i sai idan sun yarda sun bi shi, sannan zai samun ladarsu. Haka kuma ba zai karva sunan shugaba ba, sai idan sun yarda sun aikata abin da ya umurce su da aikatawa.

**Fuska ta Goma Sha Xaya**:

Ya kamata ‘yan Shi’ah su kwantar da hankali su sani ilimi a addinin musulunci kashi biyu yake. Babu wani abu daga cikin abubuwan da shugabanni ko sauran al’umma ke buqata na ilimi da ya fita daga cikin waxannan nau’o’a biyu: Nau’i’ na farko shi ne, ilimi gamagari, wanda ya haxa da sanin wajabcin salloli biyar, da azumin watan Ramalana da zakka da hajji, da haramcin giya, da zina da sata, da makamantansu. Nau’i na biyu kuma shi ne, kevantaccen ilimi, ko kuma ka ce, Rava-darni. Wanda ya haxa da, gane zakka ta wajaba a kan kaza ko tsayar da haddi kaza ya wajaba a kan wanda ya aikata laifi kaza, da matara kama da wannan.

Shi Nau’i na farko, shari’a ta hutar da kowa ta vangarensa. Ba ta da buqata da wani shugaba ya tsoma baki a ciki. Domin kuwa babu wani jijjige ko jigo na shari’a wanda yake wajibi ga samuwa face ka taras Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi bayaninsu filla-filla a nassance. Ko kuma ya bar wata ‘yar kafa a jikin waxanda ke da buqatar fahimtar malamai a ciki (Qiyasi). To, idan suna magana ne a kan ilimin da muka faxa kashi na farko, to, gayya ta gama aiki a nan. Idan kuwa na biyun ne suke magana, to ba sauran wahayi dangane da shi sai dai qiyasi.

Idan kuma har kuka yi qarfin halin cewa, ai akwai waxansu abubuwa da Manzon ya bari, waxanda nassi da qiyasi ba za su iya bayyanawa ba, sai ma'asumi ya sa baki. Kenan kuna son ne ku ce, ma'asumanci rabin Annabta ne! Ah, haka kuke nufi mana. Idan dai har ma'asumin naku na iya wajabta wani abu ko ya haramta wani, ba tare da ya kafa hujja da wata magana ta Annabi ba, ya zama mai cin gashin kansa kenan, ba mabiyi ga Annabin ba. Duk wanda ya kasance haka kuwa, to shi ma ya zama Annabi kenan. Amma duk wanda ya yarda da wani a matsayin halifan Annabi, to lalle kuwa ba zai raba gari da shi ba.

Haka kuma qiyasi, idan har ya tabbata hujja, to, dole ne a mayar da mutane zuwa gare shi. Idan kuwa bai tabbata hujja ba, to, lalle ne kuwa a tarar cewa Annabi ya riga ya yi cikakken bayani da nassi a kan jigoginsa.

Ko banza Allah Ta’ala ya riga ya faxa mana cewa:

﴿ٱلۡيَوۡمَ أَكۡمَلۡتُ لَكُمۡ دِينَكُمۡ وَأَتۡمَمۡتُ عَلَيۡكُمۡ نِعۡمَتِي وَرَضِيتُ لَكُمُ ٱلۡإِسۡلَٰمَ دِينٗا ﴾

المائدة: ٣

> *A yau Na kammala muku addininku, kuma na cika ni’imata a kanku, kuma Na yarda da musulunci ya zama addini a gare ku (5:3)*

Ka ga wannan aya nassi ce, da ke nuna cewa addini ya riga ya gama cika. Ta yadda ba ya buqatar wata tsalma daga kowa.

Amma qananan abubuwa, ba ta yiwuwa ya kasance an daddale hukunce-hukuncesu filla-filla. Dole ne a bari ijtihadi ya yi aiki a cikinsu. Ta

yadda malamai za su tantance wa kowane musulmi fuskar da zai kalla don ya dace da alqibla idan zai yi sallah, su kuma shata wa kowane alqali sifofin da ake buqata ga shedu, gwargwadon yanayin zamantakewar jama'a. Ba ta yiwuwa nassi ya qayyade irin waxannan abubuwa da makamantansu.

Tunda kuwa har haka ne, da zarar kuka yi iqirarin ma'asumancin wani shugaba a cikin irin waxannan qananan hukunce-hukunce, to, jahilcinku da girman kanku sun bayyana. Domin kuwa babu wanda ya tava iqirarin haka. Kuma ko a cikin waxanda Ali *Raliyallahu Anhu* ya naxa a matsayin wakilansa a waxansu yankuna, akwai waxanda yake da yaqinin mazanbata ne kuma kasasshi, ko suna da wasu ayubba na daban. Kuma shi kanshi akwai lokacin da ya yanke hannun wani, yana mai dogara a kan shedar da wasu mutane biyu suka bayar a kansa. Daga baya kuma ya gane ya yi kuskure har ya ce: "Mun yi kuskure a cikin wannan hukunci kuma da na san ba bisa gaskiya kuka yi wannan sheda ba, da na sa an yanke hannayenku".

Kai! Ko Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba ya jin shi ma'asumi ne a cikin irin waxannan hukunce-hukunce. Domin kuwa ya zo a cikin littafin Buhari da na Muslimu cewa ya ce: "Haqiqa kun kasance kuna kawo qara gare ni. Tana kuma yiwuwa sashenku ya kasance mafi iya salon magana a kan wani sashe. To, ku iya sani fa ina hukunci ne dabra da abin da na ji. Duk wanda na ba haqqin xan'uwansa kar ya karve shi. Domin kamar na yanka masa wani yanki ne na wuta.

**Fuska ta goma Sha biyu**:

Muna so ne mu gane, shin wannan ma'asumanci da kuke waqe, kuke kuma jin ya tabbata ga shugaban naku, kuna nufin shi ne ke da ikon zavar ayyukan xa'a ya aikata, ya kuma nisanci na savo a ra'ayi da ikon kansa? Tattare kuma da kasancewar, ku a wurinku ba Allah ne Ya halicci ikon yi ko bari, a cikin ran ma'asumin ba? Koko kuna nufin kuma dai Allah Ya halicci iradar yin haka ne a cikinsa, ta hanyar zare ikon aikata savo daga cikin ransa?

Idan kuka ce kuna nufin maganar farkon ne, alhali kuwa ba ku yi imani da cewa Allah shi ne wanda ya halicci ikon yi ko bari a cikin kowane xan Adam ba. Kenan a cikin haqiqanin manufarku, Allah ba Ya iya halitta ma'asumi.

Idan kuma kuna nufin magana ta biyu ne, to, farkon abin da kuke tutiya na cikakken iko ga ma'asumin, a kan aikata abin da duk ya ga dama, ya roshe.

Da kuma za ku dawo ku ce, a'a muna dai nufin Allah Ya zare ikon aikata savo ne daga cikin halittar ma'asumin, to, kenan wannan ma'asumi naku na da wata halitta a cikin jikinsa ta kasawa. Kamar yadda duk yadda makaho ya so ba zai iya saka xigagga ga baqaqen qur'ani ba, daidai da irin duk yadda gurgu ya so tafiya, ba zai iya ko sawu xaya ba.

Shi ko a hankalce, duk wanda ba ya iya aikata wani abu ko barin aikata shi, to ya yi kaxan ga a hore shi da aikata abin, ko barin shi. Idan kuwa har hakan ta tabbata a kansa, kenan bai cancanci lada akan duk wata biyayya da zai yi ba, domin babu wanda ya sa shi. Kenan ma'asumi a wurinku ba ya samun ladar komai a kan nisantar ayyukan ashsha, ko aikata na madalla. Babu kuwa tavewa ko naqasar da ta kai ga wannan.

A kan haka, kenan ko farar hula daga cikin musulmi, wato musulmi hannu biyu ya fi wannan ma'asumi naku daraja a wurin Allah. Domin shi da zarar ya aikata wani laifi ya tuba, an yafe masa. Kai za a ma maye masa gurbin kowane zunubi daga cikin waxancan zunubai da suka gabata, da lada. Ka ga kenan ko a wurin waxannan 'yan Shi'ah, sakamakon da musulmi falan xaya, zai samu ya fi alheri a kan zama ma'asumi. Wannan kuwa yana walwale waxancan maganganu nasu, matuqar walwaluwa.

Idan kuma muka dawo ga matashinyarsu ta biyu, muka qaddara wajabcin samar da shugaba ma'asumi. To, hakan ba ta hukuntar da kasancewar Ali *Raliyallahu Anhu* ma'asumi shi kaxai tallintal, bisa ittifaqi. Domin kuwa da yawa daga cikin ma'abuta ibada, da sufaye, da sojoji, da farar hula daga cikinsu, nada imanin cewa akwai ma'asumai da yawa a cikin shehunansu. Kamar yadda 'yan Shi'ah ke da imanin haka a cikin imamai goma sha biyu. Da yawa ma sukan yi masu inkiya da kalmar *Ash-Shaikhul-Mahfuz,* tsararren malami kenan.

To, idan kuwa har za su yi irin wannan imani a kan shehunansu, tattare da imanin da suke da shi a kan cewa darajar Sahabbai ta fi ta shehunan, to kuwa halifofin can sun fi cancanta da wannan imani na ma'asunanci, ya kasance a kansu.

Kuma ka ga irin wannan wuce wuri na 'yan Shi'ah a cikin xaukaka darajar imamansu, ya watsu qwarai a cikin wasu qungiyoyin mutane. Ta yadda za ka taras suna wuce iyaka a cikin ciccivawa da kambama shehunansu.

Misalin wannan shi ne Shi'ah *Isma'iliyyah.* Su ma sun yi imani da cewa shugabanninsu ma'asumai ne, kuma su ba 'yan-sha-biyu ne ba. Ba waxannan kawai ba har ma da yawa daga cikin talakawan sarakunan Umawiyyawa, ko ma mafi yawansu suna da imanin cewa ba za a yi wa shugaba hisabi ba balle azaba ranar lahira. Kuma wai talakawa ma Allah ba zai kama su da laifin komi ba, matuqar dai hakan ta kasance ne a bisa tafarkin yin xa'a ga shugaban. Kai suna jin wajibi ne a kansu, su yi xa'a ga shugabansu a kan komai. Kuma wai Allah ne Ya umurce su da hakan.

An riwaito cewa, Yazidu xan Abdulmalik ya so ya bi sawun Umaru xan Abdulaziz a cikin mulkinsa. Sai qungiyar wasu shaihunan zamaninsa suka same shi. Suka rantse masa da Allah, wanda ba wani Ubangiji sai shi a kan

cewa, da zarar Allah Ya naxa mutum ya zama shugaban jama'a, to kuwa zai karvi ayyukansa kyawawa ya yafe masa munana.

Hakan ta sa kake jin maganganun mafiya yawa daga cikin manyan mutanen waxannan za munna, cike da umurni da yin xa'a ga shugaba ba tare da wata togiya ba. Har sukan qarfafa zantukan nasu da cewa, duk wanda ya yi xa'a ga shugaba ya yi wa Allah ne. Wannan ne ma dalilin da ya sa idan mutane za su kwatanta biyayyar wani sai ka ji an ce, kamar xan garin Sham.

Ka ko ga ai mutanen Sham jama'ar Mu'awiyah ne, ba 'yan Shi'ar Ali ne ba.

Babu wata qungiya daga cikin irin waxannan qungiyoyi da za a ce wa, dole ne su samar da wani shugaba ma'sumi, face sun karva da cewa, wannan shugaba da muke biyayya gare shi ya wadatar da mu. Ba mu da buqata da wani ma'asumi daga cikin imamai goma sha biyu, ko da kuwa Aliyu.

Idan kuma kuka ce, ai ba a la'akari da mutanen Sham domin su kangararru ne. To, sai mu ce maku: Ai waxannan mutane sun fi ku, daga ku 'yan-sha-biyu ko har *Isma'iliyyah*wa. Domin kuwa shugabanni da shehunansu sun fi alheri, bisa ga wannan ma'asumi na fake wanda babu shi ma sam-sam-sam, babu kuma wani amfani da ya ke yi wa jama'a, ta kowane hali. Matsayinsu duk yadda yake ya fi naku.

Wasu 'yan Shi'ah na kafa hujja da cewa Ali *Raliyallahu Anhu* ma'asumi ne wai don shi kaxai ne daga cikin halifofi aka samu waxanda suka raya cewa ma'asumi ne. Sai mu ce: To, wa ya raya hakan in ba ku ba. A cikin Sahabbai babu wanda ya yi wannan iqirari ga Abubakar da Umar da Usmanu ballantana Ali.

A taqaice dai, duk lokacin da 'yan Shi'ah suka buxa baki suna raya cewa, imamansu ma'asumai ne, to, za ka tarar da akwai wasu su ma masu irin wannan da'awar a kan wasu mutane daban ba imaman Shi'ah ba. Ka ga kenan an rosa wannan tugufar ta 'yan Shi'ah ta cewa su kaxai suke irin wannan da'awa. A lokaci xaya kuma an kai qarshen ruxun da suke kawowa a kan ma'asumancin Ali da zuri'arsa.

**Fuska ta goma sha uku**:

Dole ne ko dai samuwar shugaba ma'asumi a kowane zamani ta zama wajibi ko kuma ba wajibi ba. Idan ba ta zama wajibi ba to, iqirarin 'yan Shi'ah ya bi shanun sarki. Idan kuwa har a kan qaddarawa hakan ta wajaba, to mun yarda. Amma ba mu amince da kasancewar Ali shi kaxai ma'asumi ba, ba tare da waxancan halifofi uku ba na kafinsa ba. Kai kasancewar wannan qaddarawa ma gaskiya, na wajabtar da kasancewar Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhu* ma'asumai, ba da shi ba. Dalili kuwa shi ne haxuwar kan gaba xayan Ahlun-Sunah a kan fifikon Abubakar xin da Umar a kan Ali, a

fagen daraja, da kasancewar su mafiya cancanta da zama ma'asumai – in har dole ne – a kan sa. Kuma a wurinsu, idan har ma'asumanci abu ne mai yiwuwa, to zai fi kusa ga halifofin uku na kafin Ali. Idan kuwa har ba abu ne mai yiwuwa ba, to rashin yiwuwarsa gare shi ta fi dacewa.

Kuma ku sani, miqa wuya da muka yi ga koruwar ma'asumanci daga waxancan halifofi uku, mun yi shi ne saboda imanin da muke da shi a kan cewa Allah Ta'ala bai halicci wani shugaba ma'asumi ba. Da kuwa za mu qaddara yiwuwar haka, to da lalle ko waxancen halifofin uku sun fi duk wanda ya zo bayansu cancanta da ita. Kuma wannan dalili ne ya sa muka kore ma'asumancinsu.

Wai ina ma 'yan Shi'ah suka samo wannan magana ta cewa Ali ma'asumi ne? Suna iya ce mana, ai haxuwar kan malamansu ne ta tabbatar da ma'asumancin Ali. To, a nan sai mu ce musu: Kasancewar ijma'i ba hujja ba a wurinku, ta rosa wannan hujja taku. Idan kuwa har kun yarda da kasancewarsa hujja a kan wannan matsala ta ma'asumancin Ali, a matsayinta na kanwa uwar gami a cikin gaba xayan matsalolin, to, kenan idan wasu malamai suka haxu a kan kansancewar wanda ya tsare alfarmar shari'a kuma ya yaxa ta ma'asumi, haxuwar tasu ta zama hujja kenan . Amma abin da zai ba ka mamaki shi ne, 'yan Shi'ah na kafa hujja ne da ijma'i a wannan matsala kawai. Amma a wurinsu ijma'i ba hujja ba ne. To idan kuwa har haka ne, sai sun gaya mana inda suka samo wannan magana ta kasancewar Ali ma'asumi, shi kaxai daga cikin halifofi.

Idan kuma har suka ce, a'a ai ma'asumancin nasa ya samo asali ne daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ta hanya mutawatira. To, sai mu gaya masu cewa, wannan magana daidai take da cewar da suka yi shugabancin Ali bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kai tsaye, abu ne da Annabin *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya nassanta kuma aka riwaito ta mutawatirar hanya. Kenan ba su da wata madogara a cikin matsalolin biyu baya ga wannan.

## Martani na Huxu:

Kar fa 'yan Shi'ah su manta, ijma'i a wurinsu ba hujja ne ba sai idan akwai wani ma'asumi a ciki. To, idan suka riqe shi hujja a kan tabbatar da ma'asumancin ma'asumi, hakan ta haifar da kwan-gaba-kwan-baya kenan. Watau ma'asumancin ma'asumi ba zai tabbata ba sai da yawun bakinsa. Kuma yawun bakin nasa ba zai iya zama hujja ba, sai idan an tabbatar da ma'asumancinsa. Ka ga kenan babu abin da ke iya tabbata daga cikin biyun.

A haka, kowa ya gane hujjar da 'yan Shi'ah ke qoqarin kafawa a kan ma'asumancin wani busar kura ce. Kuma ba su da wata hujja ko madogara ta ilimi a kan duk abin da suka faxa. Tattare da wannan rashin makama da ya yi masu tarnaqi, za su ce mana: Ai sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* ne da kansa ya

ce: "Ni ma'asumi ne kuma duk wanda ba ni ba, ba ma'asumi ba ne". Da za su ce mana haka a lokacin da muka nemi su faxa mana inda suka samo wannan wariya. Sai mu gaya masu cewa, ai ko wannan qarya da suka yi wa Ali xin, ba ta iya zama hujja yankakka. Domin kuwa magana ce, sallatatta da kowa ma ke iya bugun qirji ya faxa.

Haka kuma da za a qaddara tabbatuwar duniya da buqatar shugaba ma'asumi, to sai kuma a fantsama cikin kogin neman tantance shi. Da kuma a kan wannan tafarki za mu yi kicivis da xan Shi'ah Ba'isma'ile, mu nemi ya faxa mana ko waye ma'asuminsa, da kuma dalilin da ya sa yake ganin babu wani ma'asumi bayansa. Ina tabbatar maka babu wata hujja da zai iya tabbatarwa gamsassa a kan haka. Qarshenta zai shiga tubka da walwala ne, yana turmurza hancin kansa da kansa. Haka qarshen shi ma xan sha biyu zai kasance. Don ko dama walkin aro ne ke gindinsu wanda suka aro daga wurin Qadariyyawa, na imani da wajabcin riqo da mafi ingancin abu a cikin komai.

A kan wannan zance ne 'yan Shi'ah suke gina aqidar wajabcin samar da shugaba ma'asumi. Da wannan zance nasu kuwa da na waxancan duk shirme ne. Domin da su ma za a tage su a ce sai sun kawo hujja karvavva a kan haka, za su kama 'yan soshe-soshe ne. Domin kuwa asalatan hujjarsu ba ta wuce kawai, zancen wanda ma'asumancinsa bai tabbata ba, wanda suka ce ya ce: Shi ma'asumi ne.

Da kuma 'yan Shi'ah za su kutso nan su ce, to, idan har hankali ya tabbatar da buqatar samar da shugaba ma'asumi, ko bisa qaddarawa ne. Kuma aka sami cewa Ali *Raliyallahu Anhu* ya furta da bakinsa ya ce: "Ni ma'asumi ne". To babu abin da zai hana a sakar masa zama hakan, don babu wani da ya yi iqirarin haka in ba shi ba.

To, sai mu ce masu: Wannan ba ta fisshe ku. Domin kuwa ko an qaddara samuwar ma'asumi a duniya tabbas. To, ba za a rufe ido a karvi zancen wani don kawai ya yi qarfin halin cewa: "Ai ni ne ma'asumin" ba. Don tana yiwuwa ya kasance wani na can ma'asumin na gaskiya ba shi ba. Ko da kuwa ba wanda ya ji shi yana kururuta cewa shi ma'asumi ne. Domin kuwa yana yiwuwa ya rufa ma kansa asiri, ya qi bayyana ma'asumancinsa. Kamar yadda 'yan Shi'ah suka yardar wa Malam-na-Voye cewa ya rufa wa kansa asiri, ya fake don tsoron azzalumai.

To, duk da ma hakan akwai buqatar a tabbatar da cewa shi Ali *Raliyallahu Anhu* ya saka wa kansa rigar ma'asumantaka, kafin a yarda da hakan, ko da an daure an qaddara yiwuwarsa. Allah kuwa Ya tsare Ali, don tabbas bai ce haka ba.

### Ga Kuma Amsa ta Biyar

Idan har 'yan-sha-biyu ba su da wata hujja a kan wannan matsala ta ma'asumanci sai zancen da suka cirato daga ma'asumin. To, mun ji mun karvi

zancen nasa, a cikin wannan matsala. Amma ba za mu kammala karvar zancen ba don mun yi imani da cewa babu wani mahaluki a duniyar nan da zai iya cirato zancen daga gare shi, ta hanya mutawatira, a yayin da muke da dubun-dubatar riwayoyi daga gare shi, waxanda ke tabbatar mana da cewa bai tava qudurta shi ma'asumi ne ba.

**Amsa ta Shida**

Damar da shi Alin ya ba wa alqalansa ta su yi hukunci da abin da ya sava wa ra'ayinsa, na tabbatar da cewa, ba ya ji a ransa ko masoso cewa shi ma'asumi ne. Ta tabbata da isnadi ingantacce cewa, Ali *Raliyallahu Anhu* ya tava cewa: "Ra'ayina ya yi daidai da ra'ayin Umar a kan kada a sayar da waxanda suka haifi 'ya'ya maza daga cikin kuyangi a da. Amma yanzu ina ganin ana iya sayar da su". Nan take sai wani alqali daga cikin alqalansa, wanda ake kira Abidatus Salmani ya ce: "Ra'ayin can naka da ya yi daidai da na Umar, a matsayinku na jama'a ya fi soyuwa gare mu bisa wannan ra'ayin naka a matsayinka na tilo".

Haka kuma alqali Shuraihu ya kasance yana hukunci da ijtihadinsa, ba tare da ya shawarci Alin ba, ko neman tabbatarwarsa. Kuma Alin bai tava walwale hukuncin da ya yi ba. Hasali ma abin da yakan ce masu shi ne, ku yi hukunci kamar yadda kuka saba yi. Kuma ma da yawa shi kansa ya kan yi wata fatawa ko hukunci, ya kuma dawo ya walwale wannan ijtihadi da ya yi, da wani ijtihadin daban. Kamar dai yadda hakan kan faru ga takwarorinsa Sahabbai. Kuma waxannan, zantuka da muka riwaito daga gare shi, da isnadai ingantattu suna nan jibge.

## 3.1 Wai Allah ne ya Naxa Ali!

Xan Shi'ar ya ce: Fuska ta biyu, lalle wajibi ne ya kasance akwai nassi a kan duk wanda zai zama shugaba (Imami) saboda mun riga mun tabbatar da cewa, ba zai yiwu a bar mutane da zaven ba. Kuma saboda duk wanda za su zava da kansu ba zai fi wani na daban ba. Kuma zaven nasu yakan iya haifar da yamutsi da tashin hankali da fitinu waxanda suka fi girma. Kuma babu wani daga cikin shugabannin wannan al'umma wanda shugabancinsa ya tabbata a nassance, sai fa Ali. Kuma kan malamai ya haxu a kan haka. Kenan shi ne kawai wanda shugabancinsa ya inganta.

### Martani:

Gaba xayan waxannan zantuka, na farko da na biyu shirme ne. Amma jayayyar da ake da ita ta fi qamari a kan zance na biyu, wato cewa, an yi ij'ma'i a kan nassancin shugabancin Ali kawai. Domin kuwa akwai qungiyoyin mutane da dama, daga cikin magabata da waxanda suka rufa masu baya, daga cikin

masana Hadisi da Furu'a da Falsafa, da suka tafi a kan cewa akwai nassi a kan shugabancin Abubakar *Raliyallahu Anhu*. Akwai kuma wata qungiya ta 'yan Shi'ah da suka tafi a kan cewa akwai nassi a kan Abbas.

Ka ga kenan cewar da ya yi, an yi ijma'i a kan Ali, qarya ce da ximinta. Shi kuwa wannan xan Shi'ah, marubucin wannan littafi, duk da yake yana daga cikin fitattun 'ya'yan qungiyar tasa to, ko shakka babu gaba xayansu jahilai ne. Idan ba haka ba, kai ka san ba ta yiwuwa ga wanda ke da isasshen ilimi a kan zantukan malamai ya yi iqirarin haxuwar kansu a kan irin wannan xanyar magana.!

Wata fuska ta martani kuma ita ce: Gaba xayan wannan kaiwa da komowa da muke ta yi da ku, ba ya wuce neman yarda da kasancewar nassi a kan shugabancin wani ko qin yarda da shi. To, idan har muka yarda da kasancewarsa, a matsayinmu na Ahlus-Sunnah, abin da kuke cewa a cikin dame na biyu na wannan magana ya faxi; wato cewarku nassi ya kasance ne a kan Ali. Don ko mun riga mun turmuje ku da hujja, don mun tabbatar maku da akwai masu cewa akwai nassi a kan Abubakar. Idan kuwa muka qi yarda tun farko da akwai nassin, kenan wajabcin samun nassi a kan shugabancin wani ya faxi, domin babu mu a cikin ijma'in.

Sanannen abu ne cewa, ijma'i a wurinku ba hujja ba ne, zancen ma'asumi shi ne hujja. Kenan sai an koma an lalabo zancen wanda ake iqirarin ma'asumancinsa kafin a iya tabbatar da ingancin nassin ko ma samuwarsa. Ka ga kenan a qarshe da nassin da ma'asumancin babu wanda zai tabbata. Balle zancen wani da zai ce: "Ai Ni ne ma'asumin da ake nufi, ni ne kuma wanda nassi ya tabbatar da shugabancinsa" ya zama hujja. To, ai ba a gama gane ingancin zancen nasa ba. Ka ko ga ko shakka babu irin wannan ruxu da kwan-gaba-kwan-baya, kai matuqa ne a fagen jahilci.

Harwayau dai akwai tambaya a nan, shin cewar can da kuka yi, dole ne ya kasance akwai nassi a kan shugabancin duk wanda za a shugabantar, shin kuna nufin ne, dole ne ya kasance an samu nassin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya faxa qarara a cinkinsa cewa: "Wane ga shi, shi ne halifa idan na wuce. Saboda haka ku saurare shi, ku yi masa xa'a" shi kenan kuma ya tabbata halifan da haka? Koko hakan ba ta isa, sai jama'a sun taru sun naxa shi?

Idan kuka ce, kuna nufin sharaxi na farko. To, sai mu amsa maku da cewa, mu kan ba mu yarda da wajabcin samun nassi a cikin irin wannan siga ba. Haka ma ra'ayin Zaidiyya ya yi daidai da na jama'a a kan rashin yarda da irin wannan nassi. Kun kuma san Zaidiyyar nan wani reshe ne a Shi'ah. Kuma ba ku xauki suna da wata matsala da Ali ba balle ku tuhumce su.

Haka ita kuwa cewar da xan Shi'ar ya yi wai: Saboda rashin nassi a kan shugabancin wanda ya kamata ya zama shugaba ne, aka samu jayayya da tajin-

tajin. To, a nan sai mu ce: Ai, ko da mun qaddara samuwar nassi ko nassosa a kan wanda ya cancanci shugabanci, aka kuma bi diddigin waxannan nassosa aka tabbatar da ba su da sankara, don qarfin hujja da dalilinsu ya isa ko ina. To, hakan ba za ta hana jayayya da tajin-tajin ba. Domin kuwa ko a cikin hukunce-hukunce hakan kan faru. Hakan kuwa kan kasance ne saboda ba kowaxanne hukunce-hukunce ne aka samu bayaninsu filla-filla a nassance ba, ta yadda da soja da farar hula daga cikin al'umma kowa na iya fahimtarsu.

To, idan kuwa har irin waxannan nassosa na iya wadatarwa a cikin abin da ya shafi manya-manyan al'amurra, waxanda sanin su ya ke wajaba a kowane zamani, to kuwa wadatuwa da su a cikin qananan al'amurra, irin naxin wani shugaba tantantacce ya fi cancanta. Dama kuma mun riga mun bayyana maku a baya kaxan cewa, abu ne mai sauqi Annabawa su furta nassosa a kan hukunce-hukuncen manyan abubuwa savanin qanana.

To, kuma harwayau da waxancan nassosa za su taho da bayyanin dalilai a kan kasancewar wani sashe daga cikin jama'a, mafiya cancanta da shugabanci fiye da wasu, to sai a wadatu da hakan, a fita batun naxa wancan a matsayin halifa.

Kuma ai ka ga, dalilan da suka tabbatar da kasancewar Abubakar *Raliyallahu Anhu* mafi cancanta da shugabancin, bayyanannu ne. Babu kuma wani Sahabi da aka samu ya ja tsawo a kan haka. Ko waxanda suka yi 'yar tankiya a cikin wannan sha'ani daga cikin Ansaru, ba sun yi haka ne, saboda suna musun kasancewar shi Abubakar *Raliyallahu Anhu* mafifici daga cikin Sahabbai Muhajiruna ba. Shi wanda ya wakilce su a cikin wannan tankiya ya nemi a naxa halifofi biyu ne; xaya daga cikin Ansaru xaya daga cikin Muhajiruna.

Da wani daga cikin dakarun 'yan Shi'ah zai yi qarfin halin murza gashin baki ya ce mana, ai da Ansaru na da iko da sun hana wancan shiri na naxa halifa xaya kuma daga cikin muhajiruna, bisa qaddara samuwar waxancan nassosa. To, sai mu kuma mu mayar wa kura da aniyarta, mu ce, ko da akwai waxancan nassosa ai da su Ansarun na iya fatali da su; su juya masu baya.

Kamar yadda muka faxa kuma, nassosan hukunce-hukunce iri biyu ne: i) Nassi Gama-gari, wanda ya shafi ginshiqan hukunce-hukunce, da kuma ii) Nassi Rava-danni.

Idan cewar da kuka yi dole ne a samar da nassi a kan shugaba, kuna nufin nassin da zai tantance sharuxan shugaba da na talakawa da hakimai da su mufuti, da shedu da liman da ladan da kwamandan yaqi, da ire-iren waxannan hukunce-hukunce. To, sai mu ce ku mayar da wuqarku kube. Domin dama akwai su jibge, Alhamdu lillahi. Babu wani hukunci daga cikin sauran hukunce-hukunce, da aka bari huntu a wannan vangare.

A xazu kun kafa hujja a kan wannan nassi da cewa zai hana al'umma faxawa a cikin ruxani, wanda ka iya haifar da varnace-varnace masu girma fiye da irin waxanda kuka wajabta samar da nassi don kawarwa.

To, kada ku manta da cewa akasin haka ne ya faru. Domin kuwa tsawon kwanakin halifancin Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhum* irin waxancan varnace-varnace ba su faru ba. Sun dai faru ne a lokacin halifan da kuke iqirarin samuwar nassi a kansa, ba tare da kowa ba. A zamaninsa ne al'amurra suka dagule. Sai ga shi nassin da kuke riqewa a matsayin abin da zai kawo zaman lafiya da kwanciyar hankali, bai kasance haka ba. Waxancan halifofi kuwa da ba ku xauka bakin komai ba, a zamaninsu ne wancan abu na rahama da luxufi da kuke rajin samuwarsa ya tabbata; ana zaton wuta maqera sai ga ta masaqa.

Ba mamaki, dole hakan ta kasance saboda kun wajabta wa Allah abin da ba ya wajabtuwa a kansa. Kun kuma bayar da labari irin na qanzon kurege, sai hakan ta tabbatar da kasancewarku maqaryata, jahilai.

## 3.2 Wane Nassi ne ke Iya Samuwa?

Ko dai ya kasance Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bayar da labarin mutumin da zai gade shi, tare da kwarzanta yadda shugabancin nasa zai kasance. Ta haka sai gaba xayan al'umma ta gane cewa, lalle idan aka naxa wane za a ce madalla. Domin ya sami tabarrukin shugaban halitta. Kun ga ba sauran wata jayayya. Ko bai buxa baki ya ce ai ga ni ni ne ba, sai al'umma ta zave shi. Kamar yadda ta faru ga Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma*.

Ko kuma ya kasance Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bayar da labarin irin abubuwan da ke tabbatar da nagartar shugabanni. A kuma ga faruwarsu qarara, kamar yadda aka gani a lokacin halifancin Abubakar da Umar xin dai harwayau.

Ko kuma ya umurci wani daga cikin waxanda ke zuwa ziyararsa a lokacin da yake jinya, da cewa, idan ta Allah ta kasance gare ni ku bi wane. Ko kuma idan wani abu ya faru ku nemi wane. Ka ga hakan kenan ta tabbatar da kasancewar wanen halifa, bayan wancewarsa. Irin haka kuwa ta faru a kan Abubakar *Raliyallahu Anhu* a hadisin waccan mata da muka gabatar.

Ko kuma a taras da wata takarda da ya rubuta, ya bayyana cewa: Haqiqa Allah da muminai ba za su aminta da shugabancin kowa ba sai na wane. Haka xin ma ta faru a kan Abubakar *Raliyallahu Anhu*.

Ko ya yi umurni da sa wani mutum gaban sahu idan shi ya cika. Ka ga sai wannan ya zama halifa bayansa, ba tare da wata hamayya ba.

Ko a samu ya yi horo da kwaikwayon sunnar halifofi shiryayyu masu shiryarwa. Ya kuma faxi takamaiman lokacin da halifancinsu zai kasance. Da

ha kansai a gane cewa duk waxanda suka ci nasarar zama halifofi a tsakanin wannan lokaci su ne shiryayyun halifofi da ya yi magana a kansu.

Ko ya kevance wasu zavavvun mutane, ya ba su wasu ayyuka, da ake iya riqawa matsayin silali. Kamar yadda ya zo a cikin Buhari da Muslimu cewa, ya ce wa Aishah: "Ki kira mini babanki da wanki, ina son in rubuta ma Abubakar wata takarda, da zata hana mutane su yi savani a kansa". Sai kuma dai ya ce: "Ba komai. Allah da Muminai sun kau da kai daga kowa ban da Abubakar". Da haka sai aka san cewa Abubakar ne Allah Ya zava. Shi ne kuma kawai wanda muminai za su yi wa muba'yi'a. Hakan kuwa ita ta faru.

Kuma akwai wasu hadissai ingantattu da ke tabbatar da cewa, shi ma Abubakar xin ya san da haka. Ya dai kame bakinsa ne saboda hillanci irin na Baquraishe. Kamar yadda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kame nasa. Domin idan al'umma ta dace da wannan zave na Allah da Manzonsa, ba tare da katsalanda ko tirsasawar kowa ba, hakan za ta fi haifar da alheri gare ta, tare da nuna irin iliminta da matsayin da take da shi a wurin Allah.

### 3.3 Wai Ali Kaxai ke Iya Kare Shari'a

Xan Shi'ar ya ce: Abu na uku: Haqiqa wajibi ne shugaba ya kasance mai kiyaye al'farmar shari'a, bisa dalilin yankewar wahayi, tunda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya wuce, da kuma kasawar Alqur'ani da Sunnah a kan bayyana qananan hukunce-hukunce filla-filla, da kuma abubuwan da za su ci gaba da faruwa zuwa ranar qiyama. A kan haka dole ne a samu wani shugaba, wanda Allah Ta'ala zai naxa da kansa. Ya kuma kasance tsrararre daga talalaviya da kuskure (ma'asumi). Don kada wasu hukunce-hukunce su salwanta. Ko a qara wasu a cikin na asali a kan ganganci ko kuskure. Babu kuwa wanda ke da waxannan siffofi sai Ali, ijma'an.

## Martani:

Martaninmu a nan zai kasance kamar haka:-

1) Ba mu yarda dole ne sai an samu wani mutum guda wanda zai kiyaye alfarmar shari'a ba. A'a, a imaninmu tsare alfarmar shari'a wajibin al'umma ne baki xaya. Domin kuwa yadda taron jama'a za su tsare alfarmarta wani mutum xaya tal ba zai iya ba. A yayin da ita kuwa jama'ar tana iya kiyaye alfarmar shari'a yadda mutum xaya zai iya, har ma ta daxa. Domin ko a fagen ba da labari, maganar mutane da yawa ta sha malin ta mumtum xaya. A kan haka, duk lokacin da hukuncin shari'a ya samu shedar wani adadi na jama'a amintattu to, buqata ta biya. Ko banza ma'asumancin taron jama'a ya fi girma a kan ma'asumancin wanda ba Annabi ba, ko waye shi. Ko da an qaddara

kasancewar Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhu* ma'asumai, to abin da Muhajiruna da Ansaru suka riwaito ya fi wanda kowanensu zai riwaito a xaixaice. Wani kuma abin lura shi ne, a duk lokacin da aka sami mafi yawan mutane na sukar wani mai riwaya, to, babu wani hukunci na shari'a da ke iya tabbata ta hanyar sa. Balle daxa a sami da yawa daga cikin al'umma na kafirta shi. Amma mutawatiri shi ne haxuwar bakin mutane da yawa akan batu ko da kuwa ba a gama tantance kasancewarsu adilai ba.

2) Tun da yake ka ambaci ma'asumanci a farkon wannan magana. To, ba mu sani ba ko za ka aminta da wanda zai kiyaye alfarmar shari'a ko da kuwa ba ma'asumi ne ba? Idan ka aminta, sai mu ce, ba mu yarda da cewa, Ali ne ya fi kowa tsare alfarmar littafin Allah da sunnar Manzonsa ba, ko kuma ya fi kowa naqaltar su. Abin da muka yi imani da shi shi ne, Abubakar da Umar sun fi shi naqaltar littafin Allah da sunnar da Manzonsa.

3) Shin kiyaye alfarmar shari'a da wannan shugaba zai yi a matsayinsa na ma'asumi, na nufin babu wani abu na shari'a da za a iya gane ingancinsa sai ta bakinsa? Koko hakan na yiwuwa ko ba da shi ba? In dai har ana iya kiyaye alfarmar shari'a ba sai da shi ba, to, babu buqatar kasancewarsa kenan ballai zamansa ma'asumi. In kuwa kun ce, ba a iya sanin kome sai ta bakinsa. To, kenan babu wata hujja da za a iya kafawa a kan doron qasa, sai an jingina ga abin da ya riwaito. To, ya za mu tabbatar da riwayar kafin mu san ma'asumi ne? Kuma babu wani ma'asumi in ba shi ba?

4) Me zai hana 'yan Shi'ah su gamsu da abin da Allah *Subhanahu WaTa'ala* Ya wadatar da al'umma da shi na tsare shari'a a qarqashin kowaxanne mutanen ilimi kamar ilimin Alqur'ani da na hadisi da furu'a da makamantansu? Da haka, ai Allah *Subhanahu WaTa'ala* Ya hutar da al'umma daga buqatar wani mutum xaya a cikin wannan nauyi.

5) Idan har tsare alfarmar shari'a da karantar da ita ba ya yiwuwa sai ga mutum xaya, kuma ma'asumi. To, ai shi wancan da kuke jiran bayyanarsa yau shekarunsa fiye da 460 yake a voye, bai karantar da kowa wani abu na shari'a ba. A tsawon waxannan shekaru wane ne ya karantar da ku Alqur'ani da tarihin Annabi da hukunce-hukuncen da ya zo da su? Idan kun ce: Mun sami gaba xayan waxannan ilimoma ne ta hanyar abin da muka gada na kunne ya girma kaka. To, kenan kun yarda kunne ya girmi kaka na iya tabbatarwa da tsare alfarmar shari'a da karantar da ita gaba xaya. Al'ummar Annabi kuwa ta samu komai na shari'a ta mafi ingancin hanyoyin da kunne ya girmi kaka. Ba ta buqatar ma'asumanku.

6) Me kuke nufi da yankewar wahayi da kasawar Alqur'ani da Sunnah a kan yin bayani dalla-dalla? Kuna nufin bayanin hukunce-hukuncen qananan abubuwa? Koko manyan da ke da dangantaka ta qud-da-qud da su? Ai ba wani zance na shugaba da ya wuce irin wannan matsayi. A duk lokacin da shugaba zai yi wani zance da mutane, dole ne ya yi shi a sigar ta gama gari don ya haxe matsayinsu na taro. Ba abu ne mai yiwuwa gare shi ba ya kevance aikin da kowa zai yi a xaixaice a kowane lokaci, da kevantattar magana ba. To, ina laifin Manzon Allah don ya yi irin wannan? Kuma ina laifin Alqur'ani? Wannan shi ne kasawa? In ko kuna nufin Manzon ya kasa furta dukkan kalaman da ake buqata, to, babu wanda yake iya yin su, don shi ne mafi cikar girma a kan duk wani Imami da za ku kawo.

7) Allah Ta'ala Ya riga ya gaya mana cewa:

﴿ وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن رَّسُولٍ إِلَّا بِلِسَانِ قَوۡمِهِۦ لِيُبَيِّنَ لَهُمۡۖ ﴾ إبراهيم: ٤

*Kuma ba mu aika wani Manzo ba face da harshen mutanensa, domin ya bayyana masu (14:4)*

Ya kuma ce:

﴿لِئَلَّا يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَى ٱللَّهِ حُجَّةُۢ بَعۡدَ ٱلرُّسُلِۚ ﴾ النساء: ١٦٥

*Domin kada wata hujja ta kasance ga mutane a kan Allah bayan (zuwan) Manzanni (4:165)*

Kuma Ya ce:

﴿وَمَا عَلَى ٱلرَّسُولِ إِلَّا ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ ٥٤﴾ النور: ٥٤

*Kuma babu abin da yake a kan Manzo face iyarwa bayyananna (24:54).*

Da waxansu ayoyi masu kama da waxannan.

To, a nan sai mu ce: Shin bayanin da Manzo ya yi wa halitta ya isa hujja a kansu ko bai isa ba?

Cewa bayanin nasa bai isa hujja ba, na tabbatar da manufar wanda ya ce haka; na nufin ayoyin ba su karva sunansu ba. Idan kuwa muka aminta da cewa bayanin nasu ya isa hujja, to, ba a da buqatar da wani bakanike, wanda mutane za su yi qishirwar bayaninsa, balle kiyaye alfarmar karantarwarsa. Hasali ma irin baiwar da Allah ya yi wa mutane ta qarfin basirar hardacewa da karantar da zantukan Manzon Allah, da bayaninsa, ta wadatar a wannan fage. Kuma ga shi Allah ya yi alkawarin kiyaye alfarmar abin da ya saukar na wahayi, ta yadda ba a iya canza komai ko qara shi a cikinsa.

A taqaice wannan iqirari da waxannan hasararrun mutane ke yi, na cewa addinin musulunci ba zai kai gaci ba, balle a fahimce shi, sai da sa hannun wani mutum kevantacce, ita ce varna mafi girma da wani zai iya yi wa asalin addini. Duk kuwa wanda zai faxi irin wannan magana, tattare da kuma ya san abin da yake sakamakonta, to, babu shakka zindiqi ne, kuma mulhidi, wanda ke nufin yamutsa hazon addini. Kuma duk wanda ake riwaitowa tare da yayata irin maganar daga bakinsa, to jahilci da vacewarsa sun wuce min-sharrin.

8) Yau da kullum ta tilasta wa mafi yawan musulmi sanin cewa, fiye da kashi casa'in cikin xari na wannan al'umma sun sadu da saqonnin Alqur'ani da Sunna ne ba ta hanyar Ali ba. Domin kuwa a lokacin da Umar *Raliyallahu Anhu* ya ci birane da yaqi, ya tura wasu Sahabbai a matsayi malamai zuwa Sham da Iraqi don su karantar da jama'a su kuma wayar masu da kai. Kuma ta hanyar mutanen waxannan garuruwa ne ilimi ya bazu a cikin duniyar musulunci. Abin da Allah Ya hukunci Ali *Raliyallahu Anhu* da isarwa ga musulmi na ilimi bai fi wanda xan Mas'udu da xan Jabalu da takwarorinsu suka isar ba. Wannan magana kuwa da nake gaya maka sananna ce a duniya. Kuma da za a tsaya ga iyakar abin da shi Ali *Raliyallahu Anhu* ya faxa na addini, da an wayi gari yau addini sai gida-gida. Duk abin da aka riwaito daga Ali, ba wani mai yawa ne ba, idan ana zancen addini gaba xaya. Kuma ko wannan xan kaxan ma bai iso ma al'umma ta hanya mutawatira ba. Kuma ga shi a wannan zamani namu babu wani ma'asumi, balle mu koma gare shi don tantance riwayoyin, sai Malam-na-Voye da kuke cewa. 'Yan Shi'ah dai kun ji kunya in kun san ta.

### 3.4 Wai Dole ne a Samu Shugaba Ma'asumi!

Xan Shi'ar ya ce: Abu na huxu: Haqiqa Allah mai iko ne a kan samar da shugaba ma'asumi, kuma halin da duniya ke ciki na nuna buqatar haka. Yin haka kuwa ba wata varna ba ce. Saboda haka samar da shi ta wajabta. Kuma kan malamai ya haxu a kan cewa, duk wani wanda ba Ali ba, bai cancanci wannan matsayi ba. Kenan babu yadda za a kauce wa kasancewarsa wannan shugaba. Ba kuma abin da ya rage. Domin ikon Allah a kan haka ya bayyana. Kuma buqatuwa ga hakan ta bayyana, saboda rikice-rikicen da ke faruwa a duniya. Ta kuma bayyana cewa babu wata varna a cikin yin haka, domin da an fahimci akwai ta, da buqatar samar da shi xin ta kau. Shi kuwa wajabcin samar da shi ya tabbata ne saboda, da zarar iko da buqata sun tabbata, abin da zai iya kuma yi masu shamaki ya kau, to aiki ya wajaba.

**Martani:**

Wannan magana tasa ta ginu ne a kan yarda da ijma'i. Mun kuma riga mun tabbatar da cewa, da zarar ijma'i ya tabbata a matsayinsa na ma'asumi, to al'umma ba ta da buqatar da Ali *Raliyallahu Anhu* ya kasance ma'asumi. Kamar yadda idan ma'asumancin bai samu ga ijma'in ba, to, duk wani dalili da za a kafa da shi a kan kasancewar Ali ma'asumi ba karvavve ba ne. Ka ga da haka kenan gaba xayan fuskokin biyu sun yi duhu.

Wani abun mamaki ma shi ne irin yadda 'yan Shi'ar nan ke kodayaushe, qoqarin kafa hujja a kan duk abin da suke iqirari, da Nassi da Ijma'i. Sai ka ji suna cewa: Akwai nassi ko kan malami ya haxu a kan kaza. Alhali kuwa su ne mafi nisan mutane daga sanin nassosa da wuraren da kanun malamai suka haxu, da yadda ake kafa hujja da su. Savanin Ahlus-Sunnahti Wal-jama'ah. Waxanda sunansu ma kawai na nuna irin yadda sha'aninsu ke tsattsage da nassosa ingantattu da magana da harshe xaya in sun fi su dubu (Ijma'i). ka ga ashe kenan idan ana neman masu biyar Nassi da Ijma'i sau da qafa, da zarar an same su, magana ta qare, mai zuwa Makka ya haxu da Annabi.

Bari mu koma ga wancan iqirari nasu, mu yi bayanin dalilan da suka sa muke ganin sun vace a cikinsa, ta fuskoki kamar haka:

**Fuska ta farko:** Ba mu aminta da cewa akwai wata buqata ga samar da shugaba ma'asumi ba. Dalili kuwa shi ne, kasancewar ita al'ummar tamu baki xaya ma'asumiya, a duk lokacin da ta zama tsintsiya maxaurinki xaya. Wannan ya ishe mu. Kuma hakan na daga cikin abin da malamai suka ambata a cikin hikimar kasancewar al'umma ma'asumiya.

**Fuska ta biyu:** Idan kuma 'yan Shi'ar suka ce: A'a, ai muna nufin samun shugaba ma'asumi a cikin al'ummar, zai qara gwavin ma'asumancinta!

To, sai mu ce masu: Idan haka ne kuwa, ya kamata gaba xayan wakilan shugaban su ma a wajabta kasancewarsu ma'asumai domin ma'asumancinta ya qara kauri. Idan kuwa har duk lokacin da aka samu daxin ma'asumi xaya ko fiye, hakan ta fi dacewa ga al'umma, to da za a wadatu da kasancewarta ma'asumiya a matsayinta na al'umma, ha kan zai fi daxa tabbatar da bangon ma'asumancinta da moriyarsa kai tsaye.

Kar kuma ku manta da cewa, ba duk abin da mutane ke jin shi ne mafi kamala Allah ke aikatawa ba. Balle hakan ya zama wajibi a kansa.

Haka kuma daidaita wani da Annabi a cikin wannan sha'ani na daga cikin mafi girman shubuha, da qoqarin bice girman Annabi da turmuza fifikonsa. Domin kuwa idan yin imani da gaba xayan abin da wannan shugaba ma'asumi zai faxi wajibi ne, kamar yadda imani da gaba xayan abin da Annabi ya faxa yake wajibi, to annabta ba ta da wani matsayi kenan. Bayan kuma ga

shi Allah Ya umurce mu da yin imani da gaba xayan abin da Annabawa suka zo mana da shi. Inda kuwa har akwai wani mai daraja irin tasu, da an wajabta mana imani da gaba xayan abin da zai faxa. Ka ga ba wani banbanci kenan ko?

**Fuska ta uku:** Shi wannan ma'asumi da kuke cewa akwai buqatar samuwarsa, yana da cikakken iko ne a kan tabbatar da kyautatuwar rayuwar jama'a da tunkuxe masu varna? Koko dai ba ya da shi? In dai har ba ya da shi to, ba zai daxa al'umma da komai ba. Domin kuwa cikakken iko shi ne sharaxi a kan haka. Amma kasancewarsa ma'asumi kawai ba tare da wancan cikakken iko ba, na kawai tabbatar da samuwar wani mutum ne na gari, wanda bai banbanta da sauran masu wa'azi ba.

Duk da wannan nauyi da muka rage maku na san kuna iya cewa: A'a muna nufin ma'asumin na da cikakken iko.

To kun kawo kanku mahalaka. Domin kuwa wannan cikakken iko da kuka ce waxannan imamai goma sha biyu na da shi, bai sa suka tabbatar da wani gyara ko suka tunkuxe wata varna ba. Kun ga ashe kenan kun mayar da su azzalumai ba ma'asumai ba. Domin sun qi yin gyara alhalin suna da iko a cewarku. Idan kuwa ba su da ikon ne, to, su kasasshi ne kenan. Dole ne ku naxa ganwo ku xau xayan waxannan qaddarori ko ma dukkansu. Wato, kasancewarsu kasasshi ko ba ma'asumai ba. Ciwon ido sai shafa!

Idan kuwa haka ta tabbata, to, mu lalura ta wajabta mana gane koruwar wancan dalili da kuke kafawa a kan samar da shi ma'asumin. Ko banza lalura ta fi qarfin bakin dalili.

### 3.5 Wai Ali ya fi Sauran Sahabbai – Inji shi!

Xan Shi'ar ya ce: Abu na biyar: Haqiqa wajibi ne shugaba ya kasance mafificin daraja a kan waxanda yake shugabanta. Aliyu kuwa shi ne mafificin daraja a kan mutanen zamaninsa, bisa dalilai. Kenan ba makawa a kan kasancewarsa shugaba. Saboda munin gabatar da wanda aka fi a kan wanda ya fi, bisa ma'aunin hankali da nassi. Allah Ta'ala Ya ce:

﴿أَفَمَن يَهْدِيٓ إِلَى ٱلْحَقِّ أَحَقُّ أَن يُتَّبَعَ أَمَّن لَّا يَهِدِّيٓ إِلَّآ أَن يُهْدَىٰۖ فَمَا لَكُمْ كَيْفَ تَحْكُمُونَ ٣٥﴾
يونس: ٣٥

*Shin fa, wanda yake shiryuwa zuwa ga gaskiya ne mafi cancantar a bi shi, ko kuwa wanda ba ya shiryarwa sai dai a shiryar da shi? To, mene ne a gare ku? Ya ya kuke yin hukunci? (10:35)*

Za mu tattauna wannan magana tasa ta hanyoyi biyu:

**Hanya ta farko:** Bari mu soma daga inda ka tsaya, wato cewa Ali *Raliyallahu Anhu* shi ne mafificin daraja daga cikin mutanen zamaninsa. Abin da muka yi imani da shi, wanda kuma aka riwaito ta hanya tabbatatta daga shi Alin kansa da wasu ba shi ba, shi ne Abubakar ne mafi girman daraja a cikin wannan al'umma, bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama,* Umar kuma na rufa masa baya.

**Hanya ta biyu:** Eh, gaskiya ne. Mu ma mafi yawa daga cikin mutanenmu sun aminta da shugabantar da wanda yake mafifici, matuqar haka na yiwuwa. Amma kuma kamata ya yi xan Shi'ar ya shinfixa wata hujja a kan wannan iqirari nasa. Ko banza akwai malamai da dama da ke qalubalantar sa a kan haka. Wannan aya da ya kawo kuwa ba hujja ba ce a gare shi. Domin iyakacin abin da take cewa shi ne: Wanda ke shiryarwa zuwa ga tafarkin gaskiya ba daidai yake ba da wanda sai an shiryar da shi.

To, wanda ke shiryarwa ba lalle ne ya fi wanda ya shiryu ta hannunsa kome da kome ba. Kamar yadda mutum na iya samun shiriya ta hannun wanda ya fiya daraja da ilimi.

Kuma haqiqanin wanda yake shiryarwa zuwa ga gaskiya, ba tare da wata togiya ba shi ne Allah. Shi kuwa wanda ba ya iya shiryar da kowa, hasali ma shi ake shiryarwa, sifa ce ta duk wani mahaluki da ba ya da ikon xora kowa a kan hanya sai shi kansa idan Allah Ta'ala Ya xora shi a kanta. Wannan shi ne abin da wannan aya ke nufi. Wato bauta wa Allah ta fi bautawa wani mahaluki.

Mu koma farkon ayar don mu qara fahimtar ta. Ga abin da take cewa:

﴿ قُلْ هَلْ مِن شُرَكَآئِكُم مَّن يَهْدِىٓ إِلَى ٱلْحَقِّ ۚ قُلِ ٱللَّهُ يَهْدِى لِلْحَقِّ ۗ أَفَمَن يَهْدِىٓ إِلَى ٱلْحَقِّ أَحَقُّ أَن يُتَّبَعَ أَمَّن لَّا يَهِدِّىٓ إِلَّآ أَن يُهْدَىٰ ۖ فَمَا لَكُمْ كَيْفَ تَحْكُمُونَ ﴿٣٥﴾ ﴾ يونس: ٣٥

*"Ka ce: "Shin, daga abubuwan shirkinku akwai wanda yake shiryarwa zuwa ga gaskiya?" "Ka ce: "Allah ne Yake shiryarwa zuwa ga gaskiya. Shin fa, wanda yake shiryarwa ne mafi cancantar a bi shi, ko kuwa wanda ba ya shiryarwa sai dai a shiryar da shi?" (10:35)*

Idan muka daxa xauko karatun daga ayoyi huxu kafin wannan, ma'anar za ta qara fitowa fili. Duba yadda Allah yake cewa:

﴿ قُلْ مَن يَرْزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ أَمَّن يَمْلِكُ ٱلسَّمْعَ وَٱلْأَبْصَٰرَ وَمَن يُخْرِجُ ٱلْحَىَّ مِنَ ٱلْمَيِّتِ وَيُخْرِجُ ٱلْمَيِّتَ مِنَ ٱلْحَىِّ وَمَن يُدَبِّرُ ٱلْأَمْرَ ۚ فَسَيَقُولُونَ ٱللَّهُ ۚ فَقُلْ أَفَلَا تَتَّقُونَ ﴿٣١﴾ ﴾ يونس: ٣١

*Ka ce, "Wane ne Yake azurta ku daga sama da qasa? Shin, ko kuma wane ne Yake mallakar ji da gani, kuma wane ne Yake fitar da mai rai daga mamaci…? (10:31)*

Har zuwa inda Yake cewa: *"Ka ce "Shin daga abubuwan shirkinku akwai wanda yake shiryarwa zuwa ga gaskiya?" (10:35)*

Haka kuma akwai malamai da dama da ke da ra'ayin wajabcin shugabantar da mafifici, idan babu wata maslaha a cikin shugabantar da wanda aka fi xin, kuma ya kasance zukata sun fi karkata gare shi. Amma kuma wannan wajabcin na samun gindin zama ne, a lokacin da aka tabbatar da shugabantar da shi mafificin ba zai haifar da wata matsala ba. Amma kuma duk waxannan jaye-jaye da bincike-bincike, sun taqaita ne ga waxanda ke ganin cewa Ali shi ne mafifici a kan Abubakar da Umar. kamar Zaidiyyah da wasu daga cikin Mu'utazilawa. Ko kuma waxanda suka yi jemage, kamar wani vangare na Mu'utazilawan. Su ke irin wannan bincike.

Amma Ahlus-Sunnah, wannan magana ta wajabcin shugabantar da mafifici, abu ce karvavviya a wurinsu. Kuma Abubakar Siddiqu shi ne mafificin a wurinsu. Ka ga su 'yan Shi'ah duk da yake abin da suka faxi a nan gaskiya ne, amma ba su iya kare shi da dalilai. Wannan kuwa ya faru ne saboda sun toshe wa kansu hanyoyin ilimi masu yawa, ta yadda ba za su iya gane gaskiya ba balle su kare ta, don ga shi sun kasa iya tabbatar wa Harijawa da kasancewar Ali *Raliyallahu Anhu* musulmi. Ko tabbatar wa Marwaniyawa da ingancin shugabancinsa. Ga shi ko sun jefa kansu cikin irin abin da waxanda suka yaqe shi, suka riqa dalili. Don tsananin jahilcin da suke da shi da abin da maganganunsu suka qunsa na varna da tubka da walwala, da biyar son zuciya bisa jahilci.

## 4.0 Zango Na Huxu:
## Hujjojinsu Na Alqur'ani

### 4.1 Ayar ﴿ إِنَّمَا وَلِيُّكُمُ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ﴾ المائدة: ٥٥

Xan Shi'ar ya ce: Hujjojin da ke tabbatar da shugabancin Ali daga cikin littafi mai girma sun fi a qirya. Sannan ya ce:

**Dalili na farko:** Faxar Allah Ta'ala da Ya ce:

> *Abin sani kawai, majivincinku Allah ne da Manzonsa, da waxanda suka yi imani, waxanda suke tsayar da sallah, kuma suna bayar da zakka, alhalin su masu ruku'i ne (5:55)*

Kan malamai ya haxu, inji shi, a kan cewa wannan aya ta sauka ne a kan Ali *Raliyallahu Anhu*.

Ya ci gaba da cewa: Malam Sa'alabi ya riwaito daga Abu Zarri, wai ya ce: "Na ji Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da waxannan kunnuwa nawa. In qarya nake yi su kurumce. Na kuma gan shi da waxannan idanu nawa. In qarya nake yi su makance. Yana cewa: Aliyu shi ne limamin 'yan ga mu mun fito, kuma ajalin kafirai. Duk wanda ya taimake shi, abun taimako ne. Kuma haqiqa Ni, na yi sallar azzahar watarana tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai wani mutum ya miqe ya yi bara cikin masallaci, ba a sami wanda ya ba shi komai ba. Sai ya xaga hannayensa sama, shi mai roqon. Ya ce: "Ya Ubangiji! ka sheda, na yi bara a cikin masallacin Manzonka babu wanda ya ba ni ko tarau". A lokacin da yake wannan magana Ali *Raliyallahu Anhu* na kusa yana ruku'i. Sai ya miqo masa qaramin yatsansa na dama, da ke xauke da zobe. Mai roqon ya karva ya zare zoben. Ashe lokacin da wannan abu ke faruwa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* na gani. Qare sallarsa ke da wuya, shi Annabin, sai kawai ya xaga kansa sama wai. Ya ce: "Ya Ubangiji! haqiqa Musa ya roqe ka da cewa: "Ya Ubangiji! Ka buxa mini qirjina. Kuma ka sauqaqe mini al'amarina. Kuma ka warware mini wani qulli daga harshena. Su fahimci maganata. Kuma ka sanya mini wani mataimaki daga iyalaina. Haruna xan'uwana. Ka qarfafa halittata da shi. Kuma ka shigar da shi a cikin al'amarina. (25:32) Sai Ka karva masa ta hanyar saukar da ayar da ke cewa: Za mu qarfafa damtsenka da xan'uwanka, kuma mu sanya maku wani dalili, saboda haka (maqiyanku) ba za su iya kai gare ku ba". (28:35) Wai, sai Annabi ya ci gaba da cewa: "To ya Ubangiji! Ni ne Muhammadu Annabinka kuma zavavvenka. Ya Ubangiji! Ni ma ka buxa mini qirjina. Kuma ka sauqaqa mini al'amarina. Kuma ka sanya mini mataimaki daga cikin iyalaina. Kuma ya kasance Aliyu, don ka qarfafa halittata da shi".

Abu Zarri ya ce, inji xan Shi'ar: Kafin Manzon Allah ya rufe bakinsa sai ga Jibrilu *Alaihis Salamu* ya sauka daga wurin Allah. Ya ce: "Ya kai Muhammadu, karanta". Ya ce: "Me zan karanta"? Jibrilu ya karva masa da

cewa: “Karanta: *Abin sani kawai, majibincinku Allah ne da Manzonsa, da waxanda suka yi imani wanxanda suke suna tsayar da sallah, kuma suna bayar da zakka alhalin su masu ruku’i ne (5:55).*

Xan Shi’ar ya ci gaba da cewa: Kuma malamin nan masanin Fiqihu wanda ake kira Ibnul Magazili, ya riwaito cewa, wannan aya ta sauka ne a kan Ali. Kuma kalmar can ta “Waliyyi” wadda ke nufin “Majivinci” tana nufin wanda ke da cikakken iko a kan abu. Kuma wannan aya ta tabbatar wa Alin da wannan wilaya kamar yadda Allah Ta’ala Ya tabbatar wa kansa da Manzonsa da ita.

**Martani:**

Muna tabbatar wa wannan xan Shi’ah da cewa: Wannan magana tasa ba ta ko kai matsayin a riqa ta zato ba, balle ya sami sassafci. Domin kuwa duk gaba xayan wannan rattahi da ya yi vata ne, kuma qarya ce tsagwaronta. Irin wadda wawaye kan kitsa. Ko da wannan magana ta xan tsalma wani abu a cikin kansa na ilimi, wanda ake iya ba matsayin zato a mata kanshari’a, to yarda da ambaton ta hujja abu ne da shari’a ke matuqar qyama. Domin kuwa ana amfani da kalamar “Hujja” ne a musulunci a kan abin da aka ambata qarara, wanda ya fa’idantar da ilimi tabbatacce. Kamar cewar da Allah Ta’ala Ya yi:

﴿ وَقَالُوا۟ لَن يَدْخُلَ ٱلْجَنَّةَ إِلَّا مَن كَانَ هُودًا أَوْ نَصَٰرَىٰ ۗ تِلْكَ أَمَانِيُّهُمْ ۗ قُلْ هَاتُوا۟
بُرْهَٰنَكُمْ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿١١١﴾ ﴾ البقرة: ١١١

*Kuma suka ce: “Babu mai shiga Aljanna face waxanda suka zama Yahudawa ko Nasara. Waxancan tatsuniyoyinsa ne. Ka ce: “Ku kawo dalilinku, idan kun kasance masu gaskiya (2:111).*

Da kuma inda Ya ce:

﴿ أَمَّن يَبْدَؤُا۟ ٱلْخَلْقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ وَمَن يَرْزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ ۗ أَءِلَٰهٌ مَّعَ ٱللَّهِ ۚ قُلْ هَاتُوا۟ بُرْهَٰنَكُمْ إِن كُنتُمْ
صَٰدِقِينَ ﴿٦٤﴾ ﴾ النمل: ٦٤

*Ko wane ne yake fara halitta sa’annan kuma ya mayar da ita? Kuma wane ne ya azurta ku daga sama da qasa? Ashe akwai wani abin bauta wa tare da Allah? Ka ce, ku kawo dalilinku, idan kun kasance masu gaskiya (27:64).*

Duk wanda ke iqirarin cewa shi mai gaskiya ne, to dole ne ya kawo hujja a kan haka. Duk kuwa abin da za a iya karva da sunan gaskiya, to lalle ne ya kasance qarara.

Amma gaba xayan abin da ya ambata matsayin hujjoji tsattsage suke da qarya: Babu xaya daga cikinsu da gaskiya ta share wa fage. Balle a sami wanda ya yi mata he!. Don hasali, ba abu ne mai yiwuwa ba 'yan sharar fagen gaskiya su yi wa qarya da vata zagi. In Allah Ya yarda nan gaba kaxan za mu tona asirin waxannan qaryace-qaryace xaya bayan xaya. Tare da samar wa kowane qwai da za mu yi zakara. Domin kuwa yarda da ambaton waxannan waqoqi nasa da sunan hujja na daga cikin mafi munin qarya.

Sannan kuma xan Shi'ar ya dogara a kan wasu zantuka da yakan riwaito daga wasu mutane a cikin tafsirin waxannan ayoyi kuma sau tari qarya ce yake yi masu. Ko da hakan ta tabbata gaskiya, to mafi yawan mutane ba su yarda da shi a kan haka ba. Idan kuwa har zancen wani mutum xaya, wanda ba a gama tantance gaskiyarsa a cikin zancen ba. Da kuma kasancewar mafi yawa daga cikin mutane sun yi ban hannun makafi da shi a kan zaman haka hujja. Idan irin wannan zance na iya zama hujja, to, yana kuwa iya kafa hujjoji da yawa. A qarshe sai tarayyar hujjojin nasa su ci karo da juna ta hanyar tubka da walwala. Alhali kuwa hujjoji ba su tubka da walwale junansu, matuqar sun karva sunan hujja.

Kai! In Allah Ta'ala Ya so za mu bayyana kasancewar waxannan hujjoji da ya kafa qarya, a kan waxancan abubuwa da yake iqirari. Za mu ko yi haka ne ta hanyar shimfixi qwararan hujjoji waxanda ba su cin karo da juna. Domin daxa fayyace kasancewar kalaman nasa soki burutsu, da zarar an kalle su kallo xaya. Kuma duk wanda Allah bai toshe wa basira ba yana iya tabbatarwa da gane haka. Haka kuma wannan gwagwarmaya da za mu shiga, za ta kafa hujjoji a kan kasancewar Alqur'ani da addinin musulunci da Annabcin Manzon Allah gaskiya; kuma suna ban hannun makafi da gaba xayan ruvavvin hujjojin da xan Shi'ar ya kafa.

Eh! Ruvavvi ne a haqiqa, ta yadda duk mai kaifin hankali da ya xan nazarce su, ya kuma kairdadi abubuwan da suke iya haifarwa, zai tabbata cewa wutarsu na iya canye koren gandun dajin imani.

Abu na gaba da za mu ce shi ne: Ko shakka babu mayar da martani a kan yadda ya rikita wannan aya wajibi ne. Za mu kuma yi shi ta fuskoki kamar haka:

### Fuska ta farko:

Kafin komai, muna son xan Shi'ar ya tabbatar mana da ingancin wannan magana. Wato ya sake maimaita wancan hadisi, amma a cikin siga irin wadda ke sa hujja ta samu kafuwa. Domin kuwa jingina shi kawai da ya yi ga tafsirin Sa'alabi, ko iqirarin haxuwar kan malamai a kan sa, waxanda kuma ba masana ilimin riwaya ba ko waxanda ake iya gasgantawa idan sun riwaito wani abu. Sai fa idan ana iya tantance ingancin isnadinta.

**Fuska ta biyu:**

Cewar da ya yi: "Kan malamai ya haxu ga cewa ayar ta sauka ne a kan Ali", magana ce ta banza kuma sosai, irin wadda aka saba yayatawa. Abin da ya tabbata dai, kamar yadda kan masana sirrin riwaya ya haxu, shi ne, waccan aya ba ta sauka kan Ali kawai ba. Kuma Alin bai yi sadaqa da zobe a cikin sallah ba. Haka kuma kan malaman hadisi ya haxu a kan cewa wannan qissa da xan Shi'ar ya riwaito qarya ce tsagwaronta.

Haka kuma kan malaman ya haxu a kan cewa, godogo da Sa'alabi da xan Shi'ar ya yi, a matsayin wanda ya riwaito wasu maganganu daga gare shi, ba wani kayan gabas ne ba. Domin Sa'alabi na riwaito hadissan Gizo da Qoqi a cikin tafsirinsa. Kamar hadissan da ya kan riwaito, ya saka su a farkon kowace sura don bayyana falalarta. Da wasu abubuwa masu kama da haka. A kan haka ne ma suke yi masa laqabai da: "Da'u fataken dare".

Haka almajirinsa Al-Wahidi da wasu daga cikin malaman tafsiri makamantasu suke, suna riwayar qwaya da burtuntuna. Abin da kawai muke nufin tabbatarwa a nan shi ne, kasancewar wannan marubuci jahili kuma maqaryaci, don kowa ya gane.

Babban abin da ke tabbatar da haka shi ne cewar da ya yi: Haqiqa kan malamai ya haxu a kan cewa ayar ta sauka ne a kan Ali. Abin mamaki ni a wurina shi ne: Wane ne daga cikin ma'abuta ilimi ya naqalto wannan magana, a irin wannan al'amari, har shi ya same ta? Domin kuwa ba a yarda da ijma'i sai idan an ji haka daga bakin wani fitaccen malami a fannin riwaya.

Hakan ta sa ba a sauraren duk wani zaqaqurin magana, ko malamin tafsiri, ko na tarihi ko makamantansu, idan ya riwaito abu ba tare da tabbataccen isnadi ba. Sai kawai a saka maganar kwandon shara. To, ya kake zato idan ya yi iqirarin haxuwar kan malamai a kan wata magana ta qarya?!

**Fuska ta uku:**

Hala xan Shi'ar bai san cewa, malaman tafsirin da ya cirato wannan magana daga littafansu, da waxanda suka fi su ilimi, sun daxe da cirato wata magana da ke walwale wannan da yake iqirari ba? Shi malam Sa'alabi, ya riwaito a cikin wannan tafsiri nasa cewa, xan Abbas ya tafi a kan cewa, wannan aya ta sauka ne a kan Abubakar. Ya kuma riwaito Abdulmalik na cewa: "Na tambayi baban Ja'afar a kan wanda wannan aya ta sauka. Ya karva mani da cewa: "A kan gaba xayan muminai". Na ce masa: "Wasu mutane na cewa: "Ta sauka ne a kan Ali". Sai ya ce: "To ai Aliyu na daga cikin muminai". An kuma samo irin haka daga malam Dhahhaku.

**Fuska ta Huxu:**

Mun yafe wa xan Shi'ar qaryar ijma'i da ya yi. Muna so ya tabbatar mana da maganar ta hanya xaya ingantancciya. Domin wanda Sa'alabi ya ambata mai rauni ne. A cikinsa akwai mazajen da ba a yarda da su ba. Balle daxa wanda xan magazili ya riwaito, wanda shi rauninsa ya vaci matuqa. Hadisan da ya tattara a cikin littafinsa, ko kurtu a makarantar ilimin hadisi ya san cewa qaryayyaki ne kawai aka kitsa. To isnadin nan guda xaya rak ingantacce da muke nema gare shi muna son ya qunshe wannan magana da waccan.

**Fuska ta biyar:**

Da wannan aya na magana ne a kan cewa Aliyu ya bayar da zakka a daidai lokacin da yake ruku'i, kamar yadda suke iqirari, da hakan ta zama wani sharaxi na wajabci a cikin cancantar shugabanci. Ta yadda musulmi ba za su jivanci kowa ba sai Ali shi kaxai. Ba zancen Hassan ko Husaini ko sauran Banu Hashim ake yi ba. Wannan kuwa ya sava wa abin da ku kanku 'yan Shi'ah kuke cewa.

**Fuska ta shida:**

Ayar dai ta zo ne da lafazin jam'i ba na mutum xaya ba. Don haka, ba ta xanfaruwa a kan Ali shi kaxai.

**Fuska ta bakwai:**

Ta kuma tabbata cewa, Allah Ta'ala ba ya farin ciki, balle ya gode wa mutum a kan aikata komai, sai idan abin nan yardadde ne a wurinsa; ta hanyar kasancewarsa wajibi ko mustahabbi. Ita kuwa sadaqa da kyauta da 'yanta bayi da ba da haya da aure da saki, da ire-iren su. Malaman musulunci sun yi ittifaqi a kan cewa aikata su a cikin sallah ba xa'a ba ne, balle su zama wajibi ko mustahabbi. Hasali ma da yawa daga cikin malaman na ganin aikata xayansu cikin sallah na vata ta, ko da ba a yi magana ba. Kai tana ma iya vaci dalilin wata ishara da aka fahimci maqasudinta, a wurin wasu daga cikin malamai. A yayin da wasu malaman suka qara da cewa, babu wani abu da ake iya mallaka ta wannan hanya, sakamakon rashin wani sanadari na shari'a a cikin harkar. Kuma da irin wannan aiki abin so ne to, da Annabi ya kasance farkon wanda ya aikata shi, ya kuma kwaxaitar da Sahabbansa a kan haka. Da kuma an sami cewa Aliyun ya tava aikata hakan a wasu lokuta.

Rasa xaya daga cikin waxannan abubuwa, na tabbatar da kasancewar sadaqa a cikin sallah ba wani aiki na madalla ba. Musamman ma da yake aikin tallafa wa mabuqacin ba ya wucewa. Ta yadda mai sadaqar zai iya haqura har ya qare sallah, sannan ya yi kyautar. Domin idan dai har sallah ta karva sunanta, to, ba za ta bayar da damar yin haka ba.

**Fuska ta Takwas:**

Mu qaddara cewa yin sadaqa a cikin sallah shari'a ne. Da ba a kevance lokacin ruku'i don aikata ta ba; aikata ta a lokacin da ake zaune ko tsaye ya fi dacewa. Amma sai a ce babu wanda zai zama shugaba gare ku sai xaya daga cikin waxanda ke bayar da sadaqa a lokacin da suke ruku'u? To, za a sami wani ya yi sadaqar a lokacin da yake tsaye ko zaune, bai cancanci wannan shugabacin ba ko?

**Fuska ta Tara:**

Cewar da 'yan Shi'ah suka yi: faxar Allah Ta'ala a cikin ayar: *Kuma suna bayar da zakkah alhali su masu ruku'i ne (5:55)* wai hakan na nufin wanda zai bayar da zakkar ya kasance yana cikin ruku'i. Magana ce da ba ta sauraruwa. Domin Aliyu *Raliyallahu Anhu* ba ya cikin waxanda zakka ta wajaba kansu a wannan zamanin na Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* saboda kasancewarsa talaka. Kuma ita zakkar azurfa na wajaba ne a kan wanda ya mallaki nisabi tsawon shekara. Aliyu kuwa ba ya cikin waxanda suka mallake shi.

**Fuska ta Goma:**

Wani abin kuma shi ne, da yawa daga cikin malaman fiqihu sun tafi a kan cewa fitar da zobe da bayar da shi a matsayin zakka ba ya isa, sai a lokacin da aka aminta da wajabcin zakka a cikin kayan ado. Aka kuma yarda da fitar da wani abu daga cikinsu a matsayinta. Sane muke da cewa, akwai malaman da suka yarda da a fitar da qimar abin da ya wajaba xin. To, amma ai yin wannan awo da gwaji don fitar da qimar, abu ne mawuyaci a cikin sallah. Kuma hasali ma ita qimantawar kanta ta sassava gwargwadon sassavawar yanayi.

**Fuska ta Goma Sha xaya:**

Wannan aya ba ta nufin a bayar da zakka lokacin da ake ruku'i. A'a matsayinta daidai yake da na ayar da ke cewa:

﴿ وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ وَٱرْكَعُوا۟ مَعَ ٱلرَّٰكِعِينَ ﴾ البقرة: ٤٣

*Kuma ku tsayar da sallah, kuma ku bayar da zakka, kuma ku yi ruku'i tare da masu yin ruku'i (2:43).*

Daidai kuma ta ke da ayar da ke cewa:

﴿ يَٰمَرْيَمُ ٱقْنُتِى لِرَبِّكِ وَٱسْجُدِى وَٱرْكَعِى مَعَ ٱلرَّٰكِعِينَ ﴾ آل عمران: ٤٣

*Ya Maryamu! Ki yi qanqan da kai ga Ubangijinki, kuma ki yi Sujada, kuma ki yi ruku'i tare da masu ruku'i (3:43).*

Gaba xayan waxannan ayoyi biyu suna umurni ne da ruku'i, kamar yadda ita ma waccan ayar ke yi.

**Fuska ta Goma Sha biyu:**

Mafi yawan amintattun malaman tafsiri na da da na yanzu, sun aminta da cewa wannan aya ta sauka ne, domin hani daga jivintar kafirai, da horo da jivintar muminai. Kasancewar wasu munafikai, irin su Abdullahi xan Ubayyu na jivintar Yahudawa, bisa dalilin cewa wai, suna taka-tsantsan ne, kada watarana reshe ya juye da mujiya. Shi kuwa wani daga cikin muminai wanda ake kira Ubadata xan Samitu ya ce wa Manzon Allah: "Ni kam ina Jivintar Allah da Manzonsa ne kawai. Kuma ba zan ko haxa hannu da waxancan kafirai ba balle jivintar su".

**Fuska ta Goma Sha uku:**

Duk wanda ya yi nazarin Alqur'ani da kyau, zai fahimci cewa, takin qasar wannan aya (siyaqinta) na tabbatar da wannan abu da muka faxa. Domin kuwa a can kafin wannan aya kaxan cewa Allah Ta'ala Ya yi: *Ya ku waxanda suka yi imani! Kada ku riqi Yahudawa da Nasara majivinta. Sashensu majivinci ne ga sashe. Kuma wanda ya jivince su daga cikinku, to lalle ne shi, yana daga cikinsu. Lalle Allah ba Ya shiryar da mutane azzalumai (5:51).*

Ka ga wannan hani ne Allah ya yi daga jivintar Yahudawa da Nasara. Sannan sai kuma Ya ce: *Sai ka ga waxanda a cikin zukatansu akwai cuta, suna tsoron gaugawa a cikinsu, suna cewa: 'Muna tsoron kada wata masifa ta same mu. To, akwai tsammanin Allah Ya zo da buxi ko kuwa wani umurni daga wurinsa sai su wayi gari suna da-na-sani a kan abin da suka voye cikin zukatansu (5:52)* har zuwa inda Ya ce: *Saboda haka suka wayi gari suna masu hasara (5:53).*

A nan kuma Allah Ya bayyana siffofin waxanda suke akwai cuta a cikin zukatansu ne. Wadda hakan ke sa su jivintar kafirai da munafukai.

Bayan haka kuma ya ce:

> *Ya ku waxanda suka yi imani! Wanda ya yi ridda daga cikinku daga addininsa, to Allah zai zo da wasu mutane, Yana son su, kuma suna son Sa, masu tawali'u a kan muminai, masu izza a kan kafirai. Suna yin jihadi a cikin hanyar Allah, kuma ba su tsoron zargin mai zargi. Waccan falalar Allah ce, Yana bayar da ita ga wanda Yake so. Kuma Allah Mayalwaci ne, mai ilimi.*

A nan kuma Ya ambaci irin mugun aikin waxanda suka yi ridda, tare da tabbatar da hakan ba ta cutar da addinin Allah da komai. Ya kuma faxi siffofin waxanda zai maye gurbinsu da su.

Bayan haka ne Ya ce:

*Haqiqa, Allah ne kawai majivincinku da Manzonsa, da waxanda suka yi imani, waxanda suke suna tsayar da sallah, kuma suna bayar da zakka alhalin su masu ruku'i ne. Kuma wanda ya jivinci Allah da Manzonsa da waxanda suka yi imani, to, rundunar Allah su ne masu rinjaye (5:56).*

Waxannan ayoyi kuma sun qunshi bayani ne a kan yanayi da halayen waxanda suka shiga musulunci daga cikin munafikai, da kuma na waxanda suka yi ridda daga addini, da kuma na muminai waxanda duga-dugansu suke kafe a kan turbar musulunci fai da voye.

Da yake salon tafiyar waxannan ayoyi na cikin sigar "Jam'i" ne, tana magana ne a kan gaba xayan muminai waxanda suka siffanta da waxannan siffofi. Ba ta kevanta ga Abubakar ko Umar ko Aliyu ko waninsu ba. Sai dai su ne mafi cancantar al'umma da shiga cikin ma'anar ayoyin.

**Fuska ta Goma Sha Huxu:**

Lafuzzan da xan Shi'ar nan ya ambata a cikin waxancan hadisai na daga cikin abubuwan da aka tabbatar da kasancewarsu qarya, wadda aka yi wa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama.* Domin kuwa Aliyu ba shi ne Imamin 'yan ga mu mun fiton rundunar musulmi ba. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne Imamin wannan al'umma ciki da waje. Haka kuma ba Aliyun kawai ne ajalin kafirai ba. Ya dai kashe wasu daga cikinsu, kamar yadda wasu Sahabbai takwarorinsa suka kashe wasu; babu wani daga cikin masu jihadin can, da aka yi artabu da kafirai tare da shi face akwai wani sashe na kafirai, da ya aika lahira.

Kuma ka ga cewar da xan Shi'ar ya yi wai Annabi ya ce: Allah zai taimaki duk wanda ya taimaki Ali, zai kuma tavar da duk wanda ya tavar da shi, hakan ba ta faru ba. Mun kuwa san Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba ya faxar abin da ba gaskiya ba. Kuma su kansu 'yan Shi'ah sun tabbatar wa duniya da cewa gaba xayan al'ummar ta tavar da Alin, har zuwa lokacin da aka yi wa halifa Usmanu kisan gilla.

Alhali kuwa sanannen abu ne cewa babu lokacin da wannan al'umma ta sami gagarumin taimako daga wurin Allah, irin lokacin halifancin waxancan Sahabbai uku na kafin Ali *Raliyallahu Anhu.* Kuma ko lokacin da aka kashe halifa Usmanu *Raliyallahu Anhu* mutane kasuwa suka yi gida uku: Kashi na xaya ya goyi bayan Ali ya taya shi yaqi. Kashi na biyu kuma ya shaya daga da shi, kashi na uku kuma ya yi qoqarin shiga tsakani. To, ko a wannan lokaci Allah bai taimaki rundunar Ali *Raliyallahu Anhu* a kan waxancan rudunoni biyu ba. Rundunar Mu'awiyah ce Allah Ya ba nasara, har ya zama shugaba. Su ne kuma suka sami nasarar murqushe kafirai da cin garuruwa. Taimakon da Ali ya samu daga wajen Allah, a nan bai fi irin wanda takwarorinsa suka samu ba, wajen yaqar Harijawa da kafirai.

Haka kuma addu'ar da xan Shi'ar ya ce Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi bayan Alin ya yi sadaqa da zoben qarya ce lafiyayya. Domin kuwa sanannen abu ne cewa, akwai Sahabban da suka bayar da sadaqar wasu abubuwa saboda Allah, a waxansu lokuta da ake da buqata da su, waxanda kuma amfaninsu da darajarsu ta fi na wancan zoben da Aliyu ya bai wa wancan mutum.

Ya zo a cikin Buhari da Muslimu cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Babu wata dukiya da ta amfane ni, kamar dukiyar Abubakar. Mafi baiwa gare ni da abokantakarsa da dukiyarsa daga cikin mutane kuma shi ne Abubakar. Da na kasance mai riqon wani badaxayi daga cikin mutanen da ke bayan qasa, da na riqi Abubakar".

Haka kuma Usmanu ya bayar da gudunmuwar raqumi dubu saboda Allah, a lokacin da za a je yaqin tsanani (Tabuka). Har Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Duk abin da Usmanu zai aikata, daga yau, ba zai cuce shi ba".

Ka ji iyakar abin da Annabin ya ce, a kan waxannan Sahabbai.

Wani abin tambaya ma a nan shi ne: Ya za a yi Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya roqi Allah da cewa: Ka sanya mini wani mataimaki daga cikin mutanena. Ya kuma kasance Aliyu. Don ka qarfafa al'amarina da shi? Bayan kuwa a lokacin har an yi hijira zuwa Madina, an kuma sami nasara kan kafirai. Ta hanyar taimakon da Allah ya yi wa Manzon da qarfinsa da ikonsa, da kuma na taron muminai. Kamar yadda Yake cewa:

﴿ وَإِن يُرِيدُوٓاْ أَن يَخۡدَعُوكَ فَإِنَّ حَسۡبَكَ ٱللَّهُۚ هُوَ ٱلَّذِيٓ أَيَّدَكَ بِنَصۡرِهِۦ وَبِٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٦٢ ﴾ الأنفال: ٦٢

*Shi ne wanda Ya qarfafa ka da taimakonsa, kuma da muminai (8:62)*

Ya kuma ce:

﴿ إِلَّا تَنصُرُوهُ فَقَدۡ نَصَرَهُ ٱللَّهُ إِذۡ أَخۡرَجَهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ثَانِيَ ٱثۡنَيۡنِ إِذۡ هُمَا فِي ٱلۡغَارِ إِذۡ يَقُولُ لِصَٰحِبِهِۦ لَا تَحۡزَنۡ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَنَاۖ ﴾ التوبة: ٤٠

*Idan ba ku taimake shi ba, to, haqiqa Allah Ya taimake shi, a lokacin da waxanda suka kafirta suka fitar da shi, suna su biyu, a lokacin da suke cikin kogon dutse, sanda yake cewa da sahibinsa; "Kada ka yi baqin ciki, haqiqa Allah Yana tare da mu" (9:40).*

Wanda yake tare da shi xin, a lokacin da Allah ya yi masa wannan taimako, shi ne Abubakar, bayan da kafirai suka fitar da shi; sun kasance su

biyu kacal, Allah ne na ukunsu. Haka kuma shi ne ya kasance tare da shi a cikin dabi a lokacin yaqin Badar ba tare da kowa daga cikin Sahabbai ba.

Babu wani Sahabbai ko bayan Abubakar, face akwai wata rawa ta a zo a gani da ya taka a cikin fagen taimaka wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.* Ko shakka babu kuma Allah zai saka masu a kan wannan.

Duk wanda ke iqirarin cewa wai, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya roqi Allah Ya qarfafi al'amarinsa da wani mutum kevantacce, kamar yadda Annabi Musa ya roqa, ya shara wa Annabi qarya, ya kuma zalunce shi.

Kuma ko shakka babu Shirka da Ilhadi da Munafunci ne suka haxu suka haifi Shi'anci. Sai dai ba kodayaushe ne hakan ke bayyana a fuskarsu ba.

**Fuska ta goma sha biyar:**

Iyakar tawilin da ake iya yi wa wannan aya, ko 'yan Shi'ah su sami sassauci, shi ne: Ayar na cewa lalle ne muminai su jivinci Allah da Manzonsa da mumunai 'yan'uwansu. Ka ga hakan ta haxa har da Ali, tunda shi ma mumini ne, sai su jivince shi. Kenan babu wani kokwanto a kan cewa jivintar Ali wajibi ne a kan kowane mumini, kamar yadda yake wajibi a kansu su jivinci takwarorinsa muminai.

Allah Ta'ala na cewa:

﴿ وَإِن تَظَٰهَرَا عَلَيۡهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ هُوَ مَوۡلَىٰهُ وَجِبۡرِيلُ وَصَٰلِحُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَۖ ﴾ التحريم: ٤

*Kuma idan kun taimaki juna a kansa, to, haqiqa Allah shi ne mataimakinsa, da Jibrilu da salihan muminai (66:4).*

A nan Allah Ya bayyana mana cewa, duk wani salihi daga cikin muminai mataimaki ne ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kuma Allah *Subhanahu* da mala'ika Jibrilu mataimakansa ne. Babu wani abu a cikin waxannan ayoyi da ke nuna maganar shugabanci ballantana a ce Ali ko wani take nufi.

**Fuska ta goma sha shida:**

Kuma da Allah *Subhanahu WaTa'ala* na nufin jivinta da ma'anar Shugabanci, da cewa zai yi: Abin sani shi ne shugabanku shi ne Allah da Manzonsa da waxanda suka yi Imani. Ba zai ce: Duk wanda ya jivinci Allah da Manzonsa ba. Domin kuwa a qa'idar harshen Larabci ba a cewa, an jivinci wanda aka naxa. Sai dai a ce: An naxa shi shugaba.

**Fuska ta goma sha bakwai:**

Rashin yiwuwar haka na daxa tabbata, idan aka yi la'akari da cewa Allah *Subhanahu WaTa'ala* Ya fi qarfin a ce masa shugaban wasu, ko sarkinsu. Allah ya fi qarfin haka; shi dai mahaliccinsu ne, mai azurta su,

Ubangijinsu, mamallakinsu, wanda komai da kowa yake hannunsa. Ba a cewa: Allah shi ne Sarkin Musulmi, kamar yadda za a iya ce wa Ali ko wani shugaba haka. Kai ko Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fi qarfin a ce masa sarki. Matsayinsa ya wuce haka nesa. Ai ko Abubakar Siddiqu *Raliyallahu Anhu* ka ga musulmi ba su ambace shi sarki ba, sai dai suka yi masa laqabi da halifan Manzon Allah. Umar ne farkon wanda aka ambata da laqabin Sarkin Musulmi daga cikin halifofi.

**Fuska ta goma sha takwas:**

Ba duk wanda Allah Ya ba shugabanci ne komai adalcinsa ba, mutanensa ke kasancewa rundunar Allah, kuma mai rinjaye. Domin kuwa da yawa Allah kan shugabantar da mutane adalai a kan munafukai da kafirai. Kamar yadda aka sami kafiran amana da munafukai a Madina qarqashin kuma jagorancin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama.*

## 4.2 Ayar ﴿بَلِّغْ مَا أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ﴾ المائدة: ٦٧

Xan Shi'ar ya ce: Faxar Allah Ta'ala da Ya ce:

﴿ ۞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلرَّسُولُ بَلِّغْ مَآ أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ ۖ وَإِن لَّمْ تَفْعَلْ فَمَا بَلَّغْتَ رِسَالَتَهُۥ ۚ وَٱللَّهُ يَعْصِمُكَ مِنَ ٱلنَّاسِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٦٧﴾ ﴾ المائدة: ٦٧

*Ya kai Manzo! Ka iyar da abin da aka saukar zuwa gare ka daga Ubangijinka. Kuma idan ba ka aikata ba, to, ba ka iyar da manzancinsa ba kenan (5:67).*

Xan Shi'ar ya ce, kan malamai ya haxu a kan cewa wannan aya ta sauka ne a kan Ali *Raliyallahu Anhu.* Kuma Abu Nu'aimi al-Hafizu daga cikin malaman sunnah, ya riwaito daga Adiyyu, da isnadinsa cewa: Wannan aya ta sauka ne ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a kan Aliyu xan Abu Xalib. An kuma samo daga cikin tafsirin Sa'alabi, wanda ya ce: Ma'anar wannan aya ita ce: Ka iyar da abin da aka saukar gare ka daga Ubangijinka a cikin falalar Ali. Ya ci gaba da cewa: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kama hannun Ali, a lokacin da wannan aya ta sauka gare shi, ya ce: Duk wanda na kasance majivinci gare shi, to Aliyu majivincinsa ne.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa, tunda kuwa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne majivinci Abubakar da Umar da sauran Sahabbai *Raliyallahu Anhu* bisa ijma'i, kenan Aliyu zai kasance majivincisu, ta hanyar zamowa Imami (Shugaba). Kuma harwayau dai ya zo a cikin tafsirin na Sa'alabi, inji shi, cewa: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tara mutane a lokacin da yake a *Ghadir Khum* ya kama hannun Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce: *Duk wanda na kasance majivinci gare shi, to, Aliyu majivincinsa*

*ne*. Nan take wannan magana ta tuma, ta watsu a cikin garuruwa. Har ta kai kunnen Harisu xan Nu'umanu al-fihiri. Sai ya hau taguwarsa ya iske Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a wurin da ake kira Abxahu yana cikin taron Sahabbansa. Ya ce masa: Ya kai Muhummadu! ka gaya mana cewa, Allah Ya hore mu da shaidar da ba wanda ya cancanci bauta sai shi, kuma kai Manzon Allah ne, muka yarda maka. Ka kuma hore mu da yin salloli biyar, da fitar da zakka daga cikin dukiyarmu, da mu azumci watan Ramalana, duk muka karvar maka. Amma duk wannan ba ta ishe ka ba, sai ka xaukaka likkafar qaninka, ka fifita shi a kanmu? Don na ji kace: Duk wanda ka kasance majivinci gare shi, to Aliyu majivincinsa ne. To, wannan kuma daga wurin Allah ne ko daga wurinka? Sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya sha masa billahil-lazi cewa, umurni ne daga wurin Allah.

Sai kawai Harisu ya buga rigarsa ya tasar wa taguwar can tasa, yana cewa: Ya Ubangiji idan dai har gaskiya ne, wannan magana daga wurinka take, to ka yi mana ruwan duwatsun wuta daga sama. Ko ka zo mana da wata azaba mai raxaxi. Ai bai kai wurin taguwar ba sai Allah Ya jefe shi da wani dutse na wuta a maxiga, ya fito ta duburarsa, nan take ya faxi matacce. Allah Ta'ala kuma Ya saukar da cewa: *Wani mai tambaya ya yi tambaya game da azaba, mai aukuwa. Ga kafirai, ba ta da mai tunkuxewa. Daga Allah mai mata kai (70:1-3).*

Xan Shi'ar ya rufe maganarsa da cewa, wai, wani malami daga cikin Jumhuru (yana nufin Ahlus-Sunnah), da ake kira Naqqashu ya riwaito wannan magana a cikin tafsirinsa.

Don mayar da martani a kan wannan magana sai mu ce, bismillahi:

**Fuska ta farko:**

Tumun fari dai, wannan magana gaba xayanta qarya ce zaharani. Abu mafi zama qarya ma, a cikin maganar duk bai fi cewar da ya yi kan malamai ya haxu a kan saukar ayar a kan Ali ba. Babu wani malami xaya daga cikin malaman da suka san abin da suke yi, wanda ya faxi wannan magana ko waccan.

Ta kuma tabbata cewa kan malamai ma'abuta ilimin hadisi ya haxu a kan cewa, akwai qaryayyaki da yawa a cikin abin da Abu Nu'aimi ke riwaitowa a cikin littafansa: *Al-Hilyatu* ko: *Fala'ilus-Sahabah.* Haka ma cikin abin da Naqqashu da Sa'alabi da Wahidi ke riwaitowa a cikin tafsiri. Sun kuma haxu su malaman can a kan cewa wannan hadisi da Sa'alabi ya riwaito a cikin tafsirinsa, na qarya ne. Nan gaba kaxan za mu bayyana dalilan da muka gano kasancewarsu na qarya ta hanyarsu. Tare da tabbatar da rashin kasancewar Sa'alabi cikin jerin ma'abuta ilimin hadisi.

Amma kafin haka, bari mu ambaci wata qa'ida a nan, wadda ke cewa: Kasancewar ana samun qarya da gaskiya da yawa a cikin riwayoyi, ya sa dole

a koma ga ma'abuta ilimin hadisi, a matsayinsu na rariya uwar tata a fagen, don a rarrabe tsakanin garin taba da na gero. Kamar yadda ake komawa ga malaman nahawu don banbancewa tsakanin Nahawun Larabawa da na Ajamawa. Da kuma yadda ake komawa ga malaman Lugga, don tantance abin da yake mallakar luggar da wanda ba mallakarta ba. Da kuma yadda ake tuntuvar malaman waqa da na Xibbu a kan abin da ya shafe su. Kowane "Allazi" daga cikin ilimi, da nashi "amanu" da aka san shi da shi. Wani ko "kafaru" ake samu gare shi. To, malaman Hadisi su ne mafiya girman daraja a kan sauran malamai. Su ne kuma mafiya gaskiya da xaukakar matsayi, da kishin addini.

**Fuska ta biyu:**

A cikin wannan hadisi da xan Shi'ar ya kawo, akwai abin da ke tabbatar da kasancewar sa qarya, ta fuskoki da dama. Xauki cewar da ya yi: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kasance a Ghadir.. zuwa qarshe, ka dube ta.

Muna tabbatar wa xan Shi'ar cewa, kan gaba xayan mutane ya haxu a kan cewa, duk abin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya faxa a *Ghadir Khum*, nada alaqa ta qud-da-qud da Hajjin bankwana. Har su 'yan Shi'ah sun yarda da hakan. Saboda haka ne ma suka xauki ranar 18 ga watan zul-hajji a matsayin ranar Idi. Annabi kuwa bai sake komawa Makka ba bayan wannan hajji, Ya dai koma ne zuwa Madina bayan kammala aikin. Inda ya ci gaba da rayuwa tsawon sauran kwanakin Zul-hajji da Muharram da Safar. Allah Ya karvi rayuwarsa a farkon watan Rabai'ul Awwal. Ka ji wannan ko?

To, ka tuna xan Shi'ar cewa ya yi a cikin hadisin, bayan wai Annabi ya qare wancan jawabi ga jama'ar da ya tara a *Ghadir Khum*, har maganar ta watsu a cikin garuruwa. Ko kafin Harisu ya kawo masa waccan takakka, har wai ya isa wani wuri da ake kira Abxahu. Ita kuwa Abxahun nan idan ba ka sani ba, a Makka take. To auna wannan magana da ta samanta kaxan. Kai ne alqalin kanka.

Mu a wurinmu, wannan magana qarya ce irin wadda ba mai yin ta sai jahili wanda bai san wurin da ake kira *Ghadir Khum* ba.

Wani abin kuma shi ne: Ita wannan surah da ya ce ta sauka a *Ghadir Khum* kan malamai ya haxu a kan ta sauka ne a garin Makka kafin hijira; shekaru goma ko fiye kafin saukar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a *Ghadir Khum*. To, yaya kuma za a ce ta sauka ne bayan haka?

Ayar da kuwa xan Shi'ar ya ce Sahabi Harisu ya yi amfani da ita, ta sauka ne gab da qare yaqin Badar, kafin qissar *Ghadir khum* da shekaru da dama. Kuma ta sauka ne akan maganganun Abu Jahali da takwarorinsa. Sanannen abu ne dai a wurin malamai cewa, babu wani musulmi da irin haka

ta tava kasancewa tare da shi, na yin fito-na-fito da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Abin al'ajabi a nan, babu wani Sahabi da aka sani da irin wannan suna. Abin da ke qara tabbatar da wannan magana tatsuniya ce.

**Fuska ta uku:**

Abin da matuqar ban mamaki; Ga shi xan Shi'ar na raya cewa sun tabbatar da shugabancin Ali *Raliyallahu Anhu* ta hanyar amfani da waccan aya ta Alqur'ani. Alhali kuwa babu wani abu a cikin ayar da ke nuna haka ko kaxan. Ayar cewa ta yi: *Ka isar da abin da aka saukar zuwa gare ka daga Ubangijinka (5:67).* Wannan lafazi kuwa ya qunshi gaba xayan abin da aka saukar gare shi daga Ubangijinsa; bai taqaita a kan wani abu kevantacce ba.

Duk wanda ya yi iqirarin cewa, sha'anin shugabancin Ali *Raliyallahu Anhu* na daga cikin abin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya isar na manzanci ko aka umurce shi da isarwa, to ya gigice, kuma babu wata aya ta Alqur'ani da zai iya tabbatar da hakan da ita.

**Fuska ta huxu:**

Ta tabbata cewa, idan aka haxa hancin wannan aya, da abin da ake da shi a hannu na tarihin Annabi. Savanin abin da 'yan Shi'ar nan ke faxi, shi ne sakamakon da hakan za ta bayar; cewa dai, Allah bai saukar da ita ayar a kan sha'anin Ali ba. Bai kuma hori Annabi da hakan ba. Don lalle, da hakan na cikin saqonnin da Allah Ya hori Manzon da isarwa, da ya isar da shi; ba zai sava wa Allah ba.

Duk wanda ya zargi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da voye wani abu na wahayi, haqiqa ya yi qarya. Domin kuwa Allah Ta'ala cewa ya yi: *Ya kai Manzo! Ka iyar da abin da aka saukar zuwa gare ka daga Ubangijinka. Kuma idan ba ka aikata ba, to, ba ka iyar da Manzancinsa ba kenan (5:67).* Inji Nana A'ishah.

Irin wannan sha'ani na daga cikin abubuwa masu matuqar muhimmanci a tarihin musulunci, wanda kuma mutune ke da qwarin guiwa, da karsashin ganin sun riwaito shi, in da ya faru. Ko shakka babu da ya tava faruwa da sun riwaito shi, kamar yadda suka riwaito abubuwa masu kama da shi, daga hadisan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Musamman idan aka yi la'akari da irin yadda riwayoyin da ba su da asali, suka yawaita a kan darajojin Ali. Waxanda madubin ilimi ya tabbatar da kasancewar su qarya. Idan kuwa har mutane za su vata lokaci su riwaito irin waxannan qaryace-qaryace, to babu abin da zai hana su riwaito abin da yake na gaskiya da haqiqa kansa, matuqar ya kai kunnuwansu.

Musamman kuma da yake Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya umurci al'ummarsa da isar da abin da duk suka ji daga gare shi. Don haka wannan magana dai baquwa ce. Ga qarin dalili a kan haka:

A lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rasu, wani daga cikin Ansaru ya bayar da shawarar a naxa sarakuna biyu; xaya daga cikinsu, xaya kuma daga cikin Muhajiruna. Aka sa qafa aka haure wannan shawara. Tare da tabbatar masa da cewa, babu yadda za a yi a ce madalla da shugabancin nan matuqar ba a hannun Quraishawa yake ba. Kuma Sahabbai sun riwaito hadisai a wurare da dama, daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* inda yake cewa: *Shugabanci a hannun Quraishawa yake tabbata.*

Har wannan majalisa ta xunkin duniyar musulunci ta ci ta watse, babu wanda ya riwaito wani abu da ke ko ishara zuwa ga shugabancin Ali. Kai ba a ma tava jin haka ba ko a wani zama mai kama da wannan. Qarshe dai musulmi suka yi wa Abubakar mubaya'a. Tattare kuwa da kasancewar a cikinsu akwai da yawa daga cikin banu Abdu-Manafi, Waxanda suka haxa da banu Umayyata da banu Hashimu da wasunsu. Waxanda sun fi son Ali xan Abu-Xalib da kusanta zuwa gare shi fiye da Abubakar. Amma babu xaya daga cikinsu da ya lalabo wannan "nassi". Haka aka yi a zamanin halifancin Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhum.* Kai! Ko lokacin da shi Alin *Raliyallahu Anhu* ya hau gado, ba a ji daga bakinsa, ko na wani daga cikin danginsa, ko na wani daga cikin Sahabbai ba, cewa ya ji wani "nassi" a kan shugabancinsa. Bayan tutar Shi'ah ta fara reto ne aka fara jin xuriyar wannan "nassi".

## 4.3 Ayar Cikar Addini

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Hujja ta uku daga cikin Alqur'ani ita ce: Faxar Allah Ta'ala da Ya ce:

﴿ٱلۡيَوۡمَ أَكۡمَلۡتُ لَكُمۡ دِينَكُمۡ وَأَتۡمَمۡتُ عَلَيۡكُمۡ نِعۡمَتِي وَرَضِيتُ لَكُمُ ٱلۡإِسۡلَٰمَ دِينٗا﴾ المائدة: ٣

*A yau Na kammala muku addininku, kuma Na cika Ni'imaTa a kanku, na kuma yarda musulunci ya zama addini a gare ku (5:3).*

Wai saukar wannan ayar ke da wuya, inji xan Shi'ar sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Girma ya tabbata ga Allah a kan kammala addini da tunfaye ni'ima, da yardar da Ubangiji ya yi da manzancina da kuma shugabanci ga Ali bayan na wuce. Daga nan kuma wai sai ya ce: *Duk wanda na kasance majivinci gare shi, to Aliyu majivincinsa ne. Ya Ubangiji ka jivinci duk wanda ya jivenci shi. Ka qi duk wanda ya qi shi. Ka taimaki duk wanda ya taimake shi. Ka yarvar da duk wanda yarvar da shi.* Qarshen maganar xan Shi'ar kenan.

**Martani:**

Martaninmu a kan wannan magana zai kasance ta fuskoki kamar haka:

**Fuska ta farko:**

Bayyana ingancin wannan hadisi kawai ke iya zama dalili ga wannan xan Shi'ah inda yana yiwuwa. Amma jingina shi kawai ga Abu Nu'aimi a matsayin riwaya, ba ta sa ya zama ingantacce. Abu Nu'aimi dai tun farko bai cikin mariwaitan ingantattun hadissai. A littafinsa kowane iri akwai.

**Fuska ta biyu:**

In ban da a littafin Abu Nu'aimi, wanda ba madogara ne ba, ba inda ake iya samun wannan hadisi daga cikin littafan hadisi da ake dogara da su, ballantana a samar masa wani isnadi ingantacce. Don haka ne ma masana hadisi suka haxu a kan cewa qarya ne.

**Fuska ta uku:**

Abu ne tabbatacce a cikin littafan ilimi cewa, wannan aya ta sauka ne ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a lokacin da yake tsayuwar Arafa. Kuma wani mutum daga cikin Yahudawa ya tava ce wa Umar xan Haxxabi: "Ya kai Sarkin Musulmi! Akwai wata aya a cikin littafinku, wadda kuke karantawa. Da mu Yahudawa aka saukar wa ita, da mun riqi ranar saukar ta, ranar idi". Umar ya ce: "Wace aya ke nan?" Bayahuden ya ce: *A yau Na kammala muku addininku, kuma na cika ni'imata a kanku, kuma Na yarda musulunci ya zama addini a gare ku (5:3).* Sai Umar ya ce masa: lNa kuwa san rana da wurin da wannan aya ta sauka. Ta sauka ne a ranar Arafa kuma a filin, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na tsaye". Dubun dubautar hanyoyi sun tabbatar da wannan riwaya ta Umar.

Kuma ita wannan rana, tana gaban ranar *Ghadir Khum* da kwana tara. Ta kuma kasance ne ranar Juma'a 9 ga watan Zul-Hajji. To, ta yaya wani zai ce ta sauka ne ranar Ghadir?.

**Fuska ta huxu:**

Babu wani abu a cikin wannan aya, da ke iya zama dalili a kan shugabancin Ali, ta kowane hali. Iyakar abin da ta qunsa shi ne, labarin da Allah ya bayar na kammalawarsa ga addini da tunfaye ni'ima ga muminai, da yarda da musulunci ya zama addini. Kenan duk wanda ya yi iqirarin cewa, ta wannan hauji ayar ta zama dalili a kan shugabancin Ali, ya sheqa qarya lafiyayya.

**Fuska ta biyar:**

Addu’ar da xan Shi’ar ya kawo cewa Manzon Allah ya yi, “Ya Ubangiji ka jivinci wanda ya jivinci Ali, ka qi wanda ya qi shi. Ka taimaki wanda ya taimaki shi. Ka yarvar da wanda ya yarvar da shi”. Qarya ce, Annabi bai yi ta ba.

Amma cewa Manzon ya ce: “Duk wanda nake majivinci gare shi, to Aliyu majivincinsa ne”. Malamai nada maganganu biyu a kai. In Allah Ta’ala Ya so za mu ambato su idan lokaci ya yi.

**Fuska ta shida:**

Sanannen abu ne cewa Addu’ar Annabi ba ta faxuwa qasa; da ya yi da Allah Ya qarva. Amma bai karva wannan ba. Wanda hakan ke tabbatar da cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai yi ta ba. Abin da ke tabbatar da haka shi ne, kasancewar Sahabban Annabi da sauran musulmi sun kasu kashi uku a lokacin da Alin ya zama halifa. Wani kashi ya bi shi, ya zamo rundunarsa, wani kuma ya yaqe shi, wani kuma ya shiga tsakani. Mafi yawan nagartattun magabata na cikin wannan kashi na qarshe.

Wani abin mamaki ma shi ne, bai yi nasara a kan waxanda suka yaqe shi xin ba. Hasali ma su suka yi nasara a kansa. Da mulki ya koma hannunsu kuma, suka darzaza suna ta cin garuruwa, suna share kafirai.

Kuma ya zo cikin ingantaccen hadisi cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Wata jama’a ba za ta gushe daga cikin al’ummata ba, tana taimakon gaskiya ta yadda wanda ya sava masu ko ya yarvar da su, ba zai cuta masu da komai ba, har al’amarin Allah ya zo. Ma’azu xan Jabalu ya ce: Suna Sham.

Hakan ko ta tabbata. Domin ba a tava yin nasara a kan rundunar Mu’awiyah ba. A lokacin da suka yaqi Ali ko kafin haka ko bayan haka. Ka ga kenan Annabi bai yi waccan addu’a ba. Don ga shi rundunar Ali ba ta yi nasara kan ta Mu’awiyah ba. Hasali ma duk da ‘yan Shi’ah, waxanda ke jin Ali nasu ne su kaxai, sun kasance audugar kasuwa; ba a tava jin sun yi kaye ba. Duk wata nasara da ka ji sun yi, sun yi ta ne da taimakon wasunsu: Ko dai musulmi ko kafirai. Tattare kuma da iqirarin da suke yi na kasancewa mataimakan Aliyun. Ina taimakon na Allah da zai samu ga wanda ya taimaki Alin?

Wannan hujja kaxai da wasunta, sun isa tabbatar da kasancewar wannan hadisi qarya.

**4.4 Ayar** ﴿وَٱلنَّجۡمِ إِذَا هَوَىٰ ۝١ مَا ضَلَّ صَاحِبُكُمۡ وَمَا غَوَىٰ ۝٢﴾ النجم: ١ - ٢

Xan Shi’ar ya ce: Hujja ta huxu ita ce: faxar Allah Ta’ala: Ina *rantsuwa da tauraron a lokacin da ya faku. Ma’abucinku bai vata ba, kuma bai qetare haddi ba (53:1-2)*. Xan Shi’ar ya ce: Malamin nan masanin fiqihu Aliyu xan magazili, Bashafi’e, ya riwaito daga xan Abbas, wanda ya ce: Na kasance

watarana zaune a wurin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* tare da wasu samari daga cikin banu Hashim. Sai wani tauraro ya faxi. Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Duk wanda wannan tauraron ya faxa gidansa shi ne "Wasiyyina"; wanda zai gade ni, idan na qaura. Sai kawai waxannan samari suka tashi, suka bi sawun tauraron. Sai kawai suka taras ya faxa gidan Ali *Raliyallahu Anhu,* suka dawo suka gaya wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa: Haqiqa ka vace a cikin son Ali. Nan take kuma sai Allah Ta'ala Ya saukar da waxannan ayoyin.

**Martani:**

Martaninmu a kan wannan magana zai kasance ta fuskoki kamar haka:

**Fuska ta farko:**

Muna son xan Shi'ar ya tabbatar mana da ingancin wannan magana, kamar yadda muka saba. Domin kuwa nassi da ijma'i sun tabbatar cewa, magana a kan jahilci haramun ce.

Allah Ta'ala na cewa:

﴿ وَلَا تَقْفُ مَا لَيْسَ لَكَ بِهِۦ عِلْمٌ ﴾ الإسراء: ٣٦

*Kuma kada ka bi abin da ba ka da ilimi game da shi (17:36).*

Ya kuma ce:

﴿ قُلْ إِنَّمَا حَرَّمَ رَبِّيَ ٱلْفَوَٰحِشَ مَا ظَهَرَ مِنْهَا وَمَا بَطَنَ وَٱلْإِثْمَ وَٱلْبَغْيَ بِغَيْرِ ٱلْحَقِّ وَأَن تُشْرِكُوا۟ بِٱللَّهِ مَا لَمْ يُنَزِّلْ بِهِۦ سُلْطَٰنًا وَأَن تَقُولُوا۟ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعْلَمُونَ ﴿٣٣﴾ ﴾ الأعراف: ٣٣

*Ka ce; Abin sani kawai, Ubangijina Ya hana abubuwan alfasha; abin da ya bayyana daga gare su da abin da ya voyu da zanubi da cin zalun jama'a ba da wani haqqi ba, kuma da ku yi shirka da Allah, ga abin da bai saukar da wani dalili ba gare shi, kuma da ku faxi abin da ba ku sani ba, ga Allah (7:33)*

Duk abin da manzanni suka zo da shi daga wurin Allah dalili ne. Amma dalilin ba ya zama hujja sai an san shi ta hanya ingantatta. Saboda haka duk wanda zai kafa hujja da wani abu da aka ce an samo daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* to wajibi ne a kansa ya tantance ingancinsa, kafin ya qudurta shi, ko ya yi aiki da shi, balle ya kafa hujja akan mutane. Kuma ko ya inganta, lalle ne a duk lokacin da ya kafa wa wani hujja da abin, to ya yi masa bayanin yadda aka yi ya inganta. Idan kuwa ya kasa yin haka, to ya zama, malam ba ka da hujja.

Ka ga a haka ba ta yiwuwa ko alama, a kafa hujja a kan wani abu da ya shafi tushen addini da hadisin da ba a san ingancinsa ba. Musamman idan ya kasance, yarda da shi na haifar da zubewar mutuncin zavavvun mutane.

Shi dai wannan xan Shi'ah da za a turke shi, a kan ya faxi lokacin da wannan abu ya faru, ba zai iya ba. Ko ya ce zai iya kuwa qarya yake yi don bai sani ba. Kamar yadda, da za a karva masa cewa: Eh, tafi mun ji, ba ka san lokacin ba. To, faxa mana yadda ka gane cewa riwaya ce ingantatta? Wannan ma ba zai iya ba. Don iya gane haka abu ne da ke da buqatar cikakkiyar masaniya da tarihin mariwaita. Shi kuwa jahili ne a wannan fage. Da kuwa yana da masaniya da halayensu, da ya riga kowa gane cewa wannan hadisi qarya ne.

Idan kuwa har aka yi sa'a tashin fari, ya ce: Ban san komai ba game da hadisin. To, tambayar da za a kashe shi mari da ita ita ce: To don me za ka kafa hujja da abin da baka san ingancinsa ba?

Abu na biyu kuma shi ne, magazili kansa, ba masanin hadisi ne ba. Haka yake kamar Abu Nu'aimi da takwarorinsa. Kuma ba ya cikin masu kawo hadissan qwarai. Hanyarsu xaya da Sa'alabi. Magazili asalatan hadisi ba safararsa ba ne. Ya dai kawai far ma abubuwan da wasu mutane suka tattara ne a cikin littafai, na darajoji da falalolin Ali, ya harhaxa ya rubuta. Kamar yadda Akhdabu Khuwarizm ya yi. Babu xaya daga cikinsu da ya san hadisi. Abubuwan da kowanensu ya riwaito cike yake da Gizo da Qoqin Hadisai. Irin waxanda ko xan sharar makarantar hadisi, na iya gane su.

**Fuska ta uku:**

Wani kuma abin da ke tabbatar da kasancewar wannan hadisi qarya, shi ne cewa xan Abbas ya shedi saukar Suratun-Najmi, bayan da tauraron ya faxa gidan Ali *Raliyallahu Anhu*. Alhali kuwa wannan sura na daga cikinsurorin farko da suka sauka a Makka. Shi kuwa xan Abbas ko da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya cika bai balaga ba, yana matashi. Wannan shi ya tabbata a cikin Buhari da Muslimu, daga bakinsa.

Ka ga kenan, lokacin da wannan aya ta sauka, ko dai ya kasance ba a haifi xan Abbas xin ba sam-sam-sam, ko kuma yana yaro, irin wanda ba ya iya gane komai. Domin kuwa ko lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi hijira, shekarun xan Abbas ba su wuce biyar ba. A kan haka abu mafi zama kusa da gaskiya shi ne, ko da wannan aya ta sauka, ba a haifi xan Abbas ba. Tunda tana daga cikinsurorin farko da suka sauka na Alqur'ani.

**Fuska ta huxu:**

Babu inda tarihi ya nuna tauraro ya tava faxowa qasa a Makka ko Madina, ko wasu garuruwa kusa da su. Eh, gaskiya ne, lokacin da aka aiko Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ana yawaita jifa da taurari. Amma duk da

haka ba a samu cewa, tauraro ya tava saukowa qasa ba. Da hakan ta zama wani abu na keta hankali, kuma sananne a duniya. Hasali ma kai! Wani abu ne da bai tava faruwa a faxin duniya ba, balle ya zama abin kakabi. Kuma babu ma wanda irin wannan labari zai riqa fitowa bakinsa sai mafi wauta daga cikin mutane, wanda kuma ya ce wa musailamu cas; saboda cikar rashin kunya da wasa da addini. Kamar kuma yadda babu wanda zai saurare shi, balle har ya yarda da shi, sai mafi jahilci da wauta daga cikin mutane, wanda ke da wayewa da ilimin da ba su cika cikin cokali ba.

**Fuska ta biyar:**

A lokacin saukar wannan sura ta *Najmu* Aliyun kansa yaro ne qarami da bai ko balaga ba, balle a yi zancen aurensa da Nana Fatima. Kuma a lokacin ba a ko farlanta sallah ba, a cikin sigarta ta raka'o'i huxu da uku da biyu. Haka kuma ba a farlanta zakka ko hajji, ko azumi, da sauran muqarraban qa'idojin musulunci ba.

Shi kuwa zancen zaven wani a matsayin Yarima mai jiran gadon Annabci, in har hakan abu ne karvavve, kamata ya yi ya kasance bayan komai ya kammala. Kamar dai yadda suka kitsa tatsuniyar *Ghadir Khum*. Ka ga ko a kan haka, ba gaskiya ba ne a ce abin ya faru a wancan lokaci.

**Fuska ta shida:**

Abin da malaman tafsiri suka haxu a kai, dangane da sha'anin wannan aya, ya sava ma wannan tatsuniyar ta 'yan Shi'ah. Domin su cewa suka yi, wannan tauraro da Allah *Subhanahu WaTa'ala* Ya yi rantsuwa da shi a farkon surar, ko dai yana nufin tauraro daga cikin taurarin sama ko na Alqur'ani. Babu wanda ya ce wani tauraro ne da ya sauka a gidan wani a Makka.

**Fuska ta bakwai:**

Ko shakka babu duk wanda ya ce wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya vace, kafiri ne. To, kafirai Annabi yake horo da riqon Ali a matsayin halifansa, ko su yake bar wa wasicci da shi?

**Fuska ta takwas:**

Idan kuma har wancan tauraro da xan Shi'ar ya ce ya sauka a gidan Ali, aradu ce ta faxa gidansa. To, saukar aradu a gidan mutum ai ba karama ba ce. Idan kuwa ya ce tauraron sama ne, to, ai taurarin sama ba su faxowa. Idan kuwa yula ce, to, shexanu a kan jefa da ita.

To, ko da za mu qaddara cewa, shexanin da aka jefa ne ya sheqa gidan Ali xauke da wutar, to, ai wannan ba wani abu ne da ke nuna xaukakarsa ba. Balle ma dai hakan ba ta tava faruwa ba.

### 4.5 Ayar Tsarkake Ahlul-Baiti

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta biyar ita ce: Faxar Allah Ta'ala da ya ce:

﴿إِنَّمَا يُرِيدُ ٱللَّهُ لِيُذۡهِبَ عَنكُمُ ٱلرِّجۡسَ أَهۡلَ ٱلۡبَيۡتِ وَيُطَهِّرَكُمۡ تَطۡهِيرٗا ٣٣﴾ الأحزاب: ٣٣

*Allah Na nufin Ya tafiyar da qazanta ne kawai daga gare ku, ya mutanen Babban Gida! Kuma ya tsarkake ku, tsarkakewa. (33:33).*

Ahmad xan Hambali, inji shi, ya riwaito a cikin Musnadinsa daga Wasilatu xan Asqa'u, wanda ya ce: Na tafi neman Aliyu a gidansa. Sai Fatima *Raliyallahu Anha* ta ce: Ya tafi wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.* Sai ga su sun dawo tare. Suka shigo, ita kuma ta shigo tare da su. Sai Ya zaunar da Aliyu dama gare shi. Fatima kuma a hagu. Hassan da Husaini kuma a gabansa. Sannan ya kundume su cikin mayafinsa, ya karanta wannan aya. A qarshe ya rufe da cewa: "Ya Allah! Ka sheda, haqiqa waxannan su ne mutanen gidana".

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: An samo daga Ummu Salamata, wadda ta ce: "Watarana Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* na cikin gidansa sai ga Nana Fatima *Raliyallahu Anha* ta shigo xauke da wata tukunyar qarfe, a cikinta da tuwon vula, ta isa da ita wurinsa. Sai ya ce mata: Koma ki kira mani maigidanki da 'ya'yanki biyu. Nan take sai ga Aliyun da Hasan da Husaini sun iso, suka kuma shigo suka zauna suna cin wannan tuwo. Da shi da su, a lokacin duk suna kan wani mashinfixi nasa. Wanda a qarqashinsa akwai wani bargo Bahaibare".

Ta ci gaba da cewa: Ni dai ina cikin xaki sai na ji Allah Ta'ala ya saukar da waccan aya. Qare saukar ta ke da wuya, sai kawai ya ja sashen bargon ya lulluve su da shi. Sannan ya xaga hannuwansa ya ce: Waxannan su ne mutanen gidana. Allah ka tafiyar da qazanta daga gare su, ka tsarkake su, tsarkakewa. Yana yi yana maimaitawa. Ta ce, sai na kutsa kaina cikinsu na ce: Ni ma ina daga cikinsu ya Manzon Allah. Sai ya ce: Ina dai yi miki fatar alheri.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Akwai dalili a cikin wannan aya na ma'asumancin Ali. Musamman da aka qarfafa maganar da lafazin "kawai" da saka harafin "Lam" a cikin bayanin Jumlar. Da kuma kevancewa a cikin zancen, ta hanyar amfani da "Ahlul-baiti" (Mutane Babban gida). Da kuma nanata maqasudin maganar, cewa: Ya kuma tsarkake ku. A qarshe kuma aka qara qarfafa ta da "tsarkakewa". Wannan na nuna ba wani ma'asumi bayansu, inji shi. Saboda haka sai Ali ya zama shugaba. Musamman ma da yake ya sha iqirarin haka, a wurare da dama. Kamar inda ya ce: "Wallahi xan Abu Quhafata (Abubakar) ya karvi halifanci ne kawai. Amma ya san matsayina gare ta matsayin rai ne a cikin gangar jiki". Kuma tunda har tsarki ya tabbata

gare shi, ba zai faxi qarya ba. Ka ga kenan shi ne wanda ya cancanci shugabancin.

To, bari mu duba wannan magana tasa. Shi dai wannan hadisi haka yake. Kuma babu shakka wannan labari ya faru. Nana A'ishah *Raliyallahu Anha* na da riwaya ga wannan labari. Ga abin da ta ce kamar yadda ya zo a cikin Sahihu Muslim: "Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fita watarana da hantsi, yana yafe da wani gwado mai kauri, wanda aka saqa shi da baqin gashi. Sai ga Hasan xan Aliyu ya zo, sai ya shigar da shi cikinsa. Sannan kuma Husaini ya zo, shi ma ya shigar da shi. Sai kuma ga Nana Fatima ta zo, ita ma ya shigar da ita. Can kuma sai ga Ali ya zo, shi ma ya shigar da shi. Sa'annan ya ce: *Allah na nufin ne ya tafiyar da qazanta daga gare ku ya ku mutanen Babban Gida, kuma Ya tsarkake ku, tsarkakewa (33:33).*

Wannan hadisi sananne ne, musamman ta hanyar Ummu Salamata wadda ta zo cikin littafin Ahmad da na Tirmizi. Amma dai duk da haka, babu wani dalili a cikin hadisin da ke nuna kasancewar waxancan mutane ma'asumai, ko shugabanni. Ballantana abin da zai keve Ali shi kaxai ba tare da Fatimar ba.

Da farko dai, waccan aya daidai take da xaya ayar wacce Allah ya ce a cikinta:

﴿مَا يُرِيدُ ٱللَّهُ لِيَجْعَلَ عَلَيْكُم مِّنْ حَرَجٍ وَلَٰكِن يُرِيدُ لِيُطَهِّرَكُمْ وَلِيُتِمَّ نِعْمَتَهُۥ عَلَيْكُمْ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴿٦﴾﴾ المائدة: ٦

*Allah ba Ya nufin domin Ya sanya wani qunci a kanku (5:6)*

Daidai kuma take da cewar da Allah ya yi:

﴿يُرِيدُ ٱللَّهُ بِكُمُ ٱلْيُسْرَ وَلَا يُرِيدُ بِكُمُ ٱلْعُسْرَ﴾ البقرة: ١٨٥

*Allah Yana nufin sauqi a gare ku, kuma ba ya nufin tsanani a gare ku (2:185).*

Haka kuma daidai take da cewar da ya yi :

﴿ يُرِيدُ ٱللَّهُ لِيُبَيِّنَ لَكُمْ وَيَهْدِيَكُمْ سُنَنَ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكُمْ وَيَتُوبَ عَلَيْكُمْ ۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ﴿٢٦﴾ وَٱللَّهُ يُرِيدُ أَن يَتُوبَ عَلَيْكُمْ وَيُرِيدُ ٱلَّذِينَ يَتَّبِعُونَ ٱلشَّهَوَٰتِ أَن تَمِيلُوا۟ مَيْلًا عَظِيمًا ﴿٢٧﴾﴾ النساء: ٢٦ - ٢٧

*Allah Yana nufin ya bayyana muku, kuma Ya shiryar da ku hanyoyin waxanda suke gabaninku kuma Ya karvi tubar ku. Kuma Allah masani ne mai hikima. Kuma Allah Yana nufin*

*Ya karvi tubarku. Kuma waxanda suke bin sha'awowi suna nufin ku karkata, karkata mai girma (4:26:27)*

Wannan kalma ta "Nufi" da aka yi ta nanatawa a cikin waxannan ayoyi, aka kuma danganta ta ga Allah Ta'ala, abin da take nufi shi ne: Allah na son abin nan da ya yi nufi, kuma ya yarda da shi. Ya kuma shar'anta shi ga muminai, tare da umurnin su da aikata shi. Kalmar ba ta nuna Allah Ya riga ya tabbatar da kasancewar abin da ya biyo bayanta, koko ba makawa sai hakan ta faru.

Babban dalili a kan haka shi ne, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai wadatu da saukar ayar kawai ba, sai da ya roqi Allah da cewa: "Ya Ubangiji waxannan su ne mutanen gidana, ka tafiyar da qazanta daga gare su, ka kuma tsarkake su, tsarkakewa". Ka ga wannan roqon tabbatuwar waxancan abubuwa ne yake yi a wurin Allah. Da ayar na nufin abubuwan sun riga sun tabbata, to, ba sai ya yi roqo da fadanci ba. Don babu buqatar haka. Saboda bakin alqalami ya riga ya bushe.

Da kuma 'yan Shi'ah za su ce mana: Eh, to mun ji waccan aya ta Alqur'ani ba ta nufin tababatuwar wancan nufin da Allah ya yi na tsarkakewa da tafiyar da qazanta. To, amma ai addu'ar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi masu na nuni ga haka. Domin kuwa addu'arsa ai ba ta faxuwa qasa ko? Sai muce: Iyakar abin da muke son tabbatarwa a nan shi ne: Shi dai Alqur'ani ba ya xauke da wani abin da ke nuna tababatuwar abin can da xan Shi'ar ke iqirari na tsarkakewa da tafiyar da qazanta. Balle ya tabbatar da ma'asumancin Ali ko shugabancinsa. Shi kuwa riqon hadisi a matsayin dalili, wani abu ne daban.

## Mataki na biyu:

Mu xauka cewa Alqur'ani ya tabbatar da tsarkinsu da tsirarsu daga qazanta. Kuma waccan addu'a da Annabi ya yi karvavva ce; dole ne abin da ta kunsa na tsarki da tsira daga qazanta xin can ya tabbata. Babu wani abu a cikin haka da ke nuna kuvuta daga aikata kuskure. Dalili kuwa shi ne: Umurnin da Allah ya yi wa matan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba ya nufin sun kuvuta daga aikata kuskure. Hasali ma kuskure abin gafartawa ne ga kowa; har su. Abin da salon tafiyar ayar ke nunawa shi ne: Allah na nufin ya tafiyar da qazantar varna da alfasha daga gare su, ya kuma wanke su tsabal daga kowane irin zunubi.

A taqaice dai "tsarkakewa" da Allah ke nufi, kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya roqa ba ta nufin ma'asumanci ittifaqan. A wurin Ahlus-Sunnah babu wani ma'asumi sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. A ya yin da su kuma 'yan shai'a suke cewa: Ba wani ma'asumi baya ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Imami. Ka ga kenan an samu haxuwar kai a kan cewa wancan ma'asumancin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da

Imamai suke kevanta da shi, ya koru daga mata da 'ya'ya mata na Annabin, da ma wasu matan ba su ba.

Idan kuwa haka ne, kenan wancan tsarki da xan Shi'ar ke iqirari, wanda mutanen can huxu suka samu, bai qunshi kasancewarsu ma'asumai ba, irin wancan ma'asumanci da 'yan Shi'ar suka tabbatar kawai ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Imamu. Kuma waccan addu'a da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi babu wannan ma'asumanci a cikinta; bai roqa wa Ali ko waninsa ita ba. Ya dai kawai roqi Allah ne ya tsarkake su su huxu gangame; bai kevance kowa daga cikinsu da addu'ar ba.

Game kuma da cewar da ya yi wai: Aliyu ya yi iqirarin kasancewarsa mafi cancanta da halifanci. Kuma tun da har tsarkakakke ne daga qazanta, duk abin da ya faxi gaskiya ne, to, ga amsa:

Tun farko mu, ba mu yarda da Aliyu ya yi wannan magana ba. Domin kuwa muna da cikakkar masaniya da cewa, har zuwa lokacin da aka yi wa halifa Usmanu kisan gilla Aliyu *Raliyallahu Anhu* bai yi wannan furuci ba. Ko da kuwa yana da sha'awa a cikin zuciyarsa na son ganin ya zama halifa. Amma bai tava yin wata kalma mai nuna yana da wani wasicci daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na zama halifa ba da xai.

Mun riga mun sakankance da cewa, duk wanda ya ce Aliyu *Raliyallahu Anhu* ya tava faxar wata magana mai kama da waccan, to ya xauki alhakinsa. Sanin da muke da shi, na kasancewar Ali *Raliyallahu Anhu* mai tsaron Allah, ba za ta bari ya furta abin da ba gaskiya ba. Kuma abin da gaba xayan shababai suka san qarya ne.

Kuma cewa matsayin Ali *Raliyallahu Anhu* ga halifanci kamar matsayin rai ne ga gangar jiki. Kuma wai, Abubakar ya san da haka, ba magana ba ce. Domin kuwa ina aka samo ta? Da za a yi shekarun Abarshi ana bincike ba za a samar wa wannan magana gindin zama ba. Ba inda aka same ta sai cikin *Nahjul-Balaga* da ire-irensa. Littafin da malamai sun san mafi yawan abin da ke cikinsa ba komai ba ne face zuqi tamallau.

Ya za a kafa hujja da wannan hikaya, wadda sai bayan shekaru xari huxu da rasuwarsayyidina Ali aka fara jin xuriyarta? Lokacin da masu qarin gishiri a cikin tarihi suka yawaita. Saboda gari nasu; sun kafa daula ta kansu, wadda ke karvar duk abin da suka faxa; ko gaskiya ne ko qarya. Babu wanda ke turke su a wannan lokaci ya ce sai sun tabbatar da ingancin abin da suka faxa.

Muna nanata cewa, ba mu yarda Ali ya faxi waccan magana ta wasicci ba. Amma idan kun nace ya faxa bayan ta tabbata qarya, to, sai ku faxa mana in qarya ba ta cikin ababen qazanta da aka tafiyar masa.

Wannan bisa ga taku fassara ta tabbatar da tafiyar da qazantar, ba nufi kawai ba. Babu kuwa wani abu a cikin Alqur'ani da ke tabbatar da tafiyar da

qazantar, ko kasancewar qarya da kuskure cikin ayarinta, koko tabbas Ali ya faxi waccan magana. Duk abin da za a faxa don qoqarin tabbatar da kasancewar waxannan riya ce-riya ce gaskiya, kame-kame ne kawai, babu su cikin Alqur'ani. Balle har a ce ga wata hujja cikinsa da ke tabbatar da shugabancin Ali.

### 4.7 Ayar:

﴿ فِي بُيُوتٍ أَذِنَ ٱللَّهُ أَن تُرۡفَعَ وَيُذۡكَرَ فِيهَا ٱسۡمُهُۥ يُسَبِّحُ لَهُۥ فِيهَا بِٱلۡغُدُوِّ وَٱلۡأٓصَالِ ﴿٣٦﴾
رِجَالٞ لَّا تُلۡهِيهِمۡ تِجَٰرَةٞ وَلَا بَيۡعٌ عَن ذِكۡرِ ٱللَّهِ وَإِقَامِ ٱلصَّلَوٰةِ وَإِيتَآءِ ٱلزَّكَوٰةِ يَخَافُونَ يَوۡمٗا تَتَقَلَّبُ فِيهِ
ٱلۡقُلُوبُ وَٱلۡأَبۡصَٰرُ ﴿٣٧﴾ ﴾ النور: ٣٦ - ٣٧

Hujja ta shida, inji xan Shi'ar ita ce: Faxar Allah Ta'ala:

> *Akwai wasu mazaje a cikin gidajen da Allah ya yi umurnin a xaukaka, kuma a ambaci sunansa a cikinsu, suna yin tasbihi a gare shi, safe da maraice. Kasuwanci ko ciniki ba su xauke musu hankali daga ambaton Allah da tsayar da sallah da bayar da zakka. Suna tsoron wunin nan da zukata da gannai ke firgita a cikinsa (24:36-37).*

Xan Shi'ar ya ce: Sa'alabi ya ce, ta wani isnadi daga Anas da Buraidata, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya karanta wannan aya, sai wani mutum ya miqe tsaye ya ce: "Waxanne gidaje ne waxannan ya Manzon Allah?" Sai ya ce: "Gidajen Annabawa". Wai sai Abubakar ya miqe tsaye ya ce: "Ya Manzon Allah! Ko gidan Ali na daga cikinsu?" Sai ya karva masa da cewa: "Eh. Shi ne ma mafi girmansu, saboda an siffanta wasu maza da ke cikinsa, da wani abu da ke nuna fifikonsu". Saboda haka sai Aliyu ya kasance shi ne shugaba. Idan ko ba haka aka yi ba, to hakan za ta wajabtar da gabatar da maqasqanci a kan mafifici.

### Martani:

Kafin komai, muna neman wannan marubuci ya tabbatar mana da ingancin wannan riwaya. Domin kuwa kan Ahlus-Sunnah da na Shi'ah ya haxu a kan cewa, jingina magana kawai ga Sa'alabi ba ya zama hujja. Domin Sa'alabi na cikin malaman da ke amsa sunan sunnah kawai bai isa hujja a kan karva duk maganarsa ko da kuwa tana maganar darajar halifa Abubakar ne, sai fa in an tabbatar da ingancinta. Kamar dai xan Shi'ar yana son ne ya ce, ga wani malami nan daga cikinku na kafa muku hujja da shi, don ya faxi abin da ya zo daidai da ra'ayina. To, ai Ahlus-Sunnah gaskiya suke bi ba malamai ba.

To. Ta ya ya riwayar fataken dare mai maqoshin kolo a riwaya, wanda ke yaki halas yaki haram; da sahihi da la'ifi duk hajarsa ce take zama hujja akanmu?

Kuma kasancewar wannan hadisi qarya, a idon masana, shi ya sa malaman hadisi ba su ambace shi a cikin littafansu waxanda ake dogara da su ba. Tattare kuwa da cewa, waxansunsu kan xan yi sassafci wani lokaci a kan riwayar masu rauni. Kai wasu ma ana da tabbacin har na qage akwai a cikinsu; sai dai su ne mafi qanqanta a adadi. Amma duk da haka, da za ka ba su warqa-warqa, ba za ka tsinci wannan hadisi da makamantansa a ciki ba. Saboda qaryarsu ta vaci. Ta yadda ba su ambatuwa a cikin irin waxancan kundaye.

Malamai sun haxu a kan cewa wannan aya na magana ne a kan masallaci. Babu kuma wani gida; na Aliyu ko na wani da ya siffanta da waxannan siffofi. Duk musulmi sun aminta cewa, gidan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fi na Aliyu daraja, amma ba su ce, wannan aya shi take nufi ba. Kuma babu ma wasu maza a cikin gidan nasa; sai shi xaya, da matan da ke ciki. Shi ya sa lokacin da Allah ya yi magana a kan abin da ya shafi gidan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa ya yi: *Kada ku shiga xakunan Annabi (33:53).* A wani wurin kuma ya ce wa matan Manzo: *Kuma ku tuna abin da ake karantawa a cikin xakunanku (33:34).*

A cewar xan Shi'ar, kenan duk sauran muminai ba su da wani rabo a cikin ayar. Alhali kuwa wanda ya dubi ayar da kyau zai ga cewa, duk wanda ya siffanta da abubuwan da ta faxa to, yana cikin ta.

Bayan haka kalmar "gidaje" da Allah Ya ambata a cikin ayar, Ya ce kuma Ya yi umurni da a xaukaka su, a kuma ambaci sunansa a ciki, idan yana nufin wata ibada ne ta daban da masallatai ba su kevanta da ita ba; Wato yin zikiri da wasu nafiloli a gida ba masallaci ba, to, duk gidajen muminai na karva wannan sunan, ba ma sai gidajen Annabawa kawai ba, ballantana na Aliyu.

Idan kuwa tana nufin ibadar da masallatai suka kevanta da ita. Kamar sallolin farilla da ba a yi sai a cikin masallatan, to, ai gidan Aliyu ba masallaci ba ne. kuma a haka duk da darajar gidajen Annabawa da kasancewar su Annabawan na zaune a cikinsu ba za su shiga a cikin ayar ba kenan.

To, bisa ga wancan hadisi da ya kawo cewa, ayar tana nufin "Gidajen Annabawa" babu wani gida na wani Annabi a Madina, bayan gidan da matansa *Sallallahu Alaihi Wasallama* ke zaune. Kenan ba maganar gidan Aliyu *Raliyallahu Anhu*. Idan kuma suka ce, ai ana nufin gidan da wani Annabi ya taka qafarsa, to, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya shiga gidajen da yawa daga cikin Sahabbai, ba na Aliyu kawai ba.

Duk yadda aka kaxa aka raya, ba yadda za a yi a tabbatar da cewa hadisin na nufin gidan Ali a kevance, a matsayinsa na xaya daga cikin gidajen Annabawa ba tare da na takwarorinsa da magabatansa daga cikin Sahabbai ba.

### 4.7 Ayar Mawaddah

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta bakwai ita ce: Faxar Allah Ta'ala:

﴿قُل لَّآ أَسۡـَٔلُكُمۡ عَلَيۡهِ أَجۡرًا إِلَّا ٱلۡمَوَدَّةَ فِي ٱلۡقُرۡبَىٰۗ﴾ الشورى: ٢٣

*Ka ce: Ba ni tambayar ku wata sakayya a kansa, face dai soyayya a cikin zumunta (42:23).*

Ahmad xan Hambali ya riwaito, inji xan Shi'ar, a cikin Musnadinsa daga xan Abbas, wanda ya ce: Lokacin da ayar ta sauka Sahabbai sun tambayi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da cewa: Su wane ne makusantanka waxanda soyayyarsu ke wajaba a kanmu? Ya ce: Aliyu da Fatima da 'ya'yansu biyu. Haka zancen ya zo a cikin tafsirin Sa'alabi, in ji shi. Akwai kuma kwatankwacinsa a cikin Buhari da Muslimu. Babu kuwa wani daga cikin Sahabbai bayan Aliyu da iyalan nasa, da son su ke wajabta. Kenan Ali shi ne mafifici a girman daraja, sai ya kasance shugaba. Sava masa na nuna rashin son sa, kamar yadda xa'a ga umurninsa ke tabbatar da ana son sa. Kenan wajibi ne a yi masa xa'a. wannan kuwa shi ne zama shugaba.

### Martani:

Da farko muna son wannan xan Shi'ar ya tabbatar mana da gaskiyar wannan hadisi. Sannan kuma muna tabbatar masa da cewa, Ahmad bai riwaito wannan hadisi a cikin Musnadinsa ba. To, ballantana Buhari da Muslimu. Kai abin da ma ke cikin waxannan littafan na takin saqa ne da hadisin da ya kawo xin. Amma ba mamaki, domin mun san bai san waxannan littafai ba, yana dai amsa kuwwar wasu da ya ji sun faxa ne kawai.

A wurin malamai wannan hadisi qarya ne. Ahlus-Sunnah kuma sun yi ittifaqi a kan cewa Suratus-Shura da wannan aya take cikinta, ta sauka ne a Makka. Da duk wata sura da ke farawa da haruffa. Kowa kuwa ya san Ali bai auri Nana Fatima ba a Makka. Ko a Madinar ma sai bayan yaqin Badar. Ka ga kenan wannan aya ta girmi Hassan da Husaini da shekaru. To, ta yaya za a ce Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fassara wannan aya da wajabcin soyayya ga wasu makusanta da Allah bai riga ya halitta ba, balle har a san su a so su?!

Tafsirin wannan aya, da ke cikin Buhari da Muslimu, wanda aka samo daga xan Abbas ya sava ma abin da wannan xan Shi'ah ya faxa. Abin da ya zo a cikinsu shi ne, cewar da Sa'idu xan Jubairu ya yi: An tambayi xan Abbas a kan ma'anar wannan aya, sai na yi farat na ce: "Tana nufin kada ku rava ga makusantan Muhammadu ku cutar da shi". Sai xan Abbas ya ce: "Ka yi gaugawa. Ai ba wani gida na Quraishawa face Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* nada dangi a ciki". Ya ci gaba da cewa: "Ayar na nufin: Ba ni

tambayar ku wata sakayya a kansa. Amma ina roqon ku da ku dubi zumuncin da ke tsakanina da ku".

To, ka ji ta bakin xan Abbas; masanin Alqur'ani. Kuma mafi ilimi daga cikin Ahlulbaiti, bayan Ali *Raliyallahu Anhu*. Kuma wannan ita ce fassara, ba fassarar xan Shi'ar ba. Domin soyayya a cikin zumunta ya ce, ba ga zumu ba.

Abin lura a cikin wannan al'amari shi ne, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba ya neman wani sakamako daga kowa, a kan saqon da yake isarwa na Ubangijinsa, har abada. Ladarsa na wurin Allah. Kamar yadda ya ce: *Ka ce, "Ba ni tambayarku wata sakayya a kansa kuma ba ni daga masu qaqalan faxarsa (39:36).* Da kuma inda ya ce: *Shin kana tambayar su wata sakayya ne, saboda haka suka zama masu jin nauyin biyan tarar? (52:40)* Da kuma inda ya ce: *Ka ce, "Abin da na roqe ku na wani sakamako, to amfaninsa naku ne. Sakayyata ba ta ko ina sai a wurin Allah, (54:47).*

Irin togiyar da ke cikin wannan aya ita malaman lugga ke ce ma yankakkiya, saboda banbantar farkon maganar da qarshenta. Kamar yadda Allah ya ce: *Ka ce, "Ba ni tambayar ku wata sakayya a kansa sai dai wanda ya so riqa wata hanya zuwa ga Ubangijinsa (25:57).* Riqa wata hanya zuwa ga Ubangiji ba sakayya ce ga Manzo ba, haka ita ma qaunar sa saboda zumunta ba sakayya ce garai ba.

Amma fa kar ka zaci muna so ne mu kore wajabcin nuna soyayya ga Ahlul-Baiti. Ko kaxan. So da qaunar mutanen gidan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* wajibi ne. Amma ba da wannan aya, wannan wajabci ke tabbata ba. Kuma wannan soyayya ba ita ce ladar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Tana dai daga cikin abubuwan da Allah Ya hore mu da su, kamar yadda Ya hore mu da sauran ibadodi. Duk kuwa wanda ya xauki wannan soyayya ta mutanen Babban Gida, a matsayin wani abu da zai saka wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da shi na lada, to haqiqa ya tafka kuskure, mai girma. Kuma inda a ce haka ne, to da mu ba wata sakayya ta lada da za mu samu a kan haka. Domin kuwa abin da ya cancanta da shi ne, na lada a kan isar da manzancinsa muka ba shi.

Ita kuwa cewar da xan Shi'ar ya yi wai jivintar halifofi uku na kafin Ali bai wajaba ba, ba gaskiya ba ne. Domin kuwa ai ta tabbata cewa Allah na son su. Duk kuwa wanda Allah ke so, to, ya zama wajibi a kan kowane musulmi ya so shi. Domin son wanda Allah ke so, da qin wanda Allah ke qi wajibi ne. Hasalima ma ha kanshi ne igiya mafi qarfi daga cikin yaggwan imani. Kuma su waxancan halifofin, suna daga cikin manya-manyan waliyan Allah masu taqawa, irin waxanda Allah Ya wajabta jivinta. Kai ta ma tabbata a nassin Alqur'ani cewa Allah Ya yarda da su, su kuma sun yarda da shi. Duk kuwa wanda Allah Ya yarda da shi, to, lalle ko yana son sa. Daga nan zaka gane cewa, son halifofi uku na farko da jivintar su ya fi zama wajibi a kan son Ali da

jivintar sa shi kaxai. Domin wajabcin so da jivinta na tafiya ne daidai da xaukaka. Su ko sun fi shi xaukaka babu shakka.

Cewar da xan Shi’ar ya yi wai, sava wa Ali na nuna rashin son sa. Kamar yadda xa’a ga umurninsa shi ne son nasa. Daga nan ya fitar da wajabcin yi masa xa’a da zamowar sa shugaba. Sai mu ce: Idan dai har soyayya na wajabtar da xa’a kamar yadda xan Shi’ar ya ce, to, ai soyayyar ma’abuta kusancin can ta wajaba ko? Kenan su ma wajibi ne a yi masu xa’a. A kan wannan ma’auni kenan wajibi ne musulmi su naxa Fatima *Raliyallahu Anha* halifanci. Idan kuwa har yin hakan vata ne. To kuwa ko hakan can vata ne.

Abin da ya kamata mu sani shi ne, so da qauna ba su wajabtar da kasancewar wanda ake yi wa su shugaba nan take, ta yadda da zarar son mutum ya wajaba, sai a naxa shi shugaba. Ai son Hassan da Husaini wajibi ne tun kafin su zama shugabanni. Shi ma Ali *Raliyallahu Anhu* son sa wajibi ne tun Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* na raye, ga shi ko bai zama shugaba ba. Amma dai wajabcin son sa na nan duk kuwa da jinkirin da shugabancin nasa ya yi har zuwa bayan kashe Usman.

Wannan na tabbatar da cewa, abin da ke tsakanin ‘yan Shi’ah da Ahlus-Sunnah daidai yake da wanda ke tsakanin Kirista da Musulmi. Kirista sun ce Masihu Allah ne. Amma Ibrahimu da Musa da Muhammadu *Alaihimus Salamu* ba su kama qafar Sahabban Isah *Alaihis Salamu* a daraja ba. Haka abin yake a nan. Domin ‘yan Shi’ah sun ce Aliyu shi ne Imami Ma'asumi, ko Annabi, ko ma dai, shi ne Allah. Amma sauran halifofi uku na farko, ba su kama qafar Ashtaru ba da makamantansa. A kan haka ne jahilcinsu da zaluncinsu suka gagari yawun alqalami siffantawa. Domin sun kasance suna godogo da riwayoyin qarya da ruxaxxun lafuzza da mummunan qiyasi, suna kuma ji da iqrarin cewa riwayoyi ne na gaskiya, kai mutawatirai ma. Kuma lafuzzan can nasu nassosa ne qwarara, ga su sarai. Kuma duk hujjar da za su kafa ta hankali, hujja ce gar.

## 4.8 Ayar:

﴿ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَشْرِى نَفْسَهُ ٱبْتِغَآءَ مَرْضَاتِ ٱللَّهِ ۗ وَٱللَّهُ
رَءُوفٌۢ بِٱلْعِبَادِ ﴿٢٠٧﴾ ﴾ البقرة: ٢٠٧

Hujja ta takwas, inji xan Shi’ah, ita ce: Faxar Allah Ta’ala: *Kuma akwai daga cikin mutane wanda yake sayar da kansa, domin neman yardar Allah (2:207).* Sa’alabi ya ce: A lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tashi yin hijira, sai ya bar Aliyu xan Abu Xalib, don ya biya basosan da ke kansa, ya kuma mayar da ajiye-ajiyen da ke hannunsa na mutane. Ya kuma umurce shi da ya kwana a kan shimfixarsa, a daren da zai fita zuwa kogon dutse, daidai lokacin da mushrikai suka yi wa gidan nasa

qawanya. Ya ce masa: Ya kai Aliyu! ka rufa da koren bargon nan nawa bahadrame, ka kwanta a kan shinfixata. Da yardar Allah babu wani mugun abin da zai same ka. Haka ko aka yi.

Nan take sai Allah Ta'ala Ya yi wahayi ga Jibrilu da Mika'ilu, cewa; haqiqa Ni na qulla zumunci tsakaninku. Na kuma hukunta shekarun xayanku su fi na xaya tsawo. Wane ne daga cikinku zai fice wa xan'uwansa waxannan dogayen shekaru? Sai kowanensu ya zavi kansa. Daga nan sai Allah Ya sake yi masu wahayi da cewa: Me zai hana ku yi koyi da Aliyu xan Abu Xalib? Na qulla zumunci tsakaninsa da Muhammadu, yau ga shi can kwance a kan shifixarsa yana fansar sa da rayuwarsa. Saboda haka ku sauka qasa ku kare shi daga maqiyansa. Sai suka sauka. Jibrilu ya tsaya wurin kansa, mika'ilu kuma wurin qafafunsa. Daga nan sai Jibrilu ya ce: Wai! Wai!! Wai!!! Lalle Aliyu xan Abu Xalib ka isa. Tirkashi! Yau kai ne Allah ke yi wa mala'iku alfahari da kai? Nan take kuma sai Allah Ya saukar da wannan aya da muka faxa a kan Ali, a daidai lokacin da Manzon ya kama hanyar Madina.

Wai kuma xan Abbas ya ce: Wannan aya ta sauka a kan Ali, a daidai lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya gudu daga mushrikai zuwa kogon dutse. Wannan irin daraja da ba wanda ya samu sai shi Ali, na nuna fifikonsa a kan gaba xayan Sahabbai. Saboda haka shi ne Imamu kenan. Inji xan Shi'ar.

**Martani:**

Muna son xan Shi'ar ya tabbatar mana da ingancin wannan riwaya. Mun gaji da riwayoyin Sa'alabi marasa kan gado. Malamai magadan Annabawa sun daxe da watsar da wannan hadisi. Kuma lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi hijira tare da Abubakar *Raliyallahu Anhu* zuwa Madina, ba nufin Quraishawa ba ne su kashe Aliyu. Suna dai neman Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne da Abubakar don su kashe. Har ma sun riga sun sanya diyyar kowannensu a matsayin goron wanda ya kashe shi. Kamar yadda hakan ta tabbata a cikin ingantattun littafan riwaya irin su Buhari.

Annabi ya umurci Aliyu ne da kwanta shimfixarsa, don su za ci cewa yana cikin gidan bai fita ba, balle su bi sawunsa. Domin ba suna nufin kashe shi a cikin gidansa ba. Safiya na yi sai suka ga ashe Aliyu ne, suka kunyata. Saboda haka ne ma ko baqar magana ba su gaya masa ba. Sai ma dai kawai suka tambaye shi inda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yake, kuma a cikin lalama. Ya ce masu bai sani ba.

Babu wani tsoro da ake ji wa Ali a lokacin daga kowa. Matsalar ta tattare ne a kan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da amininsa; su ake ji wa tsoro. Da Quraishawan can nada wani mugun nufi da Ali, da sun far masa, a

lokacin da suka gan shi. Amma rashin yin haka, ya tabbatar da ba shi suke nema ba. To, ina wata fansa da ya yi wa Manzon Allah, da ransa a nan? Babu.

Wanda dai ta tabbata ya fanshi Manzon Allah da ransa; ta hanyar shiga tsakaninsa da halaka, tare da yarda da cutuwa a madadinsa shi ne Abubakar *Raliyallahu Anhu.* Domin shi ne a kan hanyarsu, idan ya tuna ana iya dafafo su ta baya, sai ya koma bayan Annabi. Ya kuma koma gabansa, idan ya tuna ana iya taka qaya ko wani abu. Shi ne kuma ke zuwa yana shaqo masa labarai. Ka ga idan akwai wani abu da ake tsoro na haxari, ya gwammace ya same shi, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tsira.

Mun jiya, fansarsa ya yi. To, ai ba shi kaxai ya tava fansar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba. An samu Sahabbai da dama, da suka fanshe shi, da rayukansu a fagagen daga, ba kan gado ba. Akwai waxanda suka kwanta dama a gabansa. Wasu kuma aka sharce masu hannaye; kamar Xalhatu xan Ubaidullahi. Kenan da an qaddara cewa wancan abu da Ali ya yi, fansa ce ya yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da ransa, to, da hakan ta kasance wani abin xaukaka da, shi da wasu Sahabbai suka yi tarayya a ciki. Balle kuwa asalatan babu wani abu da ake ji wa Aliyun tsoro.

Bayan haka kuma idan xan Shi'ar bai manta ba, ai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ce wa Ali ya yi: Ya kai Aliyu! ka rufa da koren bargon nan nawa bahadrame, ka kwanta a kan shinfixata. Da yardar Allah babu wani mugun abin da zai same ka. Kenan Annabi ya lamunce masa, ya tabbatar masa da cewa babu wani abu da zai same shi. Wannan lamuncewa ta Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ta sa ya samu natsuwa. Ya yi baccinsa har da minshari.

Sannan wannan hadisin a karan kansa, tsatstsage yake da abubuwa bayyanannu da ke tabbatar da cewa qarya ne. Na farko: Wancan abu da ya ce ya faru ga Mala'iku, bai dace da su ba, domin varna ne. Babu wanda yunwa ko tsoro ke kamawa daga cikinsu, balle a yi tunanin yiwuwar xayansu ya fice wa xaya wani abin ci ko aminci. To, ta yaya za a ce: Allah Ya ce: Waye daga cikinsu zai fice wa xaya tsawon rayuwa? Kuma zancen qulla zumunci tsakaninsu da ya yi, abu ne marar asali a tsakanin mala'iku. Hasali ma ba ruwan wani da wani a cikinsu, aikin Jibrilu daban, bai shafi Mika'ilu ba. Na Mika'ilu daban bai shafi na Jibrilu ba. Kamar yadda ya zo a cikin Asaru, cewa Jibrilu aikinsa ya shafi wahayi ne da gudunmuwar nasara ga zavavvun Allah, a yayin da kula da arziqi da ruwan sama ke hannun Mika'ilu.

Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai tava qulla zumunci da Ali ko waninsa ba. Duk abin da aka riwaito, wanda ke qoqarin tabbatar da haka qarya ne.

Duk da hadisin da aka riwaito a cikin wannan sha'ani, tattare da rauni da varnar da ke cikinsa, iyakar abin da ke cikinsa shi ne, Annabi ya qulla

zumunci da Aliyun a Madina. Abin da Tirmizi ya riwaito kenan. Amma zumuncin da ake cewa ya qulla da shi a Makka, wala. Tatsuniya ce ta kowace fuska.

To, mu koma ga maganar waxancan Mala'iku. Cewa Jibrilu da Mika'ilu sun sauko don ba da kariya ga wani, na daga cikin manya-manyan maganganu yasassu. Domin kuwa Allah mai iko ne ga kare duk wanda ya so daga cikin halittarsa, ba tare da haka ba. Lokacin da kawai aka riwaito cewa waxannan mala'iku biyu sun tava saukowa qasa, shi ne ranar yaqin Badar, ko shi don su taya Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* daga. Sai kuma lokacin waxansu abubuwa masu girma irin waxannan. Da sun tava saukowa don bayar da kariya ga wani mutum, to da Annabi ne da amininsa, waxanda maqiya ke nema ruwa a jallo.

Ita dai wannan aya da muke cece-ku-ce a kanta, tana cikinsuratul Baqara ne. Ita kuwa surar ta sauka ne a Madina bisa haxuwar kan malamai. Ba a daidai lokacin hijirar ne ta sauka ba. Wasu kuma sun ce, ta sauka ne lokacin da Suhaibu ya yi hijira, mushrikai suka bi sawunsa. A inda ya miqa masu dukiyarsa baki xaya, ya isa Madina emti. Sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya jinjina masa da cewa: Cinikinka ya yi riba ya kai baban Yahaya. Wannan qissar mashahuriya ce a cikin tafsiri, saboda malamai da dama sun riwaito ta.

Game da maganar xan Shi'ar da ya ce: Babu wanda ya sami waccan xaukaka wai, ta fansar Annabi da rayuwa, sai Ali. Saboda haka wai hakan ta tabbatar da kasancewarsa mafifici. Kenan shi ne Imamu. Abin da za mu ce a nan shi ne: Idan haka ne, Alqur'ani da ijma'i sun tabbatar da cewa ko shakka babu wata xaukaka ta samu ga Abubakar *Raliyallahu Anhu* a lokacin hijira, wadda ba ta samu ga wani Sahabi ba. Kenan shi ne Imamu.

Dalilinmu a kan haka shi ne gasgantaccen zancen nan da ba sofanen qarya a cikinsa, wato faxar Allah Ta'ala:

﴿ إِلَّا تَنصُرُوهُ فَقَدْ نَصَرَهُ ٱللَّهُ إِذْ أَخْرَجَهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ثَانِىَ ٱثْنَيْنِ إِذْ هُمَا
فِى ٱلْغَارِ إِذْ يَقُولُ لِصَـٰحِبِهِۦ لَا تَحْزَنْ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَنَا ﴾ التوبة: ٤٠

*Idan ba ku taimake shi ba, to, lalle ne Allah Ya taimake shi, a lokacin da waxanda suka kafirta suka fitar da shi suna su biyu. A lokacin da suke cikin kogo, da yake ce wa abokin tafiyarsa: "Kada ka damu. Haqiqa Allah na tare da mu (9:40).*

Baya ga Abubakar kuwa, babu wanda ya sami wannan xaukaka yanke. Savanin bajintar bayar da rayuwa a matsayin kariya. Wadda ko da ta inganta cewa Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi a can, to, an sami Sahabi ba guda ba, da ya yi irin wannan.

## 4.9 Ayar Mubahala

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta tara ita ce: Faxar Allah Ta'ala:

﴿فَمَنْ حَآجَّكَ فِيهِ مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَكَ مِنَ ٱلْعِلْمِ فَقُلْ تَعَالَوْا۟﴾ آل عمران: ٦١

> *To, wanda ya yi musu da kai a cikinsa, a bayan abin da ya zo maka na ilimi, to, ka ce: "Ku zo mu kirayi 'ya'yanmu da 'ya'yanku da matanmu da matanku da kanmu da kanku, sa'annan kuma mu qanqantar da kai, sa'annan kuma mu sanya la'antar Allah a kan maqaryata (3:61).*

Xan Shi'ah ya ce: Gaba xayan Jumhuru, yana nufin malaman Sunnah, sun naqalto cewa *'ya'yanmu* a cikin wannan ayana nufin Hasan ne da Husaini. *Matanmu* kuwa na nufin Fatima. A ya yin da *Kanmu* ke nufin Ali. Wai kuma wannan aya dalili ce a kan tabbatar shugabancin Ali. Domin Allah Ta'ala ya daidaita shi da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Alhalin ko yin kat-kat-kat da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* abu ne da ba shi yiwuwa. Kenan waccan daidaitawa da aka yi musu, tana nufin shugabancin qoli. Da kuwa akwai wani wanda ba waxancan mutane da Manzon ya gayyato ba. Waxanda ke daidai da su ko fiye, a xaukaka da cancantar amsa du'ai, da kuwa Allah Ya umurci Manzon da gayyato su. Domin idan wannan lokaci ya wuce ba wani; iyakar damar kenan.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Babu wanda zai kasa tantance dalilin da ke cikin wannan aya, wanda ke tabbatar da abin da muke son tabbatarwa, sai wanda xan Lisu ya gurvata zuciyarsa, ya mamaye sasanninta. Ya kuma qawata masa son duniya, wadda kuwa samunta bai yiwuwa sai da zalunci.

**Martani:**

Maganar mubahala gaskiya ce. Ayar Alqur'ani ce ta faxe ta. Kuma bayan saukar ta ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kira Sayyidina Ali da Nana Fatima da Hasan da Husaini ya gabatar da su don yin ta. Labarin yana cikin Sahihu Muslim daga Sa'adu xan Abu Waqqasi. Amma wannan ba ya nuna wani dalili a kan shugabanci ko fifiko.

Cewarsa kuwa Aliyu yana daidai da Manzo, don Allah ya kira shi "kansa" kuma wai wannan na nufin shugabancin qoli, ba magana ce da take kan hanya ba. Domin kuwa babu wani dalili da ke iya tabbatar da ita. Yin wannan fassara ma na nuna ragguwar fahimta ga harshen Larabci. Duba wata aya mai kama da wannan da take cewa: *Inda ma a lokacin da kuka ji shi, muminai maza da mata sun yi zaton alheri ga kan su (24:12).* Kenan muminai maza da mata sun daidaita?.

Kuma ma ai wancan abu da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi ba abun mamaki ko tinqaho ba ne, domin kuwa, da ma ana mubahala ne tare da gayyato makusanta. Musamman da yake su abokan mubahalar sun gayyato makusantansu ne. To, dole ne shi ma ya gayyato irinsu. Da zai gayyato waxanda ba su ba daga cikin irin danginsa na nesa, abin da ake nufi ba zai sami tabbata ba. Ko da kuwa waxannan xin sun fi waxancan girma a wurin Allah.

Haka kuma da xan Shi'ar ya ce: Da akwai wani wanda ba waxancan mutane da Manzon ya gayyato ba. Waxanda ke daidai da su ko fiye, a xaukaka da cancantar amsa du'a'i. Da kuwa Allah Ya umurci Manzon da gayyato su. Domin idan wannan lokaci ya wuce ba wani; iyakar damar kenan.

**Martani:**

Ai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai gayyato waxancan mutane don du'a'in da za a yi ya sami karvuwa a wurin Allah ba, saboda su. Du'a'in da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* zai yi shi kaxai, ya isa. Inda kuwa har ya kira su ne, don ana nufin du'a'in ya karvu, albarkarsu, to, da ya gayyato gaba xayan muminai ya yi fadanci da albarkarsu. Kamar yadda ya kan roqi ruwan sama a wurin Allah tare da su. Yake kuma roqon sa'ar yaqi ta hanyar fita da dattijai daga cikin Muhajirai. Kuma ai an riwaito ya kan ce wa Sahabbai: "Kuna tsammanin nasarar da kuke samu da arziqi, ba albarkacin masu rauni daga cikinku ne ba; saboda addu'o'insu da sallolinsu da ikhlasinsu?"

Kuma sanannen abu ne cewa, duk da kasancewar waxancan mutane da Manzo ya gayyato, waxanda Allah ke karvar addu'arsu, yawan bakuna a cikin du'a'i na qara mata qaimin samun karvuwa. Amma ba ana nufin ya kirasu ne, don du'a'insa ya sami shiga ba. A'a an yi haka ne don daidaitawa tsakanin iyalinsa da na waxancan. Mun kuma sakankance a tilas cewa, da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* zai gayyato Abubakar da Umar da Usmanu da Xalhatu da Zubairu da xan Mas'udu da Ubayyu xan Ka'abu da Mu'azu xan Jabalu da wasunsu don halartar wannan mubahala, da sun kasance mafi girman mutanen da za su karva wannan kira nasa, waxanda kuma du'ainsu zai fi na waxanda ba su ba karvuwa a wurin Allah. Amma Allah *Subhanahu WaTa'ala* bai umurce shi da gayyato su ba, don hakan ba za ta iya tabbatar da abin nufi ba.

Wannan abin nufi kuwa shi ne waxancan mutane, abokan mubahala, su gayyato waxanda a al'ada suke tausaya wa. Kamar 'ya'yansu da matansu, da mazansu; waxanda kuma duk, suke mafi kusancin mutane gare su. Ka ga da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* zai gayyato wasu manisantansa, da sai su ma su gayyato irinsu. Kuma da mubahalar ba ta karva sunanta ba, kamar yadda za ta karva shi idan kowane vangare ya gayyato makusantansa. Domin kuwa

da ma a xabai’ar xan Adamu, ya fi tsoratar wa makusancinsa wani abin qi, a kan manisancinsa. Saboda haka Allah Ya murci Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da waxancan mutane, kowa ya gayyato makusancinsa.

A haka ta tabbata babu wani dalili a cikin wannan aya da ke tabbatar da abin da xan Shi’ar ke qoqarin tabbatarwa, asalatan. Amma saboda irin halinsa da ire-irensa, irin halin Nasara na karkata da ke cikin zukatansu, sai suna kama reshe su bar tushe. Maganarsa cewa kalmar “kanmu” na nufin daidaitawa, idan aka yi amfani da ita tsakanin abubuwa biyu ta sava wa yadda ake amfani da ita a harshen Larabaci.

Ita ma kalmar *matanmu* a cikin ayar, ba ta kevanta ga Nana Fatima ita kaxai ba. Duk da yake ita kaxai ce Manzon ya gayyato. Amma da Zainab da Ummu Kulsum da Ruqayya na raye a lokacin, duk wadda ya gayyato a cikinsu ko su duka, na iya zama makwafinta. Abin ya tsaya a kanta ne, don babu wata sai ita a lokacin, sauran sun riga sun rasu.

Haka nan kalmar *Kanmu* ba ta taqaita ga Ali kawai ba. Domin sigar jam’i gare ta, kamar yadda *matanmu* da *‘ya’yanmu* ke da. Annabi ya gayyato Hasan da Husaini ne, saboda babu wanda ke da dangantaka ta jini da shi, a matsayinsa na Annabi sai su. In da kuwa Qasim na raye a lokacin, ko wani cikin qannensa da kowanne aka kira daga cikinsu ya wadatar.

**4.10 Ayar:**

﴿ فَتَلَقَّىٰٓ ءَادَمُ مِن رَّبِّهِۦ كَلِمَٰتٖ فَتَابَ عَلَيۡهِۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ٣٧ ﴾ البقرة: ٣٧

Xan Shi’ar ya ce: Hujjarsa ta goma ita ce, faxar Allah Ta’ala: *Sai Adamu ya karvi wasu kalmomi daga Ubangijinsa. Saboda haka, ya karvi tubarsa (2:37).*

Ya ci gaba da cewa, malamin nan masanin fiqihu, Ibnul-Magazili Bashafi’e ya riwaito, da isnadinsa, daga xan Abbas, wanda ya ce: An tambayi Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a kan kalmomin nan da Adamu ya karva daga Ubangijinsa, har Ya karvi tuba a kansa. Sai ya karva da cewa: Ya roqe shi ne Ya yafe masa albarkacin Muhammadu da Aliyu da Fatima da Hasan da Husaini.

Xan Shi’ar ya ce, a kan haka ne Allah Ya yafe masa. Wannan kuwa, inji shi, xaukaka ce da ba wanda ya same ta daga cikin Sahabbai, balle ya riski Aliyu a cikinta. A kan haka sai ya zama shugaba. Saboda yin kafaxa-da-kafaxa da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin yin tawassuli da shi da aka yi zuwa ga Allah Ta’ala.

**Martani:**

Da farko, muna neman marubucin da abin da muka saba na tabbatar da ingantacin wannan riwaya. Domin kuwa mun riga mun san cewa, kasancewar Ibnul Magazili ya riwaito magana ba ya sa ta zama hujja, bisa haxuwar kan ma'abuta ilimi.

Wannan hadisi dai Abul-Faraji Ibnul Jauzi ya ambace shi cikin: *Al-Maudu'at* wato kundin Hadisan Gizo da qoqi.

Alqur'ani mai tsarki kuma ya riga ya fassara waccan aya, tare da bayyana kalmomin da Adamu ya karva daga wurin Ubangijinsa, waxanda ya yi fadanci da su har aka karvi tubarsa, da cewa su ne a cikin faxar Allah Ta'ala: *Ya Ubangijinmu! Mun zalunci kanmu. Kuma idan ba ka gafarta mana ba, kuma ka yi mana rahama, haqiqa muna kasancewa daga cikin masu hasara (7:23).*

Wannan dai ita ce fassarar magabata. Kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai tava umurtar wani da amfani da irin waxancan lafuzza a cikin du'a'i don neman gafarar Allah ba. Kai ko a cikin wani du'a'i da ba na neman gafara ba, ba a samu ya tava umurnin wani da haka ba. Hasali ma bai shar'anta wa al'ummarsa roqon Allah da irin wannan tawassuli ba. Da kuwa irin wancan lafazi karvavve ne a matsayin shari'a da ya shar'anta wa al'umarsa shi.

Babu kuma inda Alqur'ani ko Sunnah suka zo da halaccin rantsuwa ga Allah ta hanyar amfani da sunayen Mala'iku ko Annabawa. Ma'abuta ilimi da dama, irin su; Abu Hanifata da Abu Yusufa, sun bayyana fili cewa: Tawassuli ga Allah da wani mahaluqi ba ya halatta.

Wani abu kuma da ke tabbatar da kasancewar wannan magana ba shari'a ba, shi ne; kasancewar Adamu xaya daga cikin manyan Annabawa, ba ta yiwuwa ya roqi Allah yana tawassuli da wanda bai kai darajarsa ba. Ko shakka babu Annabinmu *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fi Adamu girman daraja. Amma shi kuma Adamun ya fi Aliyu da Fatima da Hasan da Husaini girman daraja.

### 4.11 Ayar: ﴿إِنِّي جَاعِلُكَ لِلنَّاسِ إِمَامًا﴾ البقرة: ١٢٤

Xan Shi'ar ya ce: Hujjarsa ta goma sha xaya akan wajabcin shugabantar da Ali tun fari, ita ce: Faxar Allah Ta'ala:

﴿ ۞ وَإِذِ ٱبْتَلَىٰٓ إِبْرَٰهِـۧمَ رَبُّهُۥ بِكَلِمَٰتٍ فَأَتَمَّهُنَّ ۖ قَالَ إِنِّى جَاعِلُكَ لِلنَّاسِ إِمَامًا ۖ قَالَ وَمِن ذُرِّيَّتِى ۖ ﴾ البقرة: ١٢٤

*Haqiqa, Ni mai sanya ka ne shugaba ga mutane. Ya ce: Kuma daga zuri'ata* (2:24).

Ya ce: Malamin nan masanin fiqihu, Ibnul Magazili Bashafi’e ya riwaito daga xan Mas’udu, wanda ya ce: Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Du’ain nan ya tuqe ne a kaina da Ali. Domin babu xayanmu da ya tava yin sujada ga gunki. Saboda haka ne Allah Ya zave Ni Annabi, Ya zave Aliyu Wasiyyi. Xan Shi’ar ya ce, wannan nassi ne da ke tabbatar da shugabancin Ali.

**Martani:**

Da farko: Ina asalin wannan hadisi naku?

Na biyu: Ma’abuta ilimin hadisi sun daxe da soke shi

Na uku: Cewa wannan du’a’in ya tuqe ne a kan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Ali, maganar kawai ce. Ba ya kuma halatta a jingina ta ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Domin kuwa cike take da tuqa da walwala. Ko kafin wannan al’umma, wannan addu’ar ta shafi wasu mutane daga cikin zuri’ar Annabi Ibrahim (AS); suka zama Annabawa.

In ko yana nufin du’a’in ya tuqe a kan Muhammadu da Aliyu ne, a cikin wannan al’umma, to, kenan hakan na nufin ba yadda za a yi Hassan ko Husaini ko waninsu ya zama Imamu daga baya. Sun ko zama. Ka ga waccan magana ta tashi, bisa haxuwar al’umma. Dalilin kuwa da ya kafa da cewa, waxannan mutane, ba su tava yin sujada ga gunki ba, wata siffa ce da sauran musulmin da suka zo bayansu suka siffanta da ita.

Na huxu: Rashin tava yin sujada ga gunki, wata daraja ce da duk wanda aka Haifa a cikin musulunci yake tarayya da Ali a cikinta. Amma ai musulmi magabata na da fifiko a kan irin wannan. To, ta yaya za a xaukaka wanda aka fi, a matsayin wanda ya cancanci wannan daraja, ga kuwa wanda ya fi shi?

Na biyar: Idan ‘yan Shi’ah suka ce, Ali *Raliyallahu Anhu* bai tava sujada ga gunki ba, saboda ya karvi musulunci tun bai balaga ba. Kuma haka bayan ya musuluntar ma bai yi ba, tunda musulmi ne. Babu wani abin alfahari a cikin wannan. Tunda kowane musulmi haka yake. Da ma shari’a ba ta hau kan yaro ba, balle. Idan kuwa suka ce: A’a, ba muna magana ne a kan bayan musuluntarsa ba, muna yi ne kan kafin haka. To sai mu ce masu: Wannan kuma sani sai Allah. Mu dai ba mu san wannan magana ba. Kuma shi xan Shi’ar da ke faxar wannan magana ba ya daga cikin mutanen da ake shiga xaka da zancensu.

**4.12 Ayar:** ﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ سَيَجْعَلُ لَهُمُ ٱلرَّحْمَٰنُ وُدًّا ﴿٩٦﴾﴾ مريم: ٩٦

Hujjar xan Shi’ar ta goma sha biyu wai ita ce: Faxar Allah Ta’ala: *Lalle ne waxanda suka yi imani, kuma suka aikata ayyuka na qwarai, mai rahama zai sanya so a gare su (9:96).*

Ya ce: Hafizu Abu Nu'aimi Al-Asbahani ya riwaito da isnadinsa daga xan Abbas, wanda ya ce: Wannan aya ta sauka ne a kan Ali. Kalmar "so" kuma na nufin Allah zai sa sonsa a cikin zukatan muminai. Ya ci gaba da cewa: Kuma ya zo a cikin tafsirin Sa'alabi daga Bara'u xan Azibu, wanda ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce wa Ali *Raliyallahu Anhu*: Ya kai Ali! Ka ce: Ya Ubangiji! ka yanka mani wani rabo a wurinka. Ka kuma sa ni abin so a cikin qirazan muminai. Wai daga nan sai Allah Ya saukar da wannan aya.

Xan Shi'ar ya rufe maganarsa da cewa: Babu wanda ya sami wannan lamuni sai shi. Saboda haka shi ne Imamu na gaskiya.

To, mun ji. Amma ku saurara:

Dole ne tun da farko malamin ya tabbatar mana da ingancin wannan riwaya, kafin komai. Idan kuwa ya kasa, to, ya sani kan malamai ya haxu a kan cewa, kafa hujja da wani abu da bai kama qasa ba, abu ne yasasshe. Domin yin haka magana ce a kan jahilci, da qoqarin shiga sharu ba hanu, da shiga kokowa ba karhu, balle laya. Haka kuma Ahlus-Sunna da Shi'ah gaba xaya sun tafi a kan cewa wannan asali da xan Shi'ar ya ambata wa wannan magana ba ya amfanar da komai.

Malamai masana sirrin hadisi sun haxu a kan cawa waxannan hadisai biyu qarya ne. Kuma cewar da Allah Ta'ala Ya yi a cikin waccan ayar: *Lalle ne waxanda suka yi imani, kuma suka yi ayyuka na qwarai (19:96)* magana ce gama-gari, da ta shafi gaba xayan muminai. Saboda haka ba ya yiwuwa a kevance Ali da ita. Domin kuwa ta shafi waninsa. Dalilinmu a nan shi ne, 'yan Shi'ah ba su musun kasancewar Hasan da Husaini da wasunsu daga cikin waxanda suke gani da gashi a ka, kuma duk wannan aya ta shafe su. Wannan haxuwa da aka samu, a kan ra'ayi xaya ta nuna rashin kasancewar Aliyu wanda ayar shafa kawai.

Ita kuwa cewar da ya yi wai, babu wanda ya sami irin waccan daraja daga cikin Sahabbai sai Ali, yasassar magana ce kamar ta bayanta. Domin kuwa Sahabbai su ne qarni mafi alheri. Waxanda suka yi imani suka kuma aikata aiki na qwarai daga cikinsu, su ne mafifita a kan kowa.

Sannan Alqawarin da Allah *Subhanahu WaTa'ala* Ya yi na sanya so ga waxanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka na qwarai, gaskiya ne. Kuma sanannen abu ne cewa, Allah Ya sanya son Sahabbai a cikin zukatan musulmi, musamman ma dai son halifofi, kuma musamman Abubakar da Umar daga cikinsu. Ta tabbata cewa, gaba xayan Sahabbai da Tabai'ai na matuqar son waxannan halifofi biyu – fiye da Ali - alhali ko su ne mafi alherin al'umma.

**4.13 Ayar:** ﴿إِنَّمَآ أَنتَ مُنذِرٌۖ وَلِكُلِّ قَوۡمٍ هَادٍ ۝٧﴾ الرعد: ٧

Xan Shi'ar ya ce: Hujjarsa ta goma sha uku ita ce: Faxar Allah Ta'ala:

> *Abin sani kawai, kai mai gargaxi ne. Kuma a cikin kowaxanne mutane, akwai mai shiryarwa (13:7).*

Ya ce: Xan Abbas ya faxa a cikin littafin *Al-Firdausi* cewa: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Ni ne mai gargaxin, Aliyu kuma mai shiryarwa. Ta hanyarka ne ya kai Aliyu duk mai shiryuwa zai shiryu". Ya ce, kuma Abu Nu'aimi ya riwaito irin wannan. Kuma a bayyane take cewa hadisin na tabbata da shugabanci da kasancewar Ali abin jivinta.

**Martani:**

Babu wani dalili da ya tabbata a kan ingancin wannan riwaya. Saboda haka hujja ba ta kafuwa da ita. Kuma ma'abuta ilimi sun haxu a kan cewa akwai qagaggun hadisai da dama a cikin littafin *Al-Firdausi*. Ta yadda kasancewar an samo wata riwaya daga cikinsa kawai, ba ya zama dalilin ingancinta a matsayin hadisi. Kamar yadda riwayar Abu Nu'aimi ga wata magana ba ta nuna ingancinta. Wannan maganar kuma qarya ce, bisa haxuwar ma'abuta ilimin hadisi. Saboda haka, wajibi ne a qaryata ta a kuma saka ta kwandon shara.

A zahiri wannan qagaggen hadisi na nufin ta hanyar Aliyu ne kawai mutane za su iya shiriya, ba da Annabi ba. Babu ko musulmin da zai yarda da wannan magana, balle ya faxe ta. Domin kuwa kai tsaye tana nufin an raba aikin gargaxi ne da shiryarwa a tsakaninsu; an ba kowa xaya. Wannan mai gargaxi wanda ba a shiruwa ta hanyarsa. Wancan kuma shi ne mai shiryarwa koda bai yi gargaxi ba. Shakka babu, musulmi ba zai yarda da faxin haka ba.

Allah Ta'ala Ya riga Ya Siffanta Muhammadu da cewa shi mai shiryarwa ne. A inda Ya ce: *Kuma lalle kai haqiqa, kana shiryarwa zuwa ga hanya madaidaiciya. Hanyar Allah (42:52-53)* To, ta qaqa za a ce mai shiryarwa shi ne wanda ba a siffanta da haka ba, alhali ga wanda aka siffantar?!

Sannan cewa wai Annabi ya ce wa Ali: Ta hanyarka ne duk wanda zai shiriya zai shiryu. Zahirin wannan magana, babu wanda zai shiryu kenan daga cikin al'ummar Muhammadu sai ta hanyar Ali. Qarya kuwa kenan. Domin dubun-dubatar mutane sun yi imani da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* sun kuma shiriya ta hannunsa, kai har ma sun shiga Aljanna, ba tare da sun ji kalma ko xaya daga bakin Ali ba. Haka kuma mutane da yawa sun shiriya ta hannun Sahabban da suka zauna tare da su, bayan cin garuruwansu da yaqi da aka yi. Suka kuma ci gaba da zama muminai ba tare da sun ji ko da kalma xaya daga bakin Ali ba. To, ta yaya zai yiwu a ce wai Annabi ya ce masa: Ta hanyarka ne duk mai shiriya zai shiryu?!

Wani abin kuma shi ne: Wasu malamai sun ce ma'anar wannan aya ita ce: Haqiqa kai mai gargaxi ne kawai. Amma mai shiriyar da kowaxanne mutane shi ne Allah Ta'ala. Wannan fassara ce mai rauni. Haka nan kuma cewar da wasu malaman suka yi ayar na nufin: Kai mai gargaxi ne kuma mai shiryarwa ga kowaxanne mutane. Ita ma fassara ce mai rauni.

Ingantattar fassara dai ita ce: Kai mai gargaxi ne kawai kamar yadda aka aiko ma kowace al'umma nata mai gargaxi wanda yake shiryar da ita. Kamar dai yadda wata ayar ta ce: *Kuma babu wata al'umma face wani mai gargaxi ya shuxe a cikinta (35:24).*

Wannan zancen wasu malaman tafsiri ne irin su, Qatadatu da Ikrimatu da Abud-Dhuha da Abdurrahmani xan Zaidu.

Amma waccan fassara da xan Shi'ar ya yi, ta hanyar taqaita ayar a kan Ali *Raliyallahu Anhu* varna ce tabbas. Musamman idan aka yi la'akari da cewa Allah Ta'ala Ya yi: *Kuma a cikin kowaxanne mutane akwai mai shiryarwa (13:7).* Ka ga kenan wannan na nufin, mai shiryarwa a cikin waccan al'umma, ba shi ne mai shiryarwa a cikin wannan ba. Ashe masu shiryarwa suna da yawa kenan. Idan kuwa haka ne, ta yaya za a ce Ali shi ne mai shiryarwa ga gaba xayan mutane, tun daga Annabi Adamu har ga na qarshe?!

## 4.14 Ayar: ﴿ وَقِفُوهُمْۖ إِنَّهُم مَّسْـُٔولُونَ ﴿٢٤﴾ ﴾ الصافات: ٢٤

Xan Shi'ar ya ce: Hujjar ta goma sha huxu ita ce: Faxar Allah Ta'ala: *Kuma ku tsayar da su. Don haqiqa su, waxanda ake yi wa tambaya ne (37:24).* Ya ce, an samo ta hannun Abu Nu'aimi daga Sha'abi daga xan Abbas, wanda ya ce, wannan ayana nufin za a tambaye su ne a kan shugabancin Ali. Haka kuma wai, ya zo a cikin littafin: *Al-Firdausi*, daga Abu Sa'id Al-Khudri *Raliyallahu Anhu* daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Ya ce: Idan har kuwa za a tambaye su, a kan shugabancin Ali, kenan shi ne wanda ya cancanta da shugabancin bisa wajabci. Babu kuwa wanda irin haka ta tabbata a kansa daga cikin Sahabbai sai shi. Kenan shi ne Imamu.

Bismillahi, mun fara:

Tun da har kan malamai ya haxu a kan jingina magana ga littafin *Al-Firdaus* da na Abu Nu'aimi, ba ya zama hujja, to, muna son marubucin ya faxa mana wata hanya, wadda wannan magana ta inganta tata. Domin ba mu kokwanto cewa, wannan magana an fesa ta ne.

Kuma takin qasar waxannan ayoyi, na takin saqa da yadda xan Shi'ar ya fassara. Domin kuwa cewa Allah Ta'ala Ya yi: *Ku tara waxanda suka yi zalunci, da abokan haxinsu, da abin da suka kasance suna bauta wa; wanin Allah. Saboda haka, ku gargaxa su zuwa ga hanyar wutar Jahima. Kuma ku*

*tsayar da su, lalle su, waxanda ake yi wa tambaya ne. Me ya same ku ba ku taimakon juna? A'a su a yau masu miqa wuya ne (37:22-26).*

Ka ji abin da Allah *Subhanahu WaTa'ala* Ya ce. To, kuma ka gani, duk Wannan magana ta shafi mushrikai ne, masu qaryata ranar sakamako. Allah zai tambaye su ne a kan kaxaita shi da Imani da manzanninsa, da ranar qarshe. To, me ya haxa wannan da cewa za a tambaye su ne kan "Son" Ali?

Mu xauka cewa ma suna daga cikin masoyansa. Kana ganin hakan za ta amfane su da wani abu, tattare da kasancewarsu kafirai kuma mushrikai? Ko kuma kana ganin qin da suke yi masa wani abu ne, wanda suka qi Annabawan Allah da littafansa da addininsa, balle Ali?

Kuma ka sani, babu wanda zai yi qarfin halin fassarar Alqur'ani hakan can, har kuma ya jingina fassarar ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai zindiqi, mulhidi, wanda bai san girman addini ba, mai qoqarin bice hasken musulunci. Ko qasurgumin jahili, wanda bai san abin da yake faxa ba. Wai ma shin mene ne banbancin son Ali da son Xalhatu da Zubairu da Sa'adu, da Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhum*?! Duk xaya ne.

**4.15 Ayar:** ﴿وَلَتَعۡرِفَنَّهُمۡ فِي لَحۡنِ ٱلۡقَوۡلِ﴾ محمد: ٣٠

Xan Shi'ar ya ce: Hujjarsu ta goma sha biyar ita ce: Faxar Allah Ta'ala: *Kuma lalle kana sanin su ga tuntuven harshe (47:30).* Abu Nu'aimi ya riwaito da isnadinsa, daga Abu Sa'id Al-Khudri, wanda ya ce: Tuntuven harshen da Allah ke nufi a cikin wannan ayar shi ne, furta qiyayyarsu ga Ali *Raliyallahu Anhu.* Xan Shi'ar ya rufe maganarsa da cewa: Babu kuwa wanda haka ta tabbata gare shi daga cikin Sahabbai sai Ali. Kenan ya fi su girman daraja. Shi ne kuma Imamu.

**Martani:**

Da farko, muna neman ingancin wannan batu. Na biyu kuma, mu sanar da kai cewa, malaman hadisi sun qaryata wannan magana da kuka jingina ga Abu Sa'id.

Na uku: Ko da ta inganta cewa Abu Sa'id ya faxi wannan magana bisa qaddarawa, ai shi xaya ne daga cikin Sahabbai. Kan ma'abuta ilimi kuma ya haxu a kan cewa: Idan maganar wani Sahabbai ta ci karo da ta wani Sahabin irinsa, to, ba za ta iya zama hujja ba. Kuma ana sane da irin yadda Sahabbai da yawa ke jin qaiqayi a kan Ali *Raliyallahu Anhu* kuma bai tava kafa masu hujja da zancen wani Sahabi ba, sai dai da Alqur'ani da sunna.

Na huxu: Fassara wannan aya ta Alqur'ani da irin wannan magana, qarya ce bayyananna. Domin kuwa tuva-tuvan harshen da aka san munafukai da su, ba su qunshi furta qin Ali ba.

Na biyar: Wani abin kuma shi ne: Qyama da qiyayyar da Ali ke yi wa kafirai da munafukai ko alama ba ta kama qafar wadda Umar ke yi musu ba. Don haka ne ma suka fi cin azaba a hannun Umar fiye da Ali. Kai babu wani lokaci da za su haxu da wata azaba a hannun Ali, face qiyayyarsu da Umar ta tsananta.

### 4.16 Ayar: ﴿ وَٱلسَّٰبِقُونَ ٱلسَّٰبِقُونَ ﴿١٠﴾ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلۡمُقَرَّبُونَ ﴿١١﴾ ﴾ الواقعة: ١٠ - ١١

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta goma sha shida akan wajabcin shugabancin Ali ita ce: Faxar Allah Ta'ala: *Da waxanda suka gabata iyakar gabaci. Waxannan su ne waxanda aka kusantar (ga Allah) (56:10-11).* Abu Nu'aimi ya riwaito daga xan Abbas, wanda wai ya ce: waxanda suka gabata a cikin ayar na nufin Ali. Kuma wai Ibnul-Magazili ya riwaito daga xan Abbas, wanda ya ce: "Yusha'u xan Nuni ya riga kowa a wajen Annabi Musa. Shi Musa ya riga kowa a wajen Haruna. Ma'abucin Yasin ya riga kowa ga Annabi Isa. Shi ko Aliyu ya riga kowa ga Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama"*. Kuma babu wanda ya sami wannan daraja da xaukaka daga cikin Sahabbai sai Ali. Saboda haka shi ne Imamu kenan. Inji xan Shi'ar.

**Martani:**

Kasancewar ana samun qaryace-qaryace da yawa, a cikin abubuwan da, waxannan malamai da xan Shi'ar ya kafa hujja da su ke riwaitowa, muna neman marubucin ya tabbatar mana da ingancin wannan naqali. Domin Ibnu Abbas bai faxi wannan magana ba. Ko da kuma ya inganta cewa ya faxe ta, ba za ta zama hujja ba, matuqar zancen nasa ya ci karo da na wanda ya fi shi qarfi.

Kuma ai cewa Allah Ta'ala Ya yi: *Kuma magabatan farko daga Muhajiruna da Ansaru da waxanda suka bi su da kyautatawa, Allah Ya yarda da su, su kuma sun yarda da shi, kuma Ya yi masu tattalin gidajen Aljanna: qoramu suna gudana a qarqashinsu (9:100).* Ya kuma ce: *Sa'anna mun gadar da littafin, ga waxanda muka zava daga cikin bayinmu. Kuma daga cikinsu, akwai mai zalunci ga kansa, kuma daga cikinsu akwai mai tsa kaitawa, kuma daga cikinsu akwai mai gabata da ayyukan alheri da izini Allah (35:32).*

Magabatan farko, da waccan aya ta yi bisimilla da su, su ne fa waxanda suke bayar da dukiyarsu tun kafin qarfin musulunci, suka kuma yi jihadi. Su ne kuma mafiya xaukaka a kan waxanda ba su bayar da dukiyarsu ko suka yi jihadi ba, sai bayan xaukakar addini, kamar yadda ya ce. A cikinsu kuwa har da waxanda suka yi *Bai'atur-Ridhwani*, adadinsu bai kasa mutum dubu xaya

da xari huxu ba. To ya za a ce wani mutum xaya ya yi wa irin wannan al'umma fintinqau?!

Kuma cewa wannan falala ta riga zuwa ga musulunci, ba ta tabbata ga wani daga cikin Sahabbai ba sai Ali, ba gaskiya ba ce. Malamai da sauran al'umma, sun qari junansu sani a kan wanda ya fara musulunta; Abubakar ne ko Ali.

Amma abin lura a cikin wannan magana shi ne; ko da Ali ya riga musulunta, an yi ittifaqi a kan cewa, yana yaro ne qarami a lokacin, wanda ba mukallafi ba. Don haka babu wani kokwanto a kan cewa musuluncin Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya fi kamala da amfani. Ka ga kenan a haka, kan malamai ya haxu a kan kasancewar musuluncin Abubakar *Raliyallahu Anhu* marigayi ga kamala. Akwai ma waxanda suka ce ya riga Alin musulunta, ba tare da wata togiya ba. To, ta yaya za a ce Aliyu ya riga shi musulunta, alhali kuwa babu wani dalili ko hujja a kan haka?!.

## 4.17 Ayar:

﴿ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَهَاجَرُوا۟ وَجَٰهَدُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ أَعْظَمُ دَرَجَةً عِندَ ٱللَّهِ ۚ وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْفَآئِزُونَ ﴿٢٠﴾ ﴾ التوبة: ٢٠

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta goma sha bakwai ita ce: Faxar Allah Ta'ala: *Waxanda suka yi imani, kuma suka yi hijira, kuma suka yi jihadi, a cikin hanyar Allah, da dukiyoyinsu, da rayuwarsu, su ne mafi girma ga daraja, a wurin Allah (9:20).*

Sannan ya ce, Ruzainu xan Mu'awiyah ya riwaito a cikin littafin: *Al-Jam'u Bainas-Sihahis-Sitta* cewa, wannan aya ta sauka ne a kan Ali, lokacin da Xalhatu xan Shaibata da Abbas suka yi wani alfahari. Babu kuwa wani Sahabi da ya sami irin wannan xaukaka sai Ali. Kenan shi ne mafifici daga cikinsu, kuma Imamu. Inji xan Shi'ar.

## Martani:

Martaninmu a kan wannan magana zai kasance kamar haka:

Muna neman marubucin ya tabbatar mana da ingancin wannan magana. Domin kuwa Ruzainu ya ambaci wasu abubuwa a cikin littafinsa, waxanda ba su da inganci.

Na biyu: Abin da ya zo a cikin Buhari ya sava wa abin da Ruzainu ya ambata. Abin da Nu'umanu xan Bashiru ya riwaito a cikin Buhari, cewa: Na kasance gindin munbarin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai wani mutum ya ce: Ba zan damu da ban aikata wani aiki bayan musulunci ba, in na

shayar da alhazai ruwa ba. Wani kuma ya ce: Ba zan damu da ban aikata wani aiki ba bayan musulunci, in na yi hidimar masallacin Harami. Wani kuma ya ce: Duk jihadi a tafarkin Allah ya fi waxannan abubuwa da kuka ambata daraja. Nan take sai Umar *Raliyallahu Anhu* ya kwatse su, ya ce: Ku daina xaukaka sautukanku gindin minbarin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma ga shi yau juma'a. Amma ku bari idan an qare sallar juma'a, in shiga in yi wa Annabi fatawa a kan wannan abu da kuke savani a kansa. Nan take sai Allah Ta'ala Ya saukar da: *Shin kun sanya shayar da mahajjata da rayar da masallaci mai alfarma kamar wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira, kuma ya yi jihadi a cikin hanyar Allah? Ba su daidai a wurin Allah (9:19).* Muslimu ne ya fitar da hadisin.

Wannan ingantaccen hadisi na tabbatar da cewa, maganar Aliyu *Raliyallahu Anhu* ta fifita jihadi a kan hidimar masallacin da shayar da mahajjata, ta fi inganci bisa maganar waxancan Sahabban biyu da suka fifita waxannan abubuwa biyu a kan jihadi. Kenan Aliyu *Raliyallahu Anhu* shi ne mafi dacewa da gaskiya a cikin wannan mas'ala, a kan waxanda suka yi ja-inja da shi. Wannan ko shakka babu gaskiya ne.

Amma kuma wancan zance na fifiko ta hanyar Imani da Hijira da Jihadi, riga ce da ta shiga wuyan gaba xayan Sahabbai, waxanda suka yi imani, da hijira, da jihadi. Babu wata daraja da Ali ya kevanta da ita a nan.

## 4.18 Ayar Ganawa

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta goma sha takwas ita ce: Faxar Allah Ta'ala:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا نَٰجَيۡتُمُ ٱلرَّسُولَ فَقَدِّمُواْ بَيۡنَ يَدَيۡ نَجۡوَىٰكُمۡ صَدَقَةٗۚ﴾ المجادلة: ١٢

> *Ya ku waxanda suka yi imani! Idan za ku gana da* Manzon Allah*, to, ku gabatar da 'yar sadaqa a gabanin ganawarku (58:12).*

Wai an samo, inji shi, daga hannun Hafiz Abu Nu'aimi zuwa ga xan Abbas, wanda ya ce: "Haqiqa wannan aya na bayyana, Allah *Subhanahu WaTa'ala* Ya haramta ganawa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai tare da an gabatar da wata 'yar garawa. Amma haka ba ta sa Sahabbai suka riqa gabatar da sadaqar ba; sai kowa ya qi. Aliyu *Raliyallahu Anhu* ne kawai ya gabatar da ita. Babu wani daga cikin musulmi da ya yi haka bayan sa".

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: An samo a cikin tafsirin Sa'alabi, cewa xan Umar ya ce: "Wasu darajoji uku sun kasance ga Ali *Raliyallahu Anhu* Waxanda da zan sami xaya daga cikinsu, da ta fi soyuwa gare ni a kan garken jayayen raqumma. Na farko, Aurar masa da Fatima. Na biyu, danqa masa tuta da aka yi ranar yaqin Haibara. Na uku kuma, Saukar ayar Munajati a kansa".

Kuma wai Ruzainu xan Mu'awayya ya riwaito daga Aliyu *Raliyallahu Anhu* wanda wai ya ce: "Babu wanda ya yi aiki da wannan aya sai ni. Kuma a dalilina ne Allah Ya sassafta wa wannan al'umma". Wannan kuma na nuna kasancewarsa mafifici a kan sauran Sahabbai. A kan haka kuma shi ne mafi cancanta da shugabancin, inji xan Shi'ar fa, ba inji ni ba.

## Martani

Eh, abu ne tabbatace cewa Ali *Raliyallahu Anhu* ya gabatar da wata 'yar sadaqa a lokacin da buqatar ganawa da Manzon Allah ta kama shi, kamar yadda ayar ta umurta. Amma kuma sai Allah *Subhanahu WaTa'ala* Ya hukunci shafe ayar kafin buqatar ganawa da Manzon ta kama wani Sahabi bayan Alin, balle har ya gabatar da garawar.

Amma kuma abin lura a nan shi ne, ayar ba ta wajabta wannan sadaqa a kan Sahabbai ba, ta dai umurce su da yin ta ne idan buqatar ta same su. Ka ga kenan wanda buqatar ba ta kama ba, babu wannan sadaqa a kansa. Tunda kuwa har ganawar ba wajibi ce kansu ba, kenan sadaqar ma ba wajibi ba ce. A kan haka ba za a zargi kowa ba, idan ya yi biris da abin da ba wajibi ba. Haka kuma duk wanda ba ya da ikon gabatar da sadaqar daga cikinsu, wanda kuma tabbas da buqatar ganawar za ta kama shi, ta kuma taras da ikon gabatar da sadaqar, da ya gabatar. To, ko ganawar irin wannan ya yi hannu biyu, yana da ladar niyya. Shi kuwa wanda buqatar ganawar ba ta kama ba, balle ya gabatar da garawar ko yana da ikon yin haka, ba za a ce masa kasasshe ko naqqasasshe ba. Kai ko da wanda ganawar ta maqare ya kuma yi, amma saboda matsolanci ya kasa gabatar da sadaqar komai, ba za a yi masa kallon hadarin kaji ba, don mustahabbi ne kawai ya bari. Wannan kuma ba ya daga cikin halin Sahabbai halifofi balle a shede su da shi.

Haka kuma babu wanda zai iya ce maka yana da wata masaniya a kan kasancewar halifofin can uku halarce lokacin da wannan aya ta sauka. Abu ne mai sauqi ko da aka saukar da ita wasu daga cikinsu ba su nan. Ko kuma ta kasance babu abun sadaqar hannu a lokacin. Ko ma kai babu buqatar ganawar sam-sam, ga wasunsu.

Kada ka yi mamakin waxannan hasashe-hasashen. Domin kuwa ana da tabbacin cewa shiga shantun qadangare ayar ta yi wa duniyar Sahabbai, nan take aka shafe ta. Balle ko kace ta xauki wani lokaci mai tsawo da yake da wuya a ce buqatar ganawar ba ta kama wani daga cikinsu ba.

Da kuma za mu qaddara ta kama su xin amma kuma ba su gabatar da sadaqar ba, suka kuma ganar, hakan ba komai ba ne. domin kuwa mun riga mun yi bayani a wurare da dama cewa, aikata mustahabbi da wani zai yi, ba ya wajabta kasancewarsa mafificin daraja, kai tsaye a kan wanda bai aikata ba.

Hasali ma Tirmizi ya riwaito hadisi daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da ke cewa: “Ba ya kamata ga mutanen da Abubakar yake a cikinsu, wani wanda ba shi ba ya yi masu limanci”.

Kuma ai ka ga raquma dubu da halifa Usmanu ya raka wata ruduna ta musulmi da su, sun fi qarfin waccan ‘yar sadaqa da Aliyu ya yi nesa ba kusa ba. Domin kuwa ko banza ciyar da dukiya domin jihadi farilla ne. Savanin waccan ‘yar sadaqa domin ganawa, wadda kawai aka sharxanta a kan wanda buqatar ganawar ta kama; ta yadda wanda bata kama ba, sadaqar ba ta ko hau kansa ba.

Kuma harwayau ka ga a kan wasu Ansaru ne dai, Allah Ta’ala Ya saukar da: *Kuma suna fifita waxansu a kan kawunansu, ko da suna da wata lalura (59:9)* .

A taqaice, idan ana zancen bajinta a fagen ciyar da dukiya a kan tafarkin Allah da wasu al’ammurra na addini, ba a zancen Ali *Raliyallahu Anhu*. Da yawa daga cikin Muhajiruna da Ansaru sun yi masa fintinqau a fagen; sun sami darajar da bai samu ba. Domin kuwa Allah bai hukunce shi da mallakar wata dukiya ba a zamanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.*

**4.19 Ayar :**

﴿ وَسْـَٔلْ مَنْ أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ مِن رُّسُلِنَآ أَجَعَلْنَا مِن دُونِ ٱلرَّحْمَٰنِ ءَالِهَةً يُعْبَدُونَ ﴿٤٥﴾ ﴾ الزخرف: ٤٥

Xan Shi’ar ya ce: Hujja ta goma sha tara ita ce: Faxar Allah Ta’ala: *Kuma ka tambayi waxanda muka aika a gabaninka daga Manzanninmu (4:45)*

Wai Abu Nu’aimi ya fitar da cewa, Allah ya tara Annabawa tare da Annabi Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* daren da aka yi Isra’i da shi. Sannan Ya ce masa: “Ka tambaye su ya kai Muhammadu cewa: A kan me aka aike ku? Wai sai suka ce: An aike mu ne don tabbatar da ba wanda ya cancanci bauta sai Allah. Da kuma iqirarin Annabcinka da shugabancin Aliyu xan Abu Xalib”. Xan Shi’ar ya shafa fatiha da cewa: Wannan magana ce ga-ta-sarai, da ke tabbatar wa Ali da shugabanci.

**Martani:**

Muna neman marubucin ya tabbatar mana da ingancin wannan magana. Amma kuma kai mai karatu, kada ka yi zaton neman da muke wa wancan marubucin da ya tabbatar mana da ingancin wannan mummunar qarya da makamantanta, sakamakon shakkar da muke da ita ne a kan kasancewar su qarya da xumi-xuminta. Ko alama ba haka abin yake ba. Muna yin haka ne, don bayar da ‘yar sanyi ga abokin tattaunawarmu. Domin da ba mu da masaniya da kasancewar maganganu nasa qarya, to, da ba mu kafa hujja da su

ba, ta hanyar neman ya tabbatar da ingancinsu. Domin kuwa yin haka kamar kafa hujja ne da abin da ba a san ingancinsa ba, wanda kuwa yin haka ba ya halatta ittifaqan.

Duk wani xan makaranta da ya sanya qafarsa a cikin ilimin hadisi ya san ko shakka babu, wannan magana shegiyar nan ce ‘yar gidan Musailamu. Kuma varna ce da duk mai hankali da kishin addini ba zai gasgata ba. Babu kuma ba mai qirqira irin waxannan maganganu sai wawayen mutane marasa kunya. Ta yaya za’a tambayi Manzanni *Alaihis Salamu* a kan abin da ba ya cikin tushen imani?

Hasali ma gaba xayan musulmi sun haxu a kan cewa; Yau da mutum zai yi imani da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kuma bi shi sau da qafa, ya kuma rasu Annabin na raye, ba tare da ya san Allah Ya halicci wani da ake kira Abubakar ko Umar ko Usmanu ko Aliyu ba, hakan ba za ta cutar da shi da komai ba, balle ta hana shi shiga aljanna.

To, idan har wani daga cikin al’ummar Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* na da irin wannan garanti, ya za a ce yana wajaba a kan Annabawa *Alaihimus Salamu* su yi imani da wani daga cikin Sahabbai?! Wannan ba ta savuwa; wai bindiga a ruwa.

### 4.20 Ayar: ﴿لِنَجۡعَلَهَا لَكُمۡ تَذۡكِرَةٗ وَتَعِيَهَآ أُذُنٞ وَٰعِيَةٞ ١٢﴾ الحاقة: ١٢

Xan Shi’ar ya ce: Hujja ta ashirin ita ce: Faxar Allah Ta’ala: *Kuma wani kunne mai kiyayewa ya kiyaye (shi) (6:12)*

Ya ce: Sa’alabi ya faxi a cikin tafsirinsa cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Na roqi Allah *Subhanahu Wa Ta’ala* ya sa kunnen nan ya kasance naka, ya kai Ali”. Haka kuma an samo ta hannun Abu Nu’aimi, wanda ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Ya kai Ali! Haqiqa Allah Ya umurce Ni da in ja ka a jiki, in kuma karantar da kai don ka kiyaye. Saboda haka ne ma aka saukar mani da wannan aya. Kuma kai ne kunnen mai kiyayewa”.

Xan Shi’ar ya qara da cewa: babu wanda ya sami wannan xaukaka sai Ali. Saboda haka shi ne shugaba.

### Martani:

Da farko muna neman bayani a kan ingancin madogarar wannan magana. Domin kuwa Sa’alabi da Abu Nu’aimdu na riwaito abubuwan da ba su iya tsayawa a matsayin hujja, bisa haxuwar kan malamai. Sannan kuma, masu ilimi sun haxu a kan cewa wannan hadisi qagagge ne.

Wannan ayoyi ba tana magana ne a kan kunnen wani mutum xaya daga cikin mutane ne ba. A'a, magana ce da ta shafi gaba xayan 'ya'yan Adamu. Karanto daga farko ka ji. Allah ya ce: *Lalle ne mu, a lokacin da ruwa ya qetare haddi, mun xauke ku a cikin jirgin ruwan nan. Domin Mu sanya shi, abin tunawa gare ku, kuma duk kunne mai kiyayewa ya kiyaye (shi) (69:12).*

Hore ma 'yan adam hawan jirgin ruwa, na daga cikin manya-manyan ayoyin Allah. Dubi abin da a wani wurin Allah Yake cewa: *Kuma aya ce a gare su kasancewar haqiqa mun xauki zuriyarsu a cikin jirgin, wanda aka yi wa lodin. Kuma muka halitta masu abin da suke hawa daga irinsa (36:41-42)* Ya kuma ce: *Ashe, ba ka ga lalle jirgin ruwa na gudana ba a cikin teku da ni'imar Allah, domin ya nuna muku daga ayoyinsa? Lalle a cikin wannan akwai ayoyi ga dukan mai haquri, mai godiya (31:31).* To, ta yaya za a yi duk wannan al'amari ya taqaita ga buqatar kiyayewar kunnen wani mutum xaya daga cikin mutane?

Gaskiya ne. Kunnen Ali *Raliyallahu Anhu* na xaya daga cikin waxannan kunnuwa masu kiyayewa. Kamar yadda ba mai musun kasancewar kunnuwan Abubakar da Umar da Usmanu da wasunsu *Raliyallahu Anhum* daga cikin waxannan kunnuwa. Ka ga kenan abin bai kevanci Aliyu kawai ba. Wannan kuwa kowa ya san da shi; ba kunnen Ali ne kawai mai iya kiyaye waxancan ni'imomi na Allah ba.

Ko kana ganin kunnen Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba kunne ne mai kiyayewa ba? Ko kuma kunnen Hasan da Husaini da Ammaru da Abu Zarri da Miqdadu da Salmanul-Farisi, da Sahalu xan Hunaifu, da sauran mutanen da 'yan Shi'ah suka yarda suna da imani. Duk kunnuwansu ba su daga cikin kunnuwa masu kiyayewa?

Idan kuwa har akwai waxansu mutane da ke da irin waxannan kunnuwa masu kiyayewa, bayan Ali, to, cewa wannan falala ba ta samu ga kowa ba sai shi, wasa da hankali ne.

A haka kuma, ko shakka babu, wannan xan Shi'ah, ya yi jahilci da zalunci, don ya gina al'amurransa a kan turbar qarya saboda ya vatar da mutane. Ta kuma tabbata cewa babu wata qungiya daga cikin qungiyoyin bidi'a da ta riqi sungumin ragga a matsayin makami kamar 'yan Shi'ah. Savanin Mu'utazilawa da makamantansu, waxanda ke da wasu hujjoji da dalilai da ke rikita hankalin da yawa daga cikin ma'abuta ilimi da hankali. Amma 'yan Shi'ah, ba su tava mallakar wata hujja da wani ke iya gamsuwa da ita ba, face jahili da azzalumi da mai biyar son zuciya. Wanda ke karvar duk abin da ya dace da ra'ayinsa; gaskiya ne ko qarya.

**4.21 Surar:** ﴿هَلْ أَتَىٰ عَلَى ٱلْإِنسَٰنِ حِينٌ مِّنَ ٱلدَّهْرِ لَمْ يَكُن شَيْـًٔا مَّذْكُورًا ۝١﴾ الإنسان: ١

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta ashirin da xaya ita ce: *Suratul Insan.* Ya ce: Ya zo a cikin tafsirin Sa'alabi, ta hanyoyi da dama, cewa: Watarana Hasan da Husaini sun kwanta rashin lafiya. Sai kakansu *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tafi duba su tare da gangami na xaukacin Larabawa. Sai suka ce: "Ya kai baban Hasan! me zai hana ka yi alkawarin azumi, godiya ga Allah idan 'ya'yan nan naka sun warke?" Sai ko ya sha alwashin azumin kwana uku. Haka nan mahaifiyarsu Fatima da kuyangar gidansu Fiddhatu, su ma suka yi. Sai kuwa Allah Ya ba su sauqi. A lokacin kuwa babu qwaya balle tiya a gidan Muhammadu. Saboda haka sai Aliyu ya ranto sa'i uku na alkama. Nan take Fatima ta gurje sa'i xaya. Ta toya curi biyar na waina da shi, domin kowanensu ya samu xaya.

Bayan da Ali *Raliyallahu Anhu* ya qare sallar magariba tare da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya iso gida sai aka kawo abincin aka xora a gabansa. Haka ke da wuya, sai wani almajiri ya yi sallama, yana cewa: Ga wani miskini daga cikin talakawan musulmi. Ku taimakan da sadaqar abin ci, Allah Ya saka maku da na aljanna. Ali na jin haka, sai ya yi umurni da a xauki gaba xayan abincin can a ba shi. Haka kuwa aka yi. Su kuwa a wannan dare da yininsa, suka zauna haka nan, ba su saka komai bakin salati ba sai baqin ruwa.

Kashegari kuma Fatima ta toye sa'i guda. Sai abin da ya faru jiya ya sake faruwa da wani almajiri daga cikin bayi. A rana ta uku aka sake maimaita labarin jiya da na shekaranjiya, amma tare da wani maraya wanda ya yi masa koken an kashe babansa ranar yaqin Aqaba. Suka kwana uku ba su saka komai a bakinsu ba, ga su ko suna azumi.

Rana ta huxu na kamawa, bayan alwashin da suka sha na azumin kwana uku ya cika, sai Aliyu ya kama Hasan da hannunsa na dama, Husaini kuma da na hagu. Ya tasar wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* iska na kaxa su kamar yadda yake kaxa 'yan tsaki, saboda tsananin yunwa. Ganin su haka ke da wuya sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Wannan hali da na gan ku a ciki, shi ne abin da ya fi komai baqanta mani rai. Ku tashi mu isa gidan 'yata Fatima in ji yadda aka yi". Isarsu ke da wuya, suka taras da ita kwance cikin xaki fatar cikinta ta lahe ga qashin bayanta. Saboda tsananin yunwa, har idanunta sun yi kogo. Da Annabi ya gan ta cikin wannan hali, sai ya ce: "Allah ka agaje mu, yau ga mutanen gidan Muhammadu yunwa na shirin kashewa".

Nan take sai Jibrilu ya sauka yana mai cewa: Ya kai Muhammadu, saurari abin da Allah ke taya ka murna da shi, a kan abin da ya sami mutanen gidanka. Sai Annabi ya ce: Mene ne wannan abu ya kai Jibrilu? Sai ya karanta masa:

﴿هَلْ أَتَىٰ عَلَى ٱلْإِنسَٰنِ حِينٌ مِّنَ ٱلدَّهْرِ لَمْ يَكُن شَيْـًٔا مَّذْكُورًا ۝١﴾ الإنسان: ١

*Lalle ne mudda ta zamani ta zo a kan mutum wadda bai zamo wani abin ambato ba a cikinta (75:1).*

Xan Shi'ar ya ce: Wannan falala ce mai tarin yawa, da wani bai samu ba kafin Ali *Raliyallahu Anhu* wadda kuma ke nuna cewa shi ne mafifici a kan duk wanda ba shi ba. Shi ne kuma Imamu kenan.

A nan sai mu ce: Qanqurus qan qusu.

**Martani:**

A wannan karon ba mu ko buqatar a tabbatar mana da wannan tatsuniya. Mun dai gaji da waxannan riwayoyin Sa'alabi marasa kan gado. Kuma irin riwayoyinsa da na ire-irensa ba su raba gardama koda a mas'ala ta mustahabbi balle aqida, ballantana fassarar Alqur'ani da bayanin dalillan saukar sa.

Ma'abuta ilimin hadisi a matsayinsu na jagorori masu yanke hukunci a cikin wannan sha'ani, sun yi ittifaqi a kan kasancewar wannan hadisi qarya. Kuma zancensu shi ne, abin kamawa a wannan babi.

Daga cikin abubuwan da ke tabbatar da kasancewar wannan hadisi qarya har da cewa, kowa ya sani Ali *Raliyallahu Anhu* bai auri Nana Fatima ba sai a Madina. Bai kuma yi baiko da ita ba sai bayan yaqin Badar. Bayan haka ne kuma aka haifi Hasan da Husaini, tsakanin shekara ta uku da huxu bayan hijira. Ita kuma wannan sura ta sauka ne a Makka kamar yadda malaman tafsiri da riwaya suka haxu a kan haka. Wannan ko yana qarfafuwa da salon tafiyar surar wanda masana suna gane na surorin Makka ne.

To, ka ga kenan duk wanda ya ce: Surar ta sauka ne bayan rashin lafiyar Hasan da Husani, ya tabbata maqaryaci, don ba a halicce su ba lokacin saukarta.

Kuma yin nazarin qwaqwaf ga takin qasar wannan hadisi da lafuzzan da ke cikinsa, ya ishi mutum gane cewa tatsuniya ce da jahilai suka qirqira. Xan kalli cewar da xan Shi'ar ya yi wai, kakansu ya je duba su, tare da gangamin xaukacin Larabawa. To, duk wanda ya san tarihi, ya san cewa faxin wannan magana a Madina jahilci ne. xaukacin Larabawa da suke kafirai za su je duba shi?

Kuma don Allah dubi cewar da ya yi wai Larabawa sai suka ce: Ya kai baban Hasan! Me zai hana ka sha alwashin, don godiya ga Allah idan 'ya'yan nan naku biyu sun sami sauqi. Alhali kuwa Aliyu ba ya karvar wani abu na addini daga Larabawan. Alwashi kuwa addini ne. A'a yana karva ne daga wurin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Inda ha kan wani umurni ne na xa'a ga Allah, to, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ya kamata ya hore

shi da shi, bisa cancanta ba waxannan Larabawa ba. Idan kuwa hakan ba xa'a ba ce, kai ka san ko sun hore shi ba zai aikata ba. To wai, ta yaya ma zai saurare su, ba tare da ya waiwayi Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a kan lamarin ba?!

Ya tabbata a cikin Buhari da Muslimu cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya hana irin wannan alwashi, da ya ce: Haqiqa alwashi ba ya tahowa da alheri, ana dai matse marowaci ne kawai da shi.

Idan kuwa har Aliyu da Fatima da suran mutanen gidansu ba su san da wannan magana ta Annabi ba, wadda gaba xayan Al'umma ta sani, to tasgaro ya tabbata a cikin iliminsu. To, in haka ne, ina maganar ma'asumanci ta kwana?

Idan kuwa har suna da masaniya da haka, suka kuma aikata abin da Allah da Manzonsa ba za su gode ba, to, babu wata lada da za su samu a ciki. Tunda har an hana su daga hakan; hani na haramci ko na karhanci. Runtse ido su aikata hakan kuwa, na tabbatar da rashin cikar addininsu ko hankalinsu ko iliminsu, in kun yarda.

Aliyu da Fatima ba su da wata kuyanga da ake kira Fiddatu. Kai ba su ba, ko cikin makusantan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* babu mai ita. Babu ma wata kuyanga a faxin garin Madina da aka sani da wannan suna. Babu wani ma'abuci ilimi da ya ambaci wannan kuyanga a cikin tarihin waxannan mutane.

Abin dai da ya tabbata a cikin Buhari, shi ne cewa, wani Sahabi daga cikin Ansaru ya fice wa wani baqonsa abincinsa na dare, ya lallashi qananan 'ya'yansa suka yi barci. Shi da matarsa suka kwana wahalce. A kan haka ne ma Allah Ta'ala Ya saukar da: *Kuma suna fifita waxansu a kan kawunansu, kuma ko da suna da wata lalura (59:9).*

Kuma ko shakka babu, wannan yabo da Allah ya yi ma wannan Ansari, ya fi wanda ya yi a cikin ayar *Suratul Insan* da suke zaton ta sauka a kan Ali, wadda ta ce: *Kuma suna ciyar da abin ci, a kan suna buqatarsa, ga matalauci da maraya da fursuna (76:8).* Don wannan yana daidai da inda Allah Ya ce: *Kuma ya bayar da dukiya, a kan yana son ta, ga mai zumunta da maraya da, matalauta (2:177).*

Kuma a cikin wannan qissa da xan Shi'ar ya qaga, akwai abin da bai dace a jingina shi ga Aliyu da Fatima ba. Saboda abin ya sava wa abin da shari'a ta yi umurni da shi; wato barin qananan yara cikin lalurar yunwa har tsawon kwanaki uku. Ta hanyar sa su yin xoreri na kwanakin. Irin wannan yunwa na vata hankali da jiki da addini. Ka sani kuwa wannan bai yi daidai da qissar Ba ansaren nan ba. Domin shi dare xaya ne kawai ya bar 'ya'yan nasa, ba tare da sun ci abin ci ba, alhalin kuma ba su yini da azumi ba. Ka ga ai qananan yara na iya daure wannan, savanin kwanaki uku; yini da dare.

Wani abun kuma shi ne, cewar da xan Shi'ar ya yi a cikin wannan tatsunita wai marayan can ya ce: "Mahaifina ya rasu ranar yaqin Aqabah". Ita ma wannan magana qarya ce bayyananna. Domin kuwa babu wani yaqi da aka yi a wannan dare na Aqabah. Illa dai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya karvi bai'ar Ansaru a wannan dare kafin a yi hijira, balle a yi umurni da jihadi.

Wannan magana na nuna cewa bayan kasancewar wannan hadisi qagagge, yana daga cikin qaryace-qaryace da jahilan mutane waxanda ba su san tarihin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba suka qago. Domin da xan Shi'ar ya ce, marayan ya ce: "Mahaifina ya rasu ranar yaqin Uhudu". Da hakan tafi zama kusa ga gaskiya. Kuma ai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya riga ya xauke nauyin gaba xayan yaran waxanda suka yi shahada tare da shi. Saboda haka ne ma ya tava gaya wa Fatima *Raliyallahu Anha* a lokacin da ta roqi ya samar mata mai hidima, cewa: "Ba zan qyale marayun Badar ba, in xauki nauyin samar maki mai hidima"

.

**4.22 Ayar:** ﴿ وَٱلَّذِى جَآءَ بِٱلصِّدْقِ وَصَدَّقَ بِهِۦٓ ۙ أُو۟لَـٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُتَّقُونَ ﴿٣٣﴾ ﴾ الزمر: ٣٣

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta ashirin da biyu ita ce: Faxar Allah Ta'ala: *Kuma wanda ya zo da gaskiya, kuma ya gasgata a game da ita, waxancan su ne masu taqawa (39:33).*

Ya ce: An samo daga hannun Abu Nu'aimi daga Mijahidu cewa: *Wanda ya zo da gaskiyana nufi*n: Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Wanda kuma *ya gasgata a game da ita* na nufin Ali xan Abu Xalib *Raliyallahu Anhu*. Wai kuma an samo ta hannun malamin nan masanin fiqihu Bashafi'e – Ibnul Magazili – daga Mujahidu cewa, ayar na nufin: Muhammadu ya zo da gaskiya, Aliyu kuma ya gasgata shi.

Xan Shi'ar ya ciga da cewa, wannan falala ce da, Aliyu ya kevanta da ita. Shi ne Imamu kenan.

**Martani:**

Martaninmu a kan wannan magana zai kasance ta fuskoki kamar haka:

**Fuska ta farko:**

Wannan magana da xan Shi'ar ke yi, ba a cirota ta daga bakin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba. Sannan maganar Mujahidu shi kaxai ransa, ba ta zama hujja, idan ma har ta inganta. To, ina ga ba a da tabbacin shi ya faxe ta? Tare kuma da masaniyar da ake da akan qaryar wanda ya xauko ta?.

Duk da haka kuma dai, abin da ta tabbata daga Mujahidu ya ci karo da wannan. Domin kuwa cewa ya yi: kalmar "Gaskiya" a cikin ayar na nufin

“Alqur’ani”. A ya yin da ta “wanda ya gasgata” ke nufin mumini matuqar ya yi aiki da ita. Ka ga kenan shi a wurinsa ayar, gama-gari ce.

**Fuska ta biyu:**

Ko shi wannan tafsiri da ya tabbata daga Mujahidu, abin da ya shahara a wurin ma’abuta tafsiri ya ci karo da shi. Domin kuwa shugaban sahun masu tafsiri, wato Imamux-Xabari, ya ambaci wata riwaya, wadda ya danganta ga Ali *Raliyallahu Anhu* ta hanyar isnadinsa. Wadda yake cewa a cikinta: *Wanda ya zo da gaskiya* a cikin ayar na nufin Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama*. *Wanda kuma ya gasgata* na nufin Abubakar. Ba Xabari kawai ba, akwai ma wasu malamai da suka tafi a kan haka.

**Fuska ta uku:**

A taqaice dai lafuzzan wannan aya game-gari ne kai tsaye. Ba su kevanci Abubakar ko Aliyu ba. Magana xaya ita ce, duk wanda ya sami shiga qarqashin inuwarta, hukuncinta ya shafe shi. Kuma ko shakka babu Abubakar da Umar da Usmanu da Ali *Raliyallahu Anhum* sun fi kowa a cikin wannan al’umma cancanta da shiga qarqashin inuwarta. Amma dai ba su toshe hanyar shigar wasu ba.

**4.23 Ayar:**

﴿وَإِن يُرِيدُوٓاْ أَن يَخۡدَعُوكَ فَإِنَّ حَسۡبَكَ ٱللَّهُۚ هُوَ ٱلَّذِيٓ أَيَّدَكَ بِنَصۡرِهِۦ وَبِٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٦٢﴾ الأنفال: ٦٢

Xan Shi’ar ya ce: Hujja ta ashirin da uku ita ce: Faxar Allah Ta’ala: *Shi ne wanda Ya qarfafa ka da taimakonsa, kuma da muminai (8:62).*

Ya ce: An samo ta hannun Abu Nu’aimi daga Abu Hurairata, wanda ya ce: “Akwai shi rubuce a kan al’arshi cewa: *Babu wanda ya cancanci bauta sai Allah, shi kaxai ba ya da abokin tarayya. Muhammadu bawansa ne kuma Manzonsa. Na kuma qarfafa shi da Aliyu xan Abu Xalib.* Wannan shi ne ma’anar zancen Allah, a cikin littafinsa da Ya ce: *Shi ne wanda ya qarfafa ka da taimakonsa kuma da muminai (8:62).* Wato yana nufin ya qarfafa shi da Ali. Wannan kuma na daga cikin manyan darajojin da babu wanda ya same su daga cikin Sahabbai sai shi. A kan haka shi ne shugaba (Imamu) kenan.

**Martani:**

Kamar kodayaushe, muna neman marubucin ya tabbatar mana da ingancin wannan riwaya. Domin kuwa sanannen abu ne cewa, kan malamai ya haxu a kan riwaya ba ta zama hujja don kawai an jingina ta ga Abu Nu’aimi ba.

Mun san cewa Abu Nu'aimi nada littafi mai suna: *Fala'ilus-Sahaba*. Amma kuma ai ya ambaci wani yanki na darajojin a farkon littafin: *Hilyatul Auliya'i*. Idan shi ma 'yan Shi'ah na kafa hujja da shi, to ya riwaito wasu darajoji na Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhum* waxanda ke rosa duk abin da suke gina. Idan kuwa har ba su kafa hujja da abin da ya riwaito, to kada su sake dogaro da naqalinsa.

Abin da Ahlus-Sunnah ke yi kodayaushe shi ne, komawa su auna duk abin da Abu Nu'aimi da ire-irensa suka riwaito, da ma'aunin ma'abuta ilimi a wannan fanni. Ta hanyar biyar hanyoyin da ake gane gaskiya ko qaryar hadisi da su. A nan ne ake yi wa isnadi da mazajen da ke cikinsa binciken qwaqwaf. Don a gane in su amintattu ne, ko a'a. da kuma neman tabbacin saduwar mariwaitan da junansu. Sannan a bi diddigin sauran hanyoyin da za su iya qarfafa hadisin in har akwai. A lokacin da malamai ke wannan fixa, ba ruwansu da abin da aka riwaito, ya shafi darajojin Ali ne ko na waninsa. Duk abin da bincikensu ya tabbatar gaskiya, nan take za su inganta shi. Babu kuma abin da zai hana su qaryata duk abin da ya tabbata qarya.

Bayan haka, sai mu ce: Ma'abuta ilimin hadisi sun yi ittifaqi a kan cewa, wannan hadisi qagagge ne. Wallahi mu ba mu shakkar kasancewar wannan hadisi zuqi ta mallau. Kuma wallahi, Abu Hurairata bai faxe shi ba, sam. Haka abin yake a cikin duk hadisai ko maganganun da muka kushe na wannan xan Shi'ah.

Kuma ai ka ga cewa Allah Ta'ala Ya yi: *Shi ne wanda Ya qarfafa ka da taimakonsa kuma da muminai. Kuma Ya sanya soyayya a tsakanin zukatansu. Da ka ciyar da abin da yake cikin qasa, gaba xaya, da ba ka sanya soyayya a tsakanin zukatansu ba, amma kuma Allah Ya sanya soyayya a tsakaninsu (8:62-63).* Ka ga waxannan ayoyi da aka haxa hancinsu, sun nuna cewa, waccan kalma ta *Muminai* waxanda Allah Ya qarfafa Manzon da su bayan taimakonsa, adadi ne na jama'a, waxanda Allah ya sanya danqon soyayya a tsakanin zukatansu, kuma Sayyidina Ali, xaya ne daga cikinsu. Bai mallaki wasu zukata ba can daban, da yake sa soyayya a tsakaninsu. Kuma shi "tilo" ne, a yayin da waccan kalma ta muminai ta ke cikin sigar "Jam'i". Ka ga wannan nassi ne, da kai tsaye ke nuna, Allah ba Ya nufin wani mutum xaya kevantacce. Saboda haka ba ya halatta ga wani ya shiga gaban Allah, ya ce: Ayar na nufin Ali ne, wahdahu la sharika lahu.

Abu ne sananne a kan tilas, kuma ta dubaiban hanyoyi, cewa nasarar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya samu ta yaxa addini, ba da sa hannun Aliyu ne kawai ya same ta ba. Duk da yake yana daga cikin na farko-farko a shiga musulunci, a daidai lokacin kuma addinin na cikin rauni. Ai ba don Allah Ya shiryar da wasu mutane zuwa ga imani da hijira da taimakawa ba, da kasancewar Aliyu kawai wanda ke cikinsa, ba ta taimaka masa da komai ba. Kuma hasali ko imani da hijira da taimakawar da mutane suka yi ba wai Ali ne

ya sanya su ba. Ba a kuma san Ali da tsayuwa wajen kira zuwa ga musulunci a Makka ko a Madina ba, kamar yadda aka san Abubakar da yin haka. Ba a kuma cirato wani ya musulunta a farkon musulunci ta hannun Ali ba. Kai, ko bayan hijira. A tarihi ma dai babu wani Sahabi da aka ce a hannun Ali ya musulunta. Amma da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi masa gwamna a Yaman, ba za a yi mamaki ba idan an ce wani ya musulunci a hannunsa can. Wannan yana yiwuwa. Amma ai su ba Sahabbai ne ba. Abin da kowa ya sani ne ko cewa, akwai manya-manyan Sahabbai da suka musulunta ta hannun Abubakar, bisa ga kuma shawararsa.

Kuma Ali bai yi ja-in-ja da mushrikai irin yadda Abubakar ya yi ba, ba su kuma nuna tsoronsa irin yadda suke tsoron Abubakar da Umar ba. Kai, duk wata gudunmawa da ka san sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* ya tava bayar wa musulunci, to, akwai takwarorinsa daga cikin Sahabbai da suka ba da irinta ko fiye da ita. Wannan kuwa abu ne da, duk masanin tarihi ya san da shi. Sai maqaryata da ciwonsu ba ya da magani.

Amma yin qarya a irin waxannan lamurra abu ne mai haxari, saboda dangantakarsu da addini. Kuma Allah ya ce: *Kuma wane ne ya fi zalunci bisa ga wanda ya qirqira qarya ya jingina ta ga Allah, ko kuma ya qaryata gaskiya a lokacin da ta je masa? (29:68).*

Ya kamata kai ma ka tambayi kanka. Ya za a ce, duk gwagwarrmayar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya sha, da nasarorin da ya samu, duk da taimakon wani Sahabbai ne tallintal ya same su? Ina tarin gudunmuwar da gaba xayan muminai daga cikin magabatan farko, da Muhajiruna da Ansau, waxanda suka yi masa bai'a a qarqashin bishiya, da waxanda suka rufa masu baya cikinsutura, suka ba shi? Ina waxanda suka ba da jinainansu a Badar da Uhud da sauran yaqoqa?

**4.24 Ayar:** الأنفال: ٦٤ ﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ حَسۡبُكَ ٱللَّهُ وَمَنِ ٱتَّبَعَكَ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٦٤ ﴾

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta ashirin da huxu ita ce: Faxar Allah Ta'ala da ya ce: *Ya kai Annabi! Allah Ya ishe ka, kai da duk wanda ya bi ka daga muminai (3:64).* Wai Abu Nu'aimi ya ce: Wannan aya ta sauka ne a kan Ali. Kuma wai daraja ce da ba wanda ya samu daga cikin Sahabbai sai Ali. Kenan shi ne Imamu. Inji shi.

**Martani:**

Da farko: Wannan magana ba ta inganta ba.

Na biyu kuma: Wannan magana ba ta zama hujja, ko da an qaddara ingancinta.

Abin da ayar ke nufi shi ne, Allah Ya isar wa Manzon da muminai, mabiyansa. Kuma shi ne kaxai qwal wanda Ya isa kariya ga Manzon da Muminan da ke tare da shi. Ba abin da ayar ke nufi ne ba cewa, Allah da muminai sun ishi Manzo. A'a, Allah shi kaxai ne, wanda ya isar wa gaba xayan halitta.

Fahimtar jahilci da 'yan Shi'ah suka yi wa wannan ayar na cewa, Allah da muminai sun ishi Manzo, shi ya kai su ga qaga wannan qarya cewa muminan, Ali ne kaxai ake nufi.

To, wannan jahilci nasu na biyu ma, ya fi wancan na farko fitowa fili. Domin abu ne mai yiwuwa qwarai waccan fassara da suka yi ta farko, ta qyafta wa wasu mutane a matsayin gaskiya. Amma ta biyu, ko alama. Babu mai hankalin da zai kasa tantance gaskiyarta. Domin kuwa ba Aliyu ne kawai daga cikin halitta, ya kama wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* harkar addini ba. Da kuwa shi ne kawai ya kasance tare da shi a fagen, da addinin bai tsaya ba balle ya kawo yau.

Ai ba a ma maganar Ali a irin wannan fage. Domin kuwa ko kansa bai iya amfana wa komai ba, a lokacin da ma mafi yawan rundunar da ke bayan qasa take bayansa. Ka tuna lokacin da Mu'awiyah ya yaqe shi, da irin jaruntakar da ya nuna har ya rinjaye shi. Daxa ko duk ta hanyar da ya bi, ya dai rinjaye shi. Ko ta hanyar qarfin tuwo ko makirci da yaudara. Ai da ma yaqi xan zamba ne.

To, ka ga a hankalce, idan Aliyu *Raliyallahu Anhu* ya kasa isar wa kansa da komai, a irin wannan lokaci da Musulunci ya game duniya. Kuma mafi yawan mutane da ke bayan qasa ke biye da shi. Ta yaya zai isar wa Manzo da wani abu a lokacin da gaba xayan mutanen duniya ke qiyayya da shi?!

Da 'yan Shi'ah sun ce ma na, ai Aliyu *Raliyallahu Anhu* ya kasa rinjayar Mu'awiyah da waxanda ke tare da shi ne, saboda rudunar Aliyun ba ta biyayya gare shi; duk lokacin da ya yi gabas sai su yi yamma. Sai mu ce masu: Idan har musulmin da ke tare shi ba su yi masa xa'a ba, yaya za a yi kafiran da ba su yarda da shi da Annabin ba, su yi masa xa'a?!

Kuma sannannen abu ne a kan tilas cewa mutane, a lokacin da suka shiga addinin musulunci, sun fi kasancewa masu biyayya ga gaskiya. Ta ya za a yi wanda ya haxa hannu da Allah a cikin aikin tsayar da addinin Muhammadu a kan qafafunsa, har aka rinjayi kafirai, mutane suka musulunta ya kasa bayar da irin wannan goyon baya don a rinjayi wata 'yar qungiya da ta yi tawaye a kansu, waxanda adadinsu bai kai na kafiran da ke akwai ba, a lokacin da aka aiko Manzo, balle su yi qarfinsu. Tattare kuma da kasancewarsu mafi zama kusa da gaskiya fiye da su?

**4.25 Ayar:** ﴿يُحِبُّهُمۡ وَيُحِبُّونَهُۥٓ﴾ المائدة: ٥٤

Xan Shi’ar ya ce: Hujja ta ashirin da biyar ita ce: Faxar Allah Ta’ala:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَن يَرۡتَدَّ مِنكُمۡ عَن دِينِهِۦ فَسَوۡفَ يَأۡتِي ٱللَّهُ بِقَوۡمٖ يُحِبُّهُمۡ وَيُحِبُّونَهُۥٓ أَذِلَّةٍ عَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ أَعِزَّةٍ عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ يُجَٰهِدُونَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلَا يَخَافُونَ لَوۡمَةَ لَآئِمٖۚ ذَٰلِكَ فَضۡلُ ٱللَّهِ يُؤۡتِيهِ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ ٥٤﴾ المائدة: ٥٤

*Ya ku waxanda suka yi imani, duk wanda ya yi ridda daga cikinku; ya bar addininsa, to, da sannu Allah zai zo da waxansu mutane waxanda yake so, suna son sa, masu tawali’u ga muminai, masu izza a kan kafirai. Suna yin jihadi a cikin hanyar Allah kuma ba su tsoron zargin wani mai zargi. Wannan falalar Allah ce, da yake bayar da ita ga wanda ya so. Kuma Allah Mayalwaci ne, masani (5:54)*

Wai Sa’alabi ya ce: Wannan aya ta sauka ne a kan Ali *Raliyallahu Anhu*. Kuma wai wannan na nuna shi ne Mafifici daga cikin Sahabbai, kuma shi ne Imamu.

**Martani:**

Qaryar qaryace-qaryace ta qare. Domin Sa’alabin ma bai faxi wannan magana ba. Abin da ya ce a cikin tafsirinsa a matsayin fassarar wannan aya shi ne: Ali da Qatadatu da Hasan sun ce: “Ayar na nufin Abubakar da Sahabbansa”. Shi kuwa Mujahidu ya ce: “A’a, tana dai nufin mutanen Yaman”. Mujahidu bai tsaya a nan ba, sai da ya kafa hujja da hadisin Iyalu xan Gunmu, da ke cewa: “Su ne mutanen Yaman”. Ya kuma kafa hujja da wani hadisi a kan haka.

To, ka ga shi kansa Sa’alabi ya riwaito cewa Aliyu kansa ya fassara ayar da cewa, tana nufin Abubakar da jama’arsa. Ali kuwa yana cikin jama’ar Abubakar.

Waccan magana kuwa tasa, babu hujja a cikinta. Saboda haka karvarta ba ya wajabta. Don ta ci karo da wadda ta fi ta shahara da bayayyana, wato wannan da ke cewa ayar ta sauka ne a kan Abubakar da jama’arsa, waxanda ya yaqi ma’abuta ridda tare da taimakonsu. Wannan shi ne abin da aka sani, kamar yadda ya gabata. Su dai waxannan maqaryata na so ne su xauke duk wata daraja da ta zo kan Abubakar, su kai ta ga Ali. Wannan kuma na daga cikin mummunan makirci, wanda kuwa dodo ne da ba ya cin kowa sai mai shi.

Abin da ya inganta a wurin masana tarihi shi ne, Abubakar ne ya yaqi ma’abuta ridda tare da taimakon jama’arsa. Su ne suka yaqi Musailamatal-

Kazzabi, wanda ya ce shi Annabi ne. Suka murqushe shi tare da magoya bayansa banu Hanifata da mutanen Yamama, waxanda a ka ce yawansu ya kai dubu xari. Suka kuma yaqi Xulaihatul-Asadi, wanda shi ma ya yi da'awar Annabci a Najadu, har wasu mutane da dama daga cikin qabilar Asadu da Tamimu da Gaxfanu suka goyi bayansa.

Haka kuma an sami wata mata da ake kira Sajahi, wadda ta yi da'awar Annabta. A qarshe kuma ta auri Musailamatul-Kazzabi kafin a kashe shi. Maqaryaci ya auri maqaryaciya kenan.

Ko shakka babu waxanda suka yaqi murtaddai, na daga cikin waxanda Allah ke so, kuma suke son sa. Kuma su ne mafi cancantar mutane da shiga qarqashin inuwar wannan aya. Haka nan su ma waxanda suka yaqi sauran kafirai na Farisa da Ruma, wato Abubakar da Umar da waxanda suka kama masu, daga cikin mutanen Yaman da sauransu, duk sun shiga cikin wannan aya. Saboda hake ne ma, aka samu riwaya cewa, an tambayi Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a lokacin da wannan aya ta sauka, a kan su wane ne? Sai ya nuni Abu Musal Ash'ari, ya ce: "Su ne jama'ar wannan".

Wannan abu ne sananne bisa lalura. Kuma an san shi ta hanya mutawatira cewa, waxanda suka tanka tare da xora jinkan musulunci, kuma suka tabbata cikinsa, a lokacin da mutane ke fitarsa, suka yaqi murtaddai, da kafirai, na cikin waxanda Allah ke so, suna son sa, masu tawali'u a kan muminai, masu izza a kan kafirai. Suna yin jihadi a cikin hanyar Allah kuma ba su tsoron zargin wani mai zargi. Shi kuwa Ali *Raliyallahu Anhu* ko shakka babu yana xaya daga cikinsu. Sai dai ba shi ne mafi cancanta da wannan siffa ba, fiye da Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhum* kamar yadda arangamar da ya yi da kafirai da masu ridda ba ta fi wadda suka yi da su girma ba. Kuma alherin da ya tabbatar wa addini ta hanyar wannan jihadi, bai fi wanda suka tabbatar masa yawa ba.

Tabbataccen abu dai shi ne, kowane daga cikinsu na da nagartattar rawar da ya taka da inganccen aikin da ya tavuka, da kyakkyawan Kufan da ya bari a cikin musulunci. Allah kuma zai saka masu da alherinsa, albarkacin hidimar da suka yi wa musulunci da musulmi, a matsayinsu na halifofi shiryayyu, masu shiryarwa, kuma shugabanni masu kevowa, waxanda a mulkinsu suka yi hukunci adalci da gaskiya.

Wannan ita ce magana.

Amma yau a ce waxannan shugabanni na jama'a, waxanda amfanin da suka tabbatar a cikin addini da duniya ya fi a qirga, wai, su ne kafirai ko fasiqai azzalumai. A ce kuma wani wanda abin da ya gudana a hannunsa na alheri, bai kama qafar wanda ya gudana a hannun xayansu ba, a xauke shi matsayin Allah ko abokin tarayyarsa, ko a kai shi matsayin abokin tarayyar Manzon Allah; a ce ma'asumi ne, da ba a yin imani sai an yarda da ma'asumancinsa; kuma duk

wanda bai yarda da hakan ba kafiri ne. A ce kuma yau kafirai, waxanda suka yi ridda ba kafirai ba ne. Waxanda suka yaqe su sun ci haqqinsu. A lokaci xaya kuma, a ce waxannan musulmi da ke sallah biyar, su yi azumin watan Ramalana, su ziyarci xakin Allah, waxanda suka daxe da shanye ruwan imani da Alqur'ani, wai su ne kafirai, saboda sun yaqi waxancan, wal-iyazu billahi.

Kai ka san ba mai faxar wannan magana sai tantirin jahili da, qarya da zalunci da shishshigi ba su ishe shi ba.

Mu qaddara cewa, wannan aya ta sauka ne a kan Ali *Raliyallahu Anhu* ko akwai mai iya qarfin halin cewa ta kevance shi ne kawai, Alhali lafazinta na nuna Jama'a?.

Nazari game qumshiyar ayar na ba ka tabbacin cewa, waxannan mutane da Allah ke magana a kansu, ba mutum xaya ba ne. Kuma ko Larabcin da Allah ya yi amfani da shi ba ya bada waccan ma'ana.

Da 'yan Shi'ah za su yi qarfin halin cewa: Waccan ayar na nufin jama'a ne, amma jama'ar su ne: Ali da magoya bayansa. To, sai mu ce: Idan har wannan aya za ta sanya wani tare da Ali, a qarqashin inuwarta, to, ko shakka babu waxanda suka yaqi kafirai da masu ridda, sun fi cancanta da shiga ciki tare da shi, a kan waxanda ba su yaqi kowa ba sai masu mayar da gaba gabas su yi sallah. Ko shakka babu mutanen Yaman waxanda suka taya Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhum* yaqi sun fi cancanta da shiga inuwar wannan aya a kan 'yan Shi'ah, waxanda ba su da abokai sai Yahudawa da Nasara da Mushrikai, A daidai lokacin da ba su da abokan gaba sai magabatan musulmi.

Kuma ai ka ga ayar cewa ta yi, Allah, zai zo da wasu mutane, Yana son su kuma suna son sa (5:54). Xauki kalmar can ta 'Wasu' ka duba ta da kyau. Za ka tabbata cewa lafazi ne da bai kevance kowa ba; haka qofarsa take sake. Tana jiran duk wanda waccan siffa ta tabbata gare shi ya shiga, ko waye shi kuwa. Ba sai Abubakar ko Aliyu ko waninsu ba. Ka ga kenan kuskure ne a ce Ali ya fifita a kan duk wanda ya yi tarayya da shi a cikin wannan falala. Balle har hakan ta wajabta kasancewarsa Imamu.

Kai, a taqaice abin da wannan aya ke nufi shi ne: Babu wani lokaci da ridda zata bayyana; mutane su rinqa barin addini, daga yau har zuwa ranar qarshe, face Allah Ya tayar da wasu, waxanda yake so, suke kuma son sa, masu sassabci ga muminai da tsanani ga kafirai, su yaqi waxanda suka yi riddar.

## 4.26 Ayar: ﴿أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلصِّدِّيقُونَ﴾ الحديد: ١٩

Xan Shi'ar ya ce: Hujjarsa ta ashirin da shida ita ce: Faxar Allah Ta'ala:

﴿وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ بِٱللَّهِ وَرُسُلِهِۦٓ أُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلصِّدِّيقُونَ ۖ وَٱلشُّهَدَآءُ عِندَ رَبِّهِمْ﴾ الحديد: ١٩

*Kuma waxanda suka yi imani da Allah da Manzonsa, waxannan su ne masu kamalar gasgatawa, kuma su ne masu shahada a wurin Ubangijinsu, (57:19)*

Ya ce: Ahmadu xan Hambali ya riwaito da isnadinsa daga wajen xan Abu Laila, shi kuma daga babansa, wanda ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* Ya ce: Masu gasgatawa guda uku ne: Habibu xan Musa, kafinta, muminin Ali Yasin. Wanda ya ce: "*Ya ku mutane! Ku bi Manzanni"*. Da kuma Hizqilu, muminin Ali Fir'auna. Wanda ya ce: *Yanzu kuna yarda ku kashe mutum don kawai ya ce: "Ubangijina shi ne Allah"?* Na qarshensu kuma shi ne Aliyu xan Abu Xalib. Shi ne kuma mafifici daga cikinsu.

Haka wai inji xan Shi'ar, malamin nan masanin Fiqihu Ibnul-Magazili, Bashafi'e da marubucin littafin: *Al-Firdausi*, duk sun riwaito irin wannan magana. Ya kammala maganar tasa da cewa, wai wannan xaukaka ce da ke nuna shugabancin Ali *Raliyallahu Anhu*.

**Martani:**

Muna son ya tabbatar mana da ingancin wannan hadisi. Domin kuwa babu shi a cikin Musnadin Imamu Ahmad. Kuma ma'abuta ilimi sun yi ittifaqi cewa ko da ya riwaito shi a cikin littafinsa na *Fadha'ilus-Sahabati* hakan ba ta nuna cewa ya inganta a wurinsa. Domin kuwa ana da tabbacin cewa, yakan riwaito abin da ya ci karo da mutane sun riwaito, ko da kuwa bai inganta ba. Kuma duk wanda ya san abin da ake ce wa ilimi, ya san cewa ba kowane hadisi ne da Ahmad ya riwaito a cikin littafinsa na *Fadha'ilus-Sahabati* yake zama ingantacce ba. Kai, ko waxanda yake riwaitowa a cikin Musnad nasa, ba kowane hadisi ne ke zama ingantacce ba. Hasali ma hadisan da wannan Musnad nasa ya qunsa, hadisai ne da mutane suka riwaito ba tare da tantancewa ba. Amma ba ya riwaya daga waxanda aka yi masu shedar qarya. Saboda haka abu ne mai yiwuwa, a sami wata makama cikin wasu daga cikinsu da ke nuna raunin wasu daga cikinsu ko ma kasancewa qarya. Sai dai ana da tabbacin cewa, mafi yawansu hadisai ne na gargaru, da kuma ake iya kafa hujja da su. Kuma tabbas ne cewa, sun fi hadisan da ke cikinsu*nanu Abi Dawuda* nagarta. Amma abin da ya riwaito a cikin *Fadha'ilus-Sahabati* bai shiga wannan vangare ba.

Cewa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Masu gasgatawa uku ne. Ya kuma taqaita hakan a kan ambaton waxancan mutane uku, magana ce da ba ta sauraruwa. Domin kuwa hadisi ingantacce ya zo da ambaton wani wanda ba Ali ba a matsayin "mai gasgatawa" ta fuskoki da

dama. Kamar inda Annabi ya ambaci Abubakar da wannan suna. To, ya za a ce haka?

Misalin wannan shi ne, hadisin da ya zo a cikin Buhari da Muslimu, daga Anas, wanda ya ce: Watarana Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya hau kan dutsen Uhudu. Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhum* suka rufa masa baya. Sai dutsen ya girgiza. Annabi ya ce masa: Kwantar da hankalinka ya kai Uhudu. Ba wasu ne a kanka ba face Annabi da Siddiqi (mai gasgatawa) da Shahidai guda biyu.

Kai, ko Alqur'ani ma, Allah *Subhanahu WaTa'ala* Ya ambaci Sayyida Maryamu da Sunan mai gasgatawa. Ka ga cewa Annabi Ya taqaita wannan kalma a kan mutanen can uku, labari ne.

To, idan 'yan Shi'ah na nufin cewa: Masu gasgatawa uku ne, na nufin babu wani Siddiqi bayan ukun, to, qarya ce. Domin kuwa hakan ta sava wa littafin Allah, da Sunnar Manzon Allah da haxuwar kan musulmi. Idan kuwa suna nufin hakan na nufin Siddiqancin waxancan mutane uku, shi ne mafi kamala, to, shi ma cewa haka kuskure ne. Domin kuwa wannan al'umma tamu ita ce mafi alherin al'umma, wadda Allah Ya samar don ceto mutane. To, ta yaya wanda ya gasgata Musa, da wanda ya gasgata Isah za su fi waxanda suka gasgata Muhammadu cika da kamala?

Kuma ai ka ga Allah Ta'ala cewa ya yi: *Kuma waxanda suka yi imani da Allah da Manzonsa, waxannan su ne masu kamalar gasgatawa, kuma su ne masu shahada a wurin Ubangijinsu (57:19).* Ka ga wannan magana na nuna cewa, duk wanda ya yi imani da Allah da Manzonsa Siddiqi ne.

Idan kuwa har kasancewa Siddiqi shi ne abin da ke sa mutum ya cancanci zama shugaba (Imamu). To wanda ya fi kowa cancantar karva wannan suna, shi ne Abubakar *Raliyallahu Anhu.* Domin shi ne wanda dalilai da dama suka tabbatar wa sunan, ta dubban hanyoyi. Kuma gaba xayan jama'a, babba da yaro, kowa ya yarda da hakan kai tsaye. Har ta kai maqiyan musulunci ma sun miqa wuya. To, ka ga kenan, a haka shi ne wanda ya cancanci zama shugaba. Idan kuwa kasancewarsa Siddiqi xin nan, ba ta wajabta kasancewarsa shugaba ba, to, wannan hujja da 'yan Shi'ah ke qoqarin kafawa ta sha kara tanda.

## 4.27 Ayar: ﴿ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمْوَٰلَهُم بِٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ سِرًّا وَعَلَانِيَةً ﴾ البقرة: ٢٧٤

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta ashirin da bakwai ita ce: Faxar Allah Ta'ala: *Waxanda suke ciyar da dukiyarsu, a dare da yini, voye da bayyane (2:274).*

Ya ce: An samo ta hannun Abu Na'aimi, da isnadinsa zuwa ga xan Abbas, wanda ya ce: "Wannan aya ta sauka ne kan Ali *Raliyallahu Anhu.*

Saboda wasu dirhamomi da ya mallaka guda huxu. Ya bayar da sadaqar xaya da dare, xaya da rana. Xaya kuma a asirce, xaya a bayyane".

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Sa'alabi ma ya riwaito wannan magana. Ka ga hakan ba ta faru ga wani Sahabi ba, inji shi. Kenan Aliyu ne mafifici daga cikinsu sai ya zama shugaba.

**Martani:**

Martaninmu a kan wannan magana shi ne:

Mene ne ingancin wannan riwaya tukuna? Dole ne a yi bayanin yadda wannan riwaya ta inganta. Saboda kasancewarta ta Abu Nu'aimi da Sa'alabi. A qashin gaskiya ma dai, wannan riwaya qarya ce.

Sannan bayyanannen abu ne cewa, wannan aya gama gari ce. Duk wanda ya ciyar da wani abu saboda Allah, da dare ko da rana, a voye ko a bayyane, ya shiga qarqashin inuwarta. Saboda ya yi aiki da ita. Daxa Aliyun ne ko waninsa. Kuma hawa da gangararta na tabbatar da rashin hujjar wanda ya kevance wani mutum xaya da ita.

Xan Shi'ar kuma ba ya da labarin ya yi walle; domin kuwa abin da ya faxa a cikin wannan qagaggen hadisi ya yi takin saqa da abin da ayar ta qunsa. Bari ka ji: Ita ayar tana magana ne a kan waxansu lokuta biyu waxanda kowane zamani ya ke da, da kuma ciyarwa a cikinsu. Da kuma wasu halaye ko yanayoya biyu, waxanda dole ne kowane aiki ya kasance ya faru cikin xayansu; Wato dole ne idan za a bayar da labari, a ce: An yi kaza ne a daidai lokaci kaza. Shi kuwa lokacin nan, dole ne ya kasance dare ne ko rana; ba na uku. Shi kuwa aikin da aka yin, dole ne ya kasance an yi shi a voye ko a bayyane. Idan mutum ya ciyar da dukiyarsa cikin dare kuma a asirce, ya haxa abu biyu kenan, wato dare da asiri. Haka kuma idan ya ciyar da ita da rana kata, kuma quruquru kowa na gani. Shi ma ya haxa abu biyu, wato rana da sarari.

Da za mu qaddara cewa Aliyu ya ciyar, kuma a kansa ne waccan aya ta sauka. To, ai iyakar abin da ya yin bai fi ciyar da dirhami huxu ba kacal ko?! Kuma qofar aikata irin wannan aiki ai tana nan buxe hayan-hayan har ranar qiyama. Waxanda kuma ke shiga da fitowa suna komawa ta cikinta ba su qidayuwa. Babu wani musulmi da ke fatar alheri, yake kuma da iko, face ka taras ya ciyar da wani abu, da yardar Allah, wani lokaci da dare, wani lokaci kuma da rana. Wani lokacin kuma asirce, wani kuma a bayyane. Ka ga wannan ba wani abu ne da za a ce wani ya kevanta da shi ba. Balle ya zama wata siffa ta wanda ya kamata ya zama shugaba.

## 4.28 Ayoyin ﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ ﴾

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta ashirin da takwas ita ce: Abin da Ahmadu xan Hambali ya riwaito daga xan Abbas cewa: Babu wata aya a cikin Alqur'ani, wadda ke farawa da: *Ya ku waxanda suka yi imani* face Aliyu ne shugaba kuma liman a cikinsu, kuma jagora mafi girman daraja. Kuma wai Allah Ta'ala Ya zargi Sahabban Muhammadu a cikin Alqur'ani, a wurare da dama. Amma bai tava ambaton Aliyu face da alheri ba. Wai kuma wannan na nuna fifikonsa a kansu, da cancantar zamansa shugaba. Ka ji kai.

**Martani:**

Martaninmu a kan wannan magana zai kasance ta fuskoki kamar haka:

**Fuska ta farko:**

Muna son marubucin ya gaya mana yadda wannan magana ta inganta. Domin kuwa tabbas babu ta a cikin Musnadin Imamu Ahmad. Kuma ko da ya riwaito shi a cikin *Fadha'ilus Sahaba*, hakan kawai ba ta tabbatar da kasancewarsa ingantacce. Balle kuwa tabbas ne bai riwaito shi ba a cikin waxannan littafai nasa biyu. Yana dai daga cikin qare-qaren da *Qaxi'iy* ya yi.

**Fuska ta biyu:**

Ko shakka babu, wannan magana qarya ce aka yi wa xan Abbas. Domin kuwa ta tabbata ta hanya mutawatira cewa, a wajen xan Abbas xin, Abubakar da Umar su ne mafifita xaukaka a kan Ali. Kuma akwai waxansu abubuwa na Aliyun da yake qyama, har ma yake aibanta shi da su. Akwai kuma wasu al'amurra da yake ganin ko alama Ali bai kyauta ba a cikinsu. Har yake cewa, a lokacin da Ali *Raliyallahu Anhu* ya qona zindiqan da suka naxa masa rawanin ubangizantaka: "Da ni ne Ali, ba zan qona su ba, saboda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya hana a yi horo da wuta. Zan kawai sare kawunansu ne. Saboda cewar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi: Kuma ku kashe duk wanda ya canza addininsa". Buhari da waninsa ne suka riwaito wannan hadisi.

A lokacin da wannan magana ta kai kunnen Ali, sai ya ce: "Oh, Allah Ya jiqan uwar xan Abbas."!.

**Fuska ta uku:**

Ce wa Aliyu ne shugaban sahun *Ya Ayyuhal-Lazina Amanu* ba yabo ne ba. In ko sun nace, sai mu ce, to, ga wata ayar: *Ya ku waxanda suka yi imani! Don me kuke faxin abin da ba ku aikatawa? Ya girma ga zama abin qyama a wurin Allah, ku faxi abin da ba ku aikatawa (61:2-3).*

To, ita ma wannan Ali shugaban sahun waxanda aka kira a cikinta? Akwai ire-iren wannan ayar da dama.

**Fuska ta huxu:**

Daidaitattar fahimta ita ce, wannan lafazi na *waxanda suka yi imani* ya haxa har da Ali *Raliyallahu Anhu,* duk da yake ba shi ne dalilin maganar ba. Ko shakka babu yadda lafazin ya haxa har da waninsa, ya haxa da shi. Babu wata wariya a cikin lafazin wannan aya tsakanin wani mumini da wani.

**Fuska ta biyar:**

Cewar da xan Shi'ar ya yi wai wasu Sahabbai sun ce: Ali shi ne shugaba kuma Imamin irin waxannan mutane, jagora kuma mafi girman daraja a cikinsu, magana ce da babu tabbas a cikinta.

To, ja ta ma hakan. Mu qaddara cewa suna nufin Ali ne farkon wanda aka yi magana da shi, ta wannan lafazi. To, ko a ha kan maganar ba ta shiga. Domin kuwa yanayin zancen na tafiya ne tare da kundume waxanda ake zancen da su, bai xaya; bai ware wani sashe, da abin da bai shafi wani sashe ba.

Iyakar abin da kuke godogo da shi a cikin wannan magana, na san duk bai fi cewar da kuka yi xan Abbas na fifita Ali a kan sauran Sahabbai ba. Tattare kuma da kasancewar wannan magana qarya, wadda aka yi ma shi, da takin saqar da maganar ta yi da abin da aka sani na zantukansa. To, mu qaddara ya ce hakan. Mu kuma kau da kai daga ban hannun makafi da ya yi da Jumhuru. Duk da haka, ba yadda za a yi hakan ta iya zama hujja.

**Fuska ta shida:**

Kowa ya san cewa, cewar da xan Shi'ar ya yi, wai haqiqa Allah Ya zargi Sahabban Muhammadu a cikin Alqur'ani a wurare da dama. Amma bai tava ambaton Ali ba face da alheri, qarya ce lafiyayya. Domin kuwa ba a tava jin inda Allah Ya zargi Abubakar a cikin Alqur'ani ba. Ai Alqur'ani ba a voye yake ba. Kai, ba a ma tava jin Abubakar ya sava wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba, balle. Abin da ma aka riwaito daga gare shi *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne abin da ya tava cewa a cikin wata huxuba: "Ya ku mutane! Ku kiyayi mutuncin Abubakar. Ku sani bai tava sava mani, da xai rana ba".

**4.29 Ayar:** ﴿صَلُّواْ عَلَيۡهِ وَسَلِّمُواْ تَسۡلِيمًا ٥٦﴾ الأحزاب: ٥٦

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta ashirin da tara ita ce: Faxar Allah Ta'ala:

﴿ إِنَّ ٱللَّهَ وَمَلَٰٓئِكَتَهُۥ يُصَلُّونَ عَلَى ٱلنَّبِيِّۚ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ صَلُّواْ عَلَيۡهِ وَسَلِّمُواْ تَسۡلِيمًا ٥٦ ﴾ الأحزاب: ٥٦

*Lalle, Allah da mala'ikunsa suna salati ga Annabi. Ya ku waxanda suka yi imani! Ku yi salati a gare shi, kuma ku yi sallama domin amintarwa a gare shi (33:56).*

Ya zo a cikin Sahuhul Buhari daga Ka'abu xan Ujrata, wanda ya ce: Mun tambayi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bayan saukar wannan aya da cewa: Ya kai Manzon Allah, ya za a yi salati gare ku mutanen Babban Gida? Domin Allah Ya riga ya sanar da mu yadda za mu yi sallama. Sai ya ce: Ku ce "Ya Ubangiji ka daxa tsira a kan Muhammadu da mutanen gidansa.

Ya kuma zo inji xan Shi'ar a cikin Sahihu Muslimu cewa, mun ce wa Manzon: "Ya Manzon Allah! Ita sallama mun riga mun san yadda za mu yi maku ita, to salati fa"? Sai ya ce: Ku ce "Ya Ubangiji ka daxa tsira a kan Muhammadu da mutanen gidansa. Kamar yadda ka daxa tsira a kan Ibrahimu da Mutanen gidansa".

Xan Shi'ar ya kammala da cewa: Ko shakka babu kuwa Aliyu shi ne mafi xaukaka a cikin mutanen gidan Muhammadu. Saboda haka ya fi kowa cancanta da shugabanci.

**Martani:**

Ko shakka babu wannan hadisi, ingantacce ne. Kuma Buhari da Muslimu sun haxu a kan sa. Kuma lalle Ali *Raliyallahu Anhu* na daga cikin mutanen gidan Muhammadu, da ke cikin salatin.

Amma kuma wannan xaukaka ba ta kevanci Aliyun kawai ba. Balle ta zama wani abin hura hanci. Domin kuwa gaba xayan zuri'ar Hashimu, da ta haxa da Abbas da zuri'arsa da Harisu xan Abdul-Muxxalabi da zuri'arsa, duk suna cikin wannan ayari. Haka 'ya'yan Annabi mata; Ruqayyatu da Ummu Kulsumi da Fatima, da gaba xayan matansa, duk suna cikin wannan ayari, kamar yadda ya tabbata a cikin Buhari da Muslimu, cewa Manzon ya ce: "Ya Ubangiji ka daxa tsira a kan Muhammadu da matansa da zuri'arsa".

Kai! Ba waxannan kawai ba, duk wanda ke da wata dangantaka da Manzon Allah, a matsayin xan cikin gida, har ranar da Allah Ya naxe qasa, na cikin wannan ayarin albarka. Kar ka yi tsammanin na manta da 'ya'uwan Ali su Ja'afaru da Aqilu, su ma suna ciki.

Ka ga sanannen abu ne sarai cewa, shigar waxannan mutane qarqashin wannan inuwa ta tsira da aminci, ba ta nufin sun fi duk wanda bai sami shiga ciki ba. Balle har hakan ta sa waninsu cancanta da shugabanci, ko ya kevanta da shi.

**4.30 Ayar:** ﴿ مَرَجَ ٱلْبَحْرَيْنِ يَلْتَقِيَانِ ﴿١٩﴾ بَيْنَهُمَا بَرْزَخٌ لَّا يَبْغِيَانِ ﴿٢٠﴾ ﴾ الرحمن: ١٩ - ٢٠

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta talatin ita ce: Faxar Allah Ta'ala: *(Allah) Ya gauraye tekuna biyu (Ruwan daxi da na zartsi) suna haxuwa. A tsakaninsu akwai shamaki, ba za su qetare haddi ba (55:19-20).*

Ya ce: Ya zo a cikin tafsirin Sa'alabi ta hannun Abu Nu'aimi daga xan Abbas, wanda wai ya ce: Tekunan can biyu da Allah Ya garwaye na nufin Ali da Fatima. Shi kuma shamakin can da ke hana su qetare haddi, shi ne Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Sannan aya ta gaban waxannan kaxan kuma, wadda ke cewa: *Lu'u'lu'u da Murjani na fita daga gare su (55:22)* Suka ce, Lu'ulu'in da Murjani, Hassan da Husaini kenan. Wai kuma babu wani daga cikin Sahabbai da ya sami irin wannan falala sai Ali. Sai ya zama shugaba kenan.

**Martani:**

Martaninmu a kan wannan magana zai kasance kamar haka:

Babu mai yin wannan magana da makamantanta, sai wanda bai san abin da yake faxa ba. Kuma wannan fassara ta 'yan Shi'ah, ko kaxan ba ta yi kama da tafsirin Alqur'ani ba; ta fi kama da renin hankali. Kuma irin wannan tafsiri na daga cikin irin tafsirin da, mulhidai da Qaramixawa da 'yan *Baxiniyyah* ke yi wa Alqur'ani. Kai sharrin ma da ke cikin wannan ya fi wanda ke cikin wancan. Hasali ma irin wannan tafsiri shishshigi ne da sukar lamirin Alqur'ani da babu wata suka da kushewa da za a yi masa, wadda ta kai ga irin ta.

Amma irin wannan shishshigi a cikin tafsiri, ba baqon abu ne ga 'yan Shi'ah ba. Kuma kaxan ma ka ji. Dubi abin da suka ce, wai kalmar *Littafi Mabayyani* a inda Allah ke cewa: *Kuma kowane abu Mun qididdige shi a cikin Babban Littafi Mabayyani* (36: 12) wai tana nufin Ali. Kuma wai kalmar *Uwar littafi* a inda Allah ke maganar Lauhul Mahfuz da ya ce: *Kuma lalle shi haqiqa, maxaukaki ne, bayyananne ne a cikin uwar littafi, a wurinmu. (43:4)* na nufin Ali, in ji su. Haka kuma wai kalmar *Bishiyar da aka la'anta* a inda Allah ke cewa: *Da bishiya wadda aka la'anta a cikin Alqur'ani. (17:60)* wai, na nufin Banu Umayyata.

Akwai irin waxannan fassarora da makamantansu da yawa a bakinsu, waxanda ba wanda zai riqa furuci da su sai wanda ba ya fatar samun gafarar Allah, bai kuma yi imani da Allah da littafinsa ba.

Akwai abubuwa da dama da ke tabbatar da wannan magana qarya ce:

**Abu na farko:** Ita ayar da ake magana a kanta a Makka ta sauka bisa haxuwar kan musulmi. Hasan da Husaini kuma a Madina aka haife su.

**Abu Na biyu:** Yi wa Ali da Fatima alkunya da tekuna, Hasan da Husaini kuma da kalmar Lu'ulu'u da Murjani. Duk abubuwa ne da harshen Larabaci ba ya xauka ta kowace fuska; daxa ga asalin kalma ko aro. To, ka ga kenan bayan qiren qaryar da xan Shi'ar ya yi wa Allah da Alqur'ani. Ya kuma yi wa harshen Larabci.

**Abu na uku:** Babu wani abu a cikin wannan al'amari da ya wuce irin wanda ke faruwa ga kowane xan Adam. Domin duk wanda ya auri wata mata har ta haifa masa 'ya'ya biyu, to wannan riga na iya shiga wuyansa.

**Abu na huxu:** Wani abu kuma da da ke qara tabbatar da qaryar wannan xan Shi'ah, a cikin wannan baquwar fassara tasa, shi ne: Ai Allah Ta'ala Ya ambaci cewa, Ya haxa wasu koguna biyu, a cikin wata aya da Yake cewa: *Kuma (Allah) shi ne Ya garwaya tekuna biyu, wannan mai daxi, mai sauqin haxiya. Kuma wannan gishiri-gishiri, gurvatacce (25:53).* Ka ga da a harshen Larabaci da na qur'ani, wannan kalma na nufin; Aliyu da Fatima da wannan ayar ta tabbatar da kasancewar xayansu abin zargi. Ahlus-Sunnah da Shi'ah kuwa duk ba su yarda da haka.

**Abu na biyar:** Ai ka ga cewa Allah Ta'ala Ya yi: *A tsakaninsu akwai shamaki, ba za su qetare haddi ba (55:20).* To, da waccan aya na magana ne a kan Alin da Fatimar, kuma shamakin shi ne Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* wanda shi ke hana xayansu ya kai farmaki ga xaya? To ka ga wannan magana ta fi kama da zargi, ba yabo ba.

**Abu na shida:** Ta kuma tabbata gaba xayan malaman tafsiri sun haxu a kan savanin wannan fassara ta xan Shi'ah. Kamar yadda Ibnu Jarir da waninsa suka ambata.

**4.31 Ayar:** ﴿وَمَنۡ عِندَهُۥ عِلۡمُ ٱلۡكِتَٰبِ ۝٤٣﴾ الرعد: ٤٣

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta talatin da xaya ita ce: Faxar Allah Ta'ala: *Da wanda yake akwai ilimin littafi a wurinsa (13:43).*

Ya ce, an samo ta hanyar Abu Nu'aimi daga Ibnul Hanafiyyah, wanda ya ce: Mai ilimin littafin can shi ne Aliyu xan Abu Xalib. A cikin tafsirin Sa'alabi kuma, samowa aka yi daga Abdullahi xan Salam, wanda ya ce: Na tambayi Ibnul Hanafiyyah cewa: Wane ne wanda ke akwai ilimin littafi a wurinsa? Ya karva mani da cewa: Shi ne Aliyu xan Abu Xalib. Wannan kuwa na nuna shi ne mafi xaukaka a cikin Sahabbai. Shi ne kuma ya dace da zama Imamu, inji xan Shi'ah.

**Martani:**

Muna son marubucin ya tabbatar mana da ingancin wannan abu da ya riwaito daga xan Salami da Ibnul Hanafiyyah. Ko da an qaddara kasancewar wannan riwaya ingantatta, ba za ta iya zama hujja karvavva ba. Domin kuwa abin da akasarin malamai suka tafi a kai ya sava masa. Kai ko shakka babu dai wannan magana qarya ce ake yi wa xan Abadussalami da xan Hanafiyyah.

Wani abin da ke tabbatar da kasancewar tafsirin xan Shi'ar nan shirme, shi ne: Ai Allah Ta'ala cewa Ya yi: *Ka ce, "Allah Ya isa zama shaida a tsakanina da ku, da wanda yake akwai ilimin littafi a wurinsa (13:43).* Ka ga da ayar na nufin Ali shi ne mai wancan ilimi na littafi, da kenan sai Muhammadu ya kafa shi sheda wa waxanda suka kafirta, a kan duk abin da zai gaya masu.

Sanannen abu ne kuwa, ko da Aliyu ya shede shi a kan Annabci, da dukan abin da zai faxa, hakan ba za ta daxe shi amfanin komai ba, balle ya rinjayi mutane da hakan a matsayin hujja. Ko kuma shedar tasa gare shi ta zama wani dalili abin kafawa. Kuma babu ma wanda zai miqa wuya ga Muhammadun saboda ita. Domin kafiran cewa za su yi: Ya aka yi Aliyu ya san haka. Lalle haxa baki suka yi da Muhammadu. Ka ga kenan a haka, su a wurinsu Muhammadu ne ya tsaya wa kansa a matsayin sheda. Kafiran kuma na iya cewa, to ai Aliyu qanin Annabi ne, kuma yana daga cikin waxanda suka fara imani da shi, abu ne mai sauqi su haxa baki don a yaudari mutane.

Amma ka ga da Ahlul-Kitabi za su tsaya wa Muhammadu shedu, a kan Annabcinsa da duk abin da zai faxa, ta hanyar amfani da abin da suka sani daga Annabawansu, da wannan sheda za ta yi amfani. Kamar yadda da a ce Annabawan na raye suka kuma shede shi a kan haka, za ta yi. Duk abin xaya ne.

Amma ka ga saboda kasancewar wannan xan Shi'ar jahili, ya zaci wannan abu xaukaka ce ga Ali. Bai san ha kansuka ce ya yi gare shi ba, da Annabin da, sanadiyyarsa ya zama mumini. Haka kuma wannan magana suka ce ga dalilan da ke xaure wa musulunci gindi. Babu kuwa mai irin wannan magana sai zindiqi, jahili wanda ya yi nisa a cikin kogin jahilci.

Idan dai xan Shi'ar yana sane ya yi wannan cavi, to, wannan musiba ce. Idan kuwa jahilci ne ya yi masa kanta, to, musibar ta qara kauri.

Allah Ta'ala Ya ambaci sheda a kan Annabcin Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* na iya fitowa daga Ahlul-Kitabi, a wurare da dama a cikin Alqur'ani. Kamar inda yake cewa: *Ka ce "Shin, kun gani, idan (Alqur'ani) ya kasance daga wurin Allah yake, kuma kuka kafirta da shi, kuma wani mai shaida daga Banu Isra'ila ya bayar da shaida a kan irinsa (46:10).*

To, ko xan Shi'ar na son ne ya ce mana Aliyu na daga cikin Bani Isra'ila?!.

**4.32 Ayar:** ﴿يَوْمَ لَا يُخْزِى ٱللَّهُ ٱلنَّبِىَّ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مَعَهُۥ﴾ التحريم: ٨

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta talatin da biyu ita ce: Faxar Allah Ta'ala: *Ranar da Allah ba Ya kunyatar da Annabi da waxanda suka yi imani tare da shi (66:8).*

Ya ce: Abu Nu'aimi ya riwaito hadisi ta hanyar Inbu Abbas, daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa: Farkon wanda za a zuba wa kayan adon aljanna shi ne Annabi Ibrahimu *Alaihis Salamu,* a kuma danqa masa takardar shedar badaxayantaka daga wurin Allah. Bayansa sai Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Saboda kasancewarsa zavavve a wurin Allah. Daga nan kuma sai Aliyu ya shiga tsakiyarsu, su garzaya zuwa aljanna. Sai kuma Ibnu Abbas ya karanta waccan aya da muka ambata, wato: *Ranar da Allah ba Ya kunyatar da Annabi da waxanda suka yi imani tare da shi (66:8).* Ya kuma ce: Shi ne Aliyu da Sahabbansa.

Xan Shi'ar ya ce: Wannan na nuna cewa Aliyu shi ne mafifici a kan duk wanda ba shi ba. Kenan shi ne Imamu.

**Martani**

Da farko muna son marubucin ya tabbatar mana da ingancin wannan riwaya. Domin muna sane da cewa, ba ta da asali. Kuma wannan riwaya qarya ce yanke. Domin zubin maganar na nuna cewa Aliyu ya fi Annabi Ibrahimu da Muhammadu girma saboda shi ne tsa kansu; sun yi masa fikafikai. Alhali kuwa Annabi Ibrahimu da Muhammadu su ne mafifita daraja a cikin halitta. Duk kuwa wanda ya fifita Aliyu a kansu, to, gara jakin gidansu da shi.

Abin da dai ya tabbata a cikin Buhari da Muslimu daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne, cewar da ya yi: Farkon wanda za a wa ado ranar qiyama shi ne Ibrahimu. Annabi bai ambaci kansa ba, balle Aliyu a cikin wannan hadisi. Kuma ka sani gabatar da Annabi Ibrahimu da Allah *Subhanahu WaTa'ala* Ya yi a cikin wannan sha'ani na tufatarwa, ba ya nufin ya fi Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* girman daraja kai tsaye.

Ka lura da kyau, cewa Allah *Subhanahu WaTa'ala* Ya yi: *Ranar da Allah ba ya kunyatar da Annabi da waxanda suka yi imani tare da shi. Haskensu yana tafiya a gaba gare su da jihohin damansu, suna cewa, Ya Ubangiji ka cika mana haskenmu, kuma ka yi mana gafara. Lalle kai, mai ikon ne a kan dukan kome (66:8).* A wata surar kuma Ya ce: *Ranar da za ka ga muminai maza da mata, haskensu na tafiya a gaba gae su, da kuma dama gare*

*su. (Ana ce musu): Bushararku a yau, ita ce gidajen aljanna, ruwa na gudana daga qarqashinsu suna masu dawwama a cikinsu. Wannan shi ne rabo mai girma (57:12).*

Ka ga nassin ayoyin gama-gari ne da ya kundume gaba xayan muminan da ke tare da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. kuma hawa da gangarar zancen na tabbatar da haka. Haka ma gaba xayan fassarorin magabata na da alaqa da waxannan ayoyi, na tabbatar da gamagarancinsu.

**4.33 Ayar:** ﴿أُوْلَٰٓئِكَ هُمۡ خَيۡرُ ٱلۡبَرِيَّةِ ۝٧﴾ البينة: ٧

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta talatin uku ita ce: Faxar Allah Ta'ala: *Lalle ne waxanda suka yi imani, kuma suka aikata ayyukan qwarai, waxannan su ne mafifita alherin, halitta (98:7).*

Ya ce: Hafiz Abu Nu'aimi ya riwaito da isnadinsa zuwa ga xan Abbas, wanda ya ce: Lokacin da wannan aya sauka, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce wa Ali *Raliyallahu Anhu*: Za ka zo ranar qiyama, kai da jama'arka kuna masu yarda da Allah, kuma yardaddi a wurinsa. Maqiyanka kuma za su zo suna abin qi da qyamar gani. Xan Shi'ar ya ce: To, tunda ko har shi ne mafificin halitta, babu ko wanda ya cancanta da zama shugaba in ba shi ba.

**Martani**

Da farko, sai mu ce masa: Wanda bai ga uwarsa ba yana maganar kakarsa? Fara tabbatar da ingancin wannan batu, sannan ka gina son ranka a kansa. Mu dai ba mu da wani kokwanto a kan kasancewarta qaraya. Gaba xayan qungiyoyin musulmi sun haxu a kan cewa, riwayar Abu Nu'aimi in ba an tantance ta ba, to, da ita da babu uwarsu xaya ubansu xaya

Kuma kan malamai da ma'abuta sanin sirrin riwayoyi ya haxu a kan cewa, wannan riwaya na daga cikin qagaggin riwayoyi.

Wani abu kuma shi ne, wannan qagaggen tafsiri na xan Shi'ar, ya ci karo da irinsa, na waxanda ke cewa: Mutanen can da suka yi imani suka kuma aikata aikin na qwarai su ne Nasibawa, masu adawa da Ali kamar Harijawa da makamantansu. Harwayau kuma waxannan mutane na cewa: Duk wanda ya jivinci Ali, ya kafirta. Da shi da shiga qarqashin inuwar wannan aya fau-fau. Kuma hujjarsu a kan wannan magana ita ce: Faxar Allah Ta'ala: *Wanda bai yi hukunci ba da abin da Allah Ya saukar, to, waxannan su ne kafirai (5:44).*

Suka ce: Duk wanda ya sa wasu maza su yi hukunci a cikin addinin Allah, ya yi hukunci kenan da abin da Allah bai saukar ba, kuma ya kafirta. Duk kuwa wanda ya jivinci kafiri shi ma kafiri ne. Saboda Allah Ta'ala na

cewa: *Kuma wanda ya jivince su daga cikin ku, to, lalle ne shi yana cikinsu (5:51)* .

Suka kuma qara da cewa: Da Ali da Usmanu *Raliyallahu Anhuma* da duk wanda ya riqe su abin jivinta, wai riddaddu ne daga addinin Allah. Saboda abin da ya faru sanadiyyar su, bayan wucewar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama,* wanda ma ya bayar da labari a kansa da cewa: "Wallahi za a kori wasu maza daga wurin kogina kamar yadda ake korar baqon raqumi daga mashayar ruwa. Sai in ce: Ya Ubangiji ai waxannan Sahabbaina ne. sai a karva mani da cewa: Haqiqa kai ba ka san abin da suka haddasa ba bayanka; ba su gushe ba suna fita daga addini sannu-sannu, tun lokacin da ka rabu da su".

To, waxannan su ne waxanda suka yi hukunci da abin da Allah bai saukar ba, a kan jinainan musulmi da dukiyoyinsu. In ji Harijawa.

Hujjar da suka kafa a kan wannan hukunci da suka yi ita ce, cewar da Annabi ya yi: "Kada ku koma kafirai bayana; sashenku na saran wuyan sashe".

Suka ce: Duk kuwa waxanda sashensu ya koma yana saran wuyan sashe, babu shakka, sun koma kafirai bayan wucewar Annabi.

Duk da kasancewar waxannan hujjoji na Harijawa da makamantansu varna tabbas. To hujjojin nan da 'yan Shi'ah ke kafawa sun fi su zama varna, domin Harijawa sun fi su hankali da gaskiya tare da biyar sawunta. Kuma sukan kwatanta gaskiya kodayaushe. Idan ma ka ce ba su qarya, ba ka yi qarya ba. Saboda su mutane ne ma'abuta addini fai da voye. Illah dai kawai jahilci ya yi masu kanta. Wanda har ya kai su faxawa cikin halaka da fita daga addinin musulunci kamar yadda kibiya ke fita daga cikin baka.

Inda dai qarya da jahilci da biyar son zuciya suka yi sansani, sai ga 'yan Shi'ah. Kuma mafi yawa daga cikin shugabaninsu da Ya'ayyuhan nasun cikinsu duk zindiqai ne, mulhidai. Ba su da wata sha'awa da ilimi da kishin addini. Kai!

> *Ba su biyar kome face zato da abin da rayukansu ke sha'awa,*
> *alhali kuwa shiriya ta daga wajen Ubangijinsu, ta je masu*
> *(53:23).*

Ko shakka babu, cewar da Allah Ta'ala ya yi: *Lalle ne waxanda suka yi imani, kuma suka aikata ayyuka na qwarai (98:7)* magana ce gama-gari da ta haxe duk wanda ya siffanta da wannan sifa. To, me zai sa a kevance Shi'ah da zancen, har kuma da wajabta hakan?

Da 'yan Shi'ah sun ce: Mun yi haka ne saboda duk wanda ba xan Shi'ah ba kafiri ne. Sai mu karva mu ce: Da akwai dalilin da ke tabbatar da kafircin wanda ba su ba, da hakan ta wadatar da ku daga wannan dogon surrutu. Idan kuwa hakan can ba ta tabbata ba, to, wannan dalili da kuka kafa ba zai amfana maku komai ba. Domin kuwa ba ya da magarzai ta fuskar naqali. Idan kuma

har akwai wani dalili da za ku iya tabbatar da kasancewar duk wanda ba xan Shi'a ba kafiri, to, ba ko wannan aya ba.

Wani abu kuma da ke tabbatar da qaryar 'yan Shi'ah a cikin wannan magana, duk bai fi tsomo xan Abbas a ciki ba. Domin kuwa sanannen abu ne ta hanya mutawatira cewa, xan Abbas na da kyakkyawar alaqa da waxanda ba 'yan Shi'ah ba fiye da yadda yake da ita da, da yawa daga cikinsu ko ma dukkan su. Ko 'yan Shi'ah, da yawa yakan zauna tare da su, ya ba su fatawowi, ya yi ja-in-ja da su. Ka ga da yana da imanin cewa 'yan Shi'ah ne kaxai waccan aya ke magana a kai, a matsayinsu na kawai waxanda suka yi imani suka kuma aikata aiki na qwarai, duk kuma wanda ba su ba kafiri ne, to, da bai aikata ko wani abu mai kama da haka ba.

Idan aka lura da kyau za a ga cewa kafin wannan aya, cewa Allah Ta'ala Ya yi:

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ وَٱلْمُشْرِكِينَ فِى نَارِ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَآ ۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمْ شَرُّ ٱلْبَرِيَّةِ ﴿٦﴾﴾ البينة: ٦

> *Lalle ne waxanda suka kafirta daga mutanen littafi da mushrikai, suna cikin wutar jahannama, suna madawwama a cikinta. Waxannan su ne mafi sharrin talikai (98:6).*

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أُوْلَٰٓئِكَ هُمْ خَيْرُ ٱلْبَرِيَّةِ ﴿٧﴾﴾ البينة: ٧

Daga nan kuma Ya ce:

> *Lalle ne waxanda suka yi imani, kuma suka aikata ayyukan qwarai, waxannan su ne mafifita alherin halitta (98:7).*

Ka ga kenan wannan aya ta biyu, na bayyana cewa, mutanen da take magana a kansu, wasu mutane ne, da suka sha banban da waxancan na cikin waccan ayar, wato Mushrikai da Ahlul-Kitabi. Kuma ai akwai wurare da dama a cikin Alqur'ani, inda Allah Ya ambaci *Waxanda suka yi imani suka kuma aikata ayyuka na qwarai*. Kuma dukan ayoyin gama-gari ne. To laifin me wannan aya ta yi da za a mayar da ita kaxai, saniyar ware?

### 4.34 Ayar: ﴿فَجَعَلَهُۥ نَسَبًا وَصِهْرًا﴾ الفرقان: ٥٤

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta talatin da huxu ita ce: Faxar Allah Ta'ala:

﴿وَهُوَ ٱلَّذِى خَلَقَ مِنَ ٱلْمَآءِ بَشَرًا فَجَعَلَهُۥ نَسَبًا وَصِهْرًا ۗ وَكَانَ رَبُّكَ قَدِيرًا ﴿٥٤﴾﴾ الفرقان: ٥٤

*Kuma (Allah) shi ne Ya halitta mutum daga ruwa, sai Ya sanya (alaqarsa) zumunta da surukuta, kuma Ubangijinka Ya kasance mai ikon yi (25:54).*

Ya ce: Ya zo a cikin tafsirin Sa'alabi daga Ibnu Sirina, wanda ya ce: Wannan aya na magana ne a kan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Aliyu xan Abu Xalib, wanda ya aurar wa da Fatima. Saboda haka ne wannan aya ta sauka.

Xan Shi'ar ya qara da cewa: Ka ga wannan ba ta tabbata ga kowa ba sai Ali. Saboda haka ya fi kowa, kenan shi ne Imamu.

**Martani:**

Muna son marubucin ya tabbatar mana da ingancin wannan riwaya. Don ko shakka babu wannan qarya ce ake yi wa Ibnu Sirina. Ko da ta tabbata kuma ya faxe ta, to, haka kawai bata sa ta zama hujja. Domin sauran malamai sun sava masa a kan haka.

Wannan aya na cikin suratul Furqani ne. Ita kuwa wannan sura a Makka ta sauka. Kuma kan mutane ya haxu a kan cewa wannan aya da muqarrabanta na daga cikin ayoyin da suka sauka a Makka na surar, kafin Aliyu ya auri Fatima. To, ta yaya za a ce an saukar da ita ne a kan sha'anin aurensu?!

Tabbataccen abu ne cewa, wannan aya na magana ne a kan kowace zumunta da kowace surukuta; ba ta ware wani mutum ta bar wani ba.

Mu qaddara cewa ayar na magana ne a kan surukutar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Ali. To, wannan surukutar kawai ba ta isa tabbatar da kasancewar Ali mafi xaukaka a kan wanda ba shi ba, bisa haxuwar Ahlus-Sunnah da 'yan Shi'ah. Domin kuwa babu xaya daga cikin halifofin huxu wanda bai da surukuta da Annabi. Tattare kuma da tabbatar kasancewar wasu daga cikinsu mafiya xaukaka a kan wasu. Ka ga inda surukutar ce za ta sa mai ita zama mafi xaukaka, da hakan ta haifar da tuqa da walwala.

**4.35 Ayar:** ﴿وَكُونُوا مَعَ الصَّادِقِينَ ﴿١١٩﴾﴾ التوبة: ١١٩

Xan Shi'ar ya ce; Hujja ta talatin da biyar ita ce: Faxar Allah Ta'ala:

﴿يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا اتَّقُوا اللَّهَ وَكُونُوا مَعَ الصَّادِقِينَ ﴿١١٩﴾﴾ التوبة: ١١٩

*Ya ku waxanda suka yi imani! Ku bi Allah da taqawa, kuma ku kasance tare da masu gaskiya (9:119).*

Ya ce, wai kenan Allah Ya wajabta mana kasancewa tare da wanda aka san mai gaskiya ne daga cikin Sahabbai. Babu kuwa mai iya kasancewa haka

sai ma'asumi. Saboda haka duk yadda wanda ba shi ba ya qasura, to, ba ya fin qarfin qarya. Tunda ko har Ali, wai ma'asumi ne, to, shi ake nufi nan. Don gaba xayan halifofin huxu, shi ne kawai ma'asumi. Wai haka kuma Abu Nu'aimi ya ce a cikin wani hadisi nasa, daga xan Abbas: Ayar ta sauka ne a kan Ali.

**Martani:**

Kalmar *Siddiqu* wato gaskatau, mataki ne na qoli a layin masu gaskiya. Kenan duk "Gasgatau" mai gaskiya ne, amma ba duk mai gaskiya ne gasgatau ba. Kuma kai ka sani da yawa sun tabbatar da kasancewar Abubakar *Raliyallahu Anhu* gasgatau. Ka ga kenan wajibi ne ayar ta kasance tana magana ne har a kansa, ta rungume shi kam. Kai! Shi ne ma wanda ya fi cancanta da ayar ta nufa, fiye da wanda ba shi ba daga cikin Sahabbai.

Kuma idan har mun kasance tare da Abubakar *Raliyallahu Anhu* mun kuma aminta da ingancin halifancinsa. To, babu abin da zai sa mu yarda da kasancewar Ali shugaba ba shi ba. Ka ga kenan ayar ta yi gaba 'yan Shi'ah sun yi baya.

Kuma wannan aya, haqiqanin gaskiya, ta sauka ne a kan Ka'abu xan Maliku da wasu Sahabbai, a lokacin da suka qi fita yaqin Tabuka. Suka kuma gaya wa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* gaskiya cewa, ba su da wani uzuri a kan haka. Qarshe Allah Ya gafarta masu albarkacin wannan gaskiya da suka faxa. Maganarsu ta zo a ayar da take kafin wannan.

Kuma ko da wannan aya ta sauka a kan waxannan Sahabbai, babu wani mutum xaya da ake kaxa wa taken ma'asumanci. A kan haka ake da tabbacin cewa, cewar da Allah Ta'ala Ya yi: *Tare da masu gaskiya* haka xin kawai yake nufi. Don bai sharxanta kasancewar mai gaskiyar, ma'asumi ba.

Kuma ai Allah cewa Ya yi a kasance tare da "Masu" gaskiya. Ka ga wannan siga ce ta "Jam'i". Shi kuwa Aliyu "tilo" ne, Kenan ba shi ake nufi ba.

A qa'ida ta harshe, cewar da Allah Ta'ala Ya yi, a kasance *tare da masu gaskiya* na iya xaukar ma'ana biyu, ko dai: Ku kasance tare da su a cikin duk abin da yake gaskiya da muqarrabanta. Wato ku yi gaskiya kamar yadda masu gaskiya ke yi, kada ku yi qarya. Ka ga sai ma'anar ta zama kamar cewar da Ya yi:

﴿وَٱرۡكَعُواْ مَعَ ٱلرَّٰكِعِينَ ٤٣﴾ البقرة: ٤٣

*Ku yi ruku'i tare da masu ruku'i (2:43)*

Ko kuma a'a: Ku kasance tare da masu gaskiya a cikin komai; ko da ba ya da wata alaqa da gaskiya. Tirqashi.

Ma'anar ta biyun nan ba ta sauraruwa. Domin ba a cewa, wajibi ne mutum ya kasance tare da masu gaskiya har a cikin abubuwan halas na rayuwa. Kamar abinci da sha, da tufafi da makamantansu. A ce dole ya yi yadda suka yi kat-kat-kat.

A kan haka kenan ma'ana ta farko ita ce ingantatta. Babu wani umurni a cikin ayar a kan a kasance tare da wani mutum kevantacce. Ma'anar ayar dai, ita ce: Ku yi gaskiya, ka da ku yi qarya.

Yarda da wannan ma'ana a matsayin abin da ayar ke nufi, na sa a fahimci an yi wannan umurni ne saboda kasancewar gaskiya, na tabbatar da sauran ayyukan xa'a. Kamar yadda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Ina horon ku da, gaskiya. Saboda gaskiya na shiryarwa zuwa ga xa'a … Ka ga kenan wannan magana ta shafi duk wanda ya siffanta da gaskiya.

Mu qaddara cewa ayar na nufin a kasance tare da wanda aka "San" mai gaskiya ne. To, ai wannan kalma ta "Sani" daidai take da waccan kininta, a cikin faxar Allah Ta'ala: *To, idan kun "San" su muminai ne (60:10).* Ka kuwa san imanin wani ya fi gaskiya wuyar ganewa! To, idan kuwa har sharaxin na a "San" mutum da gaskiya ne kafin a kasance tare da shi, ya kuwa sava wa hankali a ce kalmar ta kevanta ga neman gane mai gaskiya kuma dole ya kasance ma'asumi. Kamar yadda ya sava wa hankali a nan, a taqaita kalmar ta "Sani" a kan tabbatuwar matan da ake magana a kansu ma'asumai.

Kuma ko da mun qaddara cewa, ayar na nufin a kasance tare da mai gaskiya, kuma lalle ya kasance ma'asumi. To, ba mu amince da ijma'in da ke cewa Ali *Raliyallahu Anhu* ne kawai ma'asumi ba. Ko banza kuma akwai mutane da dama waxanda suka fi 'yan Shi'ah alqadari, da ke jin shehunansu ne wannan aya ke magana a kai. Kuma su ma duk ma'asumai ne, wai. Duk da yake lafuzzan da suke amfani da su sun sha banban da 'yan Shi'ah. Amma dai duk da haka, ba mu yarda a ce su ba ma'asumai ba ne, Aliyu ne kawai. Ko dai a tabbatar masu da matsayin su duka, ko a hana wa kowa.

## 4.36 Ayar: ﴿وَٱرۡكَعُواْ مَعَ ٱلرَّٰكِعِينَ ٤٣﴾ البقرة: ٤٣

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta talatin da shidda itace: Faxar Allah Ta'ala: *Kuma ku yi ruku'i tare da masu ruku'i (2:43).*

Ya ce: An samo ta hannun Abu Nu'aimi daga xan Abbas *Raliyallahu Anhu* cewa, wannan aya ta sauka ne a kan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Ali kawai. Domin su ne farkon wanda ya yi sallah, ya yi kuma ruku'i. Ya ce: Wannan kuwa na nuna fifikon Ali, da shugabancinsa.

**Martani:**

Martaninmu a kan wannan magana zai kasance ta fuskoki kamar haka:

**Fuska ta farko:**

A wajenmu wannan riwaya ba igantatta ba ce. Kuma ga shi marubucin bai ambaci wani dalili da ke nuna ingancinta ba. Ga shi ko ma'abuta ilimin hadisi sun haxu a kan cewa wannan hadisi qagagge ne.

Da wannan ayana nufin a yi ruku'i ne tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Ali *Raliyallahu Anhu* to, da kuwa hukuncin yin hakan ya yanke a lokacin da suka rasu. Babu sauran wanda ake da buqata da ya yi ruku'i'tare da masu yin ruku'i.

Cewar da xan Shi'ar ya yi wai, Ali shi ne farkon wanda ya yi sallah tare da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* maganar kawai ce. Mafi yawan mutane na ganin cewa ba haka abin yake ba. Abubakar ya riga Ali mayar da gaba gabas yayi sallah.

Wani abun kuma shi ne: Da umurnin da wannan aya ta yi, na nufin a yi ruku'i ne tare da Manzon Allah, to, ko a haka, zancen ba ya nuna cewa wanda ya yi ruku'in tare da shi, lalle ne ya zama shugaba. Domin kuwa Ali *Raliyallahu Anhu* bai kasance shugaba a lokacin da Manzon Allah yake Annabta ba. Tattare kuma da kasancewarsa yana ruku'in tare da shi.

**4.37 Ayar:** ﴿وَٱجۡعَل لِّي وَزِيرٗا مِّنۡ أَهۡلِي ٢٩﴾ طه: ٢٩

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta talatin da bakwai ita ce: Faxar Allah Ta'ala:

*Kuma ka sanya mini wani mataimaki daga iyalaina (20:26).*

An samo ta hannun Abu Nu'aimi daga Ibnu Abbas, wanda ya ce: "Watarana muna a Makka, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kama hannun Ali da nawa. Ya yi sallah raka'a huxu. Sannan ya xaga hannayensa zuwa sama ya ce: Ya Ubangiji, musa xan Imrana ya roqe ka. Ni kuma yau Muhammadu, Annabinka ina roqan ka da ka buxa qirjina, kuma ka warware mini qullin da ke ga harshena. Don su fahinci maganata. Kuma ka sanya mini wani mataimaki daga cikin iyalaina. Ya kuma kasance Aliyu xan Abu Xalib; xan'uwana xin nan. Ka qarfafa halittata da shi. Ka kuma shigar da shi a cikin al'amarina".

Wai, kuma sai xan Abbas ya qara da cewa: "Sai na ji wani mai kira yana kira, yana cewa: Ya kai Ahmadu, haqiqa an karva roqonka".

Xan Shi'ar ya ce: Wannan nassi ne da ke tabbatar da Imamancin Ali.

To, muna bin sa bashin tabbatar da ingancin wannan magana, kamar yadda muka saba. Kuma ma'abuta ilimin hadisi sun haxu a kan cewa wannan hadisi qagagge ne kamar takwarorinsa da suka gabata waxanda ya kawo. Kai!

Yana daga cikin miyagun qaryace-qaryacen da aka yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* tabbas.

Kuma mafi tsawon zaman da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi a Makka, ba a haifi xan Abbas ba. Domin tarihi ya nuna cewa an haife shi ne a daidai lokacin da Bani Hashimu ke cikin kulokon batta. Kuma ko da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi hijira daga Makka xan Abbas bai kai shekarun iya banbancewa tsakanin ruwa da kalanzir ba. Balle ya isa shiga sahun masu yin arwalla su bi sallah.

Mu lura a nan da cewa, xan Shi'ar ya qara wata magana da bai yi irinta ba a baya. Ita ce, cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: *Ka kuma shigar da shi a cikin al'amarina (20:32).* Ka ga a nan ya fito fili ya nuna cewa Ali na tarayya ne da Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin Annabta, kamar yadda Haruna ke tarayya da Musa. Wannan magana kuwa, irin ta waxanda ke jin Aliyu Annabi ne, ce. Kuma cewa haka kafirci ne sara. Zance kuma ne na Shi'ah Gulatu, ba Shi'ah 'yan-sha-biyuh ba.

To, kuma ko a hakan ai, kasancewar wani abokin tarayyar wani, a cikin wani al'amari, ba ta nufin lalle ya maye gurbinsa bayansa kai tsaye. Kamar yadda kuke iqirarin wajabcin kasancewar Ali halifa kai tsaye, bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Bayan kuma ya kasance abokin tarayyarsa a cikin annabta, a lokacin da yake raye, wanda hakan ta sa wannan maqaryacin xan Shi'ar qarfin halin cewa wai, wannan hadisi nassi ne ke tabbatar da shugabancin Ali.

Ka ji xanbaya. Bari ka ji, ko akwai wani abu da wannan hadisi na qarya ke nunawa, duk bai wuce kasancewar Ali, abokin tarayyar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin sha'anin isar da mazancin, a lokacin da yake raye ba. Kamar yadda Haruna ya kasance abokin tarayyar Musa. Shin a shirye kake ka tsaya inda wannan nassi ya tsaya. Ka daina kafa hujja da magangaun maqaryata, da ya sassun zantukan 'yan'uwanka mavartanata, koko?!

## 4.38 Ayar: ﴿عَلَىٰ سُرُرٍ مُّتَقَٰبِلِينَ ۝٤٧﴾ الحجر: ٤٧

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta talatin da takwas ita ce: Faxar Allah Ta'ala:

﴿وَنَزَعْنَا مَا فِي صُدُورِهِم مِّنْ غِلٍّ إِخْوَٰنًا عَلَىٰ سُرُرٍ مُّتَقَٰبِلِينَ ۝٤٧﴾ الحجر: ٤٧

> *Kuma Muka zare duk damuwar da ke cikin zukatansu, suka zama 'yan'uwan juna a kan gadaje, suna masu fuskantar juna (15:47).*

Ya ce: An samo a cikin Musnadin Ahmad, da isnadinsa zuwa ga Zaidu xan Abu Aufa, wanda ya ce: Na shiga wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin masallacinsa. Na tayar da zancen zumuncin da ya qulla

tsakanin Sahabbai. Sai Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce, saura kaxan qashin bayana ya kare, nunfashina ya xauke, a lokacin da ka qulla zumunci a tsakanin Sahabbanka, Ya Manzon Allah. Idan ka yi haka ne, saboda masaniyar da kake da ita a kan cewa Allah ya yi hushi da ni, to, Allah Ya kyauta qarshenka, Ya kuma xaukaka darajarka.

Ali na sauka, sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Ina rantsuwa da wanda ya aiko ni Annabi, da gaskiya. Na aje wa kaina kai ne. Domin matsayinka a wurina, kamar matsayin Haruna ne a wurin Musa. Sai dai kawai babu wani Annabi bayana. Amma kai xan'uwana ne kuma magadina. Kuma za ka kasance tare da ni a cikin benena a aljanna. Tare kuma da 'yata Fatima. Kai xan'uwana ne, kuma abokin tafiyata".

Wai daga nan kuma Annabi sai ya karanta wannan aya. Xan Shi'ar ya kammala da cewa: Wannan zumunci da Manzon Allah ya qulla da Ali, dacewa ne da zozozon da ke tsakaninsu. Kuma wannan kevancewa da Ali ya samu da zumunta da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* na tabbatar da imamancinsa.

**Martani:**

Da farko, ina maganar ingancin wannan labari?. Muna ba da tabbacin cewa, babu wannan hadisi a inda ya faxa, ina nufin Musnadin Ahmad. Kai! Ahmad bai tava riwaito wannan hadisi ba; daxa cikin Musnad xin ko *Fadha'ilus-Sahabah*. Haka kuma xansa bai riwaito shi ba. Saboda haka cewar da wannan xan Shi'ar ya yi wai: An samo daga cikin Musnad na Ahamad qarya ce qwanqwasassa.

Abin da malaman hadisi suka faxa a kai shi ne, wannan hadisi na daga cikin qarairayin da Qaxi'i ya riwaito ta wata hanya daban ba ta hanyar Ahmad xan Hambali ba. Hanyar kuma duhu ce xib.

Kuma ka sani xan Shi'ar ya yi wa hadisin shan koko ne; bai ambaci cikonsa ba. Domin cikon hadisin shi ne: "Ali kai xan'uwana ne kuma magadina". Sai Ali ya yi farat ya ce: "Me zan gada daga gare ka, ya Manzon Allah?" Sai ya karva masa da cewa: "Abin da ake gado daga Annabawan da suka gabace Ni". Alin ya sake cewa: "Mene ne ake gado daga gare su?" Ya ce: "Littafin Allah da Sunnoninsu".

Amma kamar yadda muka gaya maka, isnadin wannan hadisi gurvatacce ne. Domin kuwa Abdulmumini xan Abbad kawai ya riwaito shi. Yana kuma daga cikin waxanda malaman hadisi suka yi wa radan-radan. Shi kuma ya karvo shi daga Yazidu xan Ma'anu, wanda malamai ba su tantance ko waye shi ba. Wataqila ma shi ya qaga hadisin. Don ya ce, ya karvo shi daga Abdullahi xan Sharhabilu, shi ma ba a san shi ba. Sannan wai, shi kuma ya karvo shi daga wani Baquraishe da ba a faxi sunansa ba, balle a gane ko waye shi.

Ba zaka yi mamaki ba idan ka ji cewa, ma'abuta hadisi sun haxu a kan qaryata irin wannan hadisi.

Ta kuma tabbata cewa, gaba xayan hadissan da ke magana a kan qulla zumunci tsakanin Muhajiruna, wasu-wasu. Da tsakanin Ansaru, wasu-wasu duk qarya ce. Kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai qulla zumunci tsakaninsa da Ali *Raliyallahu Anhu* ba. Bai kuma qulla shi tsakanin Abubakar da Umar ba. Ko tsakanin duk wani Muhajuri da Muhajuri xan'uwansa.

Zumuncin da ya qulla tabbas, shi ne na tsakanin Muhajiruna da Ansaru. Irin wanda ya qulla tsakanin Abdurrahman xan Aufi da Sa'adu xan Rabi'u. Da kuma tsakanin Salmanul-Farisi da Abud-Darda'i. Da kuma tsakanin Ali da Sahalu xan Hunaifu.

Kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi hidimar qulla wannan zumunci ne a unguwar Banun-najjari. Kamar yadda Anas ya bayar da labari a cikin wani hadisi ingattacce. Ba a cikin masallacin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* aka yi hidimar ba, kamar yadda qagaggen hadisin ya nuna. A'a, cikin gida ne da wani xan Banun-najjari ya gina a anguwar tasu, aka yi wannan hidima.

Ahlus-Sunnah da Shi'ah duka ba su yarda da cewar da xan Shi'ar ya yi wai, Annabi ya ce wa Aliyu: Kai xan'uwana ne kuma magadina. Domin kuwa idan xan Shi'ar na nufin gadon dukiya ne, to, hakan ba ta shiga. Domin kuwa Fatima *Raliyallahu Anha* ce mai wannan gado. Ko bayan ta kuwa, Ali bai gado in ga Abbas tun da matsayinsa a wajen gadon yana gaba da na Ali. Sannan Alin ba shi kaxai yake a matsayinsa na xan baffa ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba, akwai irin su Aqilu. Don me za a ce shi ne kaxai ke gadon ba da su ba?.

Idan kuma xan Shi'ar na nufin gadon ilimi ne da shugabanci. To, wannan ma maganar 'yan sanda ce, da ba a shiga xaki da ita. Kuma hujjar da suka kafa da ita ta tashi, idan aka dubi faxar Allah Ta'ala: *Kuma Sulaimanu ya gaji Dawuda (27:16)* da kuma faxarsa: *Sai ka ba ni wani mataimaki daga wajenka. Ya gaje ni (19:5-6).*

Ka ga kenan, idan wannan lafazin gado na nufin gadon dukiya da ilimi da shugabanci, kenan waxannan Annabawa, sun gadar da gaba xayan waxannan abubuwa. Kamar yadda ake son a ce Ali *Raliyallahu Anhu* ya gade su daga wurin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Wannan kuwa ko alama, ba haka abin yake ba.

A wurin Ahlus-Sunnah, Aliyu bai kevanta da gadon abin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya gadar na ilimi ba. Domin babu wani daga cikin Sahabbansa, wanda bai sami rabonsa gwargwado daga ciki ba. Kuma ilimi ba kamar dukiya ba ne. Ba a cewa sai an yi raba daidai a cikinsa, ta yadda wani ba zai fi wani ba. A'a, babu wata rigima a cikin sha'anin ilimi. Ba a cewa wannan

ba ya da ikon sanin abin da wancan ya sani. Kamar yadda ake iya hana wani, wani adadi na dukiyar da wani ya karva.

Wani abun kuma da ke tabbatar da kasancewar wannan hadisi qarya shi ne, abin da ya inganta a cikin Buhari da Muslimu cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya riga ya qulla zumuncinsa da wani ba Ali ba. Saboda ya ce wa Zaidu: "Kai ne xan'uwanmu kuma abin jivanta gare mu". Kuma lokacin da ya nemi auren Aishah, Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya ce masa: "Ashe kai ba xan'uwana ba ne?" Sai ya ce masa: "Eh, Ni xan'uwanka ne, amma 'yarka halas ce gare ni".

Haka kuma hadisi ya inganta Manzon ya tava ce wa Abubakar: "Sai dai muna nan matsayin 'yan'uwan musulunci".

Kuma duk waxannan hadisai da makamantansu, suna nan cikin ingantattun littafan hadisi. Ka ko ga hakan, na tabbatar da cewa kawai qulla zumunci irin wannan, ba ya hukuntar da zama abu xaya; kafaxa-da-kafaxa da abokin zumuncin ta kowace fuska, ko dacewa da zozozo.

To, tunda kuwa har haka ne, don me za a ce zumuncin da Annabi ya qulla da Ali, in har ya inganta, na hukuntar da imamancinsa da kasancewar mafi xaukaka daga cikin Sahabbai, alhali kuwa ba da shi ne kawai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya qulla zumuncin ba?

Ta tabbata a cikin hadisai ingantattu, ta fuskoki da dama, cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Da zan yi badaxayi daga cikin mutanen duniya, to da Abubakar ne. Amma ku sani Allah Ya riga shi. Ku toshe duk qofofi in banda ta Abubakar. Kuma haqiqa, Abubakar shi ne wanda abokantakarsa da abin hannunsa suka fi amfanarmu fiye da kowa daga cikin mutane".

To ka ga wannan magana ta Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na nuna irin martabobin da Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya kevanta da su; ba tare da wani ba. Kuma a bayyane take cewa, babu wani mahaluki a bayan qasa, wanda Annabi ke so, ko ke da qima a idonsa, ko wata xaukaka, ko wani matsayi na daban a wurinsa kamar Abubakar.

Kamar yadda ya zo a cikin Buhari da Muslimu cewa, an tambayi Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa: "Wane ne mafi soyuwar mutane a wurinka?" Ya ce: "Aishah". Aka ce: "Daga cikin maza fa?" Ya ce: "Mahaifinta".

A cikin Buhari da Muslimu harwayau, Umar *Raliyallahu Anhu* ya ce wa Abubakar: "Kai ne shugabanmu, kuma mutum mafi alheri daga cikinmu. Kuma mafi soyuwa daga cikinmu a wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama"*.

To, a haka, ka ga waxannan hadisai da kan ma'abuta ilimi ya haxu a kan ingancinsu, da karvar su hannu biyu-biyu; Kuma ba a sami wani masani da ya soki lamirinsu ba. Sun bayyana cewa, Abubakar shi ne mutum mafi soyuwa da xaukaka a wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* gaba da kowa.

Ka ga kenan da zumuncin da 'yan Shi'ar ke cewa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya qulla shi ne wannan. To, da babu wata jayayya tsakaninsu da waxannan hadisai. Amma karkata akalar tarihin da suka yi, ta hanyar ba shi wani matsayi da ba wannan ba. Ta sa waxannan ingantattun hadisai sun tabbatar da kasancewar nasu qarya.

Illa dai, abin da waxannan ingantattun hadisai ke tabbatarwa shi ne: Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya fi soyuwa a wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a kan Ali. Ya kuma fi shi matsayi a wurinsa. Ya kuma fi duk wanda ba Alin ba. Kuma dalilan da ke tabbatar da haka ba su qidayuwa.

Ta tabbata ta hanyar kusan mutum tisi'in daga Ali *Raliyallahu Anhu* yana cewa: "Mafi girman daraja a cikin wannan al'umma, bayan Annabinta, shi ne Abubakar sannan Umar". Buhari ya riwaito shi, a cikin ingantaccen littafinsa.

**4.39 Ayar:** ﴿وَإِذْ أَخَذَ ٱللَّهُ مِيثَٰقَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ﴾ آل عمران: ٨١

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta talatin da tara ita ce: Faxar Allah Ta'ala: *Kuma a lokacin da Ubangijinka Ya karvi (alqawali) daga xiyan Adamu, daga bayayyakinsu, a zuriyarsu, kuma Ya shaidar da su a kan rayukansu (Ya ce): "Shin, ba Ni ne Ubangijinku ba?" Suka ce: "Na'am, Kai ne"! Mun yi shaida!" (Ya ce): "Kada ku ce Ranar Qiyama "Lalle ne mu, mun rafkana daga wannan (7:172).*

Ya ce: An samo daga cikin littafin: *Al-firdausi* na Ibnu Shirawaihi, riwayar da ya xaukaka ta hanyar Huzaifatu xan Yamani cewa: "Da mutane sun san ko tun yaushe aka raxa wa Aliyu sunan Sarkin Musulmi, da ba za su yi musun xaukakarsa ba; An naxa masa wannan suna ne tun ba a halicci Annabi Adamu ba". Sai Annabi wai, ya karanta wannan aya. Wai sai mala'iku suka ce: "Tabbas haka ne". Sai Allah Maxaukakin Sarki Ya ce: "Ni ne Ubangijinku, muhammadu kuma shi ne Annabinku, Aliyu ko Shugabanku".

Allahu Akbar!!!

Kuma wai wannan inji xan Shi'ar nassi ne qarara da ke tabbatar da shugabancin Ali.

To, mun ji.

**Martani:**

Da farko dai, wannan hadisi bai inganta ba. Idan kuma xan Shi'ar na jin ba haka ba, to ga fili ga mai doki, sai ya tabbatar mana da yadda aka yi ya inganta.

Amma kar a manta fa, gaba xayan ma'abuta ilimin hadisi sun haxu a kan cewa, kasancewar mai littafin *Al-firdausi* kawai, ya riwaito hadisi, ba ta nuna cewa hadisin ingantacce ne. Tabbataccen abu ne cewa marubucin wannan littafi; wato Ibnu Shirawaihi Al-Hamadani Ad-Dailami ya ambaci hadissai ingantattu da dama a cikin wannan littafi. Ya kuma ambaci waxanda ba su kai su ba, har ma da qagaggu. Kuma kasancewarsa daga cikin ma'abuta ilimi da riqon addini, da rashin kasancewarsa mai yin qarya shi kansa, duk ba su hana ya naqalto abin da ya haxa da qarya da gaskiya a cikinsu. A haka sai aikinsa ya zama irin na da yawa daga cikin mutanen da suka tarkata hadisai kawai; masu kai da marar shi.

Ma'abuta ilimin hadisi sun haxu a kan kasancewar wannan hadisi qagagge ne.

Makamar maganar da ke cikin wannan aya ita ce, cewar da Allah ya yi: *Shin ba Ni ne Ubangijinku ba? suka ce "Na'am. Kai ne"! (7:172)* ka ga ba a ambaci wani Annabi a nan ba, balle wani shugaba.

Kuma xan dubi abin da Yake cewa a aya ta gaba: *Ko kuwa ku ce: "Abin sani kawai, ubanninmu suka yi shirka daga farko, kuma mu, mun kasance zuriya daga bayansu (7:173).* Ka ga kenan wannan aya na tabbatar da cewa alqawarin tauhidi ne tsintsa Allah Ya karva. Ba na Annabci ba, balle abin da ba shi ba.

Sanannun hadisan da ke cikin: Musnad da Sunan da Muwaxxa, da littafan tafsiri da wasu littafai duk, ba su qunshi wata magana mai kama da wannan ba. Da kuwa akwai ta, da gaba xayan mutane ba su yi biris da ita ba. Sai kawai a ji ta ga bakin wanda gaskiyarsa ba ta bayyana ba; hasali ma maqaryaci aka san shi?!

Wani abin lura kuma a nan shi ne: Wancan alqawari da Allah Ya karva a cikin ayar, Ya karve shi ne daga gaba xayan zuri'ar Adamu. Idan kuwa wancan tafsiri na 'yan Shi'ah ya tabbata, kenan wajibi ne Aliyu ya kasance shugaba a kan Annabawa baki xaya; tun daga Nuhu *Alaihis Salamu* har ka dire ga Muhammadu*Sallallahu Alaihi Wasallama*. Wannan kuwa magana ce irin ta mahaukata. Waxancan Annabawa sun wuce tun kafin Allah ya halicci Ali. To, ta yaya zai iya zama shugaba a kansu?.

Qololuwar abin da Aliyu ke iya zama shi ne shugaba a kan mutanen zamaninsa. Amma shugabancin waxanda aka halitta kafin sa, da waxanda za a halitta bayan sa, qarya ce da babu mai sheqa ta sai wanda bai san abin da yake faxi ba. Wanda kuma ba ya jin kunyar a kan abin zai fito bakinsa.

**4.40 Ayar:** ﴿فَإِنَّ ٱللَّهَ هُوَ مَوۡلَىٰهُ﴾ التحريم: ٤

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta arba'in ita ce: Faxar Allah Ta'ala: *Lalle Allah shi ne mataimakinsa, da Jibrilu da salihan muminai. Kuma mala'iku mataimaka ne a bayan haka (66:4).* Kan malaman tafsiri, inji shi, wai, ya haxu a kan cewa *Salihan muminai* a cikin wannan aya na nufin Ali *Raliyallahu Anhu.* Kuma Abu Nu'aimi ya riwaito da isnadin zuwa ga Asma'u 'yar Umaisu, wadda ta ce: "Na ji Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na karanta wannan aya, ya kuma kare da cewa, inji ta, wai salihan muminai xin nan na nufin: Aliyu xan Abu Xalib".

Shi kuwa mutumin ya cika zancensa da cewa: "Kevantuwar Ali da wannan matsayi na nuna fifikonsa a kan sauran Sahabbai. Kenan shi ne Imamu. Kuma ayoyin da ke tabbatar da shugabanin nasa sun fi bakin bunu". Ya ce: "Za mu taqaita a kan waxannan da muka ambata kar magana ta tsawaita".

**Martani:**

Da farko, cewar da ya yi, kan malaman tafsiri ya haxu a kan cewa *Salihan muminai* a cikin ayar na nufin Ali *Raliyallahu Anhu* qarya ce bayyananna. Babu wata haxuwa da suka yi a kan haka. Babu kuma wani malamin tafsiri ko na hadisi da ya naqalto haxuwar kan malaman (Ijma'i) a kan haka. To, daga bakin wa xan Shi'ar ya samo ijma'in ?

Kuma littafan tafsiri cike suke maqil da savanin wannan fassara. Domin kuwa Ibnu Mas'ud da Ikrimata da Mujahidu da Dhahhaku da wasunsu, duk cewa suka yi: "Salihan muminai a cikin wancan ayar na nufin Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma*". Kuma wasu malaman tafsiri irin su Xabari da wasunsu duk, sun kawo wannan magana.

Maganar kevance Ali da kasancewa *Salihan muminai* ba ta inganta daga bakin kowa ba, balle ta tabbata.

A bayyane take cewa cewar da Allah Ta'ala Ya yi: *Da salihan muminai* suna ne da ke game duk wani salihi daga cikin muminai. Kamar yadda ya zo a cikin Buhari da Muslimu cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Haqiqa mutanen gidan su wane ba mataimakana ba ne. Mataimakana kam, Allah da salihan muminai". Kasancewar muminan kirki mataimakan manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuwa ba ta nufin zamansu shugabanni a kansa.

Haka kuma xan Shi'ar ya ce, ayoyin da ke tabbatar da shugabancin Ali sun fi bakin bunu, wai. Amma muna da yaqinin cewa, komai yawansu, ba za su

amfane su da komai a cikin manufarsu ba. Ko da kuwa sun yi masu halin hankaka. Balle kuma mun san waxannan da ya ambata su ne tatattun abin da ke hannunsu na ayoyi. Illa dai ita qofar qarya buxe take har kullum gare su.

Da kowa zai xauki irin halinsu, da mutane da dama sun mayar masu da martani da irin qaryace-qaryacensu. Duk dai abin da kenan, kodayaushe Allah kan bice bilar qarya da mamakon ruwan gaskiya, itacen su jiqe, tokar ta bi ruwa. Boni kuma ya tabbata a kan maqaryata saboda abin da suka kasance suna aikatawa.

## 5.0 Zango Na Biyar
## Hujjojin Shi'ah Daga Cikin Hadissai

### 5.1 Hadisin Liyafar Kiran Jama'a

Xan Shi'ar ya ce: mataki na uku ya qunshi dalilai daga cikin hadisai goma sha biyu, waxanda aka riwaito daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*:

Hadisi na farko shi ne, abin da gaba xayan mutane suka riwaito, inji shi, cewa, a lokacin da ayar da ke cewa:

﴿ وَأَنذِرْ عَشِيرَتَكَ ٱلْأَقْرَبِينَ ﴿٢١٤﴾ ﴾ الشعراء: ٢١٤

*Kuma ka yi gargaxi ga danginka mafiya kusanci (26:214)*

ta sauka, sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tara jimlar mutane arba'in na Bani Abdulmuxxalibi a gidan Abdulmuxxalibin, ya sa aka shirya masu abinci na mudun alkama xaya da qafar akuya, aka kuma tanadi sa'i xaya na madara.

Gaba xayan taron nan suka ci suka kuma sha, daga wannan qwaryaqwaryar liyafa suka yi hani'an ba tare da sun rage ta da komai ba. Hakan kuwa ya ba su mamaki matuqa, domin kuwa akwai da yawa daga cikinsu wanda ke iya zaunawa ya yi kalaci da tuttunar akuya ya taushe da wasakin ruwa ko yawansa na madara. Da haka sai jikinsu ya fara gaya masu cewa, lalle wataqila wannan alamar Annabcin Muhammadu ce. Qarewarsu ke da wuya sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Ya ku zuriyyar Abdulmuxxalibi! Ku sani lalle Allah ya aiko ni da saqon gaskiya zuwa ga halitta baki xaya. Ya kuma aiko ni zuwa gare ku musamman, don ya ce mani: *Ka kuma yi gargaxi ga danginka mafiya kusanci (26:214).* Saboda haka nake kiran ku zuwa ga waxansu kalmomi guda biyu, masu sauqin faxi ga harshe masu nauyi a kan sikeli, waxanda za ku iya mallakar Larabawa da Bobayi da su, sauran al'ummomi kuma su zama raqumi da akala a hannunku, ku kuma sami shiga Aljanna ku tsira daga wuta, duk a sanadinsu. Waxannan kalmomi su ne: Ku sheda babu wanda ya cancanci bauta sai Allah, kuma ni Manzon Allah ne. Wane ne daga cikinku zai karva wannan kira nawa a cikin wannan al'amari ya kuma taimake ni a kan tabbatar da shi, wanda zai zama xan'uwana, mataimakina kuma wanda zai gaji halifata bayan na wuce?. Duk suka yi tsit.

Sai Amirul Muminina (Ali *Raliyallahu Anhu*) ya ce: Ni, ya Manzon Allah! Zan taimake ka a kan wannan al'amari. Sai Manzon Allah ya ce masa: Zauna. Ya sake tambayar su, babu wanda ya ce masa uffan. Sai na sake tashi, inji Ali *Raliyallahu Anhu* na karva masa kamar yadda na karva da farko. Ya sake cewa in zauna. Ya kuma sake maimaita yekuwar can tasa, karo na uku, babu wanda ya ce masa qala daga cikinsu. Na sake tashi na karva masa cewa, Ni zan taimake ka ya Manzon Allah, a kan wannan al'amari. Sai ya ce mani: "Zauna. Kai ne xan'uwana, mataimakina kuma wanda zai gaji halifata bayan

wucewata. Sai sauran mutanen suka tashi suna ce wa Abu Xalib: Ga irinta nan, gurinka ya cika, ka shiga addinin xan xan'uwanka, ga shi ya shugabantar da xanka a kanka.

**Martani:**

Za mu kore wannan hujja da dalilai guda takwas.

**Dalili na farko:**

Mene ne ingancin wannan labari?

Malaman da suka naqalci sirrin ilimin hadisi na sane da cewa, cewar da wannan marubuci ya yi gaba xayan mutane sun riwaito wannan hadisi qarya ce tsagwaronta.

Babu wani littafi daga cikin littafan malamai musulmi waxanda ake iya dogara da su a fagen ilimin riwaya, wanda ya zo da wannan Hadisi. Ina nufin gaba xayan *Sihahu* da *Masanidu* da *Sunanu* da *Magazi* da *Tafsirai* irin waxanda ake ambaton isnadi a cikinsu, waxanda kuma ake iya kafa hujja da su. A sane nake cewa, akwai wannan Hadisi a cikin wasu littafai na tafsiri, waxanda marubutansu ba su damu da ingancin hadisan da suke riwaitowa ba. A cikinsu akwai ingantattun hadisai da masu rauni, kamar tafsirin: Sa'alabi da Wahidi da Bagadadi, kai har ma da na Xabari da na Abu Hatim. Gaba xayan ma'abuta ilimi sun haxu a kan cewa kasancewar xaya daga cikin waxannan malamai ya riwaito hadisi, ba hujja ba ce a kan ingancinsa. To, tunda kuwa har ta tabbata cewa waxancan littafai akwai wake da shinkafa a cikinsu, to, dole ne a tabbatar mana da kasancewar wannan hadisi mai inganci ba mai rauni ba.

**Dalili na Biyu:**

Za mu iya karvar wannan qirarrar riwaya da xayan sharuxxa biyu; Ko dai marubucin ya kawo mana isnadin wannan hadisi, irin wanda masu ilimi ke kafa hujja da shi a lokacin da suke musayar ra'ayi, a cikin wata mas'ala ko da kuwa rava darni ce. Ko kuma ya kawo mana wani malamin hadisi xaya amintacce, irin wanda jama'ar musulmi ke dogara da maganarsa, wanda ya inganta wannan hadisi.

Na kawo waxannan sharuxxa ne, domin kuwa ga al'ada idan masana fiqihu guda biyu na musanyar ra'ayi a kan wata mas'ala ta furu'a, babu wanda zai tashi daga ra'ayinsa sai idan an kafa masa hujja da wani hadisi mai ingantaccen isnadi, irin wanda baya tunkuxuwa, ko wanda wani shahararre kuma amintaccen malamin hadisi ya inganta. Idan kuwa ba a samu xayan haka ba, sai dai a tashi kowa daga cikinsu yana a kan ra'ayinsa.

Wannan a cikin mas'aloli na hukunce-hukunce kenan. To ina ga sha'anin aqida wadda ita ce jigon addini? An wayi gari ana amfani da irin waxannan tatsuniyoyi ana sukar magabata da malaman wannan al'umma da

manufar rosa shikashikan musulunci. Ba zai yiwu ba ko kaxan, a cikin irin wannan muhimmiyar matsala, mu karvi kowane hadisi wanda ba a san isnadinsa ba, kuma babu wani malami daga cikin jigajigan malaman riwaya da ya tabbatar da zamansa hadisi balle ingancinsa.

**Dalili na uku:**

Masana hadisi sun tabbatar da kasancewar wannan hadisi qiren qarya. Saboda haka ne ma, babu xaya daga cikinsu wanda ya riwaito shi a cikin littafansu waxanda ake kafa hujja da su. Kai ko wanda ke da qanqanuwar masaniya da ilimin hadisi, ya san wannan hadisi qarya ne.

**Dalili na Huxu:**

A lokacin da wannan aya ta sauka yawan maza a cikin zuri'ar Abdulmuxxalibi bai kai arba'in ba. Domin kuwa ayar ta sauka ne a garin Makkah, a farkon al'amari. Kuma har Manzon Allah ya bar duniya mazaje daga cikinsu ba su kai wannan adadi ba.

**Dalili na Biyar:**

Cewar da marubucin ya yi wai akwai da yawa daga cikin zuri'ar Abdulmuxxalibi wanda ke iya zaunawa shi kaxai ransa, ya yi kalaci da tuttunar akuya ya taushe da wasakin madara. Wannan magana qarya ce, don a tarihi ba a san banu Hashim da irin wannan mugun ci ba. Babu wanda aka ji labarin yana kalaci da tuttunar akuya ko ya shanye wasakin madara.

**Dalili na Shida:**

Cewar da marubucin ya yi wai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Wane ne daga cikinku zai karva wannan kira nawa a cikin wannan al'amari, ya kuma taimake ni a kan tabbatar da shi, wanda zai zama xan'uwana, mataimakina kuma wanda zai yi halifanci bayana". Ko shakka babu wannan magana qarya ce suka yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Bai dace a jingina irin wannan magana gare shi ba. Dalili kuwa shi ne, imani da Allah da manzonsa tare da taimakon manzon a kan tabbatar da haka kawai, bai zama dalilin samun wancan matsayi.

Idan kuwa har tana zama dalilin hakan, ai gaba xayan muminai sun yarda da Allah da Manzonsa, sun kuma taimaki Manzon Allah a kan tabbatar da wannan aqida; sun sayar da rayuwarsu, sun saxaukar da dukiyarsu, sun bar garuruwansu, sun watsar da danginsu, sun yi haqurin xaixaicewa cikin garuruwansu bayan suna zaune wuri xaya. Sun yi haqurin walaqanci bayan a da su ne maxaukaka, sun yarda da talauci bayan a da suna cikin wadata, sun rayu cikin tsanani bayan a da suna cikin yalwa, ba don komai ba sai don yaxa addinin Allah da tabbatar da shi. Tarihin waxannan mazaje sannane ne a faxin duniya. Amma tattare da haka mafi yawa daga cikinsu ba su gaji halifar Manzon Allah bayan rasuwarsa ba.

To kuma idan har ta tabbata Manzon Allah ya faxi waccan magana a cikin mutum arba'in, to, ya ko kamata a ce gaba xaya ko mafi yawansu sun karva masa. To, idan xayan hakan ta faru, wane ne daga cikinsu zai gaje shi?

**Dalili na Bakwai:**

Wani abin da ke tabbatar da zaman wancan hadisi qarya, shi ne kasancewar ta tabbata cewa, Hamza da Ja'afaru da Ubaidatu xan Harisata duk sun karva wa Manzon Allah kamar yadda Ali ya karva masa a wancan lokaci.

**Dalili na Takwas:**

Abin da ya zo a cikin ingantattun littafan hadisi dangane da saukar waccan aya, ya sha bamban da abin da wannan marubuci ya kawo. Abin da ya zo a cikin Buhari da Muslimu shi ne: An samo daga Ibnu umar da Abu Hurairata daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*: A lokacin da ayar da ke cewa: *Kuma ka yi gargaxi ga danginka mafiya kusancin (26:214)* ta sauka, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kira Quraishawa suka taru, ya fara da su kafin sauran mutane, inda ya ce: Ya ku banu Ka'abu xan Lu'ayyu! Ku ceci kanku daga wuta, ya ku banu Murrata xan Ka'abu! Ku ceci kanku daga wuta, ya ku banu Hashimu! Ku ceci kanku daga wuta, ya ku banu Abdulmuxxalibi! Ku ceci kanku daga wuta. Ya ke Fatima 'yar Muhammadu! Ki ceci kanki daga wuta. Ku sani ba ni iya shiga tsakaninku da Allah. Iya abin da nake iya yi maku na haqqin dangantaka da zumunta zan yi".

## 5.2 Hadisin Ghadir ba Hujja ne ba

Hadisi na biyu a cewar sa, shi ne: Ingantaccen hadisi xan asuli, wanda aka samo daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa a lokacin da faxar Allah *Subhanahu WaTa'ala* ta sauka:

﴿ ۞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلرَّسُولُ بَلِّغۡ مَآ أُنزِلَ إِلَيۡكَ مِن رَّبِّكَۖ وَإِن لَّمۡ تَفۡعَلۡ فَمَا بَلَّغۡتَ رِسَالَتَهُۥۚ وَٱللَّهُ يَعۡصِمُكَ مِنَ ٱلنَّاسِۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٦٧ ﴾ المائدة: ٦٧

*Ya kai Manzo! Ka iyar da abin da aka saukar zuwa gare ka daga Ubangijinka (5:67).*

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi magana da mutane a cikin huxuba, a wani wuri da ake kira *Ghadir Khum*, ya ce masu: "Ya ku jama'a! Ashe ba ni da iko da ku fiye da yadda kuke da iko da kanku?" Suka ce, tabbas kana da shi ya Manzon Allah. Sai wai ya ce: "To, duk wanda nake da iko da shi Aliyu na da iko da shi". "Ya Ubangiji ka jivinci al'amarin wanda ya jivinci Ali, ka juya baya ga duk wanda ya juya masa baya, ka taimaki duk wanda ya taimake shi, ka kuma tozarta duk wanda ya tozarta shi". Wai kuma daga nan sai Umar ya ce: "Ai daxa ta qare. Daga yau kai ne ubangidana kuma ubangidan gaba xayan Musulmi da muminai maza da mata".

Mun riga mun ba marubucin amsa a kan wannan aya da wannan hadisi, tare da tabbatar masa da kasancewar yadda ya karkata akalar ayar, qarya. Don ayar ta sauka ne kafin hajjin bankwana da lokaci mai tsawo. Ita kuwa maganar da ya yi a *Ghadir Khum* ta kasance ne a ranar sha takwas ga watan Zul-hajji bayan ya kammala hajjinsa ya kama hanya zuwa gida. Watanni biyu bayan haka da wasu 'yan kwanaki sai Allah ya karvi ransa. Kuma tarihi ya tabbatar da cewa babu wani abu na shari'a da ya sauka ga Manzon Allah zuwa ga mutane, a ranar da ya sauka a *Ghadir Khum*, daxa ko, abin ya shafi Ali *Raliyallahu Anhu* ne ko waninsa, a kan sha'anin shugabanci ko wani abu wanda ba shi ba. Babu ko xaya.

A sane muke cewa, Tirmizi ya riwaito wannan labari da kuma Ahmad a cikin Musnad nasa. Amma iyakar abin da Annabi ya ce shi ne: "Duk wanda nake abin jivintar sa, to Ali ma majivincinsa ne". Amma abin da xan Shi'ar ya zo da shi na cewa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ci gaba da cewa: "Ya Ubangiji ka jivinci al'amarin wanda ya jivinci Ali, ka kuma bayar da baya ga duk wanda ya ba shi baya..." Ko shakka babu wannan qari ne kuma qiren qarya; Manzon Allah bai ce haka ba. Haka nan kuma cewar da ya yi wai Umar ya ce: "Daga yau kai ne ubangidan gaba xayan muminai maza da mata". Shi ma wannan qarya ce tabbas.

To, fita batun ma wannan baki xaya. Ita kanta waccan magana da ya ce Annabi ya ce: "Duk wanda nake abin jivintar sa, to Ali ma majivincinsa ne" Babu ta a cikin Sihahu, illa dai wasu malamai kawai suka riwaito ta. Wasu malaman kuma kamar su Buhari da Ibrahimul-Harbi da wasu da dama da cikin masana ilimin hadisi, suka tsaya cik a kan wannan sha'ani. A qarshe dai duk sun yi suka a cikin hadisin tare da raunana shi. Imamu Ahmad ne kawai aka samu ya inganta hadisin kamar yadda Tirmizi ya yi. Malam Abul-Abbas xan Uqdata ma har littafi ya wallafa inda ya tattara hanyoyin da aka samo hadisin ta su.

Ka ga tun daga nan mu Allah Ya hutar da mu, amsarmu ta samu qarin qarfi. Wato idan har ta tabbata Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai faxi wannan magana ba, to batu ya qare; Ummu ta gaida Aisha. Idan kuwa har ya faxe ta, to, lalle ba yana nufin Ali *Raliyallahu Anhu* zai gaji matsayinsa ne bayan ya wuce ba, don babu wani harafi a cikin maganar da ke nuna haka. Al'amari ko mai girma irin wannan lalle ne idan za a yi magana a kansa a yi ta dalla-dalla.

Ko shakka babu wannan hadisi baya nufin tabbatar da halifanci ga Ali *Raliyallahu Anhu*. idan kuwa don taqamar kalmar "Maula" ce, wadda Annabi ya yi amfani da ita a cikin hadisin, to, ta yi gabas ne shi kuwa xan Shi'ar ya yi yamma. Wannan kalma ta "Maula" da kalmar "Waliyi" xan Juma ne da xan Jumai; rawa xaya suke takawa. Don ka ga ai Allah *Subhanahu WaTa'ala* cewa Ya yi: *Abin sani kawai majivincinku Allah ne da Manzonsa, da waxanda suka yi imani (5:55)*. A wata ayar kuma ya ce: *Kuma idan kun taimaki juna a kansa, to, lalle ne Allah shi ne mataimakinsa, da Jibrilu da salihan Muminai. Kuma*

*mala'iku a bayan wannan mataimaka ne (66:4).* A cikin waxannan ayoyi guda biyu, Allah *Subhanahu WaTa'ala* ya bayyana cewa, akwai alaqa tsakanin shi da Manzonsa a gefe xaya, da salihan muminai a gefa xaya ta hanyar jivintar al'amari da taimakekeniya, gwargwadon iko da matsayin kowane vangare.

Wato jivintar al'amari da taimakekeniya a wannan tsakani, na nufin rahama da jinqai na ganin dama daga wurin Allah da Manzonsa zuwa ga muminai, da xa'a da bauta na yarda da amincewa daga wurin muminai zuwa ga Allah *Subhanahu WaTa'ala*. kamar dai yadda ta tabbata cewa tsakanin Allah *Subhanahu WaTa'ala* da muminai akwai son juna.

Kenan Allah shi ne majivincin al'amarin muminai kuma mataimakinsu. Don haka ne ma ya fitar da su daga cikin duhun kafirci zuwa ga hasken imani. To, tunda kuwa har haka ne, jivintar al'amari da taimakon Allah da na Manzonsa zuwa ga muminai, da kasancewar Ali *Raliyallahu Anhu* majivincin muminai na nufin so ne da qauna, savanin qiyayya da gaba. Irin wannan so da qauna ne kuwa, muminai ke yi wa Allah da Manzonsa gwargwadon matsayinsu. Babu kuwa wani mumini da ya fi wani a wannan matsayi. Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* kuwa na xaya daga cikin wanda ke so da qaunar muminai kamar yadda su ma suke so da qaunarsa.

A taqaice dai akwai banbanci matuqa tsakanin kalmomin *Waliyyu* da *Maula* waxanda muka qare sharhi a kansu, da kuma kalmar *Wali*. Kalmomi guda biyu na farko, kamar yadda bayani ya gabata, na nufin so da qauna, jinqai da taimako. Ita kuwa kalma ta biyu na nufin shugabanci. Kuma asalin waxannan kalmomi a tafsirin Larabci ba xaya ba ne.

Shi wannan hadisi da muke taqaddama a kansa ya zo ne da xayan waxannan kalmomi na farko, wato *Al-Maula* da *Al-Waliyyu.* A Hausance abin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce shi ne: "Duk wanda yake akwai so da jinqai tsakanina da shi, to, a samu hakan a tsakaninsa da Ali". Ba cewa ya yi: Duk wanda nake shugaba a gare shi, to Ali ya zama shugabansa ba.

Duk wanda ya fassara wannan hadisi da cewa, Manzon Allah na nufin ya zavi Ali *Raliyallahu Anhu* a matsayin halifansa, ya yi kuskure ba xan qarami ba. Wilayar da Annabi ke nufi irin ta so da qauna, na tabbata ne a matakin musaya tsakanin vangarora biyu: Wato soyayya da qawanceceniya. Kamar yadda muminai ke son Allah, shi kuma yana son su.

Kuma kasancewar Manzon Allah na da iko da muminai fiye da yadda suke da shi da kansu, daraja ce wadda shi kaxai ya kevanta da ita a duniya a matsayinsa na Annabi.

### 5.3 Hadisin Matsayin Ali

Hadisi na uku a cewarsa, shi ne faxar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da yake ce ma Ali: "Matsayinka a wurina kamar matsayin Haruna ne a wurin Annabi Musa. Sai dai ka sani babu wani Annabi a bayana". Wai da wannan zance ne Manzon Allah ya tabbatar wa Ali *Raliyallahu Anhu* da irin gaba xayan martabobin da Haruna ke da su, a wurin Annabi Musa ba tare da

rage komai ba. Daga cikin martabobin na Haruna kuwa akwai kasancewarsa halifan Annabi Musa, a lokacin da yake raye. To, da kuwa ya rayu bayan rasuwar Annabi Musa, da lalle ne zai gaji halifarsa, wanda savanin haka kuwa, zai tabbatar da wata kasawa a cikin zatinsa. Tunda kuwa har Haruna ya waqilci Annabi Musa a matsayin shugaban bani Isra'ila, a sakamakon 'yar tafiyar da ya yi don ganawa da Allah, to, babu wanda ya cancanci zama halifan Annabi Musa bayan rayuwarsa kamar shi Harunan.

**Martani:**

Amsarmu a kan wannan magana ita ce: Tabbas wannan hadisi gaskiya ne. Don Buhari da Muslimu da wasunsu, sun riwaito shi. Kuma Manzon Allah ya faxi wannan magana ne a lokacin da zai tafi yaqin Tabuka. Amma wannan ba abin tinqaho ba ne, don ba a kan sa aka fara ba. A duk lokacin da aikin Umara ko Hajji ya zo, ya kan waqilta wani daga cikin Sahabbai ya tsare birnin Madina. Kamar yadda ya waqilta Sayyidina Umar a lokacin da zai je yaqin da aka sani da suna *Gazwatu Dhi Amrin*. Ya kuma waqiltar da Bashiru xan Abdulmundhir a lokacin da zai je yaqin banu Qainuqa'a. Ya waqilta Abdullahi xan Ummu Maktumi a lokacin da ya je *Fur'u* don yaqar Quraishawa. Malam Muhammadu xan Sa'ad da waninsa duk sun ambaci wannan.

A taqaice dai, sanannen abu ne a tarihin musulunci cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai tava fita ya bar birnin Madina haka nan sake ba. Lalle ne ya waqilta wani ya tsare ta. Kuma littafan tarihi cike suke da jerin sunayen Sahabban da ya kan waqilta lokaci-lokaci don wannan aiki. Sau biyu Manzon Allah na tafiya aikin Umara daga Madina; Umarar "Hudaibiyya" da ta rankonta, don da ya je a karon farko bai samu yinta ba, ya dawo bisa ga yarjejeniyar da aka sani da suna *Sulhin Hudaibiyyah.* Ya kuma tafi hajjin bankwana. Su kuwa yaqoqa ya yi fiye da ashirin. A duk waxannan tafiye-tafiye Manzon Allah yakan naxa wani Sahabi ne ya tsare gari kafin ya dawo.

Wannan waqilci da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya naxa Ali *Raliyallahu Anhu* a wannan lokaci, shi ne mafi rauni da qarancin daraja bisa ga waxanda suka gabace shi. Dalili kuwa shi ne, a duk waxancan lokutan a kan taras cewa a cikin birnin na Madina akwai mazaje da dama, da shi wannan waqili zai shugabanta. Amma a wannan karo saboda girman Tabuka, Manzon Allah bai xauke wa kowa nauyin halartar yaqin ba, sai fa mata da qananan yara da tsofaffi. Sai ko marasa lafiya in akwai. Sannan an bar munafukai da wasu mutane guda uku da suka yi gangancin rashin fita, kuma daga bisani Allah ya yi masu afuwa.

Wannan dalili ne ya sa Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* ya fito yana kuka. Ya tunkari Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Ya Manzon Allah! Za ka bar ni a gari ba kowa ciki sai mata da qananan yara?

Ka ga tun a nan taba ta banbanta da garin gero. Don shi Haruna rundunar bani Isra'ila ce gaba xayanta Annabi Musa ya bar masa kulawa da ita,

shi kuwa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai bar komai ba a gida sai tattaka da baragurbi, in ka xebe shi sayyidina Alin xin *Raliyallahu Anhu*.

Kai aje ma duk wannan, idan muka dawo ga tsurar ruwan zatin harshe, za mu ga cewa, a duk lokacin da wani ya ce: matsayin wannan abu kamar ya ce ne: Abu kaza ya yi kama da abu kaza. Shi kuwa irin wannan, kamantawa ne kawai. Hakan ba ta nufin abubuwan guda biyu sun yi kunnen doki a cikin komai. A'a, yanayin zatin zancen ne alqali.

Dubi abin da Buhari da Muslimu suka riwaito, a lokacin da Manzon Allah ya shawarci Sayyidina Abubakar da Sayyidi Umar *Raliyallahu Anhuma* a kan makomar fursunonin yaqin cin garin Makkah, Abubakar ya ce, su fanshi kansu. Umar kuma ya ce, a aika su lahira. Sai Manzon Allah ya ce: Ku bari in yi maku fashin baqin matsayin waxannan mazaje biyu: Kai Abubakar ka yi kama da Annabi Ibrahim a cikin wannan shawara taka. Don cewa ya yi: *Sa'annan wanda ya bi ni, to, lalle shi, yana daga gare ni, kuma wanda ya sava mini, to lalle ne kai mai gafara ne, mai jinqai (14:56)*. Ka kuma yi kama da Annabi Isa, a inda ya ce: *Idan ka azabtar da su, to lalle ne su bayinka ne, kuma idan ka gafarta masu, to, lalle kai ne Mabuwayi Mai hikima (5:118)*. Kai kuwa Umar ka yi kama da Annabi Nuhu a cikin shawararka, inda ya ce: *Ya Ubangiji! Kada ka bari a kan qasa, daga cikin kafirai, ko wanda ke zama a cikin gida (71:26)*. Ka kuma yi kama da Annabi Musa inda ya ce: *Ya Ubangiji ka shafe a kan dukiyoyinsu kuma ka yi xauriya a kan zukatansu ta yadda ba za su yi imani ba har sai sun ga azaba mai raxaxi (10:88)*.

Kwatantawar da Manzon Allah ya yi wa waxannan Sahabbai da waxannan Annabawa ta fi wadda ya yi wa Ali da Haruna. Don darajar Haruna ba ta kai ga ta Nuhu da Ibrahimu da Musa da Isah ba. Don waxannan su ne *Ulul Azmi, m*afi daraja daga duk manzanni. Amma ba a tava jin wani ya ce darajar Sahabban daidai take da ta Annabawan ba. Iyakar abin da kwatancen ke nufi shi ne, Sahabban sun yi kama da Annabawan a cikin tsanantawa ko sauqaqawa a cikin al'amarin Allah.

Zahiri da baxinin wannan hadisi na nuna cewa, Manzon Allah na nufin matsayin Ali *Raliyallahu Anhu* a wurinsa, a daidai wannan lokaci, kamar matsayin Haruna ne a wurin Annabi Musa, a lokacin da ya waqilce shi bayan da ya tafi ganawa da Maxaukakin Sarki. Haka kuma wannan waqilci ba wata martaba ce da Ali *Raliyallahu Anhu* ya kevanta da ita ba. Don ya yi waxansu waqilce-waqilcen waxanda suka fi wannan xaukaka. Ka ga zancen a xauki wannan waqilci wasu kayan gabas bai taso ba.

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai kevance Ali *Raliyallahu Anhu* da wannan matsayi ba. Ya dai gaya masa wannan magana don sanyaya ransa, ganin irin yadda ya fito yana kuka a kan barin sa tsaron mata da qananan yara. Kuma shi ya sa bai yi irin wannan magana ga sauran waxanda ya waqiltar kafin Ali ba. Don su ba su fahimci cewa akwai wata naqasa cikin shugabanci da waqilcin da aka sa su ba. Don haka, hadisin bai nuna cewa, ba mai irin wannan matsayi na Haruna a wurin Musa sai Ali.

Wasu kuma daga cikin 'yan Shi'ah cewa suke yi, wai Manzon Allah ya tabbatar wa Ali da dukan matsayin da Haruna ke da shi, ban da na Annabta. Wannan magana ba gaskiya ba ce. Ce wa Ali da Manzon Allah ya yi: "Ba ka son ka zama a wurina kamar yadda Haruna yake a wurin Musa?" Na nuni kai tsaye a kan cewa ya faxi wannan magana ne kawai don ya rarrashi Ali, ya kuma nuna masa fahimtar da ya yi wa al'amarin ba haka take ba. Haka kuma akwai qarfafa guiwa da washe tunani zuwa ga Ali, don Manzon Allah ba ya da niyyar cire shi daga waqilcin.

Kuma ba ka ganin cewa Manzon Allah ya yi: "Kamar yadda Haruna yake a wurin Musa"? Yana nufin kama ne kawai. Don haqiqanin matsayin Haruna a wurin Musa ba ya samuwa ga wani. Kamar dai yadda ya kamanta Sahabban can biyu da Annabawan can huxu a hadisin Buhari da Muslimu.

Wani abin da ke qara tabbatar da haka, shi ne tura Ali *Raliyallahu Anhu* da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi don ya bi Sayyidina Abubakar wurin aikin hajji inda yake waqiltar Manzon Allah, bayan dawowarsu daga yaqin Tabuka. Da ya riski Abubakar a hanya, ya sanar da shi saqon da yake tafe da shi, sai Abubakar xin ya tambayi Ali *Raliyallahu Anhu* cewa: To, a matsayin shugaba ka zo, ko mabiyi? Ali ya karva masa da  cewa, A'a, ni mabiyi ne. Haka kuwa aka yi. Ali ya ci gaba da zama qarqashin shugabancin Abubakar, yana bin sa sallah, yana kuma biyar umurninsa, har ma Abubakar xin ya sa shi maimata wa mutane abin da yake faxa: "Ku saurara ya jama'a! Daga bana sai bana. Kada mushriki ya sake zuwa hajji. Kada kuma wanda ya sake yin xawafi tsirara".

Kuma xan Shi'ar ya ce wai, waqiltar da Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi wa Manzon Allah yana raye saboda tafiyar da ya yi wurin yaqi ta 'yan kwanuka na tabbatar da kasancewar sa mafi cancanta da gadon halifanci bayan rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Amsa a nan ita ce, ai kafin waqiltar da Ali *Raliyallahu Anhu* a wannan lokaci, an waqiltar da wasu Sahabbai, waqilci irin wanda kuma ya fi wanda Ali ya yi martaba, don jama'ar da suka kula da su ta fi wadda Ali ya kula da ita qima. Kuma bayan an dawo daga yaqin Tabuka ai wani Manzon Allah ya waqilta kafin ya je hajjin bankwana ba Ali ba, don ya tsare garin Madina. Waqilcin kuwa da aka sa Ali ya yi na tsare garin Madina bai fi wanda sauran Sahabbai suka yi kafinsa da bayansa ba, balle hakan ta zama dalilin zamansa halifa bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Idan kuwa ci gaba da waqilci har lokacin da Manzon Allah ya canza mutum ne sharaxi, to, xorewar shugabancin wanda aka shugabantar qarshe ya fi cancanta. Wato wanda ya waqilci Manzon Allah a hajjin bankwana, ba wanda ya waqilce shi kafin sa ba.

A taqaice dai, kamar yadda muka faxa ba Ali *Raliyallahu Anhu* ne kawai Manzon Allah ya waqilta wa riqon garin Madina ba, kuma hakan ba ta nuna Ali ya fi sauran waxanda aka waqiltar xin, ko kuma hakan ta zama hujja a kan shugabancinsa bayan wucewar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Wannan xaukaka ta waqiltar Manzon Allah ta shafi duk gaba xayan waxanda suka tava yin ta. Amma saboda jahilcin 'yan Shi'ah sai su yi hankaka; su taqaita darajojin a kan Ali *Raliyallahu Anhu* shi kaxai. Tattare da cewa akwai da yawa daga cikin Sahabbai waxanda suka fi shi kamala. Haka dai dama suka saba; karkata akalar nassosa da tabbatattun abubuwa na tarihi.

### 5.4 Wakilcin Ali a Madina

Hujja ta huxu inji xan Shi'ar, ita ce kasancewar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya waqilta Ali *Raliyallahu Anhu* ga tsare garin Madina tattare da kasancewar tafiyar da zai yi wurin yaqin taqaitacciya ce, ta 'yan kwanuka kaxan. Don haka, wannan qwaqqwaran dalili ne ga Ali *Raliyallahu Anhu* ya kasance shi ne zai gaje halifar Manzon Allah bayan rasuwarsa, ba wani ba. Kuma wai Manzon Allah bai karvi ragamar shugabancin daga Ali *Raliyallahu Anhu* bayan ya dawo daga wurin yaqin ba, har Allah ya yi masa wafati. Wannan ma wani dalili ne da ke qara tabbatar da cancanntar Ali *Raliyallahu Anhu* fiye da kowa ga zama halifan Manzon Allah bayan rayuwarsa a garin na Madina da sauran garuruwan musulunci inji shi. Kuma wai wannan hukunci ne shafe zane.

**Martani:**

Amsarmu a nan ita ce: Ko shakka babu wannan hujja da makamantanta waina ce irin ta wake a hannun alanqosa. Ga amsoshi da martaninmu daki-daki.

**Martani na Farko:**

A shafi na farko na wannan martani, muna tabbatar wa 'yan Shi'ah cewa, tarihi ingantacce ya tabbatar da cewa Sahabi Abubakar ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi nuni ga ya gaje halifarsa bayan rayuwarsa, ba Ali ba. Kamar yadda muka tabbatar a baya. Idan kuwa har 'yan Shi'ah suka kafa kai ga qasa suka ce a'a. Sai mu tuna masu da cewa ai 'yan'uwansu Rawandiyawa, waxanda bori xaya suke wa tsafi da su, sun tafi a kan cewa Abbas ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya waqilta don ya gaji halifarsa. Amma kuma tabbatacciyar Magana a bakin gaba xayan masana ingancin riwayoyi, ita ce da Alin da Abbas, babu wanda Manzon Allah ya yi nuni ga ya gaji halifarsa. Abubakar *Raliyallahu Anhu* xin dai da ba su qauna shi ne Manzon ya zava.

Idan kuma har wata riwaya ta inganta wadda ke nuna cewa, Manzon Allah bai yi nuni ga wanda zai gaje shi ba, to, ba wan ba wan kenan a wannan vangare. Abin da zai biyo baya shi ne inganci da tabbatar halifancin Sahabi Abubakar wanda al'umma ta zava bayan Annabi, zave kuwa na cancanta.

**Martani na biyu:**

Abin da xan Shi'ar nan ya yi na qoqarin tabbatar da cancantar Ali *Raliyallahu Anhu* ga maye gurbin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bayan rasuwarsa, bisa dalilin waqilta shi da ya yi a gurbinsa a lokacin da yake raye, qiyasi ne. 'Yan Shi'ah kuwa ai ba su yarda da qiyasi ba. Amma mu da muka yarda da qiyasi, muna iya qiyastawa, mu daidaita waqilta Umar da ya yi a lokacin da yake raye, ba tare da ya yi wani nuni a kan xorewar waqilcin nasa har bayan ransa ba. Don iyakar ikon da Manzon yake da shi a kan al'ummarsa lokacin da yake raye ne, ta hanyar shatawa da tsara siyasar ta kai tsaye ko ta hanyar waqilinsa. Amma da zarar rai ya yi halinsa, to, wannan nauyi da aka xora masa, da ma kowane iri ya kau. Kamar yadda Allah Ta'ala Ya ce ta bakin Annabi Isah *Alaihis Salamu*: *Kuma na kasance mai shaida a kansu a lokacin da nake cikinsu (5:117).* Bai ce waqilina zai ci gaba da zama mai shaida a kansu ba. Ka ga wannan dalili ne a kan cewa Annabi Isa bai naxa wa al'ummarsa halifa kafin ya rasu ba. Haka kuma wannan hujja ce a kan cewa ba wajibi ba ne ga Annabawa su naxa wanda zai gaje su tun suna raye.

Qarewa da qarau ma, ta tabbata an riwaito cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tava cewa: "Iyakar abin da zan cewa shi ne, irin abin da Annabi Isah ya ce: "Kuma na kasance mai shaida a kansu a lokacin da nake raye a cikinsu (5:117)".

**Martani na Uku:**

Mun yarda cewa, shugaba ya sanya waqili don kula masa da waxansu talakawansa a lokacin da yake raye wajibi ne. Sawa'un shugabancin nasa na manzanci ne ko na sarauta, kasancewar hannu xaya ba ya tanka dame. Dole ne ko shakka babu, ya waqiltar da wani ga jama'a a lokacin da baya nan. Don shi waqilin ya jagorance su a sallah, ya hore su da alheri, ya kuma hane su mugun aiki, ya karva wa mai haqqi haqqinsa idan wani azzalumi ya zalunce shi, ya hukunta wanda ya cancanci hukunci daga cikinsu bisa gaskiya da adalci. Duk a madadin wanda ya waqilta shi. Kamar dai yadda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* kan yi ga dukkan abin da baya iya zartarwa da kansa, a lokacin da yake raye. Kamar yadda ya naxa kwamandodi, don su riqa bai wa mujahidai sallah, su jagorance su a wurin jihadi, tare da gudanar da sha'anin aikinsu. Haka kuma ya naxa gwamnoni a duka garuruwan da musulunci ya ci. Amma bai ce ga wani da zai tabbata a kan wani muqami, ko ya gaji halifarsa bayan ya rasu ba.

Babu wani dalili da zai sa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi haka. Ya riga ya isar da saqon Allah, kuma shi ne kaxai wanda shari'a ta wajabta wa al'umma yi masa xa'a yana raye ko bayan rasuwarsa. Amma zancen wanda zai ci gaba da jagorantar su a bayansa, wannan haqqi ne da iko nasu, su zavi wanda suke so, suke kuma ganin dacewarsa. Kamar yadda suke da ikon yin haka a cikin kowace irin farilla wadda ba ta aini ba (kamar duk wajibban da wani ke iya xauke wa wani) wadda ke buqatar mutum xaya gaban

sahu daga cikin al'umma. Wannan ya isa dalili a kan rashin zaman waqilcin da aka bayar ana raye dalili a kan xorewarsa har bayan ran wanda ya tsayar da shi.

**Martani na Huxu:**

Naxa wakili a lokacin rayuwar shugaba wajibi ne kamar yadda Annabi ya yi.

Gaba xayan masu hankali sun yarda da wannan hujja tamu, don savanin haka ba abu ne mai yuwuwa ba ko alama. Idan kuwa har yana yiwuwa, to kuwa lalle ne mai mutuwar ya naxa gaba xayan waxanda za su jivinci al'amurran jama'a xaya bayan xaya; tun daga Sarakunan yanka har zuwa ga Dagatai da shaggun Hakimai wanda hakan kuwa na da matuqar wuya.

**Martani na Biyar:**

Rashin naxa magaji da Manzon Allah ya yi, shi ne abu mafi dacewa da cikar xaukaka gare shi a matsayinsa na Manzo. Allah shi ya nufe shi da haka. Kuma har koyaushe Allah kan xora shi a kan abin da yake shi ne mafifici. Kuma yanke hukuncin xorewar waqiltar tasa a lokacin da yake raye, har bayan ransa qololuwar jahilci ne.

Abin da Sayyidina Abubakar ya yi na naxa Umar a matsayin magadinsa tun yana raye, ba ya yi haka ba ne don yana da masaniyar al'umma ba za ta zave shi bayan rasuwarsa ba. Ko alama, ba haka abin yake ba. Ya yi haka ne don wata masaniya da ya kevanta da ita a matsayinsa na shugaba. Kamar yadda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi nuni da shi Abubakar ya gade shi bisa wata masaniya da ya kevanta da ita.

**Martani na Shida:**

Mu xauka cewa Manzon Allah dole ne a kansa ya naxa magadi. Sai mu ce, to, ai ko ya naxa Abubakar. don nunin da ya yi a kansa.

Kuma cewa, bayan daworsa daga yaqin Tabuka wai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai karvi waqilcin da ya ba Ali ba. Ingantaccen tarihi ba zai bari mu je ko ina xauke da wannan magana ba. Domin ko ai da dawowar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya soma tafiyar da al'amurran Madina, ya karvi ragamar mulkin garin kenan. Intaha.

Ba da vata lokaci ba kuma, sai ya tura Abubakar zuwa hajji a shekara ta tara. Ya kuma tura Ali a matsayin mabiyinsa. Bayan sun dawo ne kuma ya sake naxa Ali *Raliyallahu Anhu* a matsayin gwamnan Yaman. Bayan haka ne kuma ya tafi hajjin bankwana, inda ya sake waqilta wani a tsaron birnin Madina. To, zai yiwu a ce, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yana Madina, Ali na Yaman, amma kuma Alin ne halifansa a can Madinar?

Su dai 'yan Shi'a jahilcinsu ba ya qarewa. Ba su da wata masaniya game da tarihin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da ma na sayyidina Alin.

## 5.5 Hadisin Wasicci

Hujja ta biyar a cewar xan Shi'ar, ita ce abin da Ahlus-Sunnah wai suka riwaito daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa, ya ce wa Ali *Raliyallahu Anhu:* "Kai xan'uwana ne, kuma mai wasiccina, kuma halifana a bayana, kuma mai biyan bashin da ake bina".

## Martani:

Muna neman marubucin ya kawo mana ta inda wannan labari ya inganta. Don mu iya abin da muka sani babu wani littafi ingantacce na hadisi da ya riwaito shi, balle ya zama hujja. Kuma babu wani malami daga cikin malaman hadisi da ya inganta shi.

Kuma cewar da ya yi malaman Ahlus-Sunnah sun riwaito shi, idan yana nufin irin su Buhari da Muslimu, waxanda ake kafa hujja da littafansu, to yayi qarya. Ba su riwaito shi ba, balle su inganta shi. Idan kuma yana nufin irin su Abu nu'aimu sun riwaito shi a cikin *Kitabul Fadha'il* da irin su Mughazili da Khaxibu da Huwarizmi da makamantansu, ko kuma a cikin wasu littafai masu kawo falala. To, malamai masana sun haxu a kan cewa, fitowar wasu hadisai ko wata magana a cikin nau'in waxannan littafai, ba ya sa a kafa hujja da su ko da akan qananan abubuwa balle manya, irin sha'anin Imamah, wadda ku 'yan Shi'ah kuka tada duniya tsaye a kan ta.

Sannan malaman hadisi gaba xaya sun haxu a kan cewa, wannan hadisi qarya ce zalla. Kamar yadda a baya kaxan malam Ibnu Hazam ya tabbatar cewa, wannan hadisi da iri-irensa zuqi ta mallau ne aka yi wa fiyayyen halitta. Kuma duk wanda ke da masaniya da ilimin hadisi komai qanqantarsa ya san haka.

Yana da kyau a sani cewa, sayyidina Ali bai biya wani bashi da ke kan Manzon Allah ba, don babu shi. Abin da ya inganta a cikin Sahihul Buhari shi ne, koda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bar duniya akwai garkuwarsa a hannun wani Bayahude, a matsayin jingina. Ya jinginar da shi ne kuwa a kan awo talatin na alkama da ya karva daga hannunsa. Ka ga waccan garkuwa ita ke biyan wannan bashi. Ba a kuma san wani bashi da ake bin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bayan wannan ba.

Kuma Buhari da Muslim sun riwaito cewa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Kada magadana su raba wani abu da na bari. Idan an cire abin da matana za su ci da haqqin ma'aikatana, to, saura sadaka ne". Ka ga da akwai wani bashi a kansa, da sai a biya daga cikin abin da ya bari, ba Ali ya biya masa ba.

## 5.6 Hadisin Qulla Zumunci

Xan Shi'ar ya ce, hujja ta shida ita ce, hadisin qulla zumunci da Anas ya riwaito cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi a tsakanin Muhajirrai da Ansaru a ranar da aka yi Mubahala. Sayyidina Ali na tsaye kuma Annabin na ganin sa a lokacin. Amma bai haxa shi zumunci da kowa ba daga cikin

Ansaru. Sai Ali ya juya yana kuka. Da Annabi bai gan shi ba, sai ya tambayi Sahabbai, ina baban Hasan ya yi ne? suka karva masa da cewa, ya koma gida yana kuka. Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya umurci Bilal da ya je ya dawo da shi, yana son ganin sa. Bilal ya bi shi. Isar sayyidina Ali ke da wuya sai sayyida Fatima *Raliyallahu Anh* ta tambaye shi, me ya faru haka kake kuka? Ya karva mata da cewa, Manzon Allah ne ya qulla zumunci a tsakanin Muhajiruna da Ansaru ya bar ni bai haxa ni zumunci da kowa ba daga cikin Ansaru. Ta ce masa ita ko: "Allah ba zai bari kayi kunya ba. Wataqila Manzon Allah na nufin shi ne abokin zumuncinka". Suna cikin haka sai suka ji sallamar Bilal. Ya ce wa Ali *Raliyallahu Anhu* Manzon Allah na son ganin ka. Da suka iso gaban fiyayyen haliyya Annabi, ya tambayi Ali akan dalilin kukansa. Ya bayyana masa dalilin. Sai Manzon Allah ya ce masa: "Ai ina nufin ni ne abokin zumuncinka. Ko ba ka son ka zama abokin zumuncin Annabinka?" Ali ya ce: "Tabbas ina so, ya Manzon Allah". Daga nan wai sai Manzon Allah ya riko hannun Ali *Raliyallahu Anhu* ya hau mimbari ya ce: ya Ubangiji! Ka sheda da ni da Aliyu ga shi mun zama jini da tsoka. Ku sani ya ku jama'a! matsayinsa a wurina, kamar matsayin Annabi Haruna ne a wurin Annabi Musa. Kuma duk wanda yake da akwai so da qauna tsakanina da shi, to, ta kasance tsakanisa da Ali. Daga nan Ali *Raliyallahu Anhu* ya sa kai, wai sai Umar ya bi shi yana faxin daxa ai ta qare. Daga yau ka zama abin so da qauna a wurina da wurin kowane musulmi. Suka ce, wai wannan zumunci da Annabi ya qulla tsakaninsa da Ali *Raliyallahu Anhu* na nuna cewa Ali ya fi gaba xayan Sahabbai wurin daraja. Saboda haka ba wanda ya cancanci ya zama halifa bayan Annabi sai shi.

**Martani:**

Muna buqatar marubucin ya tabbatar mana da ingancin wannan hadisi. Don bai faxa mana littaffin da ya ciro hadisin daga cikinsa ba, kamar yadda ya saba. Duk da yake yakan xauko hadissan ne daga cikin littafan da hujja ba ta kafuwa da su a shari'a. Kamar dai yadda ya gada ga manyan malamansa 'yan Shi'ah, waxanda ke riwaito labarai da hadissan qarya waxanda ba su da asali. Ga shi kuwa Ibnul Mubarak ya ce: "Isnadi rukuni ne na addini. Don ba don albarkacin isnadi ba, da kowa ya tsoma bakinsa da abin da ya ga dama a cikin Addini. Idan kuma aka tambaye shi dalilin ya tsaya yana 'yan kame-kame".

Malamai masana hadisi dai sun tabbatar da cewa, wannan hadisi qiren qarya ne. Babu kuma malami xaya da ya ware daga wannan da'ira. Haka kuma malaman sun tabbatar da cewa, duk wanda ya qirqiro wannan hadisi ya danganta shi ga Manzon Allah, jahili ne tubran, ta yadda bai ma san yadda zai kitsa qaryar da ba za a iya gane qarya ce ba. Ko jaririn da ke rarrafe a duniyar ilimin hadisi ya tunkari wannan hadisi zai rosa shi. Za mu qara bayani nan gaba kaxan.

Babu kuma wani hadisi da ya inganta daga Annabi cewa, ya qulla zumunci da Ali *Raliyallahu Anhu.* Dukkan su qiren qarya ne. Annabi bai qulla

zumunci da kowa ba. Kamar yadda bai qulla shi tsakanin Muhajirai wasu–wasu, ko tsakanin Abubakar da Umar, ko tsakanin Ansaru wasu–wasu a wannan lokacin ba. Amma dai abin da ya tabbata shi ne, Manzon Allah ya qulla zumunci tsakanin Muhajiruna da Ansaru lokacin da ya iso Madina. Ita kuwa Mubahala an yi ta ne ranar da wakilan qabilar Najjaru suka zo wurin Manzon Allah a shekara ta tara ko ta goma bayan hijira.

Daga cikin hadisin kansa akwai dalilin da ke bayyana zamansa qarya, kamar inda ya ce, a ranar Mubahala Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya qulla zumunci a tsakanin Muhajiruna da Ansaru. Mubahala kuwa an faxi sadda aka yi ta. A dalilinta ne aka saukar da surar Ali Imran.

Saboda haka, zumuncin da Manzon Allah ya qulla tsakanin Muhajiruna da Ansaru wanda lafiyayyen tarihi ya san da shi kamar yadda muka bayyana, ya faru ne a shekara ta farko bayan hijira a gidan Banu Najjar. Tsakanin wannan kuwa da Mubahala akwai shekaru masu yawa.

Ta kuma tabbata cewa, Manzon Allah ya qulla zumunci tsakanin sayyidina Ali da Sahalu xan Hunaifu. Ya kuma qulla wani tsakanin Muhajiruna da Ansaru. Amma tsakaninsa da Ali *Raliyallahu Anhu* waxanda dama ‘yan'uwa ne kuma ga su Muhajirai, ai ba buqatar qulla wani zumunci.

Daga qarshe, cewar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wa Ali: “Baka son ka zama a wurina kamar yadda Haruna yake a wurin Annabi Musa? Malaman hadisi gaba xaya sun yi ittifaqi a kan cewa, ya yi wannan magana ne lokacin da zai je yaqin Tabuka, bai kuma sake maimaita ta a wani wuri ba.

### 5.7 Hadisin Yaqin Haibara

Xan Shi'ar ya ce hujja ta bakwai, ita ce abin da malaman Sunnah suka riwaito cewa, a lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tsare mutanen Haibara tsawon kwanaki ashirin da tara, ana dakon yaqi. A lokacin tutar musulmi na hannun Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* sai ya samu rauni a idonsa xaya, har ya yi kumburi, ta yadda ba ya gani sosai balle ya yi yaqi da kyau. Ana haka sai Marhab, shugaban Yahudawa ya shelanta fara yaqi. Ganin haka, sai Manzon Allah ya umurci Abubakar da ya karvi tutar, ya canji Ali, ga kuwa sauran Muhajiruna. Abubakar ya karvi tutar ya tafi wai ya kasa tavuka kome, ya dawo kunya-kunya. Safiya na yi sai Umar ya karvi tutar, shi ma wai bai je ko ina ba, ya dawo ya labarta wa makusantansa abin da ya haxu da shi na cirjiya har ya dawo da baya. Daga nan sai Manzon Allah ya ce: Kai! Ku kira min Ali, shi xai ke iya wannan daga. Sahabbai suka ce, hala ka manta ba ya da lafiyan ido xaya? Ya ce, kai haka ne fa, ku nuna mani inda yake. Ku nuna mani wanda Allah ke so yake kuma son Allah, wanda kuma baya gudu ranar daga. Qarshe xai suka kira Ali ya zo. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi tofi a kan hannunsa ya shafi ido da kan Ali, nan take ya warke. Shi kuma ya danqa masa tuta. Ali ya yi yaqi mai tsanani har Allah ya ba shi nasara.

'Yan Shi'ah suka ce, wai waxancan siffofi da Manzon Allah ya siffanta Ali da su alama ce ta babu wanda ya kama qafarsa cikin sauran Sahabbai. Saboda haka, shi ya fi cancanta da zama shugaban musulmi bayan wucewar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama.*

**Martani:**

Muna son marubuci ya yi wa duniya bayanin yadda wannan hadisi ya inganta, a cikin wannan siga. Domin cewar marubucin ya yi malaman Sunnah sun riwaito wannan hadisi gaskiya ne. Sai dai ba haka amintattu daga cikinsu suka riwaito shi ba. Ingantattar magana ita ce, sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* bai ma halarci yaqin Haibara ba. A sanadiyar wancan kumburi da ya sami xayan idonsa. Daga baya ne kuma ya kasa daure wa zaman gida Annabi na fagen fama. Saboda haka sai ya haura takalmansa ya isa wurin. Kafin ya kai wurin ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce wa Sahabbai dake tare da shi: "Tutar yaqinmu a gobe zan danqa ta ne a hannun wani mutun wanda Allah da Manzo ke so, yake kuma son su, wanda kuma Allah zai ba shi nasara".

A lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ke wannan magana tutar ba ta shiga hannun Abubakar ko Umar ba. Kai ko alamar karkata ga xayansu babu. Cewa an ba su ita sun kasa tavuka komai kafin haka, qarya ce tsagwaronta. Hasali ma jin waccan magana ta Manzon Allah ce ta sa sayyidina Umar ya ce: Ban tava jin ina kwaxayin shiga gaban sahun jama'a a matsayin jagora ba, sai a wannan rana. Kuma ba ni kawai ba, duk mazajen da ke wurin, kowannensu ya yi fatar ya zama shi ne Manzon Allah zai danqa wa tutar. Amma ina! Safiya na wayewa sai kawai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kira Ali *Raliyallahu Anhu*. Kafin ya iso daga wurin da yake, sai aka gaya masa cewa, ai yana fama da ciwon ido. Da ya iso sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi masa addu'a a idon nan take kuwa ya warke, ya kuma danqa masa tutar. Allahu Akbar! Rabo ya rantse sai mai shi.

Ka ga a hankalce wannan falala da Ali *Raliyallahu Anhu* ya samu, sakamakon biyo Manzon Allah ne da ya yi tattare da yana fama da wannan rashin lafiya. Ita kuma waccan magana da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi tun Aliyun bai iso ba karamarsa ce *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Babu kuma wani lafazi a cikin hadisin da ke nuna naqasar darajar Sahabi Abubakar ko Umar. Ko alamar haka babu.

Wani abu kuma shi ne: Cewar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi Sayyidina Ali na son Allah da Manzonsa, su kuma suna son sa gaskiya ne. Amma hakan martani ne ga Nasibawa waxanda ke ganin akasin haka. Kuma ba za a saurara wa 'yan Shi'ah ba, idan suka kafa hujja da wannan magana a kan fifikon Ali *Raliyallahu Anhu* a kan sauran Sahabbai, balle har su qara da faxar abin da suka yi imani da shi cewa, gaba xayan Sahabban sun yi ridda bayan rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* in ban da Ali *Raliyallahu Anhu* da wasu kaxan daga cikinsu.

Idan ‘yan Shi’ah suka kafa hujja da waxannan maganganu, to, sai mu bar su da takwarorinsu Harijawa, waxanda ke ganin har shi Aliyun ya yi ridda, a lokacin da ya yarda da sasantawa tsakaninsa da Mu’awiyah a yaqin basasar Siffin, inda suka ce wa Ali: “Tabbas ka fita daga musulunci. Maza-maza ka dawo”.

Sannan kuma xan Shi’ar a cikin sharhin wancan hadisi da ya yi, ya ce wai, cewar da Annabi ya yi zan xamqa tutar yaqinmu ga mutum mai siffa kaza da kaza, kuma abin ya faxa hannun Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* hakan na nuna cewa, babu wani Sahabi da ke da waxancan siffofi sai fa shi Alin.

A nan muna da Martani biyu zuwa gare shi. 1) Eh, mu xauka cewa siffofin can da Annabi ya faxa da tabbacin nasara da ya ce zai samu, duk sun tabbata a kan Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu.* A hankalce da la’akari da qa’idar harshen Larabci, hakan ba ta nuna ba mai waxancan siffofi a cikin Sahabbai ba sai Ali, balle a kafa hujja da hakan a kan kasancewarsa mafi cancanta da shugabanci bayan Manzon Allah, kai tsaye. 2) Idan kuma muka cije a kan cewa, ba mu yarda da cewa waccan magana ta Annabi na nufin kevance wani daga cikin Sahabbai da waxancan siffofi, koda kuwa shi Allah ya zava da karvar tutar, ba mu yi kuskure ba. Dalilinmu kuwa shi ne maganar ta Annabi, kamar kai kace ne: Zan bayar da wannan kuxi kyauta ga wani mutum mabuqaci, ko ka ce: Yau zan ziyarci wani mutum maras lafiya, ko managarci. Koko zan danqa wannan tuta a yau hannun wani mutum jarumi. Ko wani abu mai kama da haka. Gaba xayan waxannan jumloli ba su nufin kevance wani mutum da waxancan siffofi. Duk wani mabuqaci ko maras lafiya ko managarci ya shiga cikin lissafinka, illa dai sai wanda Allah ya datar kawai.

To, mu qaddara cewa zaven sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* da Allah ya yi da waccan falala ta shigar waccan tutar a hannunsa tattare da isowarsa qarshe a Haibara, hakan ya daxa xaukaka dajararsa. Ko da mun yarda da haka, to, ba ta nufin a cikin sauran Sahabbai babu wanda ya fi shi girman daraja a wannan rana. Ko alama ba haka abin yake ba.

Harwayau dai mu qara qaddara cewa, xaukakar sayyidina Ali da martabarsa sun daxa fitowa a idon musulmi a waccan rana, hakan ba ta nufin kasancewarsa “Ma’asumi” kuma wanda ko sama da qasa za su haxu sai ya gaji halifar Manzon Allah bayan wucewarsa. Kai ba Ahlus-Sunnah ba, da yawa daga cikin ‘yan Shi’ah Zaidiyyawa da wasu daga cikin Mu’utazilawa na baya-baya da wasunsu duk sun tafi a kan haka. Sun yi imani da kasancewar Ali *Raliyallahu Anhu* mafificin daraja a cikin Sahabbai. Amma kuma ba su ga wata illa a cikin kasancewar Sahabi Abubakar halifa ba. Don su a wurinsu ya halatta mai matsa kaiciyar daraja ya jagoranci sahun musulmi, tattare da kasancewar a cikin waxanda ke bayansa akwai wanda mudun darajarsa ya cika ya batse.

**5.8 Hadisin Tsuntsu:**

Xan Shi’ar ya ce: Hujja ta takwas ita ce labarin bandataccen tsuntsu. Wai gaba xayan malaman Sunnah sun riwaito cewa: Watarana an kawo wa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* kyautar bandataccen tsuntsu, sai ya buxa baki ya ce: “Ya Ubangiji! Ka kawo wani mutum mafi soyuwa a wurinka da wurina daga cikin halittarka, wanda za mu ci wannan tsuntsu tare da shi. Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* na cikin gida yana jiran wanda Allah zai kawo. Sahabi Anas kuma wai, na zaune qofar gidan daga ciki yana cika fada. Ana haka sai Anas ya ji an qwanqwasa qofa. Da ya buxe qofar sai ya ga ashe Ali ne ya kawo jiki, sai ya ce masa: Annabi ba ya ganuwa yanzu, don yana ‘yar buqata, sai Ali ya juya. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya sake maimaita waccan addu’a, kuma sai ga Ali ya sake qwanqwasa qofa. Anas ya ce masa: Ashe ban gaya maka Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai ganuwa, yana wata buqata ba? Sayyidina Ali ya sake juyawa. Can kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya sake maimaita wannan addu’a. Sai ga sayyidina Ali ya dawo fusace, ya sake qwanqwasa qofar da qarfin gaske, har Annabi ya ji qwanqwasar ya kuma ce wa Anas ya bari Ali ya shigo.

Shigowar sa ke da wuya sai Annabi ya tambaye shi: Me ya tsayar da kai haka?” Shi kuma ya karva masa da cewa, na zo har sau uku Anas na cewa, ba ka ganuwa. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya juya kan Anas ya ce masa: “Anas me ya sa ka yi haka?” Ya karva masa da cewa: “Ina sane nayi haka ya Manzon Allah. Na so ne Allah ya kawo wani mutum daga Ansaru”. Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce masa: “Kana ganin akwai wani mutum daga cikin Ansaru wanda ya fi Ali xaukaka da daraja?” Xan Shi’ar ya kammala da cewa, tun da kuwa har Ali shi ne mafi soyuwa ga Allah daga cikin halitta a wurin Allah, to, lalle kuwa shi ya fi cancanta da zama halifa a bayan Annabi.

Shi kenan. Qanqurus qan qusu!

**Martani:**

Tun da farko, cewar da ya yi dukkan malaman Sunnah sun riwaito wannan hadisi qarya ce muraran. Kuma muna bin sa bashin ingancin wanna tatsuniya. Domin babu wanda ya riwaito shi daga cikin masana hadisi amintattu, ballantana ya inganta shi. Amma kamar yadda gama garin malamai masu kwasar karan mahaukaciya suka riwaito ire-irensa, sun riwaito shi, shi ma. Haka kuma sun riwaito masu kama da shi a game da falalar Mu’awiyah. Har ma an wallafa littafai masu yawa a irin wannan. Amma a wurin malamai masanan fannin hadisi, da waxannan hadisan da babu duka xaya.

Kuma ma a wurin malaman hadisi, hadisin bandataccen tsuntsu tatsuniya ne. Wasu malamai ma sun tattara hanyoyin da aka ce an samo

wannan hadisi ta su. Cikinsu har da Imamu Hakim An-Naisaburi da Abu Nu'aimi da Ibnu Mardawaihi da sauran su. Da aka tambayi Hakim a kan matsayin hadisin, cewa ya yi: "Bai inganta ba". Ga shi kuwa 'yan Shi'ah na ganin Hakim a cikin malamansu.

A bayyane ta ke cewa, cin naman tsuntsu ba wani abu ne mai girma na a zo a gani ba, har da za a yi fatar haxa hannu da mafi soyuwar halitta a wurin Allah cikin yin sa. Ai da shege da xan halas ba wanda ba a shar'anta wa cin abinci ba. Babu wani kusanci ga Allah da sayyidini Ali zai qara, ko wani ci gaba da addinin Allah zai samu, ko wani inganci da rayuwar musulmi zata qara don Ali ya ci naman tsuntsu tare da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Wannan fa in an qaddara ingancin hadisin kenan.

Wannan hadisi dai bai inganta ko a addinin Shi'ah don ya yi ban hannun makafi da aqidarsu. Don su, suna ganin cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya san cewa, Ali shi ne mafifici daga cikin halittun Allah, kuma don haka ne wai, ya zave shi a matsayin halifansa. Shi kuwa wannan hadisi na nuna cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai san wanda Allah ya fi so ba.

To, a nan ko dai mu xauka cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya san wannan bayani, ko a'a. idan muka qaddara cewa, ya sani, to, me ya janyo buqatar wannan addu'a? ai da sai ya ce: "Ya Ubangiji! Ka kawo min Ali, don shi ne mafi soyuwa gare ka daga cikin halittunka". Kamar yadda yake aikawa a kira masa wasu daga cikin Sahabbai. Kuma da ya ambaci Ali *Raliyallahu Anhu* a cikin addu'arsa, da Anas bai hana Alin ganin sa ba, da kuma bai yi waccan fata maras amfani ba ta gurin Allah ya kawo wani daga cikin Ansaru.

Idan kuwa muka qaddara cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai san Ali shi ne mafi soyuwar halittar Allah ba, wancan iqirarin nasu ya faxi. Kuma ya za a ce, mutum kamar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai san wanda ya fi so ba, tun da xan Shi'ar cewa ya yi a addu'ar: "Ya Ubangiji! Ka kawo wani mutum mafi soyuwa a wurinka da wurina daga cikin halittarka..".

Da za ka haxa hancin ma'anar sauran hadisai da suka inganta, za ka taras sun ci karo da wannan hadisi. To, ya za a kawar da su da wannan tatsuniya?

### 5.9 Hadisin Gaisuwar Sarauta ga Ali

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta tara ita ce, abin da malaman Sunnah suka riwaito cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya umurci Sahabbai su rinqa yi ma Ali gaisuwar sarauta, suna ce masa "Allah ya taimaki Sarkin Musulmi"! Kuma wai, ya qara da ce masu: "Ali shi ne shugaban musulmi,

kuma limamin masu taqawa, kuma shi ne jagoran masu farin goshi a gobe qiyama". Ya kuma ce, inji xan Shi'ar: "Ali shugaba ne ga kowane mumini bayana". Kuma ya qara da cewa: "Ku sani, ni da Ali kamar jini da tsoka mu ke. Kuma muna da iko ga gaba xayan muminai maza da mata fiye da ikonsu akan kawunansu".

Bisa ga wannan dalili, inji xan Shi'ar, Ali ne kaxai ya kamata ya zan shugaban musulmi a bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kuma waxannan hadisan yanke suna tabbatar da haka.

**Martani:**

Kamar koyaushe, muna neman ya ba mu tabbacin ingancin hadisan nasa. Ya faxi kuma littafan da ya cirato su. Ba kawai ya ce, malaman Sunnah sun riwaito ba. Riwaya kaxai ba ta tabbatar da hadisi in ba an bi diddigi an gano amincin mafitarsa ba. Allah kuma ya haramta qarya, musamman kuma in ta zamo a cikin addini. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi qyaci a kan wanda ya qirqira masa qarya.

To, su dai waxannan hadisan kamar na bayansu, zuqi-ta-mallau ne. waxanda ba ya halalta a ji su ga bakin wanda ya san girman Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. domin waxannan sifofi da hadisan suka ba Ali sifofin Annabi ne *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kuma ko a bayan wafatinsa ba ya dacewa a sifanta wani da waxannan siffofi in ba shi ba. Shi ne ya cancanci wannan siffa a nan duniya da gobe kiyama.

Kuma ma sai mu ce ma xan Shi'ar: Kaffatanin musulmin da suke tare da Ali a lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ke furta wannan magana – in har ya faxe ta - waxanda su ne masu farin goshin, kafirai ne a gurin ku. To, su wane ne Ali zai jagoranta?!

Tabbatattar qarya duk ba ta wuce cewa, Ali shi ne wanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya hukunta ya jagoranci al'ummar Sahabbai ba. Don na kusa da na nesa sun san yadda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ke fifita Abubakar da Umar a kan sauran Sahabbai, cikinsu har da Ali. Ko kafirai ma a lokacin, sun san da haka.

Kuma cewar da xan Shi'ar ya yi, wai, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Ali shi ne ubangidan kowane mumini bayana" qarya ce ita ma. Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne ubangida kuma masoyin kowane mumini a lokacin rayuwarsa da bayan rasuwarsa. Don so da qauna na gaskiya ba su yankewa don rayuwa ta qare.

Amma cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Ali kamar jini da tsoka ne, haka yake. Ingantacciyar magana ce, amma a cikin wani hadisi ba wannan da xan Shi'ar ya kawo ba. Ali kuwa bai kevanta da samun wannan matsayi daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba. Domin kuwa haka ya faxa a game da Julaibibu lokacin da ya yi shahada. Kai, wata qabila ma sukutum da ake kira *Ash'ariyyuna* ya ba su wannan matsayin, ya ce: "Ni da *Ash'ariyyuna* kamar jini ne da tsoka". Ya faxa masu haka saboda kyawon

halinsu da ‘yan’uwantakar da suke yi a tsakanin junansu. To, ya za a ce Ali ya kevanta da wannan, ballantana a ce, shi ne dalilin zamansa shugaba.

**5.10 Hadisin Amanoni biyu:**

Hujjar xan Shi’ar ta tara daga cikin hadisai, inji shi, ita ce: Abin da malaman sunnah suka riwaito, daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa: “Ko shakka babu zan bar maku wasu amanoni biyu da za su hana ku vacewa matuqar kun yi riqo da su: Littafin Allah da zuri’ata; iyalan gidana. Kuma ba za su rabu da juna ba har sai sun same ni a bakin tafkin Alkausara”. Da kuma wani hadisi, inji shi, da ya ce: “Iyalaina kamar jirgin Annabi Nuhu ne a cikinku. Duk wanda ya shige shi ya tsira. Wanda kuwa ya bari aka bar shi baya, to, ruwa zai ci shi.”.

Xan Shi’ar ya ce: Waxannan hadisai na nuna wajabcin saurara ma Ahlul-Baiti ga duk abin da suka faxi. To, da yake Ali ne shugabansu, ya zama tilas a kan kowane musulmi ya yi masa biyayya, ya kuma yarda da kasancewarsa halifa kai tsaye bayan rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

**Martani:**

A bisa al’adarmu, za mu soma neman ingancin wannan hadisi. Kuma mun san bai inganta xin ba a yadda ya kawo shi.

Lafazin da ya inganta, kamar yadda Muslimu ya riwaito a cikin ingantaccen littafinsa daga Zaidu xan Arqamu ya ce: Watarana muna bakin wani tafki mai suna *Khum*, a tsakanin Makka da Madina, sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tashi ya yi mana huxuba, ya ce: “Bayan haka, ya ku mutane, ku sani, ni mutum ne kamar kowa. Yau manzon mutuwata na iya zuwa, ba ni da ikon qin tafiya. Ko da na tafi dai, zan bar maku wasu abubuwa biyu masu alfarma. Na farko, shi ne littafin Allah, wanda ke tattare da haske da shiriya. Ku yi riqo da littafin nan na Allah. Ku bi shi sau da qafa.” Sai ya yi ta kwaxaitar da mu, da nuna mana muhimmancin aiki da littafin Allah. In ji Zaidu. Sannan ya ci gaba da cewa: “Da iyalaina. Ina tunayar da ku Allah game da su”.

Ka ga wannan ingantattar riwaya na nuna mana cewa, littafin nan na Allah ne kawai Annabi ke umurtar mu da bi sau da qafa, kuma duk wanda ya yi haka ya tsira. Kuma ita wannan ma’ana ta yin biyayya ga littafin Allah shi kaxai, ita ce wani hadisin ya zo da ita, kamar yadda yake a cikin Sahihu Muslim daga Jabir *Raliyallahu Anhu*, ya ce Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce, a ranar Arafa, lokacin da yake huxubar hajjin bankwana: “Haqiqa na bar maku abin da ba za ku vace ba bayana, matuqar kun yi riqo da shi. Wannan abu shi ne littafin Allah. Za a kuma tambaye ku a kaina, me za ku ce? Sai Sahabbai suka ce: “Za mu ce, mun sheda ka isar da manzanci, ka kuma yi gargaxi ga kowa”. Daga nan sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya

xaga hannuwansa sama, ya rinqa dawowa da shi yana nunin Sahabbai, yana cewa: “Ya Allah! Ka zama sheda a kan haka”. Ya maimaita haka har sau uku.

Amma cewar da xan Shi’ar ya yi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Da zuri’ata; iyalan gidana. Kuma ba za su rabu da Alqur’ani ba har sai sun same ni a bakin tafkin Alkausara”. Wannan riwayar Tirmidhi ce. An kuma tambayi Ahmad xan Hambali akan matsayinta, ya ce, riwaya ce mai rauni. Wasu malamai da dama kuma daga cikin masana sun raunana shi. Amma dai da dama daga cikin malamai na cewa, iyalan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba za su haxu a kan vata ba.

To, mu a nan muka tsaya. Kuma cikin hikimar Allah, babu wani abu guda xaya da Ahlul-Baiti suka yi tarayya da ‘yan Shi’ah a cikinsa. Allah ya tsarkake su daga wannan qazamta.

Amma cewar da xan Shi’ar ya yi, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Iyalaina kamar jirgin Annabi Nuhu ne a cikinku..”. Wannan magan ba ta da wani isnadi nagartacce. Kuma littafan da ake kafa hujja da su ba su kawo ta ba. Illa dai masu bayar da tatsuniyoyi ne suka kawo ta kamar yadda suka saba. Wannan kuwa ba zai daxa wa riwayar kome ba illa rauni bisa rauni.

To, kuma a nan hadisin ya nuna cewa, iyalan Manzo ba su rabuwa da Alqur’ani. Wannan dalili ne a kan cewa, ijma’in iyalan Manzo hujja ne. Wannan ko shi ne ra’ayin wasu almajiran makarantar Ahmad xan Hambali. Kuma shi ne Alqali ya kawo cikin littafinsa *AlMu’utamad.* To, amma iyalan Manzo su ne, dukkan banu Hashim. Waxanda suka haxa da, ‘ya’yan Abbas da ‘ya’yan Ali da na Harisu xan Abdulmuxxalibi da sauran ‘yan gidan Abu Xalib. Ali shi kaxai ba zai amsa sunan iyalan gidan Manzo ba. Kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne ubangidan Ahlul-Baiti, ba Ali ba.

Wani abu kuma da ya kamata a sani shi ne cewa, Ahlul-Baiti basu bi ra’ayin ‘yan Shi’ah na fifita Ali a kan sauran Sahabbai baki xaya ba. Ibnu Abbas ga misali, duk da yake yana tare da Ali ko a yaqoqan zamanin fitina, a fili yana faxin fifikon Abubakar da Umar a kan kowa, tun ma ba a fagen shugabanci ba.

Maganar ijma’in Ahlul-Baiti ita kanta, ta ci karo da abin da ya fi ta qarfi, shi ne, kasancewar ijma’in baki xayan musulmi hujja ce da ta tabbata da Alqur’ani da tabbatattun hadisai. Su kuma Ahlul-Baiti wani vangare ne daga cikin al’umma. Don haka, duk lokacin da al’umma ta yi ijma’i sun shiga cikin sa.

### 5.11 Wasu Hadisan Qarya

Xan Shi’ar ya ci gaba da cewa: Hujja ta sha xaya, ita ce, hadisan da malaman Sunnah suka riwaito na wajabcin son Ali da riqonsa ubangida. Ya ce: “Ahmadu xan Hambali ya riwaito a cikin Musnadinsa cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya riqa hannun Hasan da Husaini, sannan ya ce: “Duk mai sona da ni da waxannan da mahaifansu, to, yana tare da ni, a

matsayina ranar qiyama". Kuma Ibnu Khalawaihi ya riwaito, inji shi, daga Huzaifa *Raliyallahu Anhu* ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Duk wanda ke son a ba shi sandar yaqutu, wadda Allah ya halitta da hannunsa, sannan ya ce mata: kun-fa-yakunu, to, ya riqi Ali xan Abu Xalib a matsayin maigida a bayana".

Ya ce, kuma an karvo daga Abu Sa'id Al-Khudri ya ce, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce ma Ali: "Sonka imani ne, kuma qinka nifaqa ne. farkon wanda zai shiga aljanna su ne masoyinka. Farkon wanda zai shiga wuta su ne maqiyanka. Matsayinka a wurin Allah ya kai haka. Kuma kai nawa ne, ni naka ne. amma babu Annabi bayana".

Kuma an riwaito daga Shaqiqu xan Salamata daga Abdullahi ya ce: "Na ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yana riqe da hannun Ali yana cewa: "Wannan majivincina ne, ni ma majivincinsa ne. Na qi wanda ya qi, na shirya da wanda ya shirya". Kuma Akhxabu Khuwarizmi daga Jabir *Raliyallahu Anhu* ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Jibrilu ya zo min daga wurin Allah da wata koriyar takarda, an yi mata rubuta da farar tawwada cewa: *Ka gaya wa halittata, haqiqa ni, na wajabta masu son Ali".*

Xan Shi'ar ya cike maganarsa da cewa, hadisai irin waxannan ba su da iyaka waxanda aka samo daga hannun 'yan adawa. Kuma duk suna nuna fifikon Ali da cancantarsa da shugabanci.

**Martani:**

Ina ma dai a ce, marubucin nan namu zai iya kare kansa game da waxannan qarairayi da ya fesa ma fiyayyen talikkai?

Malamin yana cika bakinsa da faxin Ahmad xan Hambali ya riwaito, kuma ga dukkan alamu bai san banbancin hadisan da ke cikin littafan Ahmad ba. Ko ma ya san Ahmad yana da *Kitabul Fadha'il* wanda hadissansa galibi sun fi rauni a kan na Musnad? Kuma ko ya san baicin hadissan da Ahmad ya riwaito a cikin Musnad akwai qare-qaren da xansa Abdullahi da ya riwaito littafin ya yi? Ya kuma san Qaxi'i da ya riwaito littafin daga Abdullahi xan Ahmad shi ma ya shigar da nasa riwayoyi na daban, ba na Ahmad ba? Kuma rauni hadissan na qarshen nan yana da tsanani, kuma ba ya halalta a jingina ma Ahmad su tunda ba shi ya riwaito su ba? Iya abin da za a yi shi ne a jingina kowane hadisi a wajen riwaya ga mai shi? Anya kuwa Malam Zurqe xan Shi'ah ya san da waxannan bayanan? Sanin gaibu sai Allah. Amma dai biri ya yi kama da mutum!

Hadisin farko da xan Shi'ar ya kawo cikin hadissan Quxai'i ne na qarya. Ibnul Jauzi ya yanke masa wannan hukunci a cikin littafinsa *Al-Maudu'at*. Su ma dai sauran hadissan Ibnu Khalawaihi da na Akhxabu Khuwarizmi yi masu bugu guda.

Yi nazarin hadisin da ya ce, wai: Maqiyan Ali ne farkon wanda zai shiga wuta. Kana tsammanin Harijawa su riga Abu Jahli shiga wuta, da su

Fir'auna da Abu Lahabi da sauran tsararrakinsu na mushrikai?. Sannan cewa, masoyan Ali ne farkon masu shiga aljanna. Za su riga Annabawa da Manzanni ne? Ko yana nufin su ma Annabawan da Manzanni za su shiga aljanna ne albarkacin son da suke ma Ali kafin son Allah da son sauran masoyansa na daga Annabawa da Manzanni?

### 5.12 Hadisin Kafirta Wanda ya Sava ma Ali

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Hujja ta sha biyu daga cikin hadissai ita ce: Hadisin da Akhxabu Khawarizim ya riwaito daga Abu Zarril Gifari daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa: "Wanda duk ya yi jayayyar halifanci da Ali kafiri ne. Don kamar ya kai wa Allah da Manzonsa yaqi ne. Duk kuma wanda ya yi shakkar matsayin Ali shi ma kafiri ne". Kuma an riwaito daga Anas *Raliyallahu Anhu* ya ce: Watarana ina zaune wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai na ga Ali tafe, sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Ni da wannan da ke tafe hujjar Allah ne akan al'ummata ranar alqiyama". Kuma an samo daga Mu'awiyah xan Haidah Alqushairi inji xan Shi'ar, cewa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce wa Ali: "Duk wanda ya mutu yana qiyayya da kai, ya mutu a matsayin Bayahude ko Kirista".

**Martani:**

Su dai riwayoyin Akhxabu Khawarizim ba abin da mai hankali zai ce in ya duba su, sai dai ya ce, tsarki ya tabbatar ma Allah! Su kuma waxannan hadisai da malam Zuqa ya kawo ba su ko yi kama da hadissan da ke qamshin gaskiya ba.

Irin waxannan ruvavvun tatsuniyoyi ba su isa su girgiza imanin da musulmi duka ke da shi game da Muhajiruna da Ansar waxanda suka yi wa sayyidina Abubakar mubaya'a ba. Ga su ko Allah gwanin sarki ya tsarkake mana su sau tari a cikin Alqur'ani. Duba yadda ya bayyana mana yardarsa da su inda yake cewa:

﴿ وَٱلسَّٰبِقُونَ ٱلْأَوَّلُونَ مِنَ ٱلْمُهَٰجِرِينَ وَٱلْأَنصَارِ وَٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُم بِإِحْسَٰنٍ رَّضِيَ ٱللَّهُ عَنْهُمْ وَرَضُوا۟ عَنْهُ وَأَعَدَّ لَهُمْ جَنَّٰتٍ تَجْرِى تَحْتَهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدًا ۚ ذَٰلِكَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ﴿١٠٠﴾ ﴾ التوبة: ١٠٠

> *Kuma magabatan farko daga Muhajirai da Ansarai da waxanda suka biyo bayansu da kyautatawa, duk Allah ya yarda da su, kuma sun yarda da shi. Kuma ya yi masu tanadin Aljanna waxanda qoramu ke gudana a qarqashinsu, suna madawwama a cikinsu har abada. Wancan shi ne babban rabo.*

Kuma da za mu qaddara cewa, waxannan hadissai na qarya sun inganta. To a kaikaice hakan na tabbatar da suka ne ga shi Ali *Raliyallahu Anhu* da

tabbatar da zamansa kafiri, wanda ya qaryata Allah da Manzonsa, wal iyazu billahi. Kamar yadda ingancin nasu ke kafirta sauran Sahabbai, saboda wai sun yi jayayyar halifanci da shi.

To, mun ji. Amma shi Ali *Raliyallahu Anhu* bai tava aiki da waxannan hadissan qarya ba, don a wurinsa Sahabbai gaba xaya musulmi ne masu imani. Mafi sharrin waxanda ya yaqa su ne Harijawa, amma kuma bai kafirta su ba. Ya kuwa yaqe su mafi muni yaqi. A maimakon haka ma sai ya haramta dukiyoyinsu da waxanda aka kama daga cikinsu. Kai kafin ma su gwabza yaqin sai da ya gaya masu cewa: “Ba za mu hana ku shiga masallatanmu ba, ba kuma za mu hana ku dukiyar al’umma da ke hannunmu ba”. Kai ba ma waxannan ba, ko Ibnu Muljamu da ya soki Ali kafin ya cika abin da ya ce: “Idan na rayu, ni ke da alhakin jinina”. Amma bai ce masa kafiri ba.

Haka nan waxanda ya shaya daga da shi Ali a yaqin basasar Raqumi, riwayoyi sun tabbatar da cewa ya hana a bi wanda ya juya baya daga cikinsu, ko a ganimanci dukiyoyinsu, ko a ribace qananan yaransu da matansu. Tattare da kasancewar su kafirai idan waxancan hadisai sun inganta. Daga nan za mu san cewa, Ali *Raliyallahu Anhu* shi ne farkon wanda ya qaryata waxannan hadisai.

Bari ma ka ji, duk waxanda suka shaya daga da sayyidina Ali a yaqin basasar Siffin, bai xauke su kafirai ba. Hasali ma shi ke yi wa waxanda aka kashe daga cikinsu sallah, yana kuma cewa: “Waxannan ‘yan’uwanmu ne da suka yi mana tawaye. Muna fatar takobi ya tsarkake su”. Yana nufin fatarsa ga Allah ya gafarta masu kuskurensu na rashin yi masa mubaya’a albarkacin a zub da jininsu. Ka ga da ya xauka su kafirai ne da bai yi masu sallah ba, ballantana ya ce hakan.

A nan dai ba muna son magana a kan kafircin wani ne ba. Muna son ne a fahimci cewa, duk yadda aka kixa aka kuma raya, waxancan hadisai na nan a matsayinsu na qaryar banza, wadda aka jingina ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. A kuma gane cewa, sun yi ban hannun makafi da addinin musulunci. Wanda kuwa duk ya yarda da su waxannan hadisan to, ya kwana da sanin kafirta gaba xayan Sahabbai har da Ali. Haka kuma wanda ya yi imani da Allah da rana ta qarshe ba zai yarda harshensa ya furta waxannan hadisai yana mai jingina su ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Duk wanda kuwa ya yi haka babu shakka ya keta mutunci da alfarmar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Don haka mun tabbata cewa wani zindiqi ne mulhidi ya qaga waxannan hadisai. Allah ya la'ani wanda ya yi wannan xanyen aiki don ya hargitsa aqidar musulmi, ya ci zarafin magabata, waliyyan Allah. Kai wanda ya yi hakan ma qyacin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ishe shi inda yake cewa: “Allah ya yi tanadin masauki a gidan wuta ga duk wanda ya yi mani qarya da gangan”.

## 5.13 Matsayin Hadissan Shi'ah

Xan Shi'ar ya ce: Idan muka ga 'yan adawa sun riwaito irin waxannan hadisai, to ya wajaba a kanmu mu karve su daga gare su, ballantana ma muna da dubunsu a taska, waxanda muka riwaito daga amintattun malamanmu na hadisi. Haramun ne mu yi kunnen uwar shegu da su.

To, abin da za mu ce a nan shi ne: Ba mu aminta da waxanda 'yan Shi'ah suka aminta da su a matsayin malaman hadisi ba, Iyakar mariwaitanku su zamo kamar jahilan mariwaitan Sunnah. Kuma tunda har malamai masana sun tabbatar da cewa waxanda suka riwaito waxancan hadisai maqaryata ne, to ba ya ko halatta ga 'yan Shi'ah su ci gaba da aiki da abin da hadissan suka tabbatar, tattare da kasancewarsu mafiya qarya da jahilci a kan waxancan.

Kuma za mu gitta ma maganarsa tambayoyi kamar haka:

'Yan shi'ah ina kuka samu wata hujja da ke iya tabbatar da cewa waxanda suka riwaito waxannan hadisai a zamanin farko, amintattu ne? Don kuwa babu wani xan Shi'ah na waxannan za munna a yau, da ya riski xaya daga cikin waxancan magabata nasu, ba su kuma san komai na haqiqanin tarihinsu ba; ba su kuma da littafai da ake iya dogara a kansu don banbancewa tsakanin amintattu daga cikin magabatan nasu da vata gari. Haka kuma ba su da wani isnadi da zai taimaka masu ga sanin mazajen riwayoyin. Ta wannan fuska ma Yahudawa da Nasara sun fi 'yan Shi'ah makama, don abin da ke hannun waxannan na ilimi da ya shafi addininsu, a cikin littafan da Hilalu da Shammas suka rubuta masu, na da kafar shan iska don babu wani abu a hannun sauran mabiyan addininsu da ya sha banban da wancan da ke hannunsu. Savanin 'Yan Shi'ah. Babu wani abu da ke hannunsu face sauran musulmi na da gudumar rosa shi kodayaushe. Su kuwa ba su san komai a kan sauran musulmi ba. Kuma tabbataccen abu ne ta hanyoyi da dama kuma tabbatattu cewa, 'yan Shi'ah maqaryata ne na qarshe, tun zamamim Sayyidina Ali har kawowa yau.

Amma ka ga malaman hadisi a duniyar Sunnah, sun riwaito hadissai daga Harijawa duk da irin qyamar da suke yi ma su, da tarin ingantattun hadissan da aka samo daga wurin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a kan vacin aqidar Harijawan. Wasu hadissan nasu ma na cikin littafin Buhari A cikin Muslim akwai hadissai goma da ya riwaito daga wurin su. To, ka ga wannan sheda ce daga malaman Sunnah ga Harijawa a kan cewa, duk da bidi'arsu da ake qyama da hadissan da suka bayyana cewa, su halakakku ne, amma ba maqaryata ba ne. Ku kuwa, kowa ya sani, soja da farar hula, cewa cikakkun maqaryata ne. Shi ya sa ba hadisin ko xayanku a ingantattun littafai. Allah ya tsarkake su daga wannan.

Duk mai hankali da adalci ya san haka. Amma duk wanda zuciyarsa ce limaminsa, to, ganin idonsa ba zai yi masa fa'ida ba. Duk kuwa wanda Allah ya vatar babu wani mai iya shiryar da shi.

## Zango na Shida
## Daga Cikin Dalilan Shi'ah:
## Xabi'u Goma Sha Biyu Na Ali

Xan Shi'ar ya ce: Mataki na huxu a cikin dalilan da ke tabbatar da shugabancin Ali, shi ne xabi'unsa da suka nuna cancantarsa waxanda sun kai goma sha biyu.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Aliyu *Raliyallahu Anhu* ya kasance mafi tsentseni da gudun duniya daga cikin mutanen zamaninsa, ba Sahabbai kaxai ba. Ya kuma fi kowa ilimi da jaruntaka.

Daga nan sai xan Shi'ar ya kawo wasu karamomi da waxansu martabobi na Ali, ya kuma kafa hujja da su a kan kasancewarsa mafifici a kan Sahabbai.

### 6.1 Zuhudunsa

Ya ce: Martabarsa ta farko ita ce: Gudun duniya. Kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne kawai ya tsere masa a wannan fage.

Amsarmu a nan ita ce: Wannan magana ba gaskiya ba ce. Waxanda suka san ingantaccen tarihin Sahabbai, sun tabbatar wa duniya da cewa, waxanda suka fi kowa zuhudu na shari'ah daga cikin Sahabbai, bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* su ne Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma*.

Dalilansu kuwa su ne: shigar Abubakar *Raliyallahu Anhu* musulunci ke da wuya ya qaras da gaba xayan dukiyarsa saboda Allah, don dama shi mai arziki ne. bayan kuma ya zama halifa, hakan ba ta hana shi shiga kasuwa don neman abin sakawa bakin salati, shi da iyalinsa ba, ta hanyar saye da sayarwa. Har dai watarana Umar ya haxu da shi xauke da barguna a kansa zai je cin kasuwa. Umar xin ya qalubalance shi a kan haka. Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya karva masa da cewa: Kana zaton zamana halifa zai hana in fita don nemo wa iyalina abinci?. Daga nan Umar ya shawarci Abu Ubaidata da sauran Muhajiruna a kan yanka wa halifa Abubakar albashi daga cikin dukiyar baitulmali. A qarshe aka yanka masa albashin darhami biyu a kowace safiya. Amma duk da haka gogan naka, sai da ya sa Umar da Abu Ubaidata suka sha billahillazi, a kan zaman wannan xan kuxi halas gare shi, sa'annan fa ya fara karva.

Harwayau kuma dai halifa Abubakar bai tsaya nan ba, sai ya haxa hancin dukiyar can tasa gaba xaya ya zuba ta baitulmali. Da ajalinsa ya qarato kuma sai ya umurci 'yarsa Aishah da cewa, kada su ci ko sisi daga cikin albarkar da dukiyar can tasa ta yi a sakamakon zamanta cikin baitulmali. Ya ce wannan kan haqqin musulmi ne. A qarshe, bayan rasuwarsa abin da ya bari gado shi ne, wani gwado, da farashinsa bai kai dirhami biyar ba, da wata kuyanga 'yar habasha, wadda ke shayar da xan autansa. A wata riwaya aka ce, bawa dai ne Bahabashe aka samu da wani raqumin xibar ruwa, su ne suka zama dukiyar gadonsa. Nan take sayyida Aishah *Raliyallahu Anha* ta aika da su wurin Umar *Raliyallahu Anhu* bisa wancan umurni na mahaifinta. Isar

dukiyar ke da wuya sai Sahabi Abdurrahman xan Aufu ya ce wa Umar: Ni a ganina bai kamata a raba iyalin Abubakar da wannan dukiya ba. Umar dai ya qi karva yana mai cewa: "Na rantse da Ubangijin Ka'aba tun da Abubakar ya kalli cin wannan dukiya laifi tun yana raye, ba yadda za a yi ko ni in tara kaina gare ta bayan rasuwarsa".

Bisa wannan dalili ne malamai suka ce: Ko shakka babu Ali *Raliyallahu Anhu* mai gudun duniya ne, amma gudun duniyar Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya fi nasa. Bisa dalilin kasancewarsa mai tarin dukiya tun farkon musulunci, amma ya ba ta baya, ya miqa ta ga hidimar addini don neman yardar Allah. Ga kuma yadda ya kasance bayan ya zama halifa.

Amma shi kuwa Ali *Raliyallahu Anhu* kamar yadda xan Zanjawaihi ya ce, talaka ne a farkon musulunci, shi ake taimakawa ba ya iya taimakon kowa. Bayan haka ne ya sami dukiya wadda ta haxa da gonaki da itacen dabinai da sadaqoqi. Kuma ko da ya yi shahada yana da kuyanga goma sha tara da matan aure huxu. Wannan kuma duk halal ne, Alhamdu lillahi. Amma dai bai yi umurni da a mayar da komai daga cikin wannan dukiya zuwa baitulmali ba. Duk da yake babu wata illa a cikin rashin yin hakan don halaliyarsa ce. Bayan rasuwar tasa ne ma xansa Hasan ya gaya wa mutane a cikin wata huxuba da ya yi cewa: Mahaifina bai bar zinari ko azurfa ba. Ya dai bar dirhami xari bakwai. Ko su da ya sami dama da ya yi sadaka da su kamar yadda ya saba.

Kuma Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce: Na kasance a lokacin rayuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ni kan xaura dutse a cikina, saboda tsananin yunwa. Amma ga shi yau ni kan fitar da kusan dinari dubu Arba'in a matsayin zakka. A wata riyawa aka ce dinari dubu huxu.

Ko alama, ba a haxa Ali da Abubakar *Raliyallahu Anhu* a fagen gudun duniya, duk da yake dukansu masu gudun duniyar ne.

Shi kuwa Ibnu-Hazmi cewa ya yi: Na ji wasu na cewa, wai Ali shi ne mafi gudun duniya a cikin Sahabbai. Duk wanda ya faxi wannan magana maqaryaci ne, kuma jahili. Dalili kuwa shi ne: Idan dai har gudun duniyana nufin kakkave rai daga sha'awar kaxe-kaxe da waqe-waqe da dukiya, da abubuwan jin daxi, da karkata ga 'ya'ya da tara fadawa, wanda bani zaton akwai wata ma'ana ga kalmar zuhudu wadda ta wuce wannan. To, idan ta tabbata hakan, to, ta fuskar kakkave rai daga sha'awar dukiya, ko shakka babu halifa Abubakar ne shago a wannan fage.

Duk wanda ke da masaniya da ingantaccen tarihin Sahabbai ya san cewa, ko da halifa Abubakar ya musulunta baya rasa kuxin da suka kai dinari dubu arba'in, amma ya saxaukar da su kacokan saboda Allah. Ya yi haka ne kuwa ta hanyar fansar bayi muminai masu rauni, waxanda kafiran Makka ke azabtarwa, saboda kawai sun yarda da Allah. Kuma bai yi haka ba don su qare shi da komai da qarfinsu, illa dai da zaran ya ga ana azabtar da bawa ko baiwa don sun yarda da Allah *Subhanahu WaTa'ala* sai ya fanshe su ya 'yanta su. Haka ya ci gaba da yi, har abin da ya rage hannunsa, a dai dai lokacin da za su yi hijira tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, bai fi dirhami

dubu shida ba. Haka Sahabi Abubakar ya qulle waxannan kuxin, ya bi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai bar wa iyalinsa ko anini ba. Qarshenta kuma a can Madinah ya kashe su gaba xaya wajen xaukaka Kalmar Allah. Aka wayi gari Abubakar bai mallaki ko sisi ba, sai wata tsohuwar Abaya da yake fama da ita wadda yake shinfixawa in dare ya yi ya kwanta sama, idan kuma rai ya kai ita zai rufa a jikinsa ya fita neman abinci.

A dai dai lokacin da wasu Sahabbai suka mallaki manya – manyan gonaki da lanbuna da tarin dukiya ta halal. Ka ga sai dai wanda duk ya ba da baya ga irin wannan dukiya ya ciyar da ita wajen xaukaka kalmar Allah, ya fi wanda ya aje wata don Allah, gudun duniya.

Ya ci gaba da cewa: Ko bayan da Abubakar ya zama halifa, tarihi ya tabbatar da cewa bai aje kuyanga ko xaya ba. Bai kuma tara mahaukaciyar dukiya ba. Qarshen ta ma kafin ya rasu sai da ya qiddidiga xan abin da yake karva daga baitulmali a matsayin albashi, don ciyar da iyalinsa, ya yi umurni da a cire kwatankwacinsa daga cikin dukiyarsa a mayar baitulmali. Ita wannan dukiya da yake batun xiba a kai baitulmali, ya same ta ne, ta hanyar tara abin da ake ba shi na ganimar yaqoqan da ya halarta a tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, wanda kuma ya ci gaba da juyawa har zuwa lokacin da ya zama halifa ya fara xaukar albashi.

A irin wannan nau'i na zuhudu ne, na nisantar dukiya da ababen jin daxi halifa Abubakar ya yi wa sauran Sahabbai fintinqau; ba Aliyu ba, ba waninsa ba. Abu Zarri da Abu Ubaidata ne kawai, za'a iya kwatantawa da shi a wannan fage, daga cikin mazajen farko na Muhajiruna don su, sun xore da abin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bar su a kai na irin wannan zuhudin. Bayan waxannan biyu sai ko halifa Umar shi ma ya kwatanta irin wannan zuhun na Abubakar *Raliyallahu Anhu* Amma ko alama Aliyu *Raliyallahu Anhu* bai kai ga Umar ba a wannan fage, balle daxa ga shi uban tafiya, watau Abubakar.

Amma shi kam sayyidina Ali, ya tara dukiya amma ta halal. Ko da ya mutu kuma yana aure da mata huxu, haxe da kuyangi goma sha tara waxanda ke jiran 'yanci da farin ciki a daidai lokacin da ake kuka da baqin cikin mutuwarsa. Haka kuma ya bar bayi da barori da dama, da 'ya'ya ashirin da huxu; maza da mata, da dukiya da kayayyaki masu tarin yawa, waxanda magadansa suka samu kansu a cikin sahun manyan mawadata daga cikin attajiran wancan lokacin. Wannan magana ba a voye take ba, ta shahara matuqa, ko 'yan aji xaya a ilimin hadisi da tarihin musulunci sun san ta. Ina Ali ina Abubakar a wannan fage?!

Ta vangaren abin da ya shafi qalahucin 'ya'ya da tariyar mabiya. Tarihi ya tabbatar da cewa, tattare da halifa Abubakar nada 'ya'ya da makusanta irinsu Xalhatu xan Ubaidullahi, xaya daga cikin Muhajiruna na farko kuma na gaba-gaba a sahun ma'abuta daraja da xaukaka a cikin kowane fage a tarihin musulunci. Da kuma irin su xansa Abdurrahman.

Ga kuma irin darajar abokantakar da ke tsakaninsa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* mai daxaxxen tarihi. Da kuma kasancewarsa Sahabin da ya fi kowane Sahabi ladar hijira, qafarsa qafar Annabi. Da kuma sauran darajojinsa waxanda ko rana ba ta fi su zama sarai ba idan ta fito. Amma duk da waxannan muqamai da mata kai da halifa Abubakar ya kevanta da su, bai naxa xaya daga cikin waxannan makusanta nasa, a matsayin gwamna ba, a jahohin musulunci irin su Yaman, duk kuwa da irin faxin da take da shi da tarin aikin yi da ke cikinta. Ga kuma irin Oman da Hadramauta da Baharaini da Yamama da Xa'ifa da Makka da sauran yankunan hijaz. A tsawon halifancinsa, Abubakar bai kai ko xaya daga cikinsu a waxannan garuruwa ba, a matsayin ma'aikaci. Ba kuwa don rashin cancantarsu ba. A'a, ya yi haka ne don saunar talalaviya ta kwashe shi ya kasa tsawata masu saboda kusancinsu zuwa gare shi.

Wannan godabe na Sahabi Abubakar *Raliyallahu Anhu* shi ne wanda Umar *Raliyallahu Anhu* ya bi a lokacin da ya zama halifa. Duk da faxin daular musulunci a wannan lokaci, Umar bai kai xaya daga cikin makusantansa, bani Adiyyi xan Ka'abu a matsayin gwamna a ko xaya daga cikin biraren ba, har kuwa da waxanda shi ne da kansa ya ci su da yaqi irin su, Sham da Masar da gaba xayan daular Farisa zuwa khurasana, sai fa Nu'manu xan Adiyyu. Yana cikin dangin sayyidina Umar, da yake qaddara ta riga fata, har Umar ya naxa shi gwamna a Masar, amma kuma tun ba a je ko ina ba ya tuve shi.

Ba kuwa don komai Umar ya qi saka banu Adiyyi cikin sha'anin mulki ba illa zuhudu. Domin idan cancanta ce, babu wata qabila ko zuri'a daga cikin Quraishawa da ta fi su cancanta. Don ko a lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi hijira su gaba xaya suka kwashe, qwansu da kwarkwatarsu suka bi shi, ba su bar kowa daga cikinsu a Makka ba. A cikin waxannan dangi kuwa akwai fitattun magabata, irin su: Sa'idu xan Zaidu, xaya daga cikin *Asharatul Mubassharuna Bil Jannah*, da Abul Jahmi xan Huzaifa da Ma'amaru xan Abdullahi da Abdullahi xan Umar. Allah ya yarda da su baki xaya.

Irin wannan zuhudu ne harwayau, ya hana halifa Abubakar naxa xansa Abdurrahman a matsayin magadinsa, tattare kuwa da kasancewar xan nasa Sahabi. Haka kuma Umar bai naxa xansa sarauta ba a lokacin da yake raye, bai kuma naxa shi matsayin yarima mai jiran gado ba. Tattare kuwa da shi xan nasa na xaya daga cikin Sahabbai masu daraja kuma zavavvu, ya kuma cancanci halifanci. Kai har ma wasu sahhabai sun fara tattaunawa da amincewa a kan ya gaji mahaifinsa Umar. Ka ga ko naxa shi xin ya yi babu mai tayar da qayar gaba balle ta baya. Amma namijin duniyar bai yi hakan ba.

Amma ka ga shi Sahabi Ali *Raliyallahu Anhu* naxa shi ke da wuya sai ijtihadinsa ya nuna masa dacewar naxa makusantansa. Ya naxa Abdullahi xan Abbas gwamna a Basra, Ubaidullahi xan Abbas a Yaman, Qusamu a Makka da Ma'abadu a Madina. Duk waxannan qannensa ne su huxu, 'ya'yan baffansa Abbas. Ya kuma naxa xan yarsa Ummu Hani'i xiyar Abu Xalib a matsayin

gwamnan Khurasana. Sai kuma agolansa Muhammad xan Abubakar, ya naxa shi gwamnan Masar. Haka kuma Ali *Raliyallahu Anhu* ya aminta da mubaya'ar da mutane suka yi wa xansa Al-Hassan a matsayin yarima kafin cikawarsa.

Ba muna musanta cewa, Hassan ya cancanci zama halifa bayan Ali *Raliyallahu Anhu* ba. Ko kuma kasancewar Abdullahi xan Abbas ya cancanci zama gwamnan Basra ba. Kai, xan Abbas xin ma da an naxa shi halifa ya yi daidai. Amma manufa a nan ita ce, ba ka haxa zuhudun waxanda suka hana 'ya'yansu da 'yan'uwansu sarauta alhalin sun cancance ta, da zuhudun wanda ya naxa makusantansa kodayake sun cancanta xin.

Dubi irin Xalhatu xan Ubaidullahi, nagartaccen Sahabi, xaya daga cikin *Asharatul Mubassharun Bil Jannah.* Ba abin da ya hana Abubakar ya yi masa gwamna in ba don kusancinsu ba. Haka ma Sa'idu xan Zaidu, ko shakka babu ya kai matuqa a fagen dacewa da sarauta, kuma shi ma yana cikin *Asharatul Mubassharun Bil Jannah.* Amma Umar bai naxa shi ba, don zuciyarsa na cewa, ana barin halas don kunya.

### 6.1.2 Ali Ya Rabas Da Duniya

Xan Shi'ar ya ce: Haqiqa Ali ya saki duniya saki uku. Saboda ya kasance ba ya da abinci sai tsakin alkama, wanda ya kan rufe don kada Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* su zuba masa miya a ciki. Kuma baya da tufafi sai masu kaushi da gajarta. Rigar ma da yake sakawa ta sha dashi har ta gaji, ta yadda har aka wayi gari yana tunanin yadda zai kama ta ya dasa. Haka kuma maxaurin takobinsa da takalmansa duk na tsawo ne.

Xan Shi'ar ya ce: Akhxabu Khuwarizim ya riwaito daga Ammaru wanda ya ce: Na ji Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yana cewa: "Ya kai Aliyu! Haqiqa Allah ya yi maka wani irin ado mafi soyuwa gare shi, wanda bai tava yi wa wani daga cikin bayi irinsa ba. Ga shi ya dai saka ka mai gudun duniya kuma maqiyinta, ya kuma sanya ka mai qaunar talakawa, wanda hakan ta sa suka yarda da kai a matsayin shugaba kamar yadda ka yarda da su a matsayin mabiya. Ya kai Aliyu! Ka sani farin ciki ya tabbata ga duk wanda ya so ka, ya kuma yi gaskiya a kanka, haka kuma boni ya tabbata a kan duk wanda ya qi ka, ya kuma yi maka qarya. Waxanda duk suka so ka, suka kuma yi gaskiya a kanka su ne 'yan'uwanka a cikin addininka, kuma masu tarayya da kai a cikin al'amarinka. Su kuwa waxanda suka qi ka, suka kuma yi maka qarya, Allah ya yi alqawarin tabbatar da su a gurbin maqaryata".

Haka kuma suwaidu xan Gafalata ya ce: Na shiga wurin Ali *Raliyallahu Anhu* da la'asariyyar nan, na taras da shi zaune ya rungume kwanon madara mai zafi, ta yadda har qanshinta na bugun hancina saboda tsananin gumin da ke fitowa daga cikinta. Yana kuma riqe da gurasa wadda a jikinta nake hangen dusar alkama. Yana yi yana gutsurar gurasar da hannunsa. Idan haka ta buwaya sai ya karya ta da guwayyunsa ya jefa cikin kwanon madarar. Da na shigo sai ya ce mani: matso ka xanxana irin abin da muke kalaci da shi. Sai na ce masa, ai ina azumi ne. Sai shi kuwa ya karva mani da

cewa: Na ji manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na cewa: “Duk wanda azumi ya hana shi cin wani abinci da yake sha’awa, Allah ya yi alqawarin ciyar da shi abincin Aljanna, ya kuma shayar da shi abin shanta”. Daga nan ni kuma sai na juya ga wata kuyanga tasa da ke tsaye wajena, na sassauta murya na ce mata: Amma dai baki kyauta ba ya ke Fiddahatu. Ba ki gudun Allah ya kama ki da alhakin wannan dattijo? Irin yadda kika yi masa gurasa haka da alkama da ba a surfe ba? Sai ta karva mani da cewa: “Wallahi ba laifina ba ne”. Shi ne ya sharxanta mana rashin surfe duk alkamar da za mu yi masa abinci da ita. Sai sayyidina Ali ya ce: Maganar me kake yi da ita? Na gaya masa. Sai ya ce: “Na fanshe shi da uwata da ubana, wanda ba a tava surfe ma abinci ba, bai kuma tava jera kwana ukku yana qoshi da gurasa ba har ranar da Allah ya karvi rayuwarsa”. Ali kuma ya sayi gwado biyu, ya ce Qambar ya zavi xaya, shi kuma ya xauki xayan. Ya kuma ga hannun rigarsa ya rufe yatsarsa sai ya datse hannun rigar.

Haka kuma Dhiraru xan Damrata ya ce: Watarana na shiga wurin Mu’awiyah bayan rasuwarsarkin Musulmi Ali sai ya nemi in ba su labarin siffofin Ali. Sai na ce: Tuba nake Allah ya taimake ka. Sai ya nace a kan lalle sai na yi hakan. Na ce, to, tunda haka ne, Allah ya taimakeka! Na rantse har da Allah halifa Ali sarari ne mai qare gudun doki. Antaru ne sarkin qarfi. Shafe zane ne a fagen magana. Kuma a duk lokacin da zai yi hukunci ya kan yi adalci, marmaron ilimi na vuvvuga dama da hagunsa, kuma harshensa shi ne maqerar hikima. Ya kasance mai qyamar duniya da qawace-qawacenta.

Ya kuma fi miqe qafa da walwala a cikin dare, kuma lokacin da yake shi kaxai. Sarki musulmi Ali ya kasance mutum mai kaifin basira da zurfin tunani, ya fi kuma sha’awar tufafi masu kaushi da abinci maras taushi. Idan muna tare da shi baka iya gane wa ye sarki wa ye bafade? Don babu wata tambaya da za mu yi masa face ya bamu amsarta. Idan kuma muka gayyace shi zuwa gidajenmu ko wata harka zai tafi kamar kowa. Amma wallahi tattare da irin wannan kusanci da muke da shi, da shi, babu xayanmu da ba ya shakkar yi masa magana, saboda kwarjininsa.

Mutum ne mai girmama ma'abuta addini da jawo talakawa a jiki. Ba ya cin zarafin masu qarfi ba ya kuma zaluntar masu rauni. Hakan kuma ba ta sa masu qarfi zaton zai xaure masu gindi a kan varna, ko masu rauni su yanke qauna daga samun cetonsa. Idan rantsuwa da Allah na tava ganin shi yana cewa: “Ya ke duniya! Ki ruxi wani, ni har abada ba ni son ki ba ni qaunarki. Na sake ki saki ukku, wanda babu kome a ckinsu. A sane nake da cewa, shekarunki taqaitattu ne, haxarinki kuma mai yawa ne, rayuwa kuma a cikinki qasqanci ce”. “Kaico! Mun shiga uku.. Ga guzurinmu xan kaxan, tafiyarmu mai nisa, hanyoyinmu na cikinsunqurmin daji”.

Ina kawowa nan, sai Mu'awiyah ya fashe da kuka, yana cewa: “Allah ka yi rahama ga baban Hassan. Wallahi yadda ka siffanta shi xin nan haka yake”. “Ya kake jin baqin cikin mutuwarsa ya kai Dhirar?” Sai na ce masa: “Kamar

baqin cikin matar da aka yanka jinjirinta, tana ji tana gani. Kai, irin kukan uwar Musa da ba ji ba gani.

**Martani:**

Ba mu da ja game da abin da ya shafi gudun duniyar Ali. mun yarda da haka; bamu da wata shakka a ciki. Amma bamu yarda ya fi Abubakar da Umar a wannan fagen ba. Kai ko da waxannan hikayoyi da ya kawo ba su nuna haka.

Amma kasancewar Ali *Raliyallahu Anhu* ya saki duniya saki uku, mu mun yarda da shi, don gaskiya ne. Kuma wannan maganar ta shahara daga wurinsa. Amma ba ta nuna cewa ya fi duk wanda bai ce haka ba gudun duniya. Domin kuwa Annabinmu da Annabi Isah xan Maryam da wasunsu basu faxi irin wannan magana ba. Tattare da cewa sun fi Ali *Raliyallahu Anhu* gudun duniya. Hasali ma dai ai ba wajibi ba ne idan mutum na gudun duniya sai ya faxa wa duniya haka da bakinsa, ya ce: "Ni mai gudun duniya ne". Wanda kuma ya yi qarfin halin faxin hakan ba lalle ba ne ya kasance hakan.

Don haka, wannan maganar da ita da babu duk xaya. Faxar ta bai tabbatar da aiki, rashin faxar ta bai hana samun sa.

Haka kuma cewar da marubucin ya yi wai sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* ba ya da abinci sai gayan tsakin alkama. Wannan ma ba ya zama dalili a kan fifikonsa, saboda abubuwa biyu:

Na farko: Ko shakka babu wannan magana qarya ce.

Na biyu: Ko da ta inganta, babu yabo a cikinta. Domin kuwa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne shugaban masu gudun duniya, amma duk abin da ya tari gabansa da shi yake aiki. Bai tava cewa ba ni son wannan ba, ko lalle ne sai an samo mani wancan. Da za a kawo masa naman kaza ko na bisashe, shi zai ci. Kamar yadda idan alawa ko zuma ko wani 'yayan itace ya tari gabansa, da shi zai yi kalaci. Idan ma bai sami komai ba, da yunwa zai kwana.

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kasance idan aka kawo masa abin ci ko abin sha, kowane iri ne, idan yana sha'awarsa zai ci, idan kuwa baya sha'awarsa zai bar shi, ba tare da wani zargi ko suka ba. A sakamakon wannan ne watarana yakan xaura dutse a cikinsa don yunwa. Wani lokaci ma a kanshare wata xaya ko biyu ba a hura wuta gidansa ba.

Kuma kasancewar maxaukan takobin Ali *Raliyallahu Anhu* da takalminsa na tsawo, kamar yadda xan Shi'ar ya faxa, ba gaskiya ba ne. Koda kuma ya zama gaskiya, to ba abin yabo ba ne a gare shi. Domin kuwa an riwaito cewa, takalmin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na fata ne, maxaukan takobinsa kuma na zinari da azurfa. Kasancewar su mawadata, da yawaitar fata a wurin su na sa qin amfani da ita fatar ya zama ba abin yabo ba. An kuma riwaito Manzon Allah na amfani da takalminta.

Kamar yadda Abu Umamatal-Bahiliyyu ya ce: Haqiqa wasu mutane da ke linzamin doki da tsawo su ke kuma hawan qarqashin dawaki sun ci manyan

garuruwa da yaqi. Buhari ya riwaito wannan. Mai maganar na bayyana halin musulmi ne kafin nasara.

Hadisin Ammar da ya kawo dai yana cikin hadissan qarya. Haka ma hadisin Suwaidu xan Gaflata ba daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ba.

Amma labarin tufafin da Aliyu ya saya sananne ne. Labarin Dhiraru xan Dhamrata kuma, an riwaito shi. Sai dai babu wani abu daga cikin ko xayansu da ke nuna cewa, Ali *Raliyallahu Anhu* ya fi Abubakar da Umar Allah ya yarda da su gudun duniya. Hasali ma, duk wanda ya san tarihin Sayyidina Umar da adalcinsa da zuhudunsa, da yadda ya kauce ma naxa makusantansa ga muqamai da tauye rabon xansa daga cikin arzikin qasa daga na takwarorinsa da ya yi. Haka ita ma 'yarsa ya rubuta mata qasa ga na takwarorinta. Da irin yadda ba ya shan romo da babge, tattare da kasancewarsa wanda ya rarraba taskokin Kisran Farisa da Qaisar na Roma. Mafi yawan arzikin da Ali ya yi rabo daga cikin sauran na Umar ne. Amma duk da haka, Umar ya rasu ana bin sa bashin dirhami dubu tamanin. Ka ga ta fuskoki da dama, hakan na tabbatar da cewa, Umar *Raliyallahu Anhu* na gaba da Ali *Raliyallahu Anhu* wajen gudun duniya. Daman dai shi Abubakar *Raliyallahu Anhu* a wannan fage, ya zarce su duka.

### 6.1.3 Zuhudu Bai Zama Hujja!

Xan Shi'ar ya ce: A taqaice, tunda har babu wanda ya kama qafar Ali a zuhudu, balle wanda ya wuce shi, ta tabbata shi ne gwarzo a fagen. Haka kuma na tabbatar masa zama shugaba, don ba ya yiwuwa a gabatar da wanda bai kai shi ba a kan sa.

### Martani:

Amsarmu a nan ita ce: Mun riga mun tabbatar da cewa, Ali *Raliyallahu Anhu* bai fi Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* gudun duniya ba. Wannan kenan, kuma ko da ta tabbata cewa, ya fi sun, to, ai ba lalle ne sai wanda ya shahara a fagen zuhudu ba, ya fi kowa cancanta da shugabanci. Balle kuwa tarihi ya tabbatar da akasin haka, don dukiyar da Ali *Raliyallahu Anhu* ya mallaka ta tsabar kuxi da kuyangi, da wadda muqarrabansa suka mallaka Abubakar da Umar basu mallake ta ba, haka ma muqarrabansu.

### 6.2 Yawan Ibadarsa

Xan Shi'ar ya ce: Bayan wannan kuma Ali ya kasance mafi yawan ibada daga cikin mutane. Domin babu ranar da ba ya azumi, babu daren da ba ya qiyamul laili. Shi ne wanda ya koya wa mutane sallar dare da nafilolin rana. Kuma idan aka tara ibadun da yake yi, da addu'oi irin waxanda aka riwaito daga gare shi, ba za a iya qare su ba, sai wani sarki ya ci ya fita. Don bai tava kasa yin raka'a dubu ba cikin kowane dare da yini. Sallar dare ba ta tava wuce shi ba, ko da kuwa daren yaqi.

Kuma wai in ji, xan Abbas ya ce: Na ga Ali *Raliyallahu Anhu* watarana a fagen fama yana kirdadon rana. Sai na tambaye shi dalilin yin haka. Ya karva da mani da cewa: Ina kirdadon ta ne in gani in ta yi zawali don in yi sallah. Sai na ce masa: Sallah na yiyuwa a irin wannan halin? Shi kuwa ya ce mani: To, ai don tabbatar da sallah muke yaqin.

Ka ga kenan inji xan Shi'ar mawuyacin halin da ake ciki na yaqi bai shagaltar da Ali *Raliyallahu Anhu* daga tsayar da ibadar sallah a farkon lokacinta ba.

Kuma wai, saboda tsananin kulawarsa da ibada, idan ana son cire wani makami na qarfe daga cikin jikinsa, sai a bari sai ya kabbarta sallah, don da zarar ya fuskanci Ubangiji, to ba ya jin kira ko jifa; duk abin da zai same shi na raxaxi ba ya jinsa, haka kuma dai Aliyun ne *Raliyallahu Anhu* ya jefi tsuntsaye biyu da dutse xaya, a lokacin da ya yi sadaka da wani abu, alhali yana cikin ruku'i. A kan haka Allah *Subhanahu WaTa'ala* ya saukar da wata aya. Wai kuma akwai wani lokaci da aka kwashe kwanaki uku da sai an sauke sanwar abinci a gidan Ali *Raliyallahu Anhu* sai kawai ya rungumi tukunyar ya yi sadaka da abincin baki xaya. A kan haka ne ma Allah ya saukar Suratul Insan wadda ke farawa da:

﴿هَلۡ أَتَىٰ عَلَى ٱلۡإِنسَٰنِ حِينٞ مِّنَ ٱلدَّهۡرِ﴾ الإنسان: ١

*Haqiqa wata mudda ta zamani ta zo a kan mutum. Suratul Insan:1*

Kai babu wani lokaci da yanayi, dare da rana, zahiri da baxini wanda Ali *Raliyallahu Anhu* bai yi sadaqa a cikinsa ba. Ayar da ta umurci Sahabbai da gabatar da wata 'yar sadaka kafin su gana da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, Ali *Raliyallahu Anhu* ne sanadin saukarta, don tun kafin ta sauka ya yi hakan. Bayin kuma da ya 'yanta sun kai dubu, na qashin kansa. Ya kuma kasance a lokacin da aka sa masu linzamin tattalin arziki yana aikin lebaranci ya bai wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kyautar jingar.

Xan Shi'ar ya kammala da cewa: Wannan kasancewar ta Ali *Raliyallahu Anhu* mafi yawan bautar Allah *Subhanahu Wa Ta'ala* daga cikin mutane, na tabbatar da kasancewarsa mafi cancanta da zama halifa kai tsaye, bayan wucewar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.*

**Martani:**

Duk wanda ya san tarihin Sahabban Manzon Allah, ba ya musun cewa, waxannan labarai qaryayyaki ne kawai aka qirqira. Tattare da haka kuma babu wani abin yabo a cikinsa ga Ali *Raliyallahu Anhu* kamar yadda muka tabbatar da haka a cikin qaryayyakin da suka gabata.

Abu na farko dai, cewar da ya yi Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* na azumtar kowace rana da sallatar kowane dare, qarya ce yake yi masa. Don faxar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ta inganta inda ya ce: Amma ni, ni kan yi azumi, ni kan kuma sha. Ni kan yi sallar dare, ni kan kuma yi barci. Ina kuma auren mata. Duk kuwa wanda ya bar sunnata baya tare da ni.

Haka kuma Buhari da Muslim sun riwaito a cikin ingantattun littafansu cewa, Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya buga mana qofa, ni da Fatima a wani dare ya ce: Ba za ku tashi ku xan tava sallar dare ba? Sai na ce masa: Ya Manzon Allah! Ai ka san rayukanmu a hannun Allah suke. Idan ya yi nufin za mu tashi, sai ya tayar da mu. Sai ya juya yana buga cinyarsa yana cewa: *Kuma mutum ya kasance mai yawan jayayya [ 18:54].*

Ka ga wannan hadisi ya tabbatar mana da cewa Ali *Raliyallahu Anhu* yakan yi barcinsa a wani dare. Don ga shi har abin ya xauki hankalin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* har ya zo ya qwanqwasa masa qofa don ya tashi, ka kuma ji amsar da ya ba shi, wadda ta sa shi ya koma yana maimaita faxar waccan aya.

Kuma cewar da xan Shi'ar ya yi, daga wajen Ali *Raliyallahu Anhu* mutane suka kwaikwayi sallar dare, da nafilolin rana. Idan yana nufin akwai waxansu mutane kevantattu da suka koyi wannan ibada daga wajen Ali, to, ai wannan ba abin tinqaho ba ne, don babu xaya daga cikin Sahabbai da wasu mutane ba su koyi irin waxannan ibadu daga wurinsu ba. Idan kuma marubucin na nufin gaba xayan duniyar musulmi a wurin Ali *Raliyallahu Anhu* ne ta koyi qiyamullaili, to, qaryarsa ta sha qarya. Domin kuwa qasashen da Umar da Usmanu suka ci da yaqi, mafi yawansu, irin su Sham da Masar da qasashen yamma, duk jama'arsu na yin sallolin dare da nafilolin rana, duk da cewa ba su tava haxuwa da Ali ba. Haka kuma sauran Sahabbai suka kasance, duk suna gudanar da waxannan ibadodi tun zamanin *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama*, kuma shi ne ya koya musu su. Amma idan aka ce mutanen Kufa ne, 'yan Shi'ah, suka koya daga wajen Ali *Raliyallahu Anhu*, to, ko ba haka abin yake ba ana iya yarda.

Amma dai mu abin da muka sani na haqiqa shi ne mutanen Kufa sun koyi irin waxannan ibadodi ne daga wurin Abdullahi xan Mas'udu *Raliyallahu Anhu* da wasu Sahabbai, waxanda suka saba da mutanen Kufar, kafin Ali *Raliyallahu Anhu* ya sadu da su. Kuma ko da shi Aliyu ya isa Kufa, bai taras da su jahillan sallah ba. Mutane ne masu yawan ilimi da riqo da addini tun kafin wannan lokaci. Shi kuwa xan Mas'udu da sauran Sahabbai da ke tare da shi a qufa kafin wannan lokaci na zuwan Ali *Raliyallahu Anhu,* faxin suna da ilimi da riqo da addini bai ko taso ba.

Cewar kuma da marubucin ya yi wai, addu'oin da aka riwaito daga wurin Ali, na xaukar dogon lokaci kafin a gama su, saboda tsawonsu, wannan ma qiren qarya ne. Don mafi yawan addu'oin ba su da wani isnadi da ke danganta su ga shi Ali *Raliyallahu Anhu*. Kuma irin matsayin da yake da shi, da yanayin rayuwarsa da ta sauran Sahabbai a wancan lokaci, duk sun sava wa, abubuwan da addu'oin suka qunsa. Kuma ai addu'oin *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* su ne mafificin abin da musulmi zai roqi Allah  da shi. Su ne kuma zavavvun mutane daga cikin wannan al'umma na farko da na qarshe ke roqon Allah da su.

Ita ma cewar da ya yi Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* na sallah ra'aka dubu a cikin yini da dare, qarya ce, bata kuma xaukaka darajar Ali da komai ba. Dalili kuwa shi ne, waxannan raka'oi sun yi wa lokacin yawa. Sai fa in ba da natsuwa ake yin su ba. Kuma ko Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, tattare da kasancewarsa mafi qwazon mutane a wajen bautar Allah, bai tava wuce raka'a arba'in ba. Shiriyarsa kuwa ita ce mafi daidaitar shiriya. Tuna da nauyin jama'a da ya ke bisa kansa, to, yaushe ya sani sukunin yin waxannan raka'oi, ya kama gudanar da shugabancin jama'a da na iyalan gidansa, sai fa idan qoton kurciya ya ke yi. Wannan kuwa irin sallar munafukai ce, wadda Allah ya tsarkake Ali *Raliyallahu Anhu* daga yin irinta.

A daren yaqin Siffin kuwa, abin da ya inganta daga Ali *Raliyallahu Anhu* shi ne, ya yi zikirin da Manzon Allah ya naqalta wa Fatima na lokacin kwanciya. Ali ya ce: Tun lokacin da na ji wannan zikiri daga wajen Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ban tava wasa da shi ba. Waxanda ke tare da shi suka ce: Har cikin qurar yaqin siffin? Ya ce: Eh, na tuna shi a qarshen daren, sai na faxe shi.

Haka kuma labarin da xan Shi'ar ya bayar na salon fitar da makamin qarfe daga jikin Ali, shi ma qarya ne. Babu inda aka samu wani qarfe ya tava ratsa jikinsa. Haka zancen sadaka a cikin sallah, duk shegiyar xarin ce. Idan ka kalle ta da idon basira, za ka taras cin mutumcin Ali ne. Domin da ace yin haka abu ne karvavve a idon shari'a, to, da ya zama abin wajabtawa ga musulmi su yi haka. Da kuma an wayi gari musulmi na yin haka, kuma an taras da musulmin wancan lokaci sun yi. Wato, suna sallah suna rabon sadaka. Amma da ya zama ba a samun wani jigon musulmi da ya yarda da yin haka ba, to, mun wadatu da rashin zaman hakan ibada. Kai makaruhi ma ne.

Ita ma dai maganar gabatar da 'yar sadaka sahunsu guda waccan.

Idan muka koma kan cewar da ya yi, wai Ali ya 'yanta bawa dubu na qashin kansa. Shi ma wannan qarya ce da ba ta sauraruwa sai ga kidahuman jahillai. Ina Ali *Raliyallahu Anhu* ya ga bayin qashin kansa da suka kai wannan adadi, ko ma rabi? Wace sana'a ce ya yi ya samu waxannan kuxi? Mutumin da duk rayuwarsa an san inda ta qare wajen taimakon addini, ta fuskar jihadi da sauransu.

Ita ma cewar da malam Zurqe ya yi wai, Ali *Raliyallahu Anhu* kan yi aikin lebara a cikin tungarsu har ya taimaka wa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da kuxin jingarsa, qarya ce kamar sauran. Ga dalili:

Na farko: A wancan lokaci babu mai fita daga cikin tungar, balle ya tafi wata. Babu kuma wanda zai xauke shi qwadago ko da ya fita xin. Don mushrikai sun riga sun yi game ta kai a kansu.

Na biyu: Abu Xalib, a wancan lokaci shi ne yake xauke da nauyinsa shi kansa Ali xin.

Na ukku: Nana Khadijah ita ma a wancan lokaci, attajira ce, tana kuma tsaye iya qoqarinta a kan ciyar da dukiyarta.

Na huxu: A tarihi ba a tava jin lokacin da Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi aikin qwadago ana Makka ba. Kuma a wannan lokaci shi, qaramin yaro ne, wanda matsayinsa bai wuce na matashi ko babane ba. Saboda haka yana cikin waxanda ake taimaka wa a cikin tungar. Ko dai ya zan Annabi ke taimaka masa, tun da a hannunsa ya ke, ko kuma babansa Abu Xalib ke xauke da xawamiyarsa. To, ta ina zai taimaka ma *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* a wancan lokaci?

**6.3 Fifikonsa a Fagen Ilimi**

Xan Shi'ar ya ce: Abu na uku shi ne, kasancewar Ali *Raliyallahu Anhu* wanda ya fi kowa ilimi daga cikin mutane bayan Manzo Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Amsarmu a nan itace: Ahlus-Sunnah dai ba su yarda da wannan magana ba. Suna kuma hani daga faxinta. Abin da kan malaman Sunnah ya haxu a kai shi ne, wanda ya fi kowa ilimi daga cikin mutane bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne Abubakar, sannan Umar na rufa masa baya.

Wannan maganar ta malaman Sunnah kuwa ba akan ruwa aka gina ta ba. Domin a zamanin *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* babu wanda ke zartar da wani hukunci, yayi huxuba, ya bayar da fatawa matuqar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* na ga wuri, sai Abubakar. Kuma babu abin da ya tava shige wa mutane duhu a addininsu sai Abubakar ya warware masu matsalarsa. Ga 'yan misalai a gurguje:

- Sahabbai sun shiga ruxani a kan rasuwar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*, ya rasu ko bai rasu ba. Abubakar ne ya ba su tabbacin rasuwarsa.
- Sun kuma shiga ruxani a kan inda ya kamata a rufe shi. Abubakar ne ya bayyana masu inda za a rufe shi; a xakin Aishah *Raliyallahu Anha* bisa qwaqqwaran dalili.
- Haka kuma sun shiga ruxani a kan halaccin yaqar waxanda suka hana zakka, Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya bayyana masu halaccin yi haka.
- Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya bayyana masu ma'anar ayar da ke cewa: *Lalle za ku shiga masallacin harami, in Allah ya so kuma masu natsuwa. Suratul Fathi: 127* a lokacin da ba su gane ta ba.
- Sannan ya bayyana masu manufar maganar *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* da ya ce: "Allah ya bai wa wani bawansa zavi tsakanin duniya da lahira".
- Shi ne kuma ya fassara masu abin da kalmar "kalalatu" ke nufi a cikin Alqur'ani.

Da wasu abubuwa masu dama ban da waxannan. Kuma a duk lokacin da Abubakar ya yi wa Sahabbai irin wannan qarin haske, babu mai musanta masa daga cikinsu.

Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* kansa, ya kasance yana riwaya daga Abubakar xin kamar yadda wasu daga cikin Sahabbai suke yi. Ya zo a cikin littafai huxu na *Sunan* daga Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce: Na kasance a duk lokacin da na ji wani hadisi daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* Allah zai amfanar da ni da abin da ya so ya amfanar da ni, daga gare shi, amma a duk lokacin da wani ya ce min Manzon Allah ya ce: kaza. To, lalle ne in nemi ya rantse kafin in yarda da shi. To, Abubakar ya faxa min, ya kuma yi gaskiya. Abin da ya faxa mini shi ne, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Babu wani musulmi da zai aikata wani zunubi sa'annan ya yi alwala, ya yi sallah raka'a biyu, ya roqi gafarar Allah Ta'ala face Allah ya gafarta masa".

A taqaice dai, kan malaman Sunnah ya haxu a kan cewa, Abubakar shi ne ya fi kowa tarin ilimi bayan *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Ita kuwa cewar da ya yi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Aliyu ne mafi sanin hukunci a cikinku". Da cewarsa wai, sanin hukunci na lizimta zama mafi ilimi da addini. To, wannan hadisi bai tabbata daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba. Don ba shi da wani isnadi da ake iya kafa hujja da shi ta tsayu da qafafunta. Hadisin ma da Tirmidhi da Ahmad suka riwaito ta ingantaniyar hanya ya fi wannan qarfin isnadi, inda Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Wanda ya fi kowa sanin Halal da Haram daga cikinku shi ne: Mu'azu xan Jabalu.

Idan ma aka yi kyakkawan nazari za a tarar cewa, mu'azun *Raliyallahu Anhu* Sahabin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wa wannan sheda ta naqaltar sanin Halal da Haram, shi ya kamata a ce ya fi kowa iya hukunci daga cikin Sahabbai ba Aliyu ba. Domin kuwa sanin Halal da Haram shi ke sa iya hukunci. Qari a kan haka ma shi ne, ita waccan shedar da xan Shi'ar ya ce Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wa Ali *Raliyallahu Anhu*, babu wani daga cikin malamai fitattu da ya riwaito ta, ko da kuwa da isnadi mai rauni, balle ingantacce. Amma sanannen abu ce cewa, waxanda suka riwaito ta shaharrarun maqaryata ne.

Shi kuwa hadisin da 'yan Shi'ar kan kafa hujja da shi mai cewa: Wai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Ni ne birnin ilimi, Aliyu kuma qofarsa". Ba ya da tushe, tattare kuwa da kasancewar Tirmidhi ya riwaito shi. Ibnul Jauzi ma ya ambace shi a cikin littafensa. Ya bayyana zamansa qarya ta duk hanyoyin aka riwaito shi. Ya kuma qara da cewa, ba ma sai an tafi nesa ba. Ana iya tabbatar da haka, ta hanyar duba gangar jikin hadisin. Domin idan aka ce Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne birnin ilimi, kuma qofarsa qwara xaya ce tal, hakan za ta rosa addini. Saboda haka kan musulmi ya haxu a kan cewa ba zai yiwu ilimin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya zo ma al'umma ta hannun mutum xaya ba. Dole ne ya zo ta hanyar taron jama'a waxanda abin da suka faxa ke iya zama ilimin ga ko da na nesa balle na kusa.

Da 'yan Shi'ah za su ce mana, idan aka samu mutum xaya "ma'asumi" dole ne a karvi maganarsa. Sai mu ce masu, to, batun tabbatar da

ma'asumancin nasa fa? Shi xin ne da kansa zai ba mu tabbacin ma'asumi ne? Wannan matsala ba a kai qarshenta. Don kuwa, ba ku iya tabbatar da cewa, wani imami ma'asumi ne sai ta maganarsa. Maganarsa kuma ana amsar ta ne don yana ma'asumi. To, ya kenan?

A qarshe kuma ko da ta tabbata cewa, birnin ilimi, ba ya da wata qofa sai Ali kawai, to, hakan ba ta tabbatar da zamansa ma'asumi, balle ta tabbatar da ingancin wani abu da zai faxi a kan addini, ta yadda ba za'a iya qalubalantarsa da hujja ba.

A haka dai ta tabbata cewa, wani babban zindiqi ne jahili ya qirqira shi, don zaton haka da ya yi na iya zama yabo ga Ali *Raliyallahu Anhu*. Dama kuma ta irin wannan hanya ce zindiqai ke sukar lamirin addinin musulunci a kaikaice. Don ai ka ga mutum xaya ne ya bayar da wannan hadisi.

Bari ma ta zancen komai in ka so, karon da wannan hadisi ya yi da tarihi, ya isa tabbatar da zamansa qarya. Domin ai babu wani birni a duniyar musulunci wanda ilimin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai kai gare shi ba. Ba kuwa Aliyu ne ya kai shi duk biranen ba *Raliyallahu Anhu*.

### 6.3.2 Xan Shi'ah ya yi Hujja da wannan Aya:

﴿ لِنَجْعَلَهَا لَكُمْ تَذْكِرَةً وَتَعِيَهَآ أُذُنٌ وَٰعِيَةٌ ﴿١٢﴾ ﴾ الحاقة: ١٢

Xan Shi'ar ya ce: Kuma saboda Ali *Raliyallahu Anhu* ne ayar da ke cewa: *Don mu sanya maku ita ta zamo faxakarwa. Kuma wani kunne mai kiyayewa ya kiyaye ta (60:12)* ta sauka.

Martaninmu a nan shi ne: Wannan magana qarya ce bisa haxuwar malamai. Abin da gaba da bayan ayar ke tabbatarwa shi ne, Allah *Subhanahu Wa Ta'ala* ba ya nufin wani kevantaccen kunne na wani kevantaccen mutum da wannan aiki na kiyayewa. Duk wani kunne ko na kowa ne, yana cikin wannan manufa matuqar dai yana iya kiyaye wa'azin Ubangiji.

### 6.4 Kaifin Basirar Ali

Xan Shi'ar ya ce: kuma Ali *Raliyallahu Anhu* ya kasance mai kaifin basira da tsananin kwaxayin neman ilimi. Ya kuma yi tarayya da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a matsayinsa na mafi kamala a cikin mutane, ta yadda dare da rana ba su raba su. Wannan kuma tun lokacin da Aliyu yake yaro kowane har lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rasu.

Martaninmu a nan shi ne: Ta wace hanya 'yan Shi'ah suka sami labarin cewa Ali *Raliyallahu Anhu* ya fi Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* kaifin basira da kwaxayin neman ilimi, da kasancewar abin da ya fa'idanta da shi daga wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fi nasu?

Abin da ya inganta daga Buhari da Muslimu shi ne, cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Haqiqa a cikin al'ummomin da suka

gabace ku akwai waxanda ake sanar da su. Da xaya zai kasance a cikin al'ummata to, Umar ne".

Ko shakka babu taren da Abubakar ya yi da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin musulunci ko rabinta Aliyu bai yi ba, kai babu ma wani mahaluki da ya yi irinta. Irin damar da Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* suka samu ta haxuwa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a kowane lokaci, Ali *Raliyallahu Anhu* bai same ta ba. Su ne mutanen da Annabi ke tattaunawa da su a kan duk wani abu da ya shafi musulmi. Kuma mafi yawan matsalolin da Umar da Ali suka qara wa juna ilimi a cikinsu, ijtihadin Umar ne kan cira tuta. Kamar matsalar wadda mijinta ya rasu ya bari da ciki.

**6.4.1 Malam Zurqe Bai ko San Hadisi ba**

Xan Shi'ar ya ce wai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Karatu a lokacin qurciya kamar zane ne a kan dutse. Wai saboda haka, inji xan Shi'ar, Ilimin Ali *Raliyallahu Anhu* ya fi na duk wanda ba shi ba, don ya yi shi tun yana da qurciya.

**Martani:**

Wannan magana na tabbatar da kasancewar xan Shi'ar nan riqaqqen jahili a fagen ilimin hadisi. Wannan zance da ya ce Annabi ya yi ba hadisi ne ba, don Annabi bai faxe shi ba. Salon magana ce kawai da ta yawaita a tsakanin musulmi.

Babban abin da ke tabbatar da haka, shi ne, Sahabban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na da haqoransu talatin talatin suka karanci rukunnan imani da Qur'ani, suka koyi sunnoni, duk a cikin taimakon Allah. Shi kuma sayyidina Ali kansa ko kafin Alqur'ani ya qare sauka, shekarunsa sun cika talatin cif. Ka ga kenan, sashen Alqur'ani ne ya hardace a quruciya. Sauran kuma da girmansa ne ya hardace su. Ballantana ma dai babu tabbas game da kasancewarsa ya hardace Alqur'ani dukkansa. Domin kan malamai bai haxu a kan haka ba.

To, ba Sahabbai ba ma, Annabawan Allah, waxanda su ne mafiya ilimi a cikin halittun Allah, babu wanda Allah ya aiko a cikinsu yana xan qasa da shekaru arba'in. Hana rantsuwa a wannan magana shi ne Annabi Isah. Kuma ka ga Abu Hurairata, duk da kasancewarsa dattijo, amma a cikin shekara ukku da 'yan watanni ya hardace ilimi mai yawa a makarantar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Haxuwar Abubakar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuwa ta fi ta sauran Sahabbai.

Sai cewar da xan Shi'ar ya yi, wai, daga wajen Ali mutane suka san karatu. Qarya ce. Don mutanen garinsa Kufa sun daxe da yin karatu mai zurfi ta hannun Ibnu Mas'ud da wasu malamai kafin Ali *Raliyallahu Anhu* ya saka qafarsa a birninsu.

In ko yana tunanin kafa hujja da cewa; Baban Abdurrahman As-Sulami daga wurin Ali ne ya xauki qira'a. Sai mu ce masa, bita ce kawai ya yi. Domin kafin zuwan sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* garin Kufa Baban Abdurrahman alaramma ne, mai riqaqqar harda.

### 6.4.2 Wai Ali ne ya Qaga Ilimin Nahawu!

Xan Shi'ar ya ce: Shi kuwa ilimin Nahawu Aliyu *Raliyallahu Anhu* ne ya shimfixa shi, don shi ne ya ce wa abul Aswad: Kowace irin magana ba ta wuce abu uku, da suka haxa da: Suna, da Aiki da Harafi. Daga nan kuma ya naqalta masa fannonan li'irabi.

**Martani:**

Abin da za mu ce a nan: Shi ilimin Nahawu ba ya cikin ilimin Annabta. Qago shi aka yi. Kuma wani salo ne na kare mutuncin qa'idojin harshe, da sauqaqe wa al'umma gane Alqur'ani. A zamanin halifofi uku na farko, ba a buqaci yin sa ba, don babu wanda ke dolge a harshen Larabci. Sai a lokacin da Ali *Raliyallahu Anhu* ya koma birnin Kufa da zama ne inda ajamawa su ke. Nan ne aka riwaito sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi waccan magana ga Abul Aswad.

Ka ga sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi wannan aiki saboda wata lalura, kamar yadda aka samu cewa, wasu a bayan wucewarsa, sun tsago salon rubuta baqaqe da xigagga da wasulla, da alamomin jan baqi da konkoma shi da makamantansu, duk a kan wata lalura. Bayan haka ne malamai a Kufa da Basra suka kyautata tace ilimin Nahu da faxaxa shi. Malam Khalil kuma daga bisani ya tsago ilimin Aruli.

To, ina abin da ke nuna Ali halifa ne a cikin wannan batu?

### 6.4.3 Fiqihun Ali

Xan Shi'ar ya ce: Ali shi ne madogarar malaman fiqihu a karatunsu.

**Martani:**

Wannan magana qarya ce kamar 'yan'uwanta da muka saba ji. Babu dai wani malami daga cikin malaman fiqihun Sunna guda huxu da aka sani ko wani ba su ba, wanda ke dogara ga Ali *Raliyallahu Anhu* a fiqihunsu.

## 6.5 Jaruntakar Ali ba Dalili Ce a Nan ba

Xan Shi'ar ya ce: Sayyidina Ali ya kasance mafi jarunta a cikin mutane. Da kaifin takobinsa ne kuma qa'idojin musulunci suka sami gindin zama, kuma rakunnan musulunci suka tsaya da qafafunsu. Ba a tava cin sa da yaqi ba, kuma bai tava bugun wani abu da takobinsa ba face ya gama da shi. Da yawa kuma Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* ya yaye baqin ciki daga fuskar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.* Wai kuma sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* bai tava gudu daga fagen fama ba kamar yadda wasunsu suka yi.

Shi ne kuma ya bai wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kariya ta hanyar kwantawa a kan shimfixarsa da yin lulluvi da bargonsa, a ranar da mushrikkai suka haxa kai a kan kashe shi. Da aka yi haka sai suka zaci wancan da ke kwance kuma a lulluve *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* ne, alhali kuwa Ali ne, sai suka yi dako-dako da makamai suna jiran alfijir ya keto su far masa, su yi masa bugun a kawo wuqa, jininsa ya tafi bakin banza, tunda banu Hashim ba za su iya yaqi da gaba xayan qabilun Larabawa ba, waxanda suka haxa guiwa, suka kashe shi. A haka, sai kowa ya tsira daga cikin qabilun. Wannan jaruntaka ta sayyidina Ali ce sanadiyyar kuvutar jinin Manzon Allah daga zuba a banza. A qarshe aka samu tsira, har gurin kira zuwa ga tafarkin Allah ya tabbata.

Da gari ya waye mushrikan suka yi azmar xaixaita shi, sai ya kai masu matsanancin farmaki. Ko da dai suka ga ashe Ali ne, sai kowanensu ya ranta cikin na kare; suka watse, mugun nufi da mummunar dabararsu, suka tsaya nan.

**Martani:**

Amsarmu ga wannan ita ce: Ko shakka babu sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* na xaya daga cikin jarumawan Sahabbai waxanda kuma qoqari da yajinsu ya taimaki musulunci. Yana kuma daga cikin ‘yan sahun gaba daga cikin Muhajiruna da Ansaru, haka kuma sahun magabata daga cikin waxanda suka yi imani da Allah da ranar qarshe ba ya cika sai da shi a ciki. Gaskiya ne Ali ya kashe adadi mai yawa na kafirai da takobinsa.

Amma duk da haka, Ali bai kevanta da waxannan siffofi ba. Akwai Sahabbai da dama da suke kafaxa-da-kafaxa da shi a wannan fage. Wannan ba ya sa ya zama mafi daraja a kan Sahabbai idan ana zancen jihadi balle a kan halifofi. Balle kuma hakan ya zama dalilin zamansa shugaba a kan kowa.

Idan muka xauki wannan magana tasa dalla–dalla; muka fara da cewar da ya yi: Ali shi ne mafi jaruntaka a cikin mutane, za mu ga hakan ba gaskiya ba ne. Tabbatattar magana, ita ce Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne jarumi na qarshe a cikin mutane. Kamar yadda Buhari da Muslimu suka riwaito daga Anas, wanda ya ce: *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kasance mutum mafi kyawo da inganci da jaruntaka a cikin mutane. Watarana firgita ta kama mutanen Madina, saboda wata qara da suk ji, sai suka tasar ma inda ta fito baki xaya. Kafin su kai, sai suka haxu da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yana tafe sukane a kan wani doki na Abu Xalhata da takobi rataye a wuyansa yana ce masu, kar ku ji tsoron komai. Buhari ya ce: Annabi ya je wurin da abin ya faru tun kafin su fito.

Ya kuma zo a cikin Musnad daga Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce: Mun kasance a duk lokacin da tsanani ya kai mana mashafar turare mukan lave ne a bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Shi ne wanda ya fi mu zama kusa da abokin gaba. To, ka ga wannan magana gaskiya ce. Amma a

cikin Sahabbai akwai waxanda suka kashe fiye da adadin da Annabi ya kashe na kafirai da hannunsa.

To, ko bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, Abubakar *Raliyallahu Anhu* ma ya fi Ali *Raliyallahu Anhu* jaruntaka. Domin shi ke take sawun Manzon Allah a wannan fage. Abubakar ne kuma ya ceto musulmi daga kiximewar da suka yi ranar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rasu. Wannan masifa ita ce fitina mafi girma da nauyi a wajen musulmi. Kaxan ne daga cikinsu wanda hankalinsa bai fita daga jikinsa ba, hantarsa ta kaxa, ya ruxe, ya kaxu kamar majaujawa saboda wannan gigita a kan rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Wasu daga cikinsu na yunqurin cewa, ai ba ta yiwuwa Manzon Allah ya rasu. A daidai lokacin, wasu jiki suka yanke, suka faxi zaune, wasu kuma sun ximauce; ba su san abin da ke kaiwa yana komowa ba. Wasu kuma sai kuka suke faman rusawa kamar dai watarana ce qarama daga cikin ranakkun Alqiyama suka wayi gari a cikinta.

Nan take sai Abubakar siddiqu ya zabura, zuciyarsa cike da kuzari da saxaukantaka, ba tsoro ba fargaba, fuskarsa na nuna haquri da yaqini, ya tabbatar masu da cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* dai ya riga mu gidan gaskiya. Allah ya zavar masa abin da ke can wurinsa. A nan ne ya saki shahararrar huxubar nan tasa, bakandamiya, wadda a cikinta yake cewa: “Ya ku mutane! Duk wanda ke bautar Muhammadu to, ya sani Muhammadu kam ya kwanta dama. Wanda kuwa Allah ne yake bauta wa to, ya sani Allah rayayye ne, kuma babu ranar da zai mutu”.

Jaruntakar duk da ake buqata ga wanda ya kamata a ce shi ne shugaba bayan *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* ta tabbata ga Abubakar. Sannan Umar ne zai biyo bayansa.

Idan kuma muka koma ga zancen adadin kafiran da Ali ya kashe. Za mu tarar cewa, a tarihin yaqoqan musulunci an samu Sahabban da suka kashe fiye da abin da Ali *Raliyallahu Anhu* ya kashe daga cikin kafirai. Idan kuwa yawan adadin abin da mutum ya kashe na kafirai ne ke tabbatar da fifikonsa a jaruntaka. Kenan waxancan Sahabbai sun yi wa Ali *Raliyallahu Anhu* fintinkau a wannan fage.

Xauki misalin Bara’u xan Malik, xan’uwan Anas, wanda ya kashe qato xari ta hanyar gani-ga-ka. Wannan ban da waxanda ya kashe a cikin sahu, ko waxanda yake da hannu a cikin kashe su. To, qarewa da qarau ma shi Khalidu xan Walidu sanin adadin kafiran da ya aika lahira sai masanin gaibi, shi ne, Allah, amma dai ba mutum ba. Kansakalin takobi tara ne suka karye a hannunsa wajen yaqin Mu’uta kawai. ko shakka babu Khalidu ya kashe ninkin ba ninkin abin da Aliyu ya kashe a fagen fama.

Sai kuma cewar da ya yi a qarqashin inuwar kaifin takobin Ali ne ginshiqan musulunci suka sami zama da gindinsu, rukunansa suka tsaya a kan qafafunsu. Wannan qarya ce bayyananna ga duk wanda ya san tarihin musulunci. Amma dai babu mai musun cewa, lalle takobin Ali ya taka muhimmiyar rawa a cikin rawar da takubban wasu Sahabbai da dama suka taka

wajen sama wa musulunici mazauni a bisa doron qasa. Akwai kuma waxansu nasarori da musulunci ya samu waxanda takobin na Aliyu *Raliyallahu Anhu* ba ya da wani dogon tasiri a ciki. Kuma waxannan nasarori a tarihin musulunci su ne mafi yawa, kamar dai yaqin Badar. Takobin Ali *Raliyallahu Anhu* xaya ne kawai daga cikin takubba masu xinbin yawa da aka yi yaqin da su.

Cewar kuma da xan Shi'ar ya yi, ba a tava nasara a kan Ali a wurin yaqi ba. Ba abin tinqaho da kafa hujja ne ga manufarsa ba. Domin kuwa tarihi ya tabbatar da cewa ba a tava nasara a kan Abubakar da Umar da Xalhatu da Zubairu da wasunsu da dama daga cikin Sahabbai ba. Duk maganar guda ce. Idan kuma ma dai har an tava nasara a kansu, tarihi bai faxa ba. Kamar yadda yake yiwuwa ya kasance an tava nasara a kan Alin, amma tarihi bai gano ba balle ya tsegunta wa duniya.

Muna da yaqinin cewa, waxancan Sahabbai ba su tava cin qasa a fagen fama ba. Don ko a yaqoqa biyu waxanda musulmi suka haxu da jarabawa a cikinsu, wato yaqin Uhudu da na Hunainu, ba a yi nasara a kan waxannan Sahabbai ba. Abin da littafan tarihin yaqe-yaqe suka ambata, shi ne Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* na tare da Annabi cirje, cirjiyar matashin zaki, har mazaje suka gama cin qasa su kan suna sama. Duk kuwa wanda ya ce an kayar da su a wannan rana, to, ya yi qarya. Amma Usmanu *Raliyallahu Anhu* ya bi sahun sauran waxanda Allah ya ce, ya gafarta masu don sun ja da baya.

Amma cewar da xan Shi'ar yayi Ali *Raliyallahu Anhu* bai tava bugun wani abu da takobinsa ba face ya gama da shi. Ba mu da masaniya akan ingancin wannan magana ko rashin ingancinta. Babu wata riwaya ingantatta a hannunmu da za mu iya rosa wannan da ita. Amma da za'a sami wani ya ce Khalidu ne da Zubairu da Bara'u xan Malik da Abu Dujanata da Abu Xalhata da makamantansu waxanda ba su tava bugun wani abu da takobinsu ba face sun gama da shi, ka ga an yi kunnen doki kenan. Musamman da yake kasancewar irin su Khalidu xin, da shi Bara'u mafi shahara da wannan irin jaruntaka kamar yadda masana tarihi za su iya faxa. Don kuwa har an riwaito cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Khalidu wani takobi ne daga cikin takubban Allah, wanda Allah ya zare a kan mushrikai.

Babu wanda zai ji wani qaiqayi ko ya yi wani kokwanto, idan aka ce, wanda Manzon Allah ya siffanta da kasancewa takobin Allah, ba ya saran abu face ya gama da shi. Aka kuma taras da cewa Khalidun nan ya kashe kafirai ba adadi a fagen fama. Kuma har ya koma ga Allah bai tava gudu daga wurin yaqi ba. Wannan magana ta fi qanshin gaskiya, da an jingina ta gare shi.

Xan Shi'ar kuma ya ce wai, da yawa Ali *Raliyallahu Anhu* ya yaye wasu baqqan ciki daga fuskar Manzon Allah. Sai mu ce, ko dai *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* ke yaye baqqan ciki daga reshi, shi da sauran Sahabbai. Ai ko Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* ba wanda aka riwaito ya tava yaye wani baqin ciki daga fuskar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* su ma da ko Antaru ya san da su a fagen fama.

Amma ya tabbata a tarihi cewa, watarana Mushrikan Makka sun yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* qofar rago da nufin su kashe shi, sai Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya daka masu tsawa yana cewa: Ya za ku kashe mutum don kawai ya ce: "Allah ne Ubangijina"? A sanadiyyar haka suka yi wa Abubakar duka matsananci. Amma ba a riwaito cewa Ali *Raliyallahu Anhu* ya bai wa Manzon Allah irin wannan kariya ba.

Shi kuwa kafa hujja da xan Shi'ar ya yi da kwanciyar da Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi a kan shimfixar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a madadinsa, mun faxi cewa, Ali na da yaqinin ba abin da zai same shi. Don Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ba shi tabbacin haka.

**6.5.1 Ba Don Ali ne Kawai Aka ci Badar ba!**

Xan Shi'ar ya ce: a wajen yaqin Badar, yaqi na farko a tarihin musulunci, wanda aka yi shi a farkon wata na goma sha takwas bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya isa Madina. A lokacin Ali *Raliyallahu Anhu* na xan shekaru ashirin da bakwai, ya kashe mutum talatin da shidda shi kaxai ransa. Adadin da ya fi rabin abin da aka kashe a wurin yaqin na kafirai. Yana kuma da hannu a cikin kashe sauran adadin.

**Martani:**

Ko shakka babu Ali ya yi bajinta a ranar Uhudu. Amma wannan magana ta xan Shi'a akwai qarin gishiri a cikinta. Kuma babu wani daga cikin malaman da ake iya dogara da riwayarsu wanda ya anbace shi. Jahillai ne kawai maqaryata suka kitsa ta.

Iyakar abin da masana suka ce shi ne, mutum goma sha xaya ne kawai aka tabbatar da Ali *Raliyallahu Anhu* ya kashe shi kaxai ransa, a wannan rana. Akwai kuma mutum shida da ake jin ba shi ne ya kashe su ba. Sannan akwai wasu mutane uku da ake da tabbacin Ali *Raliyallahu Anhu* yana da hannu a cikin kisansu su ma, a ranar. Wannan shi ne abin da malamai masu gaskiya irin Ibnu Hisham, da Musa xan Uqbata da Amawi suka ambata.

To, in ya yi wannan sai dole ne ya zamo halifan farko?

**6.5.2 Kuma Wai a Hannunsa ne Aka ci Nasara a Uhudu**

Xan Shi'ar ya ce: Gaba xayan mutane sun dare wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a ranar yaqin Uhudu in banda Ali. Sai fa wasu 'yan tsiraru da suka dawo masa daga bisani, irinsu: Asimu xan Sabitu da Abu Dujanata da Sahalu xan Hunaifu. Sai kwana uku ne Usmanu xan Affana ya iso wurin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama.* Sai Annabin ya ce masa: Ai alqalami ya riga ya bushe. Kuma Malaiku sun cika da mamakim Ali a wannan rana. Ga ma abin da Jibrilu ke cewa a lokacin da yake komawa zuwa sama: "Lallai ba takobin qwarai bayan *Dhul Fiqar* (takobin Ali), Babu wani namiji kuma yau sai Ali".

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Mafi yawan mushrikan da aka kashe a wannan yaqi, Ali *Raliyallahu Anhu* ne ya kashe su. Kuma nasarar da aka samu, a hannunsa ne aka same ta.

Kuma wai Qaisu xan Sa'ad ya ce: Na ji Aliyu *Raliyallahu Anhu* na cewa: An kai mani bugu sau goma sha shida a ranar yaqin Uhudu. Huxu daga cikinsu suka kai ni qasa. Sai wani mutum mai kyakkyawar fuska da kyakkyawar kama, ya zo mani da daddaxan qanshi, ya kama kafaxata ya tayar da ni. Sannan ya ce mani: Ka fuskance su, ka yaqe su a cikin xa'ar Allah da xa'ar Manzonsa, don suna cikin yarda da kai. Ali ya ce: Sai na zo na gaya wa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama,* shi kuma ya ce mani: Ya kai Ali! Baka gane wannan mutum ba? Na ce masa: Eh, ban gane shi ba. Amma dai ya yi mani kama da Dihyatul Kalbiyyu. Daga nan sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Allah ya sanyaya zuciyarka ya kai Ali. Ai wannan mutum Jibrilu ne.

**Martani:**

Akwai qaryace-qaryace a cikin waxannan maganganu da dama, irin waxanda babu mai yarda da su sai wanda bai san tarihin musulunci ba. Na kuma yi mamakin irin yadda xan Shi'ar ke ratato tatsuniya kamar yana magana da wanda bai san abin da ya gudana a tarihin yaqe-yaqen musulunci ba.

Babbar illar qarya ta haxu da jahilci. Ai ba musulmin da bai san cewa ba wata nasara da musulmi suka yi a wannan yaqi ba. Gaskiya ne musulmi sun sami nasara a karon farin a ranar. Domin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya umurci dakaru da su tsare mashigin dutsen da ake kira *Jabalur Rumati,* ya ce kuma kada wanda ya bar wurin ko da musulmi sun yi nasara ko an yi ta a kansu.

Samun nasarar musulmi a kan mushrikai ke da wuya, sai wasu daga cikin musulmi suka yi kururuwa: Ganima! Ganima!! Kwamandansu Abdullahi xan Jabir ya ce masu: Kada wanda ya kuskura ya tafi xibar ganima daga cikinku. Amma ina! Qaddara ta riga fata. Sai suka qi saurarensa. Gangarowarsu wurin ganimar ke da wuya sai mushrikai suka kewayo masu ta baya a qarqashin jagorancin Khalidu xan Walidu, kafin ya musulunta. Sai kuma suka ji kamar ana cewa: An kashe Muhammad! An kashe Muhammad!! Ashe Shexan ne ke wannan magana ba su sani ba. Nan take wuri ya ruxe.

Mutane ko suka ci tuwon kare, har ya kasance ba a bar kowa a tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba sai mutane goma sha biyu daga cikin Sahabbai, waxanda Abubakar da Umar na daga cikinsu.

Wannan rana ta kasance ranar jarabawa da fitina ga musulmi. Mushrikai suka kama hanyar komawa suna masu nasara a kan musulmi. Saboda daxi ya yi masu yawa ma sai da suka yi kamar su dawo su sake afka wa musulmi a cikin birnin Madina, amma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya sa musulmi suka hargage su.

Wani abin da kuma tarihi ya tabbatar shi ne: Aliyu da Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhum* babu xaya daga cikinsu da ya kasance yana kariyar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a ranar. Gaba xayansu suna arangama ne da arna. Amma ba su gudu ba. Kuma a wannan yaqin an ji wa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* rauni a goshinsa. Haka ma Sahabbai da dama. Amma lafiya lau Aliyu *Raliyallahu Anhu* ya fita.

Haka kuma cewar da xan Shi'ar ya yi wai Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce: An kai mani bugu sau goma sha shidda a ranar yaqin Uhudu, huxu daga cikinsu har sun kai ni qasa.., ita ma qarya ce yake yi wa Ali *Raliyallahu Anhu,* domin babu wani littafi daga cikin sanannun littafai a wurin ma'abuta ilimi da ya kawo wannan magana, ballantana a samu isnadinta, ko a inganta ta. Abin da ya inganta a wannan yaqi ta wannan fuska shi ne, an yi wa Manzon Allah da wasu da yawa daga cikin Sahabbai rauni. Amma Ali ba wanda ya ce an yi masa ko qwalzane.

Ga abin da malam xan ishaka ke cewa: A lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya isa bakin sansanin sai Ali xan Abu xalib ya fito ya tare shi da gugar ruwa da ya xebo daga marmaro. Ya kawo ma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* don ya sha. Sai ya ji wani wari a cikinsu. A maimakon ya sha, sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya wanke jinin da ke fuskarsa da shi, ya kuma zuba saura a fuskarsa yana cewa: "Fushin Allah ya tsananta ga waxanda suka fitar da jini daga fuskar Manzonsu".

Sai maganarsa ta cewa, wai, sayyidina Usman ya zo wurin *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* bayan kwana uku. Wannan ma qarya ce tuburan. Haka ma abin da ya hikaito Jibrilu na cewa, wai, a lokacin komawarsa zuwa sama bayan gama yaqin. Takobin ma da aka sani da sunan *Dhul Fiqar* ba na Ali ba ne. Takobin *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* ne da aka ribata daga Abu Jahali ranar Badar.

Daga cikin abin da ke qara tabbatar da qaryar wannan magana har da cewa, Imamut Tirmidhi ya riwaito daga Ibnu Abbas cewa, Manzo*n Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ribaci takobinsa *Dhul Fiqar* a wurin yaqin Badar, kuma da shi ne ya yi mafarkin abin da zai faru a ranar yaqin Uhudu.

Ibnu Abbas ya ci gaba da cewa: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Na yi mafarkin wata gusxewa a bakin takobin nan nawa *Dhul Fiqar*, sai na fassara ta da wata gusxewa da za ta faru a cikinku. Na kuma gane ni a cikin mafarkin bisa wani rago, sai na fassara shi da runduna. Haka kuma na gane ni a cikin wata ganuwa, sai na fassara ta da birnin Madina. Na kuma ga ana yanke wata saniya. Na kuma san wallahi saniyar alheri ce.

Xan Abbas ya cika da cewa, duk abubuwan nan da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya faxa babu wanda bai faru ba.

Wannan magana ta takobi mai suna *Dhul Fiqar*, xaya ce daga cikin qaryace-qaryacen da wasu jahilai suka kitsa kamar cewar da suka yi Ali *Raliyallahu Anhu* ya mallaki wani takobi wanda idan ya kai baza da shi, takobin zai qara tsawo zira'i kaza da kaza, amma malamai na haqiqa sun daxe

da sanin haka bata tava faruwa ba ga takobin Ali ko na waninsa. Da takobin Ali *Raliyallahu Anhu* na qara tsawo, da ko ya qara ranar yaqinsa da Mu'awiyah.

### 6.5.3 Ali a Yaqin Taron Dangi (Ahzab)

Xan Shi'ar ya ce: A ranar yaqin Ahzab, qare haqon kadarkon ke da wuya sai ga Quraishawa sun danno qarqashin jagorancin Abu Sufyana a cikin runduna ta mutum dubu goma, wadda ta haxa da qabilar Kinanata da mutanen Tihama. Sai kuma ga qabilar Gaxfanu da masu rufa mata baya daga cikin mutanen Najadu sun danno, suka yi sansani wa musulmi sama da qasa, kamar yadda Allah Ta'ala Ya ba mu labari: *A lokacin da suka zo muku daga samanku da kuma qasa daga gare ku (33:10)* sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fita tare da musulmi dubu uku, suka saka kadarkon a gabansu, a waje xaya kuma Mushrikan can suka haxa kai da Yahudawa suka qara yawa. Hakan ta sa suka qara qwari, musamman ganin irin yadda Yahudawa suka dafa masu.

Daga nan Amru xan Abdu Wuddin da Ikrimatu xan Abu Jahali suka hau dawa kansu suka bi ta wata kafa a cikin kadarkon, suka tasar ma musulmi. Suka kuwa ce masu: Kule! Suna qalubalantar musulmi, ko akwai mai cewa Cas?

Nan take Ali *Raliyallahu Anhu* ya zabura wai, ya ce: An ce, cas! Sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya hana shi. Ya ce masa: Ka fa san Amru ne. Sai da suka yi haka har sau uku. A na huxun sai Ali ya zabura ya yi cikinsa. Rashin arziqin Amru ya kai shi ga cewa: Kulenku! Wai sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wa Ali *Raliyallahu Anhu* izinin tafiya ya fuskanci Amru a wannan karon. Shi kuma Amru da ya ga Ali *Raliyallahu Anhu* ya fito sai ya ce masa: Koma ya kai xan'uwana. Ba na son in kashe ka! Shi kuwa Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce masa: Ka manta ka yi wa Allah alqawalin cewa babu lokacin da wani Baquraishe zai kira ka zuwa ga xayan biyu sai ka karva masa xaya?

Sai Ali ya kira shi zuwa musulunci. Amru ya karva masa da cewa: Ba ni da buqata ga wannan. Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce: To, ina kiranka zuwa filin fama. Ga-ni-ga-ka. Amru ya ce: Uhum! Ali, ba na son in kashe ka fa. Shi kuwa Ali *Raliyallahu Anhu* ya karva masa da cewa: To, ni ina son in kashe ka.

Daga nan sai Amru ya sauka daga kan dokinsa, inji xan Shi'ar, suka yi karon battar karfe da Ali *Raliyallahu Anhu.* Nan take Ali *Raliyallahu Anhu* ya aika shi lahira. Sai kawai ka ga Ikrimatu ya juya, ya ranta cikin na kare. Sauran Mushrikai da Yahudawa duk suka ce qafa me na ci ban ba ki ba?

Wai kuma kan haka ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Abin da Ali ya yi wa Amru xan Abdu wuddin ya fi ibadar mutane da aljannu baki xaya.

**Martani:**

Kamar kullun, muna son malam zurqe ya gaya mana isnadin wannan labari, tare da kuma bayyana mana wanda ya inganta shi, in har akwai.

Daga cikin abin da ke tabbatar da kasancewar wannan labari nasa qarya, har da cewar da ya yi, wai Quraishawan da suka zo wannan yaqi da mutanen Kinanata da Tihama sun kai mutane dubu goma, waxanda suka haxa da Quraishawa da Kinanawa da mutanen Tihamata. Wannan itace qarya ta farko a cikin labarin. Domin kuwa abin da tarihi ya tabbatar na adadin dukkan qabilu, da suka haxa da waxancan mutanen da ya ambata, da mutanen Najadu wato Tamimawa da Asadawa da Gaxafanawa, da kuma Jama'ar Yahudawa, dududu adadinsu bai kai dubu goma ba. Kuma su qabilun nan qungiya uku ne da suka haxa da: Quraishawa da 'yan korensu, wato mutanen garin Makka da maqwabtanta. Sai kuma mutanen Najadu wato Tamimawa da Asadawa da Gaxafanawa da waxanda suka bi su don su sha miya. Qungiya ta uku kuwa ita ce Yahudawan banu Quraizata.

Bayan wannan qarya kuma, sai cewar da marubucin ya yi wai Amru xan Abdi wuddin da Ikramata xan Abu Jahali, sun hau dawa kansu suka fita ta wata kafa suka faxa cikin kadarkon. Bayan kuma wai sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi layya da Amru sai sauran mushrikan da Yahudawan suka watse nan take.

Wannan magana qarya ce da ximinta. Musulmi sun ci gaba da tsare mushrikai da Yahudawa bayan wannan lokaci. Har zuwa lokacin da Nu’aimu xan Mas'udu ya shigar da wata yaudara tsakaninsu, kuma Allah *Subhanahu WaTa’ala* Ya aika masu da iska mai tsananin gaske da Mala'iku daga sama, kamar yadda Allah Ta’ala ya ba mu labari in ya ce:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱذۡكُرُواْ نِعۡمَةَ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ إِذۡ جَآءَتۡكُمۡ جُنُودٞ فَأَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِمۡ رِيحٗا وَجُنُودٗا لَّمۡ
تَرَوۡهَاۚ وَكَانَ ٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرًا ٩ إِذۡ جَآءُوكُم مِّن فَوۡقِكُمۡ وَمِنۡ أَسۡفَلَ مِنكُمۡ وَإِذۡ
زَاغَتِ ٱلۡأَبۡصَٰرُ وَبَلَغَتِ ٱلۡقُلُوبُ ٱلۡحَنَاجِرَ وَتَظُنُّونَ بِٱللَّهِ ٱلظُّنُونَا۠ ١٠ هُنَالِكَ ٱبۡتُلِيَ
ٱلۡمُؤۡمِنُونَ وَزُلۡزِلُواْ زِلۡزَالٗا شَدِيدٗا ١١ وَإِذۡ يَقُولُ ٱلۡمُنَٰفِقُونَ وَٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٞ مَّا وَعَدَنَا ٱللَّهُ
وَرَسُولُهُۥٓ إِلَّا غُرُورٗا ١٢ ﴾ الأحزاب: ٩ - ١٢

*Ya ku waxanda suka yi Imani! Ku tuna ni'imar Allah a kanku a lokacin da waxansu rundunoni suka zo muku, sai muka aika wata iska a kansu, da waxansu rundunoni waxanda ba ku gani ba kuma Allah Ya kasance mai gani ga abin da kuke aikatarwa.*

*A lokacin da suka zo muku daga samanku da kuma qasa gare ku, kuma a lokacin da gannai suka karkata, kuma zukata suka kai ga maqosai, kuma kuka yi wa Allah ‘yan zace – zace. A*

*can ne aka jarrabi muminai, kuma aka girgiza su, girgiza mai tsanani.*

*Kuma a lokacin da Munafikai da waxanda akwai cuta a cikin zukatansu ke cewa "Allah da Manzonsa ba suyi mana alqawarin kome ba, sai ruxi (3379-12)*

Har zuwa inda Allah Subhanahu WaTa'ala ke cewa:

*Kuma Allah ya isar wa muminai daga yaqi (33:05).*

Waxannan ayoyi na Alqur'ani da abin da ma'abuta ilimin hadisi da tafsiri suka tabbatar da kansacewarsa ta dubban hanyoyi lafiyayyu, a cikin littafan tarihi shi ne muminai ba su yi yaqi a wannan rana da kowa ba. Ba kuma ta hanyar yaqi ce Allah ya tunkuxe musulmi maqiya ba.

To, yaya da rana tsaka, wani zai zo ya gaya mana cewa, wai layyar da Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi da Amru ce ta sa Mushrikai suka watse suna tavavvu.

Qarya ta gaba da wannan malam Zurqe ya yi a wannan hadisi ita ce: Cewar da ya yi wai, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Kashe Amru da Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi, ya fi ibadar mutane da aljannu baki xaya. Wannan tatsuniya ce. Kuma Allah ya tsarkake littafan hadisi nagartattu daga hikaito irinta. Kai har a naxe qasa babu mahalukin da zai iya kawo maka isnadin wannan magana ko da mai rauni ne, balle ingantacce.

Saboda haka, ba ya halatta a jingini wa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* irin wannan zulala.Ba kuma zai yiwu don mutum ya kashe kafiri xaya kowane iri ne, ya fi ibadar da mutane da aljannu ke yi wa Allah falala ba.

### 6.5.4 Gudunmawar Ali a Yaqin Banun-Nadhir

Xan Shi'ar ya ce: Sayyidina Ali ne *Raliyallahu Anhu* ya kashe wanda ya harbi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ga haqoransa na gaba, ya kuma kashe wasu mushrikai goma bayansa, sauran kuma suka ruga aguje, a ranar da aka yaqi Banun-Nadhir.

### Martani

Muna nan akan bakarmu ta neman isnadi. Na farko kenan.

Na biyu: Wannan abu da ya faxa ba gaskiya ba ne. Malamai sun haxa a kan cewa, banun-Nadhir su ne waxanda Allah *Subhanahu WaTa'ala* ya saukar da Suratul Hashri a kansu. Banun-Nadhir kuwa qabila ce ta Yahudawa, waxanda labarinsu ya faru kafin yaqin Uhudu da na Taron Dangi. Babu kuma wani abu a cikin labarinsu da ke nuna cewa an kashe wani ko an jikkata. Babu kuma wanda ya riwaito koda hadisi xaya a lokacin cewa, an karya haqoran Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.* in da aka karya masa haqora shi ne, lokacin yaqin Uhudu.

Iyakar abin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da musulmi suka yi wa banun-Nadhir a wannan rana, tsare su da suka yi; tsarewa mai tsanani, suka

kuma sassare itatuwan dabinnansu. Amma ba wanda aka kashe, ko cikin musulmi ko cikin Yahudawa.

### 6.5.5 Malam Zurqe ya Sake Fesa ta

Xan Shi'ar ya ce: A wani yaqi da aka yi mai suna *Gazwatus-Silsilati* wani balaraben qauye ya zo wurin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya gaya masa cewa: Wata jama'a daga cikin Larabawa na can suna shirin su iske ka Madina don su gama da kai. Wai sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Wa zai xauki tuta ya jagoranci wannan yaqi? Sai Abubakar ya ce: Ni, ya Manzon Allah. Sai Manzon Allah ya ba shi tutar, ya kuma haxa shi da dakarunsa mutum xari bakwai. Yayin da suka isa wurin Larabawan sai suka ce wa Abubakar: Koma wurin mutuminka *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* ka gaya masa yawanmu ya fi qarfinku xin nan. Abubakar ya koma. Kashegari sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya sake cewa: Wa zai xauki tutata ya jagoranci wannan yaqi? Wai sai Umar ya ce: Ni, ya Manzon Allah. Manzon Allah ya danqa masa tutar. Abin da ya faru ga Abubakar shi ma ya faru ga reshi.

Sai a rana ta uku, Manzon Allah ya ce: Ina Aliyu? Ali ya karva masa: Ga ni, ya Manzon Allah. Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya danqa masa tutar. Shi kuwa ya tasar ma Larabawan. Haxuwarsu ke da wuya bayan sallar asuba Ali *Raliyallahu Anhu* ya aika shida ko bakwai daga cikinsu lahira, saura kuma suka watse suna sambatu. Kuma, inji xan Shi'ar haka ce ta sa Allah Ta'ala ya rantse da wannan aiki na Sarkin Musulmi Ali inda yake cewa:

﴿وَٱلْعَٰدِيَٰتِ ضَبْحًا ۝١﴾ العاديات: ١

*Ina rantsuwa da dawa kai masu gudu suna fitar da kukan ciki (99:1).*

**Martani:**

Idan wannan malami ya haxu da almaijrai, farkon abin da za su neme shi shi ne isnadi, don tabbatar da gaskiyar maganar in har akwai shi.

Idan kuwa ya faxa hannun malami, to zai tabbatar masa da cewa, gaba xayan abin da ya kawo na waxannan yaqe-yaqe, na daga cikin dangogin qarairayin da 'yan xariqu ke watsawa irin na tarihin Antaru da Baxxalu da ire-irensu. Duk da kasancewar tarihin waxannan mazaje taqaitacce ne, kuma cikin cokali, musamman dai shi Baxxalu. Abubuwan da suka faru gare shi a zamanin daular bani Umayyata, da yaqin da aka fafata da Rumawa duk bai fi a rubuta shi cikin xan qanqanin littafi ba.

Amma sai ga shi albarkacin ire-iren wannan marubucin, tarihin ya cika kundaye da dama. Haka abin yake a cikin qagaggun labaran Shaddadu da Dunafi da Zaibaqul Misri da makamantansu. Kamar yadda suka qaga wasu

tatsuniyoyi masu ban mamaki suka jingina su ga sarki Haruna Rashid da Abu Ja'afar Al-Mansur da sauran sarakuna.

Waxannan hikayoyi, na wannan yaqi da sauran tatsuniyoyi irin su idan aka xora su a ma’aunin hankali da ilimi ba in da za su je. Babu wani littafi na tarihin yaqe-yaqe ko tarihin rayuwar magabata sananne da ya ambaci wannan yaqi. Kamar yadda babu wani zaqaqurin malami a wannan fage da ya ambace shi, irin su Musa xan uqbata da Urwatu xan Zubairu da Imamuz Zuhuri da xan Ishaqa da makamantansu. Haka waqidi da Ibnu Sa’ad, da Yahayal Umawi da Walidu xan Muslim da Muhammadu xan A’izu da sauransu. Babu xaya daga cikin waxannan da ya ambaci wannan yaqi. Haka kuma babu wani hadisi da aka ambace shi a ciki. Ko wata aya da aka ce ta sauka a kansa.

A taqaice dai yaqe-yaqen da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi musamman waxanda aka yi taho mu gama da Mushrikai a cikinsu har aka rasa rayuka, sanannu ne, kuma shahararru a kunnuwan mutanen duniya. Malaman da suka san rayuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* fiye da yadda suka san ta uwayensu, sun tattara waxannan yaqe-yaqe sun adana. Kuma sun yi haka ne a kan kari. Ka ga kenan ba zai yiwu a ce Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* yayi irin wannan yaqi na a zo a gani ba tare da waxannan malamai sun ambace shi ba. Kamar yadda ba za ta yiwu a ce an farlanta wasu salloli bayan biyar da aka sani ba, ko an farlanta wani azumi bayan na ramalana, ko ace ai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tava yaqar mutanen Farisa, daga can ya wuce Yaman, amma kuma duk malamai basu riwaito haka ba. To, wannan shi ne misalin wannan yaqi. Da hankali da shari'a duk baza su yarda da akwai wani abu da aka yi biris da shi a cikin tarihi irin wannan ba.

### 6.5.6 Gudunmawar Ali a Yaqin Banul-Musxalaq

Xan Shi’ar ya ce: kuma Aliyu *Raliyallahu Anhu* ya kashe Malik da xansa daga cikin banil-Musxalaq, ya kuma kama da yawa daga cikinsu, waxanda suka haxa har da Juwairiyyatu ‘yar Harisu wadda Annabi ya zava wa kansa. Ana haka sai ga mahaifinta ya zo a wannan rana ya ce: Ya Manzon Allah! xiyata mai girman daraja ta fi qarfin bautarwa. Sai Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya umurce shi da ya ba ta zavi: Sai ya ce: Kai, amma dai Manzon Allah ka kyauta. Daga nan sai ya juya kan 'yar tasa ya ce, ya ke 'yata kada ki kunyata danginki. Ita kuwa ta karva masa da cewa: Ni dai na zavi Allah da Manzonsa.

**Martani:**

Kamar kullum, ba za mu daina ba, muna neman isnadi. Don wannan ita ce hanyar kunyata duk wani maqaryaci.

Na biyu: Da zarar masana tarihi sun kalli wannan magana za su tofa mata yawu, su wurga ta kwandon shara, saboda warin qarya da take yi. Wannan labari na xaya daga cikin irin labaran da ‘yan Shi’ah ke qagawa. Babu

wani malamin Sunnah da ya riwaito cewa Ali *Raliyallahu Anhu* ya aikata wannan abu a yaqin banil-Musxalaq. Ali a rannan bai kashe kowa ba. Ba kuma shi ne ya ribato Juwairiyya ba. Kuma asalatan mahaifinta bai tako qafa ba, balle har a ba ta wani zavi.

Amma in don yaqi da Banul-Musxalaq an yi shi, an kuma kama Juwairiyyatu cikin fursunonin yaqi, amma nan take ta nemi a yanka mata abin da zata biya don ta fanshi kanta. Aka yanka mata, sai kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya biya mata. Daga nan ta zama cikakkiyar 'ya. Ganin haka kuma sai gaba xayan mutane kowa ya 'yanta bawan da ke hannunsa albarkacinta. Suna masu cewa: Ba za ta yiwu mu bautar da surukan Manzon Allah ba.

### 6.5.7 Ali a Ranar Haibara

Xan Shi'ar ya ce: Albarkacin Sayyidina Ali ne aka ci birnin Haibara. Da farko, Abubakar aka fara ba tutar jagorancin yaqin, sai ya kasa tavuka komai. Sannan aka ba Umar, shi ma ya kasa tavuka komai. Daga qarshe aka danqa ta ga Sarkin Musulmi Ali, ya fita ya yi yaqi mai tsanani, ya kashe na kashewa. Sauran suka nakkasa, sai kuka. Ya kuma yi wannan abin al'ajabi ne jim kaxan bayan *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi masa addu'a a idonsa mai ciwo ya warke.

Bayan wannan nasara da Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi wai, sai mutanen Haibara suka rufe masa qofar birni. Nan take Sarkin Musulmi ya valle qofar shi kaxai ransa. Ya kuma shimfixa ta a matsayin gada akan kadarkon can. Alhali kuwa qato ashirin ne ke rufe qofar da buxe ta. Ta haka, sai musulmi suka sami dannowa suka shiga birnin, suka kwashe ganimarsa. Wai kuma bayan haka ne Ali *Raliyallahu Anhu* yake cewa: "Wallahi ba don qarfin Allah ba, mutum xari biyar ba za su iya valle kofar ba".

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: "Haka kuma ta hanyar sayyidina Ali ne aka sami nasarar cin garin Makka.

### Martani:

Allah ya la'anci maqaryata. Wa ya kawo labarin daga cikin malaman tarihi ko hadisi? Ina kuma isnadinsa da ingancinsa? Ko shakka babu wannan qarya ce zalla. Domin kuwa tarihi ya tabbatar da cewa ba rana xaya musulmi suka ci birnin Haibara da yaqi ba. Garin tunga-tunga ne. Haka aka rinqa cin su da yaqi guda-guda. Wasu kuma suka miqa wuya salun-alun. A qarshe kuma suka karya alqawarin da suka yi sulhu da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a kai.

Kuma Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* ba su yi qasa a guiwa ba a waxannan yaqe-yaqe. Sai dai cewa Aliyu *Raliyallahu Anhu* ya valle qofar birni, yana iya zama gaskiya, don an riwaito hakan. Amma ba a riwaito cewa, ya shimfixa ta a kan kadarko a matsayin gada ba.

Amma ko shakka babu cewar da xan Shi'ar ya yi wai albarkacin qwazon Ali *Raliyallahu Anhu* aka ci garin Makka da yaqi, qarya ce. Rawar da Ali *Raliyallahu Anhu* ya taka a cikin wannan yaqi, ba ta fi wadda sauran Sahabbai suka taka armashi ba. Shahararrun hadisan da suka yi magana a kan wannan yaqi na cin garin Makka sun tabbatar da haka. Kamar yadda suka tabbatar da cewa, sayyidina Ali ya yi qudurin kashe wasu surukai biyu na yayarsa Ummu Hani'i waxanda ta ba mafaka. Amma hakan ta faskara, saboda ta yi gaggawar kai qararsa ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* wanda ya sa hannu a kan mafakar da ta ba su. Kuma sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi niyyar auren 'yar Abu Jahali *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fusata har ya yi magana a kan wannan, sai Ali ya janye wannan zancen.

### 6.5.8 Ali a Yaqin Hunainu

Xan Shi'ar ya ce: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fita a ranar yaqin Hunainu tare da musulmi dubu goma. Wai sai Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya yi masu mugun baki, ya ce: Ba za a iya yin nasara a kan mu ba yau saboda yawanmu. Sai ga shi an yi nasara a kansu. Babu wanda ya rage tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai mutane tara daga cikin banu Hashim. Sai kuwa xan Umar Aiman. Shi kuma Sarkin Musulmi yana gabansa yana fama da takobinsa har ya kashe mutum arba'in. Ya kuma karya lagonsu.

Martaninmu a nan, bayan buqatar da muke da ita ta marubucin ya bayyana mana inda ya ji wai Abubakar ya yi wa musulmi mugun baki. Don ko ba wanda ya faxi wannan mugun lafazi na qiren qarya daga cikin littafan tarihin yaqe-yaqe ko na rayuwar musulmi, ko na hadisi ko tafsiri da makamantansu. Labarin da ya inganta game da wannan magana shi ne: Babu mai iya galaba a kanmu yau don ba rashim yawa. Kuma wasu ne daga cikin musulmi suka faxe shi ba Abubakar ba.

Haka kuma cewar da ya yi: Babu wanda ya rage tare da Manzon Allah daga cikin banu Hashim sai mutum tara, ita ma qarya ce. Kamar yadda kan malamai ma'abuta ilimin hadisi da tarihin yaqe-yaqe ya haxu a kan kasancewar Ali *Raliyallahu Anhu* ya kasance gaban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yana fama da takobinsa har ya aika mutum arba'in lahira, qarya ce.

## 6.6 Kuma Wai, Ali ya San Gaibi

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta biyar ita ce hasashe-hasashen da Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi a kan waxansu abubuwa kafin su faru. Kamar hasashen da ya yi na cewa, Xalhatu da Zubairu ba suna nufin tafiya aikin umarah ne ba, a lokacin da suka nemi yin haka daga gare shi. A inda ya ce masu: Wallahi ni, ina hasashen ba kuna nufin tafiya umara ba ne, kuna dai so ku yi amfani da wannan dama ne, ku tafi varna. Haka kuma ta kasance.

Watarana kuma yana zaune a wani wuri da ake kira Zi-Qarnin yana karvar mubaya'a, sai ya gaya wa jama'ar da ke nan cewa, wasu mutane dubu xaya ba daxi ba ragi za su zo maku, daga garin Kufa don yin mubaya'a gare ni a kan mutuwa. Haka kuwa ta faru. Kuma qarshen wanda ya zo daga cikinsu shi ne Uwaisul-Qarni. Haka kuma ya bayar da labarin za a kashe Zus-Sudayyah, kuma ta faru.

Kuma wai, wani ya bayar da labarin cewa, wasu mutane za su qetaro, a cikin labarin yaqin Naharawan. Ali ya ce: Ba za su qetaro ba. Wani kuma ya sake bayar da irin wannan labari. Ya sake cewa: ba za su qetaro ba. Kuma wallahi idan suka qetaro kwanansu ya qare. Haka kuwa aka yi. Kamar kuma yadda ya bayar da labarin shi kansa za a kashe shi, kuma hakan ta faru.

Haka kuma Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* wai ya gaya wa wani mutum da ake kira Shaharbanu cewa, wani la'ananne zai yanke qafafunsa da hannayensa ya kuma rataye shi. Sai ga shi kuma Mu'awiyah ya yi masa wannan aika-aika. Ya kuma labarta wa Misamu at-Tammaru cewa shi ne mutum na goma da za a rataye a lokaci xaya, a qofar gidan Amru xan Huraisu, ya kuma nuna masa wani guntun kututture na shi, da itaciyar dabino da za a rataye shi a kanta. Haka kuwa aka yi. Ya kuma gaya wa Rushaidu al-Hajri cewa, za a datse hannayensa da qafafuwansa da harshensa, a kuma rataye shi. Ta faru. Ya kuma labarta wa Kumailu xan Ziyad cewa Hajjaju ne zai kashe shi, ya kuma yanka Qambar. Sai kuma ga shi hakan ta kasance. Haka kuma ya faxa wa Bara'u xan Azibu cewa, za a kashe Hasan, xansa shi Ali, ba kuma za ka taimake shi ba. Ya kuma gaya masa inda kisan zai afku. Haka kuma ta faru; ba daxi ba qari.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa, kuma wai Ali *Raliyallahu Anhu* ya bayar da labarin mulkin Banul Abbas, da kuma cewa Turkawa za su karve mulkin daga hannunsu. Ya qara da cewa: Mulkin Abbasiyyawa mulki ne mai sauqi da babu tsanani a cikinsa, ta yadda da Turkawa da Dilamawa da Indiyawa da Barbar da Xailasana sun taru ba za su iya karve shi ba. Amma haka za ta faru ne a lokacin da aka wayi gari sugabanni da barori daga cikinsu sun saki hanya, suka kama gabansu. Da zarar haka ta faru sai Allah Ya ba wani sarki na turkawa galaba a kansu. Wanda zai faro daga inda mulkinsu ya fara, yana tafe yana cin qasashensu xaya bayan xaya. Babu wata tuta da za a xaga sama don a yaqe shi face ya kave ta. Duk kuwa wanda ya sha gabansa kashinsa ya bushe. Haka zai ci gaba da tafiya har ya yi galaba a kansu har qarshe ya danqa kambun nasararsa a hannun wani mutum daga cikin zuri'ata, wanda ke faxin gaskiya yana kuma aiki da ita.

Xan Shi'ar ya kammala da cewa: haka kuwa aka yi. Don ana nan sai ga Hulaku ya bayyana daga wajen Khurasana daidai inda mulkin Abbasiyawa ya fara, har Abu Muslim al-Khurasani ya yi masu mubaya'a.

**Martani:**

Ko shakka babu, babu wanda ya fi Ali *Raliyallahu Anhu* cancanta da yin hasashe a kan wani abu da bai faru ba. Kai girman darajarsa ma ya wuce nan. Kai an samu ma daga cikin mabiyan Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* wanda ke iya hasashen fiye da haka ninkin ba-ninkin, balle Ali. Amma kuma hakan ba ta sa suka kasance daga cikin waxanda suka fi kowa cancantar sarauta ba. Kuma irin wannan baiwar ma gata nan ko a wannan zamani namu balle nasu.

A wancan zamani an samu cewa Huzaifatul-Yamani da Abu Hurairata da wasu daga cikin Sahabbai kanyi wa mutane ninkin waxannan hasashe-hasashe. Kuma har ma Abu Hurairata kan tuqe isnadinsu zuwa ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* irin abin da Huzaifata ya yi, da ya kawo isnadinsa.

Akwai littafan karamomin waliyyai da labaransu da dama da aka wallafa, kamar littafin *Zuhudu* na Imamu Ahmad, da *Hilyatul Auliya'*i na Asfahani, da *Sifatus-Safwati* na Ibnul Jauzi, da *Karamatul Auliya'i* na Khallal, da irinsa na Ibnu Abid Dunya, da na Lalaka'i. Duk a cikinsu akwai karamomin manyan waliyyai, cikinsu har da mabiyan Abubakar da Umar, kamar Ala'u xan Hadrami, gwamnan Abubakar da wasu da dama waxanda in ana maganar sayyidina Ali su sha'aninsu bai ma taka karya ya karya ba. To, ina wata hikima ga kafa hujja da irin waxannan karamomi akan cancantar shugabanci?

Kuma labaran nan da ya kawo babu wanda yake da isnadi bale mu yanke masa hukunci. Amma kuma daga cikinsu akwai waxanda muke da yaqinin ingancinsu, akwai kuma waxanda ba mu iya tabbatar da kasancewarsu gaskiya ko qarya.

Amma dai ita cewar da ya yi Ali ya yi hasashen za su danqa kanbun nasararsu ga wani mutum daga cikin zuri'arsa, qarya ce kawai ya yi wa Ali *Raliyallahu Anhu* wadda ya xauko ta daga na baya-baya cikin malamansu.

Haka kuma jin da waxansu Gulatu ke yi na cewa Ali *Raliyallahu Anhu* ya san duk abin da zai faru gobe da jibi, ba tare da wata iyakancewa ba, shi ma qarya ne. ko wani sashe na gaibi bai sani ba balle dukansa. Sanin gaibu sai Allah!

## 6.7 Ana Karva Addu'ar Ali

Xan Shi'ar ya ce hujja ta shida ita ce: Aliyu ya kasance abin qarva wa du'ai. Ya roqi Allah ya karve hankalin Busra xan Arxa'ata. Aka kuwa sa masa tavin hankali. Haka kuma ya roqi makanta ta sami Aizaru, ta kuma same shi xin. Ya kuma roqi kuturta ta kama Anas a lokacin da ya voye imaninsa, ta kuma same shi xin. Kamar yadda ya roqar wa Zaidu xan arqamu kuturta shi ma, ta kuma same shi.

**Martani:**

Marubucin ya sani akwai daga cikin Sahabbai wanda ya yi wa Ali *Raliyallahu Anhu* fintinqau a wannan fage. Haka kuma an samu daga cikin tabi'una masu irin wannan karamar. Za'a kuma ci gaba da samun irinsu matuqar akwai mumini a bisa doron qasa. Sa'adu xan Abi waqas bai tava roqon Allah ba face Allah ya karva. Ya zo a cikin Buhari cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ya roqa masa Allah da cewa: "Ya Allah ka datar da duk harbin da zai yi, ka kuma karvi duk du'ain da zai yi". Haka kuma ya zo a cikin Sahihu Muslim cewa Umar ya aika wani mutum zuwa Kufa don ya tambayo masa labarin Sa'ad, a lokacin yana gwamna. Sai ya taras cewa mutane na faxin magana mai kyau game da shi. Amma wannan mutum bai qare rangadi ba sai da ya kai ga wani mutum daga cikin Bani Absu. Da ya tambaye shi labarin Sa'ad, sai ya qarva masa da cewa: Ai ba ya fita yaqi, ba ya kuma kula da talakawa, ba ya rabo dai dai. Da Sa'ad ya ji haka sai ya roqi Allah da cewa: "Ya Allah, idan ka san abin da wannan ya faxi a kaina qarya ce, amma ya yi don mutane su gani su yabe shi. To, ya Allah ka tsawaita rayuwarsa, ka kuma tsananta talaucinsa ka kuma sa fitina ta yi masa zoba.

Sai ga shi wannan mutum tsufa ya ci shi har ga qashi, har idanunsa sun yi kwarmi. Yana biyar kuyangi yana bobowa a kan hanya, yana cewa: Allah ne ya jarabce ni da haka sanadiyar mugunyar addu'ar da Sa'ad ya yi a kaina.

Duk da rashin isnadin da waxannan qissoshi da xan Shi'ar ya jingina ga Ali, akwai abubuwan da babu kokwanto akan kasancewarsu qarya! Kamar mugunyar addu'ar da ya ce ya yi wa Anas da kuturta, da makanta da ya ce ya roqa ma Zaidu xan Arqam.

**6.8 Wata Hujjar Banza**

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: hujja ta bakwai ita ce: a lokacin da Ali *Raliyallahu Anhu* ya fuskanci siffin, sai qishirwa ta riski jama'arsa a kan hanya. Sai ya ce su xan ratse kaxan. Ratsewarsu ke da wuya sai suka hangi wani xan gidan bauta. Sai suka qwala ma wanda ke cikinsa kira, suka tambaye shi ko Allah ya sa yana da xan ruwa? Sai ya ce masu ina! Ai tsakanina da ruwa ya kai tafiyar kwana biyu ga mai tafiya qasa. Ba don da ya kasance ana kawo mani xan wanda zan tsotsa ba kowane wata, da qyar in ga qarshensa, ai da qishi ya kashe ni. Sai kawai Sarkin Musulmi ya nuna wani xan wuri kusa da cocin, ya ce a tona shi. Ana tonawa sai ga wani fandun getso, aka yi aka yi a xauke shi aka kasa. Nan take Ali *Raliyallahu Anhu* ya sa hannu shi kaxai ransa ya ije shi, sai ga ruwa. Suka sha suka yi tanqal.

Qarewarsu ke da wuya, inji xan Shi'ar, sai wannan malamin kiristan ya faxo, ya ce wa Ali *Raliyallahu Anhu*: Lallai na tabbata ko dai kai Annabi ne, ko kuma wani babban mala'iki a faxar Allah. Sai wai Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce masa: A'a, babu ko xaya. Illa dai ni ne wanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bar wa wasiccin halifancinsa in ya wuce. Nan take wai sai malamin ya musulunta a hannun Ali. Sai kuma ya ce, haqiqa wannan coci

daman an gina ta ne a kan sunan wanda zai valla wannan fardun getso, wanda kuma zai fitar da ruwan da ke qarqashinta. Kuma an yi malamai da dama a gabanina, amma ba su riske ka ba. Kuma a qarshe dai wannan malami ya yi shahada tare da shi Sayyidina Ali.

Sannan xan Shi'ar ya ce, Sayyid Al-Himyari ya waqe wannan labari na Ali.

**Martani:**

Wannan qissa ko shakka babu tana xaya daga cikin qarairayin da jahilai ke tsammanin su wani abu da ke bayyana darajar Ali *Raliyallahu Anhu*. Alhali kuwa ba haka abin yake ba. Hasali ma duk wanda ya qirqiri wannan qarya ya jahilci matsayin Ali *Raliyallahu Anhu* da darajojinsa, balle ya san irin abin da ya dace a jingina gare shi na yabo da gwarzantawa. Da ya sani da bai danganta xaukakar Ali *Raliyallahu Anhu* ga nuna fandun getso ba, da fitar da ruwa a qarqashinsa ba.

Irin wannan ba wani abin godogo ba ne, don ya sha samuwa ga wasu halittu da yawa, waxanda darajarsu ba ta kama ko qafar ta Ali *Raliyallahu Anhu* ba. Kamar yadda ta sha faruwa har ga wasu daga cikin masoya Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhum*. Fiye ma da irin wannan. To, babban abin mamaki ma da la'akari shi ne, da a ce faruwar irin waxannan gamdakatar ya taqaita ne ga sauran mutane, sai a ce wata ni'ima ta karama ce daga wurin Allah. To amma, sai ka taras hakan ta faru har a cikin waxanda ba salihai ba.

Shi kuwa sauran abin da ke cikin wannan qissa, kamar cewar da ya yi wai malamin ya ce: An gina wannan coci a kan sunan wanda zai tona fandun getso ya kuma fitar da ruwa a qarqashinsa. Wannan ba al'adar musulunci ce ba, balle Ali ya xaukaka da ita. Coci-coci ne da wuraren bautar Yahudawa da na masu bautar addinin kakanni ake ginawa a kan sunayen waxanda suka qaga su. Amma su musulmi ba su gina wuraren ibadarsu wato masallatai, waxanda Allah ya yi kira a xaukaka a kuma inganta don ambaton sunansa kawai a ciki, sai a kan sunan Allah. Ba dai a kan sunan wani abin halitta ba.

A qarshe kuma ita ma cewar da ya yi wai Ali *Raliyallahu Anhu* ya ce: Shi ne wanda Manzon Allah ya bari ya gaje halifarsa bayan ya wuce, qarya ce yake yi wa Ali. Domin kuwa ta tabbata Ali *Raliyallahu Anhu* bai tava furta wannan magana ba da xai; ko a zamanin halifofi uku kafinsa, ko a kwanukan yaqin siffin.

## 6.9 Wai Ali ya yi Yaqi da Aljannu!

Xan Shi'ar ya ce hujja ta takwas ita ce: Abin da malaman Sunnah suka riwaito cewa, a lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fita zuwa yaqin Banil-Musxalaqu, dare ya yi masu a kan hanya, a kusa da wani kwazazzabo mai zurfi. Kwaram, sai ga Jibrilu *Alaihis Salam* ya sauko ya gaya wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa, akwai wasu Aljanu da suke zaune a wannan kwazazzabo, kuma suna shirin cutar da shi da

Sahabbansa. Nan take sai Manzon Allah ya kira Aliyu ya yi masa addu'a ya kuma umurce shi da kutsawa cikin kwazazzabon, ya kuwa kutsa ciki, ya kashe Aljannun.

**Martani:**

Martaninmu a nan shi ne: Abu na farko dai, matsayin da Ali ke da ya fi qarfin wannan abu ya zama wani abin alfahari gare shi, ko da hakan ta tabbata. Domin kuwa an samu cewa wasu da ba su kai darajarsa ba ma sun yi irin wannan aiki. Amma kuma tattare da haka, wannan hadisi na xaya daga cikin hadisan qarya waxanda aka jingina ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Ali kamar yadda malamai masana hadisi suka tabbatar. Babu kuma wani abu mai kama da haka da ya faru a yaqin Banul-Musxalaq.

Kuma cewar marubucin wai malaman Sunnah ne suka riwaito wannan hadisi. Idan yana nufin cewa, an riwaito hadisin ne ta wani isnadi tabbatacce, ko a cikin wani littafi da ake iya dogara da kasancewar kawai ya riwaito abu, ko wani wanda aka yarda da shedunsa a kan hadisi ya inganta shi. To ba haka ba ne. Haka ma in yana nufin mafi rinjayen malamai sun riwaito shi. Duk wannan qarya ne. Amma idan yana nufin wani daga cikin waxanda hujja ba ta kafuwa da abin da suka riwaito, ya riwaito shi; to, babu wata fa'ida da hakan ke iya tabbatarwa.

**6.10 Rana ta Sake Hudowa Saboda Ali!**

Xan Shi'ar ya ce hujja ta tara ita ce: Sake hudowar da rana ta yi har sau biyu saboda buqatar Ali *Raliyallahu Anhu* ga hakan. Na farko a zamanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Na biyu kuma bayan rasuwarsa.

Xan Shi'ar ya ce: Na farko, ya faru ne kamar yadda Jabir da Abu Sa'id al-Khudri suka riwaito cewa, watarana Malaika Jibrilu ya sauka ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* don ya gana da shi a kan wani muhimmin batu daga wurin Allah. A lokacin da gahin wahayi ya buge Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai san lokacin da ya jefa kansa a kan qafafun Aliyu *Raliyallahu Anhu* ba. Bai kuma farfaxo ba, sai bayan da rana ta faxi. Ala tilas Ali *Raliyallahu Anhu* ya sallaci La'asar daga zaune yana mai nuni don ba ya iya sauke *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* daga jikinsa. A lokacin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya farka, sai ya umurce shi da cewa: Ka roqi Allah ya sake dawo maka da rana don ka sallaci La'asar xinka a tsaye. Nan take kuwa ya roqi Allah, sai ranar ta sake hudowa ya yi sallar a tsaye, inji xan Shi'ah.

Na biyu, kuma inji shi, ya faru ne a lokacin da Ali *Raliyallahu Anhu* ya ke qoqarin qetare tekun Furata a Babila tare da jama'arsa. A daidai lokacin da wasu daga cikin jama'arsa ke can suna fafutukar qetarewa da dawa kai, sai Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi sallar tare da wasu daga cikin jama'a. Mafi yawansu kuma ba su samu yin sallar ba. daga qarshe suka yi qorafi a kan haka. Ganin

haka sai wai, Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* ya roqi Allah ya sake dawo masa da rana. Ya kuwa yi hakan. Kamar yadda al-Himyari ya waqe wannan labari.

**Martani:**

Martaninmu a nan shi ne: Muna fatar xan Shi'ar ya fahimci cewa martabar Ali *Raliyallahu Anhu* da xaukakarsa a wurin Allah *Subhanahu WaTa'ala* da kasancewarsa masoyi a wurinsa, abu ne sananne ta hanyoyi tabbatattu, waxanda qwaqqwaran ilimi ya tabbatar, ta yadda ba sai an qara masu gishiri da irin qarairayi marasa tushe ba.

Ba mu musun cewa, akwai wasu malamai da suka riwaito wannan hadisi na sake hudowar rana ga Ali *Raliyallahu Anhu* irin su Xahawi da Alqali Iyal da wasunsu, waxanda suka kuma lissafa al'amarin a jerin karamomin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Amma malamai masu darajar tankaxe qwaya daga tsakuwa a fannin ilimin hadisi, sun tabbatar da cewa, wannan hadisi matsayin tatsuniyar Gizo da Qoqi ya ke. Kamar yadda malam Ibnul Jauzi ya ambaci hadisin a cikin littafinsa *Al-Maudhu'at* (Gizo da Qoqin Hadisai). Ya kuma ce: Ko shakka babu wannan hadisi qarya ce. Kuma masu riwayarsa sun rikirkita a wajen riwayar tasa.

Ita kuwa qissa ta biyu da marubucin ya ce ta faru a Babila, ko shakka babu qarya ce. Waqen kuma da Himyari ya yi ba ya zama hujja. Ko banza ba a gaban idonsa aka yi ba. Ya taras da an kitsa qaryar ne tsawon shekaru, shi kuma ya waqe ta. Kuma dama irinsa shahararren xan ta'adda ne, mai wuce gona da iri.

Kuma duk wanda ya bari sallah ta kubce masa, bai yi ta a kan lokaci ba; ba dalilin zaune ba na tsaye, to, babu abin da ke karkare zunubinsa sai tuba. Idan ya tuba kuma babu buqatar ya ranka ta. Wannan wanda ya yi sakaci kenan. Amma idan ba sakaci ya yi har sallar ta wuce shi ba, kamar ya kasance bacci ne ya kwashe shi ko mantuwa ta xibge shi har lokacin sallar ya fita, to babu wani laifi a kansa don ya sallace ta bayan faxuwar rana. Ba ya buqatar a dawo masa da ita.

Irin waxannan mas'aloli masu girma, waxanda ba a al'adanci faruwarsu ba, da sun faru kuwa, to, kusan kowa na qoqarin a ji su ga bakinsa saboda kasancewarsu a kan kari. Idan aka taras cewa mutum xaya ne ko biyu kacal suka riwaito su, kuma ga su ba amintattu ba, to, ba sai an tafi da nisa ba, an san shegiyar ce; 'yar gida Musailamu.

## 6.11 Wata Kuma Mu'ujizar Sayyidina Ali!

Xan Shi'ar ya ce hujja ta goma ita ce abin da ma'abuta tarihi suka riwaito na cewa, watarana ruwa ya yi ambaliya a garin Kufa, hankalin mutane ya tashi. Suka yi gudun ruwan ya ci su. Sai suka sheqa wurin Sarkin Musulmi Ali. Nan take Ali ya hau jakar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fita tare da jama'a. da suka isa gavar tekun Furata, sai ya sauka ya yi sallah, ya yi addu'a, ya kuma daki ruwan da wata sanda da ke hannunsa. Nan take sai

ruwan ya faxa. Sai kuma wani nau'i na kifayen da ke ciki suka kai gaisuwa gare shi. Sauran nau'o'an kuma ba su ce masa ko qala ba. Jama'ar da ke tare da shi suka tambaye shi dalilin haka. Wai sai ya karva masu da cewa: Kifayen da Allah ya nufa suka gaishe ni, su ne Allah ya tsarkake. Su kuma waxanda Allah ya hukunta da zamansu najasa, abin nisantawa sune suka yi biris da ni.

**Martani:**

Da farko dai, mun gaji da hattara sa, ina qaho? Marubucin ya kawo mana isnadin wannan qissa, wanda zai nuna tabbatuwa da ingancinta. Idan kuwa ba zai iya ba, to, ya sani fa duk wata hikaya; "Qwai ba zakara" abu ce da kowa ma ke iya samarwa. Amma hakan ba zai iya fa'idantar da komai ba.

Abu na biyu kuma shi ne: Jakar Annabi ba ta tava kasancewa hannun Ali *Raliyallahu Anhu* ba. Idan baka sani ba, to ka sani.

Abu na Uku kuma shi ne: Babu wani marubuci abin dogaro da ya riwaito wannan hikaya. Da kuwa qissa ce ingantatta, da an sami mazaje da dama sun riwaito ta a kan kari. Amma kuma sai ga shi marubucin bai ambaci isnadin qissar ba. To, ta yaya kuwa za a saurari huntuwar riwaya, don kawai wani ya ambace ta a cikin rubutunsa.

Abu na huxu kuma: Babu wani nau'i na kifi wanda ba halas ba a ci shi a shari'a. Don ta tabbata cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Ruwan gulbi mai tsalki ne, kuma mataccen namansa halas ne". Kuma Allah Ta'ala ya ce: *An halatta maku farautar ruwa da abincinsa, domin jin daxi a gare ku, kuma domin matafiya (5:96).* Haka kuma magabata daga cikin Al'umma da manyan malamai sun haxu a kan cewa, naman gaba xayan nau'o'an kifi halas ne. Ali *Raliyallahu Anhu* kuma na tare da sauran Sahabban da suka yarda da hakan. Ka ga ba ta yiwuwa ya ce wani najasa ne, wai, don bai gaishe shi ba.

Amma ba mamaki, kasancewar 'yan Shi'ah Jahilai shi ya sa suke haramta abin da Allah ya halatta, ta hanyar qirqira irin waxannan hikayoyi.

## 6.12 Ali Bai Buqatar Irin Wannan Al'amara

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta goma sha xaya ita ce, abin da masana tarihi da yawa, suka riwaito cewa: Watarana Ali *Raliyallahu Anhu* na huxuba a kan mimbari a Kufa, wai sai ga wani maciji jan-nasuru ya bayyana, ya kuma xaura anniyar hawan mimbarin da Ali ke a kai. Mutane suka firgita, sai suka yi ca! Su kashe shi. Sai wai Ali *Raliyallahu Anhu* ya hana su. A qarshe dai suka tattauna da macijin, sannan ya sauko ya tafi abinsa. Daga nan sai mutanen suka tambayi Ali *Raliyallahu Anhu* labarin macijin. Sai ya ce masu: Ai sarkin Aljannu ne, wata qissa ta rikice masa, shi ne na wayar masa da kansa a kai. Daga nan sai mutanen Kufa suka raxa wa qofar da macijin ya biyo suna "qofar maciji". Wai, daga baya ne da Umawiyyawa suka so bice wannan falala ta Ali *Raliyallahu Anhu* sai suka jibge wasu gawawwaki a qofar har tsawon wani lokaci, har sunanta ya koma "qofar Gawa".

**Martani:**

Ko shakka babu akwai mutane da dama waxanda ba su kai darajar Ali *Raliyallahu Anhu* ba, aljannu kan kai wasu buqatu irin na neman fatawa a wurin su. Wannan kuma ba tun jiya kawai ba, har ma yau. Idan ma har ta tabbata hakan ta faru, to, ai darajar Ali *Raliyallahu Anhu* ta wuce nan. Domin kuwa daraja ce da ake iya samu ga wanda ma bai kai xaukakarsa ba. Idan kuwa hakan ba ta faru ba, darajar Ali ba za ta rage da komai ba *Raliyallahu Anhu*.

Amma fa babu wanda ke buqatuwa zuwa ga tabbatar da xaukakar Ali *Raliyallahu Anhu* ta amfani da irin waxannan tatsuniyoyi sai wanda bai tava gani ko jin faruwar irin waxannan karamomi ga wani ko wasu ba. Wanda ya zauna da nagartattun mutane masu riqo da addini, waxanda fiye da irin wannan karama ta gudana gare su, ko kuma ta tava kasancewa ga shi kansa fiye da haka. Duk wanda ya shedi xaya daga cikin waxannan abubuwa ba zai ji wannan qissa ta xaga darajar Ali *Raliyallahu Anhu* da komai ba.

## 7.0 Zango na Bakwai
## Dalilan Shugabancin Sauran Imamai
## Cikon Sha Biyu

### 7.1 Samun Nassi a Kansa

Xan Shi'ar ya ce: Fasali na huxu a cikin shugabancin sauran imaman da suka rage daga cikin sha biyu. Mun sami wannan hujja ta hanyoyi da dama. Hanya ta farko ita ce "Nassi" wanda ya yaxu ya zama gama-gari a duniyar Shi'ah, suka gaji saninsa ta hanyar kunne ya girmi kaka cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce wa Husaini: "Wannan Imami ne xan Imami, xan'uwan Imami kuma baban Imamai tara. Na taran nasu shi ne jigonsu. Sunansa kamar sunana ne. Kuma laqaninsa irin nawa. Zai cika duniya da adalci kamar yadda zai tarar an cika ta da zalunci da babakere".

**Martani:**

Za mu mayar da martani a kan wannan magana ta fuskoki da dama kamar haka:

**Fuska ta farko:** Muna da tabbacin wannan qarya ce ya ke ma 'yan Shi'a. Domin kuwa wani yanki ne kawai na 'yan Shi'ar suka yarda da wannan magana ba dukansu ba. A yayin da sauran rassa na Shi'ah ke fito-na-fito da ita. Ka ga dai wannan magana ko ga qarya ba ta kai ba a idon 'yan Shi'ah Zaidiyyah. Su ne kuwa mafiya hankali da ilimi a cikin rassan Shi'ah. Su ne kuma zavavvu a cikinsu. Haka abin yake a wurin Shi'ah *Isma'iliyyah*.

A taqaice, Shi'ah na da rassa da yawa qwarai. Manya kuma daga cikinsu sun fi ashirin. Kuma gaba xayansu, idan ka xebe Isna- ashariyya, wato, 'yan-sha-biyu, babu reshen da bai qaryata wannan magana ba. To, ina zancen zama gama-gari a duniyar Shi'ah?

**Fuska ta biyu**: Wannan magana ta yi taho-mu-gama da wasu Nassosa da, rassan Shi'ah waxanda ba 'yan-sha-biyu ba, ke riwaitowa, waxanda ke walwale ta. Kamar waxanda suka aminta da cewa, wanda ba daga cikin sha biyun ba, na iya shugabanci. Ko abin da 'yan Rawandiyyah suka riwaito. A taqaice, duk abin da waxannan rassa suka tafi a kai, a kan wannan mas'ala, ya sava wa wancan da su 'yan-sha-biyu ke qoqarin tabbatarwa.

**Fuska ta uku:** Muna tabbatar wa da wannan xan Shi'ar cewa, babu wani magabaci daga cikin magabatan Shi'ah da ya riwaito wannan magana cikin wani littafi nasa, ko ya kafa hujja da ita a cikin wata huxuba. Tarihin kuwa ba voye yake ba. Wannan magana da yake qoqarin wa duniyar musulmi a yau, daga baya ne suka qaga ta, bayan rasuwar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da fiye da shekara xari biyu da hamsin. Sun qirqira wannan qarya ne a daidai lokacin da wanda suka ce shi ne imamin na sha xaya, Hasan xan

Aliyu al-Askari ya rasu. Sai suka ce wai, yana da xa Muhammad wanda ya yi dibilwa, kuma shi ne magajinsa. Na sha biyu kenan. To, a lokacin ne wannan tatsuniya ta fara bayyana.

**Fuska ta huxu:** Gaba xayan Ahlus-Sunnah da malamansu, waxanda adadinsu ya ninka na 'yan Shi'ah ninkin-ba-ninki, na da masaniya tsattsagagga wadda kokwanto ba ya iya girgizawa, a kan cewa wannan magana qarya ce aka yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Suna kuma qalubalantar 'yan Shi'ah da kiran su zuwa ga mubahala a kan haka. Kamar yadda sauran rassan Shi'ah ke kiran 'yan-sha-biyun zuwa ga haka. Da kuma malaman Shi'ah za su buga kai ga qasa su ce, lalle su, suna da masaniya a kan tawaturancin wannan magana, to, wannan masaniya tasu ba ta kama qafar wadda malaman Sunnah ke da ita ba a kan kasancewar wannan magana qarya.

**Fuska ta Biyar:** Ba a cewa magana ta zan mutawatira (gama-gari) sai ya kasance an sami waxanda ake iya karvar maganarsu a matsayin ilimi, a dama da hagu da kuma tsakiyarta. To, ita wannan magana ta rasa ko xaya. Don kafin rasuwar Hasan al-Askari babu wani da ke furta zancen Malam-na-Voye (Mahadi) a matsayin shugaba. Haka kuma babu wani ma da ke magana a kan shugabancin wasu Imamai goma sha biyu. A zamanin halifancin Ali *Raliyallahu Anhu* babu wannan magana. Haka ma zamanin Umawiyyawa. Waxanda ma ke zancen wannan shugabanci a lokacin suna raya cewa ne akwai nassi da ke tabbatar da shugabancin Ali *Raliyallahu Anhu* ne shi kaxai.

Amma iqirarin cewa akwai Nassi da ke tabbatar da shugabancin Imamai goma sha biyu da maganar "Malam-na-Voye", ba a sami wani mutum xaya da ya faxe ta ba a kwanakin farko, balle haka ta zama riwaya mai tushe.

**Fuska ta Shida**: Masu ilimi na da yaqinin cewa farkon lokacin da Shi'ar 'yan-sha-biyu ta bayyana, mutanen da ke jin cewa, akwai nassi a kan shugabancin waxancan mutane, shi ne qarshen kwanakin Halifofi shiryayyu. Wanda kuma ya qirqira wannan qarya shi ne Abdullahi xan Saba'i tare da qungiyarsa ta maqaryata. Amma kafin wannan lokaci ko vurvushinsu babu.

**Fuska ta Bakwai:** Hadisan da Sahabbai suka riwaito a kan darajoji da martabobin Abubakar, Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhum* sun fi wannan nassi, qarfin tabbata a idon jahilai ma kafin malamai. Idan kuwa har zai halatta wani ya dubi waxannan riwayoyi na Sahabbai, a kan darajojin waxannan mutane ya yi suka a ciki, to yin suka a cikin wannan riwaya ta farko ya fi halatta. Idan kuwa akwai wani uzuri da har za a iya yi wa wanda ya soki riwayar Sahabbai, to kuwa yin sa ga wanda ya soki riwayar wani shi ne mafifici.

**Fuska ta takwas:** Babu wani mutum xaya daga cikin Shi'ah 'yan-sha-biyu da ya riwaito wannan magana ta hanyar isnadi mai sadadden asali, balle

har ya zama mutawatiri. Kuma ko da an same su, to lalle ne ya kasance sun hardace wannan nassi. Kafin su iya yin haka kuwa dole ne sai sun ta maimata shi. To, muna son xan Shi'ar ya faxa mana waxanda suka hardace wannan lafazi na wannan nassi, kamar irin yadda ake hardato lafuzzan Alqur'ani, da na kalmar shahada da na kiran sallah, tsara bayan tsara har zuwa ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Lalle ne kuma wanda zai kawo xin, idan har akwai su su kasance adadi mai yawa, don daxa tabbatar da ma'anar tawaturanci.

Domin mu, a duk lokacin da muka yi iqirarin wanzuwar tawaturanci a cikin wasu darajoji na Sahabbai, to a wasu lokuta, mukan bayyana irin yadda tawaturancin nasu ya tabbata ta fuskar ma'ana, kasancewarsu ba su da waxansu lafuzza da ke da buqata da a riwaito su ta wata kevantattar siga, balle har a buqaci daddaqe su har a hardace; kamar tawaturancin da ya tabbata a kan halifancin halifofi huxu, da yaqin barasar Raqumi da na Siffin, da Auren Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Nana A'isha da na Sayyidina Ali da Fatima. Da makamantan haka.

Akwai ma lokacin da mukan tabbatar da tawaturancin a cikin lafuzzan wasu riwayoyi, waxanda ake iya riqon maganar waxanda suka hardace su a matsayin limi.

**Faska ta Tara:** Dukkan riwayoyin da aka riwaito daga Ahlul- Baiti, masu tawaturi, sun qaryata wannan riwaya taku. Babu xaya daga cikinsu wadda ke nuna cewa, akwai wani nassi a kan waxancan Imamai. Hasali ma dai su da kuke ce ma Imaman, suna qaryata ku ne, ballantana su tabbatar maku da nassin shugabancin "Sha-biyu".

### 1. Hadisin Mahadi

Xan Shi'ar ya soma da kawo wani hadisi da ke cewa: An samo daga xan Umar daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*: "Wani mutum zai bayyana a qarshen zamani daga cikin zuri'ta; sunansa xaya da nawa, kuma laqabinsa xaya da nawa. Zai cika duniya da adalci. Wannan shi ne Mahadi".

### Martani:

Hadisan da ake kafa hujja da su a kan bayyanar Mahadi ingantattu ne. Abu Dawuda da Tirmizi da Ahmad da wasunsu duk sun riwaito su, ta hanyar Ibnu Mas'ud da waninsa.

Kamar faxar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin hadisin da Ibnu Mas'ud ya riwaito cewa: "Ko da rana xaya za ta rage wa duniya, sai Allah ya tsawaita wannan rana har wani mutum ya bayyana daga Jinina, ko daga cikin mutanen gidana, sunansa zai dace da sunana. Na mahaifinsa kuma ya dace da na mahaifina. Zai cika duniya da adalci da raba daidai, kamar yadda a ka cika ta da zalunci da babakere. Akwai hadisin harwayau a cikin littafin Tirmidhi da Abu Dawuda ta hanyar Ummu Salamata *Raliyallahu Anha.*

Daga cikin waxannan hadisai kuma akwai wanda abu Dawuda ya riwaito ta hanyar Abu Sa'id wanda ke cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Mahadi na daga cikin tsatsona, a layin 'ya'yan Fatima". A cikinsa kuma ake cewa: "Zai mallake duniya cikin shekaru bakwai".

Abu Dawudan dai harwayau ya riwaito shi daga Ali *Raliyallahu Anhu* cewa, watarana ya kalli Hasan sai ya ce: "Wannan xan nawa zai zama shugaba, kamar yadda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce. Kuma wani mutum zai fito daga tsatsonsa, wanda za a kira da sunan Annabinku. Zai kuma yi kama da shi ga halaye, amma ba zai yi kama da shi ga halitta ba, zai kuma cika duniya da adalci".

To, ka ji hadissan. Amma Allah ne kaxai ya san iyakar taunar karan shanun da aka yi wa waxannan hadisai. Wasu suka kore su gaba xaya. Suna hujja da wani hadisi da ke cewa wai, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Babu wani Mahdi in ba Isah xan Maryamu ba". Wannan ko hadisi ne mai rauni da ke cikin Musnad na Shafi'i.

To, sannan su 'yan-sha-biyu da ke iqirarin cewa, mahdinsu ne na voye waxannan ingantattun hadisai ke nufi, sun manta sunan Mahdinsu: Muhammadu xan Hasan. Shi kuwa wannan Mahadi da Annabi ya bayar da labarinsa tare da siffanta shi, suransa muhammadu xan Abdullahi.

## 7.2 Samuwar Ma'asumai a Kowane Zamani

Xan Shi'ar ya ce abu na biyu da ke tabbatar da shugabancin sauran Imaman shi ne; mun riga mun bayyana cewa wajibi ne a sami Imami ma'asumi a kowane zamani. An kuma yi ijma'i a kan babu wasu ma'asumai bayan waxancan Imamai.

## Martani:

Mun riga mun rosa yankin maganarsa ta farko, cewa lalle ne a sami ma'asumi a matsayin Imami, kowane zamani. Ko ma ko a cikin 'yan Shi'ah an samu waxanda suka tafi a kan cewa waxancan imamai nasu ba Ma'asumai ba ne.

To, sannan a yau shekarar wannan ma'asumi, da suke ta quzamin zai bayyana, fiye da xari huxu da hamsin da haihuwa, kamar yadda suke tabbatarwa kuma wai ya shige ne cikin wani kogo mai dausayi a qarqashin qasa a shekara ta 260H, a lokacin yana xan shekara biyar da haifuwa. Wasu daga cikinsu kuma suka ce bai kai haka ba. Amma duk da waxannan zunzurutun shekaru, har yau tsit kake ji kamar an shuka dusa; babu wani abu na amfani ga jama'a, irin wanda shugabanni da alqalai da malamai ke gudanarwa da ya tava bayyana daga gare shi, wanda ke iya tabbatar wa duniya ko ma dai mabiyansa kawai, cewa, lalle dai akwai shi. Balle har a wayi gari a ce ya taka wata rawa daga can voye irin wadda shugaba ma'asumi ya kamata a ce ya taka. To, a irin wannan hali, ko da ta tabbata cewa akwai shi xin, me ye amfanisa? To, balle daxa idan dama babu shi!

## 7.3 Darajojin Imamai Goma Sha biyu

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta uku ita ce, darajojin da kowane xaya daga cikinsu ke da, irin waxanda ke tabbatar da zamansa Imami.

**Martani:**

Qololuwar abin da waxancan darajoji ke iya tabbatarwa shi ne cancantarsu ga zama Imamai. Amma ba za su iya tabbatar da kasancewarsu imaman ba. Kamar yadda kasancewar mutum ya cancanci zama alqali, ba tana nufin ya zama alqali ba, har sai in naxa shi.

Kuma ta tabbata cewa, akwai wasu daga cikin Quraishawa waxanda suka cancanci zama imamai, kamar yadda cancantar waxancan ta tabbata. Ka ga su ma waxannan Quraishawa suna zama imamai kenan don wannan cancanta? Mafi yawan masu hankali sun gamsu da cewa shi Imamin nasu na sha biyu Amaryar Boqo ne. A haka kuwa, babu ta yadda za a yi ya zama imami sai fa in a kan mutanen voye!.

Wasu cikin Imaman nasu, musamman na sha xaya da na sha biyu, ba wanda ya san su da wani ilimi ko riqo da addini irin wanda aka san saura da shi kamar Aliyu xan Husaini da Abu Ja'afar al-Baqir da Ja'afarus Sadiq da makamantansu. To, ta ina suka cancanta?

## 8.0 Zango na Takwas
## Ayubban Sauran Halifofi, Inji Shi

Xan Shi'ar ya ce: Fasali na biyar: Duk wanda ya yi halifanci kafin Ali *Raliyallahu Anhu* ba halifa ba ne ta fuskoki da dama.

**Martani:**

Idan xan Shi'ah na nufin musulmi ba su karvi waxancan halifofi uku a matsayin shuganni ba, ba su kuma yi masu mubaya'a ba, balle su sami wata dama ta zantar da hukunce-hukuncen shari'ah kamar haddi da sauransu, da tabbatar da cewa kowa ya sami haqqinsa. Kuma musulmi ba su yi yaqi a qarqashin jagorancinsu ba, ba su kuma yi sallolin jam'i da na idi a bayansu ba, ko waxansu abubuwa daban-daban, waxanda kalmar shugabanci ke tabbatarwa. Idan wannan ne abin da xan Shi'ar ke nufi, to, ya sha qarya. Kuma abin da ya yi xin nan girman kai ne. Tabbatuwar waxannan abubuwa da ya ke qoqarin korewa, abu ne sananne ta hanyoyin da suka fi yawan shurin masaki. 'Yan Shi'ah da sauran qungiyoyin bidi'a ba wanda bai san haka ba. Kuma ai kasancewar shugabancin waxancan halifofi ga musulmi ya karva sunansa, shi ya sa 'yan Shi'ah ke sukar su.

Kuma wani babban kuskure da suke yi shi ne, kodayaushe sai su yi ta yanke hukunci wane shugaba ne, wane ba shugaba ne ba, a dunqule; ba tare da sun yi bayani ba. Shin idan suka ce wane shugaba ne, suna nufin naxin da aka yi masa da ayyukan da ya gabatar, ko ko a'a, suna nufin ya cancanta ya zama shugaba ne kawai koda ba a naxa shi ba?

Wata irin wannan kuma sai ka taras suna amfani da kalmar "Imamu" ga wanda suka qudurce cancantarsa kawai. Amma kuma a kaikaice, sai su nuna wa duniya cewa, kalmar ta haxa cancanta da naxi da gudanarwa. Ka ji kai!

To, a taqaice idan 'yan Shi'ah na nufin Abubakar da Umar da Usmanu *Raliyallahu Anhum* sun zama halifofi ne kawai ba tare da sun dace ba. Aliyu *Raliyallahu Anhu* ne ya dace. Ko ko a'a, sun dace amma Aliyu ya fi su dacewa da ita. To wannan qarya ce. Kuma wannan fage ne na qwanciqwalinto.

Saboda haka, za mu iya basu amsa a kan wannan batu; a dunqule, kamar yadda suke yi, sannan kuma mu zo mu warware masu zare da abawa.

A dunqule, muna iya cewa: Ahlus-Sunnah na da masaniyar cewa, shugabancin da waxancan halifofi suka yi, sun yi shi ne a kan dacewa da cancanta. Wannan masaniya kuwa da muke da ita kamar yankan wuqa take. Ta yadda ba za ka taras da mutum biyu daga wasu qungiyoyin musulunci na gardama a kanta ba, sai fa idan akwai xan Shi'ah a cikinsu.

Qarewa da qarau ma, mafi yawan malaman wannan al'umma cewa suke yi Abubakar da halifofi biyu bayansa su ne mafi cancantar mutane da shugabanci a lokacin da suka yi shi. Sukan ma take kwano, su ce: Kai mu a saninmu babu wanda ya kai gare su a girman daraja cikin wannan al'umma baki xaya.

To, kuma ina son xan Shi'ar ya sani cewa, babu wani dalili qwaqqwara, kai ko ma mai rauni da za a zo mana da shi wanda zai tayar da mu daga wannan tantagaryar masaniya da muke da ita. Domin kuwa qwararan dalilai ba su kau da juna balle xaya ya farke wa xaya laya. Shi kuwa mai rauni ba ya iya komai da qwaqqwara irin wanda ke hannunmu.

Wani abin kuma shi ne, duk abin da xan Shi'ar ko wani mai suka, zai zo da shi a kan shugabancin waxannan halifofi uku, to, ba ya fita daga xayan abubuwa biyu: Ko dai ya zama riwaya ce wadda ba ingantatta ba. Ko kuma mu leqa shi mu kasa ganin abu xaya da ke iya tabbatar da rashin ingancin shugabancin nasu, a cikinsa. Da zarar kuwa hujjojin nasu suka kasa fita wannan qangi, to, ba za su iya ruguza taron haxin guiwar masaniya da ke hannunmu ba.

Da zarar kuwa irin wannan dalili yankakke ya tabbata, a kan dacewar halifofin da shugabancin, kamar yadda ya tabbata a wurinmu, to, babu buqatar sai mun ci dugadugan sauran qyaleqyalin da suka yi wa qaryar. Tsayawa bayar da amsa a kan waxannan wofintattun Shubuhohi, bayan an rosa ginshiqansu, vata lokaci ne.

Babu wani mutum da ke iya rosa masaniyar da aka sakankance da ita, alhali makamin da ke hannunsa sungumin ragga ne kawai. Kasancewarsa mai kai kora, ko wanda ake kawo wa ba za ta daxa shi da komai ba. Amma a matsayinsa na mai kariya, idan ya gama gane varnar da ke cikin shubuhohin, ya kuma sanar da wani, to, ya bunqasa iliminsa, ya kuma taimaki gaskiya ga duk mai nemanta ta hanyar fira ko tattaunawa. Idan kuwa har bai gano varnar da ke cikin shubuhar ba, wadda take matsayin gaskiya a wurin mai ita. To, shakkar da ke tare da shi ba za ta iya tunkuxe ta ba. Idan an biyo mu a hankali za mu faxi dalilai masu yawa a kan cancantar halifofin nan guda uku, da kasancewarsu sun sha gaban kowa a fagen cancantar, in Allah ya so.

### 8.1 Wai Abubakar ba Shi da Lafiya

Xan Shi'ar ya ce: na farko: Abubakar ya tava cewa: Ni fa ina da wani iska da yake bijiro mani. Saboda haka idan kun ga na yi aikin hankali, to, ku kama mani. Idan kuwa na kama daji, to ku kevo ni. Xan Shi'ar ya ce, ka ga shugaba ne ya kamata a ce ya kankamta talakawansa. Ba su su kankamta shi ba.

### Martani:

Lafazin da aka riwaito daga bakin Abubakar Siddiqu *Raliyallahu Anhu* cewa ya yi: "Akwai wani Shexani da ke bijiro mani (yana nufin a lokacin fushi). Idan da kuka ga ya bijiro mani, to, ku nisance ni don kar ku ji a jikinku". Kuma ya ce: "Ku bi ni matuqar na bi Allah. Idan kuwa na sava masa, ban cancanci ku bi ni ba".

Wannan magana da Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya yi ita ce mafi girman abin da za a yabe shi da shi. Kamar yadda za mu qara bayani da yardar Allah.

Malamai dai sun bayyana cewa, irin wannan shexani da ke bijiro wa Abubakar *Raliyallahu Anhu* yana bijiro wa kowane xan Adam a lokacin da ya ke cikin fushi. Saboda haka ne Abubkar ya ji tsoron ya cutar da wani daga cikin talakawansa a irin wannan lokaci. Shi ya sa ya hore su da kama kansu a duk lokacin da suka gan shi a cikin fushi. Kamar yadda aka samu cewa, ya zo a cikin Buhari, daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Kada alqali ya yanke hukunci tsakanin mutum biyu alhali yana cikin hushi”.

Wannan hani da Annabi ya yi, na yin hukunci a lokacin fushi, shi ne abin da Abubakar ya yi la’akari da shi; ya qudurta cewa ba zai tava yin hukunci yana fushi ba. Saboda haka ya nemi kada su kusanto shi balle su kawo masa qara, su kuma nemi ya saurare ta a irin wannan yanayi. Wannan kuwa na tabbatar da irin yadda Abubakar *Raliyallahu Anhu* ke biyayya ga Allah *Subhanahu WaTa’ala* da Manzonsa.

Babu kuma wani xan Adam da fushi ba ya bijiro wa; har kuwa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a matsayinsa na shugaban ’yan Adamu. A kan haka ma aka riwaito yana cewa: “Ya Ubangiji ka san ni mutum ne; ina fushi kamar yadda kowane mutum yake yi. Saboda haka ina roqon ka yi mani tabbataccen alqawari, irin yadda ka saba, na gafarta wa duk wani mumini da na yi wa ba daidai ba, ta hanyar sosa ransa da wata ‘yar magana, ko sa a yi masa bulala bai ji bai gani ba, a kan fushi. Ka yafe masa ka kuma kusantar da shi zuwa gare ka ranar Qiyama a dalilin haka. Buhari da Mislimu sun fitar da shi a cikin ingantattun littafansu daga Abu Hurairata.

Haka kuma cewar da halifa Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya yi: Idan na tsaya a kan gaskiya to, ku taimake ni. Idan kuwa na saki godabenta, to, ku yi mani hannunka mai sanda. Wannan magana na nuna cikar adalci da tsoron Allah da Abubakar *Raliyallahu Anhu* yake da su. Kuma wajibi ne ga kowane shugaba ya yi koyi da shi a cikin haka. Kamar yadda yake wajibi a kan talakawa su taimaki shugabansu a duk lokacin da ya hau godaben gaskiya, su qara masa qwarin gwiwa a kan xa’a ga Allah Ta’ala. Idan kuma ya saki godaben, ya faxa kurakurai, su kamo sandarsa su xora shi a kan gaskiya. Idan ya faxa zalunci da gangan, su hane shi gwargwadon ikonsu. Idan kuwa mai son gaskiya ne irin Abubakar, ba su da wani uzuri da zai sa su bar shi a kan zalunci. Idan kuwa sai an yi hasara mai yawa wadda ta fi zaluncin da suke son hana shi yi, to, ba a ce su tunkuxe qaramin sharri koda za su janyo babba ba. Don haka, sai su qyale shi, su bar shi da Allah, su bari a zauna lafiya.

Ita kuwa cewar da xan Shi’ar ya yi wai shugaba ne ake da buqatar ya kankamta talakawansa, ba su su kankamta shi ba. Wannan magana na da gyara, ta fuskoki biyu:

1) Abin da muka yarda da shi, shi ne: Dole ne a samu taimakon juna a kan xa’ar Allah da jin tsoronsa, tsakanin shugaba da talakawa. Ba a wayi gari

kowanensu na xaure wa xaya gindi a kan varna da shisshigi ba. Ana so ne su kasance tsakaninsu kamar yadda kwamandan runduna yake da dakarunsa. Kamar kuma yadda limamin sallah da jagoran hajji suke da mabiyansu. Tunda kuwa har Manzo ya riga ya iyar da manzanci; addinin musulunci ya kammala ya yaxu ta fanninsa, kuma duk wanda zai kasance shugaba a kan musulmi, ba da wani sabon addini zai jagorance su ba, ka ga shi da su kowa na da buqata da juna.

Neman sanin gaskiya wajibi ne a cikin kome, a manyan mas'aloli da qanana. Don haka, da shi da su sai su qoqarta. Idan hukunci ya bayyana an huta, sai a yi aiki da shi. Idan kuwa shugaban ne ya riga fahimtar mas'alar, to, sai ya bayyana masu. Su kuwa lalle ne su saurare shi. Idan kuwa aka yi kunnen doki; kowa bai gane ba, to sai su taru a teburin shawara har Allah ya yi masu gamo da katar.

Idan aka yi sa'a ana cikin haka, wani daga cikin talakawan ya gane bakin zaren mas'alar, to, sai ya bayyana wa shugaban. Idan kuma aka sami banbancin ijtihadi tsakaninsu da shi, to nasa ne abin rinjayarwa da xauka. Don kuwa ba ya halatta su tashi baran-baran.

2) Maganar da sayyidina Abubakar ya yi a kan sha'anin shugabanci, ta qara masa girma da xaukaka a idon al'umma. Tarihi ya tabbatar da cewa wannan al'umma ba ta girmama mahaluki ba, bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* irin yadda ta girmama Abubakar *Raliyallahu Anhu*. Ba ta kuma yi wa wani xa'a ba kamar yadda ta yi masa. Al'ummar kuwa ta yi wa Abubakar wannan xa'a ne don qashin kanta; ba don wani abu da suke kwaxayin samu ko suka samu daga gare shi ba, ko wani zalunci da suke tsoron ya far masu daga gare shi.

Dama a duk lokacin da jama'a suka yi mubaya'a ga shugaba a qashin kansu, kamar yadda Sahabbai suka yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a qarqashin bishiya. To, za ka taras sun yarda da girmansa da cancantarsa. Wannan shi ya sa a duk lokacin da wani xan canjin yawu ko wata tankiya ta shiga tsakanin Sahabbai, a zamanin halifa Abubakar *Raliyallahu Anhu* a kan wata mas'ala ta addini, to, da zarar ya shiga ciki ya yi masu bayani, za su saurare shi, su kuma miqa wuya ga hukuncin da ya yanke. Abubakar *Raliyallahu Anhu* ne kuma kawai ke da irin wannan matsayi, sai ko Umar da ya rufa masa baya, da Usman da ya rufe qofar.

Amma ka ga Ali *Raliyallahu Anhu* ba kaxan ya kai ruwa rana da su ba; ya yaqe, suka yaqe shi. A qarshe kuma ba wanda ya tayar da doron bayan wani. To, wane shugaba ne daga cikinsu ya karva cikakken sunan shugaba? Wane ne daga cikinsu ya samu damar tsayar da addini, ya dawo da murtaddai bisa godabe, ya yaqi kafirai, kuma muminai gaba xaya suka karve shi? Na bar maka amsar.

Ko shakka babu, ba wanda zai daidaita waxannan shugabanni da wancan sai mai tayayyen hankali da raggancin addini.

## 8.2 Wai Mubaya'ar Abubakar ba ta yi ba

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta biyu ita ce maganar Umar da ya ce: "Mubaya'ar da aka yi wa Abubakar ta kasance girshi ce, amma Allah ya kare musulmi daga sharrinta. Kuma duk wanda ya sake yin irinta ku kashe shi".

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Cewar da Umar ya yi "ta kasance girshi ce" yana nufin ba da son mutane aka yi ta ba. Kuma ya ce Allah da ya kare musulmi daga sharrinta. Sannan ya yi umurni da a kashe duk wanda ya sake yin irinta. Wannan ka ga yana wajabtar da suka ga Abubakar.

## Martani:

Abin da Umar ya faxa yana cikin Buhari da Muslimu, wanda aka riwaito daga xan Abbas, a cikin wata huxuba da inda yake cewa: "Na sami labarin wasu na cewa: Wallahi da zaran Umar ya mutu ni ga wanda zan wa mubaya'a. To, kada wani ya kuskura ya yi hujja da cewa, an wa Abubakar mubaya'ar a kan girshi. Ba shakka haka ne. Amma kuma Allah Ya kare musulmi sharrinsa. Yau kuma daga cikinku babu wanda mutane ke iya danqa kansu gare shi kamar Abubakar. Duk wanda ya kuskura ya yi mubaya'a ga wani mutum ba tare da shawarar sauran jama'a ba sai ya gwammace bai yi ba, don su duka za a kashe su; da shi da wanda ya wa mubaya'a".

Sannan sai Umar ya soma ba da labarin yadda aka wa Abubakar xin mubaya'a bayan cikawar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*.. A ciki yake cewa: "... Sai Abubakar ya ce: Na yarda ku zavi xaya daga cikin waxannan mutane, ku yi masa mubaya'a. Da faxin haka sai ya kama hannuna da na Abu Ubaidata, muna a tsakiyarsa. Duk abin da ya faxi bai dame ni ba sai wannan. Don wallahi na fi son a sare kaina, - in ba zunubi - a kan in shugabanci mutanen da Abubakar yake cikinsu. Wannan shi ne tunanina a wancan lokaci. Kuma har yanzu haka nake ji, ban san abin da rai zai yi tunani kafin mutuwa ba."

Ma'anar wannan magana ta Umar shi ne mubaya'ar da aka yi wa Abubakar *Raliyallahu Anhu* ta zo ne kwaram, ba tare da wani shiri a kanta ko quduri da aka tsara ba. Kamar yadda shi Umar xin ya faxa da bakinsa. Kuma yanayi ne kawai ya wajabta zaven Abubakar a lokacin da aka yi shi ba don an shirya hakan ba. Mutane ne kawai suka taru, suka kuma yi masa ita. Saboda sun san ya fi kowa cancanta da ita a lokacin. Ba ni kuma sa ran akwai wani mutum da jama'a za su taru su tabbatar da cancanta da dacewarsa irin yadda suka taru a kan Abubakar. A kan haka duk wanda ya nemi yi wa wani mutum mubaya'a ba tare da yardar sauran musulmi ba, ya jawo rarraba mai wajabta a kashe shi.

Kuma Umar ba addu'a ce yake yi, Allah ya kare musulmi daga sharrin mubaya'ar ba. Yana ba da labari ne cewa, Allah ya kare, ba abin da ya faru don an yi ta ba shiri. Kuma kan malamai ya haxu a kan haka.

**8.3 Wai Halifofi Uku Jahilai ne!**

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta uku ita ce, qarancin ilimin halifofi uku kafin Ali, ta yadda har suke dogara gare shi a cikin mafi yawan hukunce-hukunce.

**Martani:**

Babu shakka wannan magana na xaya daga cikin manya-manyan qaryace-qaryace. Don ba a tava jin lokacin da Abubakar ya nemi qaruwa da wani abu na ilimi daga Aliyu ba. Hasali ma Ali ne ta tabbata ya yi karatu wurin sa. Don ga riwayarsa nan daga Abubakar xin a cikin littafai ana karantawa.

Haka kuma qaruwar da Ali *Raliyallahu Anhu* ya yi da Umar ta fuskar ilimi ta fi wadda Umar ya yi daga gare shi. Shi kuwa Usman duk da kasancewar tarihi ya tabbatar da cewa, bai kai ilimin Abubakar da Umar ba, amma bai tava buqatuwa zuwa ga Ali ba a cikin wata harka ta ilimi. Akwai ma lokacin da wasu mutane suka kai qara ga Ali game da ma'aikatan zakka na wasu gwamnoni a zamanin Usmanu. Sai shi Alin ya aika wa Usmanu *Raliyallahu Anhu* da littafin da ke magana a kan Zakka. Sai Usmanu ya ce a koma masa da shi. Don bamu da buqata da shi.

Wannan magana ta Usmanu kuwa gaskiya ce. Domin Kuwa faralin zakka da yadda ake fitar da ita, da kuma rabonta duk ta hanyoyi huxu aka same su. Hanyar da ta fi kowace inganci daga cikinsu ita ce takardar da sayyidina Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya rubuta wa Anas xan Maliki sadda ya sa shi wannan aiki. Tana cikin littafin Buhari. Kuma da ita ne mafi yawan malamai suke hujja. Hanya ta biyu kuwa itace, littafin Umar.

Amma littafin da aka riwaito daga Ali *Raliyallahu Anhu* wanda shi ne na ukku, akwai abubuwa a cikinsa da babu wani malami da ya karve su. Kamar cewar da ya yi: Zakkar awaki ashirin da biyar ita ce, xaya bisa biyar 1/5 na akuya. Ko shakka babu wannan hukunci yayi ban hannun makafi da abin da ya zo ta hanya mai cikakken inganci (tawaturi), daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Saboda haka, wannan abu da aka riwaito daga Ali ko dai ya kuskure ne, ko an shafe shi.

Littafi na Huxu shi ne littafin da Amru xan Hazmu *Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rubuta masa shi ne a lokacin da ya aika shi zuwa Najrana.

Kuma littafin Abubakar *Raliyallahu Anhu* shi ne na qarshe a cikinsu. To, ya mai hankali zai ce ga Ali ne suke komawa wajen warware matsalolin ilimi? Ai ko alqalan da Ali ya naxa irin su Shuraihu da Abidatus-Salmani da makamantansu suna shari'a ne da abin da suka sani kuma suka karanta na ilimi ba sai daga wajen Ali *Raliyallahu Anhu* ba.

**8.4 Kuma Wai Halifofi Sun yi Abin Kunya!**

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta huxu ita ce abubuwan da, waxannan halifofi suka aikata na abin kunya waxanda muka riga muka anbaci mafi yawansu.

**Martani:**

Mu ma ai mun riga mun mayar da martani a kan waxannan zarge-zarge a dunqule da kuma xaixaice. Kuma mayar da martani game da zargin waxannan halifofi uku, ya fi sauqi da samun karvuwa ga masu ilimi da hankali, bisa ga mayar da martani a kan masu zargin Ali *Raliyallahu Anhu*. Kuma duk wanda ke da ilimi da adalci, ya kuma yi la'akari da bayanan da muka yi a baya, ba zai yi gangancin sukar waxancan Sahabbai ya wanke Ali *Raliyallahu Anhu* ba, a cikin gaba xaya matsalolin. Duk kuwa lokacin da ya yi qarfin halin tsalkake Ali da wanke shi, to, za ka tarar, waxancan halifofi uku sun fi cancanta da wannan wankan tsalki a kan sa. Kamar yadda a duk lokacin da ya ci zarafinsu, duk mai basira zai fahimci cewa cin zarafi ya fi dacewa da Ali *Raliyallahu Anhu* in har yana dacewar.

Kuma harwayau da 'yan Shi'ah za su ce sun kakkave hannayensu daga waxancan soke-soke da cin zarafi da suka yi wa halifofin can dattijai, to su sani soke-soke da cin zarafin da suka yi wa Ali *Raliyallahu Anhu* na nan tabbace, ba za su kuvuta daga gare su ba. Idan kuma sun ci gaba da rungume maganganun na sukar halifofin, hakan ba za ta rage halifofi da komai ba. Don mun riga mun bayyana kasancewar su qarya, mun kuma walwale ta da gaskiya.

### 8.5 Wai Halifofi Uku Sun Bauta ma Gumaka

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta biyar itace faxar Allah Ta'ala da ya ce:

﴿لَا يَنَالُ عَهْدِى ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿١٢٤﴾﴾ البقرة: ١٢٤

*Alkawarina ba zai sami azzalumai ba [2:124]*

Wai Allah Ta'ala na nufin alqawarinsa na halifanci ba zai je ga hannun azzalumai ba. Duk kuwa kafiri azzalumi ne, domin Allah Ta'ala ya ce a wani wurin:

﴿وَٱلْكَٰفِرُونَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿٢٥٤﴾﴾ البقرة: ٢٥٤

*Kuma kafirai sune azzalumai [2:254].*

**Martani:**

Sanannen abu ne cewa addinin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, kai da ma sauran Annabawa da Manzannin da Allah ya aiko, sun zo da cewa, ingantaccen imani na share gaba xayan zunubai da ma kafirci idan imanin ya biyo bayan sa. Kamar yadda Allah Ta'ala ya ce: *Ka ce wa waxanda suka kafirta idan sun hanu, za a gafarta musu abin da ya riga ya shige [8:38].* Kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya faxa a cikin hadisi ingantacce: "Lallai ne musulunci na karkare abin da ke gabaninsa". A cikin wani lafazin kuma cewa yayi: "Musulunci na rosa duk abin da ya kasance gabaninsa. Kuma Hijira na rosa duk abin da ya kasance gabaninta. Kuma Hajji na rosa duk abin da ya kasance gabaninsa".

A tantagaryar gaskiya ba duk wanda aka haifa da layar musulunci a wuya ba ne, ya fi wanda ya musulunta da kansa girman daraja. A'a, ai nassoshi

masu tarin yawa sun tabbatar da cewa, mafi alhairin mutane su ne waxanda suka rayu zamanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kuma mafi yawansu, sun shiga musulunci ne bayan a da sun kasance kafirai. Amma tattare da haka sun fi qarni na biyu; waxanda aka haifa cikin musulunci, girman daraja a wurin Allah. Amma 'yan Shi'ah ba su yarda da hukuncin da Allah Ta'ala da Manzonsa suka yi a wannan mas'ala ba, kuma kan magabata ya haxu a kai, hankullan masu hankali suka karva. A wajen 'yan Shi'ah *Azaru* (mahaifin Annabi Ibrahimu) ya yi imani. Haka mahaifan Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da kakanninsa, da baffansa Abu Xalib duk sun yi. A daidai lokacin da suke kafirta waxanda suka yi imani da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* imani na gaskiya kuma suka saxaukar da rayukansu a bayansa.

Kafin Allah Ta'ala ya aiko Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* babu wani mutum daga cikin Quraishawa da yake mumini; mazansu da mata, manya da qanana, halifofi ukku da shi Alin kansa. Duk ba muminai ba ne a wannan lokacin. Ba ta yiwuwa kuwa a ce manyan mutane kawai ke bautar gumaka daga cikinsu. Yaran ma, Aliyu da takwarorinsa duk ita suke yi.

Kan musulmi ya haxu a kan cewa, duk wanda ya dubi musulmi ya ce masa kafiri, bisa dalilin cewa ai kafiri ne kafin wannan rana. To, irin wannan mutum shi ne kafirin. Wannan kenan. To, balle daxa wanda ya dubi mafi xaukaka daga cikin halitta ya ce masu kafirai, ta la'akari da tsohon tarihinsu. Wal'iyazu billahi.

### 8.6 Wai Abubakar ya Nemi Yin Murabus

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta shidda ita ce cewar da Abubakar ya yi, ku yi mani murabus don ba ni ne mafi alheri daga cikinsu ba. Inji shi.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Da ta tabbata Abubakar imamu ne, da bai nemi a yi masa murabus ba. Don faxin haka ba ya halatta gare shi.

### Martani:

Kamata ya yi marubucin ya bayyana ingancin wannan magana. Idan kuwa ba zai iya ba, to ya sani ba duk abin da aka riwaito ne gaskiya ba. Kuma saqar duk da aka kitsa a kan zance da bai inganta ba, ita ma hakan.

Abu na biyu: Idan ta tabbata cewa, Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya faxi wannan magana, babu mai ikon ce masa don me? Domin kuwa babu wani dalili da zai hana a yi masa murabus xin matuqar ya nemi hakan don wani dalili na qashin kansa. Mu dai ba mu da wata masaniya a kan ya nemi murabus ko bai nema ba, balle mu ga wurin vata lokaci a kan wannan batu.

### 8.7 Kuma Wai Abubakar ya yi Nadama!

Xan Shi'ar ya ce: Dalili na bakwai shi ne abin da Abubakar ya faxa a lokacin rasuwarsa cewa: Da ma dai a ce na tambayi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ko Ansaru na da haqqi a halifanci?

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Wannan na nuna cewa, shi kansa Abubakar na jin mubaya'ar da aka yi masa haramtatta ce. Ko banza kuma shi ne fa wanda ya rufe bakin Ansaru a ranar Saqifa, lokacin da suka ce, a naxa halifofi biyu; xaya daga cikinmu, xaya kuma daga cikinku. Sai Abubakar ya ce: Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Kada a wuce Quraishawa a zaven shugabanni.

**Martani:**

Gaskiya ne Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: Kada a wuce Quraishawa a zaven shugabanci. Amma duk wanda ya ce Abubakar siddiqu ya yi kokwanton wannan magana, ko wai bai natsu da shugabancin da aka zave shi yi ba, haqiqa ya fesa qarya.

Haka kuma duk wanda ya ce wai, Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya ce: ya yi nadama a kan bai tambayi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* matsayin Ansaru a cikin halifanci ba, shi ma haqiqa maqaryaci ne. Tarin nassosan da ake da su a tarihin musulunci, a kan wannan matsala, waxanda kuma suka inganta daga bakin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba za su bari Sahabbai su yi kokwanton wani abu a cikin al'amarin ba. Balle har wani daga cikinsu yayi da-na-sanin wani abu a kai.

Wannan na tabbatar da kasancewar wannan riwaya ba gaskiya ba.

**8.8 Wai Abubakar ya Faxa Gidan Fatima ba Sallama!**

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta takwas ita ce, abin da Abubakar ya faxa lokacin da yake jinyar ajali: "Wai ni kaina! Da na sani da ban faxa gidan Fatima ba sallama ba. Da kuma lokacin da muke gidan bani Sa'idah na kuma hannun xayan mutane biyu, ya zama shugaba in zama wazirinsa".

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Wannan magana na tabbatar da cewa, lalle Abubakar ya faxa gidan Fatima, lokacin da Sarkin Musulmi Ali *Raliyallahu Anhu* da Zubairu da wasu Sahabbai ke ganawa a ciki.

**Martani:**

Babu wata sukar lamiri da za ta karvu, sai idan lafazinta na da isnadi ingantacce, a kuma taras da sukar a cikinsa varo–varo; ba sai an yi lalabe da tawili ba. Idan xayan waxannan sharuxxan suka kasa samuwa a cikin lafazi, to, ba maganar suka a cikinsa sai dai wani abu.

Ahlus-Sunnah na da yaqini da masaniyar cewa, Abubakar *Raliyallahu Anhu* bai cutar da Aliyu da Zubairu *Raliyallahu Anhu* da komai ba. Kai ko Sa'adu xan Ubadata, Sahabin da ya qi yi wa Abubakar mubaya'a, bai haxu da wata cutarwa daga Abubakar ba.

Qololuwar abin da masu faxa suka faxa shi ne, wai, Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya leqa gidan Fatima ba da izini ba da nufin ya ga ko akwai wata dukiya ta musulmi a ciki, don ya xanka ta ga waxanda suka cancanta. Daga baya kuma yayi tunanin cewa, ko barin su aka yi da ita daidai ne, don ya

halatta a ba su wani abu daga dukiyar gwamnati. Amma babu wani mai hankali da ilimi, da ya ce Abubakar ya faxa gidan har ya cutar da waxancan bayin Allah kai tsaye. Wannan magana ce irin wadda jahillai da maqaryata ke yawo da ita, jahillan masana kuma na gasgata su. Irin waxanda ke yayata cewa, wai Sahabbai sun rosa gidan Fatima, suka dake ta a ciki har ta faxi.

Gaba xayan musulmi kuwa, sun haxu a kan cewa, duk waxannan maganganu shaci-faxi ne kawai, irin waxanda sai idan an xauki mutum a matsayin dabba, sannan ne ake tallata masa su.

Kuma marubucin ya manta ya faxa mana isnadi tare da ingancin cewar da ya yi wai, Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya yi fatar ba a yi masa mubaya'a ba. To, idan ma ta tabbata cewa ya faxi hakan, to kuwa alama ce ta irin zuhudu da tsentseni da tsoron Allah da yake da su.

## 8.9 Wai Halifofi Sun Fice Daga Rundunar Usamatu!

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta tara ita ce: Cewar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi watarana: Ku shirya rundunar Usmatu. Ya daxa maimatawa tare da qarfafa son ganin an aiwatar. Kuma daga cikin waxanda ya umurta da tafiya a cikin rundunar wai, akwai Abubakar da Umar da Usmanu. Amma kuma wai bai Umarci Aliyu *Raliyallahu Anhu* da hakan ba. Ya kuma yi haka ne don hakan ta ba Aliyun damar zama halifa bayansa, ba tare da waxancan Sahabbai uku sun hana shi ba, tunda ba su nan. Amma kuma wai ba su bi umurnin ba, inji xan Shi'ar.

## Martani:

Muna son marubucin ya tabbatar mana da ingancin wannan riwaya. Don babu wanda ya riwaito da isnadi sananne. Babu kuma wani daga cikin masana riwaya da ya inganta ta. Kuma sanannen abu ne cewa, ba a kafa hujja da riwayoyi, sai bayan an gama gane ingancinsu. Idan kuwa aka ce ba za a tsare mutuncin wannan qa'ida ba, to kowa fa na da baki yana kuma da ra'ayi.

Malaman riwaya kam sun haxu a kan cewa, wannan magana qarya ce. Domin kuwa Abubakar da Usmanu ba su kasance cikin rundunar Usamatu ba. Wanda kawai ake jin ya kasance cikinta shi ne Umar *Raliyallahu Anhu*.

Kuma dalilai mutawatirai sun tabbata daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa, ya halifantar da Abubakar ya ci gaba da ba Sahabbai sallah. Haka Abubakar xin ya riqe wannan aiki har Allah ya yi wa Manzon Allah rasuwa. Shi ne kuma ma ya jagoranci sallar safe, a ranar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* zai rasuwa. Yana cikin bayar da sallar, sai Manzon Allah ya xaga labulen qofarsa ya kalli Abubakar *Raliyallahu Anhu* gaban sahu, ya yi murmushi ya koma. To, ya za a ce bayan wannan nauyi da ya xora masa, kuma ya umurce shi da biyar rundunar Usamatu?

Da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallam* ya yi nufin naxa Ali *Raliyallahu Anhu* a matsayin Yarima mai jiran gado, waxannan Sahabbai uku ba za su musa masa ba. Da kuma qaddarar Allah za ta sa su yi masa musu, da sauran

Sahabbai sun shawo kansu. Don gaba xayansu ba su saba da savawa ko bari a sava wa umurnin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba. Ba ka ganin aqalla kashi xaya cikin uku na musulmi sun tallafa ma Ali wajen yaqar da ya yi ma Mu'awiyah alhalin ba shi da wani nassi da ya sa shi yin haka? Ya kake zato da Ali na da nassi na zama halifa tun farko, amma waxancan suka amshe masa? Nawa ne daga cikin Sahabbai za su mara masa baya a wannan hali?

Da kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na nufin Ali *Raliyallahu Anhu* ya gaje halifarsa bayan wucewarsa, to, da kuwa shi zai danqa wa limancin sallah, tun yana raye. Amma bai yi haka ba. Sai ya danqa ma Abubakar *Raliyallahu Anhu*. tana da wuya ma ya yi haka don bai tava sa Abubakar qarqashin Aliyu ba.

## 8.10 Wai Abubakar Bai Tava Jagoranci a Zamanin Manzon Allah ba!

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta goma ita ce kasancewar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai tava shugabantar da Abubakar a kan kulawa da wani aiki ba. Sai dai ya shugabantar da wani a kansa.

**Martani:**

Wannan magana ba gaskiya ba ce. Ai ma shugabancin da Annabi ya sa Abubakar *Raliyallahu Anhu* babu wanda ya tava sa wa yin irinsa a tarihi, wato jagorancin aikin hajji. Ya kuma sa shi wani shugabancin ba wannan ba.

Malaman Sunnah da na Shi'ah gaba xaya sun haxu a kan masaniyar cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tava shugabantar da waxansu Sahabbai; waxanda darajarsu ba ta kai ta Abubakar ba, irin su: Amru xan Asi da Walidu xan Uqbata da Halidu xan Walidu. Ka ga haka na tabbatar wa mai hankali cewa, kodayake Manzon Allah bai naxa Abubakar gwamna a wani yanki na musulmi ba, amma bai yi haka don darajarsa ba ta kai ta waxannan da ya naxa ba.

Rashin naxa sarauta ba ya nuna shi ba wata tsiya ba ne. Wa ya sani ko Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi haka ne, don zamansa tare da shi zai fi amfani ga shi Annabin, bisa ga a ce yana can wata nahiya? Kuma yadda yake da buqata da shi a nan Madina, ta fi yadda yake da ita gare shi, idan yana can wurin sarauta. Kuma ai Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* matsayin mataimaka suke ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Ka ga ba buqatar su yi nisa, don da su ne ake xinkin duniyar musulunci.

## 5.11 Wai Manzon Allah ya Tuve Abubakar Daga Amirul Hajji!

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta goma sha xaya ita ce, tuve Abubakar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi daga aikin sa da ya yi ya isar da Suratu Bara'ati, ya maye gurbinsa da Ali.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Ka ko ga duk wanda ya kasa iya xaukar nauyin isar da sura xaya ko sashenta, ya za a yi ya dace da shugabancin qoli,

wanda ya tattara nauyin isar da hukunce-hukunce zuwa ga gaba xayan al'umma?!

**Martani:**

Kan ma'abuta ilimi ya haxu a kan cewa wannan magana qarya ce.

Yadda al'amarin yake kuwa shi ne: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya naxa Abubakar *Raliyallahu Anhu* don ya jagoranci aikin hajjin shekara ta tara. Bai kuma tuve shi ba, shi kuma bai dawo don qashin kansa ba kafin a qare. Ya jagoranci aikin a shekarar kamar yadda aka umurce shi, kuma Ali *Raliyallahu Anhu* na xaya daga cikin tawagarsa; a bayansa yake sallah, ba ya wani motsi sai da izinin Abubakar xin. Idan kuma ya hana shi qetara kara ba zai yi ba, ko ba ya kusa. Haka kuwa sauran waxanda ke tare da shi suka kasance.

Wannan shi ne sanannen abu kuma mutawatiri a wurin ma'abuta ilimi. Ba a sami ko da mutum biyu daga cikinsu ba, waxanda kalmominsu suka sava a kan cewa Abubakar ne *Raliyallahu Anhu* ya jagoranci wannan aikin a wannan shekara. To, ta yaya yau da rana tsaka wani zai gaya mana cewa wai an tuve shi?

Gaskiya ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tura Ali ya iske Abubakar *Raliyallahu Anhu* can don ya shedi warware alqawarin da ke tsakanin musulmi da mushrikai. Dalilin yin haka kuwa shi ne, babu lokacin da za su qulla ko su kwance alqawari da wata qabila daga cikinsu, face akwai wani mutum daga cikin qabilar wanda zai tabbatar da haka, kuma ba su yarda da waqilcin kowa.

Babu shakka wannan xan Shi’ar, kamar sauran malamansa, sun fi kowa jahiltar tarihin Manzon Allah da abubuwan da suka tuzgo daga gare shi na qashin kansa, da waxanda yau da gobe ta wajabta masa. Alhali kuwa ko kurtu a fagen ilimin tarihi ya san waxannan abubuwa, don inganci da bayyanarsu ya kai matuqa. Amma duk da haka sai ‘yan Shi’ah su yi wa al'amurran shan koko; su rage abin da suke so, su qara wanda suke so.

Duk da yake shi wannan xan Shi’ar sawun varawo ne ya taka; ko da aka haife shi shehunansa sun riga sun yamutsa hazo a fagen tarihin musulunci. Shi kuma da ya zo sai kawai ya hau ba tare da ya tankaxe ya rairaye ba, balle ya kai ga tsagwaron gaskiyar da ma'abuta ilimi manya da qanana suka sani a yanke.

Ita kuwa cewar da xan Shi’ar ya yi, shugabancin qoli ya tattara nauyin isar da gaba xayan hukunce-hukunce ga al'umma, magana ce vatatta. Ai al'umma sun riga sun gama naqaltar hukunce-hukuncen addini daga bakin Annabinsu *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Ba wata buqata da suke da ita ga shugaba, face irin wadda suke da ita ga malamai takwarorinsa. Babu kuma wani daga cikin musulmi da ba zai iya isar da saqon wata sura ta Alqur’ani daga Manzon Allah ba, balle a ce Sahabi guda irin Abubakar *Raliyallahu Anhu* wai bai isa a sa shi isar da irin wannan saqo ba. Ba ya kamata, balle ya halatta,

wani ya zaci cewa, ba wanda Annabi ke iya aikawa ya isar da saqon wata sura ta Alqur'ani sai Ali. Ai riwayar wani sashe na Alqur'ani ba ta tabbata da inganta sai ta hanya mutawatira. Amma kasancewar an ji shi daga bakin mutum xaya, ba ta wadatarwa.

**8.12 Kuma Wai Umar Bai Iya Hukunci ba!**

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta goma sha biyu ita ce, cewar da Umar ya yi: Lalle Muhammadu bai mutu ba. Wannan na nuna irin qarancin iliminsa. Ya kuma tava yin horo da jefe wata mata mai ciki. Aliyu *Raliyallahu Anhu* ya hana zartar da hukuncin. Sai umar ya ce: "Ba don Aliyu ba da Umar ya halaka". Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa, akwai hukunce-hukunce da dama da Umar ya yi kwava a cikinsu.

**Martani:**

Ya tabbata a cikin Buhari da Muslimu cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Haqiqa kowace al'umma da ta gabace ku na da waxanda ake labarta ma a cikinta. Idan akwai wani xaya a cikin al'ummata to Umar ne".

Annabi bai yi wa Ali *Raliyallahu Anhu* irin wannan sheda ba.

An kuma riwaito yana cewa: "Na yi mafarkin an zo mani da wani qoqo da ke xauke da nono, na sha har na ga kamar yana vuvvuga ta qunbar hannuna. Sai na ba wa Umar sauran abin da ya rage". Sai Sahabbai suka ce: Da me ka fassara shi ya Manzon Allah? Ya ce: "Da ilimi".

Ko shakka babu Umar shi ne mafi yawan ilimi a cikin Sahabbai bayan Abubakar *Raliyallahu Anhu*.

Amma zaton da Umar ya yi cewa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai rasu ba, ai wani abu ne na xan lokaci. Daga baya ta bayyana gare shi cewa ya rasu. Da yawa kuma irin hakan kan faru ga wasu mutane; su yi zaton wani bai rasu ba, daga baya kuma da kamar awa xaya ko fiye ta tabbata cewa ya rasun. Shi kansa Sayyidina Ali *Raliyallahu Anhu* akwai al'amurra da dama da haqiqarsu ta bayyana gare shi savanin yadda ya xauke su a farko, fiye da yadda wannan ta faru ga Umar. Akwai ma kai, hukunce-hukunce da dama da ya yi wa gurguwar fahimta, har kuma ya rasu yana kanta. Amma wannan bai sa aka ce shugabancinsa ya gurgunta ba. Kamar fatawar da ya yi a kan matar da aka xaura ma aure a kan bashi, kuma har ta mutu ba a yanka mata sadakin ba. Da wasu mas'aloli masu kama da haka, sanannu a wurin ma'abuta ilimi.

Ita kuwa mai cikin can, dama tun farko Umar bai san tana da shi ba. Saboda haka ya yi umurni da jefe ta don ta yi zina. Ganin haka sai Ali ya faxakar da shi. To, a kan haka ne ya ce: Ba don Aliyu ya gaya min tana da ciki ba da na sa an jefe ta. Da na kashe abin da ke cikin ta ba da sani ba.

Wannan shi ne  abin da umar ya ji ma tsoro.

Kuma duk aje wannan. Ai ba abin kunya ba ne mutun ya qaru da wani ilimi daga bakin wanda ya fiya xaukaka da sani. Domin kuwa ai Annabi Musa *Alaihis Salamu* ya qaru da sanin wasu mas'aloli guda uku daga Haliru *Alaihis*

*Salamu*. Haka kuma Annabi Sulaiman *Alaihis Salamu* ya qaru da sanin labarin Balkisu daga bakin Hudahuda.

**8.13 Wai Umar ya Qago Sallar Asham**

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta goma sha uku ita ce kasancewar Umar wanda ya qago sallar Asham a cikin jam'i, bayan kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Ya ku mutane! Ku sani, yin sallar nafila a cikin jam'i, a daren watan Ramadana bidi'a ne. Kuma sallar walaha bidi'a ce. Kuma komai qanqancin Sunnah ta fi zama alheri bisa ga bidi'a kome yawanta. Kuma ku saurara! Kowace bidia'a vata ce. Kuma kowace vata godabenta na zuwa wuta".

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Amma duk da wannan magana ta Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai ga Umar ya fito watarana da dare, a cikin watan azumin Ramalana ya ga fitilu sun haskake masallatai. Ya ce: Mene ne haka? Aka ce masa: Ai mutane ne suka taru don yin sallar alkareji, sai ya ce: Bidi'a ce, amma madallah da ita.

**Martani:**

Abin da za mu ce a nan kafin martani shi ne, ba a tava samun qungiya daga cikin qungiyoyin bidi'a da vata, wadda ta kai ga qungiyar 'yan Shi'ah tsananin rashin kunya da qarya ga Manzon Allah ba, da aron bakinsa a ci masa albasa. Duk da yake a cikinsu, akwai waxanda ba su san abubuwan da qungiyar tasu ke kai qarya ne ba. Jahilcin irin waxannan kuwa ya wuce la haula.

To, sai martani. Kamar kullum muna cajin marubucin ba samar wa wannan magana tasa madogara, kuma ta zan qwaqqwara.

Shi dai wannan hadisi masana sun daxe da sa jan biro a kansa. Ko ba komai shi wannan hadisi ba shi a cikin ko xaya daga cikin kundayen hadisi na malamai na da da na yanzu.

Tabbaccen abu ne cewa, tun a zamanin rayuwar Ma'aiki *Sallallahu Alaihi Wasallama* mutane na wannan sallah. Kuma shi kansa *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya jagoranci musulmi sallar ta asham tsawon wasu kwanuka a cikin watan azumi, kuma bai daina yin wannan sallah da jama'a ba sai don abin da ya bayyana na jin tsoron a wajabta ta. Ganin haka ya sa musulmi suka ci gaba da yin abarsu bayan yankewar wahayi da cikawarsa *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Umar *Raliyallahu Anhu* ya kira wannan sallah da suna bidi'ah babu shakka. Amma ai duk musulmi sun fahimci abin da yake nufi da kiran ta bidi'ah in ban da 'yan Shi'ah. Wannan shi ya sa ma suke yin ta a duk faxin duniyar musulmi.

A qa'idar harshen Larabci, duk abin da aka fara gudanarwa ko yi, sunansa bidi'ah ba tare da kula da hukuncinsa ba. Ita kuwa bidi'ar da shari'a ta qyamata, ita ce abin da aka aikata ba bisa wani dalili na shari'ar ba. Irin wannan bidi'ah ita ce vata. Kuma ba ita Umar yake nufi ba.

In da haxuwa a cikin masallatai don gudanar da sallar asham abu ne da shari'a ta qi, da Ali ya hana shi a lokacin da ya zama Sarkin Musulmi. Amma kasancewar ya ci gaba da abin da shi Umar xin ya tabbatar, ta nuna cewa abu ne mustahabbi. Kai, an ma riwaito daga bakin Aliyun yana cewa: "Allah ya haskaka qabarin Umar kamar yadda ya haskaka masallatanmu da sallar alkareji".

**8.14 Wai Musulmi Sun Haxu a Kan Kashe Halifa Usman!**

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta goma sha huxu ita ce: haxuwar kan gaba xayan musulmi a kan kisan halifa Usman fiye da yadda suka haxu a kan shugabancinsa da na Abubakar da Umar. Wai, saboda ya aikata wasu abubuwa da ba su halatta ba.

**Martani:**

Tabbas, wannan magana qarya ce shahararra. Babu wani mutum a birnin Madina, da sauran biranen musulunci da bai goyi bayan shugabancin Usman, suka yi masa mubaya'a ba. A kan haka ne ma Imamu Ahmad da wasu malamai suka ce, haxin kan da aka samu a kan halifancin Usmanu ba a same shi a kan sauran ba.

Su ko waxanda suka kashe halifa Usman wasu 'yan tsirarun mutane ne. Ga abin da xan Zubairu yake cewa a kai: "Sun mamayi Usmanu kamar yadda 'yan fashi ke yi daga wajen gari. Qarshe Allah ya sa aka samu sa'ar kashe mafi yawan su, saura kuma suka sulale cikin duhun dare".

To, kuma wani abu mai jan hankali a nan shi ne, yawan waxanda suka yi allawaddai da Ali *Raliyallahu Anhu*; suka yaqe shi, sun ninka waxanda suka kashe Usmanu yawa nesa ba kusa ba. Qarewa da qarau ma, an samu wasu daga cikin sojojin Aliyu xin da suka yi masa tawaye, suka kafirta shi; suka ce masa: "Ka fita musulunci. Saboda haka ba za mu sake yi maka biyayya ba sai ka sake musulunta". Daga qarshe kuma suka zamo ajalinsa.

Dubun dubatar hanyoyi da riwayoyi sun tabbatar da cewa, kan gaba xayan musulmi ya haxu a kan yi wa Usmanu mubaya'a; babu wani daga cikin musulmi da ya zama saniyar ware. Savanin mubaya'ar Abubakar Siddiqu, wadda aka sami Sa'adu xan Ubadata ya kafa kai a qasa ya ce, ba zai yi ba. Haka kuwa ta tabbata, domin tarihi ya tabbatar da cewa, har wannan Sahabi ya kwanta dama bai haxa hannu da Abubakar *Raliyallahu Anhu* da sunan mubaya'a ba. Har halifa Umar wannan Sahabi bai yi wa mubaya'a ba, wanda a lokacin halifancinsa ne Allah ya karvi rayuwarsa.

Sa'adu xan Ubadata bai qi yi wa Abubakar mubaya'a don wata illa da yake gani a cikin yin hakan ba, ba a kuma tava jin wata mugunyar magana ta fito daga bakinsa zuwa gare shi ba, bai kuma tava musa cewa, halifan shi ne mafificin daraja a cikin gaba xayan Sahabbai ba. Abin da ya faru ai shi ne, ya nemi ayi halifofi biyu; xaya daga cikin Ansaru, xaya kuma daga cikin Muhajiruna. Hakan ta ci tura, shi kuma ya cije.

Nassin da Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya kafa hujja da shi wanda ya kixe shawarar Sa'adu, in da ya ce: "A zavi shugabanni daga cikin Quraishawa", nassi ne tabbatacce. An samo ta hanyoyi da dama cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce haka. Ka ga ra'ayin da Sa'adu ya riqa kuskure ne. Sa'adu *Raliyallahu Anhu* kuwa ya zaci ra'ayinsa daidai, zato kuwa ba ya kawar da haqiqa. Kenan qin yin mubaya'ar da ya yi ba daidai ba ne.

Ita ko mubaya'ar da aka yi wa Usmanu, duk da kasancewar musulmi a lokacin sun yawaita sosai, sun kuma watsu a birane da karkaru. Wannan duk bai hana qwansu da kwarkwatarsu yi masa mubaya'a ba. Amma in da gizo yake saqa duk bai fi halifancin Ali ba. Da yake qaddara ta riga fata, sai aka sami kusan rabin musulmi a lokacin suka qi yi masa mubaya'a. Kuma da ya soma yaqi da mutanen Sham, al'umma mai xinbin yawa, har daga cikin waxanda suka yi masa mubaya'a xin suka canza sheqa zuwa wurin Mu'awiyah kamar xan'uwansa Aqilu da makamantansa. Har kwanan gobe kuwa, magoya bayan halifa Usmanu masu sukar lamirin Ali na kafa hujja da wannan a kan cewa, bai karva sunan halifa ba. Amma tattare da haka, hujjarsu ba ta xara ta 'yan Shi'ah da kome ba. Hujja ce mai raunin gaske wadda ke tabbatar da cewa, kisan da aka yi wa Ali na gilla ne. In ko haka ne, to, ina ga kisan da aka yi wa Usman?

## 9.0 Zango Na Tara
## Rashin Cancantar Abubakar ga
## Halifanci a Wurinsu

### 9.1 Rashin Samun Ijma'i a Kansa

Xan Shi'ar ya ce: Fasali na Shida mai kore hujjojin Ahlus-Sunnah a kan shugabancin Abubakar. Ya ce: Sau da yawa sukan ce wai kan musulmi ya haxu a kan shugabancinsa. Amsata a nan zuwa gare su ita ce, babu wani haxin kan da aka samu a kan haka. Domin kuwa, inji xan Shi'ar, wasu mutane daga cikin bani Hashim, da manyan Sahabbai, irin su Salmanu da Abu Zarri da Miqdadu da Ammaru da Huzaifatu da Sa'adu xan Ubadata da Zaidu xan Arqamu da Usamatu xan Zaidu da Khalidu xan Sa'idu xan Asi da xan Abbas, duk waxannan ba su goyi bayan zaman Abubakar halifa ba.

Kai, hatta da mahaifin Abubakar xin bai goyi bayansa ba. Don a lokacin da ya ji labarin cewa, an naxa halifa, cewa ya yi, wa aka naxa? Aka ce masa: "Xanka". Sai ya ce, ya 'yan bayin Allan nan biyu suka yi? Yana nufin Ali da Abbas. Aka ce masa, ai duk lokacin da ake hidima su suna can suna xawainiyra jana'izar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, sun kuma yarda da kasancewar xanka mafi yawan shekaru daga cikin Sahabbai. Wai sai ya ce, ni na tsofe masa.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Kuma gaba xayan banu Hanifata ba su yarda da shugabancinsa ba. A kan haka ne ma suka qi kai masa zakkah. Hakan ta sa ya jefe su da kalmar riddah, a qarshe kuma ya yaqe su, ya ribace su. Umar *Raliyallahu Anhu* ya qalubalance shi a kan haka, kuma bayan zamansa halifa ya mayar masu da gaba xayan mutanensu da dukiyarsu da aka ribata. Duk inji xan Shi'ar.

### Martani:

muna godiya ga Allah da ya nuna wa duniya cewa, da waxancan mutane da suka yi ridda, da waxannan 'yan Shi'ar xan juma da xan jumai. Malamai da almajirai kowa ya tabbatar da haka. Wanda ke da shakka ko sassauci a kan haka can da, to, yau kansa ya waye. Allah ya tona wa 'yan Shi'ah asiri, sun bayyana da bakinsu. Qiyayyar da suke yi wa Allah da Manzonsa da zavavvun bayin Allah da masoyansa ta bayyana. Haka kuma Allah zai ci gaba da tona masu asiri domin kuwa duk wanda Allah ya saukar wa fitina, ba wani mai iya kare shi.

Duk wanda ke da masaniya da tarihin musulunci, da zarar ya ji wannan magana zai yanke xayan hukunci biyu ne; ko dai mai faxinta ya kasance mafi jahilcin mutane da tarihin Sahabbai, ko kuma duk ya fi su qarfin halin faxin qarya. Amma ni, a zatona, jahilci ne ke damun wannan marubuci da sauran 'yan Shi'ah. Don haka suke cirato duk tunkuvar da suka ci karo da ita a cikin littafan magabatansu.

Mafi girman jahilci da vatan da ke cikin wannan magana duk bai fi sanya banu Hanifata da ya yi ba a matsayin mutanen kirki waxanda ke iya cika sahun musulmi har a kira haxuwarsu ijma'i. Kuma wai, sai bayan da suka qi yin bai'a ga Abubakar ne suka kuma qi kai masa zakkah lokacin ne ya raxa masu sunan *Ahlur Riddah* ya kuma yaqe su, ya ribace su. Alhali kuwa babu wanda bai san cewa, banu Hanifata sun karva kiran Musailamatul Kazzabi ba, a lokacin da ya yi da'awar annabta a qasar Yamamata.

Wannan al'amari na da'awar annabta da Musailamatu ya yi da biyarsa da banu Hanifata suka yi, abu ne da yake zahiri, ya kuma fi qarfin wani abu ya hana a san shi. Yaqar banu Hanifata kuma da sauran waxanda suka yi ridda da halifa Abubakar ya yi, na xaya daga cikin girman darajojinsa a idon na farko da na qarshen wannan al'umma. Su kuwa banu Hanifata su ne mafi girman waxanda suka yi ridda a tarihin musulunci a wancan lokaci. Kuma halifan bai yaqe su a kan sun qi fitar da zakkah ba. Ya dai yaqe su ne saboda sun karva kiran Musailamatu. Kuma yawansu kamar yadda ake faxa zai kai kusan mutum dubu xari.

Wani kuma abin da ke tabbatar da kasancewarsu ba musulmi ba, shi ne wata kuyanga wadda aka kamo daga cikinsu wadda Ali *Raliyallahu Anhu* ya sa xaka, wato Haulatu xiyar Jafar al-Hanafiyyah mahaifiyar Muhammadu ii. A kan wannan aiki na sayyidina Ali, wasu malamai suka kama matan da suka yi ridda a sa su xaka. Domin da a ce banu Hanifata musulmi ne masu alfarma da kiyaye ta ke wajaba, Ali ba zai sa xaya daga cikin matansu xaka ba ballantana ya sadu da ita har a haifi Muhammadu ii ba.

Haka nan ita ma cewar da xan Shi'ar ya yi, wai Umar ya qalubalanci Abubakar a kan yaqin riddah, qarya ce babba. Domin kuwa Sahabbai kacokam sun yi ittifaqi a kan yaqar Musailamatu da jama'arsa. Amma akwai wata qungiya daga cikin qabilar wadda ke waqar ita musulma ce, amma kuma suka qi fitar da zakkah. Wannan qungiya ce a farkon al'amari Umar ke ganin bai kamata yaqi ya haxa da su ba. Ya ci gaba da nacewa a kan wannan ra'ayi nasa har sai da Abubakar Siddiqu ya lurar da shi, ya kuma tabbatar masa da wajabcin yaqarsu, sannan ya yarda ya ba da gari. Wannan qissa sananna ce.

To, mu qaddara ma wannan yaqi an yi shi ne da manufar karvo Zakkah, kuma hakan ta zamo abin kunya gare su, to, abin kunyar zai fi sauqin tabbatuwa a kan wani wanda ba su ba. Idan ya wajaba a ba Ali uzuri a kan yaqinsa, to, ba Abubakar da Umar uzuri ya fi zama dahir. Domin kuwa yaqe-yaqen da Ali ya yi, ya yi su ne don a yarda da shugabancinsa, ya ci gaba da mulki a kan rayuka da dukiyoyin musulmi. To, ta ya ya za a ce yaqe-yaqe na addini ne, amma waxanda Abubakar ya yi, bayan an yarda da shugabancinsa ba addini ba?

Su kuwa manyan Sahabban da xan Shi'ar ya ce, sun qi yi wa Abubakar bai'ah, har da lissafa sunayensu xaya bayan xaya, qarya ce yake yi musu idan ka cire Sa'adu xan Ubadata. Su kuwa sauran, mubaya'ar da suka yi wa Abubakar da Umar ta fi qarfin wani ya musa ta. Domin kuwa gaba xayan

masana hadisi da iliminsa, da masana Sirah da nagartattun zantuka, da sauran dangogin ma'abuta ilimi na jiya da yau, sun yi ittifaqi a kan wannan bai'ah. Saboda ma tsananin yarda da gamsuwa da shugabancin Abubakar da Usamatu xan Zaidu ya yi, shi ya sa wa Abubakar laqabin *Halifatu Rasulillahi.* Iyakar sunan Abubakar kenan a bakin Zaidu. Ya kuma yi masa wannan suna ne gaf da za shi fita zuwa yaqi.

Haka kuma gaba xayan waxanda xan Shi'ar ya ambaci sunayensu, babu wanda bai yi wa Abubakar bai'ah ba. Sai dai shi Khalidu xan Sa'idu ne koda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wafati yana gwamna, amma sai ya ce: Wakilcin da na yi wa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya isa, ba zan iya zama wakilin wani bayansa ba. Nan take kuma ya yi murabus, kuma Abubakar ya karvi murabus xinsa. Kuma ko shakka babu, Khalidu na daga cikin Sahabban da suka yarda da halifancin Abubakar. Abin da kawai ya tabbata daga bakunan da ba sa qarya shi ne, baya ga Sahabi Sa'adu xan Ubadata babu wani Sahabi; babba ko qarami wanda bai yi wa Abubakar mubaya'a ba.

Duk da kasancewar mubaya'ar Ali ga Abubakar ta xan so ta sami 'yar tangarxa, malamai sun yi ittifaqi a kan cewa, ya dai yi masa mubaya'ar. Haka ma bani Hashim babu mutum xaya daga cikinsu da bai yi mubaya'a ga Abubakar ba. Wasu dai suna cewa ne, Ali bai yi mubaya'ar ga Abubakar ba sai bayan wata shida. Wasu kuma suka ce wan shekara. Ala ayyi halin dai sun yi masa ba a kan tilastawa.

Haka kuma gaba xayan mutane sun yi wa Umar bai'ah idan ka cire Sa'adu. To, uwa uba Usmanu. Shi ba a sami mutum xaya da ya ce ba da shi ba a cikin bai'arsa.

Haka shi ma duk abin da xan Shi'ar ya faxa dangane da Abu Quhafata, mahaifin Abubakar, malamai sun yi ittifaqi akan zamansa qarya. Amma dai yadda haqiqanin abin ya ke shi ne, Abu Quhafata tsoho ne tuguf. Yana kuma zaune ne a garin Makkah. Ya musulunta ranar da aka buxa garin, kuma daga bisani Abubakar ya zo da shi wurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ga yadda kansa da havarsa suke taf da farin gashi kamar taffa, sai ya ce: "Ai da ka bar wannan dattijon gida sai mu same shi can". Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi haka ne kuwa don girmamawa ga Abubakar.

Don haka, cewar da xan Shi'ar ya yi wai, Sahabbai sun ce wa Abu Quhafata, lalle xanka shi ne mafi yawan Sahabbai ga shekaru, qarya ce zaharan. Sahabbai irin su Abbas *Raliyallahu Anhu* sun tsofe ma Abubakar.

Maganar kore ijma'in da xan Shi'ar ya yi a kan halifancin Abubakar, ba ta samun gindin zama a fagen ilimi, bisa ga dalilai kamar haka:

1. Duk waxanda xan Shi'ar ya kawo in banda Sa'adu xan Ubadata sun yi mubaya'ar. Haka kuma mun ga yadda wata qungiya daga cikin banu Hashim suka qi yin mubaya'ar a farkon al'amari, amma bayan wata

shida ta yi ba tare da an tilasta ta ba, ko don tsoron wani abu ko kwaxayin wani.

Rashin mubaya'ar mutum xaya ko wata qungiya 'yar tsurut, ba zai rage ijma'in da ake buqata a tabbatar da shugabancin shugaba da komai ba. Shugabanci wani al'amari ne na wajibi. Kuma abu ne mai sauqi qwarai wani ya qi goyon bayan wani a kai, saboda wani abu da yake kimshe a cikin ransa. Kamar yadda ya faru ga Sa'adu.

2. Ko da mun qaddara cewa, gaba xayan Sahabban can da xan Shi'ar ya zana, ba su yi wa Abubakar bai'a ba. Kai ko da yawansu ya xara hakan can sau biyu, hakan ba zata hana shugabancin Abubakar tabbata ko karva sunansa ba. Domin kuwa haxin kan da ake nema a cikin sha'anin shugabanci, shi ne na manyan mutane, irin waxanda ba a qulla kome ko kwance shi, sai tare da su. Su ne kuma jama'ar da ake nufi da hadisin da ya zo daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Na hore ku da shiga jama'a, domin hannun Allah na tare da su".

3. Ijma'in da al'umma suka yi a kan yarda da amincewa da halifancin Abubakar ya fi wanda suka yi a kan yi wa Ali mubaya'a, nesa ba kusa ba. Domin kuwa kashi xaya cikin uku na al'umma ko qasa ga haka kaxan ko fiye, ba su yi masa mubaya'a ba. A maimakon haka ma, sai suka yaqe shi. A yayin da kuma kashi xaya suka sa masa ido da sha'aninsa; ba su yaqe shi ba, basu yaqi wani tare da shi ba. Akwai kuma waxanda suka yi masa mubaya'ah, an samu waxanda suka sulale suka yaqe shi. A kan haka, idan har ya halalta a yi suka ga shugabancin wanda wasu daga cikin al'umma ba su yi wa bai'ah ba, to, shugabancin Ali ya fi cancanta nesa ba kusa ba, da haka.

### 9.2 'Yan Shi'ah ba su Yarda da Ijma'i ba

Xan Shi'ar ya ce: Asalatan, Ijma'i ba ya zama dalili a tsurar ruwan zatinsa. Dole ne ya kasance waxanda suka haxu suna da wani dalili na hankali ko nassi. Ba su kuwa da ko xaya. A hankalce babu wani dalili da za su togu da shi. Kuma ko a wurinsu Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bar duniya ne ba tare da ya bar wasicci a kan wanda zai gaji halifarsa ba. Saboda haka wannan ijma'i nasu kuskure ne. koda kuwa an tabbatar da shi ba zai inganta ba. Kuma duk abin da aka gina a kansa vatacce ne, kuma rosasshe, inji xan Shi'ar.

### Martani:

Cewar da ya yi ijma'i ba ya zama dalili a karan kansa. Idan yana nufin ba ya wajaba a yi biyayya ga wani umurni da waxanda suka yi ijma'in suka bayar, sai idan xa'a ne ga Allah da Manzonsa, to, wannan gaskiya ne, kuma zance ne ingantacce. Amma kuma ya sani wannan ba zai rage mu da komai ba. Domin ko Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba ya wajaba a yi masa

xa'a ne don komai ba sai don kasancewar umurninsa na tabbatar da umurnin Allah. Biyayya ga Manzo na wajaba ne saboda yi masa ita yi wa Allah ne. haka kuma a duk lokacin da muminai suka haxu a kan wani abu karvavve ga shari'a, to, wajibi ne sauran musulmi su yi masu xa'a. domin yi masu ita yi wa Allah ne da Manzonsa. Kamar yadda a nassance yake wajibi musulmi su kai koke-kokensu ga Manzo, saboda yin haka kamar kai wa ne ga Allah. Domin shi Manzon ba ya hukunci da son zuciya; sai da abin da Allah ya saukar. To, haka al'amarin yake a cikin miqa wuya ga abin da al'umma ta haxu a kai na alheri, daidai yake da miqawa ga Allah *Subhanahu WaTa'ala.*

Idan xan Shi'ar na nufin ijma'i na iya zama gaskiya idan ya dace da nassi ko akasin haka, idan nassi bai zo da abin da ya qunsa ba. Idan haka yake nufi, kamar yadda muke kyautata zato,to, ya sani ya rosa kansa. Domin kuwa wannan manufa tasa na suka ne ga ijma'i kowane iri. Kuma kamar yana so ne ya ce, abu ne mai yiwuwa al'umma ta haxu a kan vata da kuskure.

To, ka ga kenan, muna iya ce wa xan Shi'ar, kar ya manta da cewa, sun tabbatar da kasancewar Ali halifa kuma ma'asumi, da wasu abubuwa masu kama da wannan na shikashikan Imamiyyah ne, ta hanyar ijma'i. sanannen abu ne cewa, ba su da wata manufa a ginshiqan addininsu kamar yadda suke faxa da bakunansu, wadda ta fi hankali da ijma'i, waxanda riwayoyin da suka yo ke take wa baya.

A duk lokacin da suka tashi irin wannan magana, sukan ce, a hankalce, dole ne ya kasance mutane na da shugaba kuma ma'asumi, wanda nassi ya tabbatar. Sai su ce kuma, kan malamai ya haxu a kan cewa, babu wani ma'asumi mai irn wannan siffa sai Ali. da irin wannan kwancikwalato ne suke qoqarin tabbatar da hujjojinsu.

Tun daga nan muna iya ce masu, idan dai har ijma'i ba ya zama hujja, to, duk hujjojin da kuka kafa a kanshikashikan addininku ta hanyar ijma'i sun sha qasa.

Da kuwa xan Shi'ar zai dawo ya ce, sun yarda da kasancewar ijma'i hujja, to, hakan zata qara tabbatar da mazhabar Ahlus-Sunnah ne kawai. Ka ga yardarsu ko rashin ta da kasancewar ijma'i hujja duk xaya.

Idan kuma xan Shi'ar ya ce, ai mu bamu tava godogo da ijma'i ba, balle mu kafa shi hujja a kan wani abu na shikashikan mazhabarmu. Abin da kawai muke dogara a kansa shi ne hankali da abubuwan da muka naqalto daga shugabanninmu ma'asumai. To, sai mu ce masa, waxannan riwayoyin naku ma basu zama hujja don ba ku iya tabbatar da ma'asumancin wani daga cikin Imaman sai in Manzo ya yi masa shaidar haka. Tunda kuwa ba a samun wannan, to, ba sauran hujjar da ta rage maku ko guda.

### 9.3 Wai Kuma Al'umma ba ta Haxu Kan Abubakar ba!

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa, kuma ai ijma'i na karva sunansa ne da yardar gaba xayan al'umma. Sanannen abu ne kuwa, hakan ba ta faru ba. Kan

gaba xayan mutanen Madina ko wani yanki nasu bai haxu a kan haka ba. Kuma ta tabbata cewa, kan mafi yawansu ya haxu a kan kashe Usman.

**Martani:**

Zancen haxuwar kai a kan shugabanci. Idan marubucin na nufin irin haxuwar kan da shugabanci ba ya iya tabbat sai da shi. To, ai ana nufin haxin kan mutane masu qarfi ne da yardarsu kawai. Ta yadda tare da goyon bayansu shugaba zai iya zartar da manufofin shugabanci, koda kuwa yawansu bai fi yatsun hannu ba. Matuqar dai sauran jama'a na shaya masu, to, koda su kaxai suka yi wa shugaba bai'a ta tabbata. Wannan shi ne abin da Ahlus-Sunnah ke kai. Ita ce kuma mazhabar manyan malaman musulunci irin su Ahmad xan Hambali.

Wannan hukunci bai haxa da zaqaquran magana ba, *Ahlul Kalam.* Su a nasu gani akwai adudda daban-daban da kowanensu ke ganin sai bai'ah ta samu kafin ta karva sunanta. Wannan aiki nasu kuwa shuka ce bisa kan faqo.

Idan kuwa xan Shi'ar na nufin ijma'i na haxuwar kai a kan cancantar wane, ko duka sun cancanta, amma wane ne ya kamata ya kasance farko, saura su biyo baya. To, abu biyu ake la'akari da su a cikin irin wannan. Ko dai haxuwar kan gaba xayan al'umma ko ta mafi yawa. Idan ka haxa da amincewar masu gari, abubuwan sun zama uku kenan. Babu kuwa wanda halifancin Abubakar bai samu ba.

Shi kuwa Usman wani yanki ne na mutane kawai suka haxa kai a yi masa kisan gilla. Yawansu daga cikin al'umma bai taka kara ya karya ba.

**9.4 Wata Suka ga Ijma'i**

Xan Shi'ar ya ce, babu wani daga cikin Sahabbai da ya fi qarfin yin kuskure. Domin ba su da wata alfarma da ke iya kare su daga faxar abin da ba gaskiya ba a lokacin da suke zartar da wani hukunci.

**Martani:**

Sanannen abu ne cewa, a duk lokacin da mutane suka haxu a kan wani abu, to, wata siffa ta samu gare su, wadda babu ta ga xaixaikunsu. Saboda haka ne ma ba ya halatta a daidaita hukuncin mutum xaya da na taron jama'a. domin kuwa a duk lokacin da mutane suke xaixaice, to, yana yiwuwa qwarai a taras da wani kuskure ko qarya, ya tusgo daga bakin xayansu. Amma a duk lokacin da kansu ya haxu yana da matuqar wahala kuskure ko qarya su fito bakinsu, a matsayinsu na masu magana da harshe xaya.

Idan kuwa har tana yiwuwa kan jama'a ya haxu a kan kuskure, to, zancen tabbatar Ali ma'asumi, kamar yadda 'yan Shi'ah ke gani, ya tashi. Domin kuwa ta hanyar ijma'i ne suka gano cewa, shi ma'asumi ne. kuma idan sharaxin yiwuwar kasancewar ijma'i kuskure ya tabbata, kenan tana yiwuwa qwarai ya kasance akwai wani ma'asumi a cikin al'umma ba Ali ba. Magana ta qare.

Ka ga kenan wannan suka da xan Shi'ar ya yi ta rosa gaba xayan abin da suka dogara a kansa na kasancewar shugaba ma'asumi. Da zarar kuwa ma'asumancin Ali ya roshe, to, mazhabar Shi'ah ta bi ruwa kenan. Haka kuma ko yarda suka yi da kasancewar ijma'in hujja, ba za ta hana ruwan ya cinye mazhabar tasu ba. Duk yadda aka kaxa ko aka raya dai, mazhabar tasu sai labari.

### 9.5 Kuma Wai Zaven Abubakar ya Sava ma Nassi

Xan Shi'ar ya ce: Mun riga mun bayyana nassin da ya tabbatar da shugabancin Sarkin Musulmi Ali. duk kuwa waxanda suka riqi ijma'i suka bar wannan nassi sun yi kuskure. Domin kuwa duk abin da aka haxu a kansa savanin abin da nassi ya qunsa, aikin banza ne.

### Martani:

Mun riga mun warware duk wata magana da ke cewa, dole ne Ali ya zama halifa kafin halifofi uku da suka gabace shi. Domin kuwa gaba xayan nassosan da suka tuzgo a kan shugabanci na tabbatar da halifancinsu ne kafin shi. Kuma amon ijma'i a kan haka ya game duniya. hujja ne kuma yankakka, ba naji-naji ba. Musamman kuma da aka sami nassosa da dama suka mara masa baya. Da wani labari zai tuzgo ya tunni wannan ijma'i, to, sai a tuhumce shi don ya tabbata zakka. Lalle ne kuma a qarshe a taras cewa, labarin qanzon kurege ne.

A qa'ida, ba ta yiwuwa ingantaccen nassi ya ci karo da lafiyayyen ijma'i. domin kuwa kowanne daga cikinsu hujja ce yankakka. Su kuwa yankakkun hujjoji, amanar da ke tsattsage da cikannansu ta dalilai da ke tabbatar da ingancinsu ba su bari su yi kabra da juna. Da wata 'yar hayaniya za ta faru tsakaninsu sai dai a sasanta su amma ba dai rabuwa ba.

Ta tabbata cewa, ingantaccen nassi da lafiyayyen ijma'i duk sun tabbatar da halifancin Abubakar. Shi kuwa nassin da 'yan Shi'ah ke cewa akwai a kan halifancin waninsa, tuni gayya ta qare aiki kansa; mun gama gane qarya ce a cikin ruwan sanyi. Muna kuma da dalilai masu yawa da ke tabbatar da haka.

### 9.6 Suka ga Hadisin Koyi da Abubakar da Umar

Xan Shi'ar ya ce: Hujja ta biyu ita ce: Abin da suka riwaito daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa, wai, ya ce: "Ku yi koyi da mutum biyu bayana: Abubakar da Umar".

Ya ce: Babu wanda ya riwaito wannan hadisi. Koda kuwa ta tabbata an riwaito shi, to, ba ya nufin mutanen biyu su zama halifofi bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. domin kuwa koyin da ake yi da malaman fiqihu bai tilasta kasancewarsu halifofi. Kuma ma ai Abubakar da Umar sun sassava a cikin hukunce-hukunce da dama, ta yadda ba ya yiwuwa a yi koyi da su baki xaya. Ga shi kuma hadisin ya ci karo da wani hadisin da suka riwaito inda suka

ce Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Sahabbaina kamar taurari su ke; duk wanda kuka koyi yi da shi kun shiriya”. Amma kuma duk da haka kan al’umma bai haxu a kan cancantar gaba xayan Sahabban da shugabanci ba.

**Martani:**

Kan gaba xayan malaman hadisi ya haxu a kan kasancewar hadisi na farko mafi qarfi a kan hadisin da ‘yan Shi’ah ke ta waqen akwai game da shugabancin Ali. Hadisin abu ne sananne, da littafan malaman hadisi da ake dogaro da su irin su Abu Dawuda da Tirmidhi da Ahmad sun riwaito shi.

Amma nassi a kan shugabancin Ali babu wani malami da ya riwaito shi. Kai qarewa ma dai, masana hadisi sun yanke masa hukuncin rashin asali. Akan haka ne ma baban Muhammad Ibnu Hazam yake cewa: Ba mu tava samun wata riwaya a kan wannan nassi da ake waqe ba, face mun taras da ita wofintacciya. Kuma ba a san wanda ya riwaito ta ba sai wani baqon haure a cikin riwayar hadisi, wai shi Abul Hamra’i.

A haka, babu dalilin da zai sa ayi qarfin halin yin suka ga wannan hadisi na koyi da Abubakar da Umar a daidai lokacin da ake qoqarin inganta wancan nassi da ake waqen akwai a kan halifancin Ali.

Tabbas, akwai dalili a cikin wannan hadisi da ke tabbatar da shugabancin waxannan Sahabbai biyu. Domin cewa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi, a yi koyi da mutum biyu bayansa. Ka ga hakan ta tabbatar da cewa, daga shi sai su. Ya kuma yi umurni da a yi koyi da su. Da kuwa su azzalumai ne ko kafirai, *Wal iyazu billahi* ba zai yi horo da ayi koyi da su ba. Har abada azzalumi ba zai cancanci zama abin koyi ba, saboda Allah Ta’ala ya ce:

﴿لَا يَنَالُ عَهۡدِي ٱلظَّٰلِمِينَ ١٢٤﴾ البقرة: ١٢٤

*Alqawarina ba zai sami azzalumai ba. 2:124.*

Da yake Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi umurni da koyi da su, ya kuma ba da labarin kasancewarsu a bayansa, wannan ya zamo hujja a kan cewa, su halifofi ne nagartattu kuma abin koyi a bayansa.

Ita kuwa cewar da xan Shi’ar ya yi wai, Abubakar da Umar sun sassava a cikin hukunce-hukunce da dama, don haka ba ta yiwuwa a yi koyi da su a lokaci xaya. Wannan magana ba gaskiya ba ce. Tarihi ya tabbatar da cewa, ba a tava jin bakunansu sun sava a kan wani hukunci savawa ba. Sai dai xayansu ya kasance reshe a kan xaya, ta yadda zai kaxaita da riwayoyi biyu; xaya tasa, xaya kuma ta xayan. Hakan ma kan faru ne kawai a cikin wasu ‘yan taqaitattun abubuwa kamar hukuncin gadon kaka tare da ‘yan’uwan mamaci. Umar na da riwayoyi biyu akan wanna mas’ala, amma xaya zancen Abubakar ne.

Ita kuwa cewar da ya yi, wai, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: “Sahabbaina kamar taurari suke..” hadisi ne mai rauni. Imamul Bazzar ya ce: Wannan hadisi bai inganta daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi*

*Wasallama* ba. Kuma ba ya cikin kowane littafi na hadisi da ake dogaro a kansa. Kuma a hadisin babu lafazin "a bayana" wadda ta zo a wancan hadisin. Ka ga kenan, koda ya inganta ba maganar halifanci yake yi ba.

### 9.7 Wai Hijirarsa Tare da Annabi ba Daraja ba ce!

Xan Shi'ar ya ce: Dalili na uku shi ne: Abubuwan da suka tuzgo na darajojin Abubakar, kamar ayar da ta sauka a kan zamansu tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin kogo, da kuma cewar da Allah Ta'ala ya yi: *Kuma mafi taqawa zai nisance ta 92:17.* Da kuma inda yake cewa: *Ka ce wa waxanda aka bari daga qauyawa za a kira ku zuwa ga waxansu mutane masu tsananin yaqi.. 48:16* Sai Ahlus-Sunnah suka ce wai, Abubakar ne zai yi kiran. Kuma ya kasance tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin dabi ranar yaqin Badar, ya kuma ciyar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Shi ne kuma wanda Annabin ya gabatar don ya yi wa mutane sallah a madadinsa.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Babu wata daraja ko fifiko da Abubakar zai kevanta da su, don ya kasance tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin kogo. Domin kuwa abu ne mai yiwuwa ya tafi da shi ne don kada asirinsa ya tonu. Haka kuma ita waccan ayar da ake kafa hujja da ita akan falalarsa, malamai ba su fahimce ta daidai ba. Ai ayar tana qoqarin fitowa da nakkas xin Abubakar ne. domin cewar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi, "kar ka sami damuwa". Hakan na nuna irin fargaba da qarancin haqurin da yake da su da kuma rashin yaqini da Allah Ta'ala. Bai kuma gamsu da kasancewa kafaxa-da-kafaxa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin wannan hali ba. Bai kuma karvi hukuncin Allah da qaddararsa ba. Abin da zai tabbatar maka da hakan inji xan Shi'ar, shi ne, da a ce damuwar da Abubakar ya samu, ya same ta ne saboda Allah da Annabi bai yi qoqarin raba shi da ita ba. Idan kuwa ya raba shi da ita ne, don ya raba shi da savon Allah, to, abin da Ahlus-Sunnah ke son tabbatarwa da ayar na falala da xaukaka ya zama qasqanci da qaranci kenan.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa, kuma ai a duk lokacin da ka ji Alqur'ani ya yi zancen saukar da natsuwa ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* to, za ka taras cewa, ya haxa har da muminai. Nan ne kawai bai ambace su ba. Wannan kuwa babbar naqasa ce da babu irinta.

Ita ko ayar da ta ce: *Kuma mafi taqawa zai nisance ta 92:17* tana nufin Abud Dahadahi ne, wanda ya saye wa maqwabcinsa wani iccen dabino. Sanadi kuwa shi ne, ya ji Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na ta fama da mai iccen ya fansar ma maqwabcin na Abud dahadahi da shi, shi kuwa Manzon ya lamunce masa wani icce a aljanna, amma mai iccen ya qi. A kan haka ya saye iccen ta hanyar musayarsa da wata qatuwar gona tasa, ya cika gurin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da shi na yin sadaqa da itaciyar ga maqwabcin nasa.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Haka nan ita ma ayar da suka kafa hujja da ita a kan kiran qauyawa zuwa yaqar wasu mutane masu qarfi, ba ta nufin Abubakar ne zai yi kiran. Allah Ta'ala na magana ne da waxanda suka qi fita yaqin Hudaibiyyah, amma da aka samo ganimar Haibara sai ga yawunsu na zuba. Sai Allah Ta'ala ya katse masu hanzari da cewa, *Ka ce ba za ku bi mu ba 48:15*. Hakan ta faru ne saboda Allah ya kevance ganimar Haibara ne saboda waxanda suka halarci yaqin Hudaibiyyah. Su ne waxanda Allah ke magana da su a waccan aya. Wato, za a kira su zuwa ga yaqar wasu mutane masu tsananin yaqin tsiya. A qarshe kuma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya gayyace su zuwa ga yaqe-yaqe da dama kamar yaqin Mu'uta da Hunainu da Tabuka da wasunsu. Ka ga kenan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne mai kiran ba Abubakar ba.

Kuma tana ma iya kasancewar mai kiran Aliyu ne. domin shi ne wanda ya yaqi hutsaye da kangararru da 'yan tawaye ya sa suka daidaita sahu. Hakan kuwa kamar ya musuluntar da su ne. Domin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Ya kai Aliyu! Duk wanda ke yaqi da kai yana yaqi da ni ne". Duk kuwa wanda ke yaqi da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* kafiri ne. Haka kuma, inji xan Shi'ar, kasancewar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin dabi a ranar yaqin Badar ba wani abin xaukaka ne ga shi Abubakar xin ba. Saboda kewar da ake cewa ya xebe ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a lokacin abu ne da hankali ba zai karva ba. Saboda kewar da yake xebewa da mahaliccinsa ta ishe shi; ba ya buqatar wani mahaluki. Abin ma kawai da ake iya fassara taren tasu da shi a lokacin duk bai fi a ce Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya zaunar da shi a wurinsa ba, don gudun ya sake maimaita ababen kunyar da ya aikata a waxansu yaqe-yaqe ta hanyar raki da gudowa. Saboda haka ne Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai hore shi da rungumar yaqi ba. Kuma ai ko alama wanda ke zaune a inwa bai kai darajar wanda ke can yana rabkewa da maza don tabbatar da kalmar Allah ba.

Ya kuma ci gaba da cewa: Ita kuma cewar da Ahlus-Sunnah suka yi wai, Abubakar ya xauki nauyin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* qarya ce. Abubakar talaka ne na qarshe; ba ya da komai, balle mahaifinsa. Saboda talaucinsa ne ma, ko abin da zai ci sai ya je yawon kwaraka a gidan Abdullahi xan Jud'an. Ka ga in da Abubakar mawadaci ne, da mahaifinsa zai fara rufa wa asiri kafin wani. Ko a lokacin jahiliyyah shi ba kowa ba ne baya ga malamin qananan yara. Bayan da musulunci ya bayyana kuma sai ya kama sana'ar xinki. Zamansa halifa ne musulmi suka hana shi wannan sana'a, sai ya ce masu, to, da me zai rayu? Sai suka yanka masa albashin dirhami uku kulli yaumin daga cikin baitil-mali.

Wani kuma dalili a kan kasancewar waccan magana ta Ahlus-Sunnah qarya, inji xan Shi'ar shi ne, Sayyida Khadijah ta riga ta yarde wa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* biyan gaba xayan bukatunsa daga cikin dukiyarta tun kafin hijira. Kuma a lokacin ba a fara yaqe-yaqe ba, balle a ce yana da

buqata da kayan yaqi da abinci mai yawa. Bayan kuma da aka yi hijira, ko veran masallaci bai yi fatarar Abubakar ba, balle ya xauki nauyin wani. Kuma da ta tabbata cewa, ya xauki nauyin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da aya ta sauka a kan haka. Kamar yadda ta sauka a kan Aliyu a cikinsuratul Insan.

Sanannen abu ne kuma, inji xan Shi'ar, cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne mafi girma daga cikin waxanda Sarkin Musulmi Ali ya xauki nauyi. Amma dukiyar da Ahlus-Sunnah ke raya cewa Abubakar ya ciyar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, tattare da yawanta, rashin saukar wata aya ko wata sura ta Alqur'ani a kan haka na tabbatar da kasancewar zancen nasu qarya.

Ya kuma ci gaba da cewa: Haka kuma cewar da suka yi wai, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya wakilta Abubakar ya ba mutane sallah, ba haka abin yake ba. A'ishah ce, Bilalu na qare kiran sallah sai ta yi kangamas ta umurce shi da ya gabatar da Abubakar a gaban sahu. Da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya farko daga magagin zazzavi, sai ya ji kabbara na tashi ana sallah. Sai ya ce, waye ke bayar da sallah? Su A'ishah suka ce: Abubakar ne. Sai ya ce: "Ku kama ni in fita". Fitarsa ke da wuya tsakanin Aliyu da Abbas sai ya kama kafaxun Abubakar, ya janye shi daga Alqibla, ya ci gaba da bayar da sallar da kansa.

Xan Shi'ar ya ce: Wannan shi ne matsayin dalilan Ahlus-Sunnah. Buqatarmu a nan ita ce, masu hankali su dibi waxannan bayanai da idon basira. Kada wani son zuciya ya hana su tsayawa bisa gaskiya, su manta abubuwan da suka ji daga uwaye da kakanninsu. Domin kuwa Allah Ta'ala ya yi hani daga haka. Kada wani abu na duniya ya hana su sadar da gaskiya ga mai ita ko hana ma mai wani haqqi haqqinsa.

Wannan shi ne qarshen abin da muka yi nufin tabbatarwa a cikin wannan matashiya. Inji xan Shi'ah.

**Martani:**

Darajojin Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* abubuwa ne da ko makaho ba ya buqatar hannunka mai sanda kafin ya tantance su. Fifikon da waxannan dattijai ke da shi ya riga ya tabbata. Abin da ko 'ya Shi'ah ke qoqarin yi shi ake ce wa canza ma tuwo suna. Ka ga kuma da haka sun faxa cikin faxar Allah Ta'ala da ya ce:

﴿ ۞ فَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن كَذَبَ عَلَى ٱللَّهِ وَكَذَّبَ بِٱلصِّدْقِ إِذْ جَآءَهُۥٓ ﴾ الزمر: ٣٢

*Wane ne mafi zalunci fiye da wanda ya yi wa Allah qarya,*
*ya kuma qaryata gaskiya a lokacin da ta je masa?*

Da kuma faxarsa:

﴿ فَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّنِ ٱفْتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَوْ كَذَّبَ بِـَٔايَـٰتِهِۦٓ ۚ إِنَّهُۥ لَا يُفْلِحُ ٱلْمُجْرِمُونَ ﴿١٧﴾ ﴾ يونس: ١٧

*Saboda haka, wane ne mafi zalunci a kan wanda ya qirqira ma Allah qarya, ko ya qaryata ayoyinsa? Haqiqa, masu laifi ba su cin nasara.*

'Yan Shi'ah kenan. To, bari mu dawo a kan maganganunsa. Mu fara da cewar da ya yi, babu wata daraja da kasancewar Abubakar tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin kogo ke nunawa.

Amsarmu a nan ita ce, nassin Alqur'ani ya tabbatar da akwai wannan falala da daraja. Duk wanda ya duba shi da idon basira zai gan su bayyane. Xauki ayar ka sake dubawa. Ai Allah cewa ya yi: *Kada ka yi baqin ciki, lalle ne Allah yana tare da mu 9:40.* ka ga anan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya bayar da bayanin kasancewar Allah *Subhanahu Wa Ta'ala* tare da shi da Abubakar, kamar yadda ya kasance tare da Musa da Haruna inda yake cewa: *Lalle ni, ina tare da ku, ina ji, kuma ina gani. 20:46.*

Bayan wannan kuma Buhari da Muslimu sun riwaito, a cikin hadisin Anas daga Abubakar Siddiq *Raliyallahu Anhu* ya ce: "Na ga qafafun mushrikai dabra da kanunmu, a lokacin da muke cikin kogo. Sai na ce, ya Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*! Da xayansu zai sunkuyar da kansa ya dubi qafafunsu, tabbas da ya gan mu". Sai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce masa: Ya kai Abubakar! Me kake zato ga mutum biyun da Allah ne na ukunsu?!

Qari a kan cewa, malaman hadisi kaf sun yi ittifaqi a kan ingancin wannan hadisi, sun kuma karve shi hannu bi-biyu, ta yadda ba a samu mutum biyu daga cikinsu da bakinsu ya sava ba a kansa. Alqur'ani ya daxa tabbatar da ma'anarsa da waccan aya.

Wannan aya da wancan hadisi na daxa tabbatar da qololuwar yabo ne ga Abubakar. saboda sun nuna cewa, Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tabbatar da imanin da Abubakar ke da shi, irin wanda ke sa Allah *Subhanahu Wa Ta'ala* ya kawo xaukin nasara ne ga Manzonsa a cikin wannan hali. Kuma Allah ya bayyana wadatuwar da Manzon ya yi da shi daga kowace irin halitta, a inda yake cewa:

﴿ إِلَّا تَنصُرُوهُ فَقَدْ نَصَرَهُ ٱللَّهُ إِذْ أَخْرَجَهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ ثَانِىَ ٱثْنَيْنِ إِذْ هُمَا فِى ٱلْغَارِ ﴾ التوبة: ٤٠

*Idan baku taimake shi ba, to, haqiqa Allah ya taimake shi a lokacin da waxanda suka kafirta suka fitar da shi, a lokacin da suke su biyu a cikin kogo.. 9:40*

A dalilin wannan aya ne, Sufyanu xan Uyainata da wasu malamai suka ce, tabbas Allah ya ga laifin gaba xayan halitta saboda wannan hali da Annabinsa ya shiga, suna ji suna gani, sai fa Abubakar ne kawai ya tsira daga

zargin. Suka kuma ce, duk wanda ya xauki waccan tare da Abubakar ya yi da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin wancan hali ba bakin kome ba, ya kafirta, saboda ya qaryata Alqur'ani. Su kuwa wasu malamai irin Abul Qasim As-Suhaili cewa suka yi: "Abubakar ne kawai aka tabbatar ya samu wannan daraja".

Idan kuwa muka dubi cewar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wa Abubakar: "Me kake zato ga mutane biyun da Allah ne na ukunsu?" za mu ga cewa, yadda wannan lafazi yake a bayyane haka ma'anarsa take. Domin kuwa ko a cikin halifofi babu wanda ya karva sunan *Halifatu Rasulillahi* sai Abubakar. Daga Umar sunan ya canza ya koma *Amirul Muminina*.

Daga cikin darajojin Abubakar a lokacin da yake cikin kogon dutse, waxanda Alqur'ani yake bayyanawa, akwai busharar da Allah Ta'ala ya yi wa Manzonsa ta nasararsa da taimako, a daidai lokacin da zai tavar da gaba xayan halitta, sai fa wanda ya tsare.

Yin wannan bushara ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a daidai lokacin da Abubakar ke tare da shi, na nuni zuwa ga wata xaukaka da shi Abubakar xin ke da ita a sakamakon haka. Kamar yadda Allah Ta'ala ke cewa: *A lokacin da kafirai suka fitar da shi.. 9:40.*

Mutum xaya ko shi ne qarancin abin da ake iya samu ya raka Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, don babu rabin mutum.

Sannan kuma Allah Ta'ala ya ce: *A lokacin da yake ce ma abokinsa: "Kada ka yi baqin ciki. Haqiqa Allah na tare da mu".. 9:40.* Wannan sai ya nuna abokin nasa na matuqar tausayawa da son taimaka masa. Hakan kuwa sai ta sa shi cikin damuwa da baqin ciki. Daman kuma abin da kan sami mutum kenan a lokacin da wani abin qi ya sami masoyinsa. Amma ko halaka ya ga maqiyinsa zai yi ba zai yi ko gezun ba.

A kan haka, da a ce Abubakar ba masoyin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba ne, kamar yadda 'yan Shi'ah ke son nunawa, ba zai sami wata damuwa ba, balle Manzon ya lallashe shi. A maimakon haka ma sai ya qume daxi da farin cikinsa.

Idan kuwa har 'yan Shi'ar suka yi qoqarin kixe wannan bayani namu da cewa, ai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai san Abubakar na qinsa a zuci ba, ganin irin yadda ya bayyana damuwarsa akan halin da suka shiga. Sai mu ce masu, to, cewar da Manzon ya yi fa: *Lalle ne Allah na tare da mu..* ta nuna cewa, idan shi bai san abin da ke cikin ran Abubakar ba, to, Allah ya sani. Don ga shi wannan aya ta ba mu labarin cewa, Allah na tare da su; su biyu, zai kuma taimake su. Ka kuwa ga ba ya halatta ga Manzon ya ba da labarin kasancewar taimakon Allah gare shi da mumuinai, ya kuma jefo wani munafuki a ciki. Ko alama ba zai yi haka ba. Domin tsararre ne shi, daga yin qari ko ragi ko kuskure a cikin isar da saqon Allah. Kuma ba ya faxar kome daga wurinsa sai gaskiya.

Ko mafi raunin hankali daga cikin mutane ba zai kasa fahimtar irin halin da ya kamata a ce Abubakar ya sami kansa a cikin wannan tafiya ba. Domin kuwa wanda yake yi wa rakiya ya gudo ne daga mutanensa, waxanda ke neman kashe shi saboda qiyayya. Kuma danginsa na gida basu iya taimakonsa da komai. Ka ga dole ne duk wanda zai riqa a matsayin aboki a cikin wannan tafiya ya kasance soyayyarsa da shi ta shafe ta kowa. Hakan kuwa ta tabbata, don ya nuna masa irin baqin cikin da yake ciki a kan halin da ya shiga. Amma kuma sai duk hakan ta zama busar iska; ya kasance yana qiyayya da shi a zuci? Bayan kuma shi ya sakankance har ga Allah cewa, shi masoyinsa ne?

Ko shakka babu, babu wanda zai yi haka sai mafi wauta da jahilcin mutane. Allah kuwa ya qasqanta duk wanda ya jingina irin wannan wauta da jahilci ga Manzonsa, kuma mafi cikar halittarsa hankali da ilimi da gogewa.

Ita ma cewar da xan Shi'ar ya yi, wai abu ne mai yiwuwa ya kasance Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tafi tare da Abubakar ne don tsoron kada asirinsa ya tonu, Quraishawa su yi sukuwar sallah a kansa, magana ce da ba ta sauraruwa, saboda waxannan dalilai:

1. Abin da duniya ta sani, kuma Qur'ani ya tabbatas shi ne, Abubakar masoyin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne, ba mqiyinsa ba. Maganar Allah kuwa ta fi ta kowa.

2. Dubun dubatar hanyoyi na ga-ta-sarai sun tabbatar da kasancewarsa masoyin Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* kuma wanda ya yarda da lamarinsa, ya kuma fi kowa zama tare da shi. Wannan magana tabbatatta ce fiye da yadda labarin Antaru da jaruntarsa ya tabbata, da hatimu da kyautarsa, da soyayya da jivintar da Ali ke da su zuwa ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama.* irin wannan kokwanto na 'yan Shi'ah game da soyayyar da Abubakar ke yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, ba ya da banbanci da irinsa da Harijawa ke yi game da Ali. to, wannan ma da sauqi. Don an sami wasu 'yan Shi'a na musun kasancewar qaburburan Abubakar da Umar a cikin xakin Annabi. Wasu daga cikin 'yan ta'addarsu ma na musun waccan tafiya da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi tare da Abubakar. Wannan feshin qarya ba abu ne farau ba a wurin waxannan mutane, domin kuwa jini da tsokarsu da qarya suka tofo. Hakan ta sa kodayaushe suke qoqarin musanta abin da duniya ta gama tabbatar da kasancewarsa gaskiya, tare da qoqarin tabbatar da abin da duniya da lahira an yarda da kasancewarsa toka.

3. Cewar da xan Shi'ar ya yi, tana yiwuwa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tafi da Abubakar ne don kada Quraishawa su kama shi, na nuna yadda 'yan Shi'ah suke cike da baqin cikin wannan bawan Allah. Dalilin da ya sa har suke fita hayyacinsu wajen canza alherinsa

ya koma sharri. In ba haka ba ai a lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fita daga Makka, kuma labarin ya game gari kamar wutar daji, suka kuma aika da dakarun da ke sintiri a kan godabbu, da alqawarin lada mai tsoka ga duk wanda ya zo da xayansu a raye ko mace. To, wanda haka ta faru a kansa ana cewa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na tsoron faruwar wata kisisina daga wajensa? Shi kansa alqawarin bayar da diyya ga duk wanda ya kawo koda gawar Abubakar na nuna suna da masaniyar alaqar da ke tsakaninsa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kamar yadda kuma hakan ke kore duk wata shakka cewa, ko yana da wata alaqa da su ta voye.

4. Fitar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi tare da sayyidina Abubakar ta kasance ne a talatainin dare. To, wace buqata gare shi ta tafiya tare da Abubakar don gudun tonon asiri? Na san xan Shi'ar zai yi fararat ya ce, ai qila ya faxa masa ne shi kaxai cewa, zai tafi. Sai mu ce: To, me ya sa ya faxa masa in har yana shakkar sa? Kuma ko me ya sa ya sirranta masa haka xin ma? Ai yana iya tafiya a lokacin da Abubakar xin bai sani ba, kamar yadda ya fita sauran jama'ar gari ba su sani ba. Kuma koda ta kasance sun kitse fitar da lokacin yin ta, ai abu ne mai sauqi idan har Abubakar xin na so ya qi fitar a tare da shi, ya kuma tona asirrin. Kai! Allah waddaran maras hankali. Abubakar xin ne fa ya nemi izinin yin hijra shi kaxai daga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, amma Manzon ya dakatar da shi, har sai da Allah ya yi masu izinin fita tare, sannan ya kira shi ya sanar da shi. A sabili da haka ma sai da Abubakar ya fashe da kuka don murna, kamar yadda ya tabbata a cikin Buhari da Muslim.

5. Tsawon lokacin da suke zaune a cikin kogo, Abdullahi xan Abubakar ne ke kai musu labarin Quraishawa. Kuma tare da su akwai Amru xan Fuhairata. Ka ga abu ne mai sauqi da maganar xan Shi'ar gaskiya ce, Abubakar ya umarci xansa ko Amru da gayyato Quraishawa domin su kama Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

6. A lokacin da maqiya suka biyo su har bakin kogo, ga qafafuwansu Abubakar na gani, ai yana iya yin kangamat ya fito don tona asirin. Sanin kowa ne babu maqiyin da ba ya fatar Allah ya nuna masa ranar da zai zama sanadiyyar halakar maqiyinsa. To, in da Abubakar ya fito ya bar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi kaxai kuwwarka banza, sai abin da ake son duk ya faru tare da haxin kan Abubakar xin ya faru. Amma Allah ya tsare Abubakar daga wannan mugun nufi nasu.

## 9.8 Gaba ta Koma Baya

Cewar xan Shi'ar, wai, ayar da Allah Ta'ala ke cewa: *Kada ka yi baqin ciki, lalle ne Allah yana tare da mu 9:40* wai, tana nuna naqasar Abubakar ne ba xaukakarsa ba. Hasali ma tana tona asirin da ke cikin birnin zuciyarsa ne na firgita da tsoro da qarancin haquri da rashin cikakken yaqini da Allah, da kuma rashin gamsuwa da yin kafaxa-da-kafaxa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

**Martani:**

Maganar nan ta xan Shi'a ta warware abin da ya fara faxa na cewa, wai Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fita da Abubakar don kada ya bar baya da qura. Idan har Abubakar maqiyin Manzon Allah ne a voye, to, babu abin da zai sa ya samu wata damuwa ko baqin ciki. A maimakon haka ma sai dai ya yi farin ciki tare da samun cikakkar natsuwa, musamman a lokacin da maqiyan Manzon suka biyo bayansu, har kuma suka iso dabra da kogon, kuma shi Abubakar xin yana ganin qafafunsu kamar za su taki kansa.

Ka ga idan har waccan magana ta farko gaskiya ce, sai xai ya ce masu, kai ar! Ku taho ga shi.

Waccan magana tasu dai ta rosa wannan, cewar da suka yi munafuki ne ta gushe, kasancewarsa mumini ta tabbata. *Alhamdu lillahi Rabbil Alamina.*

A nan yana da kyau mu yi bayanin cewa, babu munafiki ko xaya daga cikin Muhajiruna waxanda Abubakar yake cikin na gaba-gabansu. Babu wanda zai yi hijira daga cikin kafiran Makka, ya bar garinsu da dukiyarsa don ya taimaki maqiyinsa. Duk wanda ya yi hijra daga cikinsu ya yi ta ne a zavin ransa kuma don ya tsira da addininsa kamar yadda Allah ya shede su da haka. Ba mu ce ba a samun munafukai ba, amma sai a cikin xaixaikun qabilun Ansaru da suka shiga musulunci don jin tsoron mamayarsa.

Da wannan magana imanin Abubakar ya tabbata. Shi kuwa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* tun da ba wawa ba ne ko jahili, ba zai zavi abokin tafiya ba sai wanda yake shi ne mafifici daga cikin muminai. Musamman dai irin wannan tafiya mai tsananin haxari da rashin makama. Saboda haka ne ma tasiri da girman wannan hijira a zukatan musulmi ba su misaltuwa. Wannan dole ne, domin kuwa duk tubalin da aka ce za a gina tarihi da shi lalle ne ka taras da labarinsa ya haxe duniya. kamar yadda muka faxa dole ne, wanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* zai yi wannan tafiya da shi ya kasance wanda ransa ya fi kwantawa da shi a kan kowa.

Wannan kawai ya ishi Abubakar Siddiqu abin tinqaho da zama amalen Sahabbai. Domin babu xaya daga cikinsu da ya sami irin wannan xaukaka. Haka kuma na daga cikin abubuwan da ke tabbatar da kasancewarsa mafi girma a idon Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* daga cikinsu.

To, mu koma ga cewar da xan Shi'ar ya yi, wai, wancan rarrashi da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wa Abubakar na kawai tabbatar da naqasarsa ne, ba xaukaka ba. Sai mu ce, wace naqasa yake nufi

cikin biyu 1) Share imani daga zuciyar Abubakar kwatakwata. Ko 2) Rashin kammalar darajarsa, don yana tare da wanda ya fi shi cika da kamala?

Idan xan Shi'ar na nufin ma'ana ta farko ne, to, ya ci tuwon gigi. Domin ko Allah Ta'ala ya gaya wa Annabinsa cewa: *Kada ka yi baqin ciki saboda su, kuma kada ka kasance a cikin quncin rai daga abin da suke yi na makirci 16:127.* Ya kuma ce wa muminai: *Kuma kada ku yi rauni, kuma kada ku yi baqin ciki, alhali ku ne mafiya xaukaka 3:139.* Ya kuma ce: *Kuma lalle ne, haqiqa mun ba ka (ayoyi) bakwai waxanda ake karantawa da Alqur'ani mai girma. Kada ka miqa idanunka zuwa ga abin da muka jiyar da su daxi game da shi, nau'i-nau'i a gare su, kuma kada ka yi baqin ciki a kansu 15:87-88.*

A cikin waxannan ayoyi Allah ya hana Manzonsa da muminai baki xaya baqin ciki. Ashe kenan ba ta nufin wanda aka hana xin ba ya da imani.

Idan kuwa xan Shi'ar na nufin ma'ana ta biyu, wato, daraja da xaukakar Abubakar a wannan hali ba su kai na Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba, wannan gaskiya ne. babu kuma wani Ahlus-Sunnah da ke musun haka. Amma dai ba ta nufin Aliyu ko Umar ko Usmanu sun fi shi xaukaka. Haka ba za ta yiwu ba, domin babu xaya daga cikinsu da ya kasance tare da Annabi a wancan lokaci. Kai koda sun kasance tare da shi xin , hakan ba za ta sa su fi Abubakar girman daraja da xaukaka ba. Domin kuwa abin da yau da gobe suka tabbatar shi ne, a duk lokacin da qura ta musqe, tsanani ya yi tsanani, Abubakar ne ke zama zakara a fagen yaqini da haquri fiye da su. Haka kuma idan aka sami wani tajin-tajin, ko Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya gindaya wani abu, Abubakar ne kan gaba kodayaushe wajen tabbatar da natsuwa da yaqini ta hanyar yin abin da zai faranta ran Manzon da nisantar abin da ba ya so.

Wannan magana bayyane ta ke ga duk wanda ya bibiyi diddigin tarihin waxannan Sahabbai, a lokacin rayuwa da bayan rasuwar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Haka kuma abin da ya faru na natsuwa da jaruntaka da jajircewar Abubakar lokacin da suke cikin dabi tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ranar yaqin Badar da na Hudaibiyyah, duk ba a voye suke ba. To, ta yaya za a ce ya yi raggon kaya a waxannan lokuta?

Bayan wannan kuma, tsayin dakan da Abubakar ya yi ya yaqi waxanda suka yi ridda da waxanda suka yi watsi da rukunin zakkah, da yadda ya kwantar da hankalin muminai lokacin wafatin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, da shirya rundunar Usamatu na daga cikin abubuwan da ke bayyana fifikonsa.

Babu wani daga cikin Ahlus-Sunnah da ke musun fifikon Abubakar a kan Umar da Usmanu. Kuma gaba xaya suna da yaqinin cewa, Ali bai fi waxannan ukun cika da kamala ba. Duk wanda ya leqa tarihin Umar da Usman zai tabbatar da sun fi Ali haquri da juriya da rashin firgita a lokacin sabkar musibu. Dubi lokacin da 'yan tawaye suka yi wa gidan halifa Usmanu qawanya; suka hana shi shaqat. Suka ce, lalle sai ya yi murabus ko su aika shi

lahira. Bai yi murabus xin ba, bai kuma bari a yaqe su ba. Ba batun ya bayar da umurni ga wasu su kare shi ake yi ba. Haka dai aka yi cirko-cirko har suka haura suka saka shi motar shahada ya isa wurin Ubangijinsa, yana mai cike da haquri da dattaku. Ashe wannan ba mafi girman jaruntaka ne ba?!

Amma ka ga shi Ali, tarihi ya tabbatar da cewa, haqurinsa bai kai na Usmanu ba. Domin kuwa da yawa yake kasa hanqurin 'yan matsalolin da yake fuskanta daga dakarunsa, balle na abokan gaba. Savanin yadda Abubakar da Umar da Usmanu suka shanyen dafin duniya.

Kuma xan Shi'ar ya ce, wai ayar na nuna irin raki da qarancin haquri da yaqini, da rashin yarda da yin kafaxa-da-kafaxa da Annabi, da rashin amincewa da hukuncin qaddara da ke ga Abubakar. To, mun ji taka. Saurari tamu:

Zahiri take cewa ayar ta yi gabas xan Shi'ar ya yi yamma. Cewa kada a aikata abu ba ya nufin an riga an aikata. Iyakar abin da hanin ke nunawa shi ne, kada a aikata abin ko can gaba. Kamar yadda Allah Ta'ala ya ce wa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama*: *Ya kai Annabi ka ji tsoron Allah, kuma kada ka yi xa'a ga kafirai da munafukai 33:1.* Ka ga hakan ba ta nufin Annabi ba ya tsoron Allah, ko kuma yana xa'a ga waxannan mutane.

Mu qaddara cewa, Abubakar ya sami damuwar ya kuma yi baqin cikin, shi ya sa Annabi ya rarrashe shi. Ya yi haka ne don fargaban kada mushrikai su riske su su kashe Annabi, dashen musulunci ya yanqwane. Saboda haka kullum fatarsa ita ce, ya fanshi ran Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* koda shi nasa rai zai salwanta. Kamar yadda bayan fitarsu daga kogon yake kai wa da komowa gaba da bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* suna kan hanya. Da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tambaye shi dalili sai ya karva masa da cewa, ina shiga gabanka ne idan na tuna yiwuwar ka taka koda qaya ce. Idan kuma na tuna cewa, wani abu na iya kawo maka farmaki ta baya, sai in koma can. Ahmadu xan Hambali ya riwaito shi.

Haka kuma a lokacin, Abubakar bai yarda da zamansa katkatkat da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba. Amma ba da irin ma'anar da xan Shi'ar ke nufi ba. Abubakar bai yarda su mutu tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba, kamar yadda bai yarda Manzon ya mutu ya bar shi a raye ba. Ya dai fi gurin ya fanshi ran Manzon da nasa ran da iyalinsa da dukiyarsa.

Ba ga Abubakar kawai ba, haka ya kamata kowane musulmi ya kasance tsakaninsa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Kai hakan ma wajibi ne. Ka ga a wannan fage Abubakar Siddiqu ya xaga tuta. Ko banza Allah Ta'ala ya ce: *Annabi ne mafi cancanta ga muminai bisa ga su kansu 33:6*. Ya kuma zo a cikin Buhari da Muslim daga Anas daga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* cewa: "Xayanku ba zai zama mai cikakken imani ba har sai na kasance mafi soyuwa gare shi fiye da 'ya'yansa da iyayensa da mutane baki xaya.

Wannan baqin ciki da Abubakar ya yi, na nuna tsabar so da qauna da yake yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, da irin yadda yake shirye ya saxaukantar da rayuwarsa saboda shi, fai da voye. Wannan kuwa shi ne mafi qarfin imani.

Mu koma ga cewarsa, wai, hakan na nuna qarancin yaqinin Abubakar. Wannan magana varna ce gungumamma. Rarrashin ba ya nufin rashin koda irin wannan haquri da aka umurce shi da yi, balle wanda ba shi ba. Domin ai ka ga Alqur'ani da Sunnah sun wajabta wa musulmi xaukar qaddara, amma duk baqin cikin da mutum zai yi azuci, ba ya kore kasancewarsa mai haquri. Kamar yadda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce: "Haqiqa Allah ba ya kama kowa da laifi don zubar hawayen idaniya ko kukan zuci. Sai dai yana kama mutum da laifin abin da harshensa ya faxa, ko ya yi masa rahama a kansa".

Ita ma cewar da xan Shi'ar ya yi wai, rarrashi na nuna rashin yaqinin da Abubakar yake da shi, ba magana ce da ke sauraruwa ba. Domin kuwa tarihi ya tabbatar da cewa, Annabawa sun yi baqin ciki a kan wasu abubuwa. Amma ba wanda zai ce hakan na nuna rashin yaqininsu da Allah sai shakiyyi. Allah ya bamu tarihin irin baqin cikin da Annabi Yaqubu ya yi. Kuma hadisi ya tabbatar da cewa, a lokacin da Ibrahimu xan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya rasu, Manzon ya ce: "Idanunmu na zubar da hawaye, zuciyarmu na quna, amma duk da haka ba za mu faxi komai ba sai abin da Ubangiji ke yarda da shi. Tabbas muna baqin cikin rasuwar Ibrahim".

Ko sahkka babu haka ta faru, tattare da cewa, Allah Ta'ala ya hana Manzon nasa yin baqin ciki inda yake cewa: *Kuma kada ka yi baqin ciki a kansu 15:88.*

Ita ma cewarsa wai, ayar na nuna raki da rashin yardar Abubakar da hukunci da qaddarar Allah, magana ce ta rashin fahimta.

**9.9 Babu Shakka Abubakar ya Damu**

Mutumin ya ce: Da a ce baqin cikin da Abubakar ya yi a lokacin, xa'a ne ga Allah, da Annabi bai taka masa burki ba. Idan kuwa savo ne, shi ya sa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya hana shi, to, xaukakar da suke hange ta zama qasqasci kenan.

**Martani:**

Babu wanda ya ce don Abubakar ya yi baqin ciki ne kawai ya samu waccan xaukaka. Babu wanda ya ce haka. Xaukakar dai na nan cikin abin da Allah ya ce: *Idan ba ku taimake shi ba, To, haqiqa Allah ya taimake shi a lokacin da kafirai suka fitar da shi suna su biyu a cikin kogo, a lokacin da yake ce wa abokinsa: Kada ka yi baqin ciki. Haqiqa Allah na tare da mu. 9:40.*

Kasancewar Abubakar *Raliyallahu Anhu* wanda Allah ya azurta da fita tare da Annabi a wannan mawuyacin hali, ba tare da wata kwana ko gardama ba, shi ne abin da ya tabbatar da xaukaka da daraja ga baban A'ishah.

Ita kuwa cewar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi masa: *Haqiqa Allah yana tare da mu 9:40* na nuna irin karvuwar da ya samu ne ga Manzon, da irin yadda ya yarda da qurbaninsa na so da qauna, ya kuma sami cikakkar natsuwa a cikin haka. Ko shakka babu, wannan irin gagarumar gudunmawa a irin wancan yanayi na tabbatar da cikar imani da tsoron Allansa. Wannan kuwa babbar daraja ce.

Bayan wannan kuma, horon da aka yi wa Abubakar da kada ya razana, na iya zama taimako gare shi na kauce wa faxawa cikin kogon damuwa. Domin kuwa ga al'ada baqin ciki kan mamayi mutum ne bai da wan ceto; ba kuma tare da ya shirya wa tahowarsa ba. Hakan kuma kan faru musamman a lokacin da babu wani sanadari da zai qarfafa masa guiwa ga hana wutar baqin cikin kamawa. Idan ko aka samu irin wannan sanadari kamar yadda ya samu ga baban A'ishah *Raliyallahu Anhu* to, qaryar baqin ciki ta qare.

Da ka dubi sigar waccan aya, za ka ga haka qarara. Domin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ce wa mutumin nasa: *Kada ka yi baqin ciki* bai tsaya nan ba, sai da ya qara tsattsage sanadarin da cewa, *Haqiqa Allah yana tare da mu.* Ka ga ya cire masa tsoro a zuci, ya kuma damqa masa garkuwa a hannu. Irin haka kuwa ne kawai ke kare mutum daga allobar baqin ciki. Rashin haxuwar hancin waxannan abubuwa biyu wuri xaya ke sa mutum ya motsa kawai, ya ji shi tsamo-tsamo cikin ambaliyar sunu da tasko. Ballantana kuma, hanin da aka yi wa Abubakar daga yin wannan baqin ciki, ba yana nufin har ya riga ya yi xin kafin rarrashin ba. A'a, an dai rarrashe shi ne don ganin duk wani dalilin da ke sa mutum faxawa cikin baqin ciki ya haxu a kansa.

To, a irin wannan hali, koda yin baqin cikin savo ne, hakan ba zata cutar da mu da kome ba. Domin kuwa rarrashin da aka yi masa, ya karva sunansa na rarrashi da qarfafa guiwa, kai har ma jaje. Ka ga abin ya zama qaddara kenan ba savo ba. Ko tafi ma duk waxannan dalilai ba haka suke ba, ai baqin ciki kan riski mutum ne ba tare da ya shawarce shi ba. Ka ga a irin nan ba zancen savo.

To, kuma duk aje komai ma, babu wani mai cikakken hankali a duniya da zai zauna da mutum tsawon lokaci, irin yadda Annabi ya zauna shekaru kusan goma tare da Abubakar a Makka face ya gane mutumin nan masoyinsa ne ko maqiyinsa. Amma a ce har kawowa cikin wannan haxari Annabi bai san matsayin tarensa da Siddiqu ba, ai ka ga wannan mummunar suka ce ga Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama.*

Bayan kuma duk wannan ma, duniya ta san cewa, Abubakar *Raliyallahu Anhu* babban masoyin Annabi ne tun daga lokacin da aka aiko masa da manzanci har zuwa rasuwarsa. Shi ne farkon wanda ya yi imani da shi, ya kuma gayyato wasu mutane suka yi. Ya saxaukantar da dukiyarsa wurin fansar waxanda suka bayar da gaskiya irin su Bilalu da makamantansa. Haka kuma Abubakar yana fita tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a lokutan hajji don kiran wasu qabilu zuwa ga imani. Babu ranar da ba ya zuwa gaban Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*; in ba da safe ba da rana.

Irin cutuwar da Abubakar ya yi a hannun kafiran Makka saboda kawai ya yi imani, sai wanda ya ji ko ya gani.

Da zarar an dubi wannan matsayi, za a tabbata cewa, taka irin wannan rawa da Abubakar ya yi sai wanda so da qaunar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* suka keta naman jikinsa. Wannan kuma na nuna cewa, ba kawai zatin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ya samu karvuwa ga Siddiqu ba, a'a, har manzancin da ya zo da shi. Saboda haka ne ma ya qi mutanensa, ya kuma yi gaba-da-gaba da aradu. A qarshe ma hakan ce ta sa ya ciyar da gaba xayan dukiyarsa ga muminai mabuqata.

Amincin da ke tsakanin Siddiqu da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai qare ba sai da mai raba masoya ta raba su. Ba a tava jin ya cutar da shi koda da kalma xaya ba, balle qoqarin kashe shi kai tsaye ko ta hanyar ba shi wata cimaka, duk da kasancewarsa masu kevantuwa da shi dare da rana.

Sannan kuma idan aka dubi matsayin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* na wanda Allah ke ba kariya, hakan na wajabta Allah ya sanar da shi abin da ke kimshe cikin zuriyar Abubakar na qiyayya da mugun nufi in har akwai su. Kamar yadda ya sanar da shi abin da ke cikin ran Abu Azzata na niyyar fatattaka shi alhalin ya zo yana bayyana imani. Hakanan kuma Allah ya sanar da shi abin da ke cikin ran Alhajabi ranar yaqin Hunainu lokacin da aka yi nasara a kan musulmi. Kuma Allah ya sanar da Manzon nasa abin da ke cikin ran Umairu xan Wahabu na son halaka shi a lokacin da Umairun ya zo Makkah a matsayin wanda ya musulunta. Ga shi kuma a lokacin yaqin Tabuka Allah ya sanar da shi mugun nufin da munafukai suka yi na kwance tamantakar taguwarsa.

Waxannan xaixaikun mutane kenan fa da saduwarsu da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ta xan lokaci ce. Ina ga Abubakar *Raliyallahu Anhu* wanda suke tare dare da rana gida da daji? A lokacin yaqin Badar ma shi kaxai aka bari tare da shi. Amma wai duk da haka a ce Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai san Abubakar na qin sa a zuci ba, abin da ko mai 'yar qaramar qwaqwalwa na iya ganewa cikin xan qanqanen lokaci! Duk wanda ya zaci haka ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da amininsa bai raga wa musulunci da musulmi ba. Mai irin wannan tunani kuwa koda ya yi haka ne akan jahilci da qoqarin bayyana irin son da yake ma Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* to, bai kamata qarancin iliminsa na addini ya hana shi gane cewa, 'yan Shi'ah fa suna hannun riga ne da musulunci.

Wani abin mamaki kuma shi ne, cewar da ya yi wai, babu inda Alqur'ani ya ambaci saukar natsuwa ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* face ya ambaci muminai tare da shi a cikinta in ba nan ba. Wai kuma babu naqasar da ta kai wannan. Marubucin yana qoqarin ya nuna Allah ya yi irin wannan magana a wurare da dama cikin Alqur'ani, alhali kuwa abin ba haka yake ba.

Natsuwar ma da Allah ya ce ya saukar a kansa, wa ya ke nufi? Manzo ne ko Abubakar? Malamai sun qari junansu sani. Kuma cewa, Abubakar ake nufi na qarfafa da xabi'ar lafuzzan da ayar ta zo da su. Domin lamirin "shi" ya rufa ma sunan Abubakar baya ne kai tsaye. Ta fuskar ma'ana kuwa, malamai suka ce, Abubakar ne ke da buqatar agajin natsuwa ba Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba. Shi kam ai tasa natsuwar har ta yi oba. Kuma idan muka fahimci maganar a matsayin saukar da natsuwa ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, to, ba kome. Kuma tun da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* xin ne ya ce masa a matsayinsa na xan rakiya: *Haqiqa Allah yana tare damu,* hakan na nufin duk natsuwa da agajin da za su sauka ga shi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a matsayinsa na uban tafiya, to, sun haxa har da abokin tafiyarsa.

**9.10 Abubakar ne Dai Ayar ke Nufi**

Xan Shi'ar ya ce: Cewar da Allah Ta'ala ya yi: *Kuma mafi taqawa zai nisance ta* wai Allah na nufin Abud-dahadahu ne, kuma ya kawo qissar da ya jingina saukar wannan aya gare ta.

**Martani:**

Surar da wannan aya take cikinta gaba xaya ta sauka ne a Makka, kamar yadda malaman tafsiri da sauransu suka amfanar. Shi kuwa labarin Abud-dahadahi ya faru ne a Madina, domin shi kansa Ba'ansare ne da bai zauna da Annabi ba sai a Madina. Kuma a Madina kawai ake da gonakin da wannan labari da ya kawo ke iya faruwa a kansu. To, ina alaqarsa da wannan ayar? Sai dai mu ce hukuncinta ya haxa da shi. Wannan ita ce rinjayayyar magana.

Mu koma ma ayar mu gani. Allah Ta'ala cewa ya yi: *Kuma mafi taqawa zai nisance ta 92:17* . Kuma a wata ayar Allah ya ce: *Haqiqa mafificinku daraja a wurin Allah shi ne wanda yake mafificinku a taqawa 49:14.* ka ga daga ma'anar waxannan ayoyi muna iya fahimtar cewa, duk wanda ya kasance mafificin taqawa a cikin al'umma to, dole ne ya shiga cikin wannan aya. Babu ko wani malami da ya tava cewa, Abud-dahadahi ne mafificin taqawa a cikin wannan al'umma koda ko malamin xan Shi'ah ne. Amma kan al'umma ya haxu bisa ga cewa, Abubakar ne yake da wannan matsayi.

Idan wanda ke ciyar da dukiyarsa don neman ya tsalkaka shi ne mafificin taqawa, kuma mafificin girma a cikin halitta shi ne mafificinsu taqawa, to lalle kuwa shi ne mafificin daraja.

To, wane ne mafi taqawa da ya zo a wannan aya? Ahlus-Sunnah sun ce, Abubakar. A yayin da 'yan Shi'ah suka ce, Ali. Dalilai da dama kuwa na nuna cancantar Abubakar da zama wanda wannan aya ke nufi. Ga wasu daga cikinsu:

**Na Farko:**

Cewa Allah ya yi: *Wanda yake ba da dukiyarsa yana tsalkaka 92:18.* Wanda tarihi ya tabbatar da ciyarwarsa ga musulunci kuwa, shi ne Abubakar. Amma shi Ali abin da tarihi ya nuna shi ne, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ke xauke da nauyinsa tun lokacin da ya xauko shi daga wurin mahaifinsa Abu Xalib, a sakamakon wata yunwa da aka yi a Makka. Ya ci gaba da rayuwa a matsa kaicin hali har zuwa lokacin da ya auri Fatima. Ko bayan wannan aure mai albarka Aliyu bai fita daga gandun gidan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a matsayinsa na wanda Annabin ke tallafa ma ba.

A sane muke, da Allah ya hore masa abin ciyarwar da ya ciyar. Wannan magana da muke faxi sananna ce qwarai ga Ahlus-Sunnah da 'yan Shi'ah.

**Na Biyu:**

Cewar da Allah Ta'ala ya yi: *Alhali babu wani mai wata ni'ima wurinsa, wadda ake neman sakamakonta 92:19* na nufin Abubakar *Raliyallahu Anhu* ba Ali ba. Abin da ke tsakaninsa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ni'ima ce ta imani, wato, ba don Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba da Abubakar Siddiqu bai tsere wa wuta sanadiyyar yin imanin ba. Biyan bashin irin wannan ni'ima kuwa sai dai Allah; ba mutum ba. Amma abin azzikin da ake iya mayar da hannun baiwa a kansa, shi ne ni'imar abin duniya. Bukin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wa Abubakar kuwa na addini ne. Wanda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wa bukin ni'imar abin duniya shi ne Ali.

**Na Uku:**

Abubakar ne wanda ba shi da wani dalili na kashe dukiyarsa saboda Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai dalilin imani. Ba kamar yadda Abu Xalib ya taimake shi saboda zumunta ba. Taimako da hidimar da Abubakar ya wa musulunci ya yi su ne kawai don neman yardar Allah Ta'ala. Kamar yadda Allah ya shedi hakan da cewa: *Face don neman yardar Ubangijinsa mafi xaukaka. To, haqiqa zai yarda da sakamakon da za a ba shi 92:20-21.*

### 9.11 Shi wannan Ayar ke Nufi

Xan Shi'ar ya ce: Cewar da Allah Ta'ala ya yi: *Ka ce wa waxanda aka bari daga qauyawa 48:16* na nufin waxanda ba su fita zuwa yaqin Hudaibiyyah ba. Amma kuma suka so fita zuwa samun ganimar yaqin Haibara. Wai, sai Allah Ta'ala ya hane su, inda ya ce: *Ka ce ba za ku bi mu ba 48:15* ya ci gaba da cewa wai, Allah ya yi haka ne saboda ya kevance ganimar Haibara kawai, don waxanda suka halarci yaqin Hudaibiyyah. Daga baya kuma Allah Ta'ala ya ce: *Ka ce wa waxanda aka bari daga qauyawa za a kira ku zuwa ga waxansu mutane masu tsananin qarfin yaqi 48:16* kuma wai Manzon Allah

*Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kira su bayan haka zuwa ga yaqoqa da yawa kamar yaqin Mu'utah da na Hunainu da Tabuka da sauransu.

Xan Shi'ar ya ci gaba da cewa: Ka ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne wanda ya yi kiran ba Abubakar ba. Tana kuma iya yiwuwa ayar ta kasance tana nufin Aliyu ne wanda zai yi kiran. Domin shi ne bayan haka ya yaqi fanxararru da kangararru da 'yan tawaye. Dawowa da ya yi da su kuwa ga yi masa xa'a dawowa ne da su a cikin musulunci, domin sun kafirta kafin hakan. Hakan na tabbata ne, inji shi, idan muka dubi faxar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da ya ce: "Ya kai Ali, duk wanda ya yaqe ka ya yaqe ni ne". Ya ce: Ka ga duk wanda ya yaqi Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* tabbas kafiri ne.

**Martani:**

Wasu daga cikin malamai sun riga sun kafa hujja da wannan aya da ta gabata a kan halifancin Abubakar *Raliyallahu Anhu* da wajabcin yi masa xa'a. Malaman kuwa sun haxa da, Imamus Shafi'i da Ash'ari da Ibnu Hazam da wasu ba su ba. Hujjar da suka kafa a kan wannan fassara ita ce faxar Allah Ta'ala da ya ce: *To, idan Allah ya mayar da kai zuwa ga wata qungiya daga cikinsu, sa'annan suka neme ka izini domin su fita, to, ka ce, ba za ku fita tare da ni ba har abada, kuma ba za ku yi yaqi tare da ni ba a kan wani maqiyi 9:83.*

Malaman suka ce, da wannan aya ne Allah Ta'ala ya umurci Manzonsa da ya gaya wa waxancan mutane da suka fita yaqin Hudaibiyyah cewa, tunda haka ne, to, ku yi ta zama, har abada ba zan sake neman fita yaqi tare da ku ba, ko kun so hakan.

Suka ce kuma, harwayau dai wannan aya ta tabbatar mana da cewa, wanda zai sake kiransu zuwa ga yaqi, ba Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ba. Sai dai wani bayansa. Ka ko ga ba kowa bayansa sai waxannan halifofi da aka sani. Su ne suka kira mutane zuwa ga yaqar Farisawa da Rumawa waxanda sun fi kowa cancantar waccan siffa da aya ta faxa ta cewa *Masu tsananin qarfin yaqi 9:16.* Kuma su ne kafiran da waxancan halifofi uku suka yaqa a kansu musulunta.

Daga wannan ingantattar fassara sai a fahimci cewa, makamar wannan aya ita ce: Za a kira ku zuwa ga waxansu mutane masu tsananin qarfin yaqi, domin ku yaqe su ko kuwa su musulunta. Ka ga idan aka fahimci ayar a haka, sai siffar waxancan mutane ta tsananin yaqi ta fito tare da umurnin da aka ba waxancan jemagu na su yaqe su ko su musulunta.

Malaman suka qara daddale wannan fassara tasu da cewa, ba ta yiwuwa ko kaxan a kira mutane zuwa ga waxancan yaqe-yaqe da aka yi da mutanen Makka bisa cewar xan Shi'ar dab da qarewar shekarar nasara. Domin kuwa ai su ne aka so su fito ayi yaqi a Hudaibiyyah. Koda kuwa ana hangen cewa, ba dukansu ne mutanen wannan wuri ba, tabbatacciyar magana dai ita ce, duk jirgi guda ya xauko su.

Wani dalilin kuma da malaman suka kafa shi ne, su mutanen da aka yaqa a wannan shekara, basu fi waxancan da suka qi fita tare da Annabi tsananin yaqi ba; dukansu Larabawan Hijaz ne, dabarun yaqinsu kuma kala xaya ne. kuma ma irin wuyar da mutanen Makkah da maqwabtanta suka gana wa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Sahabbansa a wajen yaqin Badar da Uhudu da Handaqu ta fi waccan da suka sha a hannun waxancan qabilun a shekarar yaqin Hudaibiyyah, da waxansu yaqe-yaqe da ba waxannan ba. Ka ga kenan sai dai a kira su zuwa ga yaqar wani jinsi na mutane ba waxannan ba.

Shi kuwa Annabi ya ce ma Ali: "Duk wanda ya yaqe ka ya yaqe ni", hadisi ne da bai isa a kafa hujja da shi ba. Domin kuwa ko isnadinsa xan Shi'ar bai ambata ba. Kuma ta tabbata a wajen malaman hadisi cewa jabun hadisi ne.

Idan kuma muka koma ga cewar xan Shi'ar, wai, tana yiwuwa mai wancan kiran ya kasance Ali ne ba xaya daga cikin halifofin uku ba. Saboda wai shi ne ya yaqi tsageru da kangurarru da 'yan tawaye. Wato, yana nufin rundunar da ya kara da ita a bayan A'isha *Raliyallahu Anha* da ta mutanen Sham da ke bayan Mu'wiyah. Sannan Harijawa da ya yaqa a Harura. To, wannan magana ta xan Shi'ar ba ta bisa hanya saboda la'akari da abubuwa da dama.

Waxannan mutane da Ali ya yi yaqi da su ba su fi 'yan'uwansu da ke gida tsananin yaqi ba. Kuma ma sanannen abu ne cewa, mutanen da ya haxu da su a yaqin basasar Raqumi ba su kai yawan dakarunsa ba. Ba zance Harijawa 'yan-aware ake yi ba, waxanda rundunarsa ta ninka su fiye da biyu. Haka kuma ta fi waxanda ya haxu da su a Siffin. Duk waxannan jama'a da ya yaqa a waxannan lokuta ba su xara 'yan'uwansu na gida da komai ba a fagen qarfin yaqi balle har Alqur'ani ya siffanta su da kasancewa haka.

Amma sanannen abu ne cewa, mutanen bani Hanifata da Farisawa da Rumawa sun fi waxancan mutane da Aliyu ya yaqa tsananin qarfin yaqi. Irin yadda rayuka suka salwanta a cikin rundunar da Abubakar ya yaqi waxancan isassun qabilu da ita, ko kaxan ba su salwanta hakanan a rundunar Ali ba a yaqinsa da Larabawa. Dubi yaqin da halifa Abubakar ya yi da jama'ar Musailama, su Farisawa da Rumawa ba ma maganarsu ake yi ba. Domin babu wani mai cikakken hankali da ke musu, ko shakkar kasancewar su mutane masu tsananin yaqi, idan sun gamu da abokan gaba fiye da yadda Larabawa za su yaqi junansu wa-su-wa-su. Wuyar da musulmi suka sha a hannun Larabawa kafirai a farkon musulunci, ba ta kasance saboda tsananin yaqinsu ba, ta dai kasance ne saboda rashin yawan muminai da raunin da suke da shi a lokacin. Amma ko kaxan kafiran na Makka ba su yi tsananin yaqin Farisawa da Rumawa ba.

Kuma abin da kowa ya sani ne, Aliyu bai kai wa kowa goron gayyar yaqi daga cikin mutanensa ba, don yaqar mutanen Raqumi da Harijawa. Hasali ma koda ya iso birnin Basrah bai iso da niyyar yaqi ba, kamar yadda Xalhatu da Zubairu ba su zo da ita ba, qaddara ce kawai ta riga fata. Su ko Harijawa saboda rashin yawansu, wani sashe ma na rundunarsa na iya gamawa da su nan

take. Saboda haka, ko mutum xaya daga cikin Larabawan qauyen Hijaz bai gayyato don yaqarsu ba.

Koda kuma mun qaddara cewa, wajibi ne a yi wa Aliyu xa'a a cikin yaqe-yaqen da ya yi da waxancan mutane 'yan'uwansa. To, ai ya sava wa hankali a ce Allah Ta'ala ne ya yi umurni da a bi shi wajen yaqar masu mayar da gaba gabas su yi sallah, don neman su yi biyayya ga shugabancinsa, amma bai yi umurni da yin biyayya ga waxanda ke yaqar kafirai tuburan don neman su yi imani da Allah da Manzo ba. Ko ko mu xauka cewa ma waxanda Ali ya yaqa xin kafirai ne, to, ai kafircinsu bai fi na wanda shi asalatan bai tava alwalla ba balle ya kabbarta. Hasali ma fito-na-fito ya yi da Manzon ya kuma qaryata Alqur'anin da ya zo da shi. Ko shakka babu zunubin irin wannan mutum na farko shi ne mafi girma. Kuma ladar da za a samu a cikin qoqarin ya shigo musulunci ta fi wadda za a samu ga na biyun girma.

Haka kuma koda za mu yarda da cewa, waxanda Ali ya yaqa an xauka sun yi ridda ne su ma, kamar yadda 'yan Shi'a ke cewa. To, ai sanannen abu ne cewa, riddar wanda har ya kai ga imani da akwai wani Manzo wanda ba Muhammadu ba kamar mabiyan Musailamu, ta fi nauyi bisa ga wanda wani shugaba ne kawai bai yarda da shugabancinsa ba, amma yana nan a matsayinsa na wanda ya yi imani da manzancin Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Ala ayyi halin, babu wani zunubi da za a ce waxanda Aliyu ya yaqa na da shi, face wanda mutanen da halifofin can uku suka yaqa ke da shi ya fi girma. Kamar yadda babu wata lada da daraja da za a ce waxanda suka taimaka wa Ali a waxancan yaqe-yaqe sun samu, face waxanda suka taimaka wa halifofin can uku a cikin nasu yaqe-yaqen sun samu mafi girma. Wannan ma idan mun qaddara kasancewar waxanda Ali ya yaqa kafirai, wanda kuwa tabbas ba haka ba ne. Duk ma wanda ka ji haka a bakinsa, to, ka tabbata ko cikin 'yan Shi'ah bara-gurbi ne. Amma masu sauran hankali da tunani cikinsu ba su faxar haka. Ga shi kuma an riwaito ta hanyoyi da dama daga Aliyu da mutanen gidansa cewa, waxanda suka yaqe shi ba kafirai ba ne.

Duk wannan dawara da muke yi za ta samu gindin zama ne, idan mun yarda da cewa, waxancan yaqe-yaqe da Ali ya yi karvavvu ne a idon musulunci, wanda ko ba haka ba ne. Domin kuwa magabata sun tambayi kansu, shin waxannan yaqoqa daidai suke da yaqar 'yan tawaye irin waxanda shari'a ta wajabta a yaqa? Ko kuwa ba irinsa ba ne?

Abin da manyan Sahabbai da Tabi'ai suka tafi a kai shi ne, yaqin basasar da Ali ya yi da magoya bayan A'ishah *Raliyallahu Anhu* da wanda ya yi da magoya bayan Mu'awiyah *Raliyallahu Anhu* a Siffin duk ba yaqi ne da Allah ya yi umurni da yi ba. Kuma da Allah ya sa bai yi yaqe-yaqen ba da haka ta fi zama alheri. A wajen waxannan magabata waxannan yaqe-yaqen fitinnu ne kawa, wato basasa. Wannan ra'ayin kuwa shi ne akasarin malaman Hadisi da na Fiqihu suke a kai.

Ita kuma wannan aya da muke ta magana a kanta ba ta nufin yaqi a bayan Ali kai tsaye. Domin yaqin da ya yi ba da kafirai ya yi shi ba. Kuma ai ka ga ayar cewa ta yi: *Ku yaqe su ko su musulunta.* Ka ga ko duk waxanda Ali ya yaqa sun riga sun musulunta gabanin yaqinsa. Kuma daga cikin waxanda ma ya far ma, akwai waxanda ba su yarda suka yi yaqin da shi ba, ba su kuma yaqi kowa tare da shi ba, sai suka kama kansu. To, kuma kan haka ko waxanda suka yaqe shi xin ba a ce musu kafirai. Kuma Alqur'ani da Hadisi da haxuwar kan Sahabbai har da Aliyun, duk sun tabbatar da haka. Ga abin da Allah Ta'ala ke cewa:

﴿ وَإِن طَآئِفَتَانِ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ٱقْتَتَلُوا۟ فَأَصْلِحُوا۟ بَيْنَهُمَا ۖ فَإِنۢ بَغَتْ إِحْدَىٰهُمَا عَلَى ٱلْأُخْرَىٰ فَقَـٰتِلُوا۟ ٱلَّتِى تَبْغِى حَتَّىٰ تَفِىٓءَ إِلَىٰٓ أَمْرِ ٱللَّهِ ۚ فَإِن فَآءَتْ فَأَصْلِحُوا۟ بَيْنَهُمَا بِٱلْعَدْلِ وَأَقْسِطُوٓا۟ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلْمُقْسِطِينَ ﴿٩﴾ ﴾ الحجرات: ٩

> *Kuma idan jama'a biyu ta muminai suka yi yaqi, to, ku yi sulhu a tsakaninsu. Sai idan xayarsu ta yi zalunci a kan xaya, to, sai ku yaqi wadda ke yin zaluncin har ta koma zuwa ga umurnin Allah. To, idan ta koma sai ku yi sulhu a tsakaninsu da adalci, kuma ku daidaita, lalle Allah na son masu daidaitawa 49:9.*

Ka ga duk da yaqin da ya wanzu tsakanin waxannan qungiyoyi na musulmi, Allah bai tuve masu rigar imani ba. In don tawaye kuwa, da rashin miqa wuya ga wani shugaba, ba zai fitar da mutum daga sahun musulmi ba. Haka kuma a cikin ayar Allah Ta'ala ya gaya mana ci gaba da kasancewarsu 'yan'uwa. Ka kuwa san 'yan'uwantaka ba ta kasancewa tsakanin mumini da kafiri, sai dai tsakanin musulmi tsintsa.

Amma ka ga wannan xan Shi'ar kamar bai san da akwai wannan aya ba, ba mu ce bai yarda da ita ba. Sai ga shi kai tsaye ya kafirta waxancan mutane. Har kuma da cewa, wai yaqarsu da Ali ya yi, ya yi ne don ya dawo da su cikin sahun musulmi. Har ya kafa hujja da wai Annabi ya ce, wanda ya yaqi Ali ya yaqe shi.

Babu abin mamaki da ta kaicin da ya kai cijewar da 'yar Shi'ah suka yi a kan wannan yasasshen ra'ayi suna masu dogaro da wannan yasasshen hadisi. Hadisin da ko bayan rashin madogararsa ya sava ma ingantattun maganganun Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da aka sani cewa, barin yaqi a cikin fitina ya fi alheri a kan yin sa, da kuma yabon da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi wanda ya sasanta tsakaninsu.

### 9.12 Abubakar da Manzon Allah a Ranar Badar

Xan Shi'ar ya ce: Babu wata falala ga Abubakar a cikin kasancewarsa tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin dabi ranar yaqin Badar. Domin kuwa hakan ba ta daxa Manzon da komai ba, saboda ba ya da

buqata da wani ya xebe masa kewa. Saboda wadda yake xebewa tare da Ubangijinsa ta ishe shi.

Ya kuma ci gaba da cewa: Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya zaunar da Abubakar ne a wurinsa, don gudun ya tura shi fagen fama ya dagula al'amurra. Don yana da tarihin gudowa daga yaqoqa daban-daban, inji shi. To, ka auna ka gani, wane ne mafi girman daraja, tsakanin wanda ke rafke da hannuwa alhali ga mazaje can na rafkewa, da wanda ke can ana goga qashi da shi don xaukaka kalimar Allah?!

**Martani:**

Wannan maganar da shehin ya furta ba a kan hanya take ba. Cewar da ya yi, Abubakar *Raliyallahu Anhu* na da tarihin gudu daga fagen fama a yaqoqi daban-daban, ya tabbatar da cewa, bai san tarihin yaqe-yaqen da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi ba.

Yaqin Badar shi ne yaqi na farko a tarihin musulunci. Kafin sa babu wani yaqi da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ko Abubakar suka yi da kafirai. To, a wane yaqi ya gudu kenan kafin Badar? To, ko a yaqin Badar ma da duk yaqoqan da aka yi a bayansa, ba inda Abubakar bai je ba, ba kuma inda aka bada rahoton ya yi raki, balle ya juya baya. Ko a ranar yaqin Uhudu, shi da Umar tsaye suke qyam kamar iccen giginya. Wanda dai ya shiga sahun waxanda suka firgita a ranar, jin cewa, Annabi ya mutu kamar yadda shexan ya yaxa, shi ne Usman. Kuma Allah ya gafarta masu. Amma Abubakar da Umar *Raliyallahu Anhuma* ba a sami wani malamin tarihi da ya tava cewa, suna cikin waxanda yaqi ya ci a ranar Hunainu ba. Hasali ma su suka yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ganbun tsari dama da hagu a wannan rana.

Da ta tabbata cewa, Abubakar matsoraci ne, kamar yadda wannan xan Shi'ah ya bayar da rahoto, da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai zave shi don ya zauna tare da shi a cikin dabin ba. Domin kuwa ba ya halatta a tafi yaqi tare da wanda yake haka. Ga al'ada kuma duk wanda zaka gani kusa ga uban tafiyar yaqi, lalle za ka taras da shi namijin gaske, wanda bai san tsoro ba. To, balle wanda aka zava daga cikin dubu aka ce ya zauna tare da shi.

Duk wanda ya san tarihin musulunci ya san cewa zuciyar Abubakar *Raliyallahu Anhu* ta fi ta sauran Sahabbai faxi da qarfi. Tun lokacin da aka aiko Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* Abubakar yake tsaye tsayin goxiyar Adamu, a cikin cikar jaruntaka da saxaukantaka, yana gumurzu da wahalhalu, har Allah ya karvi ransa. Ba a tava jin lokacin da ya yi raki ko qasa a guiwa gaban maqiya ba. Hasali ma lokacin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kwanta dama, sai da zukatan wasu Sahabbai suka girgiza, hantarsu ta kaxa, cikannansu suka xuri ruwa, Abubakar ne ya yi musu ganxo da yardar Allah. Haka yake a duk sauran wurare da rakin wasu daga cikinsu ya bayyana. A cikin ire-iren wannan halin ne Anas *Raliyallahu Anhu* ya ce: "Abubakar ya yi mana huxuba a lokacin da muke kamar kuraye. Bai gushe ba yana qarfafa mu har muka koma kamar zakoka".

An kuma riwaito cewa, watarana Umar *Raliyallahu Anhu* ya ce wa Abubakar: Ya halifan Manzon Allah! Ka yayyafa wa mutane ruwa. Sai Abubakar ya kama gemun Umar ya ce, me kake tsoro bayan ka musulunta, ina jaruntakar da kake da ita a zamanin jahiliyya?! Don me zan yayyafa masu ruwa; don qaryace-qaryacen da suka watsu a tsakaninsu, ko don waqe-waqen jahiliyyah?!

Ya ci gaba da cewa wai, ba a haxa wanda ke zaune rafke da hannuwa, alhali maza na can na rafkewa, da wanda ke can ana rafkewar da shi don xaukaka kalmar Allah.

Ba haka abin yake ba. Kasancewar Abubakar tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a wannan yanayi, ya fi shiga cikin filin daga. Domin kuwa,Manzon ne qarshen wanda maqiya ke son su kai ga. Saboda haka ne kashi xaya daga cikin uku na musulmi suka tsaya gadinsa, xaya kashin suka fatattaki maqiya, a yayin da sauran suka tattara ganima. A qarshe kuma Allah ya raba ta a tsakaninsu baki xaya.

Sai kuma cewar da ya yi wai, kewar da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ke xebewa da Ubangijinsa ta wadatar da shi daga buqatar wani abokin xebe kewa.

Abin da za mu ce a nan shi ne, ai wannan magana ba ta ko taso ba. Domin kuwa maganar ba ayar Qur'ani ba ce ko hadisi, balle xan Shi'ar ya yi qoqarin juya akalarta ko qaryata ta. Koda ko waxanda suka faxi wannan magana, ba suna nufin kasancewar Abubakar tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin dabin ta xebe kewar hira ce ba. A'a, suna nufin yana ba shi gudunmawa ne a cikin sha'anin yaqin da ke gudana kamar yadda sauran Sahabbai ke can kowa na bayar da tasa gudunmawa.

Idan ka fahimci abin haka, wannan matsayi da Abubakar ya kevanta da shi daraja ce da babu wanda ya samu irinta daga cikin Sahabbai. Domin babu kowa tare da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* sai shi. A yayin da ita ko waccan daraja da Aliyu *Raliyallahu Anhu* ya samu ta kasancewa cikin fagen fama, duk Sahabin da ke tare da shi a can ya same ta.

Ta kuma tabbata cewa, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Abubakar *Raliyallahu Anhu* sun fito daga cikin dabin, har Annabi ya harbi abokan gaba, harbin da Allah Ta'ala ya kwarzanta da cewa: *Kuma baka yi jifa ba a lokacin da kayi jifa; kuma amma Allah ne ya yi jifar 8:17.* Haka shi ma Siddiqu ya fatattake su, har ma bayan qare yaqin xansa Abdurrahmanu ya ce masa: "Ai na gan ka ranar yaqin Badar amma sai na lave don kar ka gan ni". Sai Abubakar ya ce masa: "Ka kuru! Da na gan ka sai wani ba kai ba".

### 9.13 Abubakar ya yi Hidimar Manzo da Dukiyarsa

Xan Shi'ar ya ce: amma cewar da Ahlus-Sunnah suka yi, wai Abubakar ya yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* hidima da dukiyarsa, ta hanyar xaukar nauyinsa, qarya ne. domin kuwa Abubakar ba mai arziki ba ne.

Hasali ma mahaifinsa talakka ne na qarshe, ta yadda kullum sai ya roqo mudu xaya daga Abdullahi xan Jud'ana kafin ya sami abin da zai sa ga baki. Da kuwa Abubakar na da dukiya, da ya xauki nauyin mahaifin nasa. Ko a lokacin jahiliyyah yara yake karantarwa. Da musulunci ya bayyana kuma sai ya kama sana'ar xunki. Bayan ya zama Sarkin Musulmi ne mutane suka hana shi wannan sana'a, suka yanka masa albashin dirhami uku kowace rana daga cikin baitul-mali don ya ci da iyalinsa.

**Martani:**

Haqiqa babu zalunci da qiren qarya kamar mutum ya musa abin da duniya ta gama sani, littafan hadisi da na tarihi da tafsiri da ire-irensu suka cika maqil da bayaninsa. A lokaci guda kuma ya yi qoqarin tabbatar da wasu riwayoyi waxanda daga bakinsa ne aka fara jin su, kuma babu wata madogara da ya ambata mai qwari balle a ji sanyi.

A irin yadda wannan magana take, ko mafi jahilci ya turke xan Shi'ar yana iya tabbatar masa da zamanta qarya, da kasancewar abin da muka faxa a matsayin masu tattaunawa da shi, gaskiya. Ina mamakin yadda mutum zai jajirce yana yayata labarin da ba ya da tushe. Idan kuma har xan Shi'ar na ganin abin da muke faxi sharholiya ce, to, ya faxa mana wani amintaccen malamin hadisi ko tarihi da ya riwaito wannan magana da shi ya faxa a kan Abubakar.

Zancen kuwa hidimar da Abubakar *Raliyallahu Anhu* ya yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ta dukiya, abu ne ingantacce, da riwayoyi suka tabbatar ta hanyoyi da fuskoki da dama. Har Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kasa barin abin a zuci ya ce: "Babu dukiyar wani da ta amfane ni kamar dukiyar Abubakar." Ya kuma tava cewa watarana: "Mafificin wanda ya amfanar da mu da kansa da dukiyarsa shi ne Abubakar". Haka kuma ta tabbata cewa, Abubakar ya fanshi wasu bayin da ba za su kasa mutum bakwai ba daga hannun kafirai, waxanda ake azabtarwa saboda imaninsu da Manzo, cikinsu har da Bilal da Amiru xan Fuhairata.

Ita ma maganar talaucin mahaifin halifa Abubakar da ya yi ba ta da asali. Koda kuma a qaddara ta inganta ba ta cutar da kome, domin gaba xayan al'amarin ya faru ne a zamanin jahiliyyah. Kuma Abdullahi xan Jud'ana ya rasu ne kafin bayyanar musulunci. Shi kuwa abu Quhafata mahaifin na Abubakar ba a tava sanin yana roqo ba. ga shi kuma mutum mai wadatar zuci, domin ko lokacin da xan nasa halifa Abubakar ya cika, kuma aka ba shi kashi xaya cikin shida na dukiyarsa a matsayin gado gaba xaya ya mayar da ita ga 'ya'yan na Abubakar.

Cewa, Abubakar malamin 'yan yara ne a lokacin jahiliyyah, abu ne da ke qara fitowa da xaukakarsa, tare da bayyana irin ilimin da yake da shi tun a wancan lokaci, idan har maganar ta kasance gaskiya. Duk da yake 'yan Shi'ah kamar mushrikan zamanin jahiliyyar Larabawa su ke. Kullum alfahari da tinqahonsu bai wuce asali da girman iyaye, ba addini ba. saboda haka za ka

taras kodayaushe, duk abin da za su yi wa wani gori da shi ba abu ne da zai nuna naqasar imani ko tsoron Allansa ba. wannan kuwa al'ada ce irin ta jahiliyyah.

Ita kuwa cewar da ya yi wai, Siddiqu ya kama sana'ar xinki bayan bayyanar musulunci har zuwa lokacin da ya zama halifa. A nan ma dai ya fesa ta. Duk da yake ko ta kasance gaskiya babu wani abin kunya ciki. Amma dai tarihi bai ambaci Abubakar ya tava sana'ar xinki ba. Abin da kawai aka sani shi xan kasuwa ne. Wani lokaci har ya kan bar gari ya tafi Sham don cin kasuwa. Wani lokaci kuma kasuwancin nasa kan daxe bai kai shi ga barin gari ba. Wannan kuwa abin alfahari ne, domin babu wata sana'a mai kadari a wajen Quraishawa da bayyana xaukakar mai yin ta kamar kasuwanci. Duk wani shahararre cikinsu a layin dukiya, zaka iske xan kasuwa ne, kuma da wannan sana'a ne suka shahara a duniya.

Gaskiya ne, bayan kasancewar Abubakar halifa ya so ya ci gaba da sana'a, amma ba ta xinki ba. Kasuwancin can dai ne nasa ya so ya xore da shi don nema wa iyalinsa abincin halas. Musulmi a lokacin suka ce atabau. Shugabanmu a kasuwa?! To, yaushe ya samu lokacin kula da ingancin rayuwarmu? Suka taru suka hana shi. Sannan suka haxu a kan yanka masa albashin da aka faxa.

Haka kuma xan Shi'ar ya ce, wai kafin hijirar Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* zuwa Madina, ya wadata da dukiyar Khadijatu *Raliyallahu Anha* kuma babu yaqi a lokacin. Saboda haka ba ya da buqata da abin hannun wani balle a ce Abubakar ya agaza masa.

To, ai ciyarwar da ake cewa Abubakar ya yi wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, ba ana nufin yana sai masa abinci ko sutura ne ba. Ta wannan vangare gaskiya, Allah ya riga ya wadatar da Manzonsa daga kowa. A'a, ana nufin ne Abubakar ya ciyar da dukiyarsa wajen hidimar bunqasa addinin musulunci don taimaka wa Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* isar da saqo. Saboda haka ya yi hidima ne don tabbatar da abin da Allah da Manzonsa ke so, ba don buqatun Annabi na qashin kansa ba. A wannan tafarki ne wannan tafarki ne ya fanshi Bialau da xan Fuhairata da Zinirratu da wasu da yawa, daga azabar da mushrikan Makkah ke yi musu.

Abu mafi ban ta kaici ma a cikin maganar xan Shi'ar duk bai fi cewar da ya yi wai, bayan hijira ma Abubakar fanko ya ci gaba da zama ba. Ta tabbata har zuwa wannan lokaci Abubakar na hidimar dukiya ga musulunci. Akwai watarana ma da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kwaxaitar da Sahabbai yin sadaqa, nan take Abubakar ya je ya kwaso gaban dukiyarsa da ke hannu ya kawo. Haka kuma Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya tava yekuwar agaza wa mutanen Suffa kamar yadda ya zo a cikin Buhari da Muslimu daga Abdurrahaman xan Abubakar. Nan take Abubakar ya tafi da uku daga cikinsu, shi kuma uban tafiyar *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kwashi goma.

Wani abin ban mamaki ma da ta kaici duk bai fi cewar da xan Shi'ar ya yi wai, da Abubakar ya yi irirn waccan hidima ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da lalle surar Alqur'ani ta sabka akan ta. Kamar yadda aka saukar da Surar *Hal Ata* a kansayyidina Ali *Raliyallahu Anhu*.

To, ka ga wannan magana ba gaskiya ba ce a wurin malaman hadisi. Amma marubutan tafsiri masu kwasar karan mahaukaciya ba a mamaki don sun ambace ta. Kuma ai waccan sura da yake magana a Makka aka saukar da ita, dalilin da ke bayyana qissar da suka jingina ga surar kitsa ta aka yi.

Muna da tabbacin cewa, ba wata sura ko wata aya da ta tava sauka don Ali ya ciyar da wani miskini ko makamancinsa, domin kuwa ba ya da sararin yin haka, musamman a lokacin da ake Makka sa'adda yake cikin gandun iyalan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da Manzon ke kula da su. A Madina kuwa, sanannen abu ne cewa, ko a lokacin aurensa da sharifiya Fatima bai samu wani sukunin yin wata hidima ba, don ba ya da kome a lokacin sai sulke.

Amma Abubakar Siddiqu, babu wata aya da ta sauka tana yabon waxanda suka ciyar da dukiyarsu saboda Allah, face shi ne farkon wanda take nufi. Kamar inda Allah ke cewa:

﴿لَا يَسْتَوِي مِنكُم مَّنْ أَنفَقَ مِن قَبْلِ ٱلْفَتْحِ وَقَٰتَلَ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ أَعْظَمُ دَرَجَةً مِّنَ ٱلَّذِينَ أَنفَقُوا۟ مِنۢ بَعْدُ وَقَٰتَلُوا۟ ۚ﴾ الحديد: ١٠

> *Wanda ya ciyar a gabanin cin nasara, kuma ya yi yaqi daga cikinku, ba ya zama daidai (da wanda bai yi haka ba). Waxancan ne mafifita girman daraja bisa ga waxanda suka ciyar daga baya kuma suka yi yaqi.. 57:10*

Ta kuma tabbata Abubakar ne na farko kuma mafifici.
Haka nan ita faxar Allah Ta'ala da ya ce:

﴿ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَهَاجَرُوا۟ وَجَٰهَدُوا۟ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ أَعْظَمُ دَرَجَةً عِندَ ٱللَّهِ ۚ وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْفَآئِزُونَ ﴿٢٠﴾﴾ التوبة: ٢٠

> *Waxanda suka yi imani, kuma yi hijira, kuma suka yi jihadi a cikin hanyar Allah, da dukiyoyinsu da rayukansu sun fi girman daraja a wurin Allah, kuma waxancan su ne masu rabo. 9:20*

Nan ma Abubakar shi ne liman.

Haka kuma malaman tafsiri irin su Xabari da Ibnu Abi Hatim da sauransu sun tabbatar ta hanyoyi da dama, daga Urwatu xan Zubairu da Abdullahi xan Zubairu da Sa'idu xan Musayyibu da sauransu cewa, ayoyin da Allah Ta'ala ke cewa: *Kuma mafi taqawa zai nisance ta. Wanda yake bayar da dukiyarsa, alhali yana tsalkaka.. 92:17-18* duk an saukar da su ne a kan Abubakar.

**9.14 Abubakar Xin ne Dai Liman**

Xan Shi'ar ya ce: Cewar da Ahlus-Sunnah ke yi wai, Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne ya shugabantar da Abubakar ya limanci Sahabbai kuskure ne. A'ishah ce dai ta umurci Bilalu bayan ya yi kiran sallah, da ya gabatar Abubakar ya yi limanci. Yayin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya farfaxo, ya ji kabarbari na tashi, sai ya ce, wane ne ke bayar da sallah? Waxanda ke tare da shi sai suka ce, Abubakar ne. Sai ya ce: Ku riqa ni in fita. Sai Abbas da Ali suka riqa shi ya fita. Ya je ya kama kafaxun Abubakar ya raba shi da Alqibla, shi kuma ya ci gaba da bada sallar.

**Martani:**

Abu na farko dai, gaba xayan malaman hadisi sun yi watsi da wannan. Idan kuma har xan Shi'ar na jin ba su yi masa adalci ba to, ga fili ga mai doki. Sai ya gaya mana wanda ya riwaito ta. Idan kuwa ba haka ba, to, jahilcin ya bayyana. Domin zaton yake yi wannan ne karon farko da Abubakar ya limanci Sahabbai. Alhali kuwa gaba xayan masu ilimi babu wanda bai san cewa, tsawon kwanakin da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi yana jinya Abubakar ne ke bada sallah ba, har Allah ya karvi ran Manzo. Ya kuma yi haka ne tare da izinin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*.

Hasali ma a rana ta farko, wani Manzo ne Annabi ya aika ma Abubakar da maganar ba A'ishah ba, kamar yadda 'yan Shi'ah ke son cewa.

Cewar da suka yi A'ishah ce ta umurci Bilalu, bayan ya gama kiran sallah da ya gabatar da Abubakar, ba haka abin yake ba. A'ishah ba ta hore shi da haka ba, a matsayin umurnin qashin kanta ko na Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*. Bilalu ne manzon da ya isar da saqon ga Abubakar bayan Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya kalli taronsu ya ce: "Ku ce wa Abubakar na ce, ya bayar da sallah".

Nassosa da dama sun tabbatar da cewa, Sahabi Abubakar ya kwashe kwanaki da dama yana limanci, kafin wannan fitowa da Annabi ya yi, ya kuma kwashe wasu kwanukan yana yi bayan haka. Domin kuwa Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* bai sake samun damar limancin sallar ba, tun ranar da ya kwanta ciwo har zuwa wadda ya cika a cikinta. Babu kuma wanda ya tava limancin sallar bayansa. Hanyoyi kuma da dama sun tabbatar da cewa, kwanakin da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya yi yana jinya suna da yawa.

To, muna neman wannan malamin da ya faxa mana wanda ya wakilci Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a sauran kwanukan. Mu a iya saninmu, babu wani mutum kafin yau da ya ce Umar ko Ali ko waninsu ne ya wakilci Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a wannan lokaci. Da yake duk sallolin nan a cikin jama'a ake yin su, da wani ya tava limancin ba Abubakar ba da duniya ta ji. Ko da suvul-da-baka ko ba a samu wanda ya ce haka ba.

Kuma ko ba a gaya maka ba, ka san bata yiwuwa Abubakar *Raliyallahu Anhu* ko wani daga cikin Sahabbai ya yi limancin tsawon wannan lokaci ba

tare da masaniyar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ba. Kai, haka ma ba zata tava faruwa ba, sai Sahabban sun nemi amincewarsa tun da ba shanu ba ne kafin su yi sallah bayan wani a madadinsa. Al'ada da shari'a duk ba za su yarda da haka ba.

## 9.15 Darajojin Abubakar a Cikin Hadissai[1]

Duk wanda ya bi diddigin littafan hadisi ingantattu zai taras da su cike da darajojin Abubakar. Kamar hadisan da ke nuna tsananin soyayyar da ke tsakaninsa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, da kariyar da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* yake yi masa idan an tava shi, da haxa hancin ayyukan alheri da yake yi a rana xaya, da haqurinsa da kusancinsa ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da kariyarsa gare shi, da shugabantar da shi akan jama'a, a mafi girman ibadu; sallah da hajji da makamantansu.

Abin da ya dame mu a nan shi ne, mu tabbatar da kevantuwar da Abubakar ya yi da abokantakar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* a cikin zauren imani, irin abotar da babu wani mahaluki da ya yi tarayya da shi a ciki. Duk abin da ke cikin wannan abokantaka, na xaukaka da daraja da kykkyawan sakamako, wani bai same shi ba baya ga Abubakar. Hasali ma da za a qididdige kevancewa wuri xaya da Abubakar ya yi da Annabi, a kuma qididdige wadda Usman da Aliyu ko waninsu daga cikin Sahabbai ya yi da shi, tasa ta fi yawa nesa ba kusa ba. Kai babu ma wani daga cikin Sahabbai da ya tava kevewa da Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* face tare da Abubakar, ko ya isko su kafin su rabu.

Dangane kuma da abin da ya shafi cikar sanin haqiqar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* da kusanci ga reshi da tsabar sonsa da gasgata shi a komai, da taimako akan yaxa addini, Abubakar ya baxa wa kowa qura a wannan layin.

Kai, babu wani abu na falala daga cikin abubuwan da ke sa abokantaka da tare su karva sunansu, irin waxanda suka fifita Sahabban Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* a kan waxanda ba su ba, face ka iske a cikinsu Abubakar ya yi wa kowa rata. Irin taren da ya yi da Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ta girma da azziki da mutunci babu wanda ya yi ta daga cikinsu.

Abin da ya zo a cikin Buhari da Muslim daga Abu Sa'id al-Khudri na qara tabbatar da haka. Watarana Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya zauna a kan mimbari, sai ya ce: "Haqiqa Allah ya bai wa wani bawa nasa zavi tsakanin duniya da abin da ke wurinsa, sai bawan ya zavi abin da ke wurin Allah". Qare faxar haka ke da wuya, sai Abubakar ya fashe da kuka yana cewa: "Mun fanshe ka da uwayenmu maza da mata ya Manzon Allah!". Abu Sa'idu ya ce: Ashe Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ne bawan da Allah ya

[1] Wannan babi mun cirato shi ne a can inda mawallafin yake mayar da martani akan cewar xan Shi'an wai, rakiyar da sayyidina Abubakar ya yi wa Manzo ba daraja ba ce. Cire waxannan hadissai daga wannan babin ya zo ne don zaren tunanin mai karatu ya tafi ba tangarxa. Masu Fassara.

ba zavin. Amma daga cikinmu babu wanda ya gano haka sai Abubakar don ya fi kowa sanin Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* daga cikinmu.

Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya ci gaba da cewa: "Babu wani daga cikin mutane da ya saxaukar da kansa da dukiyarsa gare ni kamar Abubakar. Da kuma ina da ikon zaven badaxayi daga cikin mutane da na zavi Abubakar. Amma sunan tarena da shi 'yan'uwantakar musulunci. Kada ku bar kowace qofa daga cikin qofofin da kuka buxe a masallaci sai ta Abubakar".

A wata hadisi na Buhari daga Ibnu Abbas ya ce: Watarana Annabi *Sallallahu Alaihi Wasallama* ya fita daidai lokacin da yake fama da rashin lafiyar ajali, yana xaure da wani qyalle a kansa, ya zauna a kan mimbari, ya gode wa Allah, ya kuma yi yabo gare shi. Sannan ya ce: "Haqiqa, babu wani mutum da ya saxaukar da kansa da dukiyarsa gare ni kamar Abubakr xan Quhafata. Da kuwa ina da ikon zaven wani badaxayi daga cikin mutane, da na zave shi. Amma 'yan'uwantakar musulunci ta fi komai. Ku rufe duk wata qofa mai zuwa masallaci in banda ta Abubakar". A wata riwaya ya ce: "Amma Abubakar xan'uwana ne, kuma abokina".

Gaba xayan waxannan nassosa, na bayyana irin yadda Abubakar ya kevanta da falalar abokantakar Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama*, da irin yadda ya tsare mutuncin taren fiye da kowa, har hakan ta wajabta kasancewarsa mafi cancantar zama badaxayinsa da haka na yiwuwa.

Abin da waxannan hadisai ke nunawa na kasancewar Abubakar *Raliyallahu Anhu* mafi kusanci da soyuwar mutane zuwa ga Manzon Allah *Sallallahu Alaihi Wasallama* shi ne abin da Manzo xin ya bayyana qarara a cikin hadisin Amru xan Asi da aka tambaye shi: Wa ka fi so daga cikin mutane? Ya ce: "A'ishah". Aka ce: Daga cikin maza fa? Ya ce: "Babanta". Aka ce: Bayansa fa? Ya ce: "Umar". Sannan ya lissafa wasu mutane. Buhari da Muslim suka riwaito shi. A riwayar Buhari Amru ya ce: Sai na kama bakina don kada ya kai ni na qarshe.

Allah ya daxa tsira da aminci ga bawansa kuma Manzonsa Muhammadu *Sallallahu Alaihi Wasallama* da iyalansa da matansa. Allah ya daxa yarda da Abubakar da Umar da gaba xayan Sahabbai, cikakkiyar yarda da mafi tsarkin tsira. Allah ka tayar da mu a cikin tawagarsu. Amin.